NIMA MATARSA CE!

NA

HABIBA ABUBAKAR IMAM (YAR GIDAN IMAM)

PAID GROUP 300
Ku tuntube ni ta wannan number 08174970500 a WhatsApp KO Ku tura ta account 2083086009 Habiba Abubakar Imam UBA Bank KO katin MTN.

SHAFIN FARKO

Falo ne Kato Wanda yake dauke da duk wani nau'i na kayan alatu Wanda falon hamshakan masu kudi ne kadai ake iya samunsu, falon ya kawatu kwarai matuka. Kan kujera me zaman mutum daya Taufiq ne zaune cikin shiga ta Kamala kyakkyawan matashi ne ajin farko baki ne amma bakinsa me kyaune.An cika teburin glass din gabansa da Kayan ciye ciye da lemo Kala -kala Amma babu abinda Taufiq ya iya dauka ya ci saboda zuciyarsa cike take da sake-sake na dalilin Kiran da Haj. Murjanatu tayi masa na gaggawa Wanda KO kadan Bai son duk wani dalili da zaisa ta Kira Shi domin yayi Imani da cewa bakinta bazai taba furta abinda zaisa ransa yayi masa dadi ba ,tunda bikin nan ya kusa kullum cikin fito da sabbin abubuwa take Wanda suke barazana ga Samun nutsuwarsa."wai har yanzu babu abinda kaci",muryar mujaheeda ta katse masa tunaninsa ya waiwayo Yana kallonta Fara CE Amma irin farin da akance Bai rufama muni asiri ba ahaka Ka kalleta zaka iya kiranta da kyakkyawa Kai tsaye amma da zaran Ka zuba Mata Ido zaka fahimci tsabar iya kwalliya ne zaisa Ka kirata da kyakkyawa,sai dai kallo daya zaka Mata Ka gamsu da cewa yarinya ce yar Hutu me ji da kanta wacce aka bata dukkan gata da kulawa na musamman.

" Na gaya Miki akoshe nake bazan iya cin komai ba"ta gyada Kai gami da yarfar da hannunta gefe alamar bai dameta ba ràshin cin nasa,tace "mummy tace Ka sameta afalon sama,muje KO",da sauri ya amsa da toh gami da mikewa tana gaba Yana binta abaya har zuwa falon sama Wanda har ya so yafi falon kasan kyau da tsaruwa can Kan doguwar kujera haj.murjanatu ce kishingide ,Taufiq ya zube akasa Yana gaisheta ayayinda mujaheeda ta koma kusa da mahaifiyarta ta lafe ajikinta tana sangarta kamar yadda ta Saba. haj murjanatu ta dubi Taufiq tace "Taufiq na bukaci kazo ne saboda ina son nayi wata magana da Kai Mai muhimmanci", ya Dan gyara zamansa yace "Allah yasa lafiya"ta jinjina Kai tace "lafiya kalau"ta dawo da kallonta Kan tilon yarta sannan ta dauke idonta ta tsaidashi Kan Taufiq tace "ina son kasan cewa duk duniya Bani da wani abu da nafi so sama da yata mujaheeda farincikinta da kwanciyar hankalinta shine nawa Zan iya yin komai domin dauwamar da farinciki acikin rayuwarta,hakan Yana daya daga cikin dalilin da yasa na amince Ka aureta duk da nasan ba Kai bane kalar Mijin daya dace ta aura saboda abinda Ka mallaka ba zaka iya rike yata dashi ba,Amma tunda ta nuna Kai take so dole na tayata son abinda take so babu yadda zanyi".ta hadiye yawu gami da Kara kafe Taufiq da Ido Wanda yake Jin maganganunta tamkar ana watsa

masa wuta ajiki me yasa bata taba daukarsa wani abin kwarai ba bayan duk tarin nagartar dake gareshi?kullum ta Sami Dama Saita kushe Shi ta nuna Bai dace da yarta ba .acikin isa ta cigaba da cewa "atakaice na kiraka na gaya maka cewa bqbu yadda Zan amince ace Ka aje yata acikin gidan gado inda iyayenka da Matan yayyanka suke bata taso airin wannan rayuwar ba, ba Kuma zata iya ba arana tsaka,saboda haka cikin biyu saika zabi daya ko bayan daura auren Ka dawo nan gidan da Zama KO Kuma na Baka gida acikin gidajena Wanda zaiyi dai dai da rayuwar yata inda zata wala babu takura balle tsangwama".Taufiq yayi gaggawar dago da Kansa ya dubeta ta jinjina Kai tace "eh haka nace,ya rage naka kaje kayi shawara biki dai saura sati uku",wani gululun bakinciki ya tokare makogwaronsa ahankali yace "toh shikenan,ni Zan tafi" ya fada Yana kokarin mikewa tsaye haj murjanatu ta bishi da kallo ba tare da tace masa uffan ba har ya Fara tafiya sannan mujaheeda ta taso ta biyo bayan Shi fuskarta babu KO alamar damuwa da maganganun da mahaifiyarta ta gaya mishi ya juyo ya dubeta fuska a hade yace ",da kin koma nagode ",tsayawa tayi cike da sangarta tace "Okey bye bye sai munyi waya" ta juya ta koma.

Cikin matukar bacin Rai da damuwa ya fito ya shiga motarsa discussion continue maigadi ya Bude masa get Yana a sauka lafiya hannu kawai ya daga masa ya figi motarsa ya tafi.

Tuki kawai yakeyi Amma tunani ne fal aransa,sau tari yasha tambayar Kansa shin meyasa bazai hakura da auren mujaheeda ba bayan yasan irin takun sakan dake tsakaninsa da mahaifiyarta,tunda ya Fara son yarta yake kunsar bakincikinta take kaskantar dashi don kawai mahaifinsa yayi aiki a karkashin mijinta tana ganin kaskanci ne ta aurama yarta Dan yaron mijinta bayan Mijin nata ma baya raye,Wanda Kuma take aure Bai Isa yasa KO ya hana ba,shin me yasa duk yasan wannan Amma yake kwadayin auren mujaheeda yarinyar daya fi kowa sanin irin shagwabata da sangartar da ita da mahaifiyarta tayi,sau tari yasha yin tunanin ya fasa auren Amma sai yaji ya kasa saboda masifar da Allah ya Dora masa na Sonta .Amma dole yaje ya zauna da mahaifansa ya gayá musu bukatar haj murjanatu Wanda Suma inda gajiya yaci ace sun gaji da irin korafin da da takeyi kullum.

NIMA MATARSA CE!

HABIBA ABUBAKAR IMAM
(YAR GIDAN IMAM)

PAID GROUP 300
Ku tuntube ni ta wannan number 08174970500 a WhatsApp KO Ku tura ta account 2083086009 Habiba Abubakar Imam UBA Bank KO katin MTN.

FREE PAGE

SHAFI NA BIYU

****

Taufiq ya tsaida motarsa acikin harabar gidan,ya Dan Jima acikin mota kafin ya iya bude kofar motar ya fito ,gaba daya jikinsa babu karfi,a hankali ya taka zuwa cikin gidan Wanda gidane na rufin asiri don duk Wanda ya mallaki gidan ba za'a kirashi da talaka ba.shin wane kaskanci haj.murjanatu take kallo acikin wannan zuriar?.

Kai tsaye falon mahaifinsa Alh. Yusuf lamido ya wuce sanin Yana gida awannan lokacin,cikin sallama ya shiga falon tare suka amsa sallamar da mahaifiyarsa haj.saratu wacce take aikin damama Alh Yusuf lamido fura."Ka dawo ?" Cewar haj saratu ya amsa Yana kokarin zaunawa akasan falon "na dawo umma",daganan cikin girmamawa ya gaidasu,ya cigaba da Zama ba tare daya Kara cewa komai ba bayan gaisuwar.jefi jefi mahaifan nasa suna kallonsa duk sun gama nazarin damuwar da yake ciki hakan yasa bayan Haj saratu ta gama dama furar ta ba Alh Yusuf lamido ta koma ta nemi waje ta zauna tana cigaba da kallon dan nata.

Zatayi magana kenan Alh Yusuf lamido ya rigata, "Taufiq yayane? Akwai damuwa ne?"Haj saratu tace "abinda nake son na tambaye Shi kenan don fuskarka ta nuna kana cikin damuwa menene?"

Taufiq yadan muskuta gami da gyara zamansa sannan yace"hakane ina da damuwa wacce bata wuce ta mahaifiyar mujaheeda". Haj saratu ta saki numfashi ahankali tace "Kai jamaa aikin kenan me Kuma tayi,ta Kara gindaya wani sharadinne?",Alh Yusuf lamido ya aje furarsa a gefe gami da cire gilashin fuskarsa Kamala da nagartarsa ta Kara fitowa ya dubi Taufiq yace "meya faru tsakaninku?".sannu ahankali Taufiq ya gama gaya musu duk yadda sukayi da Haj murjanatu ya Kara da cewa"Gaskiya Abba lamarin nan ya Fara Bani tsoro na Fara hangoma Kaina daukar dala babu gammo,ta yaya za'ayi ace Haj murjanatu zata dinga Dora min abubuwa masu wahala Masu kama da kora da hali na riga na yardarma Kaina cewa ta gama Raina matsayina tana kallona amatsayin Wanda be isa ba tana kallona amatsayin Wanda kamar zatayi masa alfarma Amma wannan Karon Bana Jin Zan yarda da wannan sharadin nata ni gaba dayama auran ya Fara fita araina,ta ina ta yaya Zan auri yarta Kuma na koma gidanta da Zama? KO ta yaya Zan watsar da darajata na amshi gidanta na zauna da yarta aciki meye matsayina idan nayi hakan," ya karasa magana da sauti me cike da tsantsar damuwa.

Alh Yusuf lamido yayi shuru idanunsa na kafe akasan kafet din falon,ayayinda Haj saratu ta numfasa itama duk damuwa ta baibaye fuskarta tace " Ni Kam na rasa wace irin macece Haj murjanatu,wacce ta dauki rayuwar duniya tamkar ba zaa mutu ba babu komai agabanta face arziki bata ganin kowa da daraja idan ba Mai arziki ba,fitinarta tayi yawa sai kace akanta aka fara aurar da ya,duk wulakance wulakancemta ta gama don dole ta yarda da auren saboda yarta na so Amma Kuma duk da haka ba zaa samu kwanciyar hankali da maslaha ba komai ita zata tsara Aina aka taba wannan,gaskiya Taufiq ina tausaya maka don ban hango maka farinciki acikin wannan al'amarin ba",Alh Yusuf lamido yayi saurin dakatar da ita yace "Kada kiyi masa mugun baki insha'Allah zai Sami farinciki acikin auransa" ya dawo da kallonsa Kan Taufiq yace "Taufiq Ka kwantar da hankalinka duk wani bawa baya tsallake kaddararsa idan har mujaheeda Allah ya zaba maka amatsayin Mata babu Wanda ya isa ya hana hakan kasancewa,Kuma ni duk abinda Haj murjanatu takeyi baya damuna saboda bana kallonta marigayi Alh sulaiman kadai nake kallo mahaifin mujaheeda Wanda bazan taba manta halaccinsa gareni ba nayi aiki dashi Bai min mugunta ba duk abinda na Samu na Samu ne

asanadiyyar Shi har Allah ya dauki ransa bamu taba batawa ba Bai taba fadan aibuna ba ban taba fadan aibunsa ba mutum ne me mutunci da sanin darajar Dan Adam hakan yasa nake son mujaheeda ta kasance surukata don na Kula da ita kamar yadda uba yake kulawa da yarsa" ya aje numfashi ahankali Yana cigaba da kallon Taufiq yace" Akwai halin mutum da bazaka iya canjashi ba to irin halin Haj murjanatu kenan tana da baudaddan Hali nasanta nasan halinta bata da kirki Shi Kansa marigayi Alh sulaiman baiji dadinta ba macece me izza kudi na zugata don haka yasa duk abinda takeyi baya Bani mamaki kaima Kuma ina son Ka cirema kanka damuwarta tunda kana son yarta Ka kauda kanka akanta da halinta" Haj saratu ta dubeshi tace "Amma Alh Baka ganin zakewarta yayi yawa gaba dayafa ayadda na fahimceta so take taja akalar rayuwar auren yaran nan don Bana Jin ko auran akayi zata bar Taufiq ya Zama namiji agidansa Wanda Kuma Kai kanka kasan akwai matsala,Kuma yanzu awannan sharadin data gindaya kana ga akwai hanyar bullewa yaron nan ya gyara bangaransa ya kashe kudi yayima wajen hidima, bugu da Kari idan tayi hakuri ta bari ta Fara Zama anan din inace Gini yake yi ahankali zai Gama kwana nawa ne idan Allah yasa ya gama ginin zasu tashi su koma gidansu meye abin gaggawa,meye aibu don sun Fara Zama anan KO ko rainin arzikin data Saba ne yasa zata CE haka" Alh Yusuf lamido yace "Na fahimceki kema ina son ki fahimceni ,itafa Haj murjanatu tunda bata son auren nan duk hanyar da zata bata lamarin Shi zata bi don haka biye Mata bashi da amfani" ya dawo da kallonsa Kan Taufiq ya Kira sunansa ya amsa sannan yace"kayi hakuri Ka karbi gidan da zata Baku Ku zauna,Ka cigaba da gininka ranar da Allah yasa Ka gama saika tattara Ka dawo gidanka bikin nan ya kusa kowa yasani Bana son asami wata matsala me kama da an fasa Ka kyaleta ta karata ina CE dai idan aka daura auren shikenan duk wani iko ya dawo hannuna" Taufiq ya girgiza Kai yace "Abba bana Jin KO Anyi auren nan Zan mallaki yancina da cikakken maigida Bana Jin zata barmi na tsara rayuwar gidana yadda nake so dagaske Abba ina Jin kamar nace na fasa auren nan" ya daga masa hannu yace " Kada Ka Kara fadan haka yar Alh sulaiman tafi karfin haka awajenmu kamar yadda na gaya maka ne Ka yarda da bukatar ta wahalarta adaura auren kama cirema kanka damuwa Ka fita batunta"

Taufiq ya aje numfashi ahankali cikin ràshin sanin madafar dafawa yace "shikenan Abba babu damuwa zanyi abinda kace" Haj saratu cikin ràshin gamsuwa da hukuncin tace " yanzu shikenan duk wahalar daya sha wajen gyaran wajen nan ya tashi abanza tsakani da Allah babu adalci awannan maganar na rasa abinda Haj murjanatu ta dauki kanta " Alh Yusuf lamido ya dau furarsa ya cigaba dasha Yana cewa " gyaran waje Bai tashi abanza ba ga kaninsa nan Ibrahim duk ranar daya tashi aue shiga kawai zaiyi babu wata damuwa" Shi Kansa Taufiq Bai dauka humncin da mahaifin nasa zai yanke kenan ba asanyaye ya tashi ya fita duk jikinsa babu laka.

***** ***** ***** *****

BABI NA UKU

NIMA MATARSA CE

NA

HÀBIBA ABUBAKAR IMAM

(YAR GIDAN IMAM)

FREE PAGE

PAID GROUP 300 KU TUNTUBENI TA WANNAN NUMBER TA WHATAPP 08174970500 ,KO A TURO TA 2083086009 UBA BANK HABIBA ABUBAKAR IMAM .

***** *****

Mujaheeda na kwance asaman doguwar kujera cikin kwalliya ta alfarma Kai Ka dauka wani waje zata,sai tashin kamshi take na musamman, karfe takwas da minti daya ne na dare,tana rike da wayarta iPhone 14 Ga iPhone 13 can asaman tebur gefenta Ga daya wayarta nan Samsung s22 ultra.

Hadimanta guda biyu lami da lauratu suna ta aikin Kai kawo akan bukatunta duk sun cika gabanta da abubuwan ciye ciye masu saukin ci marasa nauyi Wanda suka dace aci da daddare.Babu Wanda take kallo acikinsu idonta na Kan waya tana aikin danne danne babu abinda ya dameta.Har zuwa lokacin da Alh Mustapha labaran ya shigo falon cikin sallama duk su lami sukayi masa sannu da zuwa gami da ficewa daga falon , sannan Mujaheeda ta waiwayo ta dubeshi ahankali tace "sannu da zuwa daddy",ya dan dubeta yace " mujaheeda kina lafiya",ta amsa "lafiya lau".Dai dai lokacin Haj murjanatu ta shigo falon itama cikin shiga ta kasaita Kai da kallonta kasan kudi suna hsukatata,ta dubi yarta tace "Sun tura miki datar"ta gyada Kai tace "sun tura " ta fada atakaice,Haj murjanatu ta saki tsaki tace "Don shirme kuna sane da lokacin da ya kamata kusa data Amma wai har sai an tuna musu na rantse idan sukayi wasa Zan canja inda zaa dinga Sanya Miki data ba tare da sun dinga bata Miki Rai ba" mujaheeda ta shagwabe fuska tace "Gaskiya mummy gara kiyi hakan kawai".

Alh Mustapha labaran ya aje boyayyiyar ajiyar zuciyarsa gami da gyara zamansa zuciyarsa cike da Jin zafin yadda Haj murjanatu take lalata rayuwar yarta da kanta,ta shagwabata ta fifitata ta dauki son duniya ta Dora Mata ,duk da bashi ya haifeta ba hakika ransa Bai masa dadi ,yadda ta gurbata rayuwar yarta.ya dawo da kallonsa Kan manya manyan wayoyin da mujaheeda take rikewa Wanda duk wata datar da ake Dora musu yà ishi Haj murjanatu ta dauki hidimar marayu masu yawa.

"Ka dawo?" Muryar Haj murjanatu ta katsema Alh Mustapha labaran tunaninsa,ya juyo Yana kallonta sannan yace "eh nadawo",ta nemi kujera ta zauna tana dubansa tace " An Sami fito da Kayan"ya gyada Kai yace "eh ,masu shima har sun zo sun dauka ,sun Kuma tura sauran kudin"ta gyada Kai tace " Hakan yayi kaga an warware dasu ,hankali ya kwanta" yace " sosai kuwa".

Mujaheeda ta dubi Haj murjanatu tace "mummy Taufiq ya turo text" ta dubeta sosai tace "Kan maganar da mukayi KO me?" Ta Dan gyara kwanciyar ta tace "eh", nan da nan ta hade rai tace "yafi karfin ya Kira waya,KO ya dawo ya Fada da bakinsa shine zai turo sako saboda tsabar ràshin muhimmancin maganar agunsa". mujaheeda tace " mummy don Allah ki daina fadin irin maganganun nan akan Taufiq zuciyata fa bata min dadi " ta saki tsaki tace " saboda ke dinne ma nake daga masa kafa don babu yadda zanyi Amma har kullum bazan fasa gaya Miki ba Taufiq Bai dace da ke ba asalima nayi Imani KO bukatarki daya bazai iya dauka ya biya ba tun daga abinda kike ci zuwa kayan da kike Sawa da man da kike shafawa balle aje batun bukatunki na yau da kullum,babu abinda zai iya tsinana Miki".

Alh Mustapha labaran ya muskuta cike da ràshin jindadin maganganun da Haj murjanatu take yi yace " wai Haj me yasa kike kallon yaron nan amatsayin Wanda be isa ya auri mujaheeda ba,bayan dimbin tarbiyya da nagarta da yake dashi ta KO wace fuska mujaheeda tayi Saar Miji

baida wata makusa ,illa ke da kike kokarin dole sai kin dauka kushe kin Dora akansa ,"

Tayi saurin dubansa tace " zaka Fara ko Alh?" Ya girgiza Kai yace "Ba batun Zan Fara bane akalla ya kamata ki Fara dawowa hayyacinki ki fahimci ba kudi bane kadai jindadin rayuwa ba Kuma me arziki bane kadai me daraja da mutunci aah ina tabbatar Miki wani talakan yafi wani me kudin arziki da daraja da mutunci ba komai kudi yake saya ba ba komai kudi yake badawa ba ,haka zalika ba koina kudi yake kawo kwanciyar hankali da jindadi ba,kallon da kikema talaka ba dai dai bane"

Haj murjanatu ta Tabe Baki tace " shikenan don kana son na daidaita tsakanin talaka da me kudi sai na rungumi talaka ya Zama abokin rayuwar yata bayan kafi kowa sanin yadda yarinyata ta taso da irin rayuwar da take ciki da irin gatan Dana bata ,kasan Kuma ban hada kowa da ita ba", ya Kara gyara zamansa yace " Tunaninki da hasashenki bazan taba hanaki ba don da Zan iya hanaki da tuni nayi hakan shekara da shekaru don haka na barki da Tunaninki. Amma kisani Taufiq da kikema kallon talaka be isa ya auri mujaheeda ba ba dai dai bane, saboda Taufiq baya sahun talaka mutumin da yake da babban aiki ahannunsa ,yake da ilimi yake da abin hawa yake iya daukar hidimar wasu yake iya kyauta ya Kuma fi karfin bukatunsa to ya wuce adinga jifansa da Kalmar talauci,Kuma Samun namiji irinsa yanzu sai an tona kamata yayi ma Kima Allah godiya da yasa shine zai auri mujaheeda don babu Wanda zai iya da Halinki da nata sai Shi".

Nan da nan Haj murjanatu ta hayayyako tace " meye halin nawa da na mujaheedan? Ko kaima zaka jefeta da Kalmar ràshin tarbiyyar ne kamar yadda wasu ke fada,tunda Naga tamkar Taufiq yafi mujaheeda muhimmanci awajenka", ya girgiza Kai yace " Uba Ai Bai taba jifan yarsa da Kalmar ràshin tarbiyya sai dai yakamata ki Kula kiyi tunani KO don. Sabuwar rayuwar da mujaheeda zata shiga ayanzu ki tallafeta ki fahimtar da ita meye ma Kalmar Auren Dan nayi Imani bata sani ba"

Haj murjanatu ta hadiye yawun takaici tana kallonsa ranta abace batace uffan ba ta dubi mujaheeda wacce tayi shuru ta Dora hannunta asaman kuncinta,babu abinda ta tsana sama da ràshin zaman lafiya da hadin Kan da mahaifiyarta ba tayi da daddy in dai zasu zauna tare to minti biyar yayi yawa zaa Fara fada,sau tari tana yawan tambayar kanta wai Dama haka zaman aure yake babu komai cikinsa sai fada da tashin hankali.

" Wace amsa ya bayar" Haj murjanatu ta tambayi mujaheeda tana cigaba da kallonta , mujaheeda tadan numfasa sannan tace" yace bazai iya Zama acikin nan gidan ba, Amma zai iya Zama a daya daga cikin gidajenki, Amma shima da sharadin idan ya gama gininsa zai koma gidansa da Zama"

Haj murjanatu ta saki tsaki tace " oho dai ,ba dai zaki zauna a gidan gado ba"

Alh Mustapha labaran yayi Mata wani irin kallo yace " yanzu kina nufin inda zai zauna da matarsa ma sai kin zaba masa Haj "

" To da me kake tsammani nabar yata ta zauna a gidan gado inda zaa hanata sakat to ban raini yata don daga karshe taje ta wahala agidan wani Kato ba"

Numfashi kawai ya aje ba tare daya Kara cewa komai ba ya Mike ya shige daki,a zahiri Yana tausayin Taufiq auransa da mujaheeda ba karamin kalubale bane a gareshi,hakika don baa kawo cikas akan aure ne Amma da Shi da Kansa zai gayama Taufiq ya rabu da mujaheeda don bata dace dashi ba.

Kwarai da gaske Yana ganin darajar mahaifin Taufiq Yana ganin kimarsa Kuma Yana ganin mutuncin Taufiq Yana jinsa aransa kamar Shi ya haifeshi,

Bai son duk wani abu dazai taba kwanciyar hankali Taufiq Wanda yayi Imani auren mujaheeda shine babban ràshin kwanciyar hankalin da zai fuskanta a rayuwarsa.

***** *****

Washe gari Alh Mustapha labaran da Kansa ya tafi gidan Alh Yusuf lamido,ya Kira Taufiq duk suka hadu a falon Alh Yusuf lamido.

Sun Dade suna tattaunawa Kan maganar data kawo Alh Mustapha labaran inda ya cigaba da cewa,

" Duk wani abu da Haj tasan zatayi, Wanda ya sabama hankali bata Bari nasani asalima bata son sani cikin duk wani lamari datasan Zan iya Mata gyara aciki,shiyasa da zatayi wannan KO kadan ban sani ba,don Allah ku Kara hakuri akan halinta

Tunda aikin Gama ya Riga ya gama auren nan yazo kuyi hakuri akarasa ahaka daga sanda ya aureta babu wani sharadi KO wani iko da dole zaa bi nata." Taufiq ya numfasa cike da damuwa yace ,"Ni kam Alh Bana tunanin Ko auren nan akayi zata barmu mu sami natsuwa".

Alh Mustapha labaran yace "kaine zaka dage Ka Zama namiji agidanka KO kadan Kada Ka bata damar da zata shiga cikin lamarin gidanka," ya karasa magana Yana yi masa kallon tausayi don ya fishi sanin dala ba gammon daya dakkoma Kansa don auren mujaheeda Alh Mustapha labaran yasan shine kuskure na karshe da zaiyi a rayuwarsa Amma ta yaya zai fahimtar dashi?,

Alh Yusuf lamido ya dubi Alh Mustapha labaran yace " babu komai Alh nagode kwarai da yadda kake nuna damuwa akan lamarin yaran nan ,ina Kuma Kara tabbatar maka da cewa Ko da wasa duk wani abu da haj zata nuna KO ta bullo dashi bazai taba Sawa mu janye daga maganar auren nan ba,Kada kadamu".

Alh Mustapha labaran yajindadin maganganunsa shima yayi masa godiya kafin sukayi sallama ya tafi.zuciyarsa cike da tunanin irin sa'ar da mujaheeda tayi na shigowa cikin wannan kyakkyawar zuriar wacce Yana Mata fata gami da adduar Allah yasa sanadiyyar gyaruwar tarbiyyarta ne .

DAGA TASKAR YAR GIDAN IMAM.

********** **********

BABI NA HUDU

NIMA MATARSA CE

NA

HÀBIBA ABUBAKAR IMAM

(YAR GIDAN IMAM)

FREE PAGE

PAID GROUP 300,KU TUNTUBE NI TA WANNAN NUMBER TA WHATAPP 08174970500,KO A TURO TA 2083086009 UBA BANK HABIBA ABUBAKAR IMAM.

****

Haj murjanatu daya daga cikin manya manyan gidajenta ta zabama mujaheeda inda zata zauna tare da mijinta,bayan da mujaheeda ta tabbatar Mata da gidan yayi Mata ya dace da tsarinta.Duk da gidan lafiya lau yake baida wata matsala haka tasa akara gyara Shi tace tana

bukatar amaida Shi sabo.

Ta bangare daya Kuma tuni duk kayan dakin mujaheeda sun sauka daga Dubai Bana tsammanin hatta cokali an sayama mujaheeda daga Nigeria komai daga waje aka sayo.
Hatta kayan da zata sa na biki daga waje akayo order su.mujaheeda Kam ta samu dukkan gata don idan gata Yana yawa hakika yakamata yayima mujaheeda yawa.shirye shirya ake sosai na auren Shi Kansa gidansu gani kawai Alh Mustapha labaran yayi anata gyara babu KO Neman shawararsa hakan yasa shima baisa Kansa aciki ba,don yafi kowa sanin halin Matarsa na kushe da gwasala musamman idan batasa Ka acikin lamarinta ba.
Shi Kam Taufiq ya rasa abinda yasa ya Sami Kansa da rage zumudi da kaguwa akan auran Nasa KO don fitintunun da suke ta biyo baya ne oho,sai dai duk wani shiri shima ta bangarensa angama.
Taufiq yayi sallama ya shiga dakin mahaifiyarsa Haj saratu inda take zaune tare da babbar yarsa Haj Bilkisu ,Haj saratu ta dago cike da walwala ta dubeshi tace " yauwa Taufiq Ka karaso" ya lalubi kujera ya zauna Yana Dan murmushi yace " Eh umma " sannan ya dubi Haj Bilkisu yace " Ashe kina gidan" tace "eh Ka tasoni " yace " ni kuwa?" .
Haj saratu tace " Ka tasota mana,lefe ta kawo tace angama hada komai Kuma ya kamata akai tunda bikin nan Bai wuce Saura sati biyu ba" ya gyada Kai yace "to shine sai an kirani," ya dubi Haj Bilkisu yace "to Ai yaya keya kamata kisa Rana ki kwashi Wanda zaki kwasa kuje Ku Kai musu" Haj Bilkisu tace "to Amma dai ai a sanar da can gidan su mujaheedan cewa zaa kawo lefe" Taufiq yace " badamuwa idan kinsa lokaci sai ki gaya min ni kima Saina sanar dasu zaku zo".Haj saratu tace "eh hakan zaayi,ke kina ganin yaushe zaa Kai musu kayan" ta tambaya tana kallon Haj Bilkisu.

Haj Bilkisu ta jinjina Kai tace " Al umma ina ganin me zai hana akai musu gobe idan yaso sai Taufiq ya sanar dasu zamu zo gobe,tunda an Riga angama komai ai babu amfanin cigaba da ajiyarsu" Haj saratu ta juya ta dubi Taufiq tace"To kaji ?" .
Ya gyada Kai yace " eh, badamuwa Zan sanar dasu insha'Allah,goben sai akai kawai" " To Allah ya kaimu" cewar Haj saratu.
Haj Bilkisu ta gyara zamanta tana duban Taufiq tace " Al gaskiya kayi kokarin hada lefen nan ,don koina zaa Kai su to babu yadda zaayi a kushe kayi matukar kokari , Allah dai yasama auren albarka" gaba daya suka hada Baki da Amin.
Haj Bilkisu tace " To yanzu shikenan ba'anan gidan zaku zauna ba,agaskiya fitinar mahaifiyar mujaheeda yayi yawa,duk kyan da wajen can yayi sun raina " Taufiq ya cije baki alamar har yanzu ransa Bai masa dadi ba akan hukuncin Haj murjanatu.yace " babu yadda zanyi yaya tunda Abba ya Bani umarnin na amince,Amma insha'Allah sauri zanyi na kammal gidana mu koma can don Bana Jin Zan laminci wulakanci akan zamana agidanta,don matukar ina kaunar rayuwar yanci dole nabar musu gidansu," Haj Bilkisu tace " kwarai kuwa kayi tunani me kyau ai kawai kayi kokari Ka kammala gininka,don Bana Jin wannan matar zata sa maka Ido ba tare da tayi kokarin juyaka ba matukar kana Zama agidanta karshema gori ya biyo baya " Taufiq yace " Saima kinga irin katon gidan data bamu ,
Don mujaheeda ta kirani dole sai naje Naga gidan idan yayi min na gaya Mata Bassi nazo ba matukar yayi Mata shikenan,Amma yadda ta matsa yasa naje,gidan yayi girma da yawa Amma

tunda na fahimci yayi Mata Kuma saboda ita mahaifiyarta take son mu zauna agidan yasa nace yayi don Bana son ma wata doguwar magana".

Haj saratu ta saki tsaki ahankali tace "shikenan dai anyi Mata abinda take so,sam bana Jin wani kwanciyar hankali matukar ba auren nan Naga an daura ba,gaskiya Taufiq ina tausaya maka don banjin kayi dacen suruka sai dai babu yadda zaayi basa Bai tsallake kaddararsa "

Haj Bilkisu ta aje numfashi ahankali tace " umma sai dai addua tunda Shi Taufiq yaji ya gani Kuma Yana kaunar yarta hakanan zai cigaba da hakuri,Amma sangarta da ràshin tarbiyyar mujaheeda waye Bai sani ba,Shi Taufiq dinma AI yafi kowa sani ,kuma wace shawarace baa bashi ba Kan Kada ya Kai Kansa Amma soyayya ta makantar da Shi,AI aikin Gama ya Riga ya gama Allah dai yasa ayi a sa'a kawai".

Haj saratu ce ta amsa da da "Ameen" ,Shi kam Taufiq shuru kawai yayi ya maida Kansa kasa,duk abinda Haj Bilkisu ta fada hakane,sai dai Shi Kansa yanzu Yana Jin tamkar yayi kuskure wajen zabar abokiyar rayuwa.

A ranar Taufiq ya Kira mujaheeda ya sanar da ita batun kawo kayan lefen gobe, suna Gama wayar ta dubi Haj murjanatu da itama gama wayarta kenan da manajan daya daga cikin kamfanoninta.

" Mummy Taufiq yace Na sanar dake gobe zaa kawo lefena",

Haj murjanatu ta Tabe Baki tace " Allah ya kaimu, Allah yasa su kawo abin arziki" mujaheeda ta dubeta sosai tace "shima aiya sani,babu yadda za'ayi ya kawo min kayan lefe na banza don yafi kowa sanin banasa kayan banza" tayi murmushi sosai tace " yanzu kikayi magana kamar yata,haka nake so ki dinga daukar kanki yadda kike ,ki dinga gane matsayinki" mujaheeda tayi murmushi tace " mummy kenan ,nafasan abinda nake yi duk wani abu da zai kaskantar da darajata ke kinsan Bana so,kullum ina son Naga na wuce na tsara ,don haka Bana tsammanin Zan dankwafar da Kaina a'inda darajata zata Sami nakasu" Haj murjanatu ta dawo ta zauna kusa da mujaheeda ta janyota ta kwantar Kan jikinta cike da matsananciyar kauna.

Tace

" Mujaheeda duk duniya ban hada son ki da komai ba,shiyasa nake son Naga na share Miki duk wasu matsaloli da zasu kwanta ahanyar rayuwarki, musamman matsalar zaman aure,saboda idan mace batayi sa'ar gidan aure ba Ina tabbatar Miki ba zata taba jindadin rayuwa ba ,zata kasance tamkar wacce ta rako Mata duniya za Kuma ta rasa duk wani farinciki na rayuwa" ta Kara kwantar da kanta akan jikinta ta cigaba da cewa " Shi yasa kikaga ina tsauwalawa akan Taufiq saboda nasan babu yadda za'ayi ya iya da bukatunki Amma tunda zuciyarki tayi nisa akan sonsa yasa na amince ki aureshi Zan Kuma cigaba da wadataki da duk abinda kike so KO dashi ya gaza saboda na Sani na Kuma fahimci kina matukar sonsa don Shi kadaine mutumin da na tabbatar kina yi masa so na hakika Wanda zaki iya fsdawa wani mawuyacin Hali akansa Shi yasa nake ji Miki tsoron Kada wata Rana Taufiq yayi Miki halin su na Maza"

Mujaheeda tayi gaggawar tashi ta zauna tana kallon mahaifiyarta da wani irin Ido me cike da tsoro tace, " yanzu mummy kina tunanin akwai wata Rana da Taufiq zaiyi min halinsu na Maza,kina ganin wata rana Taufiq zai iya kallon wata mace yace Yana sonta?"

Haj murjanatu ta jinjina Kai tace " Abinda yafi komai sauki kenan wajen namiji"

Nan da nan idanun mujaheeda ya cika da hawaye tace " Amma mummy kinsan duk duniya babu abinda na tsana sama da kishiya Ko ,na rantse Dana zauna da kishiya gara n mutu.....
A gaggauce Haj murjanatu ta rufe bakinta jikinta na rawa tace " Kada ki Kara furta wannan mummunar Kalmar,ina tabbatar Miki da cewa matukar ina Raye babu ke babu Zama da kishiya Taufiq din banza ya isa ya Miki kishiya waye Shi AI ba irinku akema kishiya ba,ki kwantar da hankalinka, kada ki Kara ma wannan tunanin kinsan Bana son damuwarki"
Mujaheeda ta maida kanta ta kwantar Kan jikin mahaifiyarta tana maida numfashi ahankali, ayayinda Haj murjanatu ta cigaba da shafa bayanta tana kwantar Mata hankali da duk wasu maganganu da zasu kwantar Mata da hankali.ita kanta tasan kishin mujaheeda yayi yawa hakan Yana daya daga cikin dalilan da yasa take ganin Taufiq Bai dace da yarta ba don beyi kama da namijin da zaa yarda dashi ba Amma ya Zama dole yanzu tasan duk hanyar da zata bi wajen ganin ta cika duk wani burin murjanatu.
Ita Kam mujaheeda KO yaya maganar kishi ta ratso takan ji tamkar ranta zai fita ta rasa irin kishinta akan Taufiq Wanda bata iya boyewa,shin ta yayama mummy zatayi tunanin Taufiq zai iya Mata kishiya? Bayan ta gamsu da irin son da yake Mata ta Kuma tabbatar babu wata mace da zai so bayan ita.
**********"""""
Tun safe ake shirye shiryen zuwan masu kawo lefe.hadiman gidan ba Zama anyi girki Kala Kala na alfarma .
Haj murjanatu ta gayyato kawayenta su biyu Haj Nana da Haj Binta Mata masu ji da Kansu da kudi sai kanwar Alh Mustapha labaran Haj madina wacce ita kadai ta rage masa anan garin jigawan take aure.
Karfe daya da kwata Haj Bilkisu da kannanta biyu Harira da Haulat sai kanwar mahaifinsu Haj laraba suka isa gidan Alh Mustapha labaran.
Duk a falon kasa suka zauna bayan an cika gabansu da Kayan abinci sun Dan ci dai dai misali .
Sannan aka dawo Kan lefen akwati masu tsada seti daya masu guda shida KO wanne cike yake da Kaya .kawayen Haj murjanatu sune suka tashi suka Fara Bude kayan suna dagawa Suna Tabe baki,ganin hakan yasa Haj madina ta tashi itama tana duba kayan cike da fara'a tana yabawa tana fadin Kai Amma anyi kokari wai .
Zuwa lokacin Haj murjanatu ta gama zuwa wuya ta yima Haj madina wani irin kallo sannan tace " haba madina yaya sai wani koda Kaya kike Wanda ke kanki kinsan ba suyi ba" .
Haj Nana tace tana kallon kayan " to nima dai abinda na gani kenan duk kayan kanana ne ba masu tsada bane,nasan dai mujaheeda bata Saba sa irin wadannan kayan ba" .

Nan da nan Haj Bilkisu ta harzuka ta dubi Haulat ta dubi Haj laraba tace " Inna Ku tashi mu tafi kafin ayi batacciya don kinsan Bani da hakurin dazan juri Jin irin wadannan maganganun na wulakanci" Haj murjanatu tace " don Baki da hakuri sai akasa fadin gaskiya,Shi ai Taufiq din ya fi kowa sanin inda ya zo Neman auren ,yasan irin kayan da ya ta ke Sawa to don me zai kwaso wannan kayan akawo" a harzuke Haj Bilkisu tace " to Yan gidan Karuna masu karyar arziki ,idan bakwa so ai sai Ku fada mu kwashe kayanmu mu tafi,alabasshi sai ki saya Mata kayan da wani

Bai taba sa irinsa ba aduniya"

Haj laraba ta Mike ta dubi Haj Bilkisu tace " Kada ki sake magana idan kika Kara cewa uffan sai na bàta Miki Rai" ta dubi su Harira tace " Ku tashi mu tafi"

Haj madina tayi saurin tahowa kusa da Haj laraba tana bata hakuri " don Allah Haj kuyi hakuri Kada wannan ya kawo wata matsala don Allah kuyi hakuri".

Haj murjanatu ta saki tsaki tace " ke madina Bana son munafinci me akayi da har kike Basu hakuri ".

Haj Bilkisu ta saki tsaki ta wuce ta fice ayayinda su Haj laraba suka bita dukkan su cikin matsanancin bakinciki musamman yadda suka bsrsu suna jagwalgwala maganar gami da cigaba da kushe kayan lefen.

DAGA TASKAR YAR GIDAN IMAM 😍😍😍

********** **********

BABI NA BIYAR

NIMA MATARSA CE

NA

HÀBIBA ABUBAKAR IMAM

(YAR GIDAN IMAM)

FREE PAGE

PAID GROUP 300 KO KU TUNTUBENI TA WANNAN NUMBER TA WHATSAPP 08174970500,KO A TURO TA 2083086009 UBA BANK HABIBA ABUBAKAR IMAM.

****

Haj madina ta dubi Haj murjanatu cikin fuskar da babu yabo babu fallasa, tace " Gaskiya Haj abinda kukayi bai kamata ba wannan ba dai dai bane,ta yaya zaku kushe mutane agabansu, ina ma laifin Ku bari su tafi sai Ku Fadi duk abinda kuka ga damar fada, wannan gaskiya cin fuska ne, bayanni banga aibun wadannan kayan ba tsakani da Allah iya kokari sunyi".

Haj murjanatu tayi mata wani irin kallo sannan tace "Ai da yake duk kanwar ja ce shiyasa zakice bakiga aibun kayan ba, duk kanana ne babu wata babbar atamfa ko leshi ko shadda aciki, Kuma idan ban gaya musu agabansu cewa kayan ba suyi ba wa kike son na gaya ma,sun Dade basu ce anci musu mutunci ba"

Haj Nana ta kebe baki tace, " To ta yaya zaa yabi abinda Bai Kai ayaba ba, wannan Kaya dai an cika akwati ne Amma babu kayan arziki aciki, Kuma akalla ya kamata kasan inda kake neman aure, wannan kayan idan wani waje aka Kai godiya za'ayi tayi ana fadin bajintarsu saboda an kaisu inda ya dace dasu, Amma idan Ka Kai wani wajen na rantse da Allah tir za'ayi da Allah wadai saboda ka kaisu inda Bai dace dasu ba,don haka ni banga aibun fadin gsskiyar cewa basuyi ba".

Haj Binta ta gyara zamanta tana kallon kayan a wulakance tace " Kayafa ba suyi ba, don Allah dubi wancan leshin na rantse Shi na Saima Mai aikina shekaranjiya dubu goma sha biyar don kuma wulakanci ace irinsa za'asa a lefan mujaheeda...."

Wane leshin ne kika Saima me aikinki,? Cewar mujaheeda wacce dawowarta kenan gidan

tana rike da jakunkunan sayayyar da tayi na tarkacen kayan ciye ciye.Haj madina ta juya ta gyara zaman hijabinta ajikinta tace Allah ya bamu alheri.haj murjanatu ta zuba mata harara tace " Amin sauka lafiya" kafin ma ta Karasa magana har takai bakin kofa.

Haj murjanatu ta tashi ta ruko hannun mujaheeda wacce take aikin kallon akwatina da Kayan dake ciki, tace " Kada wani abu yadameki, kayan lefe na banza Taufiq yayi Miki Amma Kada ki damu kema kinsan Kona arziki ya kawo ba zaki sa ba don kayanki da zakisa da bikinki sun riga sun kammala", mujaheeda ta zauna asanyaye ayayinda Haj Binta tace " Allah ya riga ya rufa Miki asiri ba don haka ba da bakinciki ya kasheki don babu abu mafi zafi daya wuce ace anyima budurwa banzan lefe,

Don babu dadi Amma ta yaya yasan gidan da kika fito amma zai kawo Miki irin wannan lefen".

Mujaheeda dai tayi shuru tana Jin maganganun da suke yi itama Haj Nana tana Kara fadan nata hasashen

Tsam mujaheeda ta tashi ranta abace ta haye sama ba tare data duba kayan ba ko ta tamkama duk maganganun da suke yi ba.

Ganin hakan yasa su Haj Binta sukayi sallama da Haj murjanatu suka tafi. Ayayinda Haj murjanatu ta Kira hadiman gidan ta basu umarnin su kwashe kayan su Kai dakin baki su aje acan.

Sannan ta tashi tabi bayan yarta .

Kwance ta sameta asaman gado ta zubama saman dakin Ido, ta Sami kusa da ita ta zauna gami da Kiran sunanta ,ta juyo ta dubeta sosai fuska ba walwala sannan ta Watso Mata tambayar " mummy me yasa kike son ki dinga muzanta Taufiq".

Tambayar tazo Mata a shammace ,ta dubeta sosai tace " KO kadan bani da tunanin muzanta Taufiq, illa ke da nake kokarin Karema mutunci", ta tashi ta zauna sosai tana kallonta tace " kare mutuncina mummy Yana nufin ki sama min mutunci awajen Taufiq ne.amma abinda kike aikatawa baiyi Kama da kare min mutunci ba,ina yarda da abubuwan da kike yine saboda ina tunanin kamar Donni kike yi don Samun fsrincikina,to Amma yanzu wannan abinda kikayi na hanyar muzanta Taufiq gaban kawayenki Yana min nuni da cewa martabarki da girmanki kawai kike son karewa"

Haj murjanatu tayi saurin girgiza Kai tace " Aah mujaheeda saboda ke nakeyi" ta girgiza Kai tace " idan Donni kike yi saiki mutunta kayan lefena gaban kawayenki ki yabesu Wanda KO da ga baya kinzo kin Fadi aibunsa agabana bazan damu ba ,kamar yadda baxanga laifinki ba, Amma baa gabansu ki biyesu kuna aibata kayan ba harda cewa me aikinta ta sayama irin leshin cikin lefena, shin mummy da Taufiq zaiji ko zaiga abinda abinda kukayi akan lefensa kina tsammanin yaya zaiji?".

Haj murjanatu ta jinjina Kai tace " ban dauka hakan zai bata ranki ba Amma bazan Kara yin maganar lefen ba,ba Kuma Zan fito dasu kowa ya gani ba"

Ta dubeta sosai tace " bazaki bari kowa ya gani ba saboda kina Jin kunyar nuna kayan amatsayin lefen yarki Ko mene?"

Haj murjanatu ta dan hadiye yawu sannan tace " eh kusan haka ne" .A hankali mujaheeda ta koma ta kwanta gami da juyama Haj murjanatu baya ranta na cigaba da kuna hakan yasa duk bayanan da Haj murjanatu ta cigaba dayi Mata bayanin dalilinta nayin abinda tayi Ko zata

fahimta Amma tunda ta kwanta ta juya baya bata Kara ko da kwakkwaran motsi ba balle tasa ran zata tanka Mata harta gaji da magana ta tashi ta fice.

****

Iya harzuka Haj Bilkisu ta harzuka don harta Gama labartama mahaifiyarsa da Taufiq labarin abinda ya faru zuciyarta bata lafa daga haushi da Jin zafin maganganun dasu Haj murjanatu suka yi musu ba

Haj laraba tace " shifa aure ya gaji haka gutsiri tsomarsa yayi yawa babu wani aure da zaayi Shi Salin slin ace babu wata matsala da aka samu,saboda haka hakuri shine Kan gaba wannan ba wani abu bane " Haulat

Ta girgiza Kai tace " gaskiya goggo wannan wani abu ne don gaba daya yaya baiyi sa'ar suruka ba Ai ana barin halal don kunya meyasa ba zatayi hakurin mu tafi ba kafin suyi wulakancin da suka yi niyya ammafa agabanmu suke kushe kayan da muka Kai duk irin kokarin da yaya yayi basu gani ba "

Taufiq yayi kasa da Kansa zuciyarsa na tafasa ya kasa cewa uffan.haj saratu ta numfasa tace " To ni dai bansan me Haj murjanatu take son ayi Mata ba ,duk abinda tace ana kokarin yi duk dai don asami zaman lafiya Amma na rasa dalilin da yasa kullum take kokarin bata al'amarin nan, abin ya Fara damuna kwarai da gaske ,don ina ganin ko Anyi auran nan tamkar ba zaa samu wani kwanciyar hankali ba".

Haj Bilkisu tace cikin fusata " na rasa gane me take so Kuma me take nufi, Ko itace Yar Karuna iya karyar arzikin da zata dinga yi kenan, shin su kadaine masu kudi Kuma mu din bamu da rufin asiri ne meye abin kushe agaremu ,me yasa take jindadin wulakantamu?"

Haj laraba tace don Allah don son Annabi abar maganar nan kadama akara yinta.

A sukwane Taufiq ya tashi ya fita batare da yace komai ba Haj laraba ta bishi da cewa " Adaiyi hakuri Taufiq babu komai rayuwarma guda nawa take".

Haj Bilkisu ta juya ta cigaba da maganganun ta na bacin rai ayayinda Haj laraba ta cigaba da tausa su .azahiri Haj saratu abin ya Fara fita kanta ta gaji da wadannan kananan maganganun ,kamar yadda ta kasa gane ina matsalar take? Me Haj murjanatu take nufi? Meye tunaninta akan danta Taufiq?.irin tambayoyin da Haj saratu take ta yima kanta kenan.

Taufiq na zaune asaman kujerar fslonsa ya harde hannayensa a gaban kirjinsa Yana Kada kafafuwa Kaida kallon fuskarsa kasan Yana cikin damuwa.ya tashi ya shiga sintiri a tsakiyar falonsa.

Yana tunanin halinda yake ciki agame da lamarin mujaheeda.ya daga Kai ya na Karema falon kallo, ahankali ya tambayi Kansa shin meye aibun wannan wajen da mujaheeda ba zata iya Zama aciki ba?, Me yasa Haj murjanatu take kokarin daukarsa a sakarai ? Wane irin nakasu gareshi da suke kokarin kaskantar dashi shin ahaka zai auri mujaheeda idan ya aureta wace irin rayuwa zaiyi da ita.

Shin mujaheeda ta dace dashi kuwa? A hankali ya Sami Kansa da ba Kansa amsa da cewa mujaheeda bata dace dashi ba.

Rayuwar su ba zata taba Zama dai dai ba da muguwar rawa gwamma kin tashi baya Jin zai

iya auran mujaheeda bayan duk wadannan abubuwan dake fsruwa.
Me zai hana bazai rabu da ita ba ya Sami dai dai dashi.
Ya koma ya zauna Yana kokarin sama Kansa natsuwa da dangana akan mujaheeda. Ahankali ya Ciro wayarsa daga aljihunsa ya Danna ya Kira mujaheeda bugu daya acikin na biyu ta dauka.
" Taufiq" Bai amsa ba yace cikin dakakkiyar murya " na kiraki nayi miki godiyar cin mutuncin da mahaifiyarki tayima yan' uwana " mujaheeda ta yi saurin cewa " don Allah kayi hakuri nima banjidadi ba Kuma bana gidan hakan ya faru don Allah kayi hakuri"
Ya girgiza Kai yace " ba lefinki bane don haka basai kin Bani hakuri ba,tunda lamarin nan ya Zama haka ina ganin muyi hakuri kawai da juna Allah ya hada kowa da rabon sa don Bana Jin Zan cigaba da jure irin wannan bakin wulakancin daga mahaifiyarki,Wanda ke kanki da da gaske kina min son da kike ikirarin kina yimin da baki bari hakan na fsruwa ba Amma tunda haka kika zaba na hakura abar maganar aure.....?
Adaburce mujaheeda ta Mike duk ta gigice tace " Abin bai Kai haka ba don Allah Ka daina wannan maganar ta yaya zakace Ka fasa don Allah kayi hakuri "
Ya girgiza Kai yace " kiyi hakuri Amma ina son ki sanar da mahaifiyarki na hakura da auran yarta ta je ta aura Miki Wanda take so Wanda zata samu natsuwa dashi, ni na hakura "
Yana Gama fadin haka ya kashe wayarsa.lokaci daya mujaheeda ta kwala ihu Wanda ya dawo da hankalin Haj murjanatu kanta da take zaune afalo da saurin gaske ta tashi ta taho dakin .
Shigowarta yayi dai dai da lokacin da mujaheeda ta sulale kasa ta Fadi sumammiya tana dafe da gefen kirjinta idanun Haj murjanatu suka firfito nan da nan ta fita hayyacinta Tayo Kan yarta tana adduar Allah yasa ba ciwon zuciyarta bane ya tashi .
DAGA TASKAR YAR GIDAN IMAM

NIMA MATARSA CE
NA
HÀBIBA ABUBAKAR IMAM
BABI NA SHIDA
****

Cikin matsananciyar damuwa Haj murjanatu ta cigaba da girgiza mujaheeda tana Kiran sunanta,cikin firgitacciyar murya.
Lami ta fado dakin da sauri itama ganin abinda yake faruwa yasa ta tsuguna agaban mujaheeda itama tana Kiran sunanta ,cikin Jan Ido Haj murjanatu ta dubi lami ta bata umarnin tayi saurin taje ta sanar da direba ya fito da mota.
Fitarta yayi dai dai da lokacin da Haj murjanatu ta Mike ta tattagi mujaheeda tana nishi tayo waje da ita sauran hadiman gidan suna ganin ta Suma cike da tashin hankali suka Sanya hannu suka tayata karasawa da mujaheeda wajen mota.nan da nan aka sanyata a mota kowa cikin tashin hankali domin sun san irin wahalar da mujaheeda take sha matukar ciwon zuciyarta ya tashi.

Haj murjanatu ta kusa tafiya asibitin babu gyale sai da lami ta tuna Mata sannan ta tsaya har lamin ta kawo mata gyalen sannan direba yaja motar a sukwane zuwa care hospital, babban

asibitin kudin da mujaheeda take ganin likita a garin jigawa.

Tun kafin su isa asibitin Haj murjanatu ta Kira Dr Balarabe tasanar dashi suna hanya dafatan Yana asibitin domin ciwon mujaheeda ya tashi. Ya tabbatar Mata da cewa yanzu yake Shirin tashi Amma dole zai tsaya ya Jira zuwansu.

Isarsu asibitin babu bata lokaci aka ba mujaheeda gado sannan Dr Balarabe ya Fara bata taimakon gaggawa.

Ayayinda Haj murjanatu ta koma waje ta Sami kujera ta zauna,hawaye ta samu kanta da fitarwa kwarai matuka tana matukar Jin tausayin yarta agame da lalurarta Wanda hakan Yana daya daga cikin dalilan da suka sa take tsaye da Sanya farinciki azuciyar mujaheeda bata kaunar duk wani dalili dazaisa mujaheeda damuwa,

Hakan yasa tasha alwashin jiyar da ita dadi da gatan da zaisa natsuwa da kwanciyar hankali a rayuwarsa.

Hakanan ta Sami kanta da addu'ar Allah yasa ba dalilin abinda yafaru akan Kayan lefen ta bane,Wanda tasan laifinta ne.

Ahankali ta Ciro wayarta daga cikin Jakarta, ta danna ta Kira Alh Mustapha bugu daya ya dauka Jin muryarta cikin damuwa yasa ya Fara tambayarta abinda ya faru , ahankali ta sanar da Shi suna asibiti da mujaheeda ciwonta ya tashi.

Cikin damuwa shima ya kashe wayar ya aje komai ya baro kamfanin ya taho asibiti.

Harya karaso asibitin mujaheeda tana nan inda take har zuwa lokacin bata farfado ba.dr Balarabe da wasu likitoci guda biyu sune akanta.zuwa lokacin kuwa Haj murjanatu taci kuka har taba uku lada, idanunta sunyi jawur.

.Alh Mustapha labaran ya zauna kusa da Haj murjanatu Yana dubanta, sannan yace " meya faru da mujaheeda wani abin ya bata Mata rai ne ,,ko kuwa dai hakanan ciwon ya tashi, abinda ya dade bai tashi ba"

Tadan yi jim gami da muskutawa sannan tace " Babu abinda ya faru , hakanan naji ihunta ko kafin na shiga harta sume" ta Karasa magana tana kokarin goge hawayen da suka Fara fitowa daga idanunta.

Alh Mustapha labaran ya girgiza Kai yace " Allah ya bata lafiya " asanyaye ta amsa " Amin ya Allah".

Sai bayan issha' I sannan Allah ya nufa mujaheeda ta farfado ,idonta nakan mahaifiyarta wacce take ta murnar ganin ta dawo hayyacinta, ta dauke idonta akanta tana runtse idanunta ,kalaman Taufiq sune suke yawo a kwakwalwarta .

Hakan yasa idanunta suka cika da hawaye .Alh Mustapha labaran ya Lura kwarai da hawayen dake fitama mujaheeda, ahankali ya nemi bakin gadon ya zauna Yana kallonta gami da Kiran sunanta, bata amsa ba sai hawaye da ya cigaba da wanke fuskarta.

Yadan Matso kadan kusa da ita Yana cigaba da kallonta sannan yace " mujaheeda menene? Jikin ne? Ko wani abun Yana damunki ne ?".

Haj murjanatu ta taso " me zai dameta daya wuce ciwo" ya waiwayo ya dubeta yace ' kila bakiga damuwar da ke cikin kwayar idonta bane ,ko Kuma kingani kin zabi ki kauda Kai akan damuwarta ta " ta dubeshi sosai tace " Akan me Zan juyama damuwarta baya ,bayan duk

duniya bani da wata damuwa da ya wuce damuwarta "
Asanyaye cikin galabaitacciyar murya mujaheeda tace " idan har damuwa damuwarki ce , da baki zama sanadiyyar damuwar tawa ba".
A gaggauce Haj murjanatu tace " nice sanadin damuwarki mujaheeda?" Ta Karasa magana idanunta na kafe akanta.
Ta jinjina Kai alamar hakane. Hakan yasa Alh Mustapha labaran ya dubi mujaheeda cikin kulawa yace " ki kwantar da hankalinki ki gaya min abinda ya faru "
Cikin kuka sosai mujaheeda ta sanar da Shi duk abinda yafaru da Kuma hukuncin da Taufiq ya dauka akan hakan.ta karasa magana cikin kuka tana cewa " Kin fi kowa sanin irin son da nakema Taufiq Amma kin kasa dannems zuciyarki tsanar sa balle har ki tayani sonsa, shin meye illar Taufiq me yasa kike raina arzikinsa kike ganin tamkar bai dace dani ba , bayan NI kadai nasan irin dacen da nayi da samunsa,meye na dole sai kin muzanta Shi .
To abinda baki sani ba shine Taufiq zai iya jure ki wukakanta Shi ki ci masa mutunci kiyi . masa komai amma bazai taba jurar ki wulakanta masa yan'uwa ko iyaye ba, yasha gaya min matukar abinda kike masa ya wuce Kansa ya fada Kan iyayensa Ko yan' uwansa to zai iya hakura dani har abada"
Ta Kara tsare mahaifiyarta da Ido sannan ta cigaba da cewa " Dalilin da yasa kenan dana dawo na tadda abinda kikayi akan lefen hsnkalina ya tashi saboda bansan irin abinda kika gaya masu ba, har sai da Taufiq ya kirani ya Kuma tabbatar min da wulakancin da kikayi ya Kuma gaya min ya hakura na gaya Miki kije ki aura min Wanda kike so Wanda zaki fi samun natsuwa dashi.bsyan kinsan duk duniya bani da wata natsuwa sai da Taufiq, bani Kuma da Wanda nake so nake Samun farinciki agunsa sai Shi .Na rantse idan ba Taufiq ba babu wani da namiji dazan iya aure sai dai na zauna babu aure har na koma ga Allah ".

Haj murjanatu ta kasa magana kanta na kasa har zuwa lokacin da Alh Mustapha labaran ya tashi ya dawo kusa da Haj murjanatu ya tsaya Yana kallonta , ta dago ta dube Shi tace fuska atamke " Menene Ka tsare ni da Ido, don kawai an kawo kayan lefe na ce basuyi ba shine zai bullo da wannan maganganun na banza dama Yana neman na tafiya ne ,Kuma bai Isa ba ba' a haife Shi ba aurenki dashi ya Zama dole "
Alh Mustapha labaran yace " Auransu ya Zama dole amatsayin ki na wacce zata ce dole ayi ko me? Taufiq shine yake da ikon dazai auri mujaheeda shine Kuma yake da ikon da zaice bazai aureta ba , saboda haka wannan izzar da kikeyi babu inda zata kaiki awannan Karon ya Zama dole ki sakko kije ki gyara abinda kika bata matukar kina son kwanciyar hankalin yarki,"
Ta harzuko " To me zanyi ?" Ya gyara tsaiwarsa sannan yace " Ki nemi Taufiq ki bashi hakuri, sannan ki fita acikin salon zubar da kima da kika shiga ki rungumi abinda Allah ya kaddaro acikin rayuwar yarki kija girma da mutuncinki tun kafin ki rasa su awajen Taufiq, ki sani ke surukace wacce kike dai dai da matsayin Uwa awajen Taufiq,duk wadannan abubuwan da kikeyi ba zasu haifar Miki da da me Ido ba.
Ya kamata ki dawo cikin Tunaninki zuwa yanzu dai ko ba abinda kika karama Taufiq na muzantawa to ya sani wasuma sun sani cewar bai Miki ba , Baki sonsa zaki aura masa yarki don dole ne don tana sonsa Kuma lsifinsa daya ne don kina ganin ajinsa bai Kai ajin mujaheeda ba".

Haj murjanatu tayi shuru nadan wani lokaci sannan tace " Nice Zan nemeshi na bashi hakuri" ya jinjina Kai yace " kwarai da gaske ammafa matukar kina son mujaheeda ta tashi daka Kan gadon asibitin nan ,ta Kuma Sami lafiya da Kuma mallakar abinda take so".

Haj murjanatu ta girgiza Kai tace " Gaskiya bazan iya zuwa naba Taufiq hakuri ba, ai Bama zai yuwu ba ",

Mujaheeda ta runtse idanunta zuciyarta na wani irin tukukin ciwo lokaci daya maganganun Haj murjanatu sukasa ta Kara birkicewa nan da nan idanunta suka Fara kafewa numfashi ya Fara Mata wahalar fita , gaba daya sukayo kanta daga bisani Àlh Mustapha labaran ya fice yaje ya Kira likita .

Tambayar farko da likita ya Fara yi itace " Meya faru wani ya bata Mata raine" babu Wanda ya bada amsa acikinsu har likita ya Gama dubata yayi Mata allura wacce cikin kankanin lokaci bacci ya kwasheta.

Likita ya dubi Àlh Mustapha labaran da Haj murjanatu yace " Gaskiya dole fa Ku dinga kulawa Kan abubuwan da zasu dinga sa ta adamuwa saboda damuwa itace babbar hanyar tashin ciwonta ,Kuma ahalin yanzu ba' a bukatar yawaita tashin ciwon saboda hakan zai. Iya kaimu da dole sai anyi Mata aiki a zuciya , saboda haka don Allah a Kula "

Babu Wanda ya iya magana har ya Gama maganganunsa ya fice .

Sannan Àlh Mustapha labaran ya dubeta yace " Har yanzu kina nan akan bakanki na cewa ba zaki ba Taufiq hakuri ba ya janye maganarsa ko kuwa?".

Tayi Jim duk wata damuwa ta gama mamaye ta komai ya tsaya Mata , shin me zai faru da izza da isarts matukar tabs Taufiq hakuri? Yaron da bai Isa ba ba' wani ba ba dan wani ba Shi zata je taba hakuri don kawai ya auri yarta.

Ta dago Kai ta dubi mujaheeda da tayi nisa cikin bacci ta dubi irin ramewar da tayi farat daya kamar ta shekara tana jinya. sannan ta dawo da idonta kasan dakin ta rasa abinda ke Mata dadi . Wannan wace irin masifa ce ? , Karo na farko kenan da taji ta Kara tsanar Taufiq tsana me yawa, domin ayau ta hango abinda bata tabs hangowa ba , na cewa tabbatar Taufiq zai iya rabata da yarta matukar ta cigaba da yi masa irin wannan son da take masa.

" Ke nake Jira inji abinda kika yanke" cewar Alh Mustapha labaran, ta waiwayo a hankali ta dubeshi tace " Kai ba zaka iya zuwa Ka Sami mahaifinsa kuyi magana ba ka bssu hakurin?" Ya dubeta sosai ysce " Kin taba ganin Wanda yayi laifi daban Wanda zai bada hakuri da ban , ta yaya zanje na basu hakuri bayan bani nayi laifi ba" .

Ya karasa magana Yana kauda Kai gefe saboda Shi Kansa yau Yana son ganin karshen izzar Haj murjanatu Yana son taji abinda ake ji idan Ka muzanta agaban wani.

Ta aje numfashi ahankali sannan tace " Naji Zan kirashi awaya nasanar masa halinda mujaheeda take ciki ,nasan duk fushin da yayi idan yaji tana kwance a gadon asibiti zai taho ya dubeta don shima yasan lalurarta, saboda haka idan yazo sai muyi maganar"

Àlh Mustapha labaran ba haka yaso ba Amma baya son ta gane cewar shima Yana da ra'ayi acikin maganar hakan yasa baija ba yace " shikenan idan kina ganin hakan ne yakamata "

Batace komai ba ya dubi agogon dake daure a tsintsiyar hsnnunsa karfe goma sha daya na

dare ya dawo da kallonsa gunta yace " kina bukatar wani abu ne , don ina Jin Zan tafi gida dare yayi,"
Ta gyada Kai tace " komai akwai vabu wata bukata kana iya tafiya " ya matsa kusa da mujaheeda ya yi Mata addua ya tofa Mata a fuska sannan ya juya yayi sallama da matarsa ya tafi.

Saida ya natsu acikin mota kafin ya tada motar ya fito da wayarsa ya danna ya Kira Taufiq bugu biyu acikin na uku ya dauka cike da girmamawa ya gaishe shi , tun rana yakesa ran Samun Kiran Àlh Mustapha labaran Amma shurun da yaji shiya tabbatar masa da cewa mujaheeda bata sanar da kowa abinda ya faru tsakaninsu ba.
Alh Mustapha labaran yace " Taufiq yakamata ace zuwa yanzu kasaba da halin Haj be kamata Ka dinga juyawa kana kallon abinda take yi ba shekara hudu kayi kana neman auren mujaheeda babu abinda batayi ba yadda Ka jure Ka yi hakuri haka nake son Ka cigaba da hakuri , domin dai akwai tarin kalubale acikin wannan tafiyar dole saika jure, don haka maganar Ka fasa aure Ka ajiyeta a gefe domin adalilin maganar da Ka fadama mujaheeda yanzu haka tana kwance a asibiti ciwonta ya tashi babu yadda take ".
Gaban Taufiq yayi mummunar faduwa yayi saurin mikewa tsaye yace " ciwonta ya tashi " Àlh Mustapha labaran yace " Kwarai da gaske kaima Kuma kasan hakan zai iya faruwa ,tunda kafi kowa sanin duk irin halin ko' in Kulan da mujaheeda take nuna maka tofa kasani tana sonka so me tsanani wannan halin datake nunawa cikin irin halayenta ne da babu Wanda zai iya canjata Mata.
Amma ina son kasani mujaheeda tana matukar sonka sannu ahankali wata rana kana iya maida ita yadda kake so, wannan sangartar da shagwaba da raguwar tarbiyyar data ke dashi duk zaka iya canjata," Taufiq ya numfasa yace " nima bacin rai yasa nace na fasa domin har yanzu ban sanar da mahaifana cewa ga abinda na yanke ba saboda nasan KO kowa ya yarda Abba bazai yarda ba,"
" Nima nasan Alh Yusuf lamido bazai amince ba shiyasa ban damu ba " Taufiq yace " sha biyu saura ne yanzu na dare yanzu Zan je asibitin na dubata "
Alh Mustapha labaran yayi saurin girgiza Kai yace" Aah kada kaje " a hankali yace " me yasa Alh " a hankali Alh Mustapha labaran ya Gama gaya masa komai ba maganar hakuri da yake son Haj murjanatu ta bashi KO ta dawo hayyacinta da Kuma abinda ta fada ya Kara da cewa " ina son ta zo har gida ta baku hakuri hakan zai karya lagwanta zaa Sami sauki ko yayane saboda haka Kota kiraka Kada Ka sake Ka dauka Ko number ta canja idan kaji muryar ta to Ka kashe wayar hakan zaisa ta yarda tazo har gida ta bada hakuri , kayi hakuri da zuwa asibitin har sai ta zo gida ta bada hakuri ".
Taufiq yayi Dan murmushi tikisa Haj murjanatu da bashi hakuri lalle Shi Kansa zaiso ganin hakan " Ka fahimceni" cewar Alh Mustapha labaran Taufiq ya amsa da sauri " Na fahimceka shikenan hakan za'ayi Amma don Allah Ka dinga sanar dani halinda mujaheeda take ciki a asibitin saboda na Sami natsuwa" yayi murmushi yace " Kada kadamu ",
Daganan suka yi sallama cike da mutuntawa da girmamawa.

Alh Mustapha labaran yaja motarsa zuwa gida zuciyarsa cike da tunanin irin wannan badakalar dake fsruwa sai kace akan Haj murjanatu aka fara neman aure ya rasa irin

tunaninta. Shi Kansa ya kosa ayi ayi auran nan ko hankalin kowa ya kwanta. Sai dai abinda bai sani ba shine yin auran nema zai Zama sanadiyyar ràshin kwanciyar hankalin.

DAGA TASKAR YAR GIDAN IMAM.

NIMA MATARSA CE
NA
HÀBIBA ABUBAKAR IMAM
BABI NA BAKWAI
****

Washegari jikin mujaheeda yayi sauki sosai, sai dai kallo daya zaka Mata Ka tabbatar da tana cikin matsananciyar damuwa. Haj murjanatu kuwa sam bata jindadin irin kallon da mujaheeda take yi mata mai cike da tuhuma da dora laifi.

Ta tashi daga inda take zaune ta dawo kusa da mujaheeda ta zauna tana kallon ta cike da kulawa, ta Kara Ciro wayarta ta Kira Taufiq karo na kusan goma sha daya kenan data kirashi tun daga wayewar gari amma babu kiranta daya Wanda ya daga.

Ta Kara kallonta tace " Na Kira Taufiq sama da sau goma amma yaki daga wayata"

Mujaheeda ta waiwayo ta dubeta sosai tace " me zaiyi Miki kike kiransa" ta dan hadiye yawu sannan tace " Zan bashi hakuri ne " a gaggauce ta Kara kallonta ta maimaita maganar " zaki bashi hakuri?" Ta gyada Kai tace " kwarai da gaske matukar yin hakan zaisa ki Sami natsuwa da kwanciyar hankali to Zan bashi hakuri, Amma Kiri Kiri yaki daga wayata saboda dole sai nuna bani da kima ko daraja agunsa"

Dai dai lokacin Àlh Mustapha labaran ya shigo cike da jindadin yadda yaga mujaheeda ta sami sauki kai tsaye ya wuce bakin gadon Yana kallonta " mujaheeda yaya kike Jin jikin naki" ta gyara kwanciyar ta ahankali tace " Naji sauki daddy".

Yace " Alhamdulillah Allah ya Kara lafiya, Kuma ina son ki daina sama kanki damuwa wacce kinsan damuwar ba zata gagara na warware Miki ita ba , saboda Auranki da Taufiq insha'Allah babu abinda zai hana Shi kasancewa "

Cike da shagwaba tace " Naji daddy Amma fa har yanzu bai kirani ba"

Ya girgiza Kai yace " Kada ki damu bai kiraki bane saboda bai San kina asibiti ba"

" Ta yaya zaisan tana asibiti bayan yaki daga Kirana babu irin Kiran da banyi masa ba Amma yaki dagawa ".

Gànin idanun mujaheeda sunyi rau rau alamun son tayi kuka yasa Àlh Mustapha labaran ya dubi Haj murjanatu yace " Haj zo" ya Fadi maganar Yana fita daga cikin dakin ayayinda Haj murjanatu ta bishi abaya.

Daya daga cikin kujerun dake girke a waje Haj murjanatu ta zauna ayayinda Àlh Mustapha labaran ya cigaba da tsayuwa Yana kallonta sannan yace" Ràshin daga wayarsa ba wata damuwa bace tunda kina da damar da zaki iya zuwa har gidansu Taufiq ki basu hakuri" da sauri ta juyo tana kallonsa tace " gidansu Taufiq na basu hakuri?" Ya gyara tsaiwarsa yace" eh babu wani abu ni Zan iya daukarki muje ki basu hakuri komai ya wuce, bana Jin Kuma zai Zama

matsala kema agareki idan akayi laakari da kema kina bukatar kwanciyar hankalin mujaheeda kina son kiga ta bar kan gadon asibiti ba tare da damuwar komai ba"

Haj murjanatu ta yi ajiyar zuciya tana jinjina abinda Alh Mustapha labaran yake son ta aikata , sannan tayi masa kuri da Ido,
Tace " idan na aikata abinda kace shin yaya girmama Kaina zai kasance ? Yaya makomar martabata da kimata? Shin yin hakan daga min daraja zaiyi Ko durkushe darajata zaiyi?.

Ya girgiza Kai yace" Babu abinda zai samesu domin kin yi abinda ya dace kiyi ne Bana Jin zai Zama matsala Ko ga tsakaninki da Taufiq illama ya sassauta al'amarin zaki Kuma Sami wata martaba wacce Baki samu ba da agidansu Taufiq,
Ina tabbatar Miki wannan abinda zaki aikata zai Zama sanadiyyar gyaruwar abubuwa da dama ".
Shuru tayi tana cigaba da tunanin maganarsa , ayayinda ya cigaba da cewa " haka zalika mujaheeda zata jidadin faruwar hakan matuka, akalla Kuma nasan zaayi auren nan cikin kwanciyar hankali ".
Asanyaye cikin ràshin zabi ta gyada kanta tace " shikenan babu damuwa".

Yadanyi murmushi kadan yace " to shikenan, mujaheeda taji sauki saboda haka idan an sallameta saimu tafi gidansu Taufiq din" Kai kawai ta gyada

Daga bisani ta tashi ta koma cikin dakin ayayinda da Àlh Mustapha labaran ya fice zuwa harabar asibitin ya Kira Taufiq ya sanar dashi duk yadda sukayi da Haj murjanatu ya Kuma tabbatar masa da cewa mujaheeda taji sauki sosai, hakan ba karamin sanyaya ran Taufiq yayi ba saboda tun jiya daya ji labarin ciwon nata bai kara samin nutsuwa ba gani yake tamkar komai laifinsa ne.

Adaran ranar aka sallami mujaheeda bayan samun saukinta.
Àlh Mustapha labaran da Kansa ya Kira Alh Yusuf lamido ya sanar dashi suna nan zuwa shida Haj murjanatu Alh Yusuf lamido yaso Jin dalilin zuwan nasu amma Àlh Mustapha ya sanar dashi yayi hakuri har sai sun zo.
Azahiri Haj murjanatu ji take kamar zaa rabata da wani bangare na jikinta ko kadan bata kaunar zuwa gidansu Taufiq amma babu yadda ta iya idan har tana son ta dawo dai dai da yarta dole tayi hakan ,
Amma can cikin karkashin zuciyarta sosai take Jin ta Kara tsanar Taufiq.
Washegari Àlh Mustapha labaran da Kansa ya tuka Haj murjanatu zuwa gidan Àlh Yusuf lamido zuciyarta cike da bakincikin abinda take Shirin aikatawa mutanen da take ganin su abanza wai sune zata je ta rokesu don kawai dansu ya auri yarta gidan yaron mijinta zata je ta bada hakuri duk isarta da izzarta.
Sun Sami kyakkyawan tarba agidan su Taufiq a falon Àlh Yusuf lamido aka saukesu hade da duk Kan wani kayan ciye ciye Amma babu abu daya da Haj murjanatu ta taba , zuciyarta na cike da alhinin abinda zata aikata Wanda dai dai yake da barin mutuncinta.
Haj saratu babu wani cikakken kwanciyar hankali atare da ita kaancewar bata San abinda ya

kawosu gidan ba.

Kujerar kusa da Haj murjanatu ta samu ta zauna tana adduar Allah yasa lafiya.bata dade da Zama ba Taufiq yayi sallama ya shigo Kai tsaye kasan kafet din ya samu ya zauna.

A kaiksice Haj murjanatu ta watsa masa harara haushinsa take ji sosai aranta.

Cikin girmamawa ya gaishesu bayan sun amsa ne .

Alh Mustapha ya gyara zamansa yace " Abubuwa sun faru marasa dadi musamman Kan lefen da aka kawo , Wanda abinda ya biyo bayan kawo lefen yayi sanadiyyar da Taufiq ya tabbatar ma da mujaheeda cewar ya fasa auren ta hakan yayi sanadiyyar tashin ciwon mujaheeda harda kwanciya a asibiti jiya aka sallamota"

Haj saratu da Alh Yusuf lamido suka saki salati, Alh Yusuf lamido yace cikin ràshin jindadin abinda yafaru yace " subhanallah,yaya jikin nata yanzu" ,Alh Mustapha labaran yace " aah ta Sami sauki Alhamdulillah, dalilin da yasa kenan Muka taho saboda Haj tana da abinda take son ta fada muku".

Nan da nan Haj murjanatu taji tamkar an dora Mata dala da gwauron dutse aka musamman yadda taga duk sun zubo Mata idanu, daker bakinta ya iya budewa tace " maganar fasa aure bayan saura Bai wuce mako daya da wani abu ba bai taso ba, dalilin da yasa kenan nace Zan zo na ba da hakuri,"

Cikin matukar mamaki Haj saratu da Alh Yusuf lamido da Taufiq suka shiga kallon kallo na mamaki, ta cigaba da cewa " saboda haka Taufiq kayi hakuri Ka janye wannan maganar ,Kuma ina son Ka sani duk abinda nayi yanzu saboda yata nayi saboda ina bukatar Samun natsuwarta, tunda Allah ya jarafceta da sonka ya Zama dole nayi hakuri na rungumi hakan amatsayin kaddarar rayuwa ta".

Alh Yusuf lamido ya gyara zaman gilashinsa a Ido sannan yace "haba Haj don wannan har sai kin zo kin bada hakuri bayan irin wautar da Taufiq yayi da gsnganci ai wannan auren idan kinga bai tabbata ba to sai dai wani hukuncin ubangijin don haka babu komai ai dama baku zo ba "

Alh Mustapha labaran yace " aah gara da muka zo tayi laifi ta Kuma zo ta bada hakuri hakan ya wadatar Allah yasa ayi damu Allah Kuma ya kauda duk wata fitina dake ciki" gaba daya suka amsa da Amin ,Haj saratu tace " komai ya wuce Haj babu damuwa ai mun riga mun Zama daya, "

Ita dai Haj murjanatu tunda tayi shuru bata Kara cewa komai ba saida ta Mike ta dubi Àlh Mustapha tace " mu je ko?".

Daganan tayi musu sallama fuskarta babu yabo babu fallasa.har mota Alh Yusuf lamido da Taufiq suka rakasu haka zalika saida suka ga tafiyar su sannan suka dawo gida.

Suna shigowa Haj saratu ta dubesu cike da mamaki tace " lalle Haj murjanatu tana matukar son mujaheeda ai Bana Jin duk duniya Akwai Wanda ya isa ya take izzar Haj murjanatu harta tsaya bada hakuri, ko banza yau mun kafa tarihi gara da kayi haka Taufiq"

Alh Yusuf lamido yace " aah baiyi dai dai ba Kuma Kada Ka sake yin hakan ko da wasa, yanzu da wani mummunan abin ya samu yarinyar nan wa zaa rike a matsayin sila idan ba Kai ba ,nace Kabi komai ahankali tunda yarinyar tana sonka angama me wahalar na Kuma sha gaya maka bazan taba yarda Ko barin yar Alh sulaiman ta wulakanta ba duk yadda zanyi zanyi domin ganin na kare kima da darajata,"

Ya dubeshi sosai Ido cikin Ido yace ," Na rantse maka Ko Kai zaka wulakanta mujaheeda Ko Ka bata Mata Zan iya mamcews da cewa Nina haifeka Zan iya bata maka fiye da yadda baka tsammani, don har abada bazan tabs mantawa da abinda mahaifinta yayi min ba arayuwa"
Ya Kara kallonsa sannan yace " don haka Ka shiga taitayinka duk ranar da Ka Kara Zama sanadiyyar tashi ciwon mujaheeda zaka hadu da fushina matuka "

Yana gama fadin haka ya shige falonsa ayayinda Haj saratu da Taufiq suka bishi da kallo.

Haj saratu Kam tasan yadda maigidanta ya dauki Mahaifin mujaheeda bai hadashi da kowa ba kamar yadda yake kallon mujaheeda tamkar yar da ya haifa tabbatas tasan abinda ya fada haka yake zai iya batawa da Taufiq akan mujaheeda,
Kai wannan aure na mujaheedan da Taufiq akwai kalubale acikinsa, ita Kam Haj saratu tana tare da danta duk inda yafi Samun natsuwa nan take babu yadda zaayi taki danta saboda mujaheeda.

Har Taufiq ya koma bangarensa maganganun mahaifinsa nayi masa yawo akunne shin wane irin matsayi mahaifinsa ysba mujaheeda da har yake iya Jin zai iya bata masa akanta.
Batun yau yake ma Kansa wannan tambayar ba amma dai abinda yasani ne shine mahaifinsa na matukar son mujaheeda adalilin kyakkyawar alakar dake tsakaninsa da mahaifinta.
****
Karfe takwas na dare Taufiq ne zaune cikin falon gidan Haj murjanatu cikin kawatacciyar kwalliyarsa sai tashin wani kamshi yake na musamman.
Gefensa mujaheeda CE kallo daya zakayi mata kasan Tasha wahala nan da nan duk ta rame.
Duk maganganun da Taufiq yake yi batace komai ba , sai da GA bisani ta dube Shi cike da so da Kauna tace
" Zan rokeka wata alfarma daya ?" Ya kafeta da tsararrun idanunsa yace " ina jinki" ta maida bayanta ta kwantar sosai Kan kujera tana kallonsa sannan tace " don Allah don son Annabi ina rokonka da cewa Ko zuwa gaba Kada Ka Kara kokarin hukuntani da Kalmar rabuwa atsakaninmu, ina son Ka sani babu wasu munanan kalmomi agareni da suka wuce kace zaka rabu da ni da Kuma zaka min kishiya don Allah na rokeka Ka taimaka min Ka hana kunnuwana Jin wadannan kalaman har abada"
Taufiq yayi shuru Yana cigaba da kallonta ,ba tare daya Ce uffan ba ta cigaba da cewa" ina son Ka sani ina yi maka son da bazan iya rabaka da wata mace ba ina matukar kishinka bazan taba iya yarda Ka hada ni da wata acikin zuciyarks ba, kamar yadda bazan iya jurar Jin cewa Ka fasa aurena ba " ta tsaida idanunsa sosai akansa tace " kaga wadannan kalaman guda biyu ,zaka rabu da ni da zaka min kishiya to suna iya yin sanadiyyar rasa rsyuwata,,,,,,?

A gaggauce ya dakatar da ita Yana kallonta , yace " ki daina furta Kalmar mutuwa Kan abinda kinsan bazan iya aikatawa ba, Kalmar bazan aureki ba damuwa CE tasa ni fadar haka amma bana nufin hakan har cikin zuciyata , Kalmar Zan Miki kishiya Kuma ki ajeta a gefe saboda ni ba me raayin auren Mata biyu bane ke kadai kin isheni rayuwa".
Mujaheeda ta lumshe Ido cike da farinciki da jindadi tace " nagode ina rokon Allah yabarmu tare".

Hira suka cigaba da yi sosai suna cigaba da tsara yadda sha"anin bikin zai kasance. Sai da dare yayi sosai sannan sukayi sallama ya tafi.

Sosai yake Jin kaunar mujaheeda na Kara Samun matsuguni acikin zuciyarsa. Haka itama mujaheeda ranar kwana tayi tana farinciki idan ta tuna Taufiq yace ita kadai ta isheshi bazai taba yi Mata kishiya ba ta yarda da maganarsa ta Kuma dasata aranta. Tikisa !.

An Gama komai a sabon gidan da Taufiq zai zauna da mujaheeda yayi matukar kyau kwarai da gaske.

Sannan anyi Mata danki na garari na gani na fada duk kayan da aka sa Mata babu Wanda aka saya a Nigeria hakika an kashe dukiya a dakin mujaheeda.

Duk wani shirye shirye angama na daurin aure .zuwa lokacin kuwa mujaheeda ta Sami lafiya sosai.

Tun ranar talata aka fara shagalim biki . Sai ana gobe daurin aure da daddare Haj murjanatu ta bukaci ganin Taufiq wani karamin falonta suka zauna daga ita sai Shi .

Ta dube Shi tace " Taufiq na bukaci ganinka ne saboda wata muhimmiyar magana da nake son mu tattauna " yadan gyara zamansa yace " ina jinki"

Ta muskuta taca " Nasan baka da bukatar na sanar da Kai irin son da nake ma mujaheeda domin kasani , hakan yasa nake son na tunatar da Kai mujaheeda ta rasa mahaifinta bata da kowa sai NI sai mijina sai Kuma Kai Wanda nan gaba kadan zaka iya kwace duk wani gurbinmu agurinta, haka zalika kasan irin lalurar da mujaheeda take da ita tun tana yar karamarta lalurar ciwon zuciya Wanda hakan Yana daya daga cikin abinda yake tilsta min wadata ta da duk abinda take so da Kuma korar damuwarta tare da shawo Kan matsalolinta,

Saboda Kada ciwonta ya tashi ko ya Kara Samun wani sabon salon".

Ta numfasa sannan ta cigaba da cewa " na ba yata dukkan gata na Kula da ita da bukatunta don haka Bana son ta nemi wani abu ta rasa arayuwarta agidanka don haka na kiraka domin kayi min wani alkawari "

Yayi saurin kallonta yace " alkawari? Wane irin alkawari kenan"

Ta dubeshi Ido cikin Ido tace " tunda mujaheeda ta mallaki hankalin kanta na fahimci tana cikin sahun Mata masu matukar kishi musamman akan abinda take so duk duniya Kuma babu wani abu da take so sama da Kai, hakan yasa kullum nake kwana na tashi da tunanin yadda zaayi mujaheeda ta rayu agidanka ba tare da kishiya ba"

Ta muskuta sannan tacigaba da cewa " shiyasa nake son kayi min alkawarin ba zaka tabs yima mujaheeda kishiya ba matukar tana raye zaka yi hakuri Ka rayu da ita ba tare da kishiya ba".

Duk da Taufiq baida sha"awar Zama da Mata biyu tofa hakanan yaji ya samu Kansa da faduwar gaba da ràshin natsuwa.

" Bakace komai ba ".

Ya numfasa gami da kokarin tattaro hankalinsa guri daya yace " Haj Shi Kara aure ai kaddara ce daga cikin kaddarorin da Allah yake kaddarama bayinsa.....?

Tayi saurin katse Shi tace " kawai alkawari na roka kayi min basai kayi min wa"azi ba" ya gyada Kai yace" ni Bani da shaawar auren Mata biyu ban taba ma wannan tunanin ba "

Haj murjanatu ta dakatar dashi ta hanyar daga masa hannu lokaci daya ta Mike zuwa jikin wata kyakkyawar durowa ta bude tasa hannu ta Ciro wata tskarda hade da biro ta dawo kusa da Taufiq ta Mika masa tace " tunda baka da ra'ayi to Alhamdulillah ga tskarda nan kasa min hannu".

Ta Mika masa takarda ya Karba ita Kuma ta koma ta zauna tana kallonsa.

Ya bude takardar Yana karantawa takarda CE me nuna cewa bazai taba yima mujaheeda kishiya ba gashinan a rubuce sa hsnnunsa kawai ake bukatar.

Hakanan yaji zufa tana karyo masa duk da sanyin da ake yi.
Tace " idan har da gaske ne abinda Ka fada ,to ga tskarda nan kasa hannu, idan Kuma har Ka fada da ysudara ne to Ka Miko min takarda ta".

Shin me yasa baya son sa hannu atakardar bayan har cikin zuciyarsa yasan abinda ya fada gaskiya ne?. Taufiq yayima Kansa tambaya.komai ya tsaya masa , tunaninsa ya tsaya cak!

Amma duk da haka baisan dalilin da yasa ya Sami Kansa da sa hannu Akan takardar ba.

Haj murjanatu ta cika da farinciki bayan ya miko Mata takardar ta amsa tana murmushi , tace " yanzu na tabbatar da kana son mujaheeda, Allah yasama aurenku albarka"

Asanyaye ya amsa cikin ràshin karfin guiwa , ta dubeshi tace " shikenan kana iya tafiya ".

Ahankali ya tashi yayi sallama da ita ya fita hakanan yaji damuwa da danasanin sa hannu a takardar suna son su kamashi , duk da yaso ya tsaya yaga mujaheeda hakanan ya wuce ya tafi gida saboda ràshin jindadin zuciyarsa Wanda ya rasa dalilin hakan.

DAGA TASKAR YAR GIDAN IMAM.

NIMA MATARSA CE
NA
HÀBIBA ABUBAKAR IMAM
(YAR GIDAN IMAM)
BABI NA TAKWAS
****

Washegarin asabar karfe biyu da rabi, na rana aka daura auren Taufiq Yusuf lamido da mujaheeda sulaiman a babban masallacin jumaar dake unguwar.

Farinciki wajen mujaheeda baa magana.

Hankalinta bai tashi ba sai da zaa kaita gidanta Haj murjanatu ita ke rungume da mujaheeda tun daga mota har cikin katafaren gidanta.

Gida komai yaji sai dai fatan zaman lafiya.
Saida Haj murjanatu zata tafi ita da sauran Yan rakiyar ta sannan ta Ciro makullin sabuwar mota ta mikama mujaheeda wacce take ta aikin kuka ta rke hannunta ta saka Mata makullin motar tace " Ga makullin sabuwar motarki nan ".

Mujaheeda ta juya ta rungume mahaifiyarta tana cigaba da kuka me karfi, hakan yasa itama Haj murjanatu ta fashe da kuka.

Shin duk duniya idan ba aure ko mutuwa ba me zai rabata da gudan jininta mujaheeda.

Sun ci kuka har sun gaji daga bisani daker mujaheeda ta saki Haj murjanatu ta samu ta tafi cikin matsananciyar damuwa .

Tana adduar Allah ya hada mujaheeda da dukkan farinciki agidan aurenta.

Bata taba Jin damuwar ràshin Kara haihuwa ba tun daga mujaheeda irin na yau, domin dai tana cikin matukar kewar yarta har ta Kai gida kuka take Mai ratsa zuciya.

Ita ma can mujaheeda ba karamar wahala Taufiq yasha ba wajen ganin ya kwantar da hankalin ta saboda yadda take kuka kamar ranta zai fita.

Daker Taufiq ya samu ya shawo kanta ta hakura. Aranar ya maida mujaheeda cikakkiyar mace , ta Kuma Sami karin martaba da daraja agun Taufiq kasancewar ta Kai budurcinta dakin mijinta.

Kwana uku da aurensu Taufiq ya dauki mujaheeda ya kaita gidansu.can yabarta ya wuce office .

Sosai Haj saratu ta Kula da ita sai dai abu daya ta Lura dashi shine mujaheeda babu abinda ta iya sai kwanciya .

Hatta abinci da aka kawo Mata nan ta tsakura tabarshi atsakiyar falon Haj saratu ta kasa koda kauda kayan ballefa tace zata tashi tadan Mata wani aikin ko ba yawa. Tana nan dai akwance bata da wani aiki Saina danna waya.

Wanda Haj saratu batayi màmaki ba idan akayi laakari da irin gatan data fito ciki, sai dai ta wani bangaren zuciyarta ta Sami kanta da tausayama Taufiq domin dai tasan abubuwa da dama da Mata yakamata tayima mijinta bazai samu ba .

Ko da yazo tafiya da ita haka Haj saratu tayita binsa da kallon tausayi.

Ita Kam mujaheeda ta tabbatar tayi dacen surukai don yadda suka dauketa tamkar su suka haifeta musamman Àlh Yusuf lamido da ya fito sosai a matsayin mahaifinta ya tabbatar mata duk abinda Taufiq yayi Mata ya kasance shine mutum na farko da zata zo ta gaya masa zai tsaya Mata zai kare kimarta ba Kuma zai tabs yarda Taufiq ya zalunceta ba ko yaya ne.

Idanta tuna maganganun Àlh Yusuf lamido takan ji wani irin sanyi aranta.

Masu aiki uku Haj murjanatu ta kawoma mujaheeda.babu abinda take yi sai dai taci ta koshi ta kwanta tana aikin chatting.

Duk bukatun Taufiq tun daga Kan abinda zai ci, wankin singileti da gajerun wandunansa da kawo masa abinci duk masu aiki ne sukeyi masa babu ruwan mujaheeda.

Duk da Taufiq bai jindadin hakan to ya danne saboda Yana ganin abin a farko kila don bata Saba bane Amma Yana ganin nan gaba kadan zata karbi ragamar gidanta da Kuma kulawa dashi yadda ya dace.

Yau asabar Wanda yayi dai dai da makwanni hudu da auren Taufiq da mujaheeda, Haj murjanatu ta bukaci ganinsu .

Karfe uku da kwata na rana duka suna cikin falon Haj murjanatu.

Wani farinciki ne ke ratsa mujaheeda data ganta agida duk da kasancewar zuwanta na biyu kenan tun bayan aurenta , haka zalika itama Haj murjanatu tana zuwa kusan duk bayan

kwanaki hudu don taganta taga Kuma halinda take ciki.

Haj murjanatu ta dubi Taufiq sosai sannan tace , " Wata muhimmiyar maganace tasa nayi kiranku".

Mujaheeda tadan sassauta da danne dannen wayarta tana kallon mahaifiyarta, yayinda Taufiq ya gyara zamansa ba tare da yayi magana ba, sai dai zuciyarsa na adduar Allah yasa ba wata fitinar bace zata bullo da ita, tunda bata gajiya da tsurfa.

Tadan muskuta sannan ta cigaba da cewa " sanin kankane mujaheeda tayi karatunta har zuwa matakin degree ta Kuma fita da sakamako mai kyau" ya gyada Kai alamar hakane , ta cigaba da cewa " saboda haka duk da mujaheeda bata rasa komai arayuwarta ba hakan bashi zaisa a dankwafeta acikin gida ba a matsayin asalin matar aure, dole itama tana da bukatar ta fita tayi mu' amala ta cudanya da mutane saboda ko babu komai shima karin ilimi ne Kuma zai rage Mata zaman gida bayan kaima Ka tafi office"

Mujaheeda ta danyi murmushi har kullum tana mamakin yadda mahaifiyarta take saurin gane abinda zai sata farinciki. Ta yaya ta gane zaman gidan baya Mata dadi musamman idan mijinta baya nan , bata saba rayuwar kulle ba duk inda taso zuwa tana zuwa, don haka maganar mahaifiyarta gaskiya ne babu dalilin dunkufewa agida bayan kowace mace yanzu kokari take ta tashi tsaye .

Haj murjanatu ta katsema mujaheeda tunaninta ta hanyar cewa " hakan yasa nayi tunanin maida mujaheeda shugabar daya daga cikin kamfanonin mu , Wanda Zan bata takardun Duka kamfanonin ta bisu daya bayan daya ta zabi Wanda take ganin zata iya jagoranta, "

Ta juyo ta dubeshi Ido cikin Ido tace " Kai Kuma aikin kane Ka yarda Ka amince Mata tayi aiki saboda duk karuwar kanka ce ".

Kan Taufiq yayi nauyi hakika bai taba tsammanin Jin hakan ba don da yayi zaton hakan da tun farko ya sanar dasu baida shaawar matarsa tayi aiki amma bazai hanata yin kasuwanci daga gida ba

" Kayi shuru" cewar Haj murjanatu, ya dago Kansa ya dubi murjanatu yayi mamakin yadda ya hango farinciki a makale a fuskarta Wanda hakan ya tabbatar masa da cewa tana goyon bsyan maganar mahaifiyarta.

Ya dauke kallonsa akanta Yana saka abubuwa da dama acikin zuciyarsa, zahiri baya son matarsa tayi aiki Kuma bazai iya barinta ba saboda baiga dalilin yin aikin nata ba don kuwa babu abinda ta nema ta rasa don haka babu dalilin yin aikinta.

" Kai nake saurara " akaro na biyu Haj murjanatu ta Kara yi masa magana.

" Yaya Taufiq kayi magana mana amincewarka kawai mummy take nema."

Ya numfasa ahankali sannan yace " mummy ni a tunanina babu wani amfanin aiki ga mujaheeda, tunda bata nemi komai ta rasa ba ,"

Nan da nan mujaheeda ta canja fuska tana kallon Haj murjanatu ganin yadda fuskarta ta nuna yasa Haj murjanatu ta tabbatar ma kanta cewa mujaheeda fa tana bukatar aikin nan , don haka ta dubeshi tace " kaji wata magana, Dama ana yin aikine idan aka Rasa wani abu ai ana yin aiki

KO don Samun ilimin rayuwa bawai kasasshene yake yin aiki ba Kuma yanzu don kawai babu abinda ta nema ta rasa sai ta kasa fitowa tayi aiki aah kadaima ma wannan maganar mujaheeda dole zatayi aiki.

Ya dubeta sosai ysce " idan na amince ko ?" Cike da mamakin maganarsa duk suka dubeshi .

Haj murjanatu tace " shiyasa na kiraka saboda Ka amince din"

Ya girgiza Kai yace " To gaskiya mummy bani da raayin matata tayi aiki shiyasa bazan iya barinta tayi aiki ba, Amma Zan iya barinta tayi kasuwanci tana daga gida tunda yanzu akwai cigaba tana zaune zata saya Kuma ta sayar".

Mujaheeda ta turo Baki cike da sangarta tace " Amma ni yaya Taufiq nafi son aikin fiye da kasuwanci idan Kuma kace haka to Zan hada Duka nayi aikin da kasuwancin".

Ya girgiza Kai yace " kada kijama kanki damuwa ba gaira ba dalili domin dai ni bazan barki kiyi wani aikin kamfani ba, bayanni banga wani dalili ba"

A fusace Haj murjanatu tace " aah wai yayane Naga kana wani zakewa Kana nuna wata isa Ko don kawai kana ganin yanzu ikon mujaheeda ya dawo hannuna" ya girgiza Kai yace " ba isa nake nunawa ba, ikon mujaheeda Kuma daya dawo hannuna bani na ba Kaina ba Allah ne ya bani, haka zalika iya gaskiya ta na shaida Miki bazan iya barin mujaheeda tayi aiki ba gaskiya ".

Nan da nan ran mujaheeda ya Fara baci tayi saurin kallonsa tace " Amma kasan mummy fa kake gayama wannan maganar"

" To menene aibun maganar dana fada, don an rokeni abun da bazan iya badawa ba "

Haj murjanatu tace rai abace " ta yaya kuwa zakaga aibun maganganun da kake fada bayan kafi kowa sanin dai dai , waye Kai dazance Ga abinda zanyi da yata kace aah , mujaheeda zatayi aiki fakat babu sauran magana".

Taufiq shima zuwa lokacin ransa ya Fara baci , hakan Yana ya tashi Yana cewa " ba wani bane illa Mijin mujaheeda, Kuma na riga na yankema Kaina cewa mujaheeda ba zatayi aiki ba" ya wauwaya ya dubi mujaheeda ba damu da fushin dake makale akan fuskarta ba yace " ina waje ina jiranki idan kun gama".

Yana Gama fadin hakan bai saurari komai ba ya fice Haj murjanatu ta bishi da Ido cike da mamaki.

Ta dubi mujaheeda tace " zo nan * a shagwabe ta taso daga wajen zamanta ta fada Kan cinyar mahaifiyarta ayayinda ta cigaba da shafa Saman bayanta tana cewa " kinga irin ràshin darajar da mijinki yake nuna min KOe? Bai damu da ya nuna biyayya agareni ba ko bani na haifeki ba iya ràshin Kimata da zai dinga gani kenan" cikin bacin rai mujaheeda tace " na gani mummy, Kuma duk duniya babu abinda nake so sama da Ku dinga Samun jituwa atsakaninku "

Haj murjanatu tayi Dan Jim tana tunani ga dama ta samu na yarda zata kawo sabani tsakanin mujaheeda da Taufiq.

Tace " yanzu me kika fahimta da abinda Taufiq ya aikata" ta girgiza Kai alamar bakomai, Haj murjanatu tace " ya nuna baya son cigabanki, hakan ya tabbatar min da cewa Yana cikin sahun mazan da suke bakinciki da cigaban matansu, ta yaya bazai Miki bakinciki ba kina hawa motar data fi tashi kina kashe kudin da bazai iya kashewa ba to ta yaya Kuma zai barki a kiraki da manajan kamfani da zakiyi aiki ba a karkashin kowa ba ,

Bayan Shi yana can ya kare a karkashin wani Yana kamfanin aikin hanya ana turasu suna

wahala oganninsu na can suna shan raba.
Don haka yasanya bakinciki aransa "
Mujaheeda tayi tsam da ranta tana son yarda da maganar mahaifiyarta amma son Taufiq na kokarin hanata dora masa wannan mummunar dabiar , duk da dalilan da mahaifiyarta ta bayar zasu iya Zama gaskiya Amma ta kasa yarda,.
Sai dai abu daya ta sani wannan Karon sun Sami bambanci ra'ayi tsakaninta da Taufiq domin dai tabbas tana son yin aiki, dole Kuma zatayi,
Haj murjanatu ta dago Kan mujaheeda tana kallonta tana son ganin tasirin da maganganun ta suka yi a wajenta ,tace " saboda haka ya rage ruwanki kiyi yaki ki kwaci yancinki tun kafin abin yayi nisa aiki dai tunda kina so sai kinyi Shi , saboda haka ki nemi hanyar dazai amince ,domin idan lokaci yayi ina son ki sani ko ya amince ko bai amince ba zaki yi aiki ."

Ta gyada Kai tace " Bakomai mummy zanyi magana dashi".
Ta gyada Kai ta zuba Mata Ido tace " akwai matsala ne " ta girgiza Kai tace " bakomai mummy ina godiya".
Tayi murmushi tace " babu godiya atsakaninmu duk abinda kike so ko meye wahalarta ki fada zaayi Miki"
Tayi dariya har gefen kumatunta suka lotsa tace " Allah yabar min mummy na".
Sosai mujaheeda ta dauki lokaci kafin ta fito domin zuwa lokacin Taufiq ya kawo wuya saura kadan ya tafi ya barta sannan ta fito yadda ya hade rai itama haka ta hade rai, harta shiga motar yaja suka tafi babu Wanda yacema wani uffan.
DAGA TASKAR YAR GIDAN IMAM.

NIMA MATARSA CE.
NA
HÀBIBA ABUBAKAR IMAM
(YAR GIDAN IMAM)
BABI NA TARA.
****
Ko da suka isa gida shima babu Wanda yabi takan dan'uwansa kowa zuciyarsa a wuya take.
Abinda zaici ma masu aiki ne suka kawo masa , kadan ya ci ya tashi ya fice,ràshin sanar da ita zai fita ya Kara harzuka mujaheeda ranta yayi matukar baci.
Hakan yasa tayi ta jiran dawowarsa.bai shigo gidan ba sai karfe sha daya saura na dare. Kai tsaye daki ya wuce bai saurari mujaheeda ba bai kuma damu da irin kallon da take masa ba, yayi Shirin wanka ya shiga wanka .har ya fito ya kintsa mujaheeda na tsakiyar gado rike da wayoyi ta danna wannan ta aje ta danna wannan Karo na farko kenan da yaji ransa ya Fara sosuwa agame da yadda mujaheeda ta dauki waya da matukar muhimmanci yadda bata iya minti biyar bata dauki waya ba.
Ahankali ya gama Shirin bacci ya haye gadon ya kwanta gami da janyo bargo ya rufe jikinsa sosai.

" Yaya Taufiq" mujaheeda ta Kira sunansa tana kallon bayansa. Ya amsa ba tare daya juyo ba

ko ya motsa.
Tace " ban fahimci wannan sabon lamarin ba" " na mene ?" Ya tambaya a gajarce.
Ta jinjina Kai tace " yaya kake magana tamkar baka fahimci abinda nake nufi ba , bayan kafi kowa fahimtar abinda nake nufi, tunda Muka dawo sai wani huci da isa kake Ka fita baka cemin komai ba, ka dawo kana cigaba da cika da batsewa don kawai Baka son nayi aiki".
Ya gyara kwanciyar sa yace " eh Bana son kiyi aiki bana Jin Kuma akwai Wanda ya isa na barki kiyi aiki "
Cike da mugun mamaki tace " Amma wannan maganar da mahaifiyata kake yi ko, itace bata isa ba to shikenan atsaya anan saboda Naga abin Naka Yana so ya wuce gona da iri, Kuma Kada Ka manta wacce kake yin maganar nan akanta mahaifiyata ce wacce ban hadata da komai ba, ba Kuma zan juri Ka dinga kokarin rainata".
Afusace yace " ban rainata ba , amna ina son ki sani babu yadda zaayi Ku dinga kokarin juya rsyuwata yadda kuke so ba tun kafin auren nan akesa min dokoki yanzu Kuma bayan Auren ina tsammanin na mallaki yancina sai Kuma Ku dinga kokarin nuna gszawata da kasawata kuna kokarin maidani wani sakarai, ta yaya Zan zauna mahaifiyarki ta dinga kokarin juya akalar rayuwata kema kinsan bazai yuwu ba".
Ta yi masa kallon tsaf sannan tace " yanzu don kawai mahaifiyata tana kokarin ciyar da rayuwata gaba shine kake ganin aibu kamfanonin nan kusan duk mallaki na ne ta yaya kake neman Ka hanani taimakon mahaifiyata bayan na kawo karfin da Zan iya taimakon ta tun rasuwar mahaifina ita ke tsaye Kan ganin ta tafiyar da komai yadda yakamata meye laifinta don kawai yanzu ta nemi taimakona , zaman me zanyi agidan ? Meye laifi don na fita nayi aiki".
Yace " babu laifi sai dai ràshin raayina Akan hakan, Bana son muna Jan maganar nan , bana son mu Sami matsala ,aiki dai bana so , ba Kuma Zan barki kiyi ba Donni banga abinda zaisa kiyi aiki ba"

" Idan Kai Baka San dalilin dayasa zanyi aiki ba to ni nasan dalili Kuma dole zanyi aiki"
Cike da mamakin ràshin kunyar mujaheeda da yadda take gaya masa magana babu mutuntawa Ko girmamawa yasa ransa yayi matukar baci ya juyo afusace ya dubeta yace
" Dole sai kinyi aiki " ta gyada Kai alamun eh ya jinjina Kai yace " zanga Wanda zai sani na barki kiyi aikin "
Tace " ok zaka gsnshi kuwa"
Ya juya ya kwanta da alkawarin bazai Kara tankawa ba ,hakan yasa ta cigaba da maganganun ta Amma bai Kara tankawa ba hakan ya Kara harzuka mujaheeda Kwarai.
Washegarin ma haka suka tashi ,kamar yadda suka kwanta .haka zalika Taufiq Yana karyawa yabar gidan.
Bai dade da fita ba Haj murjanatu ta kirata awaya da son Jin abinda ake ciki.
Mujaheeda tadan numfasa tace " Aini mummy gaba daya gani nake kamar an canja min yaya Taufiq tun daga jiya" , Haj murjanatu tace " kamar yaya?"
Mujaheeda tadsn gyara zamanta asaman kujera tace " tunda Muka dawo daga gida jiya ya dauki wata isa da iko ya dora ma Kansa, duk yadda naso ya tsaya ya fahimceni ya Kuma barni nayi aikin nan yaki, asalima ya Kara tabbatar min da cewa bazai taba barina nayi aiki ba babu Kuma Wanda ya isa ya sashi yabarni"
A kufule Haj murjanatu tace " haka yace ?" Ta daga Kai tamkar tana ganinta tace " haka yace,

Kuma ko da ya fita dazu babu alamar zai sassauto domin ko ta Kaina bsi bi ba ya fita"
Ran Haj murjanatu ya Kara baci tace " Yana karya ne don bai Isa ba ki kwantar da hankalinki badai kina so ba to aiki ya Zama dole ko da hakan na nufin faruwar abubuwa da dama"
Mujaheeda tayi saurin cewa " aah mummy bana son wannan abin ya Zama wata matsala daban,akwai hanyar da nake son bi wacce matukar na bita bata bulle damu ba to dole ayi hakuri abar maganar kawai mummy" " ki fasa aikin bayan ranki na so" cewar Haj murjanatu, mujaheeda tace " eh Zan hakura tunda ina son Zama lafiya dashi , Amma sai nabi hanyar da nace din idan ban dace ba shikenan sai a hakura"
Haj murjanatu tace " wace hanya ce zaki bi" tace " Kada ki damu mummy Zan sanar dake sai na aiwatar Amma" ta gyada Kai tace " shikenan sai na jiki" daganan sukayi sallama.
Haj murjanatu ta saki tsaki matsalar talaka Kenan mutum baida ko Sisi Amna ya dinga fankama da takama ta banza da wofi shiyasa harka da talaka akwai damuwa.

****

Karfe uku da minti ashirin da biyu motar mujaheeda ta tsaya aharabar gidan Alh Yusuf lamido.
Ta Bude kofar motar ta fito sanye cikin wata hadaddiyar doguwar Riga mai matukar kyau samnu ahankali ta tunkari cikin gidan idonta nakan rumfar aje mota ràshin ganin motar surikinta ya tabbatar Mata da cewa baya gida Wanda ba haka ta so ba , Kuma ko karfe nawa zai Kai bai dawo ba ya Zama dole ta tsaya ta Jira dawowarsa domin wajensa ta zo.
Haj saratu ta tarbi surikarta sosai kamar yadda ta Saba ta wadatata Kuma da duk abinda take bukata , sai dai dabiarta da Haj saratu bata so shine na son jikin mujaheeda da aikin Tabe Taben waya .domin dai kwance take Kan doguwar kujera hankali kwance tana aikin chatting.
Sai karfe hudu da rabi da minti shida Àlh Yusuf lamido ya shigo Kai tsaye bangarensa ya wuce.
Haj saratu ta bishi da duk abinda tasan Yana da bukata a dai dai wannan lokacin .
Saida ta tabbatar ya natsa ya ci abinci yasha furarsa wacce ta Zama daya daga cikin al" adar rayuwarsa kullum sai yasha ta sau uku.
Sannan ta dubeshi tace " mujaheeda tazo tun dazu tana nemanka" yayi saurin kallonta yace " lafiya suke ko ita da Taufiq din ba wata matsala "
Tace " to ni dai bansani ba amna ina ganin da akwai matsala atsakaninsu da Naga slams ko a fuskarta amma ba wata alamar hakan,".

Yace "To Allah yasa jeki Kira min ita" ta tashi ta fice cikin kankanin lokaci mujaheeda tayi sallama acikin falon .
Cike da kulawa da murmushi yace " zoki zauna mujaheeda '
Ta wuce Kan kujera tayi zamanta tana Dan murmushi sannan ta gsidashi ya amsa Yana tambayar ta meyasa tazo ita kadai don motarta ya gani awaje.
Tadan gyara zamanta tace " ni kadai nazo Abba saboda yaya Taufiq fushi yake yi dani dalilin zuwana gareka kenan "
" Wane irin fushi meya faru?". A hankali mujaheeda ta gaya masa komai ta Kara da cewa " to ni Abba na rasa aibun wannan abin ba karkashin wani zanyi aiki ba balle yace zaa takura masa kamfanina ne babu wani abin damuwa Amma ya dage yace babu yadda zaayi nayi aiki ba Kuma Wanda ya isa yasa yabarni ,
Shiyasa nazo gunka saboda Kaine ubana Kaine Kuma nasan zaka iya gaya masa ya yarda Ko

ba ya so, kwarai ina son yin aikin nan KO don na rsgema mahaifiyata aiki "
Alh Yusuf lamido ya gyara zamansa yayi murmushi yace " ki kwantar da hankalinki in don wannan ne damuwarki ta kare na gaya Miki Zan tsaya Miki Akan komai matukar zaki samu farinciki " tayi murmushi sosai tace " Nagode Abba Allah ya Kara girma nagode sosai" ya ce " Kada ki damu,yanzu ki tashi ki tafi gida ni Zan Kira Taufiq zamuyi magana da Shi" ta amsa da toh sannan ta Kara masa godiya daga bisani tayi masa sallama ta fito.

Bata zauna ba sallama kawai tayi da Haj saratu ta kama hanyar gida , zuciyarta na cike da farinciki tana Kuma karama Allah godiya daya hadata da suriki irin Alh Yusuf lamido Wanda yake yi Mata so dai dai da irin son da uba yake ma yarsa.
Tana fita Alh Yusuf ya daga ways ya Kira Taufiq ya bashi umarnin yazo ya sameshi yanzu agida, Taufiq ya tabbatar masa yana hanya.yanzu zai Iso gidan.

Cikin kankanin lokaci Taufiq ya iso gidan ,ko kadan Bai kawo dalilin mujaheeda yasa Abbansa ya Kira Shi ba .
Lokacin daya shiga falon tare da Haj saratu ya tadda mahaifinsa da alama magana suke tattaunawa wacce ba tayima Haj saratu dadi ba don yadda ta hade rai.
Asanyaye ya zauna akasan kafet Yana gaida mahaifansa. Haj saratu ta dubeshi tace " Akwai abinci na kawo maka Ka ci ne don dai nasan ba daga gida kake ba, wata kila kana can kana yawo da yunwa"
Ya girgiza Kai yace " Kada ki damu umma, ba daga gida nake ba amma na ci abinci Bani da yunwa". Ta koma ta gyara zamanta ta rasa dalilin da yasa takema Taufiq kallon tausayi.

" Abbah gani' Taufiq ya fada Àlh Yusuf lamido ya muskuta Yana kallonsa yace " Taufiq me ya faru tsakaninka da matarka ".
Yayi saurin kallonsa yace " Kai mujaheeda tana da matsala,kiranka tayi Abbah".
Cike da mamaki Haj saratu ta dubeshi tace " Au ba da izininka Bama kenan ta zo gidan" ya juya Yana kallon mahaifiyarsa yace "zuwa gidan tayi ni ban Sani ba"
Haj saratu ta saki salati tace " lalle yarinyar nan da sauran gyara alamarinta , yanzu tasa kafa ta fita daga gidan mijinta ba tare da izinin mijinta ba "

Alh Yusuf lamido ya jinjina Kai yace " eh wannan bata kyauta ba Kuma zanyi Mata magana Zan ganar da ita tayi kuskure, Amma kafin nan"
Ya waiwayo ya dubi Taufiq yace " me yasa Baka son matarka tayi aikin kamfani"

Taufiq ya saki ajiyar zuciya yace " Abbah tun farko ni ba namiji bane me son matarsa tayi aiki, saboda akwai matsaloli kwance acikin aikin mace duk da ba duka bane aka Zama daya Amma azahiri INA ganin irin rayuwar da Mata suke yi awajen aiki, ràshin kamun Kai cudanya da Maza da sauransu duk namiji me so da kishin iyalinsa Bana tsammanin zai iya barin matarsa tayi aiki shi yasa Bana so tayi aiki, bugu da Kari Kuma babu abinda mujaheeda ta nema ta rasa da zaace dole sai tayi aiki,"
Ya aje numfashi ba tare da kowa ya katse Shi ba ya cigaba da cewa" kawai abinda na fahimta shine mahaifiyar mujaheeda tana son ta shiga cikin rayuwar aurena ya Zama itace me tsara min

abinda zanyi Wanda Kuma ni bazan lamunci haka ba"

Haj saratu ta ce" ina fa haka zai yuwu dole fa Haj murjanatu ta fita a sha" anin auren yaran nan ,Kuma gaskiya ne abinda Taufiq ya fada mujaheeda bata da wani dalili na yin aiki me take nema tana cikin gata kawai dai don fitinar tsiya da ràshin son Zaman lafiya aikin me don Allah"

Alh Yusuf lamido ya numfasa ya Fara magana.

DAGA TASKAR YAR GIDAN IMAM

NIMA MATARSA CE
NA
HÀBIBA ABUBAKAR IMAM
(YAR GIDAN IMAM)
BABI NA GOMA
****

" Ta yaya zakace mujaheeda bata da dalilin yin aiki , bayan dukiyarta ce take son ta koyi yadda zata ciyar da ita gaba,

Bayan duk irin kokarin da mahaifiyarta tayi na ganin ta tafiyar da hsrkokin ita kadai yanzu Kuma lokaci yayi da zasu hada hannu tare su taimaki junansu sai kace ba haka ba, idan har Ka yarda da matarka meye abin damuwa don kawai zatayi aiki bayan aikin nan ba na wani tashin hankali bane babu abinda zai rageka dashi".

Ran Taufiq ya shiga kuna domin fahimtar da yayi bazai samu goyon bayan mahaifinsa ba akan maganar, shin meyasa Àlh Yusuf lamido ya dauki soyayya ya dorama mujaheeda Anya kuwa hakan bazai zamo illa agareshi ba.

Haj saratu ta Kara hade rai tace " gaskiya Alh Kada Ka ce zaka goyi baysn su mujaheeda Akan maganar nan, shima Taufiq Yana da damar da zaa tsaya aji uzurinsa a Kuma girmama hukuncinsa ko kuwa shikenan Shi yayi aure ne kawai Amma baida yancin juya akalar gidansa yadda yake so"

Alh Yusuf lamido ya girgiza Kai yace " aah babu Wanda zai kwacema Taufiq wannan damar domin Allah ne ya bashi haka zalika bazan takura masa ba akan duk abinda ya yanke Amma ina son ya Sani Bana son damuwar mujaheeda ina so na bàta duk abinda ranta yake so badon komai ba sai don abinda mahaifinta yayi min arayuwa"

Haj saratu tace "abinda mahaifinta yayi maka ai Bai maka don Ka rama mishi ba , balle har tasa Ka nemi tauye hakkin danka saboda kawai farincikin mujaheeda ".

Yau dai Taufiq Yana son yaji abinda mahaifin mujaheeda yayi masa da har ya dauki Kula da yarsa da farincikinta amatsayin hanyar da zai saka ma mahaifin nata duk da kasa ta rufe masa Ido.

Yadan dubi mahaifinsa kadan yace "wai Abba me mahaifin mujaheeda yayi maka ne da Ka dauki saka masa amatsayin dole duk da baya duniya".

Ya numfasa gami da kallon Taufiq sosai , sannan yace " abinda Àlh sulaiman yayi min wani abu ne Wanda har na koma ga mahaliccina bazan taba mantawa ba .

Baya ga maidani babban yaronsa a office da bani dukkan wata daraja da kima , yayi min Kuma wani babban abu Wanda shine nake kallo nake Jin Zan iya yima yarsa komai matukar zatayi farinciki don nasan duk duniya baida wani abinda yake so sama da ita.".

Ya Kara numfasawa sannan ya cigaba da cewa " mahaifiyata ta kwanta jinya kasani ciwon koda alokacin Bani da Shi Banda kudin dazan iya daukar dawainiyarta , nasan ba zaka manta irin mugun yanayin da Muke ciki ba lokacin,

A wañnan lokacin zaayi Mata aiki na kudi masu matukar yawa Wanda alokacin KO kwatan kudin ban mallaka ba , mahaifiyata na cikin mummunan halin da ko dai mutuwa ko rayuwa, na cire rai da ita don nasan banda inda Zan Samo kudin nan, ko a office Shi da Kansa Alh sulaiman ya fahimci ina cikin wani mawuyacin hali da ya tambayeni Kuma banyi kasa a guiwa ba na gaya masa damuwar da nake ciki, ya bani hakuri tare da yima mahaifiyata fatan Samun sauki.

Amma wani abu da ya bani mamaki aranar bayan na dawo gida , na shirya na koma asibiti sai likita ya tabbatar min da cewa gobe zaa yima mahaifiyata aiki saboda an riga an biya kudin aikin."

Ya juyo ya dubi Taufiq yace " kasan waye ya biya kudin aikin Haj " ya girgiza Kai yace " aah "

Alh Yusuf lamido ya gyara zamansa yace " Alh sulaiman shine ya biya kudin aikin Haj, Kuma tun daga wannan lokacin shine ya cigaba da daukar dawainiyarta har Ta koma ga Allah ".

Ya Kara zuba idonsa Akan Taufiq yace "yanzu Wanda yayi maka haka shine kana da damar da zaka saka masa Amma Ka kasa, kasan girma da kimar Uwa ? Na rantse maka duk Wanda ya kyautatama iyayenka bazaka taba mantawa dashi ba don haka mujaheeda matukar ina raye bazan taba bari ta tozarta ba don haka ya rage naka Ka taimaka min na sauke nauyin da na dorama Kaina , barinta tayi aiki babu wata illa matukar zata kare mutuncinta ta kare naka".

Haj saratu dai fuskarta bata nuna jindadin wannan hawan kawaran da ake yima danta ba , domin bata hango adalci acikin lamarin ba, ta maida idonta Kan Taufiq tana matukar Jin damuwarsa acikin zuciyarsa

Taufiq ya numfasa hakika Bai son mujaheeda tayi aiki , babu hakan acikin tsarin auransa da ita, Amma yaya zaiyi tunda Yana son kwanciyar hankalin mahaifinsa , yadan gyara zamansa yace " Shikenan Abba, taje tayi aiki ba wani abu ".

Haj saratu tayi karaf tace " Kada Ka takura kanka idan Baka son tayi aikin nan fa dole zata hakura ". Ya dubeta yace " bakomai na barta taje tayi aikin"

Haj saratu ta kauda kanta cike da Jin haushi domin dai tasan dole akayi masa don ba haka yaso ba .hakan yasa ta Mike tsam tabar falon.

Alh Yusuf lamido ya nuna jindadin sa kwarai matuka gami da sa masa Albarka, sannan ya cigaba da kwantar masa da hankali tare da misalai Kala Kala Akan ràshin kasancewar matsala ga aikin mujaheeda, sai dai Sam ba wata gamsuwa da Taufiq yayi domin dai hankalinsa bai kwanta da hakan ba , ya Jima a gidan kafin ya wuce gida zuciyarsa cike da Jin zafin yadda mujaheeda ta kwaso matsalarsu ta kawota gaban mahaifinsa.

Ko da ya koma gida babu wani sakin fuska tsakaninsa da mujaheeda bata shiga harkarsa ba bai shiga tata ba .

Har saida suka zo kwanciya Taufiq na zaune a gefen gado , mujaheeda na tsakiyar gado tana sana' ar danna waya, ya dan juya ya dubeta ya Kira sunanta " mujaheeda", ta amsa ba tare data dube Shi ba " na'am".

" Me yasa kika dauki matsalar mu kika Kai gun Abba " ya tambayeta a gajarce , ta Dan dubeshi akaro na farko sannan tace " saboda nan ne nake ganin zaa iya nuna maka karfin iko da zaisa Ka janye kudirinka tunda ni mahaifiyata bata isa ba ,to nasan mahaifinka ya isa , Shi ba zaka iya ce masa. aah ba".

Ya Kara dubanta yace " shiyasa kika je ba tare da izinina ba " tace " to kana fushi ta ya Zan nemi izininka"

Ya nisa yace " mujaheeda Sam Sam ba irin wannan rayuwar nake mafarki yi da ke ba , ina son nayi rayuwa da ke me dadi me tsafta yadda zaa dinga kwatance damu na alheri , don haka ya Zama dole ki san yadda rayuwar aure take da yadda ake yinta domin Naga tamkar wasa kika dauki rayuwar aure"

Ta dubeshi tace , " yanzu duk me ya kawo wannan maganar, don kawai nakai kukana wajen mahaifinka da yskinin zai share min hswayena shine aibu ".

Yace " yanzu kina nufin kenan duk abinda zai faru tsakaninmu ba zaki iya hakuri ki ajeshi acikinki ba sai kin daukeshi a farsnti kin kasa kin Kai gidanmu, to ina son ki sani daga. Yau Kada ki Kara Kai karata wajen Abba don Yana sonki zai iya tsaya Miki Akan komai hakan baya nufin ni Kuma Zan rungume hannu na tsaya na Zama Dan kallo a gidana ".

Wani irin kallo take masa me wuyar fassaruwa ba tare data C
ce uffan ba , ya haye gadon gami da Jan bargo Yana fadin " aiki ko to na barki kije kiyi aiki ,"

Cike da farinciki tace " Allah yaya Taufiq Kai Amma nagode " haushi yasa yaki tankawa , haka tayita maganganun ta masu nuna alamun ta jidadi Amma Taufiq tunda ya Fadi haka Bai Kara magana ba.

Washegari mujaheeda tana ta kokarin kyautata ma Taufiq , hakan yasa shima yadan saki fuska ,saida zai fita office ne ta ce " yaya Taufiq ina son zanje gida wajen mummy anjima," ya dubeta Yana kokarin fita yace " Allah ya kiyaye hanya" bai Jira amsarta ba ya wuce abinsa.

Tun kafin sallar azahar mujaheeda ta isa gidansu, da albishir din Taufiq ya amince tayi aiki,

Haj murjanatu ta ruko hannunta tana kallonta tace " ta yaya ya amince , bayan irin hakilo da kokarin nuna isar da yake yi", tayi murmushi ta kwashe duk yadda akayi ta gaya Mata ta Kara da cewa " kinsan mummy Abban sa Yana Sona matuka , ni na rasa abinda nayi masa ma yake Sona haka, ya gaya min zai Kula da ni tamkar yadda mahaifina zai Kula da ni Kuma ayau na Kara tabbatar da hakan".

Haj murjanatu tayi dan Jim tana tunani shin me Alh Yusuf lamido yake nufi ? ko dai wata hanya ce ya bullo da ita domin kwace Mata ya da kokarin son ya maye gurbin mahaifinta , ta girgiza Kai aah bazata yarda da hakan ba domin tayi Imani da cewa wani sabon salon ysudara ne , so yake kawai ya kame zuciyar yarta .

Tace " to koma dai menene Taufiq ya rufama Kansa asiri, aiki Kuma zakiyi ba gudu ba ja da

baya, yanzu Zan Baki file din kowanne kamfani sai kije ki zauna kibi ki karanta ki fahimta daganan saiki zabi Wanda kike ganin zaki iya aiki acikinsa".

Ta gyara Zama tace " to shikenan mummy badamuwa".
Haj murjanatu tace " Amma dai sai yamma zaki tafi Ko " tace " Bana Jin komawa gidannan mummy sai yamma sosai Zan tafi".
Haj murjanatu tayi murmushi tace " yi kwanciyar ki ki huta kinji ".
A kalla sai kusan karfe takwas na dare mujaheeda ta koma gida, zuwa lokacin kuwa. Taufiq ya dawo Yana zaune afalo ransa abace duk bayan dakika daya saiya dubi bakin kofa, akufule yake ransa abace hakan yasa ko da ta shigo baiko daga Kai ya kalleta ba .
Itama bata bi ta Kansa ba ta shige daki tayi Shirin wanka ta fada bandaki, bayan fitowarta ba wata kwalliya tayi ba ,
Kayan bacci kawai ta zura ta fito ta umarci daya daga cikin masu aikinta ta yanka Mata fruit ta kawo mata daki,
Bayan ta Kai Mata fruit din, mujaheeda ta haye gado tana Shan fruit tana duba file din kamfanonin data taho dashi daga gida , hankalinta kwance babu tunanin wane Hali mijinta yake ciki? Babu tunanin Yana bukatar wani abu ko aa, balle fa ta zauna kusa dashi tayi masa hira ko taji Yana cikin damuwa ko aa.
Lalle da sauran gyara a zaman Auren mujaheeda.
Tayi nisa cikin karance karsncenta Taufiq ya shigo dakin ko kallonta baiyi ba ya shige wanka ,bayan ya fito yayi Shirin kwanciya yayi kwanciyarsa ba tare da yayi Mata magana ba , duk da zafin da zuciyarsa take yi da kuna shin me mujaheeda ta daukeshi?.

Bai dade da kwanciya ba, mujaheeda ta dube Shi hankali kwance tace " yaya bacci zakayi? " , Bai tanka Mata ba , bata samu da hakan ba ta cigaba da cewa ":daka tashi Ka tayani zaben kamfanin daya kamata nayi aiki dashi".
Ba tare da ya KO motsa ba yace " don me Zan zabar Miki inda zakiyi aiki bayan bani zanyi Miki aikin ba , ki zabi Wanda ranki yayi miki mana".
Ta dan waigo tana kallon bayansa tace " Niko kana bani mamaki, banyi tsammanin kana cikin Maza masu ruko ba da kokarin maida Mita wani sashi na rayuwarka, ni banga dalilin wannan nuna halin ko' in Kulan da kake yi da ni ba ".
Ya yi saurin yaye bargon ya tashi ya zauna Yana kallonta a fusace yace " ke Baki ga irin naki halin ko'in Kulan da kike nuna min ba, tun karfe nawa kika tafi gidansu Amma Baki dawo ba sai karfe takwas na dare Baki da tunanin ya nake ciki saboda kawai bakisan yadda zaki Kula Dani ba , kin dawo ko kallon kirki Baki min ba , wai ke mujaheeda me kike nufi ne ? Wace irin rayuwa kike tunanin zamu shimfida da irin wannan mummunar halin da kike nunawa, ".
Ta turo files din gefe tana kallonsa itama cikin fusata , tace " Kai nifa na gaji yaya Taufiq, ni ban iya fada ba da tashin hankali Bana Jura, don me zamu zauna muna Abu daya na gaji gaskiya me kake so nayi, don kawai naje gidanmu na Kai dare shine zai Zama fitina , gidan da anan Ka dakko ni yau Kuma don naje na Kai dare shine zai Zama abin tashin hankali".
Ya dubeta sosai yace " matsalar kenan, ba kisan ma kinyi kuskure ba balle ki gyara kina ganin ahaka rayuwar zata cigaba "
" To me kake son nayi? Ta tambaya a zafafe.

Ya dubeta yace " ki Zama mace ta gari?" Tayi masa wani irin kallo tace " ni ba mace ta gari bace kenan?", Ya jinjina Kai yace " dabi' unki suna kokarin nuna hakan, saboda akwai gyara masu tarin yawa acikin dabi' unki Kuma bana Jin Zan cigaba da jure irin dabi'un naki, kwata kwata kwana nawa da auren mu amma damuwoyi suna nema suyi yawa ".

Tace cikin bacin rai " yanzu dai kana ganin damuwowin daga gareni suke Ko, to duk nasan dalilin da yasa kake haka saboda kawai zanyi aiki , to kaje duk abinda kasa aranka hakane " Ya saki tsaki ya koma ya kwanta zuciyarsa na kuna cigaba da magana da itama zai iya ja masa Karin wata damuwar hakan yasa Bai Kara tankawa ba duk da maganganun da takeyi na fusata saboda zahiri taji zafin maganganun da Taufiq ya gayá Mata, Shin wace irin rayuwar aure zatayi da Taufiq? Kadafa itama ta fada sahun zaman Auren mahaifiyarta da kullum suke cikin sabani da ràshin jituwa irin rayuwar auren data tsana domin dai babu wani abin dadi aciki .
Ta kasa cigaba da duba files din saboda bacin Rai rufewa tayi ta aje itama ta kwanta dukkansu zuciyoyinsu babu dadi kowa da abinda yake sakawa.

DAGA TASKAR YAR GIDAN IMAM

NIMA MATARSA CE
NA
HÀBIBA ABUBAKAR IMAM
(YAR GIDAN IMAM)
BABI NA GOMA SHA DAYA
****

Washegari ma da wuri Taufiq ya fice, domin Yana da abubuwan yi da yawa a office, ko karyawa bai tsaya yi ba ,
Ba wata Kuma cikakkiyar sallama da yayi da mujaheeda domin sanda zai tafi tana wanka sallahu kawai ya barma masu aikinta su gaya Mata ya wuce office.
Hakan ko bakaramin bata ran mujaheeda yayi ba don aganinta ya wulakanta ta ta yaya zai gayama masu aiki su gaya Mata abinda Shi kadai ya kamata ya gayá Mata.
Wai me yake nufi ne? Ta tambayi kanta gami da sakin Dan karamin tsaki, me yayi zafi ne da yake kokarin maida karamar magana ta Zama babba gaskiya ba zata juri wannan abin ba ,don kanta bazai iya dauka ba.
Ta shirya tsaf ta wuce gidansu ba tare data nemi izini wajen mijinta ba , don Tasha alwashin ba zata Kira wayarsa ba .
Isarta gida ta nunama Haj murjanatu cewa a kamfanin sarrafa auduga take son tayi aiki saboda abubuwansu sunfi burgeta .
Haj murjanatu tace " to shikenan babu damuwa , ranar litinin zamu je Zan gabatar da ke za Kuma ki dare jujerarki , Shi Kuma Wanda yake matsayin manajan wato Alh jibrin zai koma mataimakinki , nasan Kuma zakiji dadin aiki dashi domin Yana da hankali Yana da kirki kwarai , ya taimakeni Akan kamfanin nan sosai , baida damuwa" mujaheeda tace " to mummy Allah ya kaimu".

Haj murjanatu tadan zuba Mata Ido tana karantar damuwar dake kwance Akan fuskar yarta ,

sannan tace " mujaheeda meke faruwa ne ?" Ta waigo tana kallonta tace " me kika gani?", Tace " damuwa nagani a tattare dake ,akwai wani abu da yake damunki ne, Bana son ki boye min komai domin duk duniya kinsan dai idan akwai Wanda ya kamata ki gayama damuwarki to baya na ne ".

Mujaheeda tadan numfasa gami da lankwashe Yan yatsunta har saida sukayi Kara , tace " mummy, kullum fargabata da tunanina Bai wuce ace yau na tsinci Kaina cikin irin rayuwar aurenku da kuka gudanarwa tsakaninki da daddy ba , saboda rayuwace da babu dadi , babu fahimtar juna atsakaninku , babu wata jituwa , to sai gashi nima tamkar nasa kafata acikin takalminki, shin mummy me ke Sanya ràshin jituwa atsakaninku da daddy ki gaya min KO don na kare Kaina daga fadawa irin rayuwar da kuke yi ".

Haj murjanatu ta Mike ta tashi nan da nan fuskarta ta canja damuwa suka baibaye fuskarta, cikin sautin da yake nuni da bakinciki da bacin rai tace " bazan iya gaya Miki abinda ya ke Haddasa mana ràshin jituwa ba da Alh Amma kisani abin Mai girma ne Abu ne Kuma da bazan taba mantawa dashi ba har na koma ga Allah shiyasa Ko na manta na saki jiki dashi da zaran na tuna nakan ji haushi da tsanarsa fiye da kullum ina ganin dalilin da yasa kenan farincikinmu tare baya nisa ".

Mujaheeda ta gyada Kai tace " bazan matsa Miki ki gaya min komai ba ,saboda tunda na mallaki hankalin Kaina nake son na Sani Amma kinki sanar dani, don haka KO yanzu. Bazan matsa Miki ba , duk ranar da kike ganin ta dace ki gaya min to Zan tsaya na saurareki da kunnan basira".

Haj murjanatu ta koma ta zauna tace " Zan gaya Miki alokacin daya dace " .
" Me zaki gaya Mata alokacin daya dace " muryar Alh Mustapha labaran ta tambaya lokaci daya Yana shigowa falon.

Gaba daya suka dube Shi , rai ahade Haj murjanatu tace " abinda ke tsakaninmu Wanda yake Haddasa mana ràshin jituwa alokuta da dama" .

Ya tsaya tsakiyar falon Yana yi Mata wani irin kallo Mai nuna alamun kinfi kowa iya ruko a duniya yace " tunda ke Abu baya wucewa agunki ba duk wañnan tsawon shekarun ace kin kasa mantawa tunda nake a duniya ban taba ganin mutum me ruko da Mita da ràshin mantuwa da yafiya ba irinki, sannan meye na tunanin zaki gaya ma mujaheeda wannan sirrin Wanda kinsan babu abinda zai Kara Mata sai damuwa , Amma idan kin zabi hakan kina iya gaya Mata komai".

Haj murjanatu tayi shuru zuciyarta na tafasa ranta Yana Kara baci , ji take kamar yanzu abin ya faru, wani irin tsanarsa ta cigaba da shiga cikin zuciyarta.

Ayayinda Kan mujaheeda ya daure ta Kara fadawa fagen tunani, shin meke tsakanin mummy da daddy tsawon lokaci sun kasa shawo Kan matsalarsu.

Ta dubi Àlh Mustapha labaran da shima ya hade rai gami da neman kujera ya zauna a kokarinsa na son kauda maganar ya dubi mujaheeda Yana kokarin kirkiro fara'a yace " yaushe kika zo gidan" itama tayi kokarin maida damuwarta tace " nadan Dade kadan" ya dubeta yace ' to yakamata ki shirya ki koma gidan mijinki , Kuma tahowa gida aduk lokacibekkv kike so baida amfani gidan mijinki shine fadarki ciki yakamata ki zauna kiyi Mulki ki Kula da mijinki da bukatunshi".

Haj murjanatu ta kauda Kai, mujaheeda tace cikin murmushi" to daddy ". Haj murjanatu tace " ranar litinin mujaheeda zata zamo manajan kamfanin sarrafa auduga".

Yayi saurin kallonta yace" aiki zatayi mujaheeda ".

Ta gyada Kai tace " eh". Cikin mamaki mujaheeda ta dubi Àlh Mustapha labaran tace " wai Dama Baka sani daddy ". Ya tsaida idonsa Akan nata yace " ta yaya zanyi na Sani mujaheeda bayan bani da mutunci ko kimar da zaa iya sanar da ni".

Haj murjanatu ta tabe Baki ba tare data CE uffan ba , mujaheeda ta juya tana kallonta tabbas da akwai yadda zatayi ta gyara tsakanin mahaifanta da tayi,

" Mujaheeda ki gaya min , shin da izinin mijinki zakiyi aiki KO kuwa ra' ayin mahaifiyarki ne"

Ta girgiza Kai tace " aah daddy yaya Taufiq ya amince da Kansa ya barni ".

Ya jinjina Kai yace " to Alhamdulillah, najidadi Allah yasa hakan shine mafi alheri , Allah Kuma ya Baki ikon yin dai dai" ta amsa da " Ameen" .

Daganan ya cigaba da fahimtar da ita kalubale dake cikin aikin mace da yadda dole zata kare mutuncinta a matsayin ta na matar aure,sosai mujaheeda tajidadin nasihohin Àlh Mustapha labaran domin duk abinda ya gaya Mata gaskiya ne.sai kusan karfe shida na yamma mujaheeda ta koma gida.

Kusan tare suka shiga get din gidan da Taufiq, ta rigashi tsaida mota ta fito tadan dube Shi sannan ta shige cikin gida.

Shuru Taufiq yayi acikin mota ya kasa fitowa maimakon hakama sai Kansa ya kifa ajikin sitiyarin motar, Yana maida ajiyar zuciya sai kace Wanda ya shiga gasar gudu.

Wai Anya kuwa mujaheeda ba kunnan Kashi gareta ba , ta yaya mace zata dinga fita ba tare da izinin mijinta ba, ya Lura Sam Sam mujaheeda bata San asa Mata Ido ba.anya bai hango kofar bullewa ba.

Gaba daya ji yake Yana neman ya Fara nadamar aurenta, kwata kwata yaji baya ko sha'awar shiga gidan.

Ya dade acikin motar kafin ya iya fitowa ya taka ahankali kamar Mai koyon tafiya ya shiga cikin gidan.

Ya tadda har mujaheeda ta kintsa ta canja Kaya tana zaune akujerar falo , Kan Dan karamin tebur din dake gabanta an cika Mata Shi da Kayan ciye ciye harda su cakulet.hannunta na rike da waya tana sana'ar dannawa kamar yadda ya Zama al' adar rayuwarta.

Tadan dago ta dubeshi ta danne fushinta domin dai ta Fara gajiya, tace " sannu da zuwa", ba tare daya dubeta ba yace " yauwa".

Har zai wuce daki Saiya tsaya ya dawo ya zauna Yana fuskantarta yace " daga ina kike?" Ta dan muskuta tace " daga gida nake, naje na kaima mummy files dinta na Kuma gaya Mata kamfanin Dana zaba zanyi aiki dashi"

Cikin fusata da daga murya yace " da izinin wa kika fita?".

Ta gigita da Jin tsawar daya daka Mata , cike da mamaki tace " yaya Taufiq ni kakema irin wannan tsawar kamar karya ".

Ya daga Mata hannu yace " tambayarki kawai nayi da izinin wa kika fita ,wai ke kinsan abinda kikeyi kuwa me kika dauki rayuwar aure ne, shin ma wai ni meye matsayina agunki? Da kuke kokarin maidani wani sakarai".

Kuka ta fashe dashi da karfi tana fadin " yau ni na shiga uku, na rantse wannan ba yaya Taufiq bane canja min Shi akayi"

Taufiq yace cikin daga murya "babu Wanda ya canjani illa ke , ya kike son nayi kowane magudanci baida buri agidansa daya wuce ya Sami kwanciyar hankali da natsuwa acikin iyalinsa , kwata kwata mujaheeda yaushe mukayi auren da zamu kasa mallakar farincikinmu kullum muna cikin damuwa akan me? Ki fita bada izinina ba , ki tilasta min yin abinda raina baya so , Baki San abinda Zan ci ko Zan sha ba dawainiyata tana wajen Yan aiki , bana fita da farinciki bana shigowa da farinciki gidan nan , Akan me?".

Kuka mujaheeda take yi da karfi sai kace wata karamar yarinya , hakan bausa Taufiq ya sakko ba illama haushi daya ke Kara kamashi.

Ya cigaba da fada " ni dama nasan mahaifiyarki ta kirkiro da maganar yin aikinki ne don kawai ta kawo baraka atsakaninmu Kuma ta samu hankalinta ya kwanta , Amma lalle na gaji bazan iya dauka ba"

Cikin fusata da hawaye tace " Kada Ka karasa mahaifiyata acikin maganarka, ni dai kamin Ka wulakantani yadda kake so nagode, na rantse da nasan haka zaka rikide min kamar hawainiya daban aurena ba, don kawai zanyi aiki shine zaka koma min haka, shin ko dai dagaske ne hassada da bakinciki kake yi min don baka son cigaba na".

Ya saki tsaki gami da mikewa tsaye Yana kallonta Rai a matukar bace yace " nine zanyi Miki hassada don zakiyi aiki, hmmm to kije kiyi aiki me yin aikin naki zai rageni dashi KO zai kare NI, Amma ina son ki sani bazan taba kwanciya Ku takani ba KO ku wulakantani ba, Zan rike kimata da darajata ta mijinki Kuma ya Zama dole ki bini " .yana Gama fadan haka ya tashi ya fada daki.

Mujaheeda ta Kara rushewa da kuka shin menene haka?. Bakinciki yakara kamata data tuna duk masu aikinta suna Jin wannan tijara da Taufiq yayi Mata .ya ci Mata mutunci tunda take aduniya babu Wanda ya taba tsayawa akanta yayi Mata fada irin wannan.

Shin ina matsalar take?, Tambayar da mujaheeda take fanan yima kanta kenan.

DAGA TASKAR YAR GIDAN IMAM

NIMA MATARSA CE
NA
HÀBIBA ABUBAKAR IMAM
(YAR GIDAN IMAM)
BABI NA GOMA SHA BIYU
****

Saboda tsabar bakinciki da damuwa a falo ranar mujaheeda ta kwana , shima Kuma ko da bata shigo dakin ba , bai sauke fushinsa ya lekota ba duk da shima ya kasa baccin juyi kawai yake yi.

Yana son mujaheeda matukar so, amma hakan baya nufin zai iya daukar shashancinta.

Da wuri ya tashi ya shirya zuwa lokacin mujaheeda ta shiga dakin domin itama ta yi sallah.

Ta dade Akan sallauarta tun da ta idar da sallah ta kasa tashi, maimakon hakama Saita kifa kanta asaman cinyoyinta hawaye na tsiyaya daga kwarmin idonta, ko Yaya ta tuna irin tsawa da fadan da Taufiq yayi mata sai taji wani irin kuna azuciyar ta.

Shi Kansa zuciyarsa ta raunana ,daya dubeta ya ganta takura akan sallaya kamar kayan

wanki, ko kwakkwaran motsi ba tayi.
Har zai fita ya ji ya kasa , ya Kara tsayawa yana kallonta.
Ahankali ya dawo yazo ya tsuguna agabanta. Ahankali ya Kira sunanta , da sauri ta daga kanta ,tayi mamakin ganinsa tsuguna kusa da ita, bata amsa ba illa Ido data dora masa tana Kara nazarinsa sosai.
" Wai meye damuwar ne?" Cewar Taufiq, ta maida kanta ta kwantar Akan kafafunta tana maida ajiyar zuciya ba tare data ce uffan ba.
Ya Kara kallonta bai damu da ràshin yin maganar ba ya cigaba da cewa, " bakya tunanin ya kamata mu kawo karshen wannan fitinar tun kafin tayi nisa ta zamar mana babban danasani" , ta yi kokarin daidaita muryarta tace " komai Yana hannunka ai, don ban san abinda ke cikin zuciyarka ba, amma daga abinda kayi min jiya na tabbatar da cewa ayanzu baka Sona, ba Ka kallona da mutunci ko girmamawa, Bana Jin Kuma Zan taba manta abinda kayi min, meye laifina? Wanda ko kuskuren nayi ba zaka yimin nasiha da kyakkyawan lafazi ba Saita kakkausan lafazi," ta Karasa magana tana cigaba da kuka sosai.
Hakan ya Kara sanyaya guiwar Taufiq, sisai yaji bai kyauta ba, tabbas nasiha ya kamata yayi Mata amma fushi ya rinjayi tunaninsa.
Ya dubi agogon dake daure a tsintsiyar hsnnunsa, lokaci ya tafi babu lokacin dazai zauna ayanzu ya warware matsalar dake tsakaninsu, don haka ya dubeta yace " naso muyi magana amma yin hakan zai iya sawa nayi latti , don haka kiyi hakuri idan na dawo za muyi magana ", batace komai ba harya tashi ya fice tabi bayan sa da kallo, Allah ya dora mata son Taufiq fiye da tunanin me tunani , to Kuma ta yaya zamansu zai tafi ahaka, ita kanta tana son ta gane laifinta , Amma daga irin maganganun daya gaya mata jiya tabbas tasan akwai inda ta gaza , Amma koma dai menene zata jira harya dawo domin su warware matsalarsu.

Haka mujaheeda ta zauna cikin ràshin walwala , ko masu aikinta ta kasa hada ido dasu saboda kunyar abinda Taufiq ysyi mata wanda tasan duk sun ji da kunnansu. Idanunta kuwa har kumbura sukayi saboda kuka . Haj murjanatu ta kirata sama da sau hudu ta kasa daga kiranta saboda bata so ko kadan taji wani sauyi a muryarta.
Ràshin daga Kiran kuwa bakaramin tayar da hankalin Haj murjanatu yayi ba, ta kasa jurewa haka ta aje komai direba ya dakkota ya kawota gidan mujaheeda, Wanda da mujaheeda tasan zata zo data daga Kiran nata don bata so tazo ta ganta acikin yanayin da take ciki ba .
Tana kwance Kan doguwar kujera a falo, har zuwa lokacin bata yi wanka ba, kusa da ita ta zauna ta janyota tana yi Mata kallon tsaf, tace " innalillahi wainna' ilaihirrajiun, mujaheeda menene? Meya sameki idanunki suka kumbura da kuka".
Mujaheeda ta kasa tsaida hawayenta maimakon hakama Saita kara fashewa da kuka .
Tashin hankali nan da nan Haj murjanatu ta kara gigicewa komai na duniyar ya tsaya Mata cak! Wani irin gululun bakinciki ya tokare kirjinta duk da sanyin da akeyi ji tayi zufa na tsiyayo Mata saboda tsabar tashin hankali.
Ta kwantar da ita Akan jikinta tana shafa bayanta , tun kafin tasan damuwar yarta hawaye itama ya Fara fita daga idanunta
" Mujaheeda waye ya bata Miki ki gaya min na rantse ko waye sai yayi nadama da danasani arayuwarsa". Mujaheeda ta girgiza Kai tace " aah mummy kada kice zakiyi komai don Allah " ta girgiza Kai tace " Kada ki rokeni abinda bazan iya yi Miki ba ,kece sanyin idaniysta Bani da wani

farinciki sama da naki , Bani da Uwa Bani da uba bani da wasu shakikan yan'uwa mujaheeda ke kadai gareni , na rantse babu wanda ya isa ya taba min farincikinki da kwanciyar hankalin ki ya wanye lafiya ko waye, don haka ki gaya min meya faru ".

Ahankali cikin kuka, mujaheeda ta gama sanar da mahaifiyarta duk abinda ya faru tsakaninta da Taufiq bayan dawowarta jiya daga gida.

Ta Kara da cewa " mummy bana son abinda ke faruwa atsakaninsu da yaya Taufiq saboda haka ina ganin Zan hakura da aikin nan kawai, matukar zai samu natsuwa da hakan".

Haj murjanatu tace cikin fusata " Taufiq ysyi kuskuren taba min ke , Kuma sai yayi danasani aiki Kuma sai kinyi KO zai mutu ko zaiyi rai idan Kuma Yana ganin Shi wata tsiyace to auren ma ina iya datse igiyar".

Ta dago da sauri tace " aah mummy, idan wani abu ya sami aurena bazan iya jura ba, kamar yadda nake son kiyi hakuri Kada ki dau kowane irin mataki akan Taufiq, saboda Shi Kansa da alamar yaji ba dadi don yace idan ys dawo office zamuyi magana mu warware matsalar "

Ta yi Mata kallon Baki da hankali sannan tace " yanzu kina nufin na rungume hannu nasama Taufiq Ido Yana wulakanta min ke Akan wani dalili, wannan dalilin Yana daya daga cikin abinda yasa banso kika aure Shi ba don nasan zuciyar talaka bata da tunanin alheri Akan Mai kudi duk yadda me kudi yake da talaka sai talaka ya nuna masa halin hassada da tsana, don haka dole Zan ganar da Taufiq kuskurensa".

Mujaheeda ta tashi ta kama hannun Haj murjanatu tana rokonta " don Allah mummy kada ki shiga wannan maganar, domin hakan Kara wutar rigimar kawai zaiyi, ni Kuma na sike bazan iya cigaba da yin fadan nan ba " damuwa ta Kara kama Haj murjanatu tace ": don Allah ki Sami natsuwa mujaheeda kada ciwonki ya tashi " ta girgiza Kai tace " bazai tashi ba mummy, amma don Allah Kada ki shiga maganar nan , don gaba daya Taufiq ya canja " tace " dole ya canja mana tunda ya riga ya sameki, don haka naji bazan yi masa abinda nayi niyya ba Amma ya Zama dole nayi masa magana don bazan lamunci wannan wautar ba ".

Sosai Haj murjanatu ta cigaba da fada bacin ranta ya bayyana sosai. A Karo da dama tsanar Taufiq ta Kara kama zuciyarta.

Ta dade tana kwantar ma da mujaheeda hankali bata bar gidan ba saida ta tabbatar mujaheeda ta Sami natsuwa, tayi wanka ta gyara kanta da kanta ta bata abinci a baki taci ta koshi, sannan tayi sallama da ita tabar gidan.

Tana fita kai tsaye gidansu Taufiq ta wuce , batayi sa'ar tarar da Àlh Yusuf lamido ba, sai Haj saratu da Haj Bilkisu wacce bata Dade da zuwa gidan ba.

Fusatar da Haj murjanatu take ciki yasa ta kasa dakatar da kanta daga fadan duk abinda ke cikin ranta.

" Kiyi hakuri ki zauna Haj muyi magana" cewar Haj saratu , Haj murjanatu tace " babu amfanin zamana don bashi ya kawoni ba, kawai ina son ki jama danki kunnene na rantse bazan yarda da kokarin wulakanta Yata da yake yi ba, ta ko wace fuska yata ta fishi sau babu adadi, don kawai zata yi aiki sai ya dauki kahon zuka ya dora Mata saboda tsabar hassada irin na talaka" ta dubi Haj saratu sosai wacce daga ita har Haj Bilkisu suka kura mata Ido suna kallon hayagagar masifar da take yi.

Ta cigaba da cewa " to ko tayi aiki ko batayi aiki ba, Taufiq ya sani ta fishi komai , ta fishi kudi duk abinda yake tunani ta kereshi don haka garama yayi hakuri yabar min ya Tasha ruwa don duk ranar da na Kara ganin hawaye a'idon Yata adalilinsa sai inda karfina ya kare don haka ki

gaya masa ya shiga taitayinsa, babu wani talaka dazan yarda ya wulakanta min ya don kawai Yana aurenta".

Cikin bacin rai Haj Bilkisu ta Bude baki zatayi maida ma Haj murjanatu da martani , Amma sai Haj saratu ta katseta ta hanyar dakatar da ita . Hakan yasa har Haj murjanatu ta gama cin karenta babu babbaka babu Wanda ya maida Mata magana .
Saida ta gama fadin duk abinda ke ranta sannan ta tafi .
Haj Bilkisu ta koma ta kwantar da bayanta ajikin kujera tana runtse idanunta, tace " Kai umma gaskiya Taufiq Yana bani tausayi, daga dukkan alamu bazai taba Samun farincikin auren mujaheeda ba ," Haj saratu ta numfasa cike da damuwa itama tace " hmmm ai Taufiq sai dai mu tayashi da addua amma akwai matsala, yanzu ki duba kiga yadda take masifa ko bata hada komai damu ba ta zauna tana wannan masifar sai kace kashe yar akayi , ganin hawayen ta kadai nefa ya janyo take wannan jarabar " Haj Bilkisu tace " gaskiya Taufiq baiyi saa ba, Allah ya daidaita tsakaninsu tunda dai shine ya tattagoma Kansa wannan jidalin".
Duk wañnan balain da Haj murjanatu tayi agidansu Taufiq baisa zuciyarta ta Sami sassauci daga bakincikin da Taufiq ya sanyata ciki ba, tana bayan Mota ta fito da waya ta Kira Taufiq bugu daya acikin na biyu ta dauka.
Zai gaida ta tayi saurin katse Shi, " Kai Taufiq ina son kayi gaggawar dawowa hayyacinka kasani bazan yarda Ka dinga cima yata zarafi ba don kawai ta zabeka ta aureka , tunda Kai butulu ne Mai manta mafari, ni Dama baka taba burgeni ba kamar yadda ban taba shaawar Ka aureta ba don dama nasan babu abinda zata tsinta agidanka sai bakinciki" shuru kawai yayi Yana sauraron maganganunta masu kama da saukar aradu akansa.
" Aiki mujaheeda sai tayi ko da Shi zai Zama sanadiyyar mutuwar aurenku" ananne yace " AI dama ban hanata ba taje tayi aikinta" ta saki tsaki tace " kama Hana mana , matukar hawayen mujaheeda ya Kara fita a sanadiyyar Ka sai kayi mamaki matuka don zaka gane shsyi ruwana, idan Ka fasa wulakanta mujaheeda da sata kuka baka haifu ba" tana Gama fadan hakan ta kashe wayarta tana tsaki.
Taufiq yayi kasa da wayarsa gami da rike Kansa hannu bibbiyu Yana aje ajiyar zuciya.
Yanzu mujaheeda ko yayane ba zata iya rike sirrin gidansa ba dole Saita fito ta watsa musamman ga mahaifiyarta wacce tafi kowa sanin ba sonsa take ba Amma taje tana fadin abinda tasan sai dai ya kara ruruta wutar kiyayya atsakaninsa da surikarsa shin me yasa mujaheeda tayi garajen sanar da Haj murjanatu bayan ya tabbatar Mata cewa idan ya dawo office zasu zauna su warware matsalarsu da Kansu.
Karar da wayarsa ta shiga yi shine ya katse masa tunaninsa, ganin number mahaifiyarsa yasa yayi saurin dauka, bayan ya gaisheta ne , Haj saratu tace " kana office ne ko ka koma gida ne".ya girgiza Kai tamkar tana ganinsa yace " ina office umma". Tadan numfasa tace " Taufiq meke faruwa tsakaninka da matarka, da har Haj murjanatu ta Sami damar zuwa gidana tayi tijara da wulakancin ta yadda take so, yanzu bayan fitinar daka ke ciki muma dole sai mun shiga ciki Kai baka jindadi ba mu bamu jidadi ba Akan wane dalili" a gaggauce yace " tazo gida" tace " ya wuce wai, Kai yanzu a matsayin Ka na namiji ba zaka iya Samun sabani da matarka Ku zauna Ku warware komai tsakaninku ba dole sai kun saka wasu atsakiyar damuwarku, to ina son kasani zaman aure ba haka yake ba magana ce ta rufa asirin juna tare da kauda Kai akan laifukan juna , sannan Mita da Jan magana babbar illace azaman aure duk yadda zaayi Kada

Ka bari kuyi Nisan fada Wanda zai dauki lokaci Baku sasamta ba don gwargwadon dadewar shiryawarku gwargwadon yadda zaku dinga fitama juna arai".

Sosai ya tsaya Yana sauraron nasihohin mahaifiyarsa Wanda ta Dade Akan wayar kafin ta aje.

Taufiq yaji zafin yadda Haj murjanatu taje har gidansu tayi abinda ranta yake so Wanda bai dora kefin Kan kowa ba sai Kan mujaheeda don badon ta fada Mata halinda take ciki ba duk da hakan Bai kasance ba.

Haka ya cigaba da Zama a office cikin damuwa da tunanin yadda zai bullo ma lamarin da yake neman ya Kure tunaninsa.

DAGA TASKAR YAR GIDAN IMAM

NIMA MATARSA CE
NA
HÀBIBA ABUBAKAR IMAM
(YAR GIDAN IMAM)
BABI NA GOMA SHA UKU

****

Bayan komawar Taufiq gida, yayi kokarin boye bacin ransa musamman yadda yaga mujaheeda har zuwa lokacin bata dawo yadda take ba.

Saida daddare bayan Taufiq ya gama komai na al'adar rayuwarsa yazo kwanciya .

Lokacin mujaheeda itama tayi Shirin kwanciya tana gefen gadon a zauna.

Alokacin ne Taufiq ya Kira sunanta, ta amsa ahankali, sannan yace " mujaheeda me yasa kika sanar da mahaifiyarki abinda yafaru tsakaninmu, bayan kinfi kowa sanin cewa idan kowa zai iya yimin Uzuri to banda ita, idan har kina son ni da mahaifiyarki mu samu kyakkyawan alaka Bai kamata ki dinga kokarin Kara tura Mata tsanata ba bayan tsanar data riga tayi min".

Mujaheeda ta girgiza Kai tace, " ni ban gaya Mata komai ba,", ya waigo Yana kallonta yace " to ta yaya ta sani idan har ba ke kika gaya Mata ba" ta gyara zamanta tace " gidan ta zo ta Kuma taddani a halinda dole zata San ina cikin damuwa da matsala, hakan yasa ta matsa min har saida na gaya Mata abinda yafaru". Ya girgiza Kai yace " mujaheeda na aureki ne don ina sonki , ba Kuma na fatan ace awayi gari na daina sonki , don haka ina son kisani ya Zama dole ki gane cewa aure kikeyi don haka dole ki dinga yin abinda zai dinga nuna ke matar auren ce, haka zalika ya Zama dole ki mutuntani ki girmama ni a matsayina na mijinki", ta gyada Kai tace " naji" ya Kara kallonta yace " Abinda Haj ta je ta aikata agidanmu da irin maganganun data kirani awaya ta gaya min sun bata mun rai, Amma duk abar maganar nan komai ya wuce bana son bacin rai da tashin hankali, kije kiyi aikinki Amma ki tabbatar kin tsare kanki kin katange kanki daga dukkan abinda zai biyo baya ki Kuma sani ke matar aure ce ".

Tadan dubeshi tace " Nagode insha'Allah Kuma Zan kiyaye ". To awannan dare dai komai ya dawo dai dai tsakanin Taufiq da mujaheeda.

****

Ranar litinin mujaheeda ta Fara zuwa aiki duk abinda yakamata Haj murjanatu ta yi tayi mujaheeda ta hau kujerar manaja ayayinda Àlh jibrin ya koma mataimakinta Wanda hakan ba karamin bata masa rai yayi ba , sai dai ya danne bai nuna ba, amma zuciyarsa har kuna take, ta yaya za'ayi ace aba yarinya karama irin wannan babban mukamin Wanda ko babba saiya dage,

shin mema tasani Akan aikin .

Karfe goma shabiyu na dare ne , Alh Mustapha labaran Yana zaune atsakiyar gado Haj murjanatu tana zaune a bakin gadon gaba dayansu fuskokinsu babu alamun kwanciyar hankali, Àlh Mustapha labaran ya cigaba da magana wacce da alama ya dade Yana yinta." Tsawon wannan shekarun kinsa abu a ranki kin aje kin kasa yafe min kin Kuma kasa mantawa, kina hango katuwar illar da hakan ya janyoma aurenmu?, Kin kasa Kara yarda Dani kin fahimci bakincikin da zuciyata take ciki kuwa!".

Ta waiwayo tana kallonsa zuciyarta na dawo Mata da munanan abubuwan da suka faru shekaru masu yawa da suka wuce, Wanda harta koma ga Allah bazata taba mantawa ba . Tace " Kai yanzu kana tunanin Zan iya manta abinda kayi min ko na yafe maka , aah asalima duk tsawon wadannan shekarun babu ranar da zata zo ta wuce ban tuna bakin halinka ba , shiyasa kullum Muke nesa da juna , na zabi na cigaba da zaman aure da Kai cikin ràshin yarda da nuna kauna".

Ya dubeta sosai yace " yanzu dai kina nufin ba zaki manta ki hakura ba mu karasa cikin mutuntawa da ganin kimar juna ba ".

Tayi shuru kawai ta maida kanta kasa ya cigaba da cewa " meye acikin rayuwar da yafiya zata zamo me wahala, to Allah ya sani nayi lefi na nemi gafarar Allah sannan na nemi gafarar ki Amma kinki to kisani ko awajen Allah bani da lefi idan ke baki yafe min ba to Shi ya yafe min, tunda ke bakar zuciya kike da ita".

Bata ce uffan ba ta tashi ta shige bandaki.zuciyarta cike da tunani Kala Kala.halinda take ciki Yana daya daga cikin dalilin dayasa take son ta kare mujaheeda daga fadawa kunci da cin amanar namiji Kuma duk yadda zatayi zatayi domin ganin hakan ya kasance, domin ko kadan bata son yarta ta dandani daci da tashin hankalin data dandana arayuwarta.

****

A can kauyen Durmi ta jahar jigawa, kauye ne da bai mallaki komai ba na game da ababen more rayuwa ba , kauye ne Wanda Baisan akwai wata Kalma ba wai ita romon dimukuradiyya, domin kuwa basu da hanya ba su da asibitici basu da makarantu basu da komai na jindadin rayuwa.

Acikin wani matsakaicin gida na kasa Wanda ko kofar kirki babu domin dai galan galan akasa aka sakaya kofar da ita.

Kwata kwata dakuna uku ne agidan Suma kanana ne sosai yadda babu wani wajen walawa, Sai garken jajayen awakai atsakar gidan guda uku. Tsakar gidan kuwa babu komai sai gurbayar kasa , atakaice dai gidane daka kalla zaka tabbatar cewa gidan takakawa ne kwarai da gaske wadanda Basu fi karfin komai ba na bukatun rayuwa.

Ande Dije ce zaune Akan dutsen data Saba Zama akai kusa da dabbobinta ta cika ta batse kamar atabata ta fashe .

Dai dai lokacin Hajara ta fito daga daki rike da tsintsiya da alamar Shara zatayi, Ande Dije ta watsa Mata harara ta Fara maganganun da tunda ta zauna take yinsu sai dai idan ta gaji tayi shuru.

" Ai dole tunda ta riga ta tsotsa a nono Saita nuna ita wacece barewa zatayi gudu ne danta yayi rarrafe ni dai Allah ya dora mana masifa da ni da dana bansan Kuma ranar da zai yaye mana ba".

Kamar koyaushe idan Ande Dije tana irin wadannan mugayen maganganun nata Hajara takan ji tamkar zuciyarta zata fita waje saboda bakinciki, tasan idan da sabo yakamata ta Saba amma da yske baa sabo da bakinciki yasa kullum abin yake sabo agareta .

Bata tanka ba kamar kullum, maimakon hakama Saita Fara share tsakar gidan Wanda hakan baisa Ande Dije tayi shuru ba ta cigaba da maganganunta " shegiyar yarinya kamar taci kafar kare dazaran ta fita sai anganta, waye yasan abinda take aikatawa awajen tunda baayi gadon kamun Kai ba".

Tana rufe baki, wata kyakkyawar yarinya wacce bata wuce shekaru goma sha takwas ba ta yi sallama cikin Kamala ta shigo gidan, wankan tarwada ce me cikar fuska da dogon hanci tana da matukar kyau na daukar hankali, kamar yadda Allah ya kawatata da diri kwarai .

"Inna sannu da gida" ta fada cike da nutsuwa , cike da fara'a tace " yauwa muhseena , kin Samo ruwan", ta wuce Kai tsaye wajen duron da take Tara ruwan , bata damu da irin mugun kallon da Ande Dije take watsa Mata ba tace " na Samo Inna daker , mutane sunyi yawa wannan ràshin ruwa dai ya Zama masifa".

" Ko kuma kece kika zamo masifar ba, fitinanniyar yarinya wacce bata huce takaici awa nawa da fitarki Amma ace sai yanzu zaki dawo saboda kin Zama ballagaza baki jindadin komai sai yawo ai da kinyi zamanki baki dawo ba kila da hakan yafi mana kwanciyar hankali".

Muhseena ta juye ruwan acikin roba gami da maida bayanta ta jingina jikin garu ta runtse idonta, ta Dade bata ga tsana irin wacce Ande Dije take mata ba , duk kokarin da zatayi ba ta taba gani ba sai dai taga gazawarta,

Ande Dije ta cigaba da fadan duk abinda ya fito daga bakinta Kaida gani kasan dama can tana Jira ne. Zuciyar Haja data muhseena sai tukuki take Sam Sam Hajara bata son ta tanka Mata ko muhseena ta tanka Mata hakan yasa ta aje tsintsiyar hannunta ta dubi muhseena tace " wuce daki", ba tare da cewa uffan ba ta maida bokitin ta aje ta juya ta shige daki Hajara ta bi bayanta.Aysyinda Ande Dije ta cigaba jaraba sai kace wacce akayi ma wani gagarumin laifi.

Kan yar siririyar katifar dake yashe asaman dakin me kama da harshe Hajara ta zauna, yayinda muhseena ta jingina jikin bango ta runtse idanunta ta kasa tsaida hawayenta da suka Fara malala asaman kumatunta .

Cikin matsananciyar damuwa Hajara tace " kiyi hakuri wannan jarfta ce, ina son ki sani ko wane bawa da irin jaraftar da Allah yake Dora masa , to mu dauka daga ni har ke wannan itace jarabawarmu ".

Muhseena ta bude idonta hawaye na fita tace " jarabawa kuwa mummunar jarabawa Inna , na rantse Miki lokuta da dama nakan ji ina ma Allah ya dauki raina saboda Bana Jin Zan cigaba da jurar wannan masifar ba tare da wata Rana zuciyata ta buga ba, Inna ina cikin matukar damuwa , ina cikin damuwa" ta Kara rushewa da kuka Mai cike da ban tausayi ta zame kasa ta zauna dirshan tana cigaba da kuka sosai Mai taba zuciya .

Hakan yasa itama Hajara ta Fara zubar da hawaye, tana fadin " kiyi hakuri muhseena,kiyi hakuri".

Tace cikin kuka " Inna ba maganar nayi hakuri bane , mummunar maganar da ake jifana da ita agari da wacce ake jifana agidan da yake matsayin gidanmu, sun isa su tarwatsa min duk wani

farincikina balle ma Bani da farincikin , Inna babu me Sona , babu namijin dake son ya nemi aurena asalima aga mun tsaya ko da da gaisuwa babu namijin daya ke son haka, Inna meye laifina".

Ta girgiza Kai tace " Baki da laifi muhseena Sam Sam Baki da lefi".

Tace " to Inna Ki cireni a dubu ki warware min komai ki gaya min gaskiya ko da hakan zai Zama sanadiyyar mutuwata , ki gaya min gaskiyar maganar da ake yadawa akaina".

Ta daga Mata hannu tace " na gaya Miki ki daina min tambayar nan domin tana durkusar da guiwata tana lalata tunanina tana Kuma jefani cikin mummunan yanayi, ki rabu dasu duk Wanda zai fada abinda yake so ysyi ta fada, tsawon shekarun nan ahaka Muke babu wani abu dazai wanke mu "

Muhseena tace " akwai mana Inna" ta dubeta tace " menene Shi" mujaheeda tace " gaskiya Inna , ita kadai zata wanke mu ki yi hakuri ki gaya min gaskiyar wacece ni don Allah Inna".

Gaban Hajara yayi mummunar faduwa ta waigo ta zubama gudar jininta Ido, shin me zata gaya Mata ta gamsar da ita wace gaskiya gareta da zata Kara yi Mata ado ta gaya ma muhseena.

DAGA TASKAR YAR GIDAN IMAM

NIMA MATARSA CE
NA
HÀBIBA ABUBAKAR IMAM
(YAR GIDAN IMAM)
BABI NA GOMA SHA HUDU
****

Hajara ta Kara kallon yarta cikin matukar tausayawa, tace " na rokeki muhseena kibar wannan maganar, kamar kullum bazan gaji da gaya Miki ki dauke kanki daga Jin maganganun mutane ba, komai lokacine ranar da duk lokacin aurenki yayi babu makawa Allah zai baki Mijin da zaki aura, don haka don Allah ki sama kanki hakuri da dangana duk abinda kike ji nima ina ji tashin hankalin da kike ciki na shiga Wanda ya fishi ina Kuma ciki har yanzu,

Ke kadaice sanyin idaniyata, saboda ke kadai kawai nake rayuwa idan Kuma kikace zakisa kanki acikin irin wannan yanayin to yaya kike son nayi da Kaina ."

Muhseena tasa hannu tana share hawayenta , shin ta yaya zata fahimtar da mahaifiyata cewa duk duniya babu abinda take bukata sama da amsar tambayar da tayi Mata, shin wacece ita? Meyasa ake jifanta da mummunar Kalmar da ta gurbata rayuwarta?, Meyasa mutane suke kyamatarta.

" Idan kun gama zaman dakin Al sai Ki fito ki daukar min tallan goron , idan Kuma bakincikin ne ya motsa irin na uwarki sai kibarni da kayana".

Hajara ta Kara kallon muhseena kallo me cike da tausayi tace " kiyi hakuri ki tashi kije ki daukar Mata goron, kafin ta maida abin babban al'amari, kinsan dai halinta Sarai ,".

Muhseena ta jinjina Kai tace " toh", daganan ta Mike ta wuce wajen ledar kayanta ta bude ta dakko dogon hijabinta har kasa Wanda Shi kenan Mata gaba da baya. Ta cire gelen jikinta ta

maida hijabin tasa gami da Kara goge hawayenta sosai, ta dubi màhaifiyarta cike da tausayawa da kauna tace " na tafu Inna".

Ta gyada Kai tace " Allah ya bada sa'a Allah ya tsare ki, ki kula don Allah", tace tana kokarin fita " Amin , insha'Allah Zan Kula".

Fitarta wani kuka Mai karfi ya Kara kwacema Hajara, hakika tana daya daga cikin Matan da basuyi sa'ar zuwa duniya ba, irin bakaken abubuwan da suka faru da ita arayuwa Abu ne Wanda ya Zama babban kalubale agareta, tun faruwar al'amarin bata Kara riskar farinciki ba, rayuwa kawai take amma bata San inda ta dosa ba.

Muhseena tana fita da farantin goro akanta , sukayi kacibis da babanta mallam Umar , ya tsaya Yana kallonta harta karaso tana gaidashi, yace " muhseena, Bana ce na hana tallar nan ba , meyasa kika dauka", tace " Ande Dije ba zata bari ba , dole na dauka matukar ina son Zaman lafiya agidan".

Yayi shuru Yana Jin ràshin dadi acikin ransa, ya dubeta yace " jeki" Kai kawai ta gyada ta wuce ta tafi ayayinda ya bita da kallo cike da zargin Kansa na ràshin sauke nauyin da ke Kansa Akan mujaheeda, baya jindadin yadda mahaifiyarsa ta dau kahon zuka ta Dora Mata ya rasa yadda zaiyi da ita ko ya shawo kanta ta daina nuna kiyayyarta ga muhseena.

Adamuwa ya shiga gidan har zuwa lokacin Ande Dije tana zaune awajen zamanta, lokacin Hajara ta fito ta cigaba da shararta.

"Sannu da dawowa" cewar Hajara ya amsa Yana kallonta cike da kulawa yace " yauwa Hajara ya gidan" tace " lafiya lau". Ande Dije ta saki tsaki tace " shashanci kayi ta lelen Mata sai kace akanka aka fara aure, Ka Zama shanyayye Baka da wani abu agabanka sai Hajara".

Ya Matso kusa da ita yace ," haba Ande meya kawo wannan maganar Kuma, don Allah ki dinga hakuri" ta watsa masa harara tace " Anki a dinga hakurin, nace Anki a dinga hakurin , tunda ni babu damar na yi maganar gaskiya sai kace wai na dinga hakuri tunda dama Bani da hakuri ko".

Ya durkusa kusa da ita cike da girmamawa yace " Ande don Allah ina rokonki kamar yadda nake rokonki kullum ki cire abinda ke ranki agame da Hajara da yata muhseena," ta watsa masa harara tace " yarka aina, kadaina wannan maganar kadai cigaba da rukon wahala Amma har kullum ina gaya maka Ka daina alakanta kanka da muhseena".

A gaggauce Hajara ta gama kwashe shararta, tayi saurin shiga daki jikinta na rawa kanta na Sarawa, ta koma Kan katifa ta zauna gami da takurewa.kukanta ya dawo sabo.

Komawarta daki yasa Mallam Umar ya Kara Jin ràshin dadi atare dashi, ya numfasa yace " Ande kamar fa yadda kike ganin nayima Hajara halacci na taimaketa hakanan nima Hajara tayi min halacci ta Kuma taimaka min kema kinsan haka ba Kuma zamu taba mantawa ba, don haka ni duk banga dalilin wannan abubuwan ba, shekara da shekaru ana aikin abu daya ko yayane dai zuwa yanzu aiya kamata ki sakko ki rungumi Hajara da muhseena amatsayin naki,".

Ande Dije ta Kara sakin tsaki tace " halaccin daka Mata aiyafi Wanda ta maka to ma har wane halacci tayi maka, har abada bazan taba son Hajara ba balle yarta" ya kama Kansa ya rike Yana jujjuyawa yace " saboda me Ande don me ba zaki iya sonsu ba ,bayan dimbin girmamawa da mutuntawa da suke Miki da Kuma yi Miki duk abinda kike so cikin ràshin nuna

kosawa, don Allah Ande ki sassauta musu ko don su Sami natsuwa "

" Bazan sassauta ba, duk abinda zaka fada kaje kayi ta fada".

Yasan kafiyar mahaifiyarsa da ràshin daukar shawara , don irin wannan maganar yayi tafi dubu da ita aiya tsawon shekarun da aka kwashe.

Ya nisa yace " to shikenan, Amma ina ganin lokaci yayi da ya dace ace kin daina dorama muhseena talla saboda tayi girma KO wane lokaci muna iya aurar da ita akalla zuwa yanzu yakamata ace ta Sami nutsuwa waje daya".

Tayi masa kallon tsaf tace " waye zai aureta? Waye kake tsammanin zai iya hada jibi da mummunan tsatso ko kuwa tunda kake tunda muhseena tayi girman tsayawa da samari Ka taba ganin anyi sallama da ita, babu me son hada zuria da ita, don haka idan saboda wannan dalilin kake son na daina dora Mata talla to bazan daina ba talla yanzu na Fara Dora Mata , Koko, kunu, Dan wake , goro Kai komai Naga damar dora Mata aciki Zan dora Mata tunda duk tana dauka don haka ki shiga taitayinka Ka fita harkata".

Mallam. Umar ya yunkura ya tashi domin dai yayi Imanin cewa Ande Dije ba zata taba sauraron sa ba ballefa ta taimakeshi tayi abinda kullum yake rokonta tayi masa.

Asanyaye ya wuce dakin Hajara ayayinda Ande Dije ta cigaba da maganganunta marasà dadi daga bisani itama ta tashi ta kakkabe zaninta ta shige dakinta.

Hajara tana zaune inda take hawaye take sosai, ya tsaya Yana kallonta cike da matsananciyar damuwa ya zuba Mata Ido, Yana matukar Sonta amma yakasa bata farinciki ko daya arayuwarta.

Ya danyi gyaran murya yace " nasha gaya miki kuka babu abinda zaiyi Miki bazai cire Miki damuwa ba sai dai ma ya Kara Miki ràshin nutsuwa kila Kuma ma har ya taba Miki lafiya, nasan babu dadi da zafi Kuma an dade anayi , ko yayane yakamata ace an rage wani abun ko baa daina Duka ba, Amma na rasa yadda zanyi na Gaza Hajara nagaza ki yafe min".

Hajara ta goge hawayenta tace " kadaina zargin kanka mallam, nasan da kana da yadda zakayi Ka hana abinda yake faruwa faruwa da tuni kayi , nasan Kuma kayi iya bakin kokarinka haka zalika Kai ubane Nagari ga muhseena Bani da haufi Akan irin son da kake Mata idan Kuma da ace abubuwa hannunka suke da duk hakan Bai kasance ba".

Ya numfasa yace " hakane Hajara Allah ya sani ina kaunarku ina kwadayin na Baku farinciki amma Bani da yadda zanyi ina da rauni"

Hajara ta jinjina Kai tace " nasani don haka Ka daina damun kanka , idan da sabo ai mun Saba sa halin Ande ".

Yace " akullum ina adduar Allah yaba muhseena miji nagari tayi aurenta ko ta huta da irin wannan rayuwar da babu abinda take bata sai damuwa da tashin hankali ". Ta daga hannayenta sama tace " Amin ya Allah nima shine burina kullum Kuma itace adduata".

Mallam Umar yace " baa Sami komai an sarrafa agidan ba ko"

Ta girgiza Kai tace " gari nadan samu na jikama muhseena Tasha saboda zata tafi bin layin ruwa nasan Kuma zata Dade hakan yasa na bàta Tasha" ya girgiza Kai yace cike da damuwa " kiyi hakuri, bari na Kara fita insha'Allah Zan Samo abinda zaa ci" tace " Allah ya bada saa, Allah yasa a Samo halal",

Daga waje bakin kofa muryar Ande Dije ta amshe maganar "ko haram din ne ma ya zaayi ya

samu bayan Yana tare da karfa"

Hannu ya dagama Hajara alamar Yana bata hakuri sannan ya wuce ya fita ya wuce Ande Dije tana kaiwa da komowa atsakar gida yace " Na fita" tace " adawo lafiya kasani kuma yunwa nake ji matuka" yace " Allah zai bada yadda zaayi " ya karasa magana Yana ficewa da sauri.

****

Karfe takwas saura minti hudu na dare, mujaheeda ta tsaida motarta a harabar gidan . Cikin gajiya ta shiga gida.

Taufiq na zaune a falo Yana kallo da alama Shi ya Dade da dawowa gidan, ya dago yayi Mata kallon tsaf ya raina guntun gelen dake jikinta ahankali ya dauke Kansa akanta.

Ta fada Kan kujera tana maida numfashi, tana fadin " Ashe kadawo" yace ba tare daya kalleta ba " tun karfe shida da rabi ni INA gida, aida alamu aikinki yafi nawa yawa, idan akayi laakari da irin lokacin da kike dawowa gidan kwana biyun nan".

Sautin maganarsa Yana fitar da ràshin jindadin abinda yake magana akai.ta dubeshi sosai tace " kasan karshen shekara aiki Yana cushewa to abinda ke faruwa kenan yanzu aikin yayi yawa" ya Dan gyara zamansa yace " amatsayinki na shugabar kamfanin kina da damar da zaki je office sanda kike so ki Kuma tashi sanda kike so meye na kokarin tskurama kanki ki Kuma takura ma wani, meye amfanin ki dinga dawowa gida da daddare ko a karkashin wani kike aiki amatsayinki na mace ai kya dinga kokarin dawowa gida Akan lokaci".

Ta yaye gelenta ta aje akusa da ita tace " idan har kana ganin don ina shugabar kamfani bai kamata na maida hankali Akan aikin ba da Kuma cigaban kamfanin ba to hakan ba dai dai bane, domin ya Zama dole na maida hankali na Kuma dage domin ganin na ciyar da kamfanin nan gaba"

Taufiq ya girgiza Kai yace " gidanki da mijinki sune Abu na farko da zakisa agaba kafin komai , Amma fa bance dole ba kina iya zaben aikinki fiye da komai Wanda Naga kamar hakan kika zaba".

Mujaheeda tayi shuru tana nazarin maganarsa data Fara fahimtar tamkar abin ya na taba Taufiq, bata son damuwa domin kwana biyu abubuwa sunyi sauki bata bukatar ko kadan wani sabanin ya shiga tsakaninsu.

DAGA TASKAR YAR GIDAN IMAM

NIMA MATARSA CE
NA
HÀBIBA ABUBAKAR IMAM
(YAR GIDAN IMAM)
BABI NA GOMA SHA BIYAR

****

Mujaheeda ta dan kara dubansa tace " don Allah Kada Ka sama ranka wani abu harga Allah bani da nufin na kuntata maka illa iyaka ina son na maida hankali Kan abinda ya shafi kamfanin nan saboda akwai matsaloli da yawa kwance acikinsa,".

Kai kawai ya maida kasa ba tare daya Ce komai ba, domin kuwa bai son Jan maganar itama

fahimtar hakan da tayi ne yasa ta tattara ta tashi ta shige daki domin ta gyara kanta.
Ayayinda Taufiq ya fada cikin nazarin yadda zai fahimtar da ita gaba daya baya jindadin dadin yanayin aikinta.
Karfe biyar saura kwata na yamma wayar Haj saratu ta shigo wayar Taufiq, fitowarsa kenan daga wajen aiki da nufin ma ya tashi.
Cike da girmamawa ya dauki wayar Yana kokarin gaisheta Amma jinta cikin wani yanayi na damuwa yasa yayi gaggawar tambayar ta abinda ke faruwa.
Tadan numfasa tace " Taufiq Ka hanzarta zuwa asibitin Kan tudu , an kwantar da Alh", a gaggauce yace " an kwantar dashi, yaushe ya Fara ciwon umma KO dazu da safe bayan na shigo office saida nayi waya dashi", tace " ai da Fara ciwon da kawo Shi asibiti ko awa biyu baayi ba," " gani nan zuwa umma" cewar Taufiq gami da kashe wayar, da sassarfa ya karasa bakin motarsa ya shiga lokaci daya yaja motar Kai tsaye asibitin ya wuce cike da damuwa da tashin hankali gami da adduar Allah yasa ba sosai bane.
Isarsa asibitin ya tadda mahaifinsa sosai cikin jigata na ciwo,bayanin Kuma daya samu daga bakin likita shine ciwon sugar dinshi ne ya tashi domin sugar dinsa ta hau sosai.
Yana zaune kusa da kafafun Alh Yusuf lamido Yana yi masa kallo me cike da tausayi ciwon sugar dinnan Shi kadaine yake cima Alh Yusuf lamido tuwo a kwarya Amma Taufiq ya rasa dalilin da yasa baya kiyaye dokoki da kaidojin ciwon musamman ma akan abinda yake ci.
Ya waiwayi Haj saratu yace " umma agaskiya ya Zama dole Abba ya kiyaye Akan irin abinda yake ci domin likita ya tabbatar min da cewa irin abincin da yake ci sune suke jawowa sugarsa take hawa Kuma kiyaye abinda zaici yafi Shan magani muhimmanci agareshi Amma na rasa abinda yasa Abba yake wasa da lafiyarsa bayan yafi kowa sanin wannan ciwon Yana da matukar hatsari".

Ta gyara zamanta Akan kujerar robar da take zaune akai, sannan tace " to ya zanyi dashi , babu abinda bana gaya masa Kan kiyaye dokoki Amma baya ji abinda yaso yaga dama Shi yake yi, ya ci abinda yaga dama yasha abinda yaga dama, to ta yaya zaiyi lafiya".
Taufiq yace " to aiko yanzu ya Zama dole ya kiyaye, tunda likita ya gayá min tahau sosai".
Haj saratu tace cike da damuwa" Allah dai ya bashi lafiya yasa Kuma kaffara ne".
Taufiq ya amsa da " Amin".

Taufiq ya cigaba da Zama a asibitin tare da Haj saratu har dare yayi sosai karfe goma da kwata na dare , zuwa lokacin kuwa Alh Yusuf lamido ya Farka sai dai har yanzu akwai zafin ciwo atare dashi.
Daga bisani Taufiq yayi sallama da su ya kama hanyar gida.
Yana tafe Yana mamakin hali irinna mujaheeda da bazata iya daga waya ta kirashi ba taji halinda yake ciki musamman yadda yayi dare abinda bai saba yi ba.

Fitilar motarsa ta haske wasu mutum biyu abakin titi, da sauri ya rage tafiya Yana kare musu kallo.
Gabansa yayi mummunar faduwa domin tabbas idonsà ba gizo yake masa ba mujaheeda ya gani tsaye tare da wani namiji kusa da kusa suna magana,
Yayi saurin kallon agogon hsnnunsa karfe goma sha daya saura na dare mujaheeda tana me

awaje? Ita da waye? Me suke yi? .Jerin tambayoyin da yake yima Kansa kenan.
Jikinsa har rawa yake yi saboda kaduwa, saida yayi Dan gaba sannan ya tsaida motarsa inda Yana iya hangen komai daga inda yake.

Mujaheeda ta saki jikinta sosai sunata magana da mutumin da Taufiq bai sani ba asalima bai taba ganinsa ba. Kwarai yaso yaji abinda suke fada.
Shin waye Shi ga mujaheeda, shin ko dai mujaheeda amanarsa take ci, don idan ba haka ba me zai hadata da wani katon banza da wannan tsohon Daren.
Akan idon Taufiq suka Gama maganganunsu, sannan kowa ya shige motarsa suka tafi.
Taufiq ya aje numfashi ahankali ransa a matukar bace yawun bakinsa yayi daci saboda bakinciki.
Ahankali cikin matukar fushi yaja motar ya tafi.
Mujaheeda ta rigashi shiga gida don kafin ya shigo harta shiga wanka.
A falo ya zauna duk abincin da masu aiki suka dafa na dare yana Kan tebur ko budewa babu wanda yayi.
Yana nan zaune har mujaheeda ta fito cikin shirinta na kwanciya ta dubeshi cikin kulawa tace " yaya Taufiq kadawo" ya gyada Kai alamar eh batare da yayi magana ba, tace tana wucewa wajen tebur din cin abinci " Amma dai yau kayi dare".
Ya juyo Yana kallon ta ta dakko farantin fruit tana sha daga tsaye, yace " ke Kuma yau kin dawo da wuri KO" ga mamakinsa sai yaji tace " ba lefi gaskiya yau da wuri na dawo ".

Ya Kura Mata Ido Yana mamakin karyar da ta yanko, yace " ai nayi zaton kema zakiyi dare tunda kusan kullum sai kinyi dare" ta girgiza Kai gami da dawowa kusa dashi ta zauna tana Shan kamkana tace " aah yau sai Alhamdulillah da wuri na dawo".

Ji yayi kamar ya juyo ya makure wuyanta ya Kuma tambayeta waye wannan katon da take tare dashi da wannan tsohon daren.
Kamar anyi masa allura ya Mike zumbir ya shige daki.
Bakin gadon ya zauna Yana maida ajiyar zuciya idanunsa sunyi jajir wani irin kunci ke shiga zuciyarsa.

Sosai yake kokarin ya dorama Kansa zargin mujaheeda, haushinta yake ji, idan har tana da gaskiya me zaisa tayi masa karya?.
Wannan karyar da tayi masa ta Sanya ayar tambaya akanta.
Har suka zo kwanciya Taufiq Yana cikin damuwa, duk yadda mujaheeda taso ta ja shi da hira yaki sakin jiki, ko da ta tambaye Shi dalilin yin darensa daker ya sanar da ita an kwantar da Àlh Yusuf lamido a asibiti.
Sosai mujaheeda ta Sami damuwa da Jin hakan domin dai har cikin ranta take Jin kaunar surikinta tana jinsa aranta tamkar uban da ya haifeta.
Dashi ta kwana acikin zuciyarta .tun safe kuwa tasa Masu aiki su dafa ma Alh Yusuf lamido irin abincin daya dace yaci tuwon alkama tasa suyi da miyar kubewa busasshiya wacce aka burge kaza aciki.
Ta Lura kwarai da canjin yanayin Taufiq, Wanda batasan dalili ba, ta dai Lura ko yaya aka Kira

wayarta idonsa na kanta Yana yi Mata wani irin kallo Wanda ta kasa fassara Shi.

Ya rigata fita gidan Kuma Kai tsaye asibitin ya wuce, ita Kuma mujaheeda saida aka Gama abinci sannan ta dakko ta taho asibitin Wanda kafin ta Karasa saida ta shiga super market tayi siyayya sosai tun daga Kan kayan tea da drinks Amma fa duk na masu ciwon sugar, Kaya ta sayo sosai.

Isarta asibitin ta tadda Taufiq tare da Haj saratu da Haj Bilkisu, kwata kwata Taufiq bai son Ko da hada Ido da mujaheeda haka zalika duk irin kayan data lofoma mahaifinsa KO kallonsu baiyi ba ballefa ya nuna jindadin sa ko godiya.

Alh Yusuf lamido da Kansa ya nunama mujaheeda waje kusa dashi ta zauna.ta zauna tana gaidashi tare da nuna damuwarta da kaunarta zuwa gareshi.

Shima cike da kauna yake amsa Mata tare da yi Mata godiyar hidimar data taho dashi.

Ita dai Haj saratu idonta nakan yarta tana nazarin meke faruwa tsakaninsa da mujaheeda domin tabbas tasan akwai matsala tunda su basa gajiya da Samun baraka atsakaninsu.

Ko kafin Haj saratu ta gama zubama Alh Yusuf lamido abincin da mujaheeda tazo dashi Wanda da Kansa yace azuba masa yaci. Tuni Taufiq ya fice daga dakin daga Haj saratu har mujaheedan binshi sukayi da kallo.

Mujaheeda tana tunanin meya faru ita dai tasan babu wani abu daya faru tsakaninsu Amma ta rasa dalilin da yasa tun jiya Taufiq ya canja Mata, KO yanzu har ta zo asibitin har zuwa yanzu daya fita baiyi Mata magana ba .

Haka mujaheeda ta cigaba da Zama a asibitin har tsawon wani lokaci kafin tayi sallama dasu adalilin son ta leka office .

Bayan tafiyarta ne Haj Bilkisu ta dubi Haj saratu tace " umma kina tunanin abinda nake tunani kuwa?" Tace tana kallonta " na mene?" Tace " tamkar tsakanin Taufiq da matarsa akwai matsala, kwata kwata tun zuwanta Taufiq bai karaesamun wani sukuni ba tamkar Yana Kan Kaya , baison Zama inda take".

Haj saratu tace " nima na fuskanci hakan, to matsala Kuma tsakanin Taufiq da mujaheeda ai idan da sabo yakamata asaba".

Ahankali cikin muryar ciwo Alh Yusuf lamido yace " Ku Kuma gasa Ido da ràshin son fadan alheri ba" Haj saratu tace " haba Alh ya zakace haka kullum alheri nake nufinsu dashi ".

Yace " to in dai hakane don Allah ku dinga yi musu fatan arziki, da Kuma addua ta gari". Gaba dayansu shuru sukayi.

A office mujaheeda aikin kawai take amma tunaninta na ga irin kallon da Taufiq yake Mata Wanda ta rasa gane wane irin kallone , da Kuma irin canjawar da yayi , aiya tunaninta dai bata tuna komai ba da akayi Wanda zai canjama Taufiq yanayi.Alh jibrin ya shigo da takardu ahannu yaja kujerar gabanta ya zauna Yana kallonta yace " GA takardun da mukayi dake jiya cewar Zan kawo Miki yau, Amma ya akayi Baki shigo office din da wuri ba yau ".

Tadan gyara zamanta tace " eh , surikina aka kwantar baida lafiya sai da na Gama da asibitin sannan na wuto office ".

Yace " Ayya , Allah ya bashi lafiya" ta amsa da amin.sannan ta dawo da kallonta Kansa tace "

duka file dinne" yace " eh komai na ciki duk records din suna ciki sai ki tsaya kibi ahankali ki gane " tace " to ba laifi". Daganan ya tura Mata files din gabanta sannan ya tashi ya fita ransa abace.

Alh jibrin Yana Shia office dinsa ya fada Kan kujera ya zauna Yana aje numfashin bacin rai, yace a fili , yarinyar nan tabbas tana son wuce gona da iri , tana Kuma son dakkoma kanta dala ba gammo , ta yaya take tunanin zata iya bankado almundahanar da sama da fadin da yayi da kudin kamfani na tsawon shekarun daya kwashe Akan kujerar manajan kamfanin.

Ya Kara sakin tsaki gami da buga hsnnunsa akan tebur, dai dai lokacin murtala yayi sallama ya shigo yaja kujera ya zauna Yana kallonsa yace , " ya ake ciki ne Ka kaimata files din ne".

Ya dago Yana kallonsa yace , " na kaimata aikin banza don dai babu abinda zata gani aciki" murtala yace " yarinyar nan ma fa ta cika yar rainin wayau".

Alh jibrin yace " ni Zan gaya Maka haka, wai kasan jiya duk wañnan uban dadewar data sa mukayi a office har dare, wai sai Dana kama hanyar gida ta kirani awaya wai naxo na sameta a babban titi, haka fa na juya naje na sameta , kasan me Muka tattauna " ya girgiza Kai , yace " Aah" Alh jibrin yace " wai tana tambaya ta ko akwai wani acikin maaikata da nake zargin zasu iya sama da fadin kayan kamfani, " murtala yace " to sai kace Mata mene ?" " Me ko Zan ce Mata daya wuce ni Bana zargin kowa, ammafa yarinyar nan idan tace wai zata zauna ta bubbugo sirrinmu ne na rantse maka zatayi babban kuskure arayuwarta domin ni Zan iya yin koma meye domin ganin asirina ya rufu".

Murtala yace " kwarai kuwa , ina Kuma bayanka domin tonuwar asirinka nima tonuwar asirina ne"....

DAGA TASKAR YAR GIDAN IMAM

NIMA MATARSA CE

NA

HÀBIBA ABUBAKAR IMAM

(YAR GIDAN IMAM)

BABI NA GOMA SHA SHIDA

****

Alh jibrin ya jinjina Kai cike da fusata yace, " kawai yarinya karama zata zo ma mutane da tsurfa, to matukar tace zata bankado abinda ke rufe to zata kwana aciki , Kuma hawanta kujerar manaja bazai Hana mu cigaba da yin abinda Muka sababa, yadda na ninke mahaifiyarta a Bai bai ta dauki amana da yarda ta dora min haka itama Zan tura Mata yarda da ni ko ba don Allah ba"

Murtala yayi dariya yace " ina goyon bayanka oga, Kuma Kada a manta acigaba da yaga min kamar yadda aka Saba amanace tsakaninmu babu Mai ji balle ya gani" . Haka murtala ya Kara dararrashewa Yana Kara zuga Alh jibrin.

Unin ranar Sam Taufiq bai wani samu sukuni ba a office hakanan ya ke kokarin dorama Kansa fitina ta tunanin abinda baida tabbas akai.sosai yake son sanin waye mutumin da yaga mujaheeda tsaye dashi da daddare, meye tsakaninsu?. Shin ko dai tambayarta zaiyi? Amma don me zai tambayeta bayan Kiri Kiri tayi masa karya.

Har ya tashi daga office ya wuce asibiti baya wani cikin walwala.

Ya tadda jikin Àlh Yusuf lamido da sauki domin yafi Jin sauki yanzu akan dazu, Haj saratu ta gaya masa yau tuwon alkama da mujaheeda ta kawo ya uni ci, hakan kuwa yayi masa dadi

Bai dade sosai da zuwa ba itama mujaheeda ta shigo office Kai tsaye itama daga office din take ta tashi da wuri ne saboda tana son dawowa asibitin ta Kara ganin jikin surikinta.

Haj saratu ta cigaba da Lura da yadda Taufiq yake basar da mujaheeda, itama mujaheedan zuwa lokacin ta tabbatar ma kanta da cewa akwai wani abu akasan zuciyar Taufiq to amma menene?, Domin dai aiya tunaninta babu abinda ya faru tsakaninsu. Ta cigaba da Lura da canjawar Taufiq, har zuwa lokacin da tayi sallama dasu ta kama hanyar gida can tabar Taufiq a asibitin.

Har ta Kai gida zuciyarta cike take da tunani .

Sai da ta ci abinci ta koshi sannan tayi wanka ta shirya tsaf ta fito falo ta kwanta tana danna wayarta.

Har karfe goma na dare Taufiq bai dawo ba, hakurinta ya gaza ta dakko daya wayarta ta danna ta kirashi amma har ta gama kukanta ta katse bai dauka ba.

Bata Kara Kira ba , shima bai biyo kiranta ba.

Sai karfe goma sha daya saura minti biyu Taufiq ya shigo gidan. Bayan sannu da zuwa da mujaheeda tayi masa ya amsa ba yabo ba fallasa.ido ta cigaba da binsa dashi har ya shige cikin daki, sai da ya gama wanka ya shirya ya fito falon ya zauna.

Mujaheeda ta dubeshi tace " gafa abinci can , Kona dakko na kawo maka nan".

Kallon tsaf yayi Mata sannan yace " ki dakko ki kawo min , ai baki Saba yin hakan ba , ki daina masu aiki su kawo min ko".

Ta kalleshi sosai tana Kara nazarin fuskarsa, tace " yaya Taufiq wai meke faruwa ne, gaba daya Naga Ka canja min ne, tun daga jiya nake ganin tamkar wani abu na damunka, tamkar akwai matsala, "

Ta Kara kallonsa sosai tace " idan akwai wani abu ne kayi hakuri ka gaya min , domin dai ni aiya sanina banyi maka komai ba ".

Ya Watso Mata wani irin kallo yace " Abu daya nake son ki gane ki Kuma sa aranki, duk matar da ta ci amanar aure sai Allah ya gwada Mata ishara tun a duniya kafin aje lahira, Kuma duk abinda mutum zai aikata ko a karkashin kasa ya shiga ya aikata akwai ranar da asirinsa zai tonu ranar yauma tubulal sara' il wato ranar tonuwar dukkan asirai, don haka mutum yayi komai amma ya sani akwai ranar kin dillanci".

Cikin daure Kai da rashin sanin inda maganganun sa suka sa gaba, mujaheeda tace " ban gane inda maganganun Ka suka dosa ba me kake nufi, maganar wace amana kake"

Taufiq yace " na dai gaya Miki ki kiyaye domin ranar da duk tunanina ya tabbata ranar zaki yi matukar mamakina," Yana Gama fadin hakan ya Mike ya shige daki yayi kwanciyarsa zuciyarsa da ransa na suya tsabar damuwa.

Ayayinda ya bar mujaheeda cikin matsananciyar damuwa, mamaki da daure Kai, shin me Taufiq yske kokarin nuna Mata ta rasa gane inda maganganunsa suka Sanya gaba , me yake nufi.nan mujaheeda ta cigaba da Zama tana tunanin abinda Taufiq yake nufi.

****

" Wai ba zaki fito ki dauki tallan shinkafar ba , sai kin Gama ikon naki da kinibibi, kin.kuma sani sarai idan abincina yayi kwantai sai kinyi mamakin irin hukuncin da Zan yanke akanki".

Cewar Ande Dije da take tsaye kan katuwar robar abincin, Hajara ta dubi muhseena da take kokarin Sanya hijabi tace " kiyi hakuri wata rana sai labari kije ki daukar Mata tallan Allah ya bada saa ya Kuma tsare ki gabanki da bayanki", cikin dabara muhseena ta sa hannu ta goge hawayenta domin bata son Hajara ta gani .

Da fara'arta ta juyo tana cewa " Amin Inna nagode da addua" tsawar da Ande Dije ta cigaba da yi yasa muhseena tayi gaggawar fitowa, Kai tsaye ta nufi wajen robar abincin ta dauka ta dora akanta.

Ande Dije ta daka Mata harara tace " kin Gama mulkin naki, muguwa saboda kina son abincina yayi kwantai Shi yasa kika ki fitowa ki dauka da wuri, kina sane komai bashi na karba ,nayi abincin tunda uwarki ta Zama Mai bakar kafa ta hana dana ya Sami arzikinsa sai wahala kawai da take bashi ".

Kwata kwata muhseena ta gaji da Jin wadannan maganganun ta Kuma gaji da Jin aibatawa da Ande Dije ke yima mahaifiyarta kullum .

Don haka da sauri ta fice hawaye ta fita daga idanunta , Wanda zubar da hawayen ya Zama wani bangare na rayuwarta domin kullum sai ta zubar dasu.

Can tsohuwar kasuwa muhseena ta tafi inda ta Saba Zama,ta zauna bayan ta aje kayan abincin. Hannu biyu tasa ta zuba tagumi tana kallon sauran Yara marasa gata irinta masu talla.

Duk duniya babu abinda ta ke so sama da karatu mafarkinta kenan arayuwa Amma tasan mafarkinta bazai taba Zama gaskiya ba domin bata da wannan gatan .

Acan gidan kuwa Ande Dije ke Kai gauro ta Kai Mari atsakar gida ta na ajema Hajara magana.hajara ta gaban wuta

Tana iza wutar faten da take dafawa.amna ita kadai tasan abinda take ji azuciyarta ko yaya Ande Dije ta Watso Mata magana takan ji tamkar numfashinta zai dauke.

" Babu wata nadama da zanyi aduniya sama da nadamar zamowarki suukata, domin dai Baki taba Zama alheri gareni ko ga Dana ba, Shi yasa ummaru yake bami tausayi domin dai baiyi sa'ar Mata ba".

Hajara na tsuguna gaban wuta zafin da zuciyarta take tafi zafin wutar dake gabanta .

Shin wai haka rayuwarta da ta yarta zasu Kare? Me yasa Ande Dije bata sassauta Mata? Meye laifinta a kaddarar data faru bayan Allah shine ya tsara komai yadda ya so ya Kuma ga dama.

Ande Dije ta Kara gyara zamanta abakin kofar dakinta ta cigaba da maganganunta " Ga mummunan tarihi, ga bakin hali, ga farar kafa , ga mummunan tarihi da kika aje ai dole a tausayama ummaru'.

Hawaye sosai Hajara ta Fara yi ahankali ta Mike zata shiga daki , taku biyu tayi taji kafafuwanta sun cije, ganinta ya yaye cikin kankanin lokaci ta sulale kasa ta Fadi sumammiya.

DAGA TASKAR YAR GIDAN IMAM.

NIMA MATARSA CE
NA
HÀBIBA ABUBAKAR IMAM
(YAR GIDAN IMAM)
BABI NA GOMA SHA BAKWAI
****

A gaggauce Ande Dije tayi kanta tana Kiran sunanta gami da jijjigata.

Dai dai lokacin mallam Umar yayi sallama ya shigo, ganin Hajara kwance akasa ko motsi batayi yasa cikin gigita ya karaso kanta, ayayinda Ande Dije take fadin " Alhamdulillah gara da Ka dawo ummaru'" Yana taba Hajara yana tambayar Ande Dije " meya sameta? Meya faru da ita ",

" Hakan nan naga ta yanke jiki ta Fadi, gashi nan ko numfashi naga batayi".

Mallam umar ya Kara gigicewa , da sauri ya tashi yaje ya debo ruwa ya shiga watsa Mata Yana watsa Mata Yana Kiran sunanta.

Cikin sa'a Hajara taja dogon numfashi gami da kokarin Bude idanunta kadan ta kafe idonta Akan mijinta.

Mallam Umar ya numfasa yace " sannu Hajara sannu" ta gyada Kai alamar yauwa tana kokarin tashi Amma duk yadda taso data motsa hannunta na hagu ta kasa .

" Yunkuro ki tashi" cewar mallam Umar, ta girgiza Kai tace " hannuna kamar baa jikina yake ba baya motsawa". Ande Dije ta dubeta sosai tace " kamar yaya baya motsawa".

Mallam Umar yasa hannu Yana Jan hannun Amma tamkar ba ajikinta yake ba yace " kina Jin tabi ahannun" ta girgiza Kai tace "aah bana Jin komai"

Hankalin Mallam Umar ya Kara tashi , da Kansa yasa hannu ya daga Hajara ya wuce da ita daki ya kwantar da ita Kan katifa, ya koma ya zauna Yana Jan hannunta Yana mikar dashi.

Ita Kam Ande Dije awaje ta noke bata bi su dakin ba.

Wani matsanancin ciwon Kai ke fisgar ta idanunta har hawaye suke yi saboda azaba.

Mallam Umar ya dubeta yace " Bari naje na Kira mallam kasim ya taimaka min ya dubaki".

Ya tashi da sauri ya fita , Kai tsaye gidan mallam kasim ya wuce, mallam kasim shine mutumin da yake taimakon jamaar kauyen idan Basu da lafiya domin yayi karatun asibiti shine Kuma yake tsaye domin ganin an Sami asibiti a kauyen hakan yasa da Kansa ya Bude Dan karamin asibitin da yakan duba marasa lafiya Wanda Kuma ciwon yafi karfinshi yakan Basu shawarar su wuce babban asibiti a jigawa.

Mallam Umar ya tadda mallam kasim Yana da marasa lafiyan da yake Kan dubasu bazai iya barinsu ya biyo Shi gida ba.

Hakan yasa ya bashi shawarar yaje ya taho da Hajara zuwa asibiti.

Komawarsa gidan Shi da Kansa ya gyara Hajara Ande Dije tana gani Amma ko dakin bata shiga ba ballefa ta taimaka masa wajen shiryata.

Sai da ya fita daker ya Samo mashin din da aka dauki Hajara zuwa asibiti.

Sosai Hajara ke cikin zafin ciwo nan da nan harta rame, bakinta ya bushe, kwata kwata jikinta babu dadi.

Sai da likita kasim ya Gama duba marasa lafiyan da suka cika gabansa , sannan ya dawo Kan Hajara.

Gwajin farko ya tabbatar masa da cewa jinin Hajara yayi mummunar hawa Wanda shiya Haddasa Mata ciwon Kai da Kuma ràshin aikin hannunta

Ya dubi mallam Umar sosai yace " Amma mallam Umar meke faruwa da me dakinka da ta Sami hawan jini, domin dai KO yanzu jininta ya hau sosai Kuma wannan faduwar da tayi Allah ne ya rufa asiri Amma da akwai yuwuwar ta Sami mutuwar barin jiki gaba daya".

Mallam Umar ya numfasa cike da damuwa yace " to yanzu likita hannun da baya aiki ya zaayi dashi, sannan wane irin taimako zaka bata akan ciwon hawan jinin".

Likita kasim yace " hannu akwai sa ran zai dawo dai dai zai cigaba da aiki, Zan rubuta magungunan da zatayi amfani dasu ". Ya Kara kallonsa yace " Amma abu mafi muhimmanci shine kusan damuwarta da abinda yake sata damuwar domin yaki da hakan domin kuwa duk maganin da zata sha idan bata Sami kwanciyar hankali ba babu amfanin da zaiyi Mata ajiki".

Mallam Umar ya nisa , damuwar Hajara Kam Baisan ta yadda zai magance ta ba, hawan jini Kuma Shi Kansa ya San ya cancanta Hajara ta samu don ma macece me juriya da dakewa, Amma kalubalen rayuwar da ta shiga da Wanda take ciki idan ma ciwon zuciya ne to ya ci ace ta samu.

Likita kasim ya Gama rubutu ya Mika masa takarda yace " ayi kokari asayi maganin Tasha bayan mako daya ta dawo, insha'Allah hannun zai dawo aiki, zakuma ta Sami saukin ciwon kan, sannan ta rage damuwa", yace " insha'Allah nagode ".

Daganan suka bar asibitin.har suka Kai gida mallam Umar cikin tunani yake, shin Allah ba zai kamashi ba da kasa kulawa da Hajara da yayi ? Babu wani farinciki data taba samu tunda ta aureshi tsawon wadannan shekarun Hajara tana rayuwa ne kawai saboda Allah bai yanke numfashinta a doron kasa ba.amma babu wani dadin rayuwa da take ji.

Sun koma gida suka tadda muhseena ta dawo Wanda tunda ta dawo daga tallan ta tambayi Ande Dije inda mahaifiyarta taje ta gaya Mata komai, tun lokacin ta koma bakin Kofa ta zauna tana kuka Wanda Sam Ande Dije bata bi ta kanta ba ,

Tare da muhseena Mallam Umar yabar Hajara ya fice domin ya Nemo kudin da zai sayo Mata magani, domin dai kwata kwata abinda ke aljihunsa bai wuce dari biyar ba.

Kemis din saida magunguna Wanda duk kauyen Durmi Shi kadaine, Mallam Umar yaje me kemis din ya lissafa maganin na nera dubu shida da Dari biyu shima din akwai guda daya da baa Samu ba.

Mallam Umar yayi shuru ya rasa inda zaisa Kansa tunaninsa daya shine ina zaije ya samo kudin.

Asanyaye ya dubi me kyamis din yace " Hassan da zaka taimaka min Ka Bani magungunan nan, insha'Allah bazan Maka wasa da kudi ba Ina samu Zan kawo maka , me dakina ce bata da lafiya tana Kuma bukatar maganin nan da gaggawa, ni Kuma Bani da kudin".

Hassan ya dubeshi yace " gaskiya mallam Umar na rufe bada bashi, saboda nema ake a karya ni, sakamakon wannan matsatsi da talauci da kunci da ake ciki mutane na cikin masifa ga ràshin lafiya hakan yasa kowa sai dai yazo ya ci bashi Kuma basa iya biya , to kaga idan na cigaba da bada bashi bazan Kai labari ba".

Mallam Umar ya Matso sosai wajen Kantar yace " nasan haka Hassan,Amma Ka sani

bazan taba yi maka wasa da kudi ba da zaran na Samu Zan kawo maka, nasan kana kokari kana Kuma rufama mutane da yawa asiri don haka nima don Allah Ka taimaka min yau Ka rufa min wannan asirin don Allah ".

Hassan yayi dan Jim sannan yace " gaskiya Mallam Umar don dai Ka cika min Ido ne, Kuma nima idan na hanaka nasan bazan taba Samun nutsuwa ba shiyasa kawai Zan baka ".

Cikin fara'a yace " Amma nagode Allah ya saka maka da alheri , Allah yasa kafi haka".

Yace " Amin, amma don Allah Kada ayi wasa da zaran kasamu Ka kawo min" yace " insha'Allah Kada kadamu Nagode".

Daganan ya hada masa magungunan ya bashi ya amsa ya tafi.

Mujaheeda ta na kusa da mahaifiyarta tana mammatsa Mata hannun,gami da kokarin goge hawayenta .

Tace " Inna duk arayuwata Bani da wani buri illa na jiyar da ke dadi na Kuma Zama me share hawayenki, tunda na taso ban taba ganinki cikin farinciki ba, Inna na so ace nayi karatun boko domin nasan tanan ne Zan iya cika burina" a hankali Hajara tace " Kada ki damu ,ki sani duk yadda kika so da ki sanyani farinciki idan Allah bai so ba babu yadda zaayi hakan ya kasance, Shi yasa na dau kaddara ta nasama raina kila bani da rabon farinciki a duniya ne don haka nake adduar kullum Allah ya jiyar da ni farincikin lahira" .

" Amin ya Allah ubangiji Allah ya Sanya farinciki atare dake ya Kuma yi Miki tukuici da aljanna Firdausi abisa hakurin da kikayi da halin da ta saki a duniya". Cewar Mallam Umar Yana kokarin shigowa dakin.

Kusa da katifar ya tsuguna Yana yi Mata sannu gami da fito da ledar maganin yace " muhseena jeki ki debo ruwa ta samu tasha maganin".

Da sauri ta Mike ta nufi wajen randar ruwan dake bayan kofa ta debo ruwan ta dawo da kamshi ya bare maganin ya bata Tasha.

Sannan ya cigaban da kallonta bayan ya maidata ta kwanta , a hankali ys kira sunanta " Hajara" ta amsa cikin muryar da ciwo ya Fara galabaitarwa.

Mallam Umar yace " bazan zargeki ba ba Kuma Zan Miki fada ba don damuwa tasa ciwon hawan jini yakama ki, domin baki da laifi" a gaggauce muhseena ta dubeshi sannan ta dubeta tace " hawan jini?" Ya gyada Kai yace " ciwon da ke damun mahaifiyarki kenan, Shi yasa nake son na roketa tayi hakuri ta cirema kanta damuwa domin duk abinda ke faruwa idan da sabo ya kamata ace kin Saba wata rana sai labari".

Idanu kawai Hajara ta maida ta rufe , ta yaya zata daina damuwa bayan kullum Ande Dije Saita dawo Mata da hannun agogo baya, sannan ta yaya zata raba kanta da damuwa bayan gudan jinin. Yarta ta Kai munzalin aure Amma babu Wanda ke son ya aureta , babu Mai son ya hada zuria da ita.

Muhseena ta goge hawayenta tace " don Allah Inna ki rufa min asiri ki daina damuwar komai kisa aranki duk abinda Allah yayi da bawansa dai dai ne".

Hajara batayi magana ba har mallam Umar ya Gama yi Mata nasihohi ya tashi ya fita.

Kai tsaye labulen dakin Ande Dije ya daga ya shiga gami da sallama ta amsa masa tana zaune bakin gado , Kan yar tabarmar dake shimfida atsakar dakin ya zauna gami da aje Kansa

a kasa.

Ande Dije ta dube Shi tace " lafiya kazo Ka sani agaba kamar Mai daukar karatu wani abunne".

Yadan muskuta ya gyara zamansa yace Ande nazo muyi wata magana neaiuhimmanci". Tace " toh ina jinka ya akayi". Mallam Umar yace " munje asibiti likita ya tabbatar mana da cewa Hajara tana da hawan jini "

Ta aje idonta akansa tace " to me Zan Mata don tana da hawan jini ko an gaya maka INA bada maganin hawan jini ne, tunda ita ba zata taba Zama lafiya a rayuwarta ba sai ta jefa mutane cikin masifa".

Cike da son shawo kanta yace " kusan ke ce kike da maganin hawan jinin nata, domin idan kika daure kika daina hantararta kika daina gsggaya Mata magana kika daina tsanarta tare da daukarta a matsayin ya to nayi Imani ba zaa Kara Samun hawan jini ajikinta ba"

Ta saki tsaki tace " in dai Saina dauketa a matsayin ya ne zata warke to taje tayi ta ciwonta tunda ita bata aje komai ba sai fitina ".

Yace " don Allah don son Annabi ki sassauta ma Hajara da muhseena agidan nan".

Cikin fusata ta nuna masa hanyar kofa tace," tashi Ka fita shanyayyen Hajara " zaiyi magana ta Kara dakatar dashi tace " Kada Ka ce min komai tashi Ka fita kawai".

A sanyaya mallam Umar ya tashi ya fita zuciyarsa na kuna shin yaya zaiyi? Ta ina zai shawo Kan matsalar tunda yasan Ande Dije ba zata taba bashi hadin Kai ba.

DAGA TASKAR YAR GIDAN IMAM

NIMA MATARSA CE
NA
HÀBIBA ABUBAKAR IMAM
(YAR GIDAN IMAM)
BABI NA GOMA SHA TAKWAS
****

Yasan duk yadda ya so ya fahimtar da Ande Dije kuskuren abinda take aikatawa ba zata taba fahimtar sa ba.

Amma lalle lokaci yayi da ya kamata ace Hajara da muhseena sun Sami sakewa da nutsuwa acikin gidan, amma ta yaya ? Ta ina zai Fara.

Yau jikin Àlh Yusuf lamido ya tashi da sauki sosai domin a yau din ake sa ran sallamarsa.

Da wuri mujaheeda tabar office ta taho asibitin, ta jidadin yadda yau ma Alh Yusuf lamido ya cinye abincin data kawo masa kafin ta tafi office, jikinsa Kuma da sauki sosai don tun zuwanta Yana zaune bakin gado suna hira da ita

Haj saratu kuwa tana zaune Kan tabarma ta mimmke kafafuwanta da yau ta tashi dasu da ciwo.

Jefi jefi tana kallon mujaheeda da mijinta tana mamakin irin son da Alh Yusuf lamido yakema mujaheeda itama ta Lura kwarai yadda mujaheeda take sakin jiki da nuna kauna ga Àlh Yusuf

lamido sam bata nunawa agareta ta rasa dalilin hakan ko don yafi nuna Mata kauna da kulawa ne fiye da ita oho?, Domin ita dai azahiri tana bayan danta bata Jin zata kaunaci mujaheeda fiye da yadda take kaunar danta don haka farincikin danta shine Farincikinta .

Dai dai lokacin daya daga cikin wayoyin hannunta ta shiga Kara.

Ta dubi Àlh Yusuf lamido tace " Abba Zan dauki waya" ya gyada Kai alamar babu damuwa, sannan ta dauki wayar " Ka karaso ne" cewar mujaheeda, daga daya bangaren harabar asibitin Alh jibrin ya amsa " eh ina harabar asibitin ". Tace " ok, gani nan fitowa ".

Ta Mike ta dubi Àlh Yusuf lamido tace " Abba daga office ne, zanje na karbi sako" yace " to sai kin dawo".

Ta wuce ta fice kacibis sukayi da likita zai shigo dakin, ya shige ita Kuma ta fita.

Bata sha wahalar hango Àlh jibrin ba Yana jingine jikin motarsa inda ake ajiye motoci, ta Karasa ," na saka wahala KO" ta fada tana karasowa kusa dashi , yace " Ah haba bakomai , ba wani wahala ai".

Ya koma cikin motar ya dakko wani file ya tsaya kusa da ita sosai ya Bude file din Yana nuna Mata gami da yi Mata bayani.

Dai dai lokacin Taufiq ya tsaida motarsa kusa da motar Alh jibrin dama Shi kadaine wajen daya rage inda ba mota sauran wajen duk an aje motoci.

Sosai ya dora idanunsa Akan mujaheeda da Alh jibrin, yanayin tsayuwarsa kadai ya Karema kallo ya gane Shi, shine mutumin daya ganshi tare da matarsa akan titi cikin dare

Ya Lura Sam mujaheeda ma hankalinta bai ko'ina sai Kan Alh jibrin ta tattare komai ta dora akan maganganun da suke yi, gashi sun tsaya kusa sosai yadda yayi Imani suna Jin bugun numfashin juna.

Daker ya Bude kofar motar ya fito ,Wanda har zuwa lokacin da ya fito babu Wanda ya kalli inda yake. Har saida ya tako sosai zai gotasu sannan yace " sannunku", da sauri mujaheeda ta juya tana kallon sa, tace " yaya Taufiq, yanzu Ka zo" yayi Mata kallon tsaf ba tare da ya CE uffan ba yayi wucewarsa Yana yi musu wani kallo da mujaheeda bata gane ba, Amma Shi Alh jibrin ya fahimci komai don haka yasa yayi Mata tambayar " waye wannan" ta dawo da kallonta gareshi sannan tace " maigidàna ne".

Ya jinjina Kai, irin kallon da yaga Taufiq Yana yi musu ya tabbatar akwai matsala sannan akwai matukar zargi acikin kwayar idanunsa.

Tun wuvewar Taufiq cikin asibitin mujaheeda taji ta kasa Samun nutsuwa da sakewa hakan yasa tace " Bani kawai idan na koma gida Zan tsaya na duba, abinda ban fahimta ba Zan kiraka domin Karin bayani" ya gyada Kai yace " to badamuwa, agaida Mai jikin" ta amsa " zai ji" ta dau file din tayi saurin wucewa.

Sosai Alh jibrin ya tsaya yabi bayanta da kallo yadda ta ke hanzarin komawa asibitin ya Kara tabbatar masa akwai matsala atsakaninta da mijinta.

Yayi wani bushasshen murmushi gami da jingina sosai ajikin motarsa zuciyarsa na bijiro masa da abubuwa da dama , Anya kuwa mijinta Yana son tayi aiki? Anya kuwa akwai jituwa da fahimta atsakaninsu Akan aikinta? Me yasa idanunsa suke fitar da sakon zargi akan mujaheeda,

Ya Kara yin murmushi yace a fili, wannan Mijin nata shine nake da yakinin zai iya kawo karshen aikin mujaheeda, matukar zargi ya cigaba da Samun tasiri azuciyarsa to tabbas

mujaheeda kamar tabar aiki.

Don haka ya Zama dole yasan yadda zaiyi ya Kara rura wutar da tuni ta Fara ci atsakanin Taufiq da mujaheeda.

Ya Kara yin dariya sosai sannan ya Bude kofar motar ya shiga ya rufe yaja ya tafi

Shigar mujaheeda cikin dakin ta tadda tuni an sallami Alh Yusuf lamido Haj saratu ta gama hada duk kayansu . Taufiq ya Fara daukar Kayan zai fita dasu , yayi kacibis da mujaheeda tana shigowa dakin , kallon tsaf yayi Mata , Wanda zuwa wannan lokacin ta Fara gajiya da irin wannan kallon da yake mata domin bata jindadinsa ta Kuma rasa dalilin yi Mata irin kallon

Ta matsa ya fita ba tare da sunyi ma juna magana ba.

" Ashe anyi sallama" cewar mujaheeda Haj saratu tace " aiko kina fita likita ya shigo yayi sallama bayan ya rubuta magunguna" ta Matso tace " Alhamdulillah, ina takardar maganin umma" ta dakko asaman tebur ta Mika Mata tace " gashi nan" tasa hannu ta Karba sannan ta dubi Àlh Yusuf lamido tace " Abba Bari naje wajen saida magani na sayo, gara atafi da Shi gaba daya" ya girgiza Kai yace " aah mujaheeda Kada ki wahalar da kanki ki bari Taufiq zai sayo".

Ta tsaya ta dubi Àlh Yusuf tace " Dama akwai bambanci ne tsakanina da Taufiq, Abba yanzu sayo maka magani shine wahala " ya yi dan murmushi yace " babu bambanci tsakaninki da Taufiq, je ki ki sayo min magani" tayi murmushi tace " toh".

Ta wuce da sauri tana murmushi tana bude kofa Taufiq ya shigo ita Kuma ta fita shima babu Wanda yayima wani magana.

Alh Yusuf lamido ya dubi Haj saratu yace " kingani ko, dama na gaya Miki mujaheeda zata canja to kingani tun ba'aje ko'ina ba gaba daya halinta ya canja, tasan muhimmancin dangantaka, tasan girmamawa da mutuntamu, na rantse Miki mujaheeda ina jinta araina tamkar yar da na Haifa, bana son duk wani abu dazai bata Mata rai".

Taufiq ya jingine jikin bango Yana Jin maganganun da mahaifinsa ya ke yi.

Haj saratu tace " ni Kaina na Lura kwarai da canjawarta, har Kamala ta Kara don na Lura da yadda take Sanya hijabi yanzu ko babban gyale sabanin da da bata damu da suturta kanta ba"

Alh Yusuf lamido ya dubi Taufiq yace " kaga matarka ko Taufiq ta Zama me kulawa duk ta canja, yaya zamanku INA fatan shima akwai cigaba nasan tunda tana sonka babu abinda ba zata yi ba domin kawo zaman lafiya atsakaninku"

Taufiq ya aje numfashi ahankali wannan yabon da mahaifinsa yake ma mujaheeda ji yake Yana Kara Haddasa masa kunan zuciya.

" Nace yaya yanayin zamanku" Alh Yusuf lamido ya Kara maimaitawa ayayinda Haj saratu ta zuba masa Ido tana fahimtar sakon dake lumshe akan fuskar tasa.

Yace " babu wata matsala, lafiya lau Muke zaune" yace Yana kallon Haj saratu" Alhamdulillah, to kin dai ji abinda yace sai ki cirema kanki tunanin banzan da kikeyi na tunanin akwai matsala atsakaninsu ".

Gyada kai kawai tayi domin tasan idan zata kwana son ta fahimtar dashi akwai matsalar da gaske bazai taba yarda ba tunda shima Taufiq din da alamar baya son asan matsalar dake tsakanin nasu ,Amma koma dai meye tasan Taufiq bai jindadin Zama da mujaheeda Amma Kuma ta tabbatar da cewa Yana son mujaheeda matukar so , to me ke kawo matsalar?.

Taufiq bai son maganar tayi nisa don haka ya dauki sauran kayan ya dubesu yace " mu tafi Ko?".

Alh Yusuf lamido yace " aah sai mujaheeda ta dawo taje ta sayo min magunguna ".

Ya dube Shi yace " Abba meyasa zata je ta sayo maka magani bayan gani " , " Ko da kake nan din , meye aibu don na sayo ma ubana magani" cewar mujaheeda bayan ta shigo cikin dakin rike da ledar magunguna masu yawa .

" Babu aibu amma ni nafi cancanta na sayo" tace " to gashi Kuma na riga na sayo ya ya kenan zaka mayar ne".

Da sauri Alh Yusuf lamido ya daga ma Taufiq hannu yace " Kai bana son shashanci Taufiq meye aciki don ta sayo min magani" ya juya ya dubeta Yana kokarin sakkowa daga Kan gadon yace " nagode kinji Allah yayi Miki albarka".

Taufiq zaiyi magana kenan Haj saratu tayi saurin daga masa hannu alamar yayi shuru. Hakan yasa ya juya ya fice daga dakin ransa abace.mujaheeda ta bishi da Ido ta Kara tabbatar da cewa akwai abinda ke cikin zuciyar Taufiq agame da ita.

Bayan fitarsu Duka tare, motar mujaheeda Alh Yusuf lamido ya zabi ya shiga.duk da abin ya bata ma Haj saratu da shi Kansa Taufiq din rai Basu CE komai ba Haj saratu ta shiga motar Taufiq Shi Kuma ya shiga motar mujaheeda suka tafi.

Ran Taufiq azafafe yake Yana tuki kamar zai tashi sama, hakan yasa haj saratu ta dube Shi tace " Kai Taufiq Ka dawo hayyacinka ko so kake Ka kashemu a banza a wofi ".

Nan da nan yayi saurin rage gudun Yana bata hakuri " yi hakuri umma bansan lokacin da na Kara gudun ba" .

Ta numfasa tace " ya Zama dole Ka Saba da wannan ya Kuma daina bata ranka domin dai Alh ya riga ya dorama Kansa alhakin kulawa da mujaheeda da farincikinta ya Kuma dorama Kansa Sonta, don haka babu wata riba da zaka samu matukar kace zaka dinga fada da ita". Ya runtse Ido ya Bude yace " to yaya zanyi umma shikenan Saina zauna na Zama sakarai duk abinda tayi niyya Shi zatayi Anya anyi min adalci idan akace Bani da iko Akan matata".

" Babu Wanda yace Baka da iko akan matarka, asalima Kai ne kadai Mai iko akanta, Amma meye matsalar da kuka kasa Zama lafiya bayan irin kaunar da kukeyi ma juna tana sonka kana Sonta to ina matsalar take"

Yayi shuru sannan yace " matsalar yanzu umma guda daya Ce, tunda ta Fara aikin nan bani da wani kwanciyar hankali, asalima ayanzu zargi ne ke neman shiga tsakaninmu koma nace ya shiga ".

Tayi gaggawar kallonsa tace " kasan abinda kake fada kuwa zargi wane iri?".

Yadan jinjina maganar kafin ya fada sannan yace " zargin mu'amala da Maza".

Tayi salati ta Kara zuba masa Ido tace " Kai Taufiq kasan girman wannan maganar kuwa kasan illarta kasan abinda zata haifar,ta yaya zaka Bari shaidan ya Fara naka hudubar banza don kawai Baka son tayi aiki," ta Kara kallonsa ta cigaba da cewa" kana da shaida ko hujjar wannan mummunar zargin naka".

Ya girgiza Kai yace " Bani da hujja ko shaida sai dai abinda idona ya gani Shi kadai Wanda nasan Bai Isa hujja ba" ta gyara zamanta tace " me idon naka ya gani ".

A hankali ya gayá Mata komai sannan ya Kara da cewa " umma idan tana da gaskiya Mai yasa zata min karya,sannan dazu da na shigo asibiti tare da mutumin na gansu kusa da kusa

suna maganganu".

Tace " Kai amma Taufiq kana da sakarci, mutumin da Ka gansu tare daga office dinta yake ya kawo Mata sako, sannan don Ka gansu tare da daddare abakin titi shine zai tabbatar maka da me? Tana ha'intarka? Idan ha'intarka take yi akan titi zaka gansu ko a hotel?"

Ta dubeshi fuskarsa ta Fara nuna alamun yarda da maganar da take gaya masa.

Ta cigaba da cewa " sannan karyar data maka na cewa tuntuni ta dawo, nasan tayi maka karyar ne saboda gudun Samun matsala atsakaninku don zakace tayi dare za Kuma kayi Mata fada ba tare da tsayawa kaji uzurinta ba ni macece don haka nasan tunanin hakan yasa tayi maka karya".

Sosai yaji ya gamsu da maganganun mahaifiyarsa, ta cigaba da cewa " sannan ina son daga yau duk abinda ya shiga tsakaninka da matarka Ka daina ajeshi a zuciyarka har Ka maida Shi gaba , Ka tsaya Ka kirata Ku tattauna Ku fahimci juna Kuma kuyi maganin matsalarku, Kuma Kada Ka Kara zargin matarka Akan wani dalili da baida tushe balle makama, kaji na gaya maka".

Cikin gamsuwa da maganganunta yace " nagode sosai umma, na Kuma dauki shawarar ki Zan sameta mu tattauna ". Tace " hakan ne ya kamata, kuyi magana Ku fahimci juna ".

Yace " insha'Allah ". Haj saratu ta cigaba da yi masa nasihohi musamman akan zaman aurensa, ya Kuma Zama dole ya rage saurin fushi domin shike kawo danasani.

Komawarsu gidà, sun tadda har mujaheeda ta aje Àlh Yusuf lamido ta bashi magunguna da Kuma bayanin yadda zai dinga Sha kullum, sannan tayi tafiyarta ba tare data Jira karasowar su Taufiq ba.

Hakan ya tabbatar masa da cewa itama mujaheedan ta Fara daukar zafi.yadan dade agidan nasu kafin ya tattara ya tafi gida.

Mujaheeda tayi wanka tayi kyau cikin doguwar bakar riga ta daura dankwalin rigar, sai tashin kamshi take na musamman tana aikin dubs file din da Alh jibrin ya kawo Mata . Gefenta farantin fruit dinta ne da shansu ya Zama wani bangare na rayuwarta.Acikin hakan Taufiq ya dawo yayi sallama ta amsa masa tana kokarin kallonsa, tayi kokarin daurewa ta maida fushinta da damuwarta tace," Ka dawo" tayi mamakin yadda ya amsa Mata babu fushi acikin muryarsa kamar yadda yi kwana biyu, " na dawo* ta gyada Kai tace " akwai abinci akan tebur su lamimi sun gama komai".

Ya wuce cikin daki Yana cewa " wanka nake son na Fara yi tukuna".

Harta Gama duba file din ta koma ta kwanta a doguwar kujera ta dau waya ta cigaba da dube dubenra, sannan Taufiq ya fito da shirinsa na doguwar riga Mai taushi.ya zauna Yana dubanta itama tadan dubeshi tace " na dauka abincin zaka ci". Ya gyara zamansa yace " Zan ci sai anjima, nasha fura a gida".

Ta maida kanta Kan wayarta, Taufiq yace " mujaheeda waye dazu yazo gunki a asibiti".

Ta tashi ta zauna tana kallonsa tace " mataimakina ne a office", ya maimaita " mataimakinki?" Tace "eh wani abunne, don dama dazun Naga yadda Ka canja, tamkar baka jidadin ganin mu tare ba".

Ganin baiyi magana ba yasa ta cigaba da cewa " kamar yadda na fahimci akwai wani abu acikin zuciyarka Wanda Baka gaya min ba amma Shi yake Haddasa maka yin fushi kamar yadda kayi magangsnunka a asibiti don kawai na sayama Abba magani tamkar kana jirana,

sosai abin ya bata min rai".

Taufiq ya dubeta sosai , yace " kwarai akwai abinda ya bata min Rai" tace " to menene Shi".

Yace " karyar da kikayi min rannan kikace kin dawo gida da wuri bayan na wuceki a hanya da wannan tsohon Daren ke da namiji atsaye ".

Ta zuba masa Ido gami da gyara zaman ta ce " Ka ganni?" Ya gyada Kai yace "eh ranar da aka kwantar Abba".

Tadan yi Jim alamar tunani, tabbas ta tuna ranar yayi dare Kuma ita da Alh jibrin ya gansu tsaye

Ta dawo da kallonta Kansa tace " na tuna, kayi hakuri yaya Taufiq bana nufin nayi maka karya amma na zabi nayi maka karyar ne saboda Bani da wani zabi" yace " kamar yaya baki da wani zabi" tace " eh mana, saboda Dama ina ta adduar Allah yasa baka dawo gida ba domin tabbas nasan sai kayi min fada Akan daren da nayi Kuma bsna son fadan nan , hakan yasa dana dawo nayi saa baka dawo ba , na zabi da nayi maka karya saboda a zauna lafiya".

Takara kallonsa ta cigaba da cewa " Kuma ba wani Ka ganmu tare ba illa Alh jibrin ya biyo ni munyi magana ne akan abinda ya shafi kamfani".

Taufiq ya numfasa yaji ya gamsu da maganar mujaheeda amma duk da haka Yana adduar Allah yasa duk abinda ta fada gaskiya ne.

" Da Kai me kake zato, da har yasa Ka canja don yanayin Ka Bana karyar da na maka bane yasa kayi irin wannan canjawar"

Taufiq yace Yana lankwashe hannayensa har sai da sukayi Kara " babu abinda shaidan bai kitsa min ba , ciki hàrda tunanin kina cin amanata ne da wani".

A gigice tace " subhanallah wace irin magana ce wannan, ashe koma me zaka ji ko zaka gani zai iya sawa Ka zargeni da cin amanarka, ina matar aure Ka yi min irin wannan zargin, abinda banyi ina budurwa bane kake zaton zanyi Shi ina matar aure, me zaisa na nemi Maza bayan ban rasa komai ba arayuwata". Nan da nan idanunta suka cika da hawaye kirjinta ya Fara ranta yayi matukar baci .

Ganin hakan yasa Taufiq yace " nafa gaya Miki abinda shaidan ya kitsa min ne ba wai....?" Tayi saurin Katse Shi tace " abinda shaidan ya kitsa maka ko abinda Ka kitsa ma kanka" yace " Kada ki fahimceni a Bai bai Kada kiyi zaton da bashi bane".

Tayi masa wani bushasshen kallo tace " Ka bani matukar mamaki yaya Taufiq wai anya kuwa Ka na Sona? Don na Fara shakku Akan hakan, Bana Jin da gaske kana Sona".

Yace " ya zakiyi wannan maganar INA sonki mana , ina kaunarki" ta girgiza Kai tace "aah mutumin da kake so ba zaka taba jifansa da wannan Kalmar ba ko da ko ace Yana aikata abinda kake zato, kullum masoyi kokarin boye laifin masoyinsa yake ko da a gabansa yake aikata laifin , balle Kai da idonka ne kawai ya ganni tsaye da wani ba wani abu Ka ganmu muna aikatawa ba na ràshin gaskiya Amma har kake da damar da zaka zargeni".

Gaba daya batasan sanda ta rushe da kuka ba Mai tsuma rai Taufiq ya rude yace " don Allah kiyi hakuri kiyi shuru kibar wannan maganar Kada masu aikinki su ji ".

Tayi masa wani irin kallo tace " kowa ma yaji mana, na riga na rasa dukkan tunani na bansan ta inda Zan Fara ba mijina bai yarda da ni ba bayan yafi kowa sanin ko wacece ni , kasan yadda abin nan yake da Kona rai".

Ta Mike tana goge hawayenta " Baka Sona , ya Zama dole na yarda da hakan" " nace kibar

maganar nan, na gaya Miki ina sonki...?" Ta saki tsaki ta wuce cikin daki tana Kuka sosai.

Taufiq ya kama Kansa da hannayensa biyu Yana jujjuyawa, ba haka ya so abin ya tafi ba, yaso su Sami fahimtar juna komai ya wuce, ya gane kuskuren sa tun daga lokacin da suka yi magana da mahaifiyarsa.kawai ya tambayeta waye mutumin daya gansu tare ne saboda yasan waye .Amna da yasan gaya Mata hasashensa zai Kara janyo wata babbar matsalar da bai gaya Mata ba.

Yanzu ta yaya zai shawo kanta yadda ta dauki wannan mugun zafin.

DAGA TASKAR YAR GIDAN IMAM
NIMA MATARSA CE
NA
HÀBIBA ABUBAKAR IMAM
(YAR GIDAN IMAM)
BABI NA GOMA SHA TARA

****

Daker ya Mike ya bita cikin dakin , ya zauna bakin madubi duk yadda ya so ya shawo kanta, ya Kuma wanke Kansa to fa mujaheeda ta ki sauraron Shi. Ta Kuma ki daina kukan da take yi. Hakan yasa dole ya tattara yabar gidan.

Ita Kam mujaheeda ta rasa inda zatasa kanta , sosai take Jin azuciyar ta cewa Taufiq ya daina Sonta ko Kuma Dama tun farko baya Sonta.domin tayi Imanin Wanda kake so ba zaka taba zarginsa ba balle har kayi tunanin sa da wannan mugun abun.

Amma tabbas yau Taufiq yayi matukar bata Mata rai ya jefata cikin túnani da bakinciki.

****

Hajara dai tana ta jinya, gami da Shan magunguna Amma dai har yanzu hannunta Bai dawo dai dai ba Yana motsi amma bai iya yin komai.

Hakanne yasa duk wani wahalar aikin gidan ya dawo Kan muhseena, ita take yin komai tun daga Kan girki da gyara gida da Kula da dabbobin Ande Dije.

Mallam Umar da Kansa ya hanata daukar talla domin Baisan da wanne zata ji ba. Dole tasa awannan Karon Ande Dije ta yarda da hukuncin Mallam Umar,Amma ba don ranta ya so ba.

Mallam Umar ya maida Hajara asibiti kusan sau uku tana Kara ganin likita.kuma likita kasim ya tabbatar musu da cewa Kada su damu hannunta zai dawo dai dai amma Shi Kansa baisan wane lokaci zai dauka kafin ya dawo dai dai ba, tunda komai na Allah ne.

Wannan hidima da Mallam Umar yake yi na asibitin Hajara ya Kara dorama Ande Dije haushi da tsanar Hajara, domin Saita uni ta kwana ba tare data leka dakinta ba tayi Mata sannu.

Muhseena ta rasa dalilin irin wannan tsanar da kakarta tayi musu ita da mahaifiyarta.

Sau tari Kuma tana son ta gasgata abinda mutane suke fada da Wanda ita kanta Ande Dije take fada na cewa ita ba kakarta bace.saboda dabi'un da take nuna musu kwarai zai iya yuwuwa ba kakarta bace.

To idan ba kakarta bace wacece ita agareta da mahaifinta.

Don dai ta riga tasa ma kanta yarda da tabbatar da cewa mallam Umar mahaifinta ne shine ya kawota duniya duk wani Kuma surutan mutane na batanci bazai taba Sawa ta aminta da cewa bashi bane ya haifeta.

Amma tabbas tana matukar bukatar Jin amsoshin tambayoyinta daga bakin mahaifiyarta Wanda tasan sune tambayoyi marasa dadi agareta Wanda Kuma ko kadan bata son tayi Mata tambayoyin. Ya zatayi dole haka zata cigaba da Zama da kuna da radadi acikin zuciyarta amma tana rokon Allah sassauci.

Yau jikin Hajara akwai sauki sosai harta fito tsakar gida ta zauna a shimfidar da muhseena tayi mata, muhseena tana cike da farincikin ganin irin saukin da mahaifiyarta ta samu.

Dai dai lokacin mallam Umar ya shigo , shima yajidadin ganin Hajara a waje cikin sauki.yadda yake nuna murnarsa yasa Ande Dije dake gefen dakinta a zaune ta saki tsaki, ji take kamar ta fisgo Shi ta shake Shi.

Mallam Umar ya dubi muhseena yace " Alhamdulillah yau dai naje makarantar islamiyar Ku na biya duk bashin da ake Bina, saboda haka dazaran Hajara ta Kara Samun sauki zaki koma islamiyar kinji KO". Wani irin dadi ya kama muhseena ta daga hannu sama tana yima Allah godiya sannan tana yima mahaifinta godiya kullum adduar ta bata wuce Allah yasa ta samu ta koma islamiyya yau dai Allah ya amshi adduarta.

Ande Dije ta Kara sakin tsaki tace a kausashe " haka zaka kare cikin bauta, ta Koma islamiya to ina makomar tallar da take daukar min na yamma"

Ya dubeta yace " Ande Dama talla ai ba hurumin muhseena bane,na Kuma sha gaya Miki kamar yadda nasha rokonki ki daina dora Mata talla."

Ta watsa masa harara " to idan ban Dora Mata talla ba me kake son na dora Mata so kake tayi ta zaman banza agida ita ga yar gata, tana zube agida ita ba karatu ba ita ba aure ba , ni Kuma Saina tsaya kawai ina kallon tsawonta acikin gida".

Ya juyo Yana kallonta yace " Bana son muna jayayya Akan muhseena domin baida wani amfani, muhseena yata ce duk wani nauyinta Yana Kaina, babu Kuma nauyinta daya fi komai nauyi akaina irin tarbiyyarta da karatunta, kin Kuma fi kowa sanin talla ba shine hanyar tarbiyyar ta gari don muhseena tayi girman da ya kamata ace tana killace waje daya idan bata makaranta to tana gida Amna Bai kamata a dinga ganinta a layin Yan talla ba, don haka ina rokonki don girman Allah kiyi hakuri da dorama muhseena talla tunda Allah bai nufi zatayi karatun boko Mai zurfi ba to abari ta je islamiyya ta Sami ilimin addininta Wanda shine Kan gaba arayuwa".

Ande Dije ta jinjina Kai cike da takaici tace " AI baka ganin kowa sai su, ba damuwa nasa muku Ido tunda baka yarda da na Dora Mata talla ba, taje makaranta amma da sadaka Ka nemi wani Ka bashi kayi Mata aure da hakan yafi maku alheri Duka, don idan ba sadakarta Ka bayar ba babu yadda zaayi ta Sami Mijin aure ta dinga Zama agabanku kenan , kana dai gani duk sa'anninta sunyi sure wasu harda yaya Amna ita tana nan ko da sau daya ban taba Jin anyi sallama da ita da sunan sairayi ba".

Mallam Umar ya dubi Hajara da muhseena yadda yaga damuwa da bacin ran magangsnun Ande Dije a fuskarsu yasa ya dawo da kallonsa ga mahaifiyarsa yace " don Allah kibar wannan maganar, Shi dai aure lokaci ne don haka idan Allah ya kawo Mata Miji zatayi aurenta, saboda haka kibar wannan maganar don Allah ".

Ta Mike ta kakkabe zaninta tana kokarin dage labulen dakinta tace " magana ko nabarta, nace na barta ". Ta shige daki tana maganganu.

Mallam Umar ya dawo da hankalinsa Kan matarsa da yarsa yace " Ku kwantar da hsnkalinku, duk abinda kuka ga ban Muku ba arayuwa to Bani da halin yi ne, na rantse ban hada sonku da komai ba , kullum Bani da wani tunani da ya wuce yadda zanyi na ingsnta rayuwar Ku na Kuma

sa Ku farinciki.".

Ahankali Hajara tace " na Sani mallam, Allah dai yayi maka budi na alher" muhseena tace " nasan ko zamu ji dadi ranar da Baba ya samu kudi hmmm" ta Karasa magana tana dariya sosai yajidadin hakan yace " kwarai kuwa muhseena zaku jidadi fiye da zatonki, don har makarantar boko Zan maida ke tunda nasan burinki Kenan Kuma tun daga aji uku na karamar sakandire na cireki saboda rashi, kinga ko ranar da duk na Sami kudi dole na matar da ke makaranta , saboda ni kadai nasan bakincikin da nake kwana nake tashi dashi akan ràshin cigaba da karatunki".

Muhseena ta aje numfashi ahankali tace, " don Allah Baba kadaina wannan tunanin babu komai ".

Ya girgiza Kai yace " Allah ya rufa mana asiri , Allah ya kawo mana mafita " Duka suka ce "Ameen". Daganan ya wuce ya dauki buta cike da ruwa a kofar daki ya zagaya bandaki.

Muhseena ta dubi màhaifiyarta ta Kula da canjawar da tayi fuskarta ta nuna damuwa Wanda tasan baya wuce maganganun da Ande Dije tayi.tace " Inna don Allah Kada kisa damuwa a maganganun Ande ,ni ban Gama dalilin da yasa zaki dinga damuwa akan maganganun ta abinda idan da sabo ya kamata ace kin Saba ya Kuma daina bata Miki Rai, kina sane da ciwon da ke damunki baya son damuwa ".

Ta dubeta tace " muhseena baa saboda cin mutunci da cin fuska da Kuma nuna kiyayya, musamman ga Wanda bazai taba mayar maka ba ko tsayawa ya gayá maka abinda ke cikin zuciyarsa ba, kinsan dai duk abinda Ande take min Bana iya mayar Mata ko da kalma daya, ba Kuma na fatan lokacin da zan mayar Mata da magana yazo, " muhseena tace " Amma kinsan Inna barin magana a zuciya bakaramin illa bane Kuma Ina da tabbacin hakanne ya janyo Miki hawan jini, don haka don Allah ki daina damuwa".

Ido kawai tasa Mata azuciyarta tana godema Allah daya bata ya irin muhseena, tasan dai tafita shiga damuwa amma akullum tana boye damuwarta saboda bata son Kara Mata damuwa, duk abinda tasan zai Zama damuwa agareta bata yi ko da tana son yi takan danne ta hakura.

Yarta ya daya Ce tamkar da dubu tana da halaye masu kyau, tana Kuma alfahari da ita.

****

Wannan Karon dai mujaheeda ce ta dauki zafi da Taufiq sosai, don kwata kwata taki sakar masa fuska duk da suna magana Amma fa babu wannan sakin fuskar da take masa, don ko tayi nufin hakan takan ji ta kasa da zaran ta tuno ràshin yarda da zargin da Taufiq yake Mata .

Shi Kuma Taufiq tunda ya bata hakuri bata sakko ba, shima ya fita harkarta zaman dai babu wani dadi, Taufiq zuciya da fushi ,mujaheeda girman Kai da mitar magana .to ta ina zaa Sami sauki? Ta ina zaa Sami fahimtar juna da zaman lafiya .

Bayan duk inda aure yake, Yana bukatar fahimtar juna da yima juna Uzuri da Kuma hakuri da juriya, matukar aure ya rasa daya daga cikin wannan to bazaa taba jindadinsa ba , balle Kuma ya rasa duka. Dole idan daya ya hau daya ya sauka, sannan yadda Kalmar hakuri take da nauyin fada wajen namiji idan har kika Sami Wanda zai yi lefin ya Kuma bada hakuri to lalle kiyi yaki da zuciyarki ki hakura ko da daga baya zaki koma ki tada maganar toki nuna kin hakura ahankali daga baya saiki fahimtar dashi abinda yayi din ba dai dai bane.

Alh jibrin Yana zaune a cikin office dinsa bugun kofar da akeyi ya sa ya bada izinin a shigo.

Murtala ya turo kofa ya shigo Yana murmushi, Alh jibrin ya ce " Ka kulle kofar da makulli" murtala ya juya ya rufe kofar yasa makulli ya dawo ya zauna Yana fuskantar Alh jibrin, yace " oga na amsa Kira, gani na zo".

Alh jibrin ya aje biron hsnnunsa Kan tebur yace Yana kallonsa, " wato murtala wani abu nake son na aikata tun kwanakin baya nake tunanin aikatawa Amma yanzu na ji na aminta da aikata abin, saboda hakan ina ganin kamar shine kadai hanyar dazan amshi matsayina na koma kujera na Kuma ci Karena ba babbaka kamar da, kaima Kuma Ka koma Kan kujerarka ta mataimakina, kana dai ganin yadda aka barka a yar yawo Baka da wani katamaiman matsayi asalima ko office Baka da Shi sai dai kayi ta rakube rakube".

Murtala ya canja fuska damuwar kaskancin da yake ciki ta bayyana , ya dubi Àlh jibrin yace " hmmm na rantse maka ni kadai nasan irin bakinciki da kuncin Dana ke ciki agame da wannan kaskanci da akayi min, ni dama nasan Haj murjanatu bata sona hakanne yasa tayi min Kora da Hali, Kai da take so ai ta nema maka waje ko da Bai Kai Wanda Ka Bari ba".

Alh jibrin yace " to kasan duk Wanda yayi sanadin faruwar abinda ya faru" murtala ya girgiza Kai alamar aah, sannan Àlh jibrin ya ce" mujaheeda itace silar komai , don da baa kawota aiki a kamfanin ba babu yadda zaayi mu koma baya, Wanda ni banga amfanin yin aikin ta ba, duk fa dukiyar nan mallakinta ce, to don me zata zo ta batama kanta lokaci ta Kuma hana mu farinciki , me ta rasa? Me take nema?"

Murtala yace " nima abinda nake ta tunani Kenan" Alh jibrin yace " to na Samo hanyar da aikinma zata daina balle ta cigaba da binbini da son tono asirinmu" murtala yace " to ta yaya".

Alh jibrin yace " Mijin mujaheeda alamu sun nuna min cewa baya son aikin da take yi, idanunsa Kuma suna nuna zargi agareta," murtala yace " ta yaya kasan hakan".

Yace " na hadu da mijinta kwanaki a asibiti da naje wajen mujaheeda Kai Mata files, na fahimci mijinta Bai jidadin ganin mu tare ba ransa ya baci sannan Kuma irin kallon da yake mana cike yake da zargi cikin kankanin lokaci a matsayina na namiji na fahimci abinda ke kwance acikin zuciyar Mijin mujaheeda, tsabar zargi da ràshin son aikin matarsa ne kwance acikin zuciyarsa, Shi yasa nake son na tabbatar masa da zarginsa" murtala yace " ta yaya to?"

Alh jibrin ya tashi daga Kan kujerarsa ya shiga shawagi a tsakiyar office din , murtala na binsa da kallo.

Daga bisani ya tsaya akansa yace " ina son Ka saurare ni da kunnan basira domin aikin nan tare zamu yi shi".

A hankali Àlh jibrin ya gama gayama murtala duk abinda ya tsara da yadda zasu bi abin har hakansu ta cimma ruwa.

Murtala ya Kura masa Ido yace" Amma kayi dogon nazari , Kuma Zan bada dukkan gudunmawa ta, domin tabbas wannan hanyar itace kadai hanyar da mijinta zai hanata yin aiki, mu Kuma mu mallaki abinda Muke so". Gaba daya suka kwashe da dariya.

Sannan suka cigaba da tattaunawa gaba daya sun tsaida magana daya za Kuma su Fara fafatawa daga gobe.

DAGA TASKAR YAR GIDAN IMAM

NIMA MATARSA CE

NA

HÀBIBA ABUBAKAR IMAM

(YAR GIDAN IMAM)

BABI NA ASHIRIN

****

Mujaheeda sun cigaba da Zama da Taufiq babu yabo ba fallasa , domin dai maganar gaskiya ta kasa cire abinda Taufiq yayi Mata aranta.

Kullum kafin ta tafi office ko bayan ta dawo takan je gidan su Taufiq ta duba Alh Yusuf lamido da jiki Wanda ya ji sauki sosai ya warware , Amma kullum zata ganinsa bata tafiya hannu ba komai sai tayi masa sayayya,

Wannan nuna kulawar da take masa Yana daya daga cikin dalilin da yasa ta Kara shiga ransa Yana matukar jinta araina tamkar yar da ya haifa.

Ta bangaren Alh jibrin kuwa Yana iya kokarinsa wajen ganin ya kusanta Kansa da mujaheeda, duk Kuma wani motsinsu Murtala na gefe Yana kokarin dauiar hotuna.

Yau da wuri mujaheeda ta tashi ,saboda ciwon kan da take yi, hakanan Kuma taji bata son komawa gida a wañnan lokacin dalilin hakan yasa ta wuce gidansu.

Tun zuwanta gidan tana kwance Kan cinyar mahaifiyarta. Duk yadda ta so ta boye Mata damuwar da take ciki saida ta gane tana cikin damuwa.

Duk irin abincin da Haj murjanatu tasa aka dafama mujaheeda ta kasa ci, ta Kuma kawo Mata uzirin bata jindadi ne.

Haj murjanatu tayi Jim sannan tace " ni Kam mujaheeda tun aurenki naji na rasa kwanciyar hankali, na Kuma rasa farinciki,". Mujaheeda tace "saboda mene mummy".

Tace tana bubbuga Saman bayanta kamar Wata karamar yarinya , tace " saboda ina ji ajikina kwata kwata bakya jindadin auren nan, ki dubeki kigani ko irin cikar dakin nan bakiyi ba Saima rama da kike yi kullum, mujaheeda babu abinda bazan iya yi domin Samun farincikinki ba amma kin ki Goya min baya, saboda baki son damuwar mijinki, amma ni kina son damuwata ko ".

Mujaheeda ta gyara kwanciyar ta akan cinyar mahaifiyarta gami da lumshe idanunta, tabbas tana cikin damuwar irin zamantakewar dake tsakaninta da mijinta, burinta a duniya bai wuce ta zauna lafiya da mijinta ba su Zama abokin shawara su Zama jini daya amma hakan ya faskara Kuma ta rasa hanyar shawo Kan matsalar, tunda tayi auren nan bata taba sati uku cikin farinciki ba kullum sabani kullum fada ta yaya Zama zaiyi dadi ahaka zai Kuma tafi yadda take mafarki.

" Mummy ba damuwarki nake so ba, illa iyaka bana son ki dinga Samun matsala da yaya Taufiq don bana son raini ya shiga tsakaninka".

Haj murjanatu tace" to naji, amma yanzu ina son ki gaya min menene matsalar, tsakaninki da Taufiq". Ta girgiza Kai tana kokarin boye duk wata damuwarta tace, " babu komai mummy tsakaninmu lafiya kalau" Haj murjanatu tace cikin ràshin gamsuwa da maganarta " to damuwar meye a fuskarki idan bata Taufiq ba".

Mujaheeda tace " damuwar office kawaii mummy, domin na gano kamfanin nan akwai matsaloli masu yawa acikinta"

Tayi kokarin kauda maganar da Haj murjanatu take son ayi.

Itama Haj murjanatun nan da nan tace " matsala a kamfanin?" .

Mujaheeda ta tashi ta zauna tana kallonta tace " sosai kuwa mummy, shiyasa nake mamaki da kike fadin kirki da rikon amana irin na Alh jibrin, domin bashi da wannan kamalar, Kuma ina zargin tamakar baida gaskiya".

Haj murjanatu tace cike da mamaki" me yasa kika Fadi haka, domin tabbas ina alfahari da gaskiya da rikon amanar Alh jibrin". mujaheeda tace " sanin hakan yasa ban so na gaya Miki komai ba har sai binciken da nake yi ya tabbatar da lefinsa, don haka ko yanzu babu abinda zance Miki sai na Gama bincikena."

Haj murjanatu ta jinjina Kai tace " naso Naji abinda kike tunani amma tunda kince haka Zan Jira har ki gama bincikenki amma kafin sannan ina son ki Kula matukar kulawa don Allah " ta jinjina Kai tace " insha'Allah mummy Zan Kula".

Ta jidadin zaman gidan su bata so ta koma gida amma tunda bata son Haj murjanatu ta fahimci irin zaman da take yi da Taufiq.hakan yasa ta tattara ta koma gidanta gaf da magriba.

****

Tunda aka tashi islamiyya, muhseena ta Lura kwarai da yadda wani matashi yake binta.

Har zuwa lokacin dá suka zo inda zata dauke hanyar shiga gidansu.

Sannan taji matashin saurayin yayi Mata sallama , ta amsa lokaci daya tana waigowa, saurayi ne matashi ba wani kyau gare Shi ba, Amma Yana da matukar kwarjini da Kamala Kuma kallo daya zakayi masa Ka gamsu da natsuwarsa .

" Kiyi hakuri na tsayar da ke ahanya, bayan daga islamiyya kika fito".ta girgiza Kai tace " badamuwa , wani abun kake son tambaya ko me".

Ya dan gyara tsayuwarsa yace " kawai sunanki nake son sani".

Muhseena tayi mamakin wannan tambayar domin dai karamin kauye kamar Durmi idan tace babu Wanda bai Santa ba ko labarinta to tana ganin batayi karya ba.

Kamar yadda bata taba cin Karo da wani da ya tsaya ya tambayeta sunanta ba.

Tadan dubeshi sosai tace " Amma dai da alamar kamar Kai bako ne ko".

Yadan yi murmushi yace " kusan hakanne, Amma dai nan gari na ne nan cibiyata take sai dai nace banyi rayuwa sosai acikinta ba".

Ta gyada Kai tace " sunana muhseena ".

Ya lumshe Ido ya bude yace " suna Mai dadi" tace " nagode, shikenan Zan tafi" yace " ina son yin magana da ke Amma ina ganin tsayuwa ahanyar bai yi tsari ba, don haka idan babu damuwa ina son ki amince min nazo gidan Ku bayan sallar isshai domin mu tattauna ".

Ras muhseena ta Sami kanta da faduwar gaba tunda take yau ce rana ta farko da wani saurayi yayi Mata irin wannan maganar.

A hankali tace" babu damuwa kana iya zuwa".

Yayi murmushi sosai har kasan gemunsa ya lotsa tace," to ina godiya, ina ne gidan naku".sannu ahankali ta Gama yi masa kwatancen gidan sannan sukayi sallama ta tafi.

Ba tare da tasan sunansa ba ko ta tambaya.bayanta shima yabi da kallo harta bacema ganinsa.

Tunda muhseena ta koma gida,take tunanin zuwan saurayin nan, hakan taji tana adduar Allah yasa karshen wahalarta ne yazo , don a yadda take Jin komai aranta ko waye komai talaucinsa in dai zai aureta zata yarda ta aure Shi domin ta fita daga cikin kangin da take ciki Wanda babu Wanda zai fahimci irin kangin da take ciki sai Wanda ya dandani irin rayuwar da

take ciki.

Tun bayan idar da sallar isshai , muhseena ke zaune Kan tabarma ko hijabin bata cire ba,bakinta na cike da adduar Allah yasa yazo kamar yadda yayi alkawari

Sallamar mahaifinta yasa ta dago da sauri tana yi masa sannu da zuwa

Ya amsa Yana kallonta , sannan yace " muhseena kije waje kina da bako".

A gaggauce Hajara da take zaune a gefen tabarmar da muhseena ke zaune tace " bako? Wanene". Mallam Umar yace " yanzu dana dawo daga masallaci na tadda Shi a kofar gida , shine na tambaye Shi abinda yake nema shine ya sanar da ni wajen muhseena yazo, Maza ki tashi kije, ki saurare Shi".

Ande Dije ta dago labule ta fito daga dakinta tana fadin " ikon Allah mafarki ko ido biyu yau muhseena ake sallama da ita tikisa".

Ba tare da kowa ya bata amsa ba, Hajara tace " tashi kije" .

Muhseena ta Mike ta gyara zaman hijabin da ke kanta , sannan ta wuce kofar gidan.

Tsaye ta tadda Shi, sai kamshi yake yi, hatta kayan jikinsa ba su bane na dazu ya canja .

Tayi masa sallama ya amsa, Yana kallonta duk da babu wani haske agun to hasken farin Wata ya rsgema garin duhu sosai.

Yace " gani na zo" ta Dan yi murmushi tace " barka da zuwa".daganan ya gyara tsaiwarsa cikin murya Mai cike da tabbatar da muhimmancin abinda zai fada yace " dazu shine Karo na uku da na ganki tun bayan dawowata garin, Amma tun ganina da ke na farko naji na aminta da ke, naji zuciyata ta Sami nutsuwa da ke ,ma'ana ina sonki so ba na wasa ba, so Wanda zai kaimu ga aure".

Muhseena taji wani abu ya ratsa ta cikin zuciyarta , iya tsawon shekarun da tayi a duniya sai yau ta ji abinda yammata ke ji idan saurayi yace Yana sonsu, domin dai ita bata riskar rana irin ta yau ba.

Tayi kasa da kanta dadi da kunya suna Kara lullubeta . Yace " Baki ce komai ba, Allah yasa wani bai rigani ba".

Ta girgiza Kai a hankali tace " babu Wanda ya rigaka". Yace " Alhamdulillah,". Ya cigaba da cewa.

" Ni suna Kabir , kamar yadda na gaya Miki nan itace mahaifata to hakane nan aka haifeni Amma duk rayuwata nayi ta ne a garin Kano wajen kawuna Wanda shine ya rikeni, a gunsa nayi karatu naje har matakin degree ayanzu haka Kuma ina Taya Shi rike daya daga cikin kamfanoninsa".

Ya hadiye yawu gami da Kara gyara tsayuwarsa, sannan ya cigaba da cewa " iyayena suna cikin kauyen nan mallam Hamza wanzami shine mahaifina," cike da gamsuwa muhseena tace " na fahimta ".

Yace " kinsan a yanzu daga mahaifana har uban goyi na burinsu daya shine nayi aure, to ayau dai adduar su ts karbu domin na Sami matar aure".

Tayi murmushi aranta tana adduar Allah ya tabbatar da hakan, domin dai taji ta aminta da Kabir , gashi dan gayu, gashi dan birni, ga natsuwa da Kamala. Lalle wani hanin ga Allah baiwa ne.

Sun dade Kabir na Kara gayama muhseena ko waye shi.sosai Kuma ta gamsu dashi ranta yayi fes, hakanan Kuma taji ta Bude ma soyayyar Kabir zuciyarta gaba daya.

Awannan daren dai muhseena taji ajikinta itama macece .har suka rabu da Kabir ji take

kamar wasa.

Tana zaune a Kan katifa kusa da Hajara magana suke " yace Shi dan gidan mallam Hamza wanzami ne".

Hajara ta dubi mallam Umar da shigowarsa kenan dakin tace " kaji wai sunansa Kabir Dan gidan mallam Hamza wanzami, dama mallam Hamza Yana da babban yaro ne bayan dansa marigayi habibu".

Mallam Umar yayi Jim alamar tunani , sannan ya dubesu yace, " Kai anya kuwa ko Yana dashi gaskiya ban san Shi ba".

Muhseena tace " eh , yace a Kano ya tashi , bai zauna anan ba". Hajara tace " yauwa ko da naji, to Allah dai yasa alheri , Allah ya kauda duk wata fitina yasa a fahimci juna'. Mallam umar yace " Amin ya Allah, in dai da maganar aure yazo babu wata matsala".daganan ya fice zuwa dakinsa.

Ranar daker muhseena ta iya bacci saboda murnar yau Allah ya kawo Wanda yace Yana sonta , adduar ta daya Ce Kada Allah ya kawo duk wani abu da zai kawo matsala acikin tarayyarta da Kabir, domin dai KO bata son Kabir to fa tana da bukatar tayi aure, balle tana sonsa.

DAGA TASKAR YAR GIDAN IMAM
NIMA MATARSA CE
NA
HÀBIBA ABUBAKAR IMAM
(YAR GIDAN IMAM)
BABI NA ASHIRIN DA DAYA
****

Cikin kankanin lokaci shakuwa ta shiga tsakanin muhseena da Kabir,Kai kace sun dade tare ne .

Domin yadda Kabir ya dorama Kan Shi son muhseena, kullum Yana tare da ita , da Kansa yake Zama a kusa da islamiyyarsu har a tashi sannan su jera tare ya kaita har gida , hakan Kuma bazai Hana ya dawo hira da daddare ba.

Ga kokarin yi Mata kyauta abinda bata taba tunanin samu daga wani ba ballema saurayi data cire ran zata samu .

Yana yawan bata Kudin kashewa ko da taki Karba , baya yarda ya Kan matsa mata dole Saita Karba.

Nan da nan Hajara ta Fara fin karfin wasu daga cikin bukatunta, abubuwa sun Fara yi musu kyau don akalla ko mallam Umar Bai dace da Samo komai wajen buga bugsrsa ba to Hajara bata rasa abinda zata dafa a gidan.

Awannan lokacin sosai Ande Dije ta Fara Jin haushin canjin da suka Fara samu, ta Kara matsa musu da wukakanci da kyara da muzantawa, gami da furta maganganu marasa dadi agaresu irin Wanda ta Saba fada.su Kam sun rasa wace irin tsana ce Ande Dije take musu?.

Hannun Hajara saura kadan ya warke , saboda suna Samun kudin sayen magani babu matsala shima Kuma mallam Umar Yana iya bakin kokarinsa Akan hakan , to Alhamdulillah hannun ya Fara aiki Amma har yanzu baida wani karfi, tana dai lallabawa.

Irin kulawa da soyayyar da Kabir ke nuna ma muhseena, yasa gaba daya ta Kara bude zuciyarta ta dorama kanta kaunarsa, kullum tana yima kanta adduar Allah yasa Kabir shine mafi

alheri agareta .

Domin ta yarda da hankalinsa da nutsuwarsa Uwa uba addini domin ta Lura Yana da ilimin addini sosai don sau tari Tasha tambayar ta aina ta tsaya a islamiyya tana gaya masa zai hau Kara Mata karatun.

Hatta mallam Umar Kabir ya saki jiki dashi sosai, har cikin gidan Yana shiga ya gaishesu su Kuma dan yi hira, ahaka sun San abubuwa da yawa agame dashi.hajara kullum adduar ta bata wuce Allah Kada ya kawo wata matsala agame da aurensu tunda Kabir ya tabbatar musu da cewa auren muhseena yake son yayi.

Ranar wata talata Kabir yazo wajen muhseena sun Dade suna hira kafin Kabir ya dubeta yace " muhseena, gobe idan Allah ya kaimu Zan koma Kano", tayi saurin kallonsa cikin ràshin jindadin maganar tace " zaka koma Kano?". Ya gyada Kai yace " hakan nake so, saboda tuntuni hutun dana dakko ya kare, saboda ke na Kara hutun duk da wayar da kawuna yake tayi min Akan na dawo, har karyar ciwo nayi masa saboda ban son tafiya, Amma yanzu ya Zama dole na koma saboda ya Fara fusata Kasancewar akwai aiyuka da dama a office din rashina Kuma ya tsaida tafiyar aikin yadda yakamata".

Muhseena ta jinjina Kai alamar gamsuwa da maganganunsa, tace " to gaskiya idan hakane kuwa yakamata ace Ka koma bakin aikinka". Ya dago ya zuba Mata Ido yace" ina matukar kaunarki muhseena, ban taba zuwa garin nan naji Bana son na barshi ba irin wannan Karon, ji nake kamar wani bangare na jikina Zan rasa idan na tafi na barki, na rantse Miki ban san lokacin da kika Zama wani bangare na jikina ba, ko don ban taba soyayya da wata ya mace bane sai ke oho". Tayi masa kir da Ido tace " kana nufin kace Baka tsba yin budurwa ba , duk ajinka duk iya kulawa da tattalinka duk Kuma kwarjinin da Allah yayi maka". Yayi Dan murmushi yace " hakane Kada kisa kokonto, ni ban taba soyayya ba amma nasan akwai Matan da suke so na, Amma gareni ban taba son wata ba sai ke". Tayi murmushi tace " to nagode". Ya girgiza Kai yace " ni ne da godiya , domin Samun mace irinki Mai tarbiyya da hankali da Uwa uba sassanyan kyau irinki to sai dai mutum yayi ta godema Allah".

Tayi murmushi gami da maida kanta kasa, ya cigaba da cewa " idan na tafi bazan Dade ba Zan dawo , domin Bana Jin Zan iya daukar wani lokaci batare dana ganki ba, kamar yadda bazan iya daukar dogon lokaci ba , ba tare da anyi maganar auren mu ba ,".

Cikin jindadin maganarsa ta gyara tsaiwarta tace " Allah ya tabbatar mana da alheri ".

Ya Miko Mata wata bakar Leda yace " Ga waya nan na saya Miki, nasa miki layin wayata da bana amfani dashi, saboda ina son ko bayan. Na tafi mu dinga yin magana ina Jin muryarki , nasan hakanne kawai zai rage min radadin rashinki".

Hannunta na rawa tasa hannu ta amsa tana yi masa godiya Mai yawa tare da yi masa addua.

Ya karasa hannu a aljihu ya Ciro kudi yace " gashi ,nasa miki Kati a layin wannan ki rike idan zaki karasa kati ko zakiyi wani amfanin dasu" ta girgiza Kai tace " aah don Allah Ka barshi wannan hidimar ta isa haka , ina godiya da komai amma bazan amshi wannan ba". Yace " Kada ki bata ma kanki lokaci don dole sai kin karbi kudin nan , kinji na rantse , Kuma kinsan a duniya na tsani jayayya ina son idan nace ayi, ayi idan nace abari abari , domin shine alamun mutuntawa da girmamawa". Jin hakan yasa ba tare da Kara yin wani musu ba tasa hannu ta Karba tana godiya sosai.

Kabir da muhseena sun cigaba da hira har lokaci ya ja sannan sukayi sallama cikin tsananin

begen juna , tamkar Kada su rabu.

Duk dadewar da tayi awajen Kabir Hajara ba tayi bacci ba tana zaman jiran dawowar muhseena.kai tsaye Kan katifar da Hajara ke kwance muhseena ta nufa ta zauna kusa da ita gami da Miko Mata ledar wayar.

Da sauri ta amsa ta bude ta zazzage waya ce Mai kyau , don da ganinta zatayi tsada, Hajara ta dawo da kallonta gareta tace " muhseena wannan wayar da gani ba karamar waya bace, Kabir baya gajiya da yi Miki kyauta da hidima , acikin wannan kankanin lokacin da haduwarku ni Kaina bazan iya fadin iya adadin abinda ya kashe Miki ba, tun ina hanaki Karba harna hakura abisa irin dalilan da Kabir ya gabatar a gabanmu".

Ta hadiye yawu sannan tacigaba da cewa " Amma agaskiya ayanzu Bana Jin zamu cigaba da amsar wani abin hsnnunsa ba tare da magabatansa sun shiga cikin maganar ba". Ta dora idonta sosai Kan muhseena tace " saboda ina juye Miki abubuwa da dama , ciki hàrda Bana son ki yi zurfi a soyayya Kabir , ba tare da munji gamsasshiyar magana daga bakin mahaifansa ba, don ina son kisa aranki komai ma zai iya faruwa*.

Muhseena ta hadiye fargaba da damuwarta tace " bakomai Inna duk abinda Allah ya kaddarama bawa babu yadda zaiyi domin baa fushi da yin Allah, don haka shirye nake dana dauki duk kaddarar data hau Kaina" Hajara tayi mata kallon tsaf tace " ciki hàrda kaddarar rasa Kabir a matsayin miji?" .gaban muhseena yayi mummunan faduwa hakanan taji ta gigice ta daburce, ta Kuma kasa ba mahaifiyarta amsa, domin dai ta sani rasa Kabir ba karamin masifa bane agareta.

A sanyaye ta mikama Hajara kudin hannunta tace cikin rawar murya " ga wannan kudin ya bani". Cike da mamaki Hajara ta karbi kudin tace " bayan wayar?" Tace " eh". A hankali ta kirga kudin nera dubu ashirin ne cif.

Ta Kara kallonta da sauri tace " dubu ashirin nefa, lalle Kabir Allah ya saka masa da alheri , " tace " Amin ya Allah".

Muhseena ta tashi taje ta dauro alwalar kwanciya kamar yadda ta saba kullum, ta dawo tayi Shirin kwanciya ta kwanta bayan mahaifiyarta zuciyarta cike taf da tunanin Kabir , da maganar mahaifiyarta na zata iya rasa Shi. Addua sosai ta Sami kanta da yi na Allah Kada ya kaddaro Mata rabuwa da Kabir.

****

Lokaci Mai tafiya da komai, acikin satittikan da akayi, mujaheeda ta Gama fushinta ta sakko , sun Sami zaman lafiya da Taufiq tamkar babu abinda ya faru atsakaninsu.Ta cigaban da zuwa office tare da sa Ido a duk wani motsin Alh jibrin duk da yadda yake nuna mata tsananin gaskiyarsa da biyayya agareta duk da kananan shekarunta da Kuma mugun girman da yayi mata.yana na Nike da office dinta kullum ko ta kirashi ko bata kirashi ba. Tabangaren Alh jibrin kuwa Shi kadai yasan dalilin da yasa yake kusanta Kansa da mujaheeda da sauran al' amuranta.

Yau Taufiq dashi da abokin aikinsa Nura , office suka turasu daya daga cikin kauyakun da suka Sami kwangilar yi musu hanya, Akan suje suga yanayin hanyar . Sun je sun gama komai suna hanyar dawowa saura kadan su shigo jigawa, network ya dawo , nan da nan sakonni suka shiga rige rigen shigowa cikin wayar Taufiq, domin dai sun dade suna inda babu sabis. Da yake Nura ne ke Jan motar yasa Taufiq ya bude wayarsa ya fara duba sakonnin da yake dasu.

Har suka shiga jigawa, suka karasa office Taufiq Yana aikin duba sakonni.

Isar su kamfanin nasu yasa ya aje wayar har saida suka je office din manager suka Kai masa report da komai sannan ya koma office dinsa domin su ba manager damar duba aikin nasu.

Ba wani sauran aiki da yake dashi a office hakan yasa ya fito da wayarsa domin ya karasa duba sakonnin da aka turo masa.

Sakon wata bakuwar number ya bude, domin baida number awayarsa.

Zumbir ya Mike tamkar Wanda aka yima allura, duk ilahirin jikinsa rawa yake kamar mazari.

Ya kafama hotunan da aka turo masa Ido ko kiftawa ba yayi. Hotunan mujaheeda ne tare da Alh jibrin cikin matukar kusanci. Wannan hoton Yana bakin tebur din mujaheeda gab don har tasa hannunta ta taba kirjinsa (alamar kamar mutum zai Fado maka kasa hannu Ka dakatar dashi) daya suna zaune a tebur din cin abinci, daya sun jera gaf da gaf suna magana , wani Alh jibrin ne rike da jakar mujaheeda.kai hotuna dai masu yawa Wanda kowane guda daya Yana bukatar fashion baki, da Karin bayani me yawa

Daga karshen hotunan akayi rubutu kamar haka " kadan daga cikin abubuwan da matarka take aikatawa a bayan idon Ka kenan , akwai gagarumin aiki agabanka na dawo da matarka hanya madaidaiciya domin aikinta Yana kokarin jefata a halaka koma nace ya jefata , alhakin kane Ka nuna Mata gaskiya na cewa ita din fa Matar kace ya Kuma Zama dole ta tsare mutuncinka da kimar Ka, daga mai yi maka fatan alheri ".

Duk da sanyin da akeyi zufa Taufiq yaji Yana yi, shaidan ya Sami abinda yake so nan da nan ya shiga zuciyarsa ya cigaba da kokarin gasgata hotunan ya cigaba da kokarin dasa sabon zargi ga mujaheeda, haka zalika shaidan ya hanashi yayima hotunan kallon fahimta balle hsr ys gano abubuwa da dama agame da hotunan.

Ya koma ya fada Kan kujera Yana maida numfashi tamkar Wanda ya shiga gasar gudu, wani irin bakinciki da takaici ya shiga ratsa zuciyarsa lalla mujaheeda ta cika mara hankali . Abinda ya fada Kenan , Yana Jin tamkar yaje ya shake wuyanta kowa ma ya huta.

DAGA TASKAR YAR GIDAN IMAM

NIMA MATARSA CE
NA
HÀBIBA ABUBAKAR IMAM
(YAR GIDAN IMAM)
BABI NA ASHIRIN DA BIYU
****

shin tsawon wani lokaci mujaheeda ta dauka tana cin amanarsa , kenan duk zargin da yake Mata gaskiya ne.Taufiq yasa hannunsa biyu ya dafe Kansa da yake azabar Sarawa.

Ya maida Kansa ya kwantar Kan tebur ya rasa Abinda ke yi masa dadi, komai ya tsaya masa cak.shi Kansa baisan iya lokacin daya dauka Yana cikin mawuyacin hali ba, daga karshe ya tattara komai ya aje yabar office din.

Cikin matukar damuwa da tashin hankali Taufiq ya isa gida dai dai karfe shida da rabi.ya zubama harabar gidan idanu babu motar mujaheeda alamar bata dawo ba, yasa hannu ya daki sitiyarin motar Yana girgiza Kai.

Ya kusan minti goma zaune acikin motar kafin ya iya fitowa , Yana kokarin rufe kofar motar,

hancin motar mujaheeda ya shigo cikin gidan kallo daya yayi ma motar ya dauke Kansa .

Sam Sam baya son ganin fuskarta, kafin ta Gama parking din motar tuni har ya shige cikin gidan.

Zaune mujaheeda ta tadda Taufiq Akan kujera ya zuba tagumi hannu biyu.ta aje key din motar ta akan tebur gami da aje gelen ta, tana kallonsa " yaya Taufiq mun dawo kusan tare kenan" cewar mujaheeda,

Bai tanka ba, bata damu ba ta cigaba da cewa "kaji wani irin sanyi da yamman nan, ai akwai aikin da ya kamata na tsaya na karasa nace ina gida Zan taho Kaina har ciwo yake min,"

Taufiq baice uffan ba, tadan Kara kallonsa tace " ruwa Zan Samu yanzu Mai zafin gaske nayi wanka ko na rage Jin sanyin".

" Ke don Allah Kada ki dameni da shegen surutunki na tsiya" Taufiq ya fada da karfi cikin fusata, Wanda hakan yasa mujaheeda saurin dawowa hayyacinta tana kallonsa a kidime cike da mamakin irin wannan tsawa daya katsa Mata .

Tace " yaya Taufiq lafiya zakayi min irin wannan tsawar meye yayi zafi?". Ya dubeta da jajayen idanunsa yace " komai ma yayi zafi, wai mujaheeda me kika dauki kanki ne? Sannan me kika dauki aurena da ke kanki". Duk duniya idan akwai abinda mujaheeda ta tsana to fada ne da tsawa da daga murya, don haka tuni idanunta suka Fara kokarin tara hawaye. Tace " meya faru kake min irin wannan tambayar cikin wulakanci gadara da iko, me nayi maka?". Ya saki tsaki ya Mike Yana kallonta afusace " dole nayi miki wannan tambayar idan akayi laakari da muguwar hanyar da kikasa kanki ciki, shin akanki mace ta taba yin aiki, meye Tunaninki da kike ganin zaki ci amanata Allah ya rufa Miki asiri".

Nan ne ta tsaida idanunta akansa cikin bakinciki domin ta Fara tunanin inda maganganun sa suka dosa, tace " cin amana nice nake cin amanar taka, to da nayi me?" Yace " da kike kokarin maida ni sakarai, wancan Karon har fushi kikayi da ni duk da na baki hakuri na maida laifin akaina , yadda kika nuna yasa na yarda da cewa shaidanne kawai ke son yin wasa da hankalina, sai Kuma yau Naga abinda ban taba tsammani ba, saboda haka idan da bani da shaida yanzu ina da shaidar irin cin amanar da kike min". Mujaheeda ta kasa magana ta sa hannu ta dafe kirjinta da yake bugawa, duk sanyin da take ji ta neme Shi ta rasa.dako Taufiq ya Matso kusa da ita Yana falle Mata hotuna tana gani daya bayan daya sai ji tayi zufa na kwarara asaman goshinta.

Cikin rawar harshe tace " waye ya tura maka wadannan hotunan da Banda masaniya akansu," ya daka Mata harara yace " Baki da masaniya akansu, to wacece a hoton" muryarta na rawa tace " nice, Amma bansan sanda aka dauka ba, domin duk abinda ya faru acikin hoton babu cin amana aciki, mafi yawancun hotunan an daukesu ne alokacin da Muke aiki ni da Alh jibrin" ya Kara zuba Mata harara gami da daka Mata tsawa ya Nuno Mata wani hoton Wanda tasa hannu ta taba kirjin Alh jibrin yace " wannan Kuma Kuna me aka dauke Shi , nace kuna me?". A gigice tace " ya shigo office ne kafet ya tadiye Shi shine zai Fado Kaina nayi sauri nasa hannuna nayi masa Katanga daga fada min". " Karya kike yi, nace karya kike yi" ya fada da karfi cikin matukar fusata.

Da sauri mujaheeda ta runtse idanunta tasa hannu ta dafe gefen kirjinta wajen zuciyarta da taji tana Mata mugun zafi tamkar zata keto kirjinta ta fito.

Cikin sakwannin da basu wuce biyu ba mujaheeda ta yanke jiki ta Fadi. Hakanne ya dawo da Taufiq hayyacinsa da sauri ya zube kasa Yana jijjigata gami da Kiran sunanta.nan da nan ya

gigice musamman da ya ji duk jikinta babu inda yake motsi, baisan lokacin daya dau makullin mota ya jefa a aljihunsa ba sannan ya tattageta cak ya dagata ya fita da ita Yana tsuma.Asibitin data Saba zuwa ya wuce da ita.

Bai Sami sukunin Kiran kowa ba har saida aka karbi mujaheeda aka bata gado likitoci suka shiga aiki akanta, sannan ya Sami numfasawar da ya daga waya ya Kira Haj murjanatu, sai da wayar ta kusa katsewa sannan ta dauka, cikin tashin hankali ya gayá Mata suna asibitin da mujaheeda ke ganin likita ciwonta ya tashi.

Tashin hankali Haj murjanatu ta rude ta shiga tambayar sa " me kayi ma yata ? Me kayi ma mujaheeda?" Yayi shuru Yana Jin yadda take huci awayar.

Ta cigaba da cewa" na rantse maka matukar wani abu ya sami yata sai munyi shara'a da Kai, sai Naga Wanda ya tsaya maka, sai kayi mamakin yadda Zan maida Kai abin kwatance". Da sauri ya kashe wayar domin Jin yadda Haj murjanatu ta koma tamkar wata zararriya.

Daganan ya Kira mahaifinsa ya sanar da Shi, hakama mahaifiyarsa duk sun damu.sannan ya Kira Alh Mustapha labaran ya sanar dashi.

Cikin kankanin lokaci Haj murjanatu ta iso asibitin Dama tun kafin ta iso ta Kira Dr Balarabe ta sanar dashi mujaheeda tana asibitin anan ya tabbatar Mata Yana daya daga cikin likitocin da suke kanta.ko ta Kan Taufiq bata bi ba tukuna tana tsaye bakin kofar da mujaheeda take ciki, sai dai ta Kai gauro ta Kai Mari , jefi jefi Kuma tana sakar ma Taufiq harara Wanda shima ya ke tsaye a kusa da kofar dakin ko gaisuwarsa bata amsa ba.

Fitowar likitocin yayi dai dai da isowar Alh Mustapha labaran,Dr Balarabe ne ya tsaya wajen Haj murjanatu Yana yi Mata bayani, Alh Mustapha labaran ya dube Shi yace " yanzu an Sami allurar da akayi Matan" Dr Balarabe yace " itace ta bada wahala allurar daker aka Samo ta nera dubu sittin yanzu zaa biya sannan akalla sai anyi Mata allurar sau shida kafin ta dawo yadda ake bukata".

Haj murjanatu tace da sauri " ko nawa CE za'a biya ni kawai bukatata yata ta Sami lafiya" Dr Balarabe yace " insha'Allah Zata Sami sauki babu damuwa, yanzu nan da minti talatin zata dawo hayyacinta insha'Allah ". Ya karasa maganar Yana wucewa zuwa office dinsa

Gaba daya Haj murjanatu da Àlh Mustapha labaran suka shige cikin dakin domin ganin mujaheeda. Shima Taufiq din da sauri ya bi bayansu amma Yana shigowa Haj murjanatu ta juyo a fusace cikin daga murya tace " fita Ka Bani waje, bana bukatar ganinka kusa da yata " Alh Mustapha labaran ya dubeta cikin mamaki yace" wace irin magana ce wannan bakya bukatar ganinsa kusa da mujaheeda don me? Mijinta ne fa".

' Mijin ta din me, mutumin da yake kokarin kashe min ya" Alh Mustapha labaran yace " ya kike irin wannan maganar ta yaya Taufiq zai kashe mujaheeda amatsayin sa na mijinta, ko kuwa ciwon mujaheeda bazai iya tashi hakanan ba daga Allah har sai Taufiq ya Zama sila". Zata yi magana kenan Alh Yusuf lamido da Haj saratu suka shigo dakin da yake tun kafin zuwansu Taufiq ya gayá musu dakin da mujaheeda take.

Nan da nan Alh Mustapha labaran ya shiga kokarin boye maganar da suke yi ta hanyar yi musu sannu da zuwa, amma ina Haj murjanatu fada ta cigaba da Shi" ina da yakinin shine dalilin tashin ciwon mujaheeda domin tunda ta aure Shi kullum cikin bata Mata rai yake, saboda tsabar mugunta yafi kowa sanin mujaheeda bata bukatar bacin rai amma tunda ta Fara aikin nan kullum idan bai bata Mata rai ba baya sukuni". Haj saratu tace " haba Haj ya kike irin wannan maganar , Kuma a irin wannan lokacin da bai kamata ba". Ta dubeta sosai tace " koma

dai menene bazan fasa fada ba wannan Karon duk abinda ya Sami yata bazan taba yarda ba sai munyi shara'a da Taufiq". Anan ne Taufiq ya Kai matuka gurin hasala a fusace ya bude baki zaiyi magana Alh Yusuf lamido yayi saurin daga masa hannu yace " Kada kayi magana". Hakan yasa ya hadiye abinda yayi nufin fada ya juya ya fice daga dakin cikin matukar takaici.

Alh Yusuf lamido yace " don Allah ayi hakuri abar maganar har Allah yaba mujaheeda lafiya Muji komai daga bakinta, idan har Taufiq ne ya janyo faruwar wannan al'amarin ni Kaina Zan hukunta Shi, amma yanzu dai Samun lafiyarta shine abin nema". Haj murjanatu zatayi magana kenan Alh Mustapha labaran ya dubeta yace " na hadaki da girman Allah ki yi hakuri ki bar maganar nan". Ta jinjina Kai cike da fushi ta zauna kusa da yarta tana shafa ta, hawaye ya Fara fita Mata ahankali take fadin " Allah ya baki lafiya, wannan ciwo Yana wahalar da ke inda Zan bada duk abinda na mallaka ki warke daga wannan cutar hakika dana bayar, bani da wata damuwa aduniya sama da wannan ciwon naki, Bana son bacin ranki Bana son damuwarki saboda sune sanadin tashin ciwonki Amma Kin Sami miji mara Imani Wanda Bai damu da ke ba ke kadai kike sonsa". Irin wannan maganganun Haj saratu ba zata iya jurar su ba Kuma bata son su raba abin fada a asibiti hakan yasa ta dubi mujaheeda da har yanzu tana kwance kamar matacciya tace " Allah ya baki lafiya" tana Gama fadan hakan ta juya ta fita tana cema Alh Yusuf lamido " ina wajen mota Alh" kafin ya Sami karfin guiwar tsayar da ita tuni harta fita.

Shine yadan tsaya ya Kara dubata sannan yayi musu sallama ya fita ba tare da Haj murjanatu ta ko kalleshi ba balle ta amsa sallamar da yayi Mata. Alh Mustapha labaran ne ya bi bayansa , suna fita ya shiga bashi hakuri yace " kasan halin ta bata Raina abin magana ga zargi na banza da wofi". Àlh Yusuf lamido yace " babu komai Kada kadamu, Allah dai ya bata lafiya" yace "amin, Allah ya kiyaye hanya angode" daganan sukayi sallama ya koma cikin dakin, Shi Kuma ya nufi wajen motarsa.

Tsaye bakin motar ya tadda Taufiq da Haj saratu da alama magana suke yi, yayi masa kallon tsaf tacee" Kai Taufiq ya akayi ciwon mujaheeda ya tashi meya faru ko kuwa dai hakanan ciwon ya tashi".

Taufiq yayi shuru Yana jinjina maganar da zai fada, Alh Yusuf lamido ya daka masa tsawa yace " dakai nake magana ko baka jina ne?".

Haj saratu tace " haba Alh meye na wannan tsawar, Kabi komai ahankali mana" ya dubeta rai a bace yace " Anki abi ahankalin, Dama ai nasan kece ke daure masa wajen Zama yàke yin abinda yake so, kina kallonsa tamkar wani ma'asumi da baya laifi, Kuma wannan kuskure ne".

Haj saratu zatayi magana yace " Kada kice min komai ki bari Wanda na tambaye Shi ya bani amsa" ta hadiye maganarta rai abace ta juya ba tare da tace uffan ba.

Àlh Yusuf lamido ya Kara kallon Taufiq cike da zargi yace ' me kayi Mata Taufiq ". Yadan gyara tsaiwarsa yace " Abba mun Sami sabani ne da ita". Ya aje numfashi cike da damuwa yace " wai Kai don Allah meke damunka , shin Baka shirya zaman auren ba kayi, Kai Nama fahimci baka San meye auren ba, shin Baka son yarinyar nan Ka aure ta , kafi kowa sanin lalurarta amma ba zaka tayata Samo lafiyarta ba ,".

Ya kafe Shi da Ido yace " me tayi maka?" Haj saratu tace " tun farko tambayar da ya kamata kayi masa kenan" ya dubeshi yace " to nayi masa yanzu".

Taufiq yace " Abba Zan zo gidan Zan gaya Maka komai". Ya Bude mota ya shiga sannan ya ce" ina jiranka ". Haj saratu ta shiga motar tana ma danta kallon tausayi.

Da gudu ya ja motar tabbatar Yana cikin fushi.

Taufiq ya runtse idonsa Yana kokarin maida hawayen dake kokarin fito masa, Anya yayi Saar aure kuwa? Tunda yayi auren nan bai Sami natsuwa ba balle kwanciyar hankali, Yana son matarsa Amma dalilai da yawa na son maida soyayyar kiyayya, shin yaya zaiyi?

Anya mahaifinsa zai fahimce Shi kuwa, sannan ya zaiyi da Haj murjanatu da take kokarin daura masa jakar tsaba.

DAGA TASKAR YAR GIDAN IMAM

NIMA MATARSA CE
NA
HÀBIBA ABUBAKAR IMAM
(YAR GIDAN IMAM)
BABI NA ASHIRIN DA UKU
****

Tsana da kiyayyar da Ande Dije ke yima muhseena da mahaifiyarta ya Kara kamari tunda muhseena ta daina daukar Mata talla ta koma islamiyya, ko kallon arziki bata yi Mata ko gaisheta tayi daker take amsawa.

Ga Uwa uba takaicin shigowar Kabir cikin rayuwar muhseena domin taga yadda suka Fara fin karfin abubuwa da dama, rayuwarsu ta Fara canjawa, domin dai ko bayan da Kabir ya koma Kano kullum Yana hanyar turoma muhseena sakon kudi ta asusun bankin wani abokinsa salisu Wanda shine ke kawo Mata sakon kudin ya Kuma duba masa lafiyarta kamar yadda ya dora ma salisun kulawa da muhseena.

Bugu da Kari kullum idan Kabir bai Kira muhseena ba ya kirata sau hudu a rana, irin Kuma hidimar da yake Mata Ko tace ya daina ko ya rage bai sauraronta illama yayi Mata fadan ta daina cewa haka domin ya riga ya dorama Kansa nauyin Kula da ita.

Domin dai tun Fara zuwa gidansu muhseena, Kabir ya gamsu da cewa suna bukatar taimako ya Kuma daukar ma Kansa taimaka musu da abinda Allah ya hore masa, balle yanzu da ya dauki soyayyar muhseena ya Dora aransa Yana matukar Sonta Yana jinta ajikinsa.tunda ya koma Kano bakin aikinsa baida tunani Saina muhseena sosai ya rage walwala a office domin kowa yasan halinsa na wasa da dariya baida daure fuska baida fushi ko da ko me akayi masa.

Amma tun dawowarsa daga Durmi duk ya canja ko magana bai damu da yayi ba, hatta mutanen office dinsu sun Lura da hakan.

Yana son muhseena Yana Jin tausayinta , burinsa ya aureta ya inganta rayuwarta, baya Jin akwai abinda bazai iya yima muhseena ba domin Samun kwanciyar hankalinta.

Tunda Kabir ya shigo rayuwarsu hatta abinci baya yanke musu ko babu dadi zasu dafa su ci. Hajara hannunta ya dawo dai dai Kuma Kabir dinne ya cigaba da daukar nauyin kudin maganinta.

Sosai abubuwa su kayi musu sauki.harga mallam Umar ya sami sassaucin abubuwa da dama.amma ga Ande Dije abin baiyi Mata dadi ba , tafi son tayi ta ganin Hajara cikin ràshin kwanciyar hankali da sukuni sai kace wacce tayi Mata wani mugun abu.

Muhseena na Kan waya ita da Kabir ne ya kusa awa daya da Kira Amma har zuwa yanzu bai katse ba.hajara ta shigo dakin shine shigowarta na biyu muhseena na waya ta dauki ashana

ta fita.

Kwarai itama muhseena yadda Kabir ya kamu da sonta haka itama ta kamu da sonsa , bata taba soyayya ba sai akansa don haka gaba daya ta bude zuciyarta ta saka Shi a ciki.cikin matukar so da kauna suka gama wayar gami da sallama.

Muhseena tayi kasa da wayar tana dan murmushi, dai dai lokacin Hajara ta Kara shigowa dakin.ta dubeta sosai tace " Allah yayi angama wayar" tadan yi murmushi tace " eh Inna". Hajara ta nemi gefen katifar kusa da muhseena ta zauna tana dan dubanta , kafin tayi magana muhseena tace " Inna Kabir yace jibi zai zo". Hajara ta numfasa tace ' najidadin hakan,' sannan ta Kara gyara zamanta ta cigaba da cewa " saboda ina son muyi magana da Shi sosai, Bana son sai kin Gama zura kanki kin Saba da Kabir sannan azo arabaku".

Da sauri cikin faduwar gaba muhseena ta dubi màhaifiyarta tace " Inna me yasa kikace haka".

Hajara damuwa da bayyana sosai a fuskarta ta aje numfashi a hankali tace " akwai matsaloli sosai muhseena ba Kuma na son hakan ya Kara taba rayuwarki kin sha wahalar jure Jin mugayen kalamai Akan rayuwarki da har yanzu baki Gama sanin komai akanta ba".

Jikin muhseena ya Kara matukar sanyi, tayi shuru gabanta na faduwa tana kallon mahaifiyarta cikin fargaba.

Hajara tayi dibarar goge hawayenta da ya ke kokarin fito Mata ta cigaba da cewa " ko kadan Bana son ki shiga mugun yanayin dana shiga a baya nasan zafin rabuwa da masoyin daka shaku da Shi, hakan yasa Bana son ki shiga yanayin da na shiga domin zai yi matukar nakasa Tunaninki"

Muhseena ta numfasa cikin Karin fargaba tace " Inna me yasa kike tunanin Kabir zai iya fasa aurena" ta girgiza Kai tace " ba Kabir bane nake fargabar zai fasa aurenki, mahaifansa ne nake fargabar zasu Hana Shi aurenki" " saboda me Inna". Muhseena ta tambaya a gajarce.

Hajara tayi shuru ba tare data amsa Mata ba, muhseena tace " saboda dalilin da kika kasa gaya min gaskiyarsa har yau, haka zalika saboda dalilin surutan da mutanen gari su keyi Wanda har yanzu kika kasa gaya min gaskiyar".

Hajara ta dubeta sosai tace " wace gaskiya kike son sani bayan wacce kika riga kika Sani,"

Ta Kara kallonta sosai tace " Baki da wani uba da ya wuce mallam, duk surutun Mai surutu bai isa ya canja hakan ba".

" To idan hakane Mai yasa kike fargabar mahaifan Kabir zasu Hana auren mu" Hajara tace " saboda irin maganganun da mutane ke yi Wanda kema ya ke son juya Miki tunani kullum, balle mahaifansa da suke cikin garin Durmi suka San komai, Bana son kisa kafarki acikin takalmina".

Gaba dayansu su kayi shuru na wani lokaci, sannan Hajara ta cigaba da cewa " Shi yasa nake son idan ya zo muyi magana da shi ya turo iyayensa, ke Kuma kisama kanki dangana akan duk hukuncin da ya biyo baya". Muhseena ta gyada kanta tace " insha'Allah ". Daganan ta yi tagumi komai ya tsaya Mata tunani ya addabi ruhinta kullum mahaifiyarta na nuna Mata tayi hakuri don ba lalle bane ta auri Kabir , ita Kuma zuciyarta ta kasa yakice Kabir ta kasa sassauta ma kanta soyayyarsa balle nisanta dashi, duk da kullum cikin fargaba take da damuwa gami da tunanin inda zatasa kanta idan har hakan ya kasance.

****

Da kuka mujaheeda ta farfado, da sauri Haj murjanatu ta sa hannu ta rungume ta, tana Kiran

sunanta . Jin muryar mahaifiyarta yasa tayi sauri ta Karasa Bude idanunta gami da sa daya hannunta da ba'a daura masa ruwa ba ta rungume Haj murjanatu tana Kiran " mummy ".

ÀIh Mustapha labaran ya Matso shima sosai kusa da yarsa Yana kallonta Yana Kiran sunanta.

Taufiq dake jingine jikin kofar dakin ya turo kofar ya shigo a rude ya dauka wani abu ne ya sameta don yadda ya ji ÀIh Mustapha labaran Yana Kiran sunan mujaheeda.

Idon mujaheeda dore Kan Taufiq , nan da nan ta saki Haj murjanatu cikin fushi tace " me kake yi anan yaya Taufiq, ba so kake Ka kasheni da bakinciki ba me yasa zaka zo inda nake bayan abinda kake so kenan, ".

Haj murjanatu ta riketa sosai tace "don Allah ki kwantar da hankalinki , daker aka Samo lafiyarki Bana son ki Kara fadawa halin da kika fito Kan Wanda Bai damu da ke ba Bai damu da mutuwa ko rayuwarki ba" .

Alh Mustapha labaran ya dubi Taufiq cikin mamaki yace " Taufiq meke faruwa ne, wace magana mujaheeda take yi, ko kana nufin kace duk zargin da Haj keyi Akan Ka gaskiya ne".

Kafin yayi magana Haj murjanatu tace cikin matukar fusata da tsana " duk abinda na fada akansa ba zargi bane gaskiya ne, Kuma kamar yadda na fada ne sai na dauki kwakkwaran mataki akanka sai kayi mamakin irin fansar da Zan daukar ma yata,don ban hada komai da yata ba a duniyar nan".

Mujaheeda tace Ido a runtse " don Allah daddy kacema yaya Taufiq ya fita , dagaske Bana son ganinsa ". Alh Mustapha labaran yaja hannun Taufiq suka fita daga dakin.

Tsaye sukayi a waje Alh Mustapha labaran Yana kallon Taufiq sosai idanunsa cike da neman Karin bayani.

Yace " Taufiq meke faruwa tsakaninka da matarka, na yarda da hankalinka da Kuma son da kake ma mujaheeda hakan yasa nake tunanin ba zaka taba yin abinda zai cutar da mujaheeda, sabanin yanzu da na shiga shakka tun daga yadda mujaheeda ta nuna bayan shigowarka, shin meke faruwa".

Taufiq yayi kasa da Kansa Yana Jin tamkar yayi kuskure , daga yadda idanun mujaheeda suka nuna babu komai acikinsu face gaskiya.shin ko dai yayi kuskure ne kamar yadda yayi da wajen zarginta , shin wadannan hotunan da aka turo masa sun isa su sa Shi zargin matarsa?

" Kai nake sauraro Taufiq" cewar ÀIh Mustapha labaran cikin kaguwa da son sanin amsar tambayarsa.

Taufiq ya dago ya dube Shi yace " Alh maganar tana da nauyi", Alh Mustapha labaran yace " komai nauyinta ya Zama dole Ka fada ".

Taufiq ya numfasa yace " ina cikin zargin mujaheeda ne adalilin wasu hotuna da aka turo min hakan yasa nake zargin tana cin amanata ne ".

Alh Mustapha labaran ya saki salati cikin ràshin jindadin maganar ya zuba masa Ido yace " what?(Mene)" ya gyada Kai yace " hakane Alh, bayan ganin hotunan ne na yi Mata magana shine dalilin tashin ciwon ta ".

Alh Mustapha labaran ya Mika masa hannu yace " Bani hotunan na gani ".

A sanyaye ya Ciro wayarsa a aljihunsa ya Danna ya fito da hotunan ya Mika masa wayar

yace " gasu Àlh".
Ya Mika hannu ya karbi wayar.

DAGA TASKAR YAR GIDAN IMAM

NIMA MATARSA CE
NA
HÀBIBA ABUBAKAR IMAM
(YAR GIDAN IMAM)
BABI NA ASHIRIN DA HUDU
****

Ya shiga duba hotunan daya bayan daya, har ya Gama kallo sannan ya dago Kansa Yana kallon Taufiq sosai, yace " Amma banjidadi faruwar abinda ya faru ba, babu Wanda ya zugaka ya Kuma tilasta maka ganin laifin hotunan illa shaidan".

Ya Kara matsowa kusa dashi Yana kokarin Mika masa wayar yasa hannu ya Karba a sanyaye.sannan Alh Mustapha labaran yace "Ta Yaya ko amanarka mujaheeda zata ci , ta rasa da Wanda zata ci amanarka sai Alh jibrin, mutumin da ya haifeta, Kuma amintaccen mahaifiyarta ne, Shi Kansa bazai iya cin amanar Haj ba,Kuma nayi mamakin da ka kasa gane duk Wanda ya turo maka wadannan hotunan yayi ne don kawai ya shiga tsakaninka da matarka".

Ya nisa ya cigaba da cewa " ban so faruwar hakan ba banso kayima mujaheeda magana ba ba tare da sanin ainihin gaskiya ba, Kuma Ka sani babu abinda mace ta tsana a duniya sama da mijinta ya zargeta akan abinda bata aikata ba Kuma zargi a aure babu inda yake Kai auran sai tafarkin rabuwa, ko Kuma a daina ganin mutuncin juna ".

Taufiq ya yi kasa da Kansa zuciyarsa ta Fara nadamar faruwar komai, Amma ya kasa cewa uffan.

Alh Mustapha labaran yace " don haka ina son kaje Ka zauna Ka natsu kayi ma duk hotunan nan kyakkyawan kallo da fahimta ananne zaka gane Basu dauke da abinda kake zargi" Taufiq ya gyada Kai yace " to Alh nagode ".

Alh Mustapha labaran ya Kara kallonsa yace " zuwa yanzu dai ina son ka tafi kabar asibitin saboda yadda Haj ta fusata ko ni bazan iya shawo kanta ba idan yaso idan ta sakko komai ya lafa Zan sanar da Kai da Kaina kazo mu zauna Duka ayi magana".

Shi Kansa Taufiq din zai fi bukatar ya Sami lokacin Kansa da zai zauna yayi nazari yadda ya kamata zamansa a asibitin kuwa zai iya sawa ya Sami sabani da Haj murjanatu domin yadda yake da saurin fushin nan Bai Jin duk ràshin gaskiyar sa zai yarda ta ci masa Kashi aka, don haka ya amince da abinda Alh Mustapha ya fada. Yayi masa sallama sannan ya juya ya tafi Shi Kuma ya Kada Kansa ya koma cikin dakin.

Har yanzu mujaheeda na rungume a jikin Haj murjanatu, da alama Kuma mujaheedan ta Gama gaya Mata duk abinda ya faru tsakaninta da Taufiq, idan yayi laakari da yadda ta Kara fusata matuka.

Alh Mustapha labaran ya dubeta yace " don Allah ki kwantar da hankalinki ki Sami natsuwa Haj a asibiti fa Muke ki Bari mana ta Sami sauki koma me zaayi sai ayi".

Haj murjanatu ta dubeshi da jajayen idanu tace " wannan Karon Taufiq zai gane ya tabo ni, har ya isa ya jefi yata da Kalmar zina ni ban haifi maxinaciya ba Kuma zai yi nadamar fadin hakan" Alh Mustapha labaran ya girgiza Kai yace " yaushe yace Mata mazinaciya? Aah kadafa ki maida maganar wata iri" ta Watso masa Ido tace " meye bambancin kana zargin matarka da zina , ai abinda yake nufi kenan Kuma ma don wukakanci da Alh jibrin Kai Kai gsskiya Taufiq ya ci mana mutunci ya zaluncemu".

ÀIh Mustapha labaran ya daga Mata hannu yace " naji Amma don Allah ki bar maganar nan don babu amfanin yinta anan ki bari mu koma gida tukuna".

Ya dubi mujaheeda yace " ke Kuma ki daina wannan kukan ki yi shuru don baida amfani, Kuma ba wai warkewa kikayi ba hakan zai iya sawa ciwon ya Kara tashi kin dai fi kowa sanin dalilin tashin ciwonki saboda haka ya Zama dole ki kiyaye"

Haj murjanatu tasa hannu tana goge Mata hawaye tana cewa " ki daina zubar da hawayenki Akan Wanda bai cancanta ba , Taufiq dai dole ya sake ki don ni ban shirya rasaki ba"

Gaban mujaheeda yayi mummunan faduwa duk da tana cikin fushi da Taufiq bata Jin zata iya rabuwa dashi domin har yanzu tana son sa fiye da tunanin me tunani." Subhanallah haba Haj ta yaya kike irin wannan maganar ki kashema mujaheeda aure a wane dalilin" ta ce " adalilin kashe min ya da yake son yi da Kuma zargin banza da wofi da yake yi akanta"

" To wannan ba ita bace mafita babu maganar saki, Zama dai zaayi ayima hanci tufka Amma har yaushe akayi auran da zaace zaa rabu".

Cikin fusata tace " to rabuwar aure da mutum irin Taufiq har wani abin damuwa ne, shiyasa tun farko ban so auran nan ba don nasan babu abinda zata samu a auran talaka sai bakinciki da kuntatawa amma saboda kwanciyar hankalinta na yarda ta aure Shi don gudun damuwarta Amma Shi ya kasa gane alfarmar da akayi masa na auran mujaheeda to zai sani, idan ma baya hayyacinsa ne zai dawo hayyacin nasa ".

Cikin kosawa da maganar ÀIh Mustapha labaran yace " duk naji a dai bar maganar zuwa ta samu lafiya". Ta saki tsaki gami da Kara rungume mujaheeda ji take tamkar ta cire duk wata damuwarta ta dawo da ita kanta, tana son yarta matukar so akanta zata iya yin komai.

Tun fitar Taufiq daga asibitin Yana zaune cikin motarsa ya kasa tuka motar idonsa na kafe Kan hotunan mujaheeda da Alh jibrin ya natsu ya tattara hankalinsa Kan hoton sosai yake son ya gane gaskiyar lamarin.

Kwayar idon mujaheeda acikin dukkan hotunan babu Wanda ya nuna son Alh jibrin aciki, haka zalika duk yanayin zaman daukar hoton baiyi Kama da Zama na soyayya ba.

Hatta hoton da mujaheeda ta taba jikin ÀIh jibrin ya tsaya yayi masa kallon tsaf yanayin fuskarta da yanayin data nuna a tsorace take alamar abin da batayi tsammani ba Yana gaf da faruwa, hakan yasa ya Fara gasgata maganarta na cewa kafet ne ya tadiye Shi ya kusa fadowa kanta cikin ràshin sani .

Nan da nan zuciyarsa ta Fara gaya masa Anya baiyi garaje ba , Anya baiyi saurin yanke hukunci ba.

Ya Fara ji aransa tamkar yayi kuskuren Kara zargin matarsa, wai meke faruwa ne? Zaman kwanciyar hankali da jindadi yasa ran yi da mujaheeda shin meyasa sabanin hakan ke kasancewa?. Kiran mahaifinsa daya shigo wayarsa ya katse masa komai da sauri ya dauka daga yanayin maganar ÀIh Yusuf lamido Kadai Taufiq ya gamsu da cewa baya bukatar wata

doguwar gaisuwa ko magana , ce masa kawai yayi Yana nemansa yanzun nan, Taufiq ya tabbatar masa gashi nan zuwa.

Daker ya iya tada motar, cikin matukar damuwa ya yima gidansu tsinke tare da adduar Allah yasa ba wata damuwar bace.

****

Bayan isarsa gidan zaune ya tadda Alh Yusuf lamido acikin falonsa , rike da karamin kur'ani Yana karantawa

Hakan yasa Taufiq ya dade da Zama a falon har Haj saratu itama ta shigo , bai Gama karatun ba sai daga bisani sannan ya rufe kur'anin ya Mika Shi inda yake ajewa.

Sannan ne ya dawo da kallonsa ga Taufiq gami da gyara zaman gilas din dake idonsa.

" Gani Abba" cewar Taufiq, Alh Yusuf lamido yace " surukarka ta Kira mahaifiyarka da kakkausan lafazi tayi magangsnun data Saba yi marasa dadi Wanda basai na gaya maka ba, Amma dai duk da haka na fahimtar da mahaifiyarka cewa Dan kuka Shi ke jama uwarsa jifa, don haka duk irin maganganun da ta gaya Mata Kaine Ka ja Mata".

Kasa kawai yayi da Kansa, ayayinda Haj saratu ta dube Shi sosai tace " Taufiq ina ce mun gama wannan maganar Me Kuma ya dawo da ita?".

Alh Yusuf lamido ya Kara cewa " kana Jin tambayar da tayi maka ". Taufiq ya numfasa yace " na gamsu da duk abinda kika gaya min hakan ne yasa Muka Sami daidaito a tsakaninmu komai ya wuce , to bayan hakane sai Kuma aka turo min wasu hotuna". Sannu ahankali ya gayá musu komai sannan ya fito da hotunan ya Mika ma mahaifiyarsa wayar bayan ta Gama kallo ne ta Mikama Alh Yusuf lamido shima ya amsa Yana kallo.

Alh Yusuf lamido ya dade Yana kallon hotunan Yana nazari kafin daga bisani ya Mika masa wayarsa, Yana yi masa wani sakaran kallo sannan yace " idan Baka iya kama barawo ba to lalle barawo zai kamaka , an gaya maka aure wasa ne, don me zaka dinga zargin matarka wai Kai dakatama Dama yarinyar nan baka Sonta Ka aureta?".

Haj saratu tace cikin damuwa " ni dai na fara damuwa da lamarin nan, tun da akayi auren nan babu wani kwanciyar hankali sai kace ba auren soyayya ba , na rasa inda matsalar take" Alh Yusuf lamido ya nuna Taufiq yace " matsala tana wajen danki, matukar ba zaisa hakuri acikin zaman aurensa ba ba Kuma zai daina saurin fushi da saurin yanke hukunci ba to fa bazai taba zama lafiya agidan sa ba".

Kasan illar da zargi yakema aure kuwa, Kuma Kai zaka bada shaidar kamewar mujaheeda ba sai Ka Jira wani ya baka ba, Kuma Shi Wanda ya turo maka hotunan kasan shine?" Ya girgiza Kai alamar a'ah, ya girgiza Kai yace " kaji shashanci, ko wannan ya isheka shaida, idan har gaskiya yake fada me yasa zai boye Kansa, ya bayyana Kansa mana ya gayá maka, to duk Wanda ya turo maka burinsa ya rabaka da matarka Kuma ina ganin burin nasa ya kusa cika".

Da sauri Taufiq ya dago ya dubi mahaifinsa kamar yadda Haj saratu ta dube Shi tace " burinsa ya kusa cika Kuma" yace " kwarai kuwa, domin mujaheeda yata ce farincikinta da kwanciyar hankalinta shine Kan gaba ko tana da lafiya bazan lamunci wannan wulakancin ba balle bata da lafiya ko tausayi Baka da Shi don haka gara tun wuri idan Baka Sonta ne ko Kuma zargin da kake Mata yayi kamari yadda bazai iya barin ranka ba to gara Ka sallameta Allah ya hadata da Wanda ke Sonta tsakani da Allah".

Nanne Taufiq yace agaggauce " Abba ina son matata Bana Jin Kuma akwai abinda zata yi min da Zan iya rabuwa da ita" ya girgiza Kai yace " to idan hakane me yasa kake kokarin bata dangantakarku Ko kana tsammanin mujaheeda zata taba mantawa da wannan batancin haba Taufiq Ka dinga sama kanka hakuri da juriya Kaifa namiji ne akwai gwagwarmaya sosai agabanka ya kamata kayi tunani ka tsaya Ka Zama namiji Wanda zaa dinga kwatance dashi na alheri Bana sharri ba".

Haj saratu tace " gaskiya ne Taufiq yakamata ace zuwa yanzu babu wannan maganar Ka rungumi matarka Ku zauna lafiya wannan cece kuce duk abarshi kafi kowa sanin Haj murjanatu da irin yadda take daukar zafi idan har abu ya hado da mujaheeda don haka ya Zama dole matukar kana son cigaba da Zama da mujaheeda Ka koyi yadda ake hakuri da sadaukarwa"

Alh Yusuf lamido yace " kadama ya koya ranar daya rasata ai ya gane muhimmancin abinda ya rasa".

Cikin damuwa da nadama Taufiq yace " nasan nayi kuskure don Allah Abba kuyi hakuri insha'Allah hakan ba zai Kara faruwa ba" Alh Yusuf lamido yace " bamu zaka ba hakuri ba kaje kaba wacce Ka batama hakuri".

Haj saratu tace " babu komai Allah ya daidaita tsakaninsu ya Kuma bata lafiya, wannan Kuma ya Zama na karshe duk abinda wani zai turo maka Baka da hujjar zargin matarka har sai kagani da idonka don Sharia sabanin hankali ce" yace " insha'Allah Zan kiyaye" Shi dai Alh Yusuf lamido Bai Kara tankawa ba illama rai da ya Kara hadawa ya dau wayarsa ya fita harkarsu.
Hakan yasa Taufiq yayi sallama dasu jikinsa babu laka ya tafi.

Kullum Taufiq sai yaje asibiti Amma babu wani sassauci tun daga Kan mujaheeda har mahaifiyarta domin dai mujaheeda ko magana taki masa, balle Haj murjanatu da kullum fada. Ke tsakaninta da Shi. Hatta su Alh Yusuf lamido idan suka je dubata babu wani sakin fuskar da suke Samu daga gareta asalima ko kallon kirki bata yi musu .

Acikin haka ne aka sallameta Kai tsaye gida Haj murjanatu ta wuce da yarta ba tarema da Taufiq din yasan an sallameta ba. Sai da ya je asibitin ya tadda an sallameta ta.

To meye tunanin Haj murjanatu na tafiya da mujaheeda gidà ba ta maidata gidan mijinta ba? Ya Ciro waya ya Kira Alh Mustapha labaran bayan sun gaisa ne ya gayá masa ya zo asibiti ya tadda an sallami mujaheeda Amma Kuma ba gidansa aka kaita ba.

Alh Mustapha labaran yace " Kada Ka damu Haj ta wuce da ita gida koma menene Kada kazo gidan har Saina kiraka". Gaban Taufiq ya Fadi asanyaye yace " to shikenan".

Yayi kasa da wayar cikin matukar damuwa da tunani Yana son matarsa babu Kuma Wanda ya isa ya Raba Shi da ita .

DAGA TASKAR YAR GIDAN IMAM

NIMA MATARSA CE
NA
HÀBIBA ABUBAKAR IMAM

(YAR GIDAN IMAM)

BABI NA ASHIRIN DA BIYAR

****

Muhseena ta zauna, zaman jiran zuwan Kabir, Amma yanayin aiki yasa Kabir ya daga zuwa.

Domin saida ya Kara kwanaki uku akan kwanakin da yace zai zo din, kafin Allah ya kawo Shi Durmi.

Abu biyu ne a cikin zuciyar muhseena, na daya murnar zuwansa na biyu fargabar abinda zai biyo baya.

A yammacin ranar jumaa, Kabir na zaune Kan tabarma a zauren gidan su muhseena cikin kyakkyawar shigarsa ta blue din shadda babu aiki ajikin rigar amma yanayin aikin yayi matukar kyau ya Kuma dace da jikinsa, Kabir ma'abocin sa hula ne don haka yauma ya murzata akansa ta fito ta Kara kawata kyansa matuka.

Gyefe daya cikin hijabi muhseena ce fuskarta ba wata kwalliya bace ajiki amma duk da haka tayi kyau sosai.tun zuwansa suke hira cike da so da kulawa sunyi ràshin juna tamkar wadanda suka dade ba suga juna ba, sosai Kabir ya tsaya Yana gaya Mata irin ràshin da yayi nata, duk da wayar da suke yi kullum to fa bai lafar masa da komai acikin matukar son da ràshin ta da yayi, ya Kara kafeta da sarkakkun idanunsa yace " muhseena shin kina Jin abinda nake ji agame da ke acikin zuciyata kuwa?". Ta tsaida idonta akansa sannan tace " ina Jin fiye da abinda kake ji". Ya girgiza Kai yace " aah, kina dai Jin abinda kike ji amma bana tsammanin zaki ji fiye da abinda nake ji, muhseena da ke na Fara soyayya kece mace ta farko da tun ganina da ita na farko na fada soyayyarta na Kuma yi nisa" ta dan yi murmushi tace "Nima ban taba soyayya ba sai akanka don haka abune me sauki naji fiye da abinda kake ji, idan Kuma Baka yarda ba shikenan kowa Kansa ya sani, don haka nasan ina sonka so na hakika Wanda bazan iya bayyana maka Shi ba saboda nima bansan yawansa ba".

Cikin matukar jindadin maganarta ya lumshe idanunsa ya bude ya Kara zubasu akan ta , yace " idan hakane kuwa muhseena ni banga abinda zai kawo tsaikon maganar auren mu ba, don ba dadewa ana soyayya shine kesa ayi maganar aure ba a'ah"

Ya girgiza Kai Yana cigaba da kallonta, " karfin so da kauna da Kuma yarda da dabi'un juna sannan da yarda da Zama abokan rayuwar juna saboda haka mun wuce wannan tsanin Shi yasa banga dalilin jinkirin ba".

Faduwar gaban muhseena ya tsananta duk da abinda kunnenta yake ta adduar yaji kenan, tun maganarta da mahaifiyarta ta karshe take ta adduar Allah yasa Kabir idan yazo yayi Mata maganar aure domin ta kosa ta fita daga cikin fargabar da take ciki kullum. To amma me yasa fargaba da damuwa suka mamaye zuciyarta? Me yasa take Jin faduwar gaba?.

" Banji kince komai ba muhseena ko kina ganin nayi garaje ne". Tayi saurin girgiza Kai sannan tace " aah abinda yakamata kenan, domin itama Inna tun kafin kazo tayi irin wannan maganar". Cikin zumudi yayi saurin kallonta yace " me innar tace?".

Tayi murmushi cikin Jin kunya tace " cewa tayi ya kamata idan kazo Ka turo mahaifanka ayi magana, domin asan matsaya".

Yace " Alhamdulillah, in sha Allah zanyi musu magana domin Dama burinsu nayi aure , na Kuma gaya Miki Shi Kansa kawuna da nake hannunsa a Kano maganarsa kenan kullum na fito da Mata to kinga abin duk ya kwana gidan sauki". Gaba daya su kayi murmushi.

Kabir yace " kinsan me Zan Fara yi idan mukayi aure?" Ta girgiza Kai , alamar a'ah. Kabir yace "Makaranta Zan maida ke , domin Ina son ki Sami ilimin boko Mai yawa Ina son ki Zama abin alfahari a ko'ina ina son rayuwarki ta inganta ta Zama abin sha'awa". Muhseena ta runtse idanunta wani dadi na ratsa cikin zuciyarta, tana mamakin wane irin masoyi Allah ya agajeta ya kawo Mata, son Shi ya cigaba da shiga zuciyarta azahiri Samun Kabir rahama ne agareta . Nan da nan idanunta suka Fara kokarin tara hawaye, tace " babu abinda zance maka sai godiya irin yadda kake Kula da tausayina bansan me Zan maka sakayya dashi ba". Kabir yace cikin tsantsar kauna da kulawa " muhseena ba zaki taba gane soyayyar da nake Miki ba har sai kin Zama mallakina". Tayi kokarin maida hawayen ta tace " Allah ya tabbatar".

Sun dade suna hira har aka Kira sallar magriba sannan su kayi sallama bayan ya bata Leda me cike taf da tsarabarta har Leda biyu sannan ya dubeta yace "Akwai Leda aciki a daure wannan na Inna ne".

Muhseena tayi kasa da kanta tayi masa godiya da adduar data Saba akullum yayi Mata alheri tunda ko tace ba zata Karba ba baya sauraronta Tama gaji ta daina.

Bayan tafiyarsa ne ta shiga gida cike da nishadi da farinciki.Ande Dije ce zaune a kofar dakinta fuska a daure kamar wacce aka aikoma mala'ikan daukar rai sai huci take kamar wacce akayi ma lefi.shigowar muhseena ta shiga balla Mata harara tana kallon ledojin dake hannunta haushi da takaici ya Kara kamata.ta saki tsaki tace " Allah ya kyauta mana da wulakantar da Kai, Ku rasa inda zaku dinga yin maula sai wajen saurayi ".

Hajara ta dago labule ta Kira muhseena tace " shigo daki, bance ki tanka ba Kuma". Kalaman Hajara yasa muhseena ta hadiye haushi da bakincikin maganar da Ande Dije tayi, Kai tsaye ta wuce daki, ayayinda Ande Dije ta cigaba da hayagaga tana fada sai kace wacce aka yima wani laifi.

Tana shiga dakin ta jingina jikin bango ta aje ledojin akasa , gami da runtse idanunta.

Hajara tace " Kada ki damu da maganganun Ande, domin yakamata zuwa Yanzu ace mun Saba da irin kalamanta ko da yake sabon bazai hana idan tayi maganar ran mu ya baci ba". Muhseena ta bude Ido ta dubi Hajara tace " to yanzu dai Inna me ya kawo maganar muna maula awajen Kabir , wai maula". Hajara tace " hmmm ita ina ruwanta in dai zata fada aji haushi ai burinta ya Gama cika".

Hajara ta Kara kallonta tace " ya tafi ne?" Ta gyada Kai tace " Ya tafi , ga Kaya nan yace Akwai naki aciki".

Hajara tace " Shi dai baya gajiya da dawainiya"

Muhseena ta durkusa ta kwashi ledojin zuwa gaban Hajara ta aje sannan ta Sami waje ta zauna.

Hajara ta janyo ledojin ta bude, dayar dauke take da less da atamfa da shadda sai material duk guda dai dai, sai hijabai guda biyu sai turaruka .

Hajara ta jinjina Kai tace " tabdijan amma ko Kabir ya kashe kudi ". Ta janyo dayar ta bude akwai bakar Leda Kuma aciki ta Bude atamfofi ne guda biyu.

Sai Kuma cikin ledar kayan ciye ciye ne su cakulet da sauran tarkacen kayan zaki. Hajara ta ce" wannan dinne nawa kenan" muhseena ta gyada Kai tace " eh haka yace" Hajara ta numfasa tace " Allah ya saka masa da alheri ya tsare Shi daga dukkan sharri yayi masa albarka " muhseena ta amsa da " Ameen".

Daganan Hajara ta dubeta tace " kunyi maganar da nace" ta daga Kai tace " eh Inna shine

ma ya Fara yin maganar , yanzu yace kafin ya koma zai yima mahaifansa magana". Hajara ta aje numfashi tace " to Allah yasa mu ji alheri" .

Ta Mike ta kwashi kayan tana duban muhseena tace " Zan je na kaima Ande ta gani, tunda ta ga kin shigo dasu Kada ta dauka sunfi haka, Kada Kuma tayi korafin an kawo Kaya baa nuna Mata ba, kin dai Santa ". Ta Dan tabe baki tace " ko dai me akayi ba zaa burgeta ba" tace tana fita " eh Amma gara a nuna Mata ".

Har yanzu Ande tana zaune inda take tana cigaba da kunkuni, har Hajara ta aje kayan a gabanta tana cewa " Ande ga Kaya nan Kabir ya kawowa muhseena nima harda nawa". Ande Dije ta watsa Mata harara cike da tsana da takaici tace " to me zanyi dasu, tunda daga ke sai yarki ya sani Ku kadai yake iya ma kyauta" Hajara tace " haba Ande ya zaki Fadi haka alherin Kabir kuwa ai har ke ya shafa" ta Kara hade rai tace " ya shafeni a ina Ku dai kuka Sani ni bani da ruwa acikin lamarinku ranar da duk yansanda suka zo tafiya da Ku Kan kudin da kuke cima wannan yaron babu abinda ya dameni" " in sha Allah ma hakan ba zai faru ba" cewar mallam Umar lokaci daya Yana karasa shigowa cikin gidan.

Ande ta harare Shi tace " ummm nan kafi auki, an tabo ma'asumiya Hajara ko ". Ya dubi Hajara yace " menene Hajara " tadan gyara tsaiwarta tace " Dama Kaya ne Kabir ya kawoma muhseena da ni shine nazo ina nuna Mata". Yace " dauki kayan ki koma dasu daki" Ande ta saki harara tace "Dama nace ina son gani ne , Ku kuka Sani" Hajara ta kwashi Kaya ta wuce daki Shi Kuma ya dubi Ande Dije yace " don Allah Ande kiyi hakuri ki dinga saukakama rayuwa kina da girma da kima awajen Hajara na rantse Bana son ace wata rana zata zo da zata daina ganin kimarki Wanda nasan yau da gobe komai zai iya faruwa" ta Mike tana hararsa tace " ta Dade bata daina ganin kimata ba itama kimar gareta da har zata kalli wani da kimar Hajara me? Kai dai da Allah ya yankama kazar wahala sai Ka zauna kayita figarta, aikin banza aikin wofi ". Ta kakkabe zani ta shiga daki.

Mallam Umar ya saki ajiyar zuciya, Allah Ka daidaita tsakanin matata da mahaifiyata abinda yake Fadi Kenan afili ahankali.

Daga bisani ya wuce dakin Hajara . Cikin so da girmamawa muhseena ta gaida mallam Umar gami da sannu da zuwa. Hajara ta dube Shi tace " don Allah mallam Ka daina jayayya da Ande akaina abin nan duk yakamata mu saba dashi mu Kuma dinga Kau da kai Akan dabi'un ta ".

Ya girgiza Kai yace" Allah dai ya ganar da ita kawai" ya dubi muhseena yace " yaushe Kabir din yazo" tace " dazu" yace " to idan ya Kara zuwa kice ina nemansa domin yakamata ya fito ayi maganar auren nan kowa ma ya Sami natsuwa".

Hajara ta muskuta tace " Ai Shi da Kansa ma dazu yayi maganar zai turo" cikin farinciki mallam Umar yace " Alhamdulillah najidadin hakan Allah ya nuna mana". Kiran sallar isshai yasa Mallam Umar ya fita zuwa masallaci.

****

Bayan fitowa sallar isshai ne Kabir ya wuce dakin mahaifiyarsa Hafsatu , Kai tsaye bakin kaskon wutar da Hafsatu ta aje a tsakiyar daki ya nufa domin Shan dumi.

Ya zauna ya lankwashe kafa Yana Kara hsnnunsa a wutar Yana cirewa, Hafsatu ta dube Shi cike da kulawa tace " ya sanyin nan da na Kano yake " yadanyi murmushi yace " to kano fa itama ana Shan sanyin nan , nan ma gaskiya da sanyi na rasa inda yafi wani".

Tace " Allah yasa muga wucewarsa lafiya " yace " Ameen ". Ta aje kofin hannunta tana

kallonsa tace " a kawo maka tuwon ne , miyar busasshiyar kubewa da kake so Kuma taji man shanu". Yace " har kinsa yawuna ya tsinke mama akawo min naci".

Tayi murmushi lokaci daya ta kwalama Hassan Kira dan kishiyarta sahura nan da nan ya amsa ya shigo dakin ta dube Shi tace " Hassan jeka Ka dakkoma yayanka abincinsa a dakin sahura" ya amsa da toh sannan ya fice cikin kankanin lokaci ya dawo da kwanon tuwo da miya harda yajin daddawa ya ajema Kabir agaba sannan ya koma ya dakko masa ruwa ya aje sannan ya fita.

Sosai Kabir yake Jindadin tuwon nan Yana ci suna hira da mahaifiyarsa daya daga cikin lokutan da yafi so arayuwarsa kenan ya ganshi gaban mahaifiyarsa suna hira.

" Kabir wai yaushe jiran da Muke yi zai kare ne?" Yace " mama wane irin Jira" ta gyara zamanta tace " jiran fitar da matar aurenka, Kabir Ka dubi shekarun dake kanka haka zalika duk abinda kake son Samu kusan Ka samu Ka na da rufin asirin da ko Mata nawa ne zaka iya aura Ka Kuma ciyar da su ba tare da wata damuwa ba, to meya kawo tsaikon duk da nasan aure lokaci ne Amma ya Zama dole kaima kasa niyya".

Ya hadiye lomar tuwonsa sannan yace " kwantar da hankalinki mama komai yazo karshe in sha Allah " tace " me kake nufi?" Ya danyi murmushi yace " ina nufin na Sami matar aure mama".

Nan da nan fuskarta ta washe farinciki ya kamata tace " Alhamdulillah Allah nagode maka Aina Ka Sami matar a kanon ko Aina?"

Yace cikin natsuwa bayan ya ture kwanon tuwon alamar ya Gama ci "Burinki ne ya cika domin anan kauyen Durmi na Sami Mata nasan Kuma Dama Baki da abinda kike so sama da hakan".

Fuskarta ta Kara cika da annashuwa tace " Kai najidadi, yar gidan waye?" Ya gyara zamansa cikin zumudi yace " sunanta muhseena yar gidan mallam Umar na tsohuwar kofa".

Fara'ar fuskar Hafsatu ta subuce wani abu ya tsurga Mata har cikin hanjinta, tace " yar gidan wane" yanayin sautin maganarta yasa ya dubeta sosai yace " mallam Umar na tsohuwar kofa".

Tayi zumbur ta Mike tana kallonsa cikin shakewar murya tace " ina bazai yuwu ba Kabir, ba zaka iya auran wannan yarinyar ba".

Maganar ta zamo tamkar saukar aradu Akan Kabir a gigice cikin rawar murya yace " mama don me bazan iya aurenta ba? ".

DAGA TASKAR YAR GIDAN IMAM

NIMA MATARSA CE
NA
HÀBIBA ABUBAKAR IMAM
(YAR GIDAN IMAM)
BABI NA ASHIRIN DA SHIDA
****

Hafsatu ta aje gauruwar ajiyar zuciya sannan ta lalubi kujera ta koma ta zauna tana cigaba da kallonsa, cikin shakewar murya tace " Na dai gaya maka ba zaka iya aurenta ba saboda ba

zamu yarda da ita a matsayin surukar mu ba, Kada ma Ka bari ko da wasa mallam yaji shi da yafi kowa burin Ka auro ya agidan dattako".

Cikin matsananciyar damuwa Kabir yace " mana idan ko dattako ake nema ina ganin idan aka Sami gidan Mallam Umar to an wuce wajen, haka zalika idan natsuwa da cancanta ake nema shima idan aka Sami muhseena an je matakin karshe". Ta girgiza kai tace " hmmm babu abinda Ka sani a wañnan bangaren sai abinda idonka ya gani kawai Wanda Kuma yaudara ce kawai, babu wani dattako awannan gidan kamar yadda babu wani kamun Kai da nutsuwa da zaa samu awajen wannan yarinyar ".

Kan Kabir yayi nauyi zuciyarsa ta shiga tafasa Sam Sam bai son yadda ake aibata muhseena, ya Kara kallonta cikin Jan Ido yace " aah mama babu yaudara acikin Kamala da nutsuwar muhseena na yarda da dabi'un ta sune Kuma suka ingizani wajen kaunarta adalilin hakan har na Fara sha'awar yin aure" Hafsatu ta shiga girgiza Kai tana cewa " kabar wannan maganar domin kuwa abinda kake so ba zai taba yuwuwa ba, don haka kayi gaggawar cire wannan maganar aranka, kaje Ka Samo wata yar gidan mutunci gasu nan da yawa".

Ya runtse Ido ya bude Jin abin yake tamkar Yana mafarki domin bai taba tsammanin zai Sami matsala da iyayensa wajen auren muhseena ba.

Ya gyada Kai yace cikin murya Mai cike da ban tausayi " na rantse Miki ina son muhseena so na hakika bansan yadda zanyi da Kaina ba matukar na rasata domin rashinta tamkar Rasa wani bangare ne na jikina".

Hafsatu ta saki salati da karfi tana tafa hannayenta " ni ko na shiga uku yaushe kayi zurfi a soyayyar yarinyar nan haka bayan ba zaka taba samunta ba domin dai matukar mune zamu fada aji to Baka Isa Ka auri wannan yarinyar ba".

Cikin kaguwa Kabir yace " wai mama Mai tayi da baza'a iya aurenta ba , meye laifinta?". Tayi masa kallon tsaf tace " bata da wani laifi , laifin mahaifiyarta shine ya shafeta" Kabir yace " Aiko Allah baya kama bawa da laifin wani bawa face abinda bawan ya aikata da Kansa don haka babu dalilin da zaa hukunta muhseena da laifin mahaifiyarta" ya daga hannayensa biyu alamar roko yace" don haka don Allah mama na rokeki ki Goya min baya na auri muhseena". Ta girgiza Kai tace ," bazan iya Goya maka baya baya Ka aureta ba domin Ka godema Allah da ya kasance ni Ka Fara gayama wannan maganar ba mahaifinka ba domin da kasha mamaki".

Kabir yayi ajiyar zuciya yace " don Allah mama Mai mahaifiyar muhseena tayi da har zaiyi sanadiyyar da zaa hanani auren muhseena".

Hafsatu tace " nace kabar wannan maganar, kadai sa aranka babu aure tsakaninka da ita har abada".Kabir ya dafe Kansa da hannu biyu Yana fitar da wata boyayyiyar ajiyar zuciya baya Jin tunda yazo duniya ya taba riskar Kansa cikin tsananin tashin hankali da damuwa irin na yau , daker ya iya yunkurawa ya tashi Yana gauraye hanya ya fita daga dakin ba tare da ya Kara cewa komai ba . Hafsatu ta bi bayansa da kallo cike da tashin hankali bata taba tsammanin zata taba Jin wannan maganar daga bakin danta Wanda ta dora dukkan fata akansa, burinta da yawa ya cika ta hanyar dan'uwanta Alh Musa Wanda ya daukar Mata Kabir ya inganta rayuwarsa ta hanyar bashi ilimi da tarbiyya da Uwa uba aikin yi Wanda yaja ya Sami arziki shima tunda ya wuce da bukatun Shi da nasu duk abinda take so da ga ita har mahaifinsa mallam Hamza wanzami to fa zaiyi musu, to ta yaya bayan danta nagartacce ne zasu bari ya auri yar da bata da asali, ai idan ma sukayi haka lalle sun ci amanar dansu. Ta zuba tagumi tana addu'ar Allah Kada yasa wannan lamarin ya Zama damuwa a tare dasu.

Shigar Kabir dakinsa ya fada Kan gado ya kwanta rigingine gami da runtse idanunsa , hakanan yaji wasu siraaran hawaye suna fita daga idonsa.zarihi bazai iya rabuwa da muhseena ba Amma, zaiyi yaki har sai ya aureta , domin idan yace bazai aureta ba bai San inda muhseena zatasa kanta ba Kuma zafi da radadin da yake ji ayanzu baya son ko kadan muhseena ta ji irinsa domin Shi kadai yasan abinda yake ji ayanzu. Domin har wani zazzabi yaji Yana neman ya kama Shi,baisan Yana son muhseena ba sai yau domin yadda yake Jin tamkar zaa cire masa rai.

****

Akalla yau mujaheeda ta Sami wajen kwanaki shida agidansu.taji sauki sosai, Amma duk yadda Taufiq ya so mujaheeda ta dawo gidansa abin ya fassakara domin Haj murjanatu ta hana wannan damar domin ta hana mujaheeda komawa gidan mijinta ta Kuma ki yarda iyayensa su zo ayi magana kamar yadda taki sauraren Alh Mustapha labaran Akan komai.

Burinta daya mujaheeda ta yarda ta amince Mata a raba aurenta da Taufiq, amma har yanzu bata bata wannan damar ba sannan taji yin maganar da ita kawai ta gaya Mata bata son tayi Mata maganar Taufiq ta gaya Mata ta bata Dama harta sakko daga fushin data keyi tukuna . Hakan ne yaja ma Haj murjanatu tsaikon aiwatar da abinda take so domin duk abinda mujaheeda take so ta Kuma ambata Shi take yi.

Duk irin Kiran wayar ta da Taufiq yake yi taki dagawa, sakonnin da yake turowa kuwa kullum ko dubasu batayi , domin tayi matukar daukar zafi dashi.

Tabangaren Alh jibrin kuwa burinsa ya cika ya hada fitina atsakanin Taufiq da mujaheeda. Bata zuwa office hakan yasa ya koma shike aiwatar da komai kamar da Shi da murtala suka cigaba daga inda suka tsaya tare da adduar Allah yasa sanadiyyar barin mujaheeda office din kenan Wanda hakanne zai Zama sanadiyyar Kara mallakar duk abinda ya rasa. Tun komawar mujaheeda gidà kusan kullum sai Alh jibrin yaje ya dubata agida.

Hakan yasa mujaheeda ke Kara Jin zafin Taufiq da har yake tsammanin wani abu zai iya shiga tsakaninta da mutumin data dauka tamkar babban yayanta, a shekaru kuwa tamkar mahaifinta domin tasan ya haifeta, Kai Taufiq ya zalunceta, ya ci amanar kauna da soyayyar da take masa. Bayan har kasa ta nade bazata taba son wani mutum irin yadda take sonsa ba, domin tana sonsa fiye da komai arayuwarta Shi ne kadai mutumin da take jinsa har cikin bargon jikinta.amma ta yaya zaace Taufiq bai yarda da ita ba Yana zarginta anya Taufiq Yana sonta kuwa? Tambayar da takema kanta kenan kullum.

Gaba daya Taufiq ya shiga damuwa ya rasa inda zai bulloma al'amarin, yaje wajen mahaifinsa yafi a kirga domin ya shiga cikin maganar amma ya ki.

Yauma Yana tsugune gabansa cikin damuwa, Haj saratu na gefen kujera a zaune yau dai itama cikin fushi take don haka ko maganar da take yi yanzu cikin fusata take.

" Wai meye kaifin Wanda yayi kuskure yasan yayi sannan ya bada hakuri, don me ba zaa yafe masa ba, Kuma duk Wanda ya turo wadannan hotunan shine babban shaidani Kuma Taufiq Yana dukkan damar dazai yi fushi, kuskurensa daya daya yanke hukunci cikin fushi Wanda shine ya Zama damuwa yanzu, amma don me zaa zauna ana gara yaro ana dora masa laifi".

Alh Yusuf lamido ya tsareta da Ido yace " to wa zaa daurama lefin bayan Shi saratu Kada kiso kanki fa, idan Shi Yana da tunani tun lokacin da aka turo hotunan zai gamsu da cewa duk Wanda ya turo rabuwarsu kawai yake so Shi da matarsa amma kishin banza da zato da zargi na wofi yasa ganin farko Ka aminta da mutumin da baka sani ba Ka Kuma zargi wacce Ka sani asalima abokiyar rayuwarka, to yanzu me kake so nayi?".

Haj saratu ta gyada Kai tace " nasan haka ,Amma dai ai yakamata shima a amshi uzurinsa Kuma a dawo masa da matarsa".

Taufiq ya amshe " bukatata kenan, Abba kasa Baki tunda daga mujaheeda har mahaifiyarta sunki saurarata shima Àlh da yake saurarata sunki saurarensa , akalla dai na fahimci nayi kuskure saboda haka ai yakamata ayi min Uzuri".

Alh Yusuf lamido ya dubeshi sosai yace" kana tunanin banyi maganar bane nayi magana da Alh Mustapha labaran amma ya nuna Shi Kansa bazai iya tankwara Haj murjanatu ba don haka sai mu Jira har sai mujaheeda ta sakko tunda tana sonka zata nemeka amma mu bata lokaci bayan ta warke daga jinyar jikinta da Kuma jinyar abinda kayi Mata kila zata iya nemanka".

Yayi kasa da Kansa Yana Jin shigar wata sabuwar damuwar.

Haj saratu tace " yanzu ita Haj murjanatu babu Wanda ya isa da ita Kenan abinda taga dama Shi zatayi a rayuwa, gaskiya idan ko hakane Akwai matsala, ace hatta mijinta bai isa da ita ba Kuma ahaka take son yarta itama ta dinga yin irin rayuwarta".

Alh Yusuf lamido yace " Shi yasa idan kasan halin mutum sai kaci maganin Zama dashi , yakamata Shi ya toshe duk wata hanya da zaa iya Samun damuwa tunda yasan halinsu, Kuma Allah ya kaddara auren nan to sai Shi yayi kokarin kawo gyara".

Haj saratu ta tabe baki tace " Ka Kara Kiran Àlh Mustapha gaskiya kuyi magana, shima fa Taufiq ba daga sheka ya fito ba shima Yana da uwar da take son ganin farincikinsa, idan Kai kana goyon bayan mujaheeda to ni goyon bayan dana nake".

Ya dubeta yace " kina ganin Bana goyon bayan Taufiq ne, to mujaheeda amanace agaremu ya Zama dole Kuma mu rike amana babu yadda zaayi mu wofintar da ita bayan tana da gaskiya".

Haj saratu tace " ummm ba zaka gane ba, yanzu dai Ka Kira Alh Mustapha Ka Kara masa magana ".

Ba Tare da musu ba Alh Yusuf lamido ya fito da wayarsa ya Kira Alh Mustapha labaran bugu daya ya dauka.bayan sun gama gaisawa ne Alh Yusuf lamido yace , " Alh Kan maganar yaran nan ne, yanzu haka zamu zauna amatsayin mu na manya ba zamu kawo karshen wannan matsalar ba, yakamata zuwa yanzu ace mujaheeda ta dawo dakin mijinta ".

Alh Mustapha labaran cike da damuwa yace " nafi kowa son hakan , amma na rasa tunanin Haj akan hakan ko maganar taki yarda muyi balle ta saurareni, ita kanta mujaheeda ta tabbatar min ba zatayi magana ba har sai ta sauka da ga fushinta Wanda hakan yayi dai dai domin yanke hukunci cikin fushi shike kawo dana sani kamar yadda ya kawoma Taufiq ,".

Alh Yusuf lamido yace " to yanzu meye abin yi Alh" ya nisa yace " hakuri za muyi mu Jira har zuwa lokacin da mujaheeda zata sakko, sai ayi koma meye, Kada Ku damu wannan auren in sha Allah babu abinda zai kashe Shi duk zasu Gama fushin ne su sauka don nasan mujaheeda tana son mijinta so na hakika ba Kuma zata iya rabuwa dashi ba".

Taufiq ya jidadin maganar ÀIh Mustapha amma anya yanzu mujaheeda tana yi masa son da take masa da?.

Alh Yusuf lamido ya gyada Kai yace " shikenan Alh Allah yayi mana jagora" ya amsa da Ameen sannan sukayi sallama.

Ya dawo da kallonsa ga Haj saratu da Taufiq yace " na kirashi kun Kuma ji abinda yace ko to duk sai mu cigaba da Jira".

Haj saratu ta saki tsaki tace " Kai Allah ya wadaran aure gidan karanta Kai Kuma jarabawarka kenan , to Allah ya baka ikon cinye jarabawar" tana gama fadin haka ta tashi cike da takaici ta bar falon .

Yayinda Taufiq ya Kara Mike Kafa cike da damuwa .

Hakan yasa Alh Yusuf lamido ya cigaba da yi masa nasha musamman akan zamantakewar aure Wanda hakuri da juriya da sadaukarwa sune ginshikinsa.

DAGA TASKAR YAR GIDAN IMAM

NIMA MATARSA CE
NA
HÀBIBA ABUBAKAR IMAM
(YAR GIDAN IMAM)
BABI NA ASHIRIN DA BAKWAI
****

Washe gari Kabir haka ya tashi cikin matsananciyar damuwa, hatta karyawa ya kasa yi.

Hafsatu tana lura da irin yanayin da Kabir din yake ciki amma bata ce masa komai ba.

Ya kasa Samun karfin guiwar yin komai haka zalika tunanin yadda zai shawo Kan lamarin kawai yake yi. Soyayyar muhseena ta riga tayi matukar zurfi acikin zuciyarsa, Kuma ma ta yaya zai iya kallon muhseena da iyayenta ya iya gaya musu bazai iya auren ta ba.

Hakika Yana cikin matukar rudani Yana bukatar sanin gaskiyar lamarin.

Ko da Kabir yaje wajen muhseena ya kasa sakin jiki ko fuska kallo daya zakayi masa kasan akwai damuwa a tattare dashi. Muhseena ta gane hakan jikinta Kuma yayi sanyi zuciyarta cike da adduar Allah yasa ba maganar aurensu bane ta haifar da damuwa ga Kabir, don haka ta kafe Shi da Ido gami da yi masa tambayar " lafiya kuwa, Naga gaba daya Ka canja idonka na bayyana damuwa da tashin hankali".

Yayi saurin kallonta Yana kokarin boye abinda ke cikin idanunsa,yayi Dan murmushi sannan yace " to hasashenki bai yi ba, domin dai ni babu wata damuwa dake damuna, balle tashin hankali". Ta Kara masa kallon tsaf tace " to menene matsalar?".

Ya gyada Kai Yana yi Mata wani kallo Mai cike da kauna , yace "tun jiya cikin dare wani irin zazzabi ya rufeni da ciwon Kai Mai tsanani ".

Nan da nan muhseena ta gigice tana kallonsa cike da kulawa tace " Amma shine Ka fito Ka taho cikin sanyin nan , haba Kabir".

Yace " Shi yasa tun farko naki gaya Miki don nasan sai kinyi irin wannan maganar da kikayi, ".

Ta numfasa tace " Amma akalla ko dai yayane ai yakamata Ka tsaya Ka Kula da lafiyarka, domin tafi komai muhimmanci agareni ".

Yace Yana kokarin rike kunnuwansa biyu da hannayensa, yace " Na tuba ayafe min sarauniyata". Yadda yayi shine ya bata dariya gaba daya suka fashe da dariya , tace " to kasha magani?" Yace " eh nasha Shi yasa na Sami karfin zuwa wajenki, saboda gobe lahadi nake son komawa Kano, don na so na zauna har litinin amma har an Fara Kirana na dawo gobe saboda akwai kayan da zaa sauke ma kamfani ranar litinin Kuma dole nine Zan karbi kayan".

Ta gyada Kai tace " babu komai Allah ya tsare maka hanya Allah Kuma yasa kaji sauki sosai zuwa goben". Yace " Amin". Zuciyar muhseena tana cike da son ta tambaye Shi ko yayi magana da iyayensa amma kunya da fargaba ya hanata. Sosai Kabir ya karanci fuskarsa muhseena don haka ya dan gyara zamansa akan tabarma yace " zazzabin da nayi ya hanani yin magana da Baba , saboda Bai dawo gida da wuri ba , har na kwanta,".

Ta numfasa fargabarta ta lafa, ta dube shi tace " babu komai Allah yayi mana jagora, ya Kuma Baka lafiya ". Yace " Amin" ya Kara kallonta yace " Kada ki damu zamuyi magana in sha Allah yau kafin gobe na tafi ". Tace " Kabi ahankali babu damuwa" yadan lumshe idonsa Yana Jin zafin yadda yake yima muhseena karya amma baida wani zabi da ya wuce hakan.

Anan yayi sallar magriba da issha'i sai dai yaje masallaci ya dawo ta Kara fitowa su cigaba da hira. Har mallam Umar ya dawo bayan sallar issha'i. Sun gaisa sosai cike da girmamawa. Sannan mallam Umar ya Kira Shi gefe daya, tsugunawa yayi agabansa Yana sauraronsa . Mallam Umar yace " Kabir , naso muyi magana tuntuni amma jiya muhseena ta gaya min da kanka kayi maganar zaka turo magabatanka Wanda na jidadin hakan , Ka turo su muyi magana domin dai daga Kai har muhseena babu Wanda bai Kai munzalin da zaiyi aure ba". Kabir ya jinjina Kai yace " hakane Baba".

Mallam Umar ya cigaba da cewa " muhseena tayi kyakkyawan zabi domin Kai din da daya ne tamkar da dubu Bani da haufin zaka jiyar da yata dadin data rasa jinsa a duniya domin Kabir babu abinda Ka sani acikin irin rayuwar da muhseena tayi na ràshin jindadi ina gaya maka wannan ne domin a yanzu an Kai matakin da zaka sani, da ma wasu abubuwan da dole zaka sani kafin aurenku don baka cancanci a boye maka komai ba a game da muhseena". Kan Kabir ya kàra yin nauyi zuciyarsa ta Kara sarewa, ya cigaba da yi ma Kansa tambayar menene yake neman tarwatsa mafarkinsa agame da muhseena.

" Ina adduar Allah Kada ya kawo duk wani sanadi da zai Zama silar kawo tangarda a cikin aurenku, Kuma wannan lokacin shine lokacin da ya kamata Ka bayyana ma duniya irinn son da kakema muhseena Amma hakan baya nufin ina son kayi fito na fito da kowa akan wannan lamarin", maganganun mallam Umar suna son su zo daya da maganar mahaifiyarsa da baisan inda suka dosa ba.

" Shikenan maganar Kabir, Allah ya taimaka". Kabir yace cikin sarkewar murya " nagode Baba in sha Allah komai zai tafi yadda Muke so, gobe Zan koma Amma kafin na koma zanyi magana da mahaifina" yace " to ba laifi Allah ya bada iko". Daganan ya dago Shi Kuma mallam Umar ya ratsa zai shige gida da sauri Kabir ya fito da kudi ya dunkula masa ahannu, mallam Umar ya girgiza Kai yace " aah kada muyi haka da Kai bazan Karba ba hidimar tayi yawa Kabir" " da ne fa yayima babansa kyauta ta yaya zakace ba zaka Karba ba". Bashi da sauran abin cewa daga maganar da Kabir yayi dole ya amshi kudin yace " Allah yayi maka albarka, ya Kara tsarewa", yace " Amin sai da safe" ya shige gida Yana fadin " Allah ya tashenu lafiya".

Jugum Kabir yayi komai na duniyar ya tsaya masa , baida wani karfin guiwar da zai cigaba da tsayuwa agaban muhseena don haka sallama kawai yayi da ita bayan itama ya bata kudi masu

yawa, tadan raka shi sannan ta tsaya tana kallon bayansa harya bacema ganinta duk da jefi jefi Yana waigowa Yana ganin duhunta harya wuce . Muhseena ta saki ajiyar zuciya cikin damuwar da ayanzu bata San dalilinta ba ta juya ta nade tabarmar ta shiga gida.

Tana shiga ta tadda Hajara da mallam Umar suna wata magana da bata San ta meye ba ce, amma shigarta dakin duk suka yi shuru suka shiga kame kamen Wata maganar da ban, duk da ta Kara Jin babu dadi amma bata nuna musu ba tabarma kawai ta aje ta dauki buta ta fice alamar Zata bandaki ne.

Amma tayi haka ne saboda ta Basu damar cigaba da maganar tasu wacce tasan basa son taji duk da ta riga ta sani cewa maganarta suke yi.

Tana shiga bandaki ta jingina jikin bango ta aje butar . Hakanan ta ji hawaye na kwarara a kwarmin idonta.

Me yasa mahaifiyarta ba zata gaya Mata gaskiyar lamarin rayuwarta ba, shin ko dai duk abinda mutane ke fada akanta gaskiya ne? Domin idan ba gaskiya ba ne babu yadda zaayi su dinga shakku da fargaba Akan maganar aurenta da kabir.ta Jima acikin bandakin tana kuka kafin ta share hawayenta ta fito .

Nan ma tana shiga dakin mallam Umar ya shiga kame kame Yana fadin " ina yi ma innarki bayanin yadda mukayi da Kabir ne," Kai kawai ta gyada ba tare da tace uffan ba ta shiga kakkabe yar karamar sabuwar katifarta da aka sayo Mata a cikin irin kudin da Kabir yake bata.bayan ta Gama ne ta miko na Hajara kudi cikin raunananniyar murya tace " gashi Kabir ya Bani". Hajara na karba bata saurari irin addua da takema Kabir ba tayi kwanciyar ta zuciyarta da numfashinta suna yi Mata nauyi.ido kawai ta rufe ba don wai zatayi bacci ba sai don ta ji dadin cigaba da tunanin data Saba yi arayuwarta.

****

Tabangaren Kabir shima yadda yaga rana haka ya ga dare, damuwarsa tafi ta jiya, nan da nan har ya rame yayi dan wuya.washegari duk inda yabi Hafsatu na binsa da kallo domin ta Lura kwarai da ramar da yayi hakanne yasa ta Fara fargabar Kada fa ace Kabir yayi nisa a son yarinyar nan ne yadda zai iya shiga matsala bayan rabuwarsu .

Cikin sallama Kabir ya shiga dakin mahaifinsa mallam Hamza wanzami. Yana zaune Kan buzunsa da alama Bai dade da shigowa gidan ba. Ya dago ya dube Shi yace " Kabiru Ka shigo " ya amsa yana kokarin Zama " eh Baba Dama Kai nake jiran shigowarka kafin na tafi". Yace " aah wai tafiyar dai tana nan ne yau din", ya gyada Kai yace " eh Baba, saboda sunki min uzirin gobe shima kawu Musa Yana ta Kira gara na tafi yau din kawai" yace " to ai shikenan Allah ya tsare hanya".

Kabir yace " Amin, na Riga na biya kudin shinkafa buhu daya dasu man gyada da manja su taliya kusan dai komai anjima mado zai kawo daga shagonsu". Mallam Hamza wanzami yace " Masha Allah Allah ya saka da alheri ya Kara budi na alheri yasa kafi haka". Yace " Amin Amin".

Malllm Hamza ya Dan tsare Shi da Ido sannan yace " Kabiru Naga kamar kana cikin damuwa ne Kuma fuskarka ta fada kamar Baka da lafiya".

Kabir ya dan muskuta Yana dubsn mahaifinsa yace " a zahiri Baba damuwa gare ni " ya tattaro hankalinsa Kan sa yace " damuwa Kuma wace irin damuwa Kabiru" yace " na Sami matar aure ne?" . Mallam Hamza yace" kash kajika da wata magana don Ka Sami matar aure sai hakan ya Zama damuwa, bayan kasan bamu da burin da ya wuce mu ji irin wannan furucin Alhamdulillah Kabiru ai gara kayi auren domin shine cikar kamalarka". Kabir ya numfasa yace "

akwai damuwa kamar yadda na fada domin yarinyar da nake son na aura mama ta ce bazan aureta ba na bar maganar Kai kanka Kada na gaya maka domin ba zaka yarda ba". Ananne mallam Hamza ya tattaro hankalinsa ya Kara maidawa ga Kabir yace " bazan yarda ba? To wacece yarinyar yar gidan waye Aina Kuma take?".

Sannu ahankali Kabir ya sanar dashi komai akan muhseena.

Malllam Hamza yayi dif komai ya tsaya masa ya dubi Kabir sosai yace " yar gidan mallam Umar, aah ina Kabiru kabar wannan maganar , akwai Mata da yawa babu Kuma inda zaka nemi aure ace ba zaa Baka ba don Baka da wani aibu, Amma wannan yarinyar tana da aibun da bazan taba yarda ta Zama surukata ba".

Kan Kabir ya Sara ya Kara daburcewa yace " Baba menene aibunta , Allah ya sani ina Sonta ia kadai zuciyata ta ke so Bana Jin Zan iya rabuwa da ita komai girman aibunta".

Ya watsa masa harara yace " Kai bana son shashanci ba zaka iya rabuwa da ita ba komai girman aibunta? Kasan abinda kake fada kuwa?". Kabir yace " to menene aibunta? Me tayi da baza'a iya aurenta ba?".

Cikin fusata da daga murya yace " To shegiya ce bata da uba, babu Kuma Wanda baisan hakan ba a kauyen nan, sai irinku da baku rayu a kauyen ba".

Cikin matsananciyar daburcewa Kabir ya ce" shegiya?" " Kwarai da gaske babu wai, don haka kowa so yake yayi aure cikin kyakkyawar zuria ba irin wannan ba Ka aureta kace me? Waye ubsnta kafi kowa sanin dole sai mace ta haifo da me irin halin gidan ubsnta ta yaya zaka aureta a haka?". Kabir yace cikin rawar murya " Baba ayi bincike " ya watsa masa harara yace " Ayi bincike don me? Bayan komai agaban mu akayi, watan wannan yarinyar takwas da haihuwa mallam Umar ya auri uwarta ba yarsa ba ce ". Tikisa Kabir yayi kasa da Kansa zuciyarsa na suya dai dai lokacin Hafsatu ta shigo dakin .

Mallam Hamza ya dubeta yace "kinji shirmen da danki ya zo dashi KO" ta dubi Kabir yanayinsa kadai ya tabbatar Mata da cewa maganar da ta ce yabarta Kada yayi ne yazo yayita.

Tace " Au wai sai da yayi maka wannan maganar Bai barta ba kamar yadda nayi masa umarni".

Mallam Hamza yayi tsaki yace " Bai yarda ba , Kuma ko yanzu banga alamar zai yarda ba domin har wani cewa yake yi wai ayi bincike,abinda ya faru Akan idon mu babu Wanda baisan shegiya bace agarin nan ba, don haka bazan taba hada jini dasu ba".

Hafsatu daga tsaye ta cigaba da fada " Naga alamar kasa ma kanka damuwa dubi yadda Ka rame daga jiya kawai, to kayi gaggawar rufama kanka asiri Kayi hakuri da abinda kasan ba zaka taba samu ba".

A kausashe mallam Hamza wanzami yace " ko zaka iya auren shegiya?" Da sauri ya dago yace " Na rantse Zan iya aurenta matukar muhseena ce domin bata da laifi ba zabinta bane ta kasance awannan matsayin itama ba haka ta so ba, don Allah ku barni na aureta ".

Gaba daya suka saki tsaki lokaci daya, mallam Hamza yace " to bazaka aureta ba" Hafsatu tace

" Ko da ko Ku kadai aka bari jiran duniya, babu aure a tsakaninku".

Kawai ji yayi hawaye Yana fita masa masu matukar zafi sai kace mace. Ya kasa Kara yin wata magana saboda yadda zuciyarsa ke radidi,. Ko kadan Bai ji haushin muhseena ba bai kuma tsaneta ba don ance shegiya ce,asalima tausayi da kaunarta sune suka Kara mamaye zuciyarsa . Son da baiyi Mata da ba ma yanzu Shi yake mata.

Har suka cigaba da maganganunsu masu kama da sukar mashi aransa bai tanka ba. Daga

bisani ya tashi Yana gauraye hanya yayi musu sallama ya fice ba tare daya saurari komai ba .

Haka Kabir ya tattara ya koma Kano cikin tashin hankali da damuwa mara musaltuwa. Zazzabi Mai zafi ya rufeshi har komawarsa Kano babu wani abu daya daya faranta ransa, tausayin muhseena ya Hana Shi sakat ga Sonta tamkar ana Kara turawa cikin zuciyarsa, shin ta ina zai Fara , bazai taba iya gayama muhseena bazai aure ta ba, sannan bazai iya ketare umarnin mahaifansa ba don haka ya Zama dole duk yadda zaayi yayi domin ganin ya shawo Kan mahaifansa sun amince da aurensa da muhseena. Amma ya zaiyi yadda mahaifansa suka nuna abune mawuyaci ace sun yarda Amma ya Zama dole yayi tunanin mafita domin magana ce ta rayuwarsa da muhseena ba Kuma zai taba yin wasa da ita ba.

DAGA TASKAR YAR GIDAN IMAM

NIMA MATARSA CE
NA
HÀBIBA ABUBAKAR IMAM
(YAR GIDAN IMAM)
BABI NA ASHIRIN DA TAKWAS
****

Mujaheeda na kwance a Kan gadonta dai dai misalin karfe daya saura minti hudu na dare.Alh Mustapha labaran ya turo kofar dakin mujaheeda cikin sallama lokaci daya Yana Mai kunna wutar dakin, nan da nan haske ya wadaci dakin hakan yasa mujaheeda ta tashi daga baccin da take idonta ya Kara wartsakewa alokacin da taga daddy ne a tsakiyar dakin, ahankali tace " daddy lafiya" ya karaso cikin dakin gami da zaunawa akan kujerar kwalliyar dake kusa da madubi Yana kallonta sannan yace " lafiya lau mujaheeda magana nake son nayi, bana so Kuma Haj tasan nayi miki maganar shiyasa na zabi dare a matsayin lokacin da ya dace muyi maganar".

Jin hakan yasa mujaheeda ta Kara wartsakewa daga baccin data Fara ta natsu sosai tana kallonsa tace " to daddy ina jinka". Ya jinjina Kai yace " mujaheeda nasan kin dau zafi agame da abinda Taufiq yayi Miki, Kuma banga laifinki ba, amma ina son ki sani duk inda mutum yayi laifi ya Kuma yarda da yayi laifi harna ya nemi afuwa to abune kusan da ya Zama dole ayi masa afuwa" ya cigaba da kallonta Yana cewa ' don haka babu laifi idan kin yafema Taufiq kin koma gidansa kun cigaba da rayuwarki, awannan rayuwar da ake ciki mujaheeda ko wace mace hakuri take agidan aurenta domin kuwa babu wacce take Samun abinda take so dari bisa Dari, komai jindafinki komai zaman lafiyarki komai son da Miji yake Miki dole sai kin hadu da abinda bakya so kin San dalili?" Ta girgiza Kai yace " saboda aure Ibada ne anan Kuma mace take Samun aljannarta domin Annabin rahama ya fada duk matar data sallaci sallolinta guda biyar tayi azumin watan Ramadan ta kiyaye farjinta daga zina sannan tayi ma mijinta biyayya to sakamakonta gidan aljanna ne, haka zalika dimbin ladan da Mata suke Samu agidan aurensu Bai musaltuwa don haka Zama da aure shine darajar ko wace mace haka zalika yima Miji biyayya ya Zama dole ga Mata saboda haka ina ganin lokaci yayi da zaki tattara ki koma gidan mijinki Ku rungumi junanku" ya numfasa ya cigaba da cewa " ina gaya Miki wannan ne saboda kin rasa mai gaya Miki domin mahaifiyarki itace ta cancanci ta gaya Miki gaskiya amma kiyayyar

aurenki da Taufiq ta hana ta gayá Miki, don haka don Allah na rokeki kiyi hakuri ki saurari mijinki ki Kuma koma gidanki, kullum surukinki da mijinki sai sun kirani awaya da rokon ki dawo, ni Kaina bana son su fahimci Bani da wani kima ko daraja acikin maganarki ban son su gane ban isa da mahaifiyarki ba, idan kika yarda kika koma ni Kaina kin taimakeni wajen tsira da mutuncina".

Sosai mujaheeda ta tsaya ta fahimci Alh Mustapha labaran Wanda Dama itama ta riga ta sakko tana son ta koma gidan mijinta.

Ta dan muskuta gami da dubansa tace " babu komai daddy na yarda da dukkan maganganunka in sha Allah Zan koma" ya dan yi murmushi yace " Nagode ya ta ,yanzu idan sun Kara Kira me Zan ce musu" tace " daddy Ka gaya musu Ka isa da yarka na Kuma yarda na amince Zan koma gidan Taufiq tare da mantawa da duk abinda ya faru'. Ya jidadin maganar ta yace " to shikenan koma ki kwanta kiyi baccinki Allah yayi Miki albarka " tace "Amin daddy " lokaci daya ya tashi ya fice cike da farinciki, yau dai ya samu yayi magana da mujaheeda abinda Haj murjanatu bata so.

Mujaheeda ta numfasa ta koma ta kwanta gami da rufe jikinta da bargo. Hakika tana son Taufiq so me yawa tuntuni ta ji zuciyarta ta daina Jin haushinsa ta ji tana matukar begensa don haka lalle zata koma dakinta domin tasan duk inda Taufiq yake yayi matukar yin nadama idan tayi la'akari da irin sakonnin da yake turo Mata masu nuna nadama da son ta dawo gare Shi.

Kuma ma bayan haka tana matukar Jin nauyin Alh Yusuf lamido ko don Shi zata iya yafema Taufiq ta koma gidansa.

Washegari mujaheeda da Haj murjanatu da Àlh Mustapha labaran suna Kan teburin cin abinci Suna karyawa , duk wani abincin da mujaheeda ke son ci da safe an dafa Mata.

Haj murjanatu ta Kai lomar kwai bakinta kenan ta ji maganar mujaheeda kamar daga sama tace "mummy Zan koma dakina in sha Allah", nan da nan Haj murjanatu tayi kasa da cokalin hannunta daker ta iya hadiye kwan , ta juyo gaba daya ta zuba Mata Ido tace " me kika ce?",

Kafin mujaheeda tayi magana Alh Mustapha labaran yace " tace tana son ta koma dakin mijinta Kuma wannan magana ce me kyau domin abinda ya kamata kenan". Ta sakar masa harara afusace tace " babu ruwanka da shiga maganar nan domin nasan Baka ganin lefin Taufiq duk abinda zaiyi babu assha aciki saboda duk halinku daya, Kuma Ka sani yadda na shaki bakincikinka bazan taba barin mujaheeda ta shaki bakincikin Taufiq ba don matsayin yata ya wuce haka".

Mujaheeda tayi saurin aje cokalin hannunta cikin damuwa ta buga tebur tace ' don Allah mummy kada ki Fara domin babu laifin daddy ko daya nice na yanke shawarar komawa gurin Taufiq domin ya yi nadama ya Kuma bada hakuri" afusace tace "Nadamar Shi din banza da wofi ban hakurin me ya jefeki da irin wannan mummunan zargin sannan har kiyi tunanin koma masa, ai nayi zaton kina son na baki lokaci ne idan kin gama Tunaninki sai ki bani damar raba auren Ku , domin dai kinfi kowa sanin cewa dama Taufiq bai dace da ke ba so ne kawai na Shi da kika dora ma kanki yasa na barki kika aure Shi , yanzu Kuma bayan ràshin cancanta harda ràshin iya rukon aure ke karewa ma dai Taufiq baya sonki ".

A gaggauce mujaheeda tace " Taufiq Yana Sona, babu abinda zai canja hakan, mummy nasan kin goyi bayana kin share min hawaye alokacin da na shiga damuwa amma hakan bashi zaisa kiyi tunanin kashe aurena da Taufiq ba acikin dan kankanin lokacin da nayi da aure kike son na Zama bazawara mummy?".

Shi dai Alh Mustapha labaran bai kara cewa uffan ba, domin yasan yadda Haj murjanatu ta fusata idan yace zai cigaba dasa baki acikin maganar allura tana iya tono garma tana iya fadan maganganun da zasu iya Zama damuwa Shi yasa ya ja bakinsa yayi shuru.

Haj murjanatu tace a harzuke" Yanzu kina nufin kice zaki koma gidan Taufiq duk irin abinda yayi Miki kin manta". Ta gyada Kai tace " ina son na koma, saboda na fahimci ko zargin da yake min din so ne ya haifar da haka , Kuma ko ba don hakan ba ko don mahaifinsa Zan koma gun Taufiq domin Yana so na ya Kuma fi kowa damuwa da faruwar abinda ya faru, bayan haka Kuma ina son Taufiq so na hakika son da bazan iya rayuwa babu Shi ba, na Kara fahimtar hakan ne bayan zaman da nayi a gidan nan ba tare da Shi ba".

Haj murjanatu ta saki tsaki tace " idan hakane kuwa to tir da irin wannan soyayyar da kike masa, Kuma ki shirya karbar wukakanci da ga gare Shi tunda ya riga ya gane son da kike masa yafi wanda yake Miki".

Mujaheeda ta nisa tace " mummy bana son kina damuwa akaina don Allah" tace " dole na damu akanki domin nafi kowa sanin muhimmancin ki, Kuma zanyi fito na fito da duk Wanda zai daga Miki hankali ". Mujaheeda tace " Duk dai aikin nan ne ke son Haddasa min fitina da damuwa agidan aurena bayan Kuma duk yadda na Kai da son aikin nan to na fi son mijina da Shi don haka na yanke shawarar Zan bar aikin nan kawai" Alh Mustapha labaran yayi karaf yace " Alhamdulillah da kika gane hakan babu abinda aikin nan zai amfaneki da Shi domin dai duk arzikin nan kusan naki ne babu amfanin ki wahalar da kanki Akan abinda yake mallakinki ne, zaman lafiyar aurenki ya fi komai".

Haj murjanatu ta saki wani irin dogon tsaki tace " Ka dakata anan domin Taufiq Bai Isa ya hana ki mallakar abinda kike so ba tunda kina son yin aiki dole sai kinyi bai Isa ba bai Kai wannan matsayin ba da zaki bar mafarkinki domin farincikinsa ba". Alh Mustapha labaran yace " Aiko ya isa har yayi yawa duk wañnan abinda kike yi Taufiq ya fiki iko da rayuwar mujaheeda gaba daya idan kika aje sharadi ya aje sharadi shima dole mujaheeda ta dauki sharadinsa ta aje naki Haj girman miji fa ya wuce duk yadda kike tsammani". Tace a kufule" me Ka sani akan hakan tunda kai dai baka taba Zama Miji Nagari ba , har wane girman miji Ka sani" yace " komai zamana ba Miji nagari ba babu inda addini ya baki damar da zaki ci mutuncina ko ki ki yi min biyayya ba" nan da nan ta Kara fusata tace " Anki ayi maka biyayyar, zaman dolen da akeyi".

Cikin kagauta mujaheeda ta toshe kunnanta ta Mike " na tsani wannan rayuwar na tsani abinda kuke ma junanku, ni gidan mijina Zan koma ya fi min Akan na zauna ina cigaba da ganin abinda tun da na taso nake gani na Kuma tsana" tana Gama fadan hakan ta juya da sauri ta shige dakinta.

Cikin jajayen idanu Haj murjanatu ta juyo Kan Alh Mustapha labaran tace " Kai har kana da bakin yin irin wadannan maganganun Kai da babu Allah agabanka ko kana ganin akwai ranar da Zan manta da bakin halinka agareni ko kana ganin akwai ranar da zaka wanke kanka da ga bakin fentin da kayima kanka awajena saboda haka yafi sauki kayi shuru idan aka zo magana akan aure domin baka da bakin magana".

Kwata kwata Alh Mustapha labaran baya son maganar ta Kara yin tsawo domin yasan hakan bazai haifar da da mai ido ba.don haka shima ya ture kayan karyawar tasa gefe ya tashi ya dau makullin motarsa ba tare daya tanka irin maganganun da Haj murjanatu take sakar masa ba ya fice, fadan da take yi tuni ya Fara janyo hankalin masu aikin gidan.

Haj murjanatu ta tashi jikinta babu laka tabi mujaheeda daki. Tana shiga ta tadda ita ta shiga wanka.ta tsaya jugum komai ya kwance Mata ta dauka zatayi nasarar cire Taufiq acikin rayuwar mujaheeda amma ya Zama dole ta yarda da cewa mujaheeda ba zata iya barin Taufiq ba saboda mugun son da take masa. To Amna fa babu yadda zatayi ta iya yarda da Taufiq ya tauye Mata rayuwar ya ya hanata walawa da jindadin rayuwarta lalle dole tasan yadda zatayi ta ladaftar da Taufiq ta yadda zai biyu yayi duk abinda mujaheeda take so atakaice dai tana da bukatar mujaheeda ta mallake Taufiq ya Zama rakumi da akala ta yadda ko kudi aka bashi akace ya batama yar ta rai ko ya sata damuwa bazai iya ba.tana son mujaheeda ta Zama ita kadaice me juya rayuwar Taufiq yadda ta so ta ga dama tana ganin lokaci yayi da zata mayar da Taufiq kamar yadda ta mayar da Alh Mustapha labaran ta yarda zata Zama Mijin Shi Kuma ya Zama matar.

Cikin sassarfa ta fice daga dakin mujaheeda ta shiga dakinta ta rufe kofa ta sa makulli, ta dauki wayarta ta Kira aminiyarta Haj Nana bugu biyu Haj Nana ta dauka Jin muryar Haj murjanatu cikin tashin hankali yasa ba ta ja maganar da tsawo ba tace, " Haj yaya dai lafiya kuwa" tace tana Kai gauro da Mari atsakar dakin " kina gida ne Haj" ta gyada Kai " Eh ina gida lafiya dai ko?" Ta saki numfashi tace " Ba lafiya ba gani nan dai zuwa gidan yanzu".

Haj Nana tace " To shikenan sai kinzo". Nan da nan ta fada bandaki tayi wanka cikin kankanin lokaci ta fito ta Gama shiryawa cikin kiriyar atsmfarta super exclusive ,ta dora gyalenta akanta ta dau Jakarta ta fito.

Bata ko bi ta Kan mujaheeda ba ta fice abinta .

Direba na ganinta ya Mike ya nufi wajen motoci " barka da fitowa Haj, awace motar zaa fita?" Ta dube Shi tace " ko wacce ma Ka dakko" fahimtar tana cikin sauri ya sa ya wuce da sauri ya fito da makullin daya daga cikin motocin da suka cika rufunan motocin gidan.

Ya Bude Mata ta shiga da sauri ya rufe ya shiga ya ja maigadi ya bude masa kofa ya fice Yana tambayarta " ina mukayi Haj" Kai tsaye tace " gidan Haj Nana" ya gyada Kai kamar tsohon kadangare yace "Angama ranki ya dade.

DAGA TASKAR YAR GIDAN IMAM

NIMA MATARSA CE
NA
HÀBIBA ABUBAKAR IMAM
(YAR GIDAN IMAM)
BANI NA ASHIRIN DA TARA
****

Isar Haj murjanatu gidan Haj Nana Kai tsaye ta shige cikin gidan.

Zaune a katon falonta ta isketa da alama zuwanta take jira.haj murjanatu ta fada Kan kujera tana runtse idanunta, Haj Nana ta taso da sauri ta dawo kujerar da take zaune tana yi Mata kallo me cike da alamar tambaya ta dafa kafadarta tace " Haj wai lafiya kuwa?" Ta bude idanunta da suka rine suka koma jajir ta dora akan Haj Nana gami da numfasawa sannan tace "Haj ina cikin damuwa".

Ta gyada Kai a kagauce tace " na sani, yanzu damuwar ce kawai nake son na ji menene?" Ta

huro iska daga bakinta tace " ina da damuwar data wuce na wannan sakaran yaron ne Taufiq"
Haj Nana tace " Dama nayi zaton damuwarsa ce, me Kuma yayi ya saki mujaheeda ne?" Ta saki tsaki tace " ni dama zai sakenta ai Saina fi kowa farinciki , nema kawai yake ya zamar min karfen kafa, gaba daya kamar ya asirce min ya bata ganin laifinsa Akan komai".

Haj Nana tace " aah kada dai ki ce min duk abinda ya faru mujaheeda ta manta". Ta gyada Kai " ba zata manta ba tunda ta dora ma kanta jarabar sonsa, Shi yasa nake tunanin Kada ya kassara min ya domin dai nayi Imani bazai canja halinsa ba akan zamantakewar sa da mujaheeda hakan yasa nasan mujaheeda ba zata taba fita da ga damuwa da tashin hankali ba kin Kuma fi kowa sanin babu abinda na tsana sama da damuwarta".

Haj Nana tace " nasani shiyasa tun farko na so ki hanata aurensa komai tsiya amma tunda Muka je wajen malami daya ya tabbatar sai anyi auren shikenan kika saduda, babu fa abinda zaki hada da talaka kiga dai dai, yanzu katsmaimai menene ke faruwa".

Haj murjanatu tace cike da damuwa" duk zaman nan nata agida na dauka ta hakura da Taufiq ne musamman data ce min Sam bata son na dinga Mata maganarsa, ashe wai yarinya nan Jira take ta huce daga fushin da tayi kawai dazun nan muna karyawa tace min wai zata koma dakinta, na rantse Miki Haj ji nayi kamar an buga min guduma a kahon zuci"

Haj Nana tace tana kebe baki " Haj kema fa tun farko kinsan sakacinkine tunda kin riga kin fahimci taurin Kai da son nuna isa da iko sune taken Taufiq ai kamata yayi tuni abi ta kansa a murkushe Shi, tunda dai ba zaki hana mujaheeda sonsa ba balle ki iya rabasu Kuma ma ta yaya kike son ki gogama yarki bakin fenti ki bata Mata tarihinta ta hanyar maida ita karamar bazawa, ai maimakon hakan kamata yayi a kamashi a daure ya bi ba wai ki kashe Mata aure ba tunda kika riga kika bari akayi to fa bai kamata akashe ba".

Haj murjanatu ta gyara zamanta tana kallon Haj Nana sosai tace " hakane Kuma fa, shi yasa nazo wajenki neman shawara ya za'ayi domin dai raina ya Fara raya min na bi hanyar da ba na son bi".

Haj Nana tace " hmmm wannan dai hanyar da bakya son bi din itace ya dace kibi" ta Kara muskutawa tana cigaba da cewa " mafi yawanci mazan yanzu sune suke sa Kabi hanyar da bata kamata ba saboda bakin halinsu da mugunta da kokarin maida mace baiwa gami da kuntatawar da suke yi mana, shine dalilin da yasa idon mu yake rufewa Muke fadawa hanyar da mu kanmu mun San ba dai dai bace Amma ya za muyi? Hakurin ne da wahala".

Haj murjanatu tace " hakane gaskiya ne" Haj Nana tace " Shi yasa kika ga na gwammace na zauna na rsyu ba aure tunda maigidàna ya rasu ke shaida ce ban Kara marmarin aure ba domin babu komai acikinsa face hawan jini da ciwon zuciya, Shi yasa nake mamakin Matan da mijinsu ya rasu idan Naga suna rubibin Kara aure na kance su Kam me suka tsinta a aurensu na baya da har suke marmarin Kara yin wani". Haj murjanatu ta saki ajiyar zuciya tace" hmmm aure Kam akwai jarabawa da yawa acikinsa, haka zalika duk wata fitina da mace ke fadawa na kauce hanya duk namiji ne sila yarinya da tsohuwa duk babu wacce ta tsallake siradin wukakanci da cin amanar namiji, yanzu dai ko ni aya ce irin cin amanar da Alh yayi min har na koma ga Allah bazan taba mantawa ba da cin mutunci hakan yasa nayi masa abinda nayi amma har yanzu ban huce ba duk iya shekarun nan zuciyata kamar ta fashe nake ji Kuma duk mallakar da nayi masa ban taba Samun sauki da natsuwa ba , hakan yasa akullum nake tunanin yadda Zan katange yata daga masifa irinta da namiji sai gashi Kuma ta jajibo Wanda zuciyata bata taba Samun nutsuwa da Shi ba".

Ta Kara numfasawa ta cigaba da cewa " ke shaida ce akan irin son da nakema yata da irin kulawar da na bàta babu abinda ta rasa arayuwa kudi da matsayi duk baya ta basu to ta yaya duk Zan gama wannan fafutukar sannan na bari wani can da ya ganta daga sama ya zo ya wulakanta min ya bayan yasan irin lalurar dake tattare da ita bai tayani Kula da lafiyarta bane Zan barshi ya Kara nakasa min ita ina bazai yuwu ba ba'a haife Shi ba".

Haj Nana tace tana Kara kafe idonta akan Haj murjanatu" To idan ko hakane sai dai abiyo masa ta bayan gida, domin dai kinsan Maza da kafiya da tsayawa akan kalma daya don wannan bazai taba tankwaruwa ba Kuma Kota koma haka zaa cigaba da yi babu abinda zai daina tunda ya riga ya amsa sunansa namijin bahaushe".

Haj murjanatu tace " Nima tunanin da nayi Kenan , kawai mu je wajen Mallam me guru ayi ta ta kare" (subhanallah duk Wanda damuwa zata same Shi Bai maida lamarinsa ga Allah ba ya zabi ya je wajen wanin ubangiji domin biyan bukata wannan asara ta tabbata agareshi domin yayi hannun riga da Allah da manzonsa Yana kuma cikin bata mabayyaniya matukar Kuma ya mutu akan haka to bashi da makoma face wutar jahannama abadan da'iman, ta yaya Kan duniya da iya dadewarka acikinta kayi shekara dari itama idan hakan ya riskeka kana cikin fitina ne domin awannan lokacin Baka Jindadin komai a duniya amma Ka zabi duniya akan lahirarka wacce itace madauwamiya , ance da digon wutar jahannama zai diga a duniya kamar kofar allura to da duk duniya da abinda ke cikinta sun kone kurmus to kayi tunani balle ace Kai zaa dauka ajefa acikin wannan wutar wa'iyazubillah Allah Ka barmu da imaninmu Ka rabamu da shirka).

Haj Nana tace " fakat wannan Shi kadaine mafita sai ki shirya kisa rana muje".

Ta gyada Kai tace " eh, zan bari Naga komawar ta ta idan harta dage da son yin hakan bayan ta koma Zan kiraki sai kizo muje".

Haj Nana tayi dariya tace " magana ta kare, don Allah hajiya ki saki ranki kiyi walwalarki Taufiq din banza dama aike ce kika daga masa kafa," Haj murjanatu ta saki tsaki tace " shashasha talakan banza ni dana wani me kudi ne yake wannan iko da isar dana daga masa kafa domin ya isa yayi ne, amma Kai kana talaka kana fama da ràshin kudi amma Kuma Ka dinga wulakanta wacce ko gwanjonka akayi Saita saye Ka". Haj Nana ta fashe da dariya harda kyakyatawa tace " Kai Haj baki da dama, bari naje na Samo Miki abinda zakisa a makoshinki" ta Mike tana dariya ta wuce Haj murjanatu tace " ina masu aikin naki naji gidan tsit" tace " sun tafi ganin gida" Haj murjanatu tace " ke dai bakya Jin magana na rabaki da dakko Yan aiki daga kauye kin ki, Basu da kirki kina nan zasu nemi su kasheki" dariya ta Kara Sawa tace " sabo Haj,na riga na Saba dasu" ta tabe Baki tace " hmmm ke kika Sani".

Ta dade agidan Haj Nana sai da ta Gama ciye ciyenta da shaye shayenta sannan ta Kama hanyar gida cike da daukar shawarar aminiyarta.

****

Karfe shida na yamma mujaheeda tayi sallama dakin mahaifiyarta. Tana zaune a gefen gado tana waya, mujaheeda ta Sami gefen gadon itama ta zauna tana kallonta harta Gama wayar.

Ta juyo tana kallonta tace " yaya dai?", Mujaheeda tayi sanyi da muryarta sosai tace " mummy Kan maganar dazu ne na fahimci ranki ya baci Wanda ba manufata ba Kenan, ina son na koma dakin mijinta ne kawai domin ina sonsa Kuma bazan iya rayuwa babu Shi ba".

Ta yi shuru tana kallonta Haj murjanatu tace " uhum cigaba ina jinki".

Ta langabar da Kai gefe tace " mummy bana son Kiji haushi ko ki damu, nasan kina Sona hakanne Kuma yasa bakya son ganina cikin damuwa, na Sani Yaya Taufiq ya bata min rai na Kuma ji matukar zafi akan hukuncin da ya yanke min ba tare da nuna yarda agareni ba, amma mummy yayi nadama duk da bana saurarensa kullum Saiya turo min sakon ban hakuri da rikon na dawo, akalla yanzu na gane ya San ina da amfani acikin rayuwarsa Kuma mummy ta yaya za'a raba aurena da Taufiq bayan Shi kadaine nake son na rayu da Shi har a gidan aljanna".

Ta nisa ta cigaba da cewa " don Allah mummy ki so Taufiq ko yaya ne Shi kadai ne zai bani kwanciyar hankali ".

Haj murjanatu ta Dan yi murmushi tace " Babu komai mujaheeda duk abinda kike so Shi nake so idan komawarki gidansa Shi zai Baki kwanciyar hankali to ina Miki fatan alheri" ta kwanto ajikinta cike da shagwaba tace" mummy nagode sosai, dazu bayan fitarki munyi waya da Shi mun daidaita yace zai zo bayan sallar magriba mu tafi" wani irin bakinciki ya kama Haj murjanatu haushin Taufiq ya Kara kamata ji yadda mujaheeda ta zubar da kimarta ta bashi Dama yazo ya dauketa sai kace kayan wanki ba zata bari ta koma cikin daraja da kima ba.

Bazata bari ta kirashi da kanta ba ya zo ta cimasa mutunci ta kafa masa sharadai ba, yanzu shikenan ya ci bulus haka zai zo ya dauketa babu daraja .

" Kinji ko mummy" Kai kawai ta gyada cike da takaici tace " Naji Allah ya kaimu" tace "Amin" cike da farinciki ta tashi ta fita. Haj murjanatu ta ja tsaki ta buga hannunta akan gado tace " zaka gane kurenka Taufiq zanyi maganinka zakayi nadamar yin wasa da rayuwar ya ta".

DAGA TASKAR YAR GIDAN IMAM

NIMA MATARSA CE
NA
HABIBA ABUBAKAR IMAM
(YAR GIDAN IMAM)
BABI NA TALATIN
****

Haka Haj murjanatu ta dinga kokarin boye damuwa da takaicinta agame da komawar mujaheeda gidàn Taufiq domin bata son damuwar yarta ba Kuma ta son ta San abinda take kullawa acikin zuciyarta.

Dawowar Alh Mustapha labaran guda gaf da magriba ya Kara bakanta ran Haj murjanatu domin dai tasan dalilin dawowarsa don tana Jin lokacin da mujaheeda take yin waya da Shi tana gaya masa batun komawarta bayan sallar magriba shine ya wani kunkumo ya janyo jiki ya dawo saboda tsabar ràshin aikin yi.

Hakan yasa kamar kullum ko kallon arziki ba tayi masa ba.

Mujaheeda ta Kara yin wanka ta kintsa cikin wata hadaddiyar doguwar riga me ruwan siminti sabuwa ce dal domin zamanta a gidan duk sabbin Kaya aka sayo mata Wanda har yau bata gama sa su ba.Rigar tayi matukar amsarta tayi kyau kwarai matuka idan Ka debe yar ramar da fuskarta tayi.

Ana ko idar da sallar magriba Taufiq Yana shigo da motarsa cikin get din gidan Wanda da alama sallar magriba din ma a masallacin kusa da gidan yayi saboda tsabar kaguwa ya zo wajen mujaheeda domin dai ta ji ajikinsa ya fahimci Yana fa son mujaheeda ya Kuma Saba

Zama da ita duk da zaman doya da manajan da suke yi to fa yayi matukar rashinta Yana bukatarta acikin rayuwarsa sosai yayi nadamar komai ya Kuma yarda da cewa duk me turo masa hotunan nan so ya ke ya Raba Shi da matarsa Wanda ayanzu ya katange duk wata Kofa da hakan zai Kara faruwa domin dai ayanzu ya riga ya tusama Kansa yarda da mujaheeda dari bisa dari domin duk Wanda zai bada shaidar kamalarta hakika ya yarda bayan shine domin dai shine mutum na farko da ya Fara sanin ta a matsayin ya mace .

Kai tsaye Taufiq ya shiga cikin gidan a falon kasa ya Sami daya daga cikin kujerun falon ya zauna, bai dade da zaunawa ba Alh Mustapha labaran ya fito domin ya riga yasan da isowarsa kasancewar ya hango tsayuwar motarsa ta windon sama.

Yana shigowa Taufiq ya zamo kasa ya zauna Yana kokarin gaishe shi ya amsa bayan ya zauna akan kujerar Yana ce masa Ka tashi Ka zauna Kan kujera mana, ya girgiza Kai yace " aah nan ma ya isa".

Yana rufe bakinsa Haj murjanatu ta sakko daga sama fuskarta babu yabo ba fallasa mujaheeda na binta abaya babu komai ahannunta da alama ba zata tafi da komai gida ba duk abinda asaya Mata bayan zuwanta gidan babu abinda ta dauka.

Cikin walwala mujaheeda ta zauna ganin Taufiq zube akasa yasa itama ta zauna akasa.hakan kuwa ya Kara bakanta ran Haj murjanatu haka ta zauna rai abace Taufiq ya gaisheta daker ta amsa. Sannan Taufiq yace "Nazo Zan tafi da mujaheeda ne nagode Allah ya saka da alheri ina Kuma neman afuwar duk abinda ya faru".

Alh Mustapha labaran zaiyi magana kenan Haj murjanatu tayi karaf ta amshe maganar tace " gata nan zata koma sai Ka cigaba daga inda ka tsaya,bazance Ka daina ba kayi ta yi" Alh Mustapha labaran yace " ya isa Haj don Allah ayi hakuri komai ya wuce Allah ya daidaita tsakaninsu ya kade duk wata fitina" gaba dayansu suka ce Amin banda Haj murjanatu.

Àlh Mustapha labaran yace " don Allah Ku zauna lafiya Ku hada kanku Kada wata baraka ta Kara fitowa atsakaninku" Taufiq yace "in sha Allah babu abinda zai Kara shiga tsakaninmu sai alheri" .

Daga nan Alh Mustapha ya cigaba da yi musu nasiha amma har yayi ya Gama Haj murjanatu ba tace uffan ba.ko da mujaheeda ma tayi Mata sallama a dole ta amsa tana kokarin boye bacin ranta.

Amma a lokacin da taga Taufiq yasa mujaheeda gaba sun tafi ji tayi kamar ta rushe da kuka saboda tsananin bakinciki.

Bayan tafiyarsu shima Àlh Mustapha labaran kakkabewa yayi ya haye sama saboda ya Lura da mugun kallon da Haj murjanatu take sakar masa yasan karshe abin ya dawo Kansa ta zazzage masa komai aka.

Jugum ta cigaba da Zama afalon takaici na damunta lalle lokaci yayi da Taufiq zai fuskanci hukuncinta sosai take Kara Jin tsanarsa acikin zuciyarta.

Acikin mota kuwa hira sosai Taufiq da mujaheeda suke yi bayan Taufiq din ya bata hakuri ya Kuma cigaba da labarta Mata irin zaman ràshin dadin da yake yi agidan bayan babu ita. Hakanan take jindadin yadda Taufiq yake gaya Mata son da yake Mata da irin rashinta da yayi tabbatas ta fahimci abubuwa da dama da da bata fahimta ba a game da Taufiq, murmushi kawai take yi tana jinta acikin wata sabuwar duniyar da take son kasancewa ciki.

Isarsu gidan mujaheeda ta tadda an gyara komai ko'ina sai tashin kamshi yake yi matuka su kansu masu aikinta sun jidadin dawowarta domin sunyi rashinta agidan.duk wani nau'in abincin

da mujaheeda take so sun dafa Mata an cika Kan daining dasu.

Haka Taufiq ya sata agaba har sai data ci abincin ta koshi duk da dai dama bata da yunwa atare da ita.

Awannan dare dai sun cire komai sun nunama junansu tsananin kauna tamkar Daren farkonsu mujaheeda ta mallaki mijinta yadda take so, haka zalika soyayyar sa ta Kara kama zuciyarta tana fatan zamansu ya cigaba a haka har karshen rayuwa ba tare da fada ko tashin hankali ba.

Washegari kuwa Taufiq da Kansa ya dauki mujaheeda ya kaita gidansu domin ya gayá Mata yadda mahaifinsa ya damu da ita .

Zuwansu gidan ta kara gamsuwa da irin son da surikinta yake Mata don yadda ya nuna murna da jindadin sa afili domin rasa inda zai sata yayi gaba dayama afalonsa ta tare ita dai Haj saratu wannan kauna da fifiko da yake nuna ma mujaheeda abin ya Fara tuke Mata zuciya don bata ga dalilin da ita mahaifiyarta bata kaunar dansu Shi Kuma ya rasa abin kauna sai yarta abin ma har Yana son wuce gona da iri. Domin dai hatta furar da ake Dama masa ranar tare yasa a damo da mujaheeda haka ta Dama ta Kai musu.

Bata Kara shiga sabgarsu ba har Taufiq yazo tafiya da ita suka tattara suka tafi

****

Tun bayan komawar Kabir Kano muhseena ta fuskanci ya canja saboda yadda yake nacin kiranta awaya ya rage, sai dai kullum sako na tafe hakan yasa ko muhseena tayi tunanin akwai matsala sai Kuma ta saki ranta ta dinga Jin da akwai matsala da sakon ma bazai dinga turowa ba.

Duk da taso taji yayi magana da iyayen nasa ko kuwa har ya koma Bai Sami yin maganar dasu ba domin dai tana cike da son Jin sakamakon amma nauyi da kunya sun hanata tambayar sa.

Tabangaren Kabir kuwa tun bayan komawarsa Kano damuwa ta Kara masa yawa sosai yake son muhseena Amma ya rasa hanyar da zai bulloma mahaifansa nan da nan har ya rame baya iya maida hankali akan komai sai tunani Yana so. Muhseena Yana Jin tausayinta ba zai taba iya gaya Mata bazai aureta ba kamar yadda yake Jin mawuyacin abune ya iya rabuwa da ita.

Cikin ràshin karsashi ya shigo falon cikin sallama Haj Salma ta dago ta amsa tana kallonsa batun yau ba tana ganin damuwa da ràshin nutsuwa afuskar Kabir amma kwanakin nan abin yafi girmama, " Anti an uni lafiya" Kabir ya fada Yana kokarin zaunawa akan daya daga cikin kujerun da suka cika falon, ta amsa " lafiya Alhamdulillah, ba dai har Ka dawo daga kamfanin ba". Ya gyada Kai Yana rufe fuskarsa da hannunsa yace " Na dawo, bana jindadi ne yau", ta Kura masa Ido tace " Naga alama". Daganan ta taso daga inda take ta dawo kujerar kusa dashi tana kallonsa cike da kulawa tace ' Ba ciwo kake ba, damuwa ce kawai ke damunka Kabir",ya bude fuskarsa Yana kallonta Amma ya kasa cewa komai domin yasan gaskiya ta fada ba Kuma zai iya Musa Mata ba.

Ta cigaba da cewa " Tun dawowarka daga Durmi nake ganin canji atare da Kai Ka rage walwala baka fara'a kamar da hatta abinci ina Lura wani lokacin yadda aka Kai maka haka ake dakkowa ba tare da Ka ci komai ba,shin meke damunka?",yayi shuru Yana son ya tattara kalaman da zai gaya Mata, ta kasa hakuri ta cigaba da cewa " ko kana ganin kusancinmu da babbar alakarmu bai Kai Ka gaya min damuwarka ba".

Yayi saurin girgiza Kai yace "idan akwai wacce ta dace na gayama damuwa ai bayanki be anti sallama kefa a matsayin Uwa kike agareni " ta gyara zamanta tace " uhmmm ina jinka menene damuwarka meya tsayama arai yake kokarin hanaka walwala ".

Sannu ahankali Kabir ya gayama Haj Salma komai ya Kara da cewa " Na rantse Miki anti yarinyar nan na bukatar kulawa da tausayawa ina matukar Sonta ina jinta araina fiye da Tunaninki bata da wani farinciki arayuwa da ya wuce ni to Anti Salma ta yaya Zan iya cewa bazan aure ta ba bayan girma da kima da mahaifanta suke bani da Kuma ita da bata taba soyayya da ko wane namiji ba sai ni ".

Ya karasa magana tamkar me Shirin yin kuka Haj Salma ta shiga damuwa itama tace " Duk naji Kabir amma kai Yanzu a tunaninka zaka iya auren yarinyar da ba'asan ubanta ba komai so da tausayin da kake Mata " yayi saurin daga Kai yace " Abinda nake son su Baba su fahimta Kenan Anti Zan iya auren muhseena acikin ko wane irin yanayi ko da ace itace ta aikata wannan lefin da kanta to soyayyata zata fanshi hakan balle ba ita ta aikata ba, katamaimaima bana Jin akwai Wanda yasan yadda akayi amma an dauki karan tsana an dorama muhseena idan Kuma har aka hana auren irinsu to ta yaya zaa Sami me aurensu ko kuwa haka zasu Kare rayuwa babu Mijin aure Kenan".

Haj Salma ta jinjina Kai tace " Amma fa abinda kamar wuya Kabir ,domin ko ni idan ya tabbata bata da uba bazan iya Goya maka bayan Ka aureta ba amma idan har Ka dage Zan iya yarda Amma ba haka raina ya so ba, balle iyaenmu masu azabar kafiya Anya Kabir ba zaka hakura da yarinyar nan ba".

Yayi saurin girgiza Kai yace " bazan iya ba anti ina Sonta idan na hakura da ita zanyi matukar cutuwa " dai dai lokacin Àlh Musa ya shigo falon ya tsaya Yana kallonsu yace " me akayi maka da zaka cutu Kabir" gaba dayansu suka dawo da kallonsu Kansa Haj Salma na kokarin yin magana

DAGA TASKAR YAR GIDAN IMAM

NIMA MATARSA CE
NA
HABIBA ABUBAKAR IMAM
(YAR GIDAN IMAM)
BABI NA TALATIN DA DAYA
****

Tace " yauwa Alh dama yakamata ace kana nan don kaji abinda ke faruwa". Ya lalubi kujera ya zauna Yana kallon Kabir yace ," meke faruwa Kabir". Haj Salma tace " ina fatan Ka Kula da yadda Kabir ya canja ya rame ya fita hayyacinsa". Yadan numfasa yace " Na Lura Kuma harna Kira Shi na tambaye Shi damuwarsa amma yace min babu abinda ke damunsa, Wanda na bishi da haka ne kawai saboda Bana son na takura masa yin abinda baiyi niyya ba , na dai yarda da cewa komai daran dadewa zai biyoni da damuwar sa".

Kabir yayi kasa da Kansa cike da damuwa ayayinda Haj Salma tace " matsala gareshi Alh gagaruma' daganan sannu ahankali ta Gama labarta masa komai ta Kara da cewa " to ni bansan abinda zance ba " Alh Musa ya numfasa Yana kallon Kabir kamar daga sama Kabir yaji

Alh Musa yace "Ka rabu da ita Ka nemi wata ".

Gaban Kabir yayi mummunan faduwa ya dago da sauri Yana kallonsa.

Sannan yace "kawu ina Sonta matukar so ina tausayinta idan nace bazan aureta ba bansan halinda zata shiga ba".

Alh Musa ya jinjina Kai yace "Kabir idan har da gaske ne yarinyar nan bata da asali azahirin gaskiya sai dai kayi hakuri domin kasan halin mallam Hamza matukar ya kafe akan abu to baya janyewa balle Hafsatu da idan ta tsani abu babu me iya tankwara ta, bayan haka Kuma babu Wanda baya son yayi aure agidan mutunci Kuma wannan abin Kada Ka manta yaduwa yake yi Yana bin zuria, Kuma da kake maganar kana Jin tausayinta babu Wanda ya hanaka Ka taimaka Mata kayi Mata komai na kyautatawa amma banda aure".

Kabir ya Kara tsunduma cikin tsananin tashin hankali yace " kawu kune kadai karshen fatana idan Baka Goya min baya na Bana Jin Zan samu abinda nake fata domin nasan akwai kyakkyawar fahimta tsakaninka da Baba zai iya tsayawa ya saurareka kilama har ya yarda da abinda na zo da Shi".

Alh Musa yace " yanzu me kake nufi kenan" yace " ina nufin Ka taimakeni kaje Ka yi magana da su Baba Ka fahimtar dasu irin son da nake ma muhseena da ràshin haramcin aurena da ita, kila zasu sakko su gane bata da wani laifi aduk rayuwar da ta shiga ciki".

Alh Musa yace " ta yaya kake tsammanin zanje na fahimtar dasu bayan nima ban fahimta ba domin dai ni Kaina Bana goyon bayan Ka aureta don haka zaifi maka Ka hakura kabar wannan maganar Ka nemo wata Ka aura gasu nan da yawa sai wacce Ka zaba"

Wani irin bakinciki ne ke Kara ratsa zuciyarsa Yana Jin wani abu nayi masa yawo acikin kirjinsa fahimtar da Haj Salma tayi ne na mugun yanayin daya fada yasa tayi saurin kallon Alh Musa tace" Amma Alh da an bi abin ahankali idan har Kabir ya dage ayi hakuri a Goya masa baya ya aureta" yayi Mata kallon tsaf yace" ya auri yar shege?, Ai abu daya ne zaisa na Goya masa baya shine idan har an bincika yarinyar ba cikin shege bace shine kawai Zan aminta da bukatarsa don haka da Kaina zanyi binciken nasabarta idan ya tabbata abinda ake jifanta dashi gaskiya ne to ya Zama dole kayi hakuri da ita".

Haj Salma ta dubi Kabir Wanda gaba daya nema ma yake ya fita hayyacinsa tace " to kaji Kabir kawunka zaiyi bincike Ka kwantar da hankalinka tare da adduar Allah yasa ba gaskiya bane abinda ake fade" ya kasa cewa uffan illa doddogarawa da yayi ya tashi ya fice Yana gauraye hanya inda yake tsammanin zai Sami sauki da goyon baya nan ma kofa a kulle take shin yaya zaiyi da ransa?.

Bayan fitarsa Haj Salma ta dubi Àlh Musa tace " Alh yaron nan fa yayi nisa , Yana son yarinyar nan sosai Baka ganin Hana Shi aurenta zai Zama matsala ".

Alh Musa yace " hakanan zai warware ya hakura Amma bazai yuwu ya aureta ba Bana cikin wannan maganar, kullum ana adduar ya Sami Mata yayi aure sai Kuma yazo da wannan maganar mara dadi". Ya Mike Yana cigaba da maganganunsa ya shige bangarensa yayin da Haj Salma ta buga tagumi duk abin baiyi Mata dadi ba Sam Sam bata son damuwar Kabir domin jinsa take tamkar Dan da ta Haifa a cikinta.

Muhseena dawowarta daga islamiyya Kenan ta shiga gidan.Ande Dije na tsaye atsakar gida tana aikin zazzagama Hajara fada cikin matukar fusata da bacin rai take cigaba da cewa " har kina da bakin da zaki mun wa'azi ke ai yakamata ayima wa'azi da har yanzu kika kasa fahimtar da yarki cewar Umar ba ubanta bane a yaron banza da wofi kika Samo ta akan neman duniya

kika je kikayi barin mutuncinki kika Samo ta " cikin hawayen takaici Hajara tace " ni ban Samo ta a yawon banza ba ki daina jifana da wannan mummunar maganar" cikin daga murya tace " Da Aina kika samota idan baa yawon banza ba, gashi nan kin dorama da na wahala kullum Yana cikin wahalarki ke da yarki me ake da zuria irin taki don haka ni har abada bazan taba kallon muhseena da wata nasaba ba don babu abinda na hada da ita babu ruwan biri da gada," cikin hawaye masu dumi Hajara tace " yanzu duk tsawon rayuwar da mukayi tare ba zaki iya kallon muhseena amatsayin jikarki ba" tace ," don me Zan kalleta amatsayin jikata bayan ba jikata ba ce babu abinda na hada da ita" cikin fushi Hajara tace " Shi yasa Allah ya Hana ki Samun jikar ". Ande Dije ta Kara fusata tace " in dai daga gareki Zan Sami jika to Bana bukata ".

Jikin muhseena na rawa komai ya tsaya Mata duhu take gani sosai zuciyarta tana matukar suya da karfi tace " don Allah kuyi shuru kuyi hakuri Kada kusa zuciyata ta fashe".

Agigice Hajara ta dubi inda muhseena take tsaye abinda take gani acikin idonta Shi ya tabbatar Mata da cewa ta ji duk irin maganganun da suke yi.

Ahankali ta ratso cikin tsakar gidan tana yima Ande Dije wani irin kallo tace cikin hawaye "Ande aiya rayuwar da mukayi tare ya ci ace ko yaya ne kin so ni ko da ace ina da lefi balle ace Bani da lefi Akan duk wani zargi da kuke ma mahaifiyata , haka zalika ina da tabbacin ko da ace ta wata hanyar aka same ni nayi Imani mahaifiyata ba a yawon banza ta Samo ni ba sai dai ta wani dalilin da ban, Amma don Allah na rokeki ki sassauta mana haka ki fita acikin rayuwar mu". Tana Gama fadan haka ta juya tayi ma Hajara wani kyakkyawan kallo tayi wani bushasshen murmushi sannan ta wuce daki .

Ande Dije ta kasa cigaba da fadan maimakon haka ma itama dakinta ta shiga ta saki labule.

Hajara komai ya kwance Mata faduwar gabanta ta tsananta yau dai muhseena ta ji abinda take son sani daga bakinta ta yaya zatayi ta kauda wannan tunanin daga zuciyar muhseena.

Daker Hajara ta iya Ciba kafarta tamkar wacce bata da laka a jikinta ta shiga daki.

Zaune Akan katifa ta tadda muhseena ta hada Kai da guiwa sosai sautin kukanta ke fita. Hajara ta dawo gefenta ta zauna tana kallonta tace " don Allah Kada kisa damuwa aranki duk abinda kika ji ki barshi a matsayin arashi Kada ki.... ?" Muhseena ta katseta cikin kuka tace "aah Inna Kiji tausayi na ki gaya min gaskiyar lamarin nan , domin yau itace rana ta farko da na yarda na Kuma gasgata cewa Baba bashi bane mahaifina saboda Ande ta Fadi haka agabanki amma bski Musa ba illama amsarki data Kara tabbatar da cewa abinda Ande ta fada gaskiya ne".

Kukanta ya Karu tace " meyasa ba zaki gaya min gaskiya ba bayan duniya ta sani ban Kuma tsira daga mugayen kalamansu ba ràshin gaya min gaskiyar Kuma baida duniya ta daina kallona da abinda ake fada ba to don meye yasa ba zaki iya gaya min gaskiya ba bayan nice duk duniya ya dace naji gaskiyar domin magana ce ta rayuwata da makomarta ".

Gaba daya Hajara ta Kara tsunduma cikin tashin hankali zuciyarta na gaya Mata Anya tayima muhseena adalci kuwa na kin sanar da ita gaskiyar labarinta, Anya kuwa lokaci Bai yi ba da zata gaya Mata gaskiyar komai ba.

Muhseena ta dago da idanunta shatkaf da hawaye tace " Inna don Allah ki fitar Dani daga duhu ki fitar da ni daga fitinar tunani da bakinciki da ke damuna ki gaya min wacece ni daga bakinki ya kamata naji komai Kuma ina tabbatar Miki matukar kika gaya min gaskiyar to ina tare da ke ".

Hajara tasa hannu ta goge hawayenta tana kallonta tace " muhseena babu abinda sanin gaskiyar zai Haddasa Miki da ya wuce Karin tashin hankali" tace " tashin hankali tuntuni nake

cikinsa idan Kuma kika gaya min gaskiyar to babu bakincikin da zanji Saima na Sami nutsuwa domin ni na yarda da kaddara".

Asanyaye Hajara tace " shikenan idan har kina da karfin halin Jin gaskiya to Zan gaya Miki komai ayau Zan gaya Miki duk abinda kike son sani".

Muhseena ta numfasa tace " A shirye nake Inna"

" Kada ki sake wani abu ya fito daga bakinki agame da muhseena " furucin mallam Umar ya datsema Hajara harshen yin magana, ya karasa magana ya na shigowa cikin dakin fuskarsa cike da damuwa da tashin hankali Yana kallon Hajara yace " me yasa zaki karya alkawarin da kika yi min?" Cikin hawaye Hajara tace " mallam Ka gafarceni, amma ina ganin kamar lokaci yayi da ya kamata muhseena tasan komai ".

Mallam Umar ya girgiza Kai yace " wasu abubuwan zaifi kyau abarsu a boye yadda suke don haka babu wani amfanin gaya Mata wani abu".

Cikin kuka me karfi muhseena tace " don Allah Baba Ka Bari ta gaya min Allah ya Sani kuna cutar da ni da tunani na ina bukatar sanin wacece ni waye Kuma mahaifina?".

Ji yayi kamar an caka masa mashi a kahon zuciya yace " yanzu muhseena Ashe har akwai wata rana da zaki tambayi waye mahaifinki bayan NI duk duniya kina da wani mahaifin da ya wuce ni ne?" Ta jinjina Kai tace " Bani da wani mahaifi da ya wuce Kai Baba , Amma ina bukatar sanin asalina Ku Gaya min gaskiya na gaji da wannan bakar rayuwar me cike da kyama da ràshin sanin makomata ".

Da karfi mallam Umar yace " nine mahaifinki ni na haifeki".

Ande Dije ta dage labulen dakin tana kallonsu tace" Kaine mahaifinta aina,? Kaga Ku gayama yarinya gaskiya wannan abin bazai binnu ba har karshen rayuwa" tana Gama Kara watsama wutar fetur ta saki labule ta koma, ayayinda Mallam Umar ya ji kamar duk an zare masa lakar jikinsa furucin mahaifiyarsa ya Kara bata lamarin muhseena ta watsa musu idanunta tace " gaskiya ta fada don haka Kuma gaskiyar nake son ji daga gare Ku" ta Kara kallonsu ta fada da karfi " haka ya isa, shin wacece ni waye mahaifina?".

Gaba daya sun firgita da Jin yadda muhseena ta Fadi maganar cikin karaji da tsananin fusata.

DAGA TASKAR YAR GIDAN IMAM

NIMA MATARSA CE
NA
HABIBA ABUBAKAR IMAM
(YAR GIDAN IMAM)
BABI NA TALATIN DA BIYU
****

Da sauri Hajara ta nufi inda muhseena take gaba daya ta rungumeta itama kukan take mai karfi, " ki kwantar da hankalinki" ta girgiza Kai tace " babu kwanciyar hankali atare da ni matukar baku gaya min gaskiyar lamarin ba, haba Inna yaya kuke son nayi da rayuwata na rantse Miki daurewa kawai nake yi amma na kusa gazawa zuciyata ta kusa kasa daukar wannan masifar, Inna Kuji tausayina Ku fiddani daga cikin wannan kangin"

Mallam Umar yace " ki natsu muhseena bana son ko kadan maganganun Ande su Sanya

Miki shakku acikin zuciyarki" ta waigo ta dube Shi cikin zubar hawaye tace " Baba don Allah mu daina yaudarar junanmu kinsan gaskiya kawai ku gaya min ko na Sami kwanciyar hankali, zuciyata nayi min zafi tana min kuna Ku taimaka min".

Hajara ta dubi mallam cikin hawaye tace " kayi hakuri mallam nasan kayi min dukkan halacci Kuma duk duniya muhseena bata da wani uban da ya wuce Ka, babu Kuma Wanda zata kalla amatsayin uba bayan Kai, don haka ayau ina son Ka sauke min nauyin alkawarin dake Kaina saboda na gaya ma muhseena ainihin gaskiyar da take son ji domin Samun kwanciyar hankalinta da nawa".

Damuwa ta Kara baibaye fuskar mallam Umar yace " kina ganin gaya Mata shine zaisa kwanciyar hankali gareta (ya girgiza Kai) Sam ba zai kawo kwanciyar hankali ba sai dai ya Kara cabe lamarin ya Kara Mata matsananciyar damuwa da tashin hankali, Kuma ma meye amfanin gaya Mata abinda babu Shi meye amfanin gaya Mata barnar da babu yadda zaayi a gyara don haka ban amince ba ban goyi bayan ki gaya Mata komai ba, idan Kuma kika gaya Mata to ba da yawuna ba kin Kuma take umarni na".

Muhseena ta Kara rushewa da kuka ya Matso ya dafa tsakiyar kanta yace" ke ya ta ce halak malak babu Wanda zai canja hakan Kuma amatsayina na mahaifinki na umarceii da ki bar wannan maganar ki Kuma tsaida ruwan idanunki ki fauwalama Allah komai".

Yana Gama fadin haka ya juya cikin matukar damuwa da tashin hankali mara musaltuwa ya fice daga dakin ganin Ande Dije atsakar gidan da alamun duk tana Jin abinda suke fada Kai yasa kawai zai fice daga gidan cikin daga murya tace " Ai Kai Ka dakkoma kanka bala'i ta yaya zaka kwace abinda ba Naka ba ta ina yarinyar nan ta Zama taka to Kada Allah yasa Ku Gaya Mata gaskiya tunda ta dage dole sai taji daga bakinku zata gasgata " haushi ya Kara cika masa ciki ficewa kawai yayi ba tare da yace uffan ba.

Ta saki tsaki tace " naji karfin hali wai barawo da sallama, to Kada Allah yasa Ka gaya Mata Kai ba ubanta bane hakan bashi zai hana duniya ta cigaba da gaya Mata abinda bakwa so agaya Matan ba.

Haka Hajara ta cigaba da lallaba muhseena tare da kwantar Mata da hankali duk da ta tabbatar da cewa ta riga ta kai bango domin bata taba bijirewa irin na yau ba.duk wata Kalma da ke fita daga bakin Hajara kunan zuciya sukesa muhseena daga bisani kwanciya kawai tayi Akan katifa ta runtse idanunta sosai bata bukatar Jin komai da ya wuce abarta ta cigaba da jinyar zuciyarta da take ji kamar zata fashe.

Dole tasa Hajara ta tashi ta fita domin ta fahimci muhseena bata bukatar ta Sam Sam.

Tana fita tsakar gidan ta Kara tsunduma cikin tsananin damuwa domin ganin irin kallon da Ande Dije keyi Mata , kujera yar tsuguno ta janyo ta zauna ta ba Ande Dije baya tana kokarin maida hawayenta tare da adduar Allah yasa Kada Ande tayi Mata magana don bata bukatar ta Kara Mata damuwa akan wacce take ciki, Amma addu'ar ta bata karbu ba domin kuwa cikin kausasshiyar murya Ande Dije tace " ba zaki taba rabuwa da bakinciki da ràshin sukuni ba matukar baki gaya ma muhseena ainihin gaskiyar ba domin kin cutar da ita kin zalunceta ko wannan boye Matan da kikayi ya isa ya Zama masifa atare da ke" Hajara tace " don Allah kiyi hakuri kibar wannan maganar haka" " naki na bari gaskiya ce bakya so Kuma dole Saina fada Miki , me kike tunani yasa kika ki gaya Mata bayan tuni duniya ta sanar da ita, ko kina tsoron tsana da kiyayyar da zata nuna Miki ne matukar kika gaya Mata ko ita wacece"

" Babu wani abu da zatayi ko Wanda ta riga tayi da zai sani na tsaneta komai muni da girman

abin uwata itace jarumata Zan Kuma yi Mata dukkan Uzuri, Kuma ko da me duniya zata cigaba da fada akaina matukar banji daga bakin mahaifana ba bazan taba yarda ba ko gasgatawa" muryar muhseena ce ta daki dodon kunnan Ande dije.da

A gaggauce Hajara ta juya tana kallon inda sautin maganar ya fito.
Muhseena ce tsaye akofar daki tana yima Ande Dije wani irin kallo me cike da tsana.

Ande Dije ta yi tsaki tace " umm kanku ake ji" muhseena tace " Shi yasa tunda kanmu ake ji to ki kyalemu Muji da Kan namu ki daina kokarin shiga abinda babu ruwanki aciki". Cikin fusata tace " Kada ki sake kiyi min ràshin kunyar da kika gada kika Saba " zatayi magana kenan Hajara ta taso da sauri ta kama hannunta suka koma daki tana cewa Kada kiyi magana.

Haka muhseena ta kasance cikin tashin hankali har zuwa bayan isshai da Kabir ya kirata gare Shi ne kawai ta Sami nutsuwa duk da taki yarda ya gane tana cikin damuwa.

Amma fa shima ta bangarensa sosai muhseena take tsinto sakon damuwa acikin muryarsa.wanda ta kasa daurewa sai da tayi masa tambayar " meke damunka" ya jinjina tambayar ta ta ahankali yace " me kika gani" tace " hakanan nake Jin kamar kana cikin damuwa " ya ce " aah babu wata damuwa kawai yau na gaji ne da aiki gaba daya jikina duk ya saki".

Ta numfasa tace " Amma Ka Sami damar yin magana da magabatanka kuwa agame da maganar auren mu".

Gabansa yayi mummunar faduwa ya dafe Kansa daya Sara masa.ahankali ya tattaro yawun bakinsa ya hadiye sannan yace " muhimmiyar magana ce da bai kamata ayita a waya ba shiyasa na bari harna Kara dawowa sannan muyi maganar". Ya numfasa tace ' to Allah ya dawo da Kai lafiya" ya amsa da Amin .

Hira suka cigaba da yi wacce gaba dayansu hirar bata musu dadi domin kowa cikin muguwar damuwa yake, hakan yasa su kayi sallama.komai dai sabo ya dawo ma muhseena domin ji take tamkar yau ce ranar da aka fara jifanta da Kalmar shegiya sosai take da bukatar Jin komai daga iyayenta, haka ta kwana cikin damuwa.Tun daga wannan ranar Kuma muhseena ta rasa walwalarta, hatta magana bata iya yi da kowa agidan gaba daya ta koma shuru, sai dai kallo daya zaka yi Mata Ka tabbatar da tana cikin matsanancin hali na damuwa.wanda hakan itama Hajara yasa ta Kara fadawa cikin tashin hankali domin idan akwai abinda ta tsana to bai wuce ràshin kwanciyar yarta ba, gaba daya ta rasa yadda zata bulloma al'amarin.

Shima can Kabir damuwarsa ta kasa boyuwa gaba daya nema yake ya fita hayyacinsa.

Hakan yasa Alh Musa a dole ya yarda da bukatarsa na zuwa Durmi domin tattaunawa da malllam Hamza wanzami agame da maganarsa da muhseena.

Tare da Kabir din suka tafi Durmi a Wata safiyar ranar alhamis,Kabir dinne ke Jan motar har Durmi.

Sosai mallam Hamza wanzami da Hafsatu suka jidadin zuwan Alh Musa.

Sai da su Ka ci suka koshi amma banda Kabir Wanda ko ruwa bai sha ba sannan Àlh Musa ya dubi mallam Hamza wanzami yace " mallam wajenka nazo" mallam Hamza ya dube Shi sannan ya dubi Kabir yace " Allah yasa ba maganar yaron nan bace ta shirme". Alh Musa ya nisa yace " itace mallam, Ka dubi yadda yaron nan ya rame ya lalace, ni Kaina da nace Bana cikin maganar domin tabbas in dai da gaske ne yarinyar nan bata da uba to nima ban goyi bayan ya aure ta ba, don haka yasa nazo domin na ji shin bincike ne ya tabbatar da hakan ko kuwa shaci fadan mutane ne Wanda in dai haka ne to auren Kabir da ita baida wata illa".

Mallam Hamza ya gyada Kai yace " Alh , wannan maganar ba shaci fade bane abu ne daya

faru agaban mu babu abinda bamu sani ba agame da hakan babu karya wannan yarinyar shegiya ce bata da uba cikinta Kuma babu bala'i da kalubalen da bai haifar ba ga uwarta".

Kabir ya dago yace " Zan iya aurenta ahaka komai ràshin asalinta Zan iya aurenta.....?" " Da Allah rufa min baki shashasha da bai San ciwon Kansa ba, idan Kai zaka iya aurenta to mu ba zamu iya Zama surukanta ba kaga Ka fita Ido na na maida na rufe".

Alh Musa yace " To idan ko hakane gaskiya nima ban goyi bayan ya aureta ba saboda son ina masa kwadayin Samun zuria ta gari".

Hafsatu ta shigo fahimtar maganar da akeyi ne yasa tayi ma Kabir kallon tsaf tace " ai dama nasha jinin jikina cewar ba zaka hakura da yarinyar nan cikin dadin rai ba tunda na fahimci kamar Baka San ciwon kanka ba, don inda kasan ciwon kanka ba zaka so hada zuria da yarinyar da kowa ke gudu ba tunda Muke a kauyen nan ba'a taba Samun yarinyar da ta fita zakka ta yi abin kunyar da uwarta tayi ba, akanta aka fara yin cikin shege da haifar dan shege a kauyen nan, kowa na neman tsari dasu sai Kai ne zaka ce kaji Ka gani to baka isa ba".

Ga mamakinsu hawaye ne kawai ke fita a idanun Kabir gaba daya ya Kara gigicewa." Don Allah Ku duba lamarin nan ina son muhseena duk wañnan abin da kuke fada ba ita ta aikata ba" mallam Hamza yace " Ah aiko ita ta aikata ba zaka gani ba tunda soyayyar ta ta rufe idanunka".

Alh Musa ya dube Shi cike da tausayawa yace"kayi hakuri Kabir in sha Allah zaka Sami wacce ta fita" ya dube Shi Ido na tsiyayar hawaye yace " babu wacce Zan samu wacce ta fita, ko Kai Ka ganta sau daya zaka gamsu da hankali da tarbiyyar ta Zaka Kuma yarda da ni idan nace maka babu wata kamarta ".

Hafsatu ta yi tsaki tace " Bana son Ka jama kanka damuwar da zaka zo kana wahala domin dai ba zaka aureta ba" mallam Hamza yace " babu Kai babu da ita,idan ma har zuwanka zai Zama damuwa to mun yafe kayi zamanka ma dinga yin waya" ya juya ya dubi Alh Musa yace " Alh abar maganar nan Kada ma akara tayar da ita " ya jinjina Kai yace " shikenan Allah yasa hakan shine yafi Zama alheri".

Haka dai suka Kara kamo hanya zuwa Kano ba tare da Kabir yaje sun gaisa da muhseena ba. Cikin matukar tashin hankalin da ya fi na kullum Kabir yake tuki ganin baya cikin hayyacinsa yasa Alh Musa ya karbi tukin haka zalika har suka kai Kano Kabir baice uffan ba duk da nasihohi da kwanta da hankalin da Alh Musa yake masa .

Muhseena ba ta da labarin zuwan Kabir Durmi , har sai washegari data hadu da abokinsa bayan ta taso makarantar islamiya bayan sun gaisa yake ce Mata nasan dai mutumin duk saurin da yake jiya ya zo kun gaisa ko?

Ta dube Shi cike da neman Karin bayani tace " wake nan?" Yace "Kabir mana" . Gabanta ya Fadi sosai ta dube Shi tace " yazo garin ne?'" yace " lalle na yarda Yana sauri tunda har kema ya kasa zuwa Ku gaisa, nima gilminsa na gani a mota shine na kirashi awaya yace min sauri yake".

Duk surutan da yake yi muhseena bata jinsa riga ta fada wata duniyar, hakan yasa yayi Mata sallama ya tafi .

Jikin bango ta samu ta jingina saboda jiri da ta ji Yana neman ya kwasheta.da sauri kirjinta yake bugawa, babu yadda zaayi ta yarda da cewa sauri ne yasa Kabir kasa zuwa wajenta .Wanda idan ma hakane me zaisa bazai iya gaya Mata yazo garin ba ko dazu sunyi waya amma bai gaya Mata ba .

" Shin me hakan yake nufi? Ta tambayi kanta cikin tashin hankali. Zuciyarta ta bata amsa da

cewa tabbas akwai matsala wacce Kabir be son ya gayá Mata.

Hakika maganar aurensu tana cikin jifa'i. Ta dafe kanta da ya Sara Kada fa fargabanta ta tabbata.

A hankali bakinta yake furta "Allah kasa hasashena ba gaskiya bane Allah Kada kasa na rasa Kabir Shi kadaine ya rage min a matsayin farincikina.

Gaba daya idanunta sun Fara rufewa daker take daga kafarta zuwa gida sai dai duk Wanda ya dubeta zai gamsu da cewa tana cikin matsanancin tashin hankali.

DAGA TASKAR YAR GIDAN IMAM

NIMA MATARSA CE
NA
HABIBA ABUBAKAR IMAM
(YAR GIDAN IMAM)
BABI NA TALATIN DA UKU
****

Sosai muhseena tayi kokarin boye damuwarta alokacin da ta shiga gidan, adalilin bata son mahaifiyarta ta Samu damuwa.

Sai dai duk da haka Hajara sai da ta gane damuwar muhseena. A hankali Hajara ta zauna kusa da ita tana kallonta cike da kauna tace " muhseena me ke faruwa ne naga gaba daya babu walwala atare da ke, ko wani abun ya faru ne a makarantar".

Muhseena ta girgiza Kai tace ' aah Inna babu komai" ta girgiza Kai tace " aah muhseena idan kin boye abinda ke damunki to fuskarki ta bayyana don Allah ki gaya min damuwarki". Idanunta sukayi rau rau alamar Zata yi kuka tace " Inna damuwar Kabir ce ke damuna kawai". Gaban Hajara ya Fadi ta Kara kallonta tace "me ya faru tsakaninki da Kabir din ".

Muhseena tace " Inna Kabir ya zo garin nan jiya amma bai zo guna ba Kuma bai sanar min ya zo ba ko da babu dalilin da ya hana Shi zuwa wajena ai ya kamata ya gayá min cewa ya zo garin, gaba daya tun komawarsa ya canja min sosai yadda yake nacin Kiran wayata ya rage Kuma yadda Muke dadewa muna hira yanzu bai tsayawa da mun gaisa ya ji lafiyata da damuwata sai yayi min sallama".

Hajara tayi jugum gabanta na cigaba da faduwa zuciyarta na cike da adduar Allah yasa ba fargabar su bace zata tabbata.

Muhseena ta cigaba da cewa " haka zalika har zuwa yanzu ya ki yarda yayi min cikakken bayani Akan maganar auren mu" ta waigo ta dubi Hajara Ido cikin Ido tace " Anya kuwa Inna ina da rabon auren mutumin kirki irin Kabir , Anya kuwa mafarki na zai Zama gaske ina ji araina kamar ko yaushe nasaba ta zatayi sanadiyyar rushewar farinciki na da mafarkina".Ta karasa magana hawaye na fita daga idanunta.hajara ta kasa cewa komai sai Kai ta Sadda kasa tana cike da fargaba idan har Kabir bai auri muhseena ba hakika ba muhseena ba hatta su sunyi asarar mutum mai nagarta.

Ta dawo da kallonta ga yarta ta numfasa tace " babu wani hukunci da zamu yi saurin yankewa ba har sai mun ji daga Kabir, ki kwantar da hankalinki idan ya kiraki ki tsaya kuyi magana sosai". Tana gama fadin haka ta tashi ta fita daga dakin saboda bata son karama muhseena damuwa ta hanyar fadada ta ta damuwar.

Muhseena ta koma ta kwantar da kanta Akan katifa jikinta ya Fara daukar zafi.

****

Ranar da mujaheeda ta koma office, aranar Sam Alh jibrin ya kasa boye bacin ransa domin ko tsayawa ya kasa yi yayi Mata bayanin abubuwan da suka gabata a kamfanin bayanta, duk da ta bukaci hakan maimakon hakama office dinsa ya koma ya zauna Yana cike da fushi da bakinciki sai ya Kai gauro ya Kai mari . Dai dai lokacin murtala ya shigo office din shima fuskarsa babu yabo babu fallasa ya lalubi kujera ya zauna Yana kallon Alh jibrin ba tare da yace uffan ba,

Daga bisani Àlh jibrin ya dawo shima ya zauna Yana huro iska damuwa daga bakinsa.

Murtala yace " sai hakuri oga, ni Kaina banyi tsammanin Haj zata dawo office ba,ni Nama rasa abinda take son Samu a aiki a kamfanin nan idan ba dorama Kai wahala ba Kai da dukiyar Ka ai sai Ka koma Ka zauna Ka cigaba da bada umarni". Alh jibrin ya saki tsaki yace " yarinya ce me shegiyar kafiya Kuma nima me kafiyar ce domin yanzu na Fara sai inda karfina ya kare, da kanta zata tattara tabar kamfanin nan, Ka duba kaga irin alherin da muka samu da bata office din yanzu Kuma ta dawo zata sa ni a damuwa da tambaye tambayen banza na ya akayi da kaza ya akayi da kaza'.

Murtala ya Kara sakin tsaki yace " yanzu meye abin yi oga" ya numfasa yace " Kaina ya kulle yanzu banyi tunanin komai ba tukuna, Amma zanyi tunani don bazan bari wani yayi min wasa da arzikina ba" murtala yace " ina fa oga, ni ma ina bayanka".gaba daya haka suka uni a kamfanin cikin damuwa gami da kulle kullen yadda zasu Kara bulloma al'amarin.

Karfe daya saura kwata na ranar lahadi Haj murjanatu tana zaune a falon gidan Haj Nana tana jiran ta Gama shiryawa ta fito. Har Haj murjanatu ta Fara gajiya da Zama sannan Haj Nana ta fito cikin kwalliya ta Riga da zani na atamfar Holland tana fara'a " Ayi hakuri Haj kinsan bazawara da kyale kyale". Haj murjanatu tace " kyale kyale na banza tunda ba bazawari kike nema ba" tayi dariya tace " Raba ni da bazawari mu da aure ai mun sami yanci kinsan dadewa a bautama yanci ne". Haj murjanatu ta Mike tace " uhmm muje kinji Haj". Tare suka jero har wajen motar Haj murjanatu yau ita kadai ta tuko motar ta domin in dai zata yi irin wannan tafiyar ta sirri to bata daukar direba .

Ita ke tuka motar Haj Nana na gefenta, ta dan dubeta kadan tace " yaya wajen mujaheedan ba dai wata matsala ko". Haj murjanatu ta ce " lafiya din kenan tunda ban ji wani abin ba, amma kema kinsan ai shurun bazai dore ba in dai wannan kafaffen yaron ne sai ya Kara kilama yayi abinda yafi Wanda yayi a baya,Shi yasa nake son nayima hanci tufka" Haj Nana tace ' Ai kin ma yi nawa na dauka tun ranar data koma washegari zaki zo muje".

Haj murjanatu tace " wasu uzurori ne kawai suka sha Kaina yasa ban neneki mun tafi ba". Haka dai suka cigaba da hira har suka Kai gidan mallam me guru .

Sunyi sa'a Basu tadda wasu mutane masu yawa ba, domin nan da nan layi ya zo kansu suka shiga.

Bayan sun gama gaisawa ne Haj murjanatu tayi masa bayanin abin da ke tafe dasu.ta Kara da cewa " nasan idan nace araba tsakaninsu yata zata cutu , Kuma Bana bukatar hakan don haka nake son ta mallake mijinta yadda ko da bisa kuskure ba zai taba iya bata Mata rai ba, atakaice dai mallam ina son ya Zama rakumi mujaheeda ta Zama akala sai yadda tayi dashi".

Mallam me guru yayi murmushi yace " wannan ba Wata matsala bace zata mallake Shi " daganan ya janyo carbinsa da sauran tarkacen kayan surkullensa ya bukaci sanin sunan sa ta

gaya masa .ya Jima Yana Dan bincikensa kafin daga bisani ya dago ya dubeta yace " zata mallake Shi, amma ina son ki sani rayuwar aurensu tana cike da kalubale akwai Kuma abubuwa da dama da zasu faru masu Sosa rai Wanda ko da ta mallake Shi hakan bazai hana faruwa ba".

Cikin faduwar gaba Haj murjanatu tayi saurin duban Haj Nana sannan ta dawo da kallonta ga mallam tace " Ai rigakafin damuwar ta tace yasa na ke son ta mallake Shi idan Kuma har mallakar ba zatayi maganin hakan ba ai babu amfanin mallakar". Mallam yace " Tabbas mallakar ba zata Hana duk abinda zai faru ya faru ba,Kuma ita kanta mallakar akwai ranar da zata warware sai dai idan za'a cigaba da sabuntata". Haj murjanatu tace " don Allah mallam wane abubuwa ne marasa dadin zasu faru " ya girgiza Kai yace " bangani ba ,Amma tabbas akwai matsala domin ita kanta matsalar na hangota acan wani gari amma Kuma banga katamaiman abinda zai faru ba ".

Gaban Haj murjanatu ya cigaba da faduwa ta shiga matsananciyar damuwa ta Kasa magana har sai da mallam yace " kina bukatar mallakar?"

Ta dubi Haj Nana Ido cike da neman shawara ta daga Mata Kai alamar eh, ta dawo da kallonta gare Shi tace " eh" yace " to Ku je Ku dawo jibi lokacin na Gama hada komai" tace " toh" ya gyara zamansa yace " zaki taho da dubu dari da hamsin" tace " babu damuwa".daga nan suka tattara suka tafi.

Acikin mota daker Haj murjanatu ke tuka motar Haj Nana ta dubeta tace " ki kwantar da hankalinki Haj babu abinda zai faru in sha Allah".

Ta girgiza Kai tace " Haj auren mujaheeda da Taufiq shine babbar barazanar da nake fuskanta arayuwata, Bani da wani abin so sama da mujaheeda tabbas idan aka jarabceni akanta Zan wahala kwarai, " Haj Nana tace " Dama mafi yawan lokuta anfi jaraftar Ka da abinda kafi so" Haj murjanatu ta numfasa tace " ya zanyi Haj" tace " Kada kisa aranki har ya dameki ba lalle bane abinda mallam ya fada ya tabbata Allah Shi kadai yasan gaibu". Haka Haj Nana ta cigaba da kwantar Mata da hankali Amma harta kaita gida ta aje ta wuce bata Sami nutsuwa ba harta koma gida.

Duk tunaninta bai wuce ya zata bulloma al'amarin Taufiq ba, domin dai tana da yakinin ko matsalar ce shine zai zamo me kirkirota.

Acikin kwanaki biyun nan kafin ta koma wajen Mallam me guru gaba daya damuwa ta nunata don hatta Alh Mustapha labaran ya Lura akwai abinda ke damunta amma Yana tsoron tambayar ta don bai San irin amsar da zata bashi ba.

Ranar da ta koma ta amso maganin Kai tsaye gidan mujaheeda suka wuce ita da Haj nana.sunyi sa'a Taufiq baya gida hakan yasa suka saki jiki.haj murjanatu ta dakko killin magani ta Mika Mata cikin son Karin bayani ta karbi maganin tana jujjuyawa " mummy na meye" ta tambayeta ta dan gyara Zama tace " maganin tsari ne na amso muku ke da Taufiq saboda rayuwar nan ta lalace kana can Baka damu da kowa ba amma an damu da kai, Shi yasa na karbo muku".

Mujaheeda tayi murmushi tace " nagode mummy, to ya zaayi dashi" tace" yauwa kinga wannan a cikin abincinsa Shi kadai zaki sa masa wannan Kuma naki ne hayaki zaki dinga yi dashi duk bayan magriba" ta gyada Kai tace " to shikenan in sha Allah zanyi" Haj Nana tace " Kada dai kiyi wasa dashi ki tabbatar kina yi har ya kare shima ki tabbatar kullum kinsa masa a abinci Kuma Kada ki bari wani yaga sanda zaki zuba don ba zasu gane na meye ba sai kiga

sun yi wata fassara da ban" tace" to shikenan ko Kuma na ba yaya Taufiq nasa kawai ya dinga zubawa da Kansa don Shi baida mantuwa ni ko ina iya mantawa".

A gaggauce Haj murjanatu tace " aah kada ki bashi kadama ki nuna masa ko gaya masa na kawo Miki magani kinsan Maza Basu wani yarda da irin wannan magungunan gargajiya ba" mujaheeda tace " eh Kuma fa hakane mummy".

Haka dai Haj murjanatu ta ninke mujaheeda a bai bai domin tasan matukar ta gaya Mata gaskiya ba zata taba yarda ta amshi maganin ba balle har tayi amfani dashi tasan halin yarta Sarai.

Sun Jima a gidan sosai kafin su tafi.

DAGA TASKAR YAR GIDAN IMAM

NIMA MATARSA CE
NA
HABIBA ABUBAKAR IMAM
(YAR GIDAN IMAM)
BABI NA TALATIN DA HUDU

****

Bayan mujaheeda ta dawo daga rakiyarsu .kujera ta zauna ta dauki kullin magungunan tana Kara kallonsa, a hankali ta numfasa , ita kanta ta na mamakin irin hankalin daya shigeta tun bayan aurenta, domin dai tuni zuciyarta ta shiga gaya Mata duk abinda Haj murjanatu ta fada akan maganin nan ba gaskiya ba ne, ta dan gyara zamanta tana Kara nazarin al'amarin shin har yaushe mahaifiyarta ta Fara damuwa da lamarin Taufiq balle harta Samo masa maganin tsari ?.

Nan da nan zuciyarta ta aminta da cewa lalle wannan magungunan na wani abin ne daban Wanda yake da alaka da son zuciyar mahaifiyarta amma ba maganin tsari bane domin idan shine babu yadda zaayi ta bata umarnin Kada ta nuna masa.

Zahiri ta yarda da mahaifiyarta amma bata yarda da ita ba akan lamarin Taufiq.don haka zuciyarta bata aminta da tayi amfani da maganin ba ahankali ta Mike ta nufi wajen zuba Shara ta juye maganin aciki.

Ta dawo tayi zamanta tana son Taufiq fiye da Tunanin me túnani don haka bata son duk wani abu da zai yi Mata ba don ra'ayinsa ko sonsa ba, duk da bata San maganin menene ba to tasan bazai wuce don Taufiq yayi wani abu ba ne Wanda bai yi niyyar yi ba, ita Kuma bata bukatar hakan.haka mujaheeda ta Karasa sauran ranar cike da tunanin halayen mahaifiyarta Wanda da zata iya canja Mata da tuni ta canja domin ita ayanzu jinta take kamar Wata sabuwar halitta.

Haka zalika tun dawowarta gidan mijinta take kokarin yi masa biyayya tare da kulle duk wata hanya da zasu iya Samun sabani.kuma taga amfanin abinda take yi domin dai sosai Taufiq ke nuna Mata so da kauna tare da gudun bacin ranta.

****

Tabangaren muhseena kuwa ta yi kokarin boye damuwarta ta Kuma daure duk wayar da take da Kabir bata yi masa magana ko tambayar sa dalilin ràshin zuwa gidansu da Kuma ràshin gaya Mata ya zo garin ba. Illa iyaka ta dage da adduar Allah yasa Kabir rabonta ne idan Kuma ba rabonta bane to Allah yasa Mata juriya da danganar rashinta..ita kanta Hajara da mallam Umar cikin damuwa suke fargabarsu Kuma ta dadu Akan ta da, agame da auren Kabir da

muhseena.sai dai basa nuna ma muhseena damuwarsu saboda basa son ta Kara damuwa.Ayayinda Ande Dije ta cigaba da kuntata musu da lafuzanta da ayyukanta, hatta tsakar gida Hajara bata son ta fita saboda kalaman da take jifanta dasu.

Shiko Kabir bai saduda ba duk wani Wanda yake Jin zai iya gayama mahaifinsa ya ji, ya nemi taimakonsa amma Mallam Hamza yaki saurarensu.

Domin bayan Alh Musa Kabir ya tura aminan mahaifinsa , ya tura sarkin wanzamai amma duk mallam Hamza yaki saurarensu karshe ma kiransa yayi ya tabbatar masa da cewa idan har ya Kara turo masa mutane Kan maganar muhseena sai yayi matukar bata masa rai...
Hakan ya Kara jefa Kabir cikin mawuyacin hali.

Haj Salma kuwa shawarar yaje ya Sami muhseena suyi magana ta bashi, tace yaje ya fahimtar da ita halinda ya ke ciki idan harta fahimce Shi zata San bai ci amanarta ba, domin dai duk yadda yake tunanin zafin lamarin ya wuce nan.

A dole Kabir ya dauki shawarar Haj Salma tunda baiga wata mafita ba gaba.

Ranar wata jumaa ya dauki hanyar Durmi.Tun isar sa Durmi mahaifiyarsa Hafsatu ta nemi ta sare domin ganin irin ramar da yayi matukar rama gaba daya idanunsa duk sun fada kallo daya zakayi masa Ka gamsu da cewa Yana cikin wani irin mawuyacin hali.Abinda Kuma ta Kara fuskanta ya karasa Mata tashin hankali da damuwa shine Kabir baya cin abinci domin tunda yazo aka Kai masa abinci babu abinda ya Bude ya ci.yana kwance asaman gadon dakinsa ya na cikin matukar damuwa Hafsatu ta yi sallama ta shigo amma bai ji shigowarta ba har sai da yaji karar bude kwanuka sannan ya dubi wajen .

Hafsatu ke bude kwanukan abincin da aka kawo masa, babu abinda ya ci aciki a hankali ta koma bakin gadon ta zauna tana kallonsa fuskarta cike da damuwa ta Kira sunansa " Kabir".

Ya amsa Yana kokarin tashi ya zauna, ta jinjina Kai tace ' me yasa baka ci abinci ba'. Yace asanyaye ' saboda babu wani abu da yake yi min dadi abaki tsawon wannan lokacin bana iya cin abinci ya tsurga min asalima ni babu abinda yake yi min dadi abaki amatsayin abinci".

Tace " yanzu saboda wannan yarinyar ne kake son Ka kashe kanka Kabir bayan kasan Kaine sanyin idaniyata Kaine abin alfaharina, yanzu soyayya zaka fifita fiye da rayuwarka ".

Ya girgiza Kai yace " mama wannan abu ne da ni Kaina bani da iko da Shi , don da ina da iko da tun ranar da kuka ce na rabu da muhseena da tuni na cire soyayyar ta a raina amma ya zanyi bani da iko, kullum Sonta Kara daduwa yake yi azuciyata ba raguwa ba asalima na rasa ta yadda Zan gaya Mata cewa bazan aureta ba" Hafsatu tace ' Amma sanin kanka ne da ace akwai yuwuwar mu barka Ka aureta to da munyi haka, Amma ta yaya kake ganin zamu amince da ita bayan bata da asali baa San ubanta ba kaima kasan bazai yuwu ba".

Yace " to yanzu gaya min mama ta yaya Zan sanar da ita wannan maganar me nauyi bayan na riga nayi alkawarin aurenta nama iyayenta alkawari " tace " su waye iyayen nata da zaka ji nauyin gaya musu Ka fasa aurenta bayan ga dalilinka nan, alabasshi idan Ka gaya musu dalilin sun karyata to sai su gaya maka gaskiya ". Numfasa yayi kawai ya kasa magana.

Hafsatu ta cigaba da maganganunta da Sam babu abu daya da yake dauka domin yare daya kawai kunnansa zai iya fahimta shine "kaje Ka auri muhseena ".

" Ka tashi Ka ci abinci idan ba haka ba Zan bata maka rai sosai".cewarta cikin fada.yace " Zan ci" tayi masa kallon tsaf tace "Ka tashi Ka ci yanzun nan". Baisan damuwa hakan yasa ya sakko ya bude kwanon abincin ya Fara ci, saida ta tabbatar ya ci sannan ta tashi tabar dakin zuciyarta cike da damuwa da tausayin danta.

Sai bayan sallar isshai sannan Kabir yayima gidansu muhseena tsinke.tunda yaron da ya shigo kiranta yace ta zo inji Kabir taji gabanta na matukar faduwa,ita kuwa Ande Dije Jin wani bakinciki tayi ya cika zuciyarta domin duk a tunaninta wannan dadewar da yayi be zo ba ta dauka ko ya daina zuwa ne maganar ta watse. Hakan yasa harta fito ta fita Ande Dije harara take balla Mata.

Jingine jikin bangon zauren gidan ta tadda Kabir cikin doguwar koriyar riga Kansa ya daura hula.

Saida ta shimfida tabarmar hannunta sannan Kabir ya zauna Yana yi Mata wani irin kallo me cike da kauna da tausayi.

Itama ta zauna a gefen tabarmar tana Kallonsa tana ganin irin ramar da yayi a hankali tace " kayi ciwo ne?" Ya dubeta yace " me kika gani?" Ta gyada Kai tace " Rama na gani da Kuma alamar ràshin nutsuwa da damuwa a tare da Kai" .ya yi kokarin daidaita tunaninsa da nutsuwarsa yace " Bana jindadi ne , shine dalilin daukar lokacina ban zo ba" ta nisa hakika babu ko shakka akwai abinda Kabir yake boye Mata. Tace " to damuwa da ràshin nutsuwar fa na menene". Ta tambaya da murya me cike da damuwa, yace " ke ce dai ke ganin damuwar da ràshin nutsuwar".

Tayi shuru na dan wani lokaci sannan tace "Kabir" ya amsa Yana kallonta tace " don Allah me kake boye min? Meye damuwar? Me yasa Kuma kake boye min bayan kasan sanin nawa shine Samun kwanciyar hankalina da nutsuwata" Kabir yayi saurin yin kasa da kansa adalilin idanunsa da yaji sun Fara Tara kwalla.

Muhseena ta cigaba da magana da murya me cike da ban tausayi da rauni. " Kada Ka damu da koma menene kawai Ka gaya min domin idan tashin hankali ne na Saba idan damuwa ce tunda na tsuru a duniya nake cikinta babu wani abu sabo atare da ni, don haka Kada Ka damu Ka gaya min koma menene" nan ma Kabir ya kasa magana illama dagowa da yayi ya zuba Mata raunannun idanunsa da yake kokarin maida kwallar cikinsu.

Tayi wani bushasshen murmushi tace " kadaina kallona domin ganin idonka cikin nawa zai iya cire min jarumta, Ka sani ayanzu dai babu wata magana da nake son ji wacce zata wanke min damuwa sama da gaskiya daga bakinka".

Duk shuru sukayi ganin Kabir baida niyyar yin magana yasa ta hadiye dukkan fargabarta ta tsaida idanunta akansa sannan tace " iyayenka sun hana Ka aure ni ko" Jin maganar yayi a matukar bazata hakan yasa ya daburce gaba daya ya Kuma rasa amsar da zai bata.

Ta cigaba da cewa " dalilin da yasa kenan kazo garin baka zo gidan mu ba,haka zalika shine dalilin da Ka rage Kirana a waya ko? Kamar yadda ya Zama dalilin damuwarka da ramarka gami da ràshin nutsuwar Ka, Bana son Ka boye min komai domin cigaba da boye min Shi zaisa na Kara fadawa cikin masifar cigaba da sa rai akan abinda bazan taba samu ba".

Ta Kara zuba masa Ido tace " kace wani abu mana kayi min magana na hadaka da girman Allah Ka sanar da ni Gaskiya domin ni ina son agaya min gaskiya komai dacinta fiye da ayi min karya don Samun kwanciyar hankali na".

Kabir yasa gefen hsnnunsa ya share hawayen da ya fara gangaro masa, hakan ya Kara tayar da hankalin muhseena nan da nan itama ta sami kanta da zubar da hawaye tun kafin ya bata amsa ta riga ta Sami amsar tambayarta.

Gaba dayansu kuka suka dinga yi kabir kamar ba namiji ba.sun dauki tsawon lokaci suna

kuka babu me lallashin wani.

Saida sukayi suka gaji sannan Kabir ya Fara magana me cike da tausayi da neman mafita yace " muhseena duk duniya ke ce mace ta farko data mallaki zuciyata ta mallaki soyayyata ina yi Miki son da ni Kaina bansan girma da iyakarsa ba, ina tausayinki ina kwadayin yin rayuwa ta har abada da ke, Bana Jin Kuma daga kanki Zan Kara son wata arayuwa,"

Ya numfasa sannan ya cigaba da cewa " duk abinda kika fada gaskiya ne muhseena mahaifana sun ki yarda da auren mu tun ranar farko da na Fara zuwa musu da maganar suka taka min burki naki gaya Miki ne adilin ina tunanin Zan iya shawo Kan matsalar da Kaina amma zuwa yanzu duk da ban cire rai ba na gane lamarin akwai rikitarwa da ràshin sanin tabbas".

Duk da muhseena tayi zaton Jin haka daga gareshi to fa bai hanata Jin wani mummunan sauyi da matukar tashin hankali ba atare da ita gaba daya ji tayi komai ya tsaya Mata cak kamar wacce bata da laka ajikinta.

Ya cigaba da cewa " Ranar da kika ce nazo ban neme ki ba ranar kawuna na dakko na kawo domin ya ba mahaifana baki amma shima sunki sauraronsa, burinsu kawai shine na fita harkar ki na nemi wata ".

Cikin rawar murya tace " mecece hujjarsu na raba mu?" Saida ya jinjina abinda zai fada sannan yace " Hujjarsu itace wai baki da asali.....?" Tayi saurin daga masa hannu tace " shikenan daman nayi zaton hakan Basu da lefi suna da gaskiya" ya dubeta sosai yace " kina nufin hujjarsu gaskiya ce" ta gyada Kai tace " Bani da amsar tambayarka domin nima kullum amsar nake nema ma Kaina har yanzu Kuma ban samu ba, sai dai tabbas lokacin Samun amsar tawa yayi".

Kabir ya numfasa yace " To yanzu baki da wata shawara da zaki iya bani, domin bana Jin Zan iya jurewa na karbi umarnin mahaifana" ta girgiza Kai tace " babu wata shawara da ta wuce Ka Zama jarumi Ka amshi umarnin iyayenka Kada Ka bijire musu Kabi su a hankali idan Kai Allah ya rubuta min a allon kaddara ta to babu tsumi babu dabara sai Ka aure ni komai runtsi saboda haka mu fauwalama Allah komai shine zaiyi mana maganin matsalar mu".

Ya runtse Ido ya bude yace "ina ma mahaifana zasu gane tsantsar nagartarki nutsuwa da kamalarki hakika da da kansu zasu kore Miki wancan zaton su rokeki ki aureni da kansu, har yanzu birni da kauye banga wacce ta kaiki ba , nasan muhimmanci muhseena ina Kuma sonki matukar so".

Wasu zafafan hawaye suka kwaranyo daga kwarmin idanunta ta kasa magana domin ita kadai tasan masifar da ruhinta yake ciki.

Ta dauka zata Zama jaruma amma ji take kamar ta kusa kasawa.

Kabir yace " Don Allah muhseena ki Goya min baya"

Tayi masa wani bushasshen kallo tace " goyon bayana aika samu abinda ya rage maka shine goyon bayan iyayenka Wanda shine babban abin bukata"

Yayi shuru domin dai yasan abinda kamar wuya amma baya son ya gayá Mata domin irin masifar tashin hankalin da yake gani a kwayar idonta ya girmama don dai muhseena jaruma ce kawai amma irin wannan damuwar data Kada ita.

Ko da suka cigaba da tattaunawa Kabir ya Lura gaba daya muhseena bata cikin hayyacinta hakan yasa yaga ya kamata ya barta ta samu Hutu da natsuwa.

" Zan tafi saboda na barki ki numfasa ga Kaya nan ki shiga dasu". Ta kasa cewa uffan haka

ta bishi da kallo harya tashi shima ya Dade atsaye Yana kallon ta zuciyarsa ta Kara tsinkewa a daddafe ya fice daga zauren gidan.

Muhseena ta yi kasa da kanta domin wasu sabbin hawaye da suka cigaba da yi Mata ambaliya asaman kuncinta. Akalla Kabir yakai minti goma da tafiya kafin muhseena ta iya tashi ta zubama katin katin din ledojin dake aje idanu kafin ta iya dauka suna da matukar nauyi shin meye aciki haka? .

Ledojin na rinjayarta ta shiga gidan. Abin mamaki har yanzu Ande Dije tana zaune inda ta barta.bata ko kalli inda take ba tazo zata wuce. Ande ta saki tsaki tana hararar kayan hannunta tace " wannan yaro ana cutar da Shi,komai nasa akanki yake karewa bayan kunfi kowa sanin cewa ba zai aureki ba amma kun dage dole sai kunci haramun ." Ita dai muhseena ta wuce bata ko Jin me take cewa domin masifar da take ciki yafi wannan.

Ande tace " Allah ya kaimu ranar biya zamu ga yadda zaayi ". Zuwa lokacin muhseena harta shige daki.

Da sauri Hajara ta dago tana dubanta yadda ta aje kayan da karfi ya tabbatar Mata ba lafiya. Tana aje kayan ta wuce ta fada Kan katifarta ta cigaba da wani sabon Kuka me matukar daga hankali.

Nan da nan Hajara ta tashi cikin tsuma da fargaba gami da tashin hankali ta nufota tana tambayarta " meya faru muhseena".

DAGA TASKAR YAR GIDAN IMAM

NIMA MATARSA CE
NA
HABIBA ABUBAKAR IMAM
(YAR GIDAN IMAM)
BABI NA TALATIN DA BIYAR
****

Duk tambayar da Hajara take Mata , muhseena bata tanka Mata ba sai kuka Mai tsanani da take Kara tsinkewa da shi.

Hakan ya Kara matukar tayar da hankalin Hajara, ta zauna akusa da ita gami da janyota jikinta tana lallashi tana cigaba da tambayar ta abinda ke faruwa. Amma saida muhseena ta ci kuka harta ba uku lada sannan ta dubi mahaifiyarta cikin jan idon da har ya Fara kumbura saboda kuka sannan tace " yau Kabir ya zo min da tambayar da na Dade ina yi muku irinta baku bani amsa ba, tambayar da ta rusa komai da ke tsakaninmu". Gaban Hajara ya Fadi ta zuba Mata Ido tace " ki natsu muhseena kiyi min bayanin abinda ke faruwa, ya kukayi da Kabir din ".

Muhseena ta ja doguwar ajiyar zuciya tace " Kabir ya kufce min domin mahaifansa sun tabbatar masa da cewa ba zasu taba bari ya auri shegiya mara uba ba".

Hajara ta saki wata nannauyar ajiyar zuciya tayi kasa da kanta numfashinta ya Fara Mata wahalar fita.

Muhseena takara kafeta da jajayen idanunta da suke cigaba da fitar da zafafan hawaye ta cigaba da cewa " Tun tasowata Inna ake nuna min tsana da kyara duk duniya daga soyayyar ki

Saita Baba na Samu sai soyayyar Kabir" ta muskuta tace " Bani da kawa Bani da aminiya Bani da masoyi saboda kowa na gudun hada rayuwa da ni, Inna menene lefina?".

Ta Kara hadiye wani zazzafan yawu tace " idan har Zan rayu da irin wannan tarin kalubalen akaina ta yaya kuke ganin bazan iya jurar Jin asalina daga gareku ba, bayan nafi kowa sanin sanin ko ni wacece zai wanke min abubuwa da dama dake tattare acikin zuciyata kamar yadda zai sa na Sami nutsuwa da kwanciyar hankali ".

Dai dai lokacin mallam Umar yayi sallama ya shigo dakin , kallo daya yayi musu ya tabbatar akwai matsala don haka ya Matso kusa da muhseena Yana kallonta cike da kauna da kulawa yace " muhseena lafiya? Menene ke faruwa?"

Hajara ce ta bashi amsar tambayarsa " Abinda Muke ta tunani daga mahaifan Kabir ne ya tabbata " yayi Mata kallon tsaf yace " kamar yaya?" Tace " to mahaifansa sun ce Basu yarda ya aureta ba adalilin bakin fentin da akayi mata."

Mallam Umar ya dauke wuta damuwa da tashin hankali suka bayyana karara a fuskarsa.ya kasa cewa uffan har muhseena ta tashi tazo gabansa ta tsuguna guiwa biyu tace cikin rawar murya me cike da tashin hankali tace " don Allah Baba na rokeka Ku sanar da ni gaskiyar lamarin nan ko na Sami hujjar kafawa aduk lokacin da aka zo min da tambaya irin wacce Kabir ya zo min da ita"

Mallam Umar yayi Jim na dan wani lokaci sannan yace " kiyi hakuri ki Bani kwana biyu in sha Allah zaki Sami duk abinda kike so, ayanzu dai ina bukatar haduwa da mahaifin Kabir domin mu tattauna bayan nan duk amsar tambayoyinki zaki samu ". Tace " to shikenan " daganan ta tashi ta dau buta ta fita zuwa bandaki.

Tana fita Mallam Umar ya dawo kusa da matarsa Yana kallonta kamar me neman mafita awajenta. Hajara ta dube Shi tace " kaga irin ranar da akullum nake Jin tsoron zuwanta ko, na gaya maka rike muhseena amatsayin ya da Zama uba agareta bashi zai share ko goge mummunan bakin fentin da take dashi ba kamar yadda mutane ba zasu taba maida Kai mahaifinta ba duk da cancantar da kayi saboda sun riga sun San komai". Ta Kara kallonsa tace " don haka mu daina yaudarar kanmu kawai yarinyar nan mu fito mu gaya Mata gaskiya tun kafin damuwa ta salwantar da ita". Malllam Umar yace " hakane Hajara nima ayau Naga kysutuwar mu gaya Mata gaskiya amma har sai na Sami Zama da mallam Hamza wanzami, don ina fatan mu Sami sulhu " Hajara tace " Allah dai yasa ya fahimceka duk da abin da kamar wuya". Malllam Umar yace " ràshin Kabir agun muhseena ba karamar asara bace domin shine nake da yakinin zai rike ta cikin aminci da kauna da soyayya yaro ne nagartacce Wanda zai iya Zama abin alfaharin duk wani Wanda ya same Shi amatsayin suriki, ina matukar yi Mata sha'awar aurensa". Hajara ta nisa ahankali tace " Allah dai ya kawo mana mafita".

Haka suka cigaba da tattaunawa har muhseena ta dawo daure da alwakarta.kai tsaye ta dau hijabin ta tasa gami da shimfida tabarma ta shiga sallah nafila domin Samun sassauci daga masifar da take ciki.

Hakan yasa Mallam Umar ya fice zuwa dakinsa cikin dimbin tashin hankali.

A dakinma ya rasa abinda ke masa dadi sai dai ya Kai gauro ya Kai mari.hakika Yana matukar tausayin Hajara in da Yana da halin sauya kaddarar ta hakika daya canja.yau gashi muhseena zata sa takalmin da Hajara ta cire tarihi Yana kokarin maimaita Kansa.

Ya koma ya zauna akan Dan karamin gadonsa shin ta ina zai kamo lamarin nan ta yaya zai mallakama muhseena abinda take so.haka yayi ta tunane tunane Wanda suka sa Shi tuna

shekarun baya daya taba tsintar Kansa a irin wannan yanayin da Kabir yake ciki yanzu.

Washegari mallam Umar bai saurari komai ba, yayi ma gidan mallam Hamza wanzami tsinke dai dai karfe goma da rabi na safe ya tura yaro cikin gidan yayi sallama da Shi.

Ba'a dauki wani dogon lokaci ba mallam Hamza wanzami ya fito Yana dube duben son ganin me yin sallama dashi, ganin mallam Umar yasa yayi gaggawar tsinke annurin fuskarsa.

Malam Umar ya Mika masa hannu sukayi musabaha sannan yace " mallam Hamza wajenka nazo ina son muyi wata yar magana". Malllam Hamza ya Kara tamke fuska yace " to ina jinka Allah dai yasa lafiya" ya gyara tsaiwarsa yace ' lafiya lau,illa dai nazo ne akan maganar Yara da suke son junansu". Yace " wane Yara fa Kenan?"

Duk da mallam Umar ya fahimci akwai nau'i na wulakanci acikin maganar mallam Hamza to hakan baisa ya ji haushi ko ya nuna damuwa a fuskarsa ba yace "Yara Dan wajenka Kabir da yar wajena muhseena ". Yayi masa wani irin kallo yace " yar rukonka da dai ba yarka na" mallam Umar yace " koma dai menene, to Akan maganar su nazo" ya shafi gemunsa Yana dubansa yace " to me ya faru kazo ".

Mallam Umar yace " muna da bukatar aurar da ita ne shiyasa nace bari nazo muyi magana, atakaice ma dai na ba Kabir auren muhseena ". Mallam Hamza yayi gaggawar cewa " aah bamu Karba ba , don me zaka zo kace kaba Kabir ita sai kace wata kosai ko dabino, ko an gaya maka muna da bukatar aura ma Kabir ita ne" mallam Umar yace ' haba mallam Hamza me ya kawo wannan maganar daga magana me dadi " yace Yana kokarin kallonsa " wace magana ce me dadi , don anzo ance an ba danka Yar shege shine abin dadi , to ina son Ka saurare ni ba Kabir ba muhseena take ko wa, bashi ba ita na raba tsakaninsu, saboda haka don Allah kabar wannan maganar anan kaje idan ta Sami wani Mijin tayi aurrenta amma ba dai da na ba".

Mallam umar yayi dif haushi fa da takaici suka kama Shi ,yace " Amma ban ta ba tsammanin Jin wannan maganar daga bakinka ba, meye ya kawo maganar yar shege bayan kunsani duk abinda ya Sami mahaifiyar yarinyar nan tsautsayi ne da kaddara Kuma babu Wanda ya wuce Allah ya jarafce Shi" yayi masa kallon tsaf yace " tsautsayi da kaddara ko son abin duniya da kwadayi" yace " haka dai kuke gani tunda ba Kwa yima kowa Uzuri ba Kuma Kwa son ku yima mutane kyakkyawar shaida " mallam Hamza yace ," nifa babu abinda ya dameni kawai dai Kabir dans bazai auri muhseena ba fakat magana ta kare" mallam Umar yace cikin raunanniyar murya" don Allah mallam Ka tsaya Ka fahimceni yaran nan suna son junansu ayi hakuri kusa albarka ayi auren nan " " har abada babu aure tsakanin Kabir da yarinyar da bata da nasaba, kaga mallam Umar don Allah Ka wuce Ka tafi Allah ya kiyaye hanya ". Yana Gama fadin hakan ya juya ya shige gida Yana bambancin fada.

Mallam Umar yayi jugum takaici da mamakin bakin halin mallam Hamza ya kama Shi ya kasa Ciba kafarsa ya bar kofar gidan.

Har Kabir ya fito da sauri daga cikin gidan da alama mallam Hamza ya gayá masa abinda ya faru . Har kasa ya durkusa ya gaishe shi cike da girmamawa, mallam Umar ya amsa shima idanun sa na bayyanar da kaunar Kabir acikinsu.

Mallam Umar ya dago Shi Yana kallonsa yace ' Kabir me yasa Ka boye mana abinda ke faruwa har sai da abu yayi nisan da baza'a iya gyarawa ba". Cikin rawar murya yace " saboda Bana son na muhseena a damuwa duk Kuma yadda zanyi Naga na gyara Nabi Nabi Amma babu wani canji, mahaifana sun riga sun dage dole sai dai na rabu da ita, bayan Kuma zuciyata ita kadai take so"

Cike da tausayi mallam Umar yace " sai dai kayi hakuri Kabir amma a yadda Naga mallam Hamza ya dauki maganar Bana Jin zai sakko ya karbi wannan maganar don yama ki tsayawa ya saurareni".

Kabir ya numfasa yace " ni Baba ko awane yanayi muhseena ta tsinci kanta aciki Zan iya aurenta Bana ko bukatar Jin gaskiyar maganar saboda ni ita nake so". Mallam Umar yace ' nasani , Kabir nasan kana son mujaheeda Shi yasa nake son Ka aureta domin Kai kadaine zaka iya jiyar da ita dadi da farincikin data rasa" yayi kasa da murya yace " don Allah Baba Ka taimakeni" ya dafa kafadarsa yace " Ka Sami nutsuwa Ka kwantar da hankalinka Allah zai kawo mafita" Kabir yace ' gobe Zan bar garin amma har zuwa yanzu babu wata alama da take nuna mahaifina zai sakko daga kujerar nakin da ya hau".

Mallam Umar yace " kaje kayi ta addua" ya juya zai tafi asanyaye Kabir yace " Baba yaya muhseena?" Ya juyo ya dube Shi yace " Kada Ka damu yarinya ce jaruma me tsananin tawakkali don haka komai zai zo Mata da sauki". Daganan ya wuce ya tafi yabar Kabir tsaye cikin matukar damuwa.komai ya Kara kwance masa .

Cikin matukar damuwa mallam Umar ya shiga gida da Ande Dije ya Fara kacibis tana kokarin zuwa turken awakinta, ta dakata tana yi masa kallon tsaf sannan tace " meye duk Kabi Ka fita hayyacinka wani abunne ya faru da Naga gaba daya duk Kabi Ka sukurkuce*. Ya numfasa Yana kallonta yace " gaba daya abubuwanne duk sun cabe Ande " ta Kara dubansa tace " to meya faru" sannu ahankali ya kwashe duk abinda ke faruwa ya gayá Mata ya Kara da cewa " to yanzu ma daga gun mahaifinsa nake gaba daya ya tsayama ya saurareni Kiri Kiri mutumin nan yaki, Shi kawai dansa ba zai auri muhseena ba".

Ta saki tsaki tace " Kai ko kana da abin mamaki yanzu meye lefin mallam Hamza ko Kaine tsakani da Allah zaka yarda danka ya auri mara asali kayi fa adalci don haka ni banga laifinsa ba , Kuma ma ai babu wata asara tunda daga uwar har yar sun ci kudinsa sun ci kayansa babu adadi Allah ma yasa Kada ace su biya" sosai mallam Umar yasan idan ya cigaba da tsayawa yana sauraren Ande Dije babu abinda zai karama Kansa sai damuwa hakan yasa ya wuce zuwa dakin Hajara.

Zaune ya tadda Hajara tana danna ma muhseena tsumma a Saman goshinta . " Meya sameta" ya tambaya a gigice , Hajara ta waiwayo tana dubansa tace " zazzabi ne da ciwon Kai me zafi ya kamata ".

DAGA TASKAR YAR GIDAN IMAM

NIMA MATARSA CE
NA
HABIBA ABUBAKAR IMAM
(YAR GIDAN IMAM)
BABI NA TALATIN DA SHIDA
****

Malllam Umar ya Matso Yana kallon yadda muhseena duk ta fita hayyacinta, yace " kin bata magani" ta amsa " eh na bàta amma dai har yanzu bai lafa Mata ba ko ido daker take budewa.

Ya durkusa agaban ta Yana cewa " sannu, don Allah ki sassauta ma kanki damuwa, Kada kizo ki fada wani halin daban". Hajara tace cike da damuwa ' abinda nake ta faman gaya Mata

Kenan, duk bawa baya kaucema kaddarar sa Kuma rayuwa cike take da kalubale dole mutum ya koyi juriya da jarumta".

Muhseena ta waiwayo ahankali idonta cike taf da hawaye tace " yanzu Inna ni har akwai wata juriya da jarumta Wanda ban nuna ba arayuwata, duk tsawon wannan lokacin na yarda da kaddarata amma kaddara daya ce na kasa dauka domin nayi Imani bata cikin Jerin kaddarorina hakanne ma yasa na kasa yarda da ita". Mallam Umar yace " wace iri kaddara ce " tace " kaddara kin gaya min ainihin gaskiyar lamarin" . Gaba dayansu suka dubi juna gami da numfasawa sannan mallam Umar yace ' muhseena ki kwantar da hankalinki na gaya Miki nayi miki alkawarin innarki zata gaya Miki komai".

Bata yi magana ba ya cigaba da cewa " sai dai ko kadan Bana son ki zargi mahaifiyarki ko ki dasama kanki tsanarta ko ki kasa yarda da abinda ta gaya Miki, domin tana da gaskiya babu karya acikin maganganunta".

Muhseena ta numfasa gami da Kara rufe idanunta tace "Bani da hujjar kalubalentar mahaifiyata akan ko me ta aikata, kawai ni burina shine na sanin ko wacece ni". Hajara ta goge dan guntun hawayenta tace "Zan gaya Miki , Allah dai ya baki lafiya". Bata Kara cewa uffan ba adalilin sarawar da kanta yake yi kamar zai Fado kasa, tunda take bata taba yin irin wannan ciwon ba.

Kabir kuwa Yana can ya kara fadawa cikin mawuyacin yanayi, guiwa biyu ya je ya zube ma mahaifinsa Yana rokon ya amince masa ya auri muhseena. Mallam Hamza yayi masa kallon tsaf yace " Kabir me yasa Ka dage dole saika auri muhseena" yayi sanyi da murya yace " saboda tana da mutunci kima da daraja , tunda nake ban taba ganin mace irin ta ba me matukar kamun Kai da rike talauci ba tare da kauce hanya ko gurbata tarbiyyar ba, sannan saboda ina matukar Sonta Baba tunda nake ban taba son wata ya ba sai ita, "

Mallam Hamza ya gyara zamansa akan buzunsa yace "yanzu kana tsammanin akan farincikinka mu za muyi wasa da mutuncin mu da kimarmu (ya girgiza Kai) aah bazai yuwu ba don haka Ka daina wahalar da kanka ko daurama kanka damuwa ta banza domin yin hakan bazai iya canja komai ba".

Kabir ya dago da jajayen idanunsa ya dubi mahaifinsa yace " shikenan Baba Zan rabu da ita ,Amma har abada bazan taba son wata irin yadda nake son muhseena ba Kuma har na mutu bazan fita daga cikin kuncin bakincikin ràshin ta ba ".

Malllam Hamza yace " duk abinda kaji mutum yace bazai iya ba to baisa Kansa bane don haka zaka iya cireta aranka matukar Ka so hakan, maganar Kuma ba zaka taba son wata kamarta ba wannan maganar banza ce lokaci ne kawai zai tabbatar da hakan".

Daganan mallam Hamza ya tashi ya fice ya barshi a tsugune cikin matukar damuwa mara musaltuwa. Hafsatu ta karaso kusa da Shi tana kallonsa zuciyarta na matukar kwadaita Mata ta ji tausayinsa amma bata son ta nuna masa ta Kira sunansa " Kabir" ya dago Kai ya dubeta .

Zuciyarta ta sare tausayinsa ya Kara kama ta tace " don Allah kayi hakuri Ka sama kanka juriya da dangana Ka sadaukar da soyayyar Ka saboda farincikin mu, da Kuma Samun zuria ta gari daga gareka,ina son Ka sani aurenka da muhseena babu abinda zai janyo mana sai

kaskanci don haka matukar kana son kwanciyar hankalin mu to ya Zama dole Ka rabu da ita".

Kabir ya girgiza Kai gami da numfasawa ji yake alokacin duk duniya da wuya asamu Wanda ya Kai Shi shiga damuwa da tashin hankali. Ya ce" shikenan babu komai Allah yasa hakan shine yafi Zama alheri agareni da ita kanta muhseena, Amma.....?" Hafsatu tayi saurin dakatar dashi tace " Kada Ka Kara komai akan wannan mubar maganar,".

Ido kawai ya bita da Shi ya kasa magana harta wuce.ya Mike ahankali ya shige dakinsa ya fada Kan gado gaba daya zaman garin ya ishe shi kamar Yana Kan wuta haka yake ji kwata kwata baya Jin zai iya Kara ko da kwana daya agarin.

Ya tashi kamar Wanda aka tsungula ya shiga hada kayansa ,cikin kankanin lokaci ya Gama Shirin tafiya ya so kwarai ya daure ya tafi ba tare daya Kara ganin muhseena ba amma zuciyarsa taki aminta da hakan , sosai yake kwadayin Kara ganin muhseena domin baisan ko shine ganin da zaiyi Mata na karshe ba arayuwarsa domin Shi Kansa yasan ya Zama dole ya nisanceta domin ta hakane kadai zai iya sama Kansa dangana da hakurin rashinta.

Yayi matukar kokarin boye dukkan damuwarsa ya fito ya nufi gidansu muhseena hakanan gabansa yake ta yawaita faduwa har zuwa lokacin daya isa kofar gidansu. Tsaye yake Yana adduar Samun yaron da zai aika. Dai dai lokacin mallam Umar ya fito bayansa Hajara ce rike da muhseena cikin matukar galabaita take.

Nan da nan Kabir ya gigice ya nufo su da sauri Yana tambayar abinda ya sameta.mallam Umar ya dube Shi yace " zazzabi ne ya kamata to tasha magani amma babu wani cigaba shine Naga gara mu tafi asibiti adubata" Kabir ya Matso Yana kallon muhseena yayi mamakin yadda ta koma acikin kwana daya kacal duk ta rame ta fita hayyacinta,cikin kidima ya gaida Hajara Ayayinda ya dubi mallam Umar yace " Bari na je gida na dakko mota ta sai mu tafi asibitin" mallam Umar ya girgiza Kai yace " aah Kada kadamu zamu karasa a mashin " yace "aah don Allah Baba kayi hakuri naje na dakko mota" Bai tsaya sauraran maganar da malllam Umar yake yi ba ya juya da sauri ya tafi.

Hajara ta dubi mallam Umar cike da damuwa tace " mallam mu tafi kawai" mallam Umar yace Yana kallonta " Hajara Kabir baida laifi Akan duk abinda ke faruwa, kaddarar muhseena ce tazo da haka, don haka a irin kaunar da Kabir ya nunama muhseena rabuwa lafiya cikin aminci shine abinda ya fi cancanta". Hajara ta Kara rungume muhseena tace " ko daya ban zargi Kabir da komai ba kawai dai kokari nake Naga na nisanta su domin su samu su karbi kaddarar data hau kansu". Ya gyada Kai yace " maida ta cikin gida , mu Jira ya dawo" ta amsa da toh lokaci daya ta juya da muhseena cikin gidan. Malllam Umar ya cigaba da tsaiwar jiran dawowar Kabir.

Ba' a dauki lokaci ba Kabir ya dawo da motarsa .cikin kankanin lokaci suka dunguma zuwa asibitin garin durmi.zuciyar Kabir tana kuna Jin ciwon muhseena yake tamkar acikin jikinsa ransa kwata kwata babu dadi.

Basu tadda layi sosai ba hakan yasa nan da nan likita ya gama dubata.

Kabir ya tsare likita da Ido yace " likita menene matsalar meke damunta?", Likita ya dago daga rubutun da yake yace " akwai zazzabin typhoid ajikinta, sannan tunani da damuwa sunyi Mata yawa kuma zasu iya haifar Mata da gagarumar matsala matukar baa shawo Kan matsalar ba " ya waiwaya ya dubi mallam Umar sosai yace " me take bukata ?, Tana da wata matsala ne da take Haddasa Mata irin wannan damuwar me tsanani da kwakwalwarta take neman ta gagara dauka Wanda shine dalilin ciwon kan da take me tsanani" , mallam Umar ya dubi Hajara sannan ya dawo da kallonsa ga likita Bai iya bashi amsar tambayarsa ba sai wata tambayar da ya maida masa yace " yanzu likita menene abin yi?" . Shi dai Kabir ya jingina jikin bango ya Kara fadawa cikin tashin hankali domin baya raba daya biyu shine dalilin fadawar muhseena halin da take ciki ayanzu.

Likita yace " toh yanzu dai Zan rubuta Mata mugungunan da zata yi amfani dasu na wani lokaci kafin muga abinda Allah zaiyi, amma Zan bada shawarar a kwantar Mata da hankali ko yaya ne asamu saukin tunani da damuwar da take yi". Malllam Umar yace " in sha Allah zamuyi iya bakin kokarin mu". Daganan ya Mika musu takardar maganin Kabir yayi sauri ya amsa .

Hajara dai tun zuwansu asibitin take sharar kwalla, domin abubuwa da dama suna dawo Mata kamar yadda yafaru da ita yau gashi komai ana maimaita Shi akan yarta wacce bata da laifin komai.tasan zafin abin don haka tasan yadda muhseena take ji acikin zuciyarta.

Kabir bai mayar dasu gida ba sai da ya sayi duk magungunan da aka rubuta sannan ya biya dan shsgon da ake ji dashi agarin yayi Mata sayayya masu yawa tun daga kan kayan tea da sauran tarkacen kayan bukatu. Ita dai muhseena Ido kawai take binshi dashi tana Jin wani irin zafi acikin zuciyarta.

Har cikin gidan suka shiga tare da Kabir yau itace rana ta farko daya shiga dakin Hajara, zuciyarsa ta sare tausayi ya Kara kama Shi da yaga yanayin dakin da suke rayuwa aciki ko ledar tsakar daki babu sai katifu kawai akasan daki babu gado.

Malllam Umar da Hajara duk dakin suka fice suka bar Kabir din da muhseena, Kabir ya durkusa kusa da katifar da take kwance akai Yana yi Mata wani irin kallo Mai cike da kauna yace " muhseena duk abinda kike ji acikin zuciyarki Nima haka nake ji, na rantse Miki bana jindadin komai a duniyar nan zuciyata kamar ta fashe nake jinta," ya cigaba da kallonta sannan yace" don Allah don son Annabi muhseena ki yafe min ki min afuwa domin na kasa cika alkawarin dana daukar ma Kaina na rayuwa tare da ke da Kuma tabbatar da inganta rayuwarki, ina rokonki kiyi hakuri ki cire duk wata damuwa ki sani komai na Allah ne Kuma dukkan tsanani Yana tare da sauki".

A hankali cikin jigata muhseena ta danyi wani bushasshen murmushi tace" Ka daina Bani hakuri domin babu abinda kayi min , ina Kuma tabbatar maka da cewa tarihin rayuwata ba zai taba cika ba ba tare dana saka ba , Kai mutum ne nagari Wanda ya nuna min kauna alokacin da

kowa ya hanani damar ma sanin ana so a duniya, Kaine mutum na farko da Baka kyamace ni ba, har Kuma bayan sanin nasaba ta baisa Ka kyanaceni KO Ka tsaneni ba , bayan irin hidimar da kayi da ni don haka babu abinda zakayi min ya Zama laifi".

A hankali Kabir ya goge siraran hawayen dake fita a idonsa yace " ba haka na so karshen ya kasance ba, amma babu yadda Muka iya domin ba bu jayayya tsakaninmu da iyayenmu, Amma ki sani Zan cigaba da sonki har abada ko da ban sameki ba, ba Kuma Zan taba juya bayana agareki ba, Zan cigaba da taimakama rayuwarki, har zuwa lokacin da Allah zai baki Mijin.....?
Tayi saurin dubansa cikin rawar murya tace " yanzu Kabir shikenan dai rabuwa za muyi?" Yayi kasa da Kansa ya kasa magana, ta numfasa tace " duk acikin kaddarorina wannan itace kaddara me girma da daukarta zai yi min wahala" Kabir yace " kiyi hakuri, har yanzu ban cire ran Zan aureki ba, muyi ta addua, amma dai yanzu kwanciyar hankalin ki nake so ki cire tunani aranki ki Sami nutsuwa ki sani duk abinda Allah yayi ma bawa to soyayya ce acikin rahamarsa, don haka Kada muyi fushi da yin Allah".

Ta gyada Kai tace " Zan daure Allah ya bamu ikon cin wannan jarabawar". Haka ya zauna yayi ta kwantar Mata da hankali da Kansa ya bata duk magungunan ta Tasha . Kasancewar ta Dade bata Sami bacci ba cikin magungunan da Tasha akwai na bacci aciki hakan ne yasa cikin kankanin lokaci ta samu bacci, ko bayan da tayi baccin haka ya tsaya akanta yayi ta kallon kyakkyawan fuskarta.

Mallam Umar ya leko dakin yace " Kabiru ni Zan fita" da sauri ya taho Yana fadin " ai tama samu bacci Baba, Zan tafi ne Nima". Hajara na zaune Kan kujera yar tsuguno a tsakar gidan Ande Dije na daki ko lekowa batayi ba tun dawowarsu asibitin. Kabir ya tsuguna agabanta cikin nutsuwa yace " Inna don Allah ayi hakuri da komai, Kuma ko ban Sami muhseena amatsayin Mata ba to har abada bazan taba yanke zumuncin da ke tsakaninmu ba Kuma ina nan amatsayin danku Wanda zaku iya tambayar duk abinda kuke so daga gareni". Hajara tayi dan murmushi tace " babu komai Kabir , nagode da Dukkan karamcinka sai dai kafin Ka tafi ina son na cire maka dukkan shakku dake zuciyarka Akan muhseena da ni Kaina , ina son na tabbatar maka da cewa duk abinda ake fada gaskiya ne Amma rabin gaskiyar kawai aka Sani saboda haka Zan gaya Maka komai Wanda ita kanta muhseenan ban gaya Mata ba bata San komai ba akai don haka lokaci yayi da Zan gaya muku komai " ta Kara dubansa tace " Amma Zan so na gaya maka tare da muhseena domin damuwar da take ciki tana da alaka da hakan".

Kabir ya nisa yace " Nagode Inna, da maida ni da da kikayi ,Kuma ina son ki sani ban taba dasama Kaina yarda da maganar da aka Fada ba, domin nayi Imani ko da ya tabbata bazai Zama da laifinki aciki ba".

Malllam Umar yace " najidadi da Ka fahimci haka Kabir,". Hajara ta dube Shi tace " kaje Ka dawo anjima idan ta tashi zanyi magana daku Duka" yace " toh". Daganan ya tashi yayi sallama dasu ya tafi zuciyarsa cike da damuwa gami da tausayi.

Alwashin tafiyar da ya ci yau ya fasa domin ji yayi Yana cike da son Jin labarin Hajara,

zuciyarsa ta Kara cika da tausayinsu matuka.Tunda ya koma gidan baida wani sukuni ,ya kasa tsaye ya kasa kwance ya kosa kwarai magriba ta rufa ya koma gidan mallam Umar. A daddafe ya idar da sallar magriba bai tsaya ya ci komai ba duk da rabonsa da abinci ya manta , ya tattara ya taho gidan domin bayan ma son Jin labarin Hajara ya na matukar son ganin muhseena Yana son yaga yadda jikinta ya kasance.

Kai tsaye Yana zuwa ya shige gidan da Ande Dije ya Fara yin kacibis kallon tsaf tayi masa ta ce a hankali " Kai dai Ka hada kanka da wahala ba nace Allah ya hadaka da wahala ba". Yi yayi kamar baiji abinda tace ba, cikin girmamawa ya gaisheta ta dai amsa babu yabo babu fallasa, daganan ya wuce dakin Hajara ba tare da ya damu da kallon da Ande Dije keyi masa ba. Cikin sallama ya shiga dakin, Hajara ta amsa tana bashi umarnin ya shigo.ya dage labule ya shigo idanunsa na shawagi acikin dakin cike da son ganin muhseena, can Kan katifa ya hangota ta jingina jikin filon fuskarta da alamun sauki ba kamar dazu ba. Ya zube gaban Hajara ya gaisheta ta amsa cike da kulawa, sannan ya matsa kusa da katifar muhseena Yana kallonta " yaya jikin naki" ta amsa ahankali " da sauki" ya cigaba da kallonta yace " kin sha duk magungunanki?" Ta gyada Kai tace " nasha".

Hajara ta dube Shi ta dubi muhseena tace " ina son kuyi hakuri kusa ma kanku dangana idan Allah yasa ba zaku Zama ma'aurata ba to wannan daga cikin kaddararku take don haka kuyi addua Ku Kuma fauwalama Allah komai" tadan gyara zamanta tace " Amma kamar yadda na gaya maka ne kana da matsayi aguna amatsayin da nake kallomka hakan yasa dole Zan yaye duk wani sirri na gaya muku gaskiyar komai". Muhseena ta yunkuro cike da farinciki tace " Alhamdulillah Inna wannan shine burina Zan Sami saukin radadin zuciyata matukar naji abinda na Dade ina kwadayin ji". Ta gyada Kai tace " yau zaki fita daga dukkan shakku da tunani (ta dubi Kabir) Kai Kuma Zan warware maka komai yadda ko kabar muhseena ba zaka tafi da zargi ko bakincikin komai ba, sai dai ina son kasa aranka wannan labari da Zan Baka Bai Isa ya sauko da mahaifanka daga kujerar nakin da suka hau ba Akan auranka da muhseena "

Kabir ya gyada Kansa yace " babu komai Inna ,Allah ya zaba mana abinda yafi alheri", tace " Amin Kabir Allah Kuma yayi muku albarka duka "

Sunyi shuru Duka na Dan wani lokaci kafin Hajara ta numfasa gami da yin kasa da kanta ta Fara magana cikin yanayi na damuwa da gazawa.

TO BE CONTINUE

DAGA TASKAR YAR GIDAN IMAM.

NIMA MATARSA CE

NA

HABIBA ABUBAKAR IMAM

(YAR GIDAN IMAM)

BABI NA TALATIN DA BAKWAI

****

Durmi kauye ne me ruko da al'ada da kaucema duk wani abu da zai zamanto sanadiyyar zubewar mutuncinsu. Hakan yasa suke taka tsan tsan da rayuwar yayansu gami da killacesu , duk da kasancewar talauci da ràshin wadataccen ilimi agarin to bai hana iyaye tsayawa akan tarbiyyar yayansu ba. Musamman da garin kowa ya San kowa domin a wancan lokacin

mutanen garin babu yawa.
Mahaifin Hajara mallam sule Yana daya daga cikin irin wadannan mutanen da suke kafe da idanunsu akan yayansu tare da kokarin tabbatar da tarbiyya akansu.

Duk da Hajara itace kadai Allah ya bar masa acikin Jerin yayan da matarsa daya tilo zainabu ta Haifa masa guda biyar, duk sun rasu ita kadaice tayi saura hakan yasa ya dauki kauna da so na duniya ya Dora Mata, talaka ne sosai domin bai aje ba baiba wani ajiya ba duk da gidansa babu yawa to daker ake Samun abinda zaaci .

Noma yake yi Wanda kafin wata shekarar ta zagayo ya Gama kakkabar da komai babu dai tayi kaka gida acikin rayuwarsa hatta gidan da suke ciki ba nashi bane haya yake yi, tunda shima baida wasu yan' uwa Kuma babu abinda ya mallaka daga gadon mahaifinsa tunda shima Bai da Shi.

Rayuwar Hajara ta cigaba ba yabo ba fallasa babu karatun boko sai dai makarantar allo Wanda itace kadai ta taimaketa arayuwa.zainabu kuwa babu wata Sana'a sai dai dan aikatau shima din Saita samu, hakan yasa ake zaune babu Mai taimakon wani. Rana tsaka Allah ya dorama mallam sule lalurar ciwon kafa daji ya kama masa kafa tun Yana jurewa ya na dauriya ya dingisa ya fita yadanyi buga bugarsa har abu ya Fara fassakara domin yadda kafar ta kumbura tayi suntum ga azabar ciwo mara musaltuwa dole ya tsuguna agida ana maganin gargajiya shima din sai Allah yasa an samu Wanda zai iya hakurin bada bashi . Sannu ahankali itama daya kafar ta kama ruwa mai wàri na fita daga jikinsu. Awannan lokaci babu wani tashin hankalin da Hajara da mahaifiyarta suka taba shiga sama da wannan arayuwarsu, ciwo ya samu da talauci haka zainabu take fita aikatau ita da Hajara domin Samun abinda zaa ci da Wanda zaayi magani.

Abin takaici Kuma babu mai taimaka musu domin kowa ta Kansa yake Masu Dan zuwa gaida Shi ne suke dan bada kudin da bazai isa ayi komai ba. Rayuwa fa tayi ma gidan mallam sule zafi dole tasa yar gonar tasa ta rufin asiri ya daga ya sayar domin yin magani. Alokacin ne aka basu shawarar zuwa babban asibiti a jigawa domin a duba Shi.
Aminin malllam sule mallam kallah shine yayi masa rakiya zuwa general hospital na jigawa. Gwajin farko aka gano cancer ce ta kamashi Kuma harta Fara yaduwa ajikinsa . Take suka bashi gado aka cigaba da gwaje gwaje . Mallam kallah shine ya Komama zainabu da labarin an kwantar dashi don haka itace ya kamata ta je ta zauna dashi.

Hakan yasa sauran Yan kudin gonar ta tattara washegari Mallam kallah yayi musu jagora da zainabu da Hajara zuwa jigawa. Aranar Shi ya dawo gida su Kuma suka cigaba da zaman jinyar Mallam sule.kullum cikin bukatar kudin magani ake ga abinda zasu ci kullum haka suke Zama da yunwa ko Kuma idan masu jinya sun rage abinci su Basu su ci. Zaman asibiti dai Bana kare ba domin duk kudin hannunsu sun gama kakkabewa, hakan yasa zainabu take tura Hajara wajen asibiti tana Dan nema musu taimako.

Wata Mata da take jinyar danta Haj lami idonta nakan su zainabu sosai take tausaya musu

domin ta fahimci suna cikin tsananin talauci , sau tari duk abincin da aka kawo Mata tana duba ta Basu tana Kuma Kula kwarai da hankali da nutsuwar irinta Hajara .cikin kankanin lokaci Haj lami ta Saba da zainabu ita kanta zainabun bata kyashin gaya Mata halin kuncin da suke ciki Basu da mataimaki sai Allah. Wata ranar laraba ne Haj lami ta dubi zainabu tace " gaskiya Mijin ki Yana jinya Mai wahala ,ba zaku iya da asibitin nan ba" zainabu ta numfasa tace " gamu gatan kowa Allah, ai Haj idan ba Dama tattarawa zamuyi mu koma gida kawai" Haj lami tace " to ammafa ciwon nan yayi yawa ajikinsa bazai yuwu ace wai Ku koma gida ahaka ba" tace " to ya zamuyi babu ai bata gwaninta" Haj lami ta gyara zamanta tace " da babu damuwa da nayi miki wani taimako" zainabu tace " ta yaya zaa damu da taimako ai abinda Muke nema Kenan don Allah hajiya ina jinki". Haj lami tace " tunda yarinyarki tana da nutsuwa akwai wata Haj me kudi ce sosai mijinta ya rasu ya barta da ya daya gashi baa Dade ba ta Kara aure shine take ta neman me aiki , shine Naga ko Zan Kai Mata itane ta Fara Mata aiki kafin asallameku kinga anan zata samu abinda zaku ci da Kuma kudin aikinta don Zan CE kullum ne zaa dinga bata albashinta basai wata ba kinga kafin asallame Ku akalla kun Sami abubuwan da zaku rage wahala da wannan fita neman taimakon da take yi awaje ai ina ganin gara wannan din".

Zainabu ta dubi Haj lami cike da godiya da jindadi tace " aiko idan kika min haka kin Gama min komai Kuma kin taimakeni ba Kuma Zan taba mantawa ba ". Haj lami tace " to shikenan tunda kin amince Bari nayi Mata magana". Haj lami ta dakko waya ta danna ta Kira Haj ta Dade tana yi Mata bayani kafin ta aje wayar sannan ta dubi zainabu tace " kinga ta amince , tace anjima idan ta zo gaida yarona zata ganta Saita tafi da ita" zainabu ta jinjina Kai tace " Alhamdulillah nagode Haj Allah ya saka da alheri".

suna cikin tattaunawa Hajara ta shigo, Zainabu ta dubeta tace " kin Dan Samo wani abun ko?" Ta girgiza Kai tace " babu abinda na Samo Inna magaji ne dai yasa na dawo ciki" zainabu ta ja hannunta ta zaunar da ita , cikin nutsuwa ta shiga Mata bayanin komai , sannan Hajara ta numfasa tace " babu komai Inna in dai hakan zai saku farinciki babu komai zanje nayi aikin" zainabu tace " Allah yayi Miki albarka kinji Hajara", ita kanta Haj lami ta gamsu da hankalin Hajara Shi yasa take son ta taimakesu.

Bayan magriba hajiyar ta iso da ita da mijinta, sun duba jikin Dan Haj lami da Kuma Mallam sule .hajiyar ta Dade tana kallon Hajara sosai irin Mai aikin da take so kenan me jini ajika da zata iya ko wane irin aiki ba tare da Ganda ba .shima mijin nata idonsa nakan Hajara. Haj lami ta Kara gabatar da zainabu da Kuma dalilin son yarta tayi aiki agunsu .Haj ta dubi me jinyar tace " Allah ya bashi lafiya ba bu komai ko yaushe aka sallamesu zasu iya tafiya da yarsu idan Kuma zasu barta ta cigaba da aikin to duk babu damuwa zamu fi bukatar hakan ma". Daga bisani ta dauki kudi masu yawa taba zainabu .

Mallam sule na kallo ba don ransa ya so ba aka tafi da Hajara.sai bayan tafiyarsu ne ya kasa hakuri ya dubi zainabu yace " yanzu da kika bada yarinyar nan zainabu kinsan matar nan ne kinsan duk inda take ?Baki San komai ba akansu Amma kin bada yarki an tafi da ita" zainabu tace " naji azuciyata Haj lami ba zata cutar da ni ba domin bata da kamar haka " yace " Shi mugu Dama Yana da kama ne? Ki daiyi hattara Allah Kuma ya tsare mana Hajara ". Shigowar

Haj lami Kenan ta tsinkayi maganar ta karaso tana cewa" Kada Ku damu Hajara tana kyakkyawan hannu babu abinda zai sameta in sha Allah babu matsala " zainabu ta dube Shi tace " kaji ko Mallam babu komai fa" ya jinjina Kai yace "Allah yasa ".

Duk da haka Mallam sule Bai Sami kwanciyar hankali ba sai bayan kwana biyu da direba ya kawo Hajara asibitin ta duba Shi. Nan da nan har tayi Kyan gani tana sanye da sabuwar doguwar Riga harda abinci ta kawo musu Kula biyu zainabu ta kasa dauke kallonta ga Hajara Sbd yadda tayi kyau acikin kwanaki biyu kawai harta canja.alokacin ko da Hajara ta Fara Basu labarin kirkin hajiyar zainabu Baki ta saki tace" Dama akwai irin wadannan mutanen a birni ," Haj lami tayi dariya tace " kwarai kuwa harma Wanda ya fita , ai na gaya muku Baku da matsala da Haj " Hajara tace " gaskiya ne Inna gaskiya najidadin kwanakin da mukayi tare lafiya lau ga yarta harta Saba Dani ko yanzu da kika Muka rabu."

Hankalin malllam sule da na zainabu yayi matukar kwanciya .sai yamma sannan direba ya tafi da Hajara bayan taba zainabu kudin kwanaki biyu na aikinta da aka bata. Hakan ko bakaramin farinciki ya dasa a zuciyarsu ba.

Akalla Hajara ta Sami sati biyu agidan aikinta, Kuma ta Zama Yar gida kullum tana tare da yar Haj me kusan shekaru hudu bacci ne kadai ke rabasu gashi Haj na matukar jindadin aikinta hakan yasa ta sakar Mata komai har yarta domin Hajara ke yi Mata komai. Daga bisani ma hatta bacci tare da Hajara suke yi. A gefe daya Kuma duk bayan kwana biyu Hajara tana zuwa asibiti ta Basu kudin aikinta.an sallami su Haj lami tuni Amma itama jefi jefi tana zuwa ta dubasu.

Hajara tana jindadin zaman gidan aikinta idan Ka dauke wasu acikin halayyar maigidàn da bata so ,Yana yawan sa Mata Ido kallo duk Wanda inda tabi da son ya sata aiki Yana Kure Mata da ido.domin dai Hajara shekara ra goma Sha shida ta shiga ko watanni bakwai baya akwai baikon sani akanta sa rana kawai ayanzu ya rage, Hajara tana da kyau da cikar diri kwarai da gaske ina ganin shine yake Jan hankalin Alh Amma Hajara bata taba zaton akwai wata boyayyiyar manufa azuciyarsa ba akanta.

Wata daya da sati uku da Fara aikin Hajara aka sallami Mallam sule da sharadin dawowa asibit bayan wata uku sun Kuma bashi magungunan na watanni ukun Wanda idan ya dawo zasu sa ranar da zasuyi masa aiki .bayan sallamar tashi da kanta hajiya ta bada mota aka dakko su zuwa gidanta . Su zainabu sun gigita da ganin irin arzikin gidan Haj gida kamar a aljanna cewar zainabu Shi ko Mallam sule tasbihi kawai yake yi ga ubangijin talikai .dakin baki aka saukesu akalla saida sukayi kwanaki uku sannan Haj ta cika musu mota da Kayan abinci da sutura Wanda kafin nan da kamshi Mallam sule yace abar Mata Hajara idan akasa bikinta ya kusa ta dawo gida. Sai dai harda Hajara ayima iyayenta rakiya zuwa Durmi da yar Haj daga bisani ita kanta hajiyar taga kysutuwar ta bisu domin taga inda suke zaune tunda ko cikin labari bata taba Jin wani kauye ba wai Shi durmi.don haka tare suka tafi tunda Ko suka kama hanya zainabu da Mallam sule suke shima hajiya Albarka tare da addua Kala Kala.

Suna ajesu suka juyo duk da Hajara taso ganin sani Amma mallam sule yace zaiyi masa bayanin komai .sosai mutanen kauye suka shiga surutun ina Mallam sule ya Samo wannan hamshakiyar matar meye Kuma dalilin barin Mata tilon yarsa da yayi. Amininsa Mallam kalla kadai ya tsaya yayima bayani ta Kuma fahimce Shi ya gamsu da baida wata mafita bayan wannan ba Kuma wani abu bane tunda baida Mai taimaka masa sai Allah .

Shiko sani ko da yazo gaida Mallam sule dafatan yaga Hajara bai ganta ba sai bayanin da Mallam sule yayi masa, Wanda Sam bai gamsu ba ya dai bishi da to kawai Amma ransa ya baci Bai Kuma jidadin yadda zaayi masa haka ba, kujifa bayan ko kafin Mallam sule ya tafi asibiti sau biyu ya taba gaida Shi agida ba tare da ko Sisi ba Bai Kuma taba zuwa jigawa ya gaida Shi ba . Don haka banga dalilin daukar zafi ba din yarsa ta tsaya don ta rufa masa asiri.

Hajara dai tana can jigawa tana bautar Haj da yarta da mijinta ba tare da gazawa ba .ta sadaukar da dukkan karfinta wajen yi musu hidima.wanda awannan lokacin idanun Alh Suna dore akanta kullum zuciyarsa na kitsa masa abubuwa da dama , domin ya yarda da cewa tunda yake aduniya babu wata mace da ya ji ta azuciyarsa bayan Hajara Sonta yake kwarai da gaske burinsa ace ya aureta Amma yasan masifar kishin Matarsa.

Wanda yasani tunda mijinta ya rasu suke tare Amma bata yarda zata aureshi ba har saida Allah yayima Matarsa rasuwa da kanta tace zata aureshi, yafi kowa sanin kishinta to Amma ina zai Kai tsananin so da shaawar da yakema Hajara da ko muryarta ya ji sai ya rasa aduniyar da yake saboda so.

TO BE CONTINUE

DAGA TASKAR YAR GIDAN IMAM
NIMA MATARSA CE
NA
HABIBA ABUBAKAR IMAM
(YAR GIDAN IMAM)
BABI NA TALATIN DA TAKWAS
****

Sosai Alh yake son Hajara ya rasa sukuni ,kullum zuciyarsa tana Kara kwadaita masa Hajara.

Ayayinda ita bata gane komai ba aikin gabanta take yi kawai.kullum tana tare da yar Haj shakuwa mai tsanani ta Kara shiga tsakaninsu .

Hajara tayi matukar Samun nutsuwa bata da damuwar komai domin tana cikin wadatuwa da komai, kamar yadda tasan can ma iyayenta wahala ta Ragu musu tunda suna Samu daga aikin da take yi naira bata dauka su take turoma.idan ma akwai abinda ke damunta to ba zai wuce maganar sani ba da babu wata hanya ta haduwarsu, tana son sani bata son duk wata baraka da zata iya shiga tsakaninsu. Bata gane sani na cikin damuwa akan zamanta a jigawa ba sai wani zuwa da tayi gida kusan fada sukayi sosai domin yace lalle sai dai ta aje aikin ta dawo

gida Wanda ta kasa yi masa alkawarin zata iya yin hakan domin alokacin ta Kara tabbatar da cewa itace gatan iyayenta kusan ci da shansu da kudin maganin mahaifinta duk ta sanadiyyar aikin nan take samunsu domin ita kanta tasan cewa ta hadu da mutanen kirki babu abinda zata ce ma Haj sai dai godiya mara musaltuwa.

Don haka haka ta dawo jigawa babu wata cikakkiyar fahimta tsakaninta da sani , abin Kuma Yana damunta Yana kuma yi Mata ciwo, sai dai bata da yadda zatayi iyayenta sune gaba akan komai.

Lokacin dawowar Mallam sule asibiti yayi sun dawo Kuma likita ya duba ya Kara dibar masa watanni shida akan ya dawo asa ranar aiki , sun Kuma Kara masa mgunguna, wannan daga ranar aikin da sukeyi ya Fara sa ma su zainabu shakkun ayya kuwa ba suna Jan maganar bane saboda suna ganin ko ciwon nasa Bana tashi bane, domin dai har alokacin jikinsa cikin tsanani yake sai dai sauki na Allah.kwanakinsu biyu agidan Haj ta Kara bada mota da Kayan abinci aka maidasu gida.

Alokacin ne bayan dawowarsu gida aka Sanya ranar Auren Hajara da sani watanni Tara masu zuwa.duk da daga sanin har mahaifansa babu wani Wanda ya nuna jindadi ko sha'awar hakan, kawai dai sun Zama kamar Yan abi yarima asha Kida.

Aranar da Hajara ta sanar da Haj ansa ranar aurenta , ta tayata murna ta Kuma Fara tunanin ranar da zasu rabu domin tasan zata shiga damuwar rashinta kasancewar ta saki jiki ta shaku da Hajara yarta ma ta shaku da ita tabbas tasan ranar rabuwa akwai matsala da damuwa.

Amma ta bangaran Alh kuwa ranar kasa bacci yayi , ta yaya Hajara zatayi aure bayan itace mace ta farko da yake Jin tamkar numfashinta zai fita idan ya tuna bazai iya samunta a matsayin Mata ba.ya rasa inda zaisa kanta Bai tabbatar ya fada masifar kaunarta ba sai awannan daren da Sam ya kasa runtsawa washegari ma haka ya tashi kamar Wanda yayi jinya duk Wanda ke gidannan ya fahimci akwai canji da matsala atare da Alh ,ya kasa ci ko sha, sai wani azababben ciwon Kai da ya addabe shi.bai Samun sauki sai ya dubi Hajara .lamarin ya zamto tamkar wata masifa agareshi.

Washegari bayan fitar Haj .Alh ya rutsa Hajara a dakinta, tayi gaggawar tashi daga Kan gadon tana kallonsa cike da tsarguwa da daburcewa tace muryarta na rawa " kana son wani abu ne? Ya girgiza Kai gami da zaunawa a gefen madubin kusa da gadon yayi Mata kallon tsaf sannan yace " koma ki zauna magana nake son yi da ke" asanyaye ta koma ta zauna tana kallonsa hakanan taji gabanta na matukar faduwa.

" Ansa Miki ranar aure Ko?" Cike da mamakin tambayar tace " eh " .ya ja numfashi ya aje sannan yace " hakanne yasa naji zuciyata ba zata iya dauka ba" tayi saurin cewa " me yasa?" Ya dubeta sosai kamar daga sama Hajara taji yace " saboda ina matukar sonki fiye da komai a rayuwata Hajara" tayi zumbur ta Mike tana yi masa kallo Mai cike da mamaki tace " subhanallah me zanji haka, don Allah kayi hakuri Ka rufa min asiri Ka daina wannan maganar Kada Ka Kara

yinta don Allah" ya Matso kusa da ita yace " Bana tsoron kowa ya ji Hajara ina sonki " ta juya da sauri zata fita daga dakin nan da nan yasa hannu ya fisgota ya dawo da ita cikin dakin

Hajara ta gigice idanunta suka Fara fitar da hawaye tace " don Allah Kada Ka bata min rayuwa kayi hakuri" yace cikin jajayen idanu wadanda da alamun sun manta komai basa ganin komai sai Hajara da kwadayin kasancewa da ita.

" Babu kowa agidan nan Hajara bazan iya jurewa ba , ina cikin matsanancin hali na shaawarki Bana iya bacci Baba iya yin komai sai Tunaninki ki taimakeni yau na sauke shaawata babu abinda bazan iya yi Miki ba arayuwa Zan jiyar dake dadi Zan maida ke Yar gata Zan Kula da mahaifanki Zan dauki nauyin jinyar mahaifin.....?

A gaggauce cikin tashin hankali ta dakatar dashi tace cikin hawaye " kaji tsoron Allah a matsayin ya nake awajenka domin nasan Ka haifeni ,Ka dubeni a matsayin ya Ka taimakeni Kada Ka watsa rayuwata". Ya nufota cikin rufewar idanu ta juya da gudu zata fita cikin ihu .

Nan ma karfi yasa ya janyota wannan Karon kafa yasa ya tura kofar ita Kuma yayi wurgi da ita Kan gado tana ihun neman dauki tana turje turje komai na duniya ya tsaya Mata cak tana ganin abin tamkar mafarki.irin ihun da take yi yasa ya fisgo dankwalin kanta ya tura Mata acikin bakinta gami da bankare hannayenta . Duk yadda taso ta ture Shi abin ya gagara domin dai yafi karfinta hawaye ne kadai ke fita Mata masu matukar zafi da radadi.

Shi Kam Bai San me yake yi ba Mayen shaawar Hajara ya mantar dashi komai .ba tunani domin kwakwalwarsa ta toshe bata ko yin aiki alokacin. Ya Zama tamkar dabba domin haka ya fadama Hajara ya keta Mata rigar mutuncinta ya bata tarbiyyar da iyayenta sukayi Mata shekara da shekaru .

Ya Gama duk abinda ransa ya ke so.dai dai lokacin haj ta bugo kofa ta shigo dakin da alamar ba ma yanzu ta dawo gidan ba ta Dade da dawowa.bakinta babu abinda yake fada sai innalillahi wainna'ilaihirrajiun, cikin matukar gigita da dimauta Alh ya tashi Yana kokarin maida kayansa Yana tsuma zuwa lokacin kuwa Hajara bata San a duniyar da take ba gaba daya numfashinta ya dauke ta Suma. Kan Alh taso tabi Amma ganin Hajara kwance babu alamar numfashi atare da ita yasa ta tsallake Shi ta nufi wajenta tana Kiran sunanta tana girgizata.

Ganin hakan yasa Alh ya tsallake da gudu ya fice daga dakin.iya tsorata da gigita Haj tayi ta rasa inda zatasa kanta ta Dade tana girgiza Hajara har yar karamar yarta ta shigo itama ganin Hajara kwance haka duk da batasan menene ba kuka ta shiga yi .Haj ta yaye zanin gado ta rufama hajara.sannam ta tashi cikin rawar jiki ta dakko ruwa ta shiga shafa Mata a fuska, hakanne yayi sanadiyyar dawowar Hajara hayyacinta.tana hada Ido da Haj ta Kara fashewa da kuka harda gunji Haj tasa hannu ta rungumeta lokaci daya Kuma na rasa tunanin da tayi Saita cire Haj daga jikinta ta Mike tana kallonta sosai tace " Hajara menene yafaru? Cikin rawar murya gami da galabaita ta gaya Mata komai.

Haj ta koma jikin bango ta jingina gami da lumshe idonta sai alokacin hawaye ya fita daga cikin idanunta.cikin kuka Hajara tace " ina zansa Kaina shikenan rayuwata ta kare Haj".

Haj ta Matso da sauri kusa da ita fuskarta ta canja sosai maimakon tausayin Hajara dake cikin kwayar idonta yanzu babu komai sai kyama da tsana tace " kimin shuru, Hajara na rantse Miki idan kika fitar da wannan maganar wani waje, Saina sabauta rayuwarki domin Bana wasa da mutuncina Zan iya yin komai domin tabbatar da kima da daraja ta bata salwanta ba". Hajara ta tsaida idonta akanta a gigice tace " Haj ashe bazaki taimakeni ayi adalci atsakaninmu ba kema fa kin Haifa Kuma kema ya macece ina Zan Kai wannan kuncin rayuwar" tayi Mata wani irin mugun kallo tace " na gaya Miki kibar wannan maganar anan ki rufama kanki asiri, yanzu ki tashi kije ki yi wanka ki gyara kanki Zan Kira likita ya dubaki Bana son Kuma kiyi wata magana " tana Gama fadin haka ta juya cikin matukar tashin hankali ta fice daga dakin.wanda zuwa lokacin ma tuni Alh ya fice da kayan sawansa yabar gidan.

Hajara ta Kara gigicewa ganin irin jinin da ya bata Kan gadon. A haka ta tashi cikin matukar galabaita da tashin hankali da bakinciki adaddafe ta shiga bandaki harta Gama wanka da gyara kanta kuka take tuni idanunta suka kumbura sukayi suntum.

Tana daki ta kasa fitowa zazzabi me zafi ne yayi awon gaba da ita .likita ya zo Haj ta kawo Shi har dakinta ya dubata ya Kuma rubuta Mata magunguna haka suka fita da likitan ba tare da Haj tayima Hajara magana ba sai dai kallo daya zakayi mata Ka tabbatar da cewa tana cikin matsanancin tashin hankali mara musaltuwa.

Aranar aka sayo Mata magani.amma Alh Bai dawo gidan ba har washegari Bai dawo ba. Tun Kuma daga Randa abin ya faru Haj ta daina yima Hajara magana. Itama tana dai kwance adaki ta ji sauki Amma tana cikin tashin hankali da damuwa.

Aranar Haj ta shigo ta dubeta tace ta shirya zaa kaita gida, gabanta yayi matukar faduwa ta so tayi Mata magana sosai Amma babu fuska don haka ta hadiye maganganunta .ta tashi ta shirya kayanta.haj ta Kara shigowa ta Mika Mata kudi masu yawa tace ta rike ta fito Kuma direba Yana jiranta.

Adaki Haj ta aje yarta ta kulle saboda tasan idan taga fitar Hajara to ranar bazaayi sukuni agidan ba ta dinga kuka da damuwa Kenan. Haj ta dubi Hajara tace " Zan zo garin, babu damuwa" Hajara Kai kawai ta gyada

Har suka kama hanyar Durmi Hajara tana cikin matukar tashin hankali tare da mamakin canjawar Haj .zuciyarta Kuma na bijiro Mata da tambayar ina Alh ? Sannan ya zatayi tayima iyayenta bayanin abinda ya faru? Ta ina zata Fara?.har suka Kai Durmi bata cikin sukuni.su kansu su Mallam sule sunyi mamakin ganinta domin dai sun San bata dade ba rabonta da garin.

Amma da sukayi Mata tambayar dalilin zuwanta ce musu tayi su Haj zasuyi tafiyane shine tace

tazo gida idan suka dawo Saita dawo.hakanan zainabu taji bata gamsu da abinda Hajara ta fada ba, musamman data Lura da ràshin nutsuwar da take ciki da ràshin walwala gashi fuskarta ta nuna bata da lafiya, shin meke faruwa? Tambayar farko kenan da ta Fara yima kanta.

Haka Hajara ta cigaba da Zama a Durmi cikin ràshin kwanciyar hankali da nutsuwa duk Dan Kyan da tayi yanzu ya disashe kallo daya zakayi mata kasan tana cikin damuwa.sai awani dare Wanda ya Kai sati hudu da dawowarta gida, harta kwanta zainabu ta tasheta tace " Hajara nasan ba bacci kikeyi ba domin na San tunda kika dawo daga birni bakya bacci kawai dai kina kwance ne," Jin hakan yasa Hajara ta tashi ta zauna tana kallon zainabun fuska cike da damuwa da bakinciki da tun dawowarta basa rabo da fuskarta. Zainabu tace tana kallonta " ni na haifeki Hajara Kuma nafi kowa sanin ki don haka Bana son ki boye min komai domin ko kin boye fuskarki ta bayyana damuwar da kike ciki tun daga ranar da kika dawo gidan nan, shin meke faruwa? Wani laifin kikama Haj data sa aka dawo da ke gida kince Kuma tace zata zo idan ta dawo Amma yau kusan sati hudu Kenan da dadaworki amma bata zo ba,don haka ina son ki gaya min gaskiyar komai".

Nan da nan idanun Hajara suka Kara cika da hawaye ta fado jikin zainabu ta rungumeta tsan tsan kamar zata fasa jikinta ta shiga lokaci daya Kuma kuka Mai karfi ya Kara kwace Mata.

Hakan yayi matukar gigita zainabu ta dago fuskarta tana tambayarta " ki natsu Hajara kiyi min bayani menene ?". Hajara ta cigaba da kokarin tsaida kukanta bakinta na fadin " Inna rayuwata ta Riga ta lalace, bansan ya zanyi da wannan mummunar kaddarar data Fado min ba, bansan ya zanyi ba". Furucin Hajara ya Kara gigita zainabu ta riketa sosai ta daka Mata tsawa tace " ke ki natsu ki gaya min meya faru.....
TO BE CONTINUE

DAGA TASKAR YAR GIDAN IMAM

NIMA MATARSA CE
NA
HABIBA ABUBAKAR IMAM
(YAR GIDAN IMAM)
BABI NA TALATIN DA TARA
****
Hajara ta hadiye wani zazzafan yawu tace cikin kukan da ta kasa tsaida Shi.

" Inna ina cikin tsaka mai wuya,kullum zuciyata cikin masifar Kuna da damuwa take domin.na rufe bakina naki gayama kowa damuwata balle naji saukin masifar damuwar da nake ciki"

Zainabu adaburce tace " Hajara gaya min Kada kisa zuciyata ta buga , gaya min". Sannu ahankali Hajara ta Gama sanar da mahaifiyarta komai, Wanda zuwa wannan lokacin tuni zainabu ta fita hayyacinta nannauyan numfashi kawai take saki zuciyarta kuwa kamar ana rura Mata wuta ta Kai minti daya ta kasa magana sai Ido data zubama Hajara, saida Hajara tasa

hannu tayi ta girgizata sannan zainabu ta dawo hayyacinta hade da fitar da hawaye daga kwarmin idanunta,

Cikin rawar murya tace " innalillahi wainna'ilaihirrajiun, yanzu Hajara abinda ya faru da ke Kenan Amma kika ki gaya mana bayan mune yakamata mu Fara sanin wannan bakar kaddarar " kuka take sosai tana cewa " Amma Haj ta ci amanar mu , tana nufin tace duk irin wannan ta'addancin da mijinta yayi Miki Shi take goyama baya, ta turo ki tace zata zo taki zuwa duk girman wannan maganar " Hajara ta goge hawayenta tace " tun kafin tahowata gaba daya ta canja min na fuskanci son zuciya da son Kai irin na mutanen birni Yana nan acikin zuciyarta " zainabu tace " me suka dauki mutanen kauye?, Marasa galihu ko marasa daraja wadanda Basu San yancin kansu ba?. Hajara har yanzu cikin kuka take tace " Inna ya zanyi da wannan bakincikin" zainabu ta kama Kai ta rike Kam Jin wani abu take yi Yana yi Mata yawo duhu kawai take gani agabanta ta rasa abinda ke yi Mata dadi.

Zainabu ta dago ta dubeta tace " Hajara ina son wannan maganar mu barta Bana son wani yaji wannan maganar, domin kinfi kowa sanin mutanen garin nan ba zasu taba yi mana Uzuri ko adalci ba matukar wannan mummunar maganar ta fita,mu aje ta anan mu cigaba da zaman jiran zuwan Hajiyar, duk da banji a raina zata iya taimaka mana da komai ba", ta Kara kallon Hajara tace " cuta dai an Riga an cucemu duk abinda zasu yi mana bazai wanke damuwa da bakincikin da suka jefamu ciki ba, shiko Alh bazan taba yafe masa ba har abada".

Hakika tunda zainabu take bata taba shiga bakinciki da tashin hankali irin na wannan dare ba, domin shine dalilin da itama bata Kara Samun bacci ba da daddare, duk dare hakanan suke kwanciya da ita da Hajaran duk babu mai iya runtsawa.nan da nan damuwa ta Fara nuna su duk da Mallam sule kwance yake Yana ji da Kansa to fa ya fahimci akwai damuwa haka yayi ta tambayar meke samunsu amma zainabu tana basarwa tana nuna masa damuwar ciwon sa ne kadai ke damunsa.

Amma duk da haka kullum cikin tambayar yaushe Hajara zata koma jigawa yake daga karshe dai zainabu ta gaya masa zasu Dade Basu dawo daga tafiyar da sukayi ba , shiyasa Hajara ba zata koma ba har sai sun dawo.

Ahankali kwanaki suka shude satittika suka shude ayau watannin Hajara biyu da dawowa Durmi , Wanda har yanzu wannan lokacin Bai dauke damuwa da fargabarsu Hajara da mahaifiyarta ba, musamman da har zuwa wannan lokacin babu amo babu labarin Haj.

Ciwon mallam sule Kuma kullum gaba yake yi Dan saukin ma da ake Samu yanzu babu sai dai na musulunci.

A wañnan lokacin ne Hajara ta Fara ciwon da aka Rasa Gane Kansa, laulayi sosai take yi duk abinda ta ci sai ya dawo.

Hankalin zainabu yayi mummunan tashi ta fada wani mugun damuwar domin idan har abinda

zuciyarta take raya Mata gaskiya ne tabbas sun shiga cikin babbar masifa wacce bazata misaltu ba.

Awani dare ne zainabu ta tada Hajara ta Kura Mata Ido cike da fargaba tayi Mata tambayar " Hajara yaushe rabonki da ganin al'adarki?". Duk da Hajara bata San ma'anar tambayar ba sai da gabanta ya Fadi sosai , ta gyada Kai tace " rabona da ganinsa tun ina jigawa Inna". Wata irin kibiya ta tsire zainabu a kahon zuciyarta kanta ya Sara wasu zafafan hawaye suka dinga fita Mata, ta Dora kanta a jikin cinyoyinta tana Jin kamar ta hadiye zuciya ta mutu.

Hajara ta rude da ganin mugun halin da mahaifiyarta ta fada , ta matsa kusa da ita ta ce " Inna lafiya menene? Ta dago tana dubanta duba Mai cike da tausayi tace " Hajara ke Kuma ahaka kaddarar ki ta zo , Hajara ciki gareki".

A dimauce ta dafe kirjinta hannu bibbiyu ta fiddo idanu waje tace " ciki Inna" zainabu tayi saurin rufe bakinta tace " kiyi ahankali Kada babanki ya jiyo ki, Wanda nayi Imani hakan na iya yin ajalinsa". Hajara ta rufe bakinta tana fitar da sautin kukanta a hankali.

Ta rasa a duniyar da take , bata jindadin komai , ta rasa ma wane irin tunani kwakwalwarta zatayi.haka suka hadu su kayita kuka gwajin ban tausayi.

Washegari kuwa da wuri zainabu ta dauki Hajara zuwa asibiti domin ta tabbatar da zarginta.cikin kankanin lokaci aka Gama duk wani gwaje gwaje .sakamako Kuma ya fito da tabbacin Hajara tana dauke da cikin watanni biyu.

Tashin hankali Wanda baa sa masa rana!. Tsayawa faden tashin hankalin da suka fada ciki baima taso ba illa dai Hajara da zainabu sun fada tashin hankali mara musaltuwa.

Tunda suka dawo gida zainabu take neman hanyar da zasu bi amma gaba daya kanta ya kulle, tana son yarta bata son ace zaa zubar da cikin nan ta zo ta rasa ranta adalilin hakan .

To Amma lokaci yayi da dole Mallam sule zaisan abinda ake ciki.

Amma kafin hakan ta yanke shawarar daukar Hajara zuwa jigawa gidan Alh domin dole su San abinda ake ciki lokacin Kuma karbar ma Hajara hakki da yanci yazo domin ayau komai talauci da kasawarsu sai ta yima Alh haukar da zaiyi nadamar taba Mata ya.

Basu bar garin ba saida zainabu ta Sami almajirin da zai zauna Mata da Mallam sule har su dawo.

Shi Kuma Mallam sule ta gaya masa cewa zata je gidan Haj ne saboda su gani don shurun yayi yawa.wanda ya a mince da hakan batare da tunanin komai ba , musamman da yasan komai ya tsaya tunda Dan taimakon da suke musu ya daina zuwa.gashi ba waya balle Akira asan halin da ake ciki.

Tun azuba suka bar kauyen Durmi kaf dinsu cikin mugun yanayi da tashin hankali.

Ba wasu kudi gareta ba gun matar Mallam kallah sabira ta aro kudin motar.

Sun isa jigawa da wuri Hajaran majaran, Hajara tana da hankali da nutsuwa hakan yasa da kanta tayi musu jagora har zuwa gidan Àlh a mashin.

Amma wani abin Mai Kara dasa tashin hankali shine ganin gidan a rufe, bugun duniyar nan shuru alamar babu kowa a gidan.

Duk da haka kofar gidan suka zauna suna zaman jiran tsammani ga yunwar da ko abincin suka Samu ba zasu iya ci ba saboda tsabar ràshin kwanciyar hankali.

Basu San iya tsawon lokacin da suka dauka a kofar gidan ba, kafin wani Dan dattijo ya iso kofar gidan ya Fara kokarin Bude get din gidan.

Hakan ne yasa suka tashi da sauri zainabu ta Karasa kusa dashi ta yi masa sallama sannan ta Dora da tambayarsa " don Allah masu gidan fa" ya dubeta sosai yace " ai babu kowa agidan , ba"a Riga an tare ba tukuna" tayi saurin kallon Hajara sannan ta maida kallonta ga mutumin tace " aah ina fa nufin mutanen da suke Zama agidan " ya girgiza Kai yace " oho, na fahimta na fahimta, ai sun tashi tun wajen watanni biyu da suka wuce asalima sun saida gidanne Wanda ya saya ne ya daukeni aikin gadi har yanzu Kuma Bai tare ba a gidan . Zainabu ta lalubi Katanga ta jingina domin ji tayi tana neman faduwa idanunta gaba daya suka rine suka koma jajir, kamar yadda itama Hajara ta rikice ta Dora hannu aka kukanta ya dawo sabo. Cikin rawar murya zainabu tace " don Allah ko kasan inda suka koma" ya girgiza Kai yace " Kai Banda masaniya amma dai ance basama kasar Dukansu Alh da hajiyan da yarsu ance kamar sun tafi Ko London ko'ina amma dai tabbas basa kasar" zainabu ta juya tana neman faduwa Hajara ta kamata ta rike ayayinda mutumin ya karasa Bude get din ya shige cikin gidan.

Tun anan kofar gidan zainabu ta hadu da mummunan ciwon da baa San wane iri bane illa dai sun San damuwa itace sila.

A daddafe da taimakon Hajara suka iya dawowa gida , zainabu tunda ta kwanta ko motsi bata iyawa, ita kanta bata San meke Mata ciwo ba, tasan dai babu abinda zata iya aikatawa domin babu karfi ko kadan atare da ita.damuwa da tashin hankalin Hajara ya dawo sabo duk mahaifanta suna kwance babu Mai iya tada wani tayi hidimar wannan tayi hidimar wancan ga bakin tashin hankali da damuwa da ràshin nutsuwar da yake damunta ga fitinar laulayi itama yau lafiya gobe ciwo.ta rasa abinda ke Mata dadi domin bata San ya zata bulloma al'amarin ba shin shikenan haka zata zauna ta haife abinda ke cikinta?

Dole tasa zainabu sanar da Mallam sule komai ba don komai ba sai don ya cancanci ya Sani bata Kuma San gawar fari ba tsakaninsu Kada ta rigashi mutuwa , yasan maganar ya dauka ta

yaudara Shi ne ta Kuma raina lamarinsa yasa bata gaya masa babban lamarin da ya shafi yarsa ba ,domin ayadda take Jin jikinta da yanayin damuwar da take ciki bata tsammanin tana da sauran wani lokaci nan gaba.

Sai dai kusan zainabu ta so tayi nadamar Gaya masa da tayi domin cikin kankanin lokaci jikinsa ya Kara rikicewa jikinsa ba zai iya daukar damuwar ba.domin a wañnan ranar jinyar Mallam sule ta kare ya koma ga mahaliccinsa cikin tsananin bakincikin kassara rayuwar yarsa da akayi ba tare da hskkinta ba.

Duniya ta tsayama Hajara da mahaifiyarta cak rasuwar Mallam sule ta Kara jefasu acikin matsanancin masifa Mara musaltuwa, Hajara ta dorama kanta nauyin rasuwar mahaifinta domin tana ganin kamar itace silar rasuwarsa, bata taba jin tsanar Alh ba irin na wannan lokacin hakika ya Gama da ita da rayuwarta.

Bayan rasuwar Mallam sule, rayuwa ta Kara zafafa agaresu, Ga uwa uba kus kus din da jamaar garin suka Fara na maganar cikin Hajara an rasa ta inda maganar ta Fara fitowa don tuni ta mamaye gari, har zuwa ake ana ganin Hajara da an ganta zasu ce ah gashi nan fa ga alama nan zaman birni ya biya bukata.

A'irin mutanen marasa kunya da suke zuwa ganinta yau sun fita Kenan , Hajara ta fashe da kuka me karfin gaske ta dubi zainabu wacce jinyarta ta Fara tsanani cikin kuka tace " yanzu Inna haka Zan zauna na haifi abinda ke cikina cikin wannan al'ummmar da basama Dan Adam Uzuri" zainabu ta ce cikin galabaitar ciwo " abinda ya faru da ke Baki da laifi ko daya, amma idan har kikayi yunkurin ganin bayan abinda ke cikin ki ina tabbatar Miki sai kin Zama Mai laifi fiye da Alh , don haka na umarceki da ki toshe kunnanki ki ji Kiki ji ki gani Ki ki gani Ki taimaki abinda ke cikin ki har ya shigo cikin duniyar da shima zai zo ya fafata da kaddararsa acikinta". Hajara ta zuba tagumi tana rera kuka sosai zainabu tace " ki Zama jaruma domin Bani da wani lokaci daya rage min a duniya Zan tafi na barki ke kadai ba ki da wani mataimaki ba kyama da aibatawa suke zasu Zama abokan rayuwarki".

Hajara ta Kara gigicewa ko kadan bata son taji mahaifiyarta na dorama kanta mutuwa domin dai ita kadai ta rage Mata bata da kowa a duniya .

Cikin Hajara ya shiga wata na biyar zuwa lokacin kowa ya gamsu da cewa tana da ciki, bata fita ko'ina kyama da tsana ba wacce baa nuna Mata ba duk wadanda suke alakar arziki dasu sun datse zumuncin babu Mai zuwa gidansu duk da matsananciyar jinyar da zainabu ke ciki. A wañnan lokacin sani ya tabbatar ma da Hajara ya fasa aurenta babu Shi babu ita ,ya faffada Mata maganganu masu zafi wadanda harta mutu ba zata taba mantawa dasu ba.....

TO BE CONTINUE

DAGA TASKAR YAR GIDAN IMAM

NIMA MATARSA CE

NA
HABIBA ABUBAKAR IMAM
(YAR GIDAN IMAM)
BABI NA ARBA'IN
****

Maganganun da ya gaya Mata sun fi rabuwarsu ciwo agareta. Tun daga wannan ranar Kuma gaba daya jikin zainabu ya Kara rikicewa, idan so Samu ne ace ta kaita asibiti to amma babu yadda zatayi domin abinda zasu ci ma Basu da Shi balle kudin magani.

Duk inda Zata je ta nemi taimako Hajara ta mutstsuke kunyarta taje amma babu Wanda ya saurareta babu Wanda yake nuna tausayi agareta.
Mallam kallah ne kawai wani lokacin yakansa matarsa sabira ta zuba abinci ta aika musu dashi,

Tunda Hajara take a rayuwa bata taba shiga kunci da bakinciki irin na wannan lokacin ba , gaba daya ta Zama sai kace wata mara hankali domin kanta bazai iya daukar masifar da take ciki ba .
Ko ta kofar gidansu ba'a bi saboda tsabar kiyayya.watannin cikin Hajara takwas Allah ya dauki rayuwar zainabu bayan fama da matsananciyar jinya, ta tafi tabar Hajara cikin matsatsin rayuwa da kunci mara musaltuwa, rasuwar mahaifiyarta ya taba ta ya Kara jefata cikin matsanancin hali, haka ta cigaba da Zama agidan ita kadai tunda dai ba yan'uwa gareta ba Dama daga mahaifinta sai mahaifiyarta duk dangi sun kare sai tsirarun da bazasu iya taimakonta da komai ba daya wuce kyama da kiyayya,Hajara takan uni bata ci ba ga damuwa da itace ta Zama cinta da Shanta.

Kwana takwas da rasuwar zainabu Mai gidan hayansu ya bukaci Hajara ta tattara tabar masa gidansa tunda Bana gado bane , ya Kuma San bazata iya biyan bashin kudin hayar da yake bin mahaifinta ba balle harta cigaba da biya, don haka ta fice masa agida. Duk irin magiya da rokon da Hajara tayi baisa yabarta ba, saida ta hada kayan ta agaban idonsa ta fito daga gidan ta rokeshi Akan zata kwashe sauran kayan daga baya domin yanzu ko ta kwashe bata San inda zata kaisu ba.

Hajara ta rasa inda zata shiga, har zuwa magriba tana kofar gidan azaune kafin ta yanke shawarar zuwa gidan Mallam kallah. Shima din ba wata tarba ta arziki ta samu ba daga sabira shine ma Mallam kallah ya tsaya ya saurari abinda ya faru daganan ya dubeta fuska tamke yace" yanzu Hajara kina ganin rayuwarki zatayi kyau, ace duk bakincikin ki ne ya yi sanadiyyar iyayenki, yanzu Baki da kowa da zaki kalla amatsayin naki, meye ranar kwadayi da son duniya da babu inda zai kaiki sai halaka , yanzu wa Gari ya waya, ina zaki Kai wannan dimbin hakkin da ke kanki"
Cikin kuka sosai Hajara tace " nayi maka rantsuwa Bani da laifi Akan duk abinda ke faruwa a rayuwata Allah da iyayena sune shaidata"

Sabira ta zuba Mata harara tace " ke da Allah can, kyace sune shaidar ki mana tunda kinga

basa Raye, Shi Kuma Allah sai alahira, kin dai yi asara bakinciki Kuma yanzu kika Fara ganinsa, Kuma yanzu da kika taho nan me kike so muyi Miki, ko don kinga muna tausaya Muku muna Baku abinci to ki sani saboda tausayin zainabu yasa Muke Baku abinci ba' don ke ba".

Cikin kuka Hajara tace ," don Allah Inna ki tausaya min babu inda zanje Bani da kowa ina cikin tashin hankali ga halin da nake ciki babu inda zanje sai nan".

Sabira ta saki tsaki tace " kanki ake ji Hajara ai bakinciki Baki Fara ganin komai ba, Baki da wajen zuwa to ina Wanda yayi Miki cikin ki neme Shi mana ai sai ya baki wajen Zama".

Irin kukan da takeyi shine ya taba zuciyar Mallam kallah, ya tuna amintar da ke tsakaninsa da Mallam sule.ya dubi sabira yace " rabu da ita, ki bata wancan dakin ta zauna aciki".
Bai saurari surutan da sabira take yi ba ya tashi ya fita.daker ta nuna Mata dakin ta tashi ta shiga dakin anan Mallam kalla ke aje hatsi. ta Sami gefe ta share ta gyara ta maida Shi wajen kwanciyar ta.

Zamanta agidan bata Sami sassauci ba, Saima Karin damuwa domin duk da tsohon cikinta, itace take yin aikin komai agidan , babu abinda sabira take yi, sai dai ta wanke Goma ta tsoma biyar tayi hidimarta tayi na yayanta duk da tsohon cikinta har wankin sabira da na yaranta take yi.kuma babu godi bare na gode sai hantara da wulakanci.Amma babu yadda zatayi dole ta yi hakuri tunda bata da yadda ta iya.

A haka cikin wannan matsatsin da kuncin, Allah ya sauki Hajara lafiya a gida bayan ta ci bakar wahala.
Ta haifi yarta mace, sai dai ko rigar da za'asa Mata babu sai cikin zani aka nannadeta.sai daga bisani ne tausayi yasa Mallam kallah ya fita ya sayo riguna guda biyu.

Zuwa wannan lokacin kuwa mutanen kauyen sai sintirin zuwa gidan Mallam kallah suke yi ganin yar shege kamar yadda suke fade.Tashin hankalin da Hajara ta shiga awannan lokacin bazai misaltu ba.ita kanta sabira haka ta Kara Dora Mata tsana taki taimakonta da komai ko yarta taki tabawa saboda kyama. Hajara da kanta tasama yarta suna Zainab take Mata inkiya da muhseena Wanda shine ya danne asalin sunanta muhseena ya bita.
Fita ya Kara gagararta, gashi tun bayan haihuwata Mallam kallah ya tabbatar Mata da cewa ba zai iya cigaba da ciyar da ita ba don baisan ranar da Allah zai rabasu ba don haka bazai kashe Kansa ba wajen ciyar da ita dakin Zama dai gashinan tayita Zama . Hakan yasa Hajara ta Kara fadawa mawuyacin hali domin dai ko aikatau ta fita nema babu Wanda yake bata babu Mai son yayi Hulda da ita.ga fitinar aikin sabira da yake neman ya kasheta kullum bata da Hutu.

Haka zalika kullum zuciyarta na raya Mata ta koma jigawa ta cigaba da neman Alh ko Allah zaisa ta dace, amma babu Hali tunda bata da kudin mota ko wani Wanda zai taimaka Mata ya shige Mata gaba, tunda kowa a kauyen Yana ganin ayawon banza ta Samo cikin babu wani bayani da zata yi musu Wanda zasu iya gamsuwa da cewa bata da laifi.hakika Hajara taga rayuwa.

Tana cikin wannan mawuyacin halin na ràshin madafar dafawa daga ita har jatiriyar yarta wacce Hajara take tausayi fiye da kanta domin tana jiye Mata tare da jinjina yadda zata rayu acikin wannan al' ummar sau tari ita kanta tana rayawa aranta ko dai ta gudu ne tabar garin domin tasan idan ta cigaba da Zama kila itama bakincikin ne zai kasheta.

Watannin yarta biyar muhseena ta kamu da ciwon kyanda, Hajara tayi ta sintirin kaita asibiti amma babu me bi ta kansu tunda bata da kudi babu Kuma me son ya taimaketa hatta Mallam kalla yaki taimaka Mata da komai balle sabira wacce har yanzu bata taba daukar muhseena ba saboda tsana.

Hajara na zaune a wajen asibitin ta rungume muhseena wacce numfashinta ke fita daker, kuka Hajara take kamar wacce ranta zai fita , tana zaunene zaman jiran fitar ran muhseena domin dai tuni ta cire rai da ita.

Kamar daga sama taji muryar wani bawan Allah Yana tambayarta abinda ke damunta take kuka, Wanda rabon da taji wani tausashenshan lafazi daga wani Dan Adam harta manta arayuwarta, hakanne yasa ta dago da sauri cikin tashin hankali tace " yata ce bata da lafiya amma babu Mai son ya taimakeni Bani da kudin da zanyi hidimar maganinta babu Kuma Mai taimakona".

Tausayi ya bayyana a fuskar mutumin yasa hannu ba tare da yace komai ba ya dauki muhseena a cinyarta yayi cikin asibitin da ita, ba tare daya saurari Hajara ba, ta tashi tabi bayansa da sauri.

Kai tsaye wajen likitan ya nufa ya Mika masa muhseena yace ya dubata, Hajara na gefe tana rusar kuka har aka Gama duba muhseena aka bata gado, mutumin Shi ya biya komai, Ido kawai Hajara take binsa dashi tana jinjina tausayi da karsmci irin nasa. Tunda wannan ibtila' in ya sameta babu Wanda ya taba nuna tausayi agareta sai wannan bawan Allah.

Da Kansa ya tafi ya samoma Hajara abinda zata ci.sai alokacin cikin zubar hawaye tace " nagode ina rokon Allah yaji kanka fiye da yadda kaji Kaina ya saka maka da mafificin alherinsa". Ya jidadin adduar domin yadda ya zubama Hajara Ido yace " Kada ki damu, ni sunana mallam Umar" ta jinjina Kai tace " ni sunana.....?

Malam Umar ya amshe ya karasa abinda zata ce " sunanki Hajara yar gidan Mallam sule marigayi ". Cikin dimbin mamaki Hajara ta dubeshi tace " kasan ko ni wacece amma Ka taimakeni" ya zuba Mata Ido sosai yace " nasani, Kuma batun yau nake son na taimake ki ba" tayi masa kuri da Ido tace " saboda mene?" Yace a hankali fuskarsa na bayyanar da abinda bakinsa. Ke son Fadi " saboda ina tausayinki, na dade ina Jin damuwarki a raina, duk da Baki sanni ba ni na sanki, na Kuma San wasu daga cikin matsalolinki ". Hawaye ya Kara zubo Mata gami da Dora kanta ajikin gadon da muhseena ke Kai.

Mallam Umar yace " ki sassauta ma kanki damuwa Hajara , ki dubi yadda damuwa ta maida ke duk kin tsofe duk da karancin shekarunki, ki sani kowane rayuwar bawa tana tafiya ne akan kaddarar sa saboda haka kiyi hakuri ko kya samu ki cinye wannan jarabawar" Mallam Umar ya

yi ta Mata nasiha Wanda tunda ta rasa iyayenta babu Wanda ya taba yi Mata irinsu.daga bisani ya barsu a asibitin ya tafi gida.

Tsawon wannan lokacin sai yau Hajara ta ji sassauci Akan damuwarta domin ayau ta Sami Wanda Bai kyamaceta ba , ta samu Wanda ya taimaka Mata a garin da babu me kallonta amatsayin mutum.

Tun daga wannan ranar Mallam Umar shine ya dauke dawainiyar komai na asibitin muhseena, gami da ci da Shanta, haka zalika kullum Yana tare dasu a asibitin daya dawo aikinsa nan yake yada zango.duk Kuma zuwansa Yana kokarin kwantar da hankalin Hajara tare da bata misalai da dama na rayuwa. Agaskiya haduwa da wannan bawan Allah alheri ne ga Hajara domin har ta Fara kokarin Samun nutsuwa Zama da take kamar mahaukaciya tayi ta tunani kwana biyu ta Sami sauki .

A kalla saida suka kwashe sati biyu a asibitin kafin a sallamesu, Wanda zuwa lokacin Hajara ta Saba da Mallam Umar Shi kadai ne take kallo amatsayin wani garkuwa agareta duk da bata hada komai da Shi ba, abinda yayi Mata Har abada bazata taba mantawa ba. Har aka sallameta Kuma ta koma gida sabira bata taba zuwa ta dubasu ba, Mallam kallah ma sau daya ya je asibitin.

Ko bayan komawarta gida, haka Mallam Umar ya cigaba da zuwa Yana duba muhseena Yana kuma Kai musu kayan bukata,Hajara tayima Allah godiya daya kawo Mallam Umar cikin rayuwarta alokacin da kowa ya juya bayansa a gareta.Wani zuwa da yayi ne a kofar gida ya dubi Hajara cikin nutsuwa yace " Hajara ina son naji gaskiyar yadda akayi kika Sami muhseena Bana son kiyi min karya , domin duk abinda mutanen gari suke fada akanki ban taba kamawa ba ba Kuma Zan yarda ba sai abinda ya fito daga bakinki na gaskiya". Hajara ta numfasa idanunta suka cika da hawaye domin bata taba Samun Wanda yayi Mata irin wannan tambaya ta tunani ba, kowa kawai ya yankema Kansa hukunci ne. Ya dubeta ya girgiza Kai yace " Bana son kuka, ina son ki natsu muyi magana ta gaskiya". Hajara tace " A'irin taimakon da Ka min arayuwata Bana Jin Zan iya yi maka karya ko da Don jindadi na ne saboda haka Zan gaya Maka gaskiyar komai babu abinda Zan boye maka". Sannu a hankali Hajara ta labartama malllam Umar komai.ta karasa tana goge hawayenta

Mallam Umar ya cire tagumin da ya zuba, ahankali yayi dabarar share siraran hawayen dake fita a idanunsa,. Yayi shuru na wasu dakika sannan ya numfasa yace " na yarda da duk abinda kika fada domin Naga gaskiyar a cikin kwayar idanunki" ya Kara numfasawa yace " Allah yayi Miki sakayya Hajara , Allah Kuma ya raya muhseena yayi Mata albarka'.

Hajara tace " Amin , nagode nagode da irin taimakonka agareni" ya girgiza Kai yace Kada ki damu, zaki gane gidan Alh yanzu idan Muka je jigawa" tayi saurin kallonsa tace " Zan gane" yace " to ina son ki shirya gobe zamu tafi jigawa, ki sanar da mutan gidan ". Hajara ta zuba masa Ido tana cike da mamaki tace " jigawa?" Yace " eh, zamu je mu neme Shi wata kila ko sun dawo daga inda suka tafi". Hajara ta rasa bakin godiya àgare Shi.domin harya tafi godiya take masa da fatan alheri ta Kara ganin girma da kimarsa fiye da kullum, ta ji aranta Allah ne ya kawo Mata Mallam Umar domin ya Zama sanyi acikin rayuwarta.

TO BE CONTINUE

DAGA TASKAR YAR GIDAN IMAM

NIMA MATARSA CE
NA
HABIBA ABUBAKAR IMAM
(YAR GIDAN IMAM)
BABI NA ARBA'IN DA DAYA
****

Tun daren ranar ta sanar da Mallam kallah da sabira batun zuwanta jigawa ita da Mallam Umar.

Mallam kallah yayi Mata kallon tsaf yace " Kai Shi Ko Mallam kallah da shegiyar tattaga ya ke , da tsabar iyayi, meye nasa na daukarki kuje jigawa, Kenan Shi yama yarda da karyar taki"
Sabira ta tabe baki tace " iyayi ko kinibibi, su suka sani, yin hakan dai bashi zai kankare Miki zargi da bakin fentin da ake ganinki da shi ba".

Kai kawai Hajara ta jinjina ba tare da tace komai ba, domin dai ta gaji da yi musu bayanin gsskiyarta tunda ba zasu taba yarda da ita ba, to tana ganin yi musu bayanin kullum baida wani amfani.

Maganganun da suka cigaba da yi ne marasa dadi yasa Hajara ta tashi ta shige daki.haka ta kwana cikin godiya ga Allah daya hadata da Mallam Umar domin ayanzu dai damuwa ta Fara yi Mata sauki.

Washegari da wuri Mallam Umar ya zo , sai da ya Samu kebewa da Mallam kallah yayi masa bayanin dalilin zuwansu jigawa.mallam kallah ya tamke fuska yace " zadai Ka wahalar da kanka kawai , domin duk abinda Hajara ta gaya maka karya ne , bansan dai dalilin da yasa kake son sa kanka a wahala ba" ya girgiza Kai yace " Banga karya acikin idon Hajara ba, Kuma taimako bsi taba Zama wahala ba, ni na ji ina son na taimaketa don haka babu wata damuwa in sha Allah".

Fahimtar da Mallam kallah yayi na cewar Mallam Umar bazai taba sautarensa ba yasa yayi shuru , daga bisani yayi musu fatan dawowa lafiya.
Har Hajara da malllam Umar suka Kai jigawa muhseena tana hannunsa.Babu abinda ya bace ma Hajara domin har kofar gidan Alh ta Kai Mallam Umar .

Sai dai wannan Karon wani maigadin suka tadda ba Wanda suka taba gani ba.mallam Umar ya tsaya yayi masa bayani sosai na mutumin da suke nema.
Maigadin yayi Jim alamar tunani daga bisani yace " gaskiya bansan wani mutum haka ba,

domin bashi bane agidan, ni Kaina ban wuce watanni uku da Fara aiki ba, Kuma gadin kawai nake yi na gida domin har yanzu babu Wanda ya tare agidan". Idanun Hajara suka cika da kwalla ta Kara sa hannu ta rungume yarta.

Mallam Umar ya numfasa cike da damuwa, baisan dalilin da yasa tun daga ranar da Hajara ta bashi Labarinta yaji Yana so ya taimaketa ba , tausayin ta Kuma da tausayin yarta suka tsaya masa arai , yadda ko me yake yi baya rabo da tunaninsu.

Ya dubi Hajara yace " Bana son ki cigaba da sa ma kanki damuwa, domin babu maganin da hakan zai yi Miki".

Ya Kara numfasawa yace " bazai yuwu mu ce zamu cigaba da nemansa a babban gari irin wannan ba, domin abinda kamar wuya,Amma ina son ki sani Allah baya zaluunci ya Kuma Sanya Shi abin haramtawa a gare mu, don haka ki sama ranki Allah zaiyi Miki sakayya ko a dade ko ajima ".

Cikin hawaye tace " yanzu shikenan haka yata zata rayu bata San ubanta ba ?" Ya dubeta sosai yace " ko kin ganshi yanzu , kina tsammanin cikin ruwan sanyi zai karbi muhseena amatsayin yarsa (ya girgiza Kai) bazai taba amsarta cikin dadin rai ba, Kuma a matsayin sa na me kudi Bana Jin. Zamu iya yaki dashi tunda ayanzu an maida kudi sune komai,". Ya gyara tsayuwarsa Yana cigaba da kallonta yace " KO da nace mu zo, mun zo ne kawai saboda ko da mun ganshi ya San Yana da ya da ke ko ya amince ko Bai amince ba ya dai sani ". Gaba daya Hajara ta rushe da kuka me karfi, tana fadin " ya zanyi da rayuwata, Bana Jin Zan cigaba da rayuwa a Durmi , kawai Ka tafi Ka barni anan domin idan na cigaba da Zama a can bazan taba rabuwa da tashin hankali da damuwa ba, mutanen garin Kuma ba zasu taba yi min Uzuri ba haka Zan zauna yata ta taso su cigaba da jifanta da mummunar Kalmar shegiya, karshe su jefa Mata tsanata kamar yadda suka jefama kansu".

Tausayin ta ya Kara kama Shi ya yi kasa da Kansa ya na nazarin maganar da yake son ya fada Mata.

Zuwa Dan wani lokaci ya dago ya zuba Mata Ido cike da wani yanayi da yake Jin bazai iya Hana Kansa faden abinda ke cikin ransa ba yau.

"Hajara" ya Kira sunanta a tausashe, ta amsa ahankali ba tare data dube Shi ba.yace " ina son ki kwantar da hankalinki, ni Umar Zan amshi yarki muhseena amatsayin yata Zan riketa Zan bata sunana a matsayin uba Zan kare Mata martaba da mutunci amatsayin ta na ya ta, daga karshe Zan aureki domin Zama Uwa da uba ga Hajara ba tare da mun rarraba kanmu ba".

Tikisa! Hajara jin maganar tayi kamar mafarki, tayi gaggawar kallonsa shima ita yake kallo, suka hada Ido gaba dayansu wani abu ya tsurga musu . Tace tana yi masa kallon mamaki " kasan abinda kake fada kuwa, Mallam yanzu zaka aure ni, Kuma Kaba yata sunanka a matsayin uba?" Ya gyada Kai yace " in sha Allah, domin ina ganin wannan jihadin da zanyi shine dalilin da Allah ya hanani haihuwa" tace da sauri " ya hanaka haihuwa?" Ya gyada Kai yace " eh, Hajara aurena uku duk babu wacce ta iya hakurin Zama da ni , saboda lalurata ta tashin haihuwa domin likitoci sun tabbatar min da cewa bazan taba haihuwa ba, dalilin da yasa kenan

Matan da na aura basa Zama, hakanne yasa na yanke shawarar na hakura da aure bazan Kara yi ba tunda babu wata mace da zata iya Zama da ni".

Ya aje numfashi ahankali ya cigaba da cewa " ke kanki bazan iya aurenki ba sai idan har kin amince, idan Baki amince ba babu komai duk da haka ina nan a matsayin mahaifin muhseena ". Zuciyar Hajara ta yi rauni , tausayin Mallam Umar ya kamata nan da nan taji ta aminta dashi za Kuma ta iya hakuri da ràshin haihuwar ko don ta saka Masa da irin halacci da karancin da yayi Mata arayuwa, babu abinda ta hada dashi Amma ya taimaketa ya maida damuwarta damuwarsa karshe ma ya dauki ragamar rayuwar yarta ya danganta ta da Kansa zai Zama ubanta.ita ko ta yaya zata manta dukkan wannan halaccin tace Ba zata aure shi ba saboda kawai baya haihuwa.

Mallam Umar yace " Kada ki takura kanki, idan ba zaki aure ni ba , babu komai bazan dauki hakan a matsayin wani abu ba" . Ta girgiza Kai tace " Ashirye nake na aure Ka, na rantse maka kana da babban matsayi a gareni , ba Kuma Zan taba manta halaccinka àgare NI ba, duk kyama da mugayen maganganun da ake jifana dasu Bai sa maka shakku akaina ba, Kaine mutum na farko da Ka yarda da ni bayan mahaifana, saboda haka na yarda Zan aure Ka".

Mallam Umar yayi Dan murmushi yace " To Allah ya tabbatar mana da alheri, maganar Kuma muhseena bata da uba wannan ya Zama tsohon zance ni Umar nine mahaifinta".
Karo na farko kenan da Hajara tayi murmushi sosai, tace " Nagode".
Daga bisani suka tattara suka dawo Durmi, da Kaya niki Niki Wanda Mallam Umar ya tsaya ya sayoma muhseena Duka kayan Sawa ne, Wanda tunda aka haifeta babu Wanda ya taba bata Kaya irin haka harda takalmi. Hajara ta rasa bakin godiya sai murmushi take Wanda Shi Kansa Mallam Umar tun haduwarsu Bai taba ganin murmushinta ba. Bayan komawarsu Yana Kai Hajara gida ya wuce gidansa saboda ya gaji.

Sosai sabira ta nuna hassadarta da ganin sayayya da Mallam Umar yayi musu. Don ko dubawa batayi ba.

Mallam Umar ya toshe kunnansa daga surutan mutanen kauyen, Wanda tunda maganar zai auri Hajara ta fito ake tayi, kullum baya Rasa mutanen da zasuyi sallama dashi suna bashi shawarar Kada ya sake ya auri Hajara me zaiyi da ita.Amma ya toshe kunnansa ya ki sauraran kowa.

Hatta Yan'uwansa sai da suka zo suka same Shi Akan Basu yarda da aurensa da Hajara ba. Nan ma ya nuna musu ya Riga ya zartar da hukunci Kuma bazai tashi daga Kan alkawarinsa ba . Hakan shine dalilin da suka rabu baram baram.
A Daren ranar ne Kuma mahaifiyarsa Ande Dije ta Kira Shi suka zauna ta dube Shi sosai tace " ni dai dalilin da Ka gaya min na auren yarinyar nan Bai kwanta min ba. Allah ya sani Bana son yarinyar nan Bana son hada komai da ita, ". Malllam Umar yace " Ande , kinfi kowa sanin matsalolin da nake samu da duk matan da nake aure, asalima kinfi kowa sanin babu wata mace a kauyen nan da take son ta aure ni saboda lalurata, shine dalilin da yasa na ce bazan Kara yin

aure ba,"

Ya Kara kallonta yace " ita kuwa duk da tasan matsalata ta amince ta aure ni" Ande Dije tayi tsaki tace " to ba dole ta yarda ba tunda tasan babu Wanda zai iya aurenta a kauyen nan" yace " duk da haka dai kamar yadda kike ganin nayi Mata halacci haka itama tayi min halacci ta hanyar yarda ta aure ni".

Ande Dije tace " ni dai Bana Sonta Bana son auren nan Ka hakura kawai". Cikin damuwa Mallam Umar yace " shikenan naji Ande ,Zan fasa aurenta amma Kuma ni bazan Kara yin aure ba har kasa ta nade idan kin amince da hakan shikenan ".

Ande Dije tayi masa kuri da Ido , sannan tace "Ta Yaya zaka ce ba zaka Kara yin aure ba , bayan Auren shine cikar kamalarka, a irin shekarunka ta yaya zaka ce Kai da aure har abada", shima ya dubeta yace " saboda babu wacce zata yarda ta zauna da Wanda ba zata iya haihuwa dashi ba, ni Kuma babu wacce Zan Kara rufema sirrina na aureta bata San gaskiyar komai ba, na Kuma San babu wacce zata yarda ta aure ni matukar tasan Bana haihuwa ". Ande Dije tayi shuru alamun nazari, hakan yasa Mallam Umar ya cigaba da cewa " kinga sai yadda ta kwashe da aurena na karshe irin bakar tijarar da Ramatu tayi mana , da irin fallashe sirrina da tayi cikin mutane,Amma ita Hajara ta Sani duk da haka Kuma ta amince zata aure ni, to me zai hana mu karbi Hajara ga ta marainiya bata da kowa , ".

Ya Kara dubanta yace " yarinyar nan abar tausayi ce, kuma yadda mutanen gari suka dauki lamarinta ba gaskiya ba ne ....?.

Ta daga masa " Kada kayi wani kokarin kareta, dominba Zan taba gamsuwa ba , kamar yadda bazan taba Sonta ba, amma duk da haka ba ni da wani zabi da ya wuce na yarda Ka aureta, sai dai nasan surutan mutane ma kadai ya ishe mu ,". Cikin matukar Jin dadin amincewarta yace " babu ruwan mu da surutan mutane , tunda ba mutane bane zasu tsara mana yadda zamu tafiyar da rayuwar mu, duk Kuma Wanda ya daka ta mutane to babu abinda zai yi".

Ta tabe Baki tace " Kai Kuma taka kaddarar ta aure a haka ta zo maka, Allah ya kyauta ya Baka ikon cinye jarabawar".

Tunda Mallam Umar ya Samu ya shawo Kan mahaifiyarsa, shikenan ya Kara fita batun duk surutan da mutane suke yi. Ko da zai tura neman aurenta duk yan' uwansa kin zuwa sukayi, sai liman ne ya je ya Nemo masa auren Hajara a wajen Mallam kallah.

Shi Kansa Mallam kallah ya rasa wace hau ce ta hau Mallam Umar da zai auri Hajara. Da shekarunsa da komai ya manyanta balle ace yarinta ce ke damunsa. To koma dai menene ya ji dadin hakan tunda lokacin da Hajara zata bar masa gidansa ya zo. Itama sabira ta ji dadin hakan domin dai gara Hajara ta bar Mata gida Dama batun yau ba ta gaji da Zama da ita.....

TO BE CONTINUE

DAGA TASKAR YAR GIDAN IMAM

NI MA MATARSA CE
NA
HABIBA ABUBAKAR IMAM
(YAR GIDAN IMAM)
BABI NA ARBA'IN DA BIYU
****

Wata daya kawai aka sa bikin Hajara . Haka zalika Mallam Umar Shi yayi Mata komai na daki dai dai karfina, hakan kuwa ba karamin karama Hajara kaunarsa yayi ba, ta yarda duk duniya bata da gata sama da Mallam Umar.

Mallam Umar a wañnan lokacin Yana da rufin asiri tunda Yana Dan bubbuga kasuwancinsa. Abubuwa da yawa basa masa wahalar yi.

Hakan yasa bai sami wata damuwa ba wajen tafiyar da komai na bikinsa da Hajara ba. Hatta daurin auren babu Wanda ya halarta sai tsirarun mutane da mafi yawanci ma Basu da alaka da Mallam Umar. Liman ne ya daura auren .

Daker sabira ta bi umarnin Mallam kallah ta raka Hajara gidan aurenta, tana kaita Kuma ta bar gidan. Awannan ranar Hajara tayi kuka kamar idonta zai fita taga ràshin gata yadda akayi bikinta ko bikin yar tsana ce sai haka, rasuwar mahaifanta ta dawo Mata sabuwa, tayi rashinsu matuka da gaske.

Hajara ta dauki dammarar yi ma Mallam Umar dukkan biyayya tare da mutunta Shi, domin Shi kadai gareta yanzu a duniya. Hakanne yasa duk musgunawa da Ande Dije ke yi Mata ita da yarta bai taba damunta ba. Domin dai tun zuwanta gidan Ande Dije ta maida ta tamkar baiwa komai itace take yi agidan babu Kuma yabawa ko darajawa. Ande Dije mulki take Kuma dole Hajara ta dinga bin duk abinda take so. Idan ma akwai abinda ke damun Hajara to bai wuce kiyayyar da Ande Dije ta dorama muhseena ba domin ko kusa da ita bata son ta je, bata daukarta bata kulata tsakaninsu sai kyara da mugayen maganganun da Hajara bata kaunar ta dinga yinsu Akan yarta da bata da laifin komai.

Duk da haka Mallam Umar Yana cike da damuwar abinda Ande ke yi ma su Hajara a kullum Yana kokarin fahimtar da ita ta dauki Hajara a matsayin ya muhseena Kuma a matsayin jika Amma taki. Bashi da yadda zaiyi tunda Uwa ce dole tasa sai dai ya dawo wajen Hajara yayi ta bata hakuri tare da nuna Mata ta dinga Kau da kanta akan komai wata Rana sai labari.

Hajara ta kanyi murmushi tace " Ka daina damun kanka domin ba ni da damuwa, na dauki Ande a matsayin Uwa ta don haka babu abinda zata min na ji haushinta, ai Nama gode data yarda Ka aure ni. Irin wadannan kalaman nata Suna karama Mallam Umar kaunarta da ganin mutuncinta. Ya dauki dukkan hidimar muhseena komai Yana yi Mata ga wani irin so da yake Mata har cikin jininsa Yana Jin tamkar Shi ya haifi muhseena bai wasa da duk abinda ya shafeta, duk da kullum yayi hidimar sai Ande ta ci masa mutunci amma baisa ya daina yin

abinda yake yi ba, domin ya riga ya daukar ma Kansa alkawarin Kula da muhseena a matsayin ya.

Cikin ikon Allah a kwana a tashi shekarar muhseena hudu, a lokacin Mallam Umar ya hadu da ibtila'in karayar arziki duk kasuwancinsa yayi kasa a hankali a hankali kamar wasa komai ya kakkabe ya zamana bai da komai. Alokacin komai ya Fara musu wahalar Samu tun daga Kan abinci har sauran abubuwan more rayuwa komai ya tsaya cak!.

To fa nan Ande ta Kara daukar kiyayya ta dorama Hajara domin acewarta Hajara ce mai farar kafa don Mallam Umar ya aureta ne ya tsiyace, ai daman tasan ba zata taba Zama alheri ga danta ba, ko tsakar gida daker Hajara ke fitowa saboda tsabar masifar Ande Dije, duk yadda Mallam Umar ya so ya fahimtar da ita komai da ga Allah ya ke babu hannun Hajara acikin karayar arzikinsa to fa Ande taki fahimta ko Kuma ta fahimta amma kiyayyar Hajara ta hanata ganin hakan.

Tun daga wannan lokacin har zuwa yanzu Mallam Umar cikin fafutukar rufama Hajara da muhseena asiri yake. Satittika sun shige cikin watanni , watanni sun shige cikin shekaru har zuwa girman muhseena tamkar zaa manta da labarin Hajara amma ina tunda muhseena ta Girma itama ake jifanta da Kalmar shegiya. Da Kan Shi Mallam Umar ya sa Hajara tayi masa alkawarin ba zata taba gaya ma muhseena cewa ba Shi ba ne mahaifinta ba.

Haka zalika iya wadannan shekarun har yanzu Hajara bata Kara Jin duriyar Alh ba balle Haj sun bace bat, babu su babu labarinsu.

****

Hajara ta numfasa gami da goge hawayen da ya dade Yana zuba Mata , ta dago ta dubi Kabir da muhseena gaba dayansu kuka suke sosai.

Ta jinjina Kai tace " wannan Hajarar ba wata ba ce illa ni, muhseena Kuma ba wata ba ce illa ke" ta nuna muhseena da hannunta.

Muhseena ta Kara fashewa da kuka Mai karfi , wani abu ne ya ke yi Mata yawo a cikin zuciya , kamar yadda ta ke Jin tamkar jinin jikinta Yana tafasa,kanta ya cigaba da Sarawa sosai.
Hajara ta dubi Kabir da yake kokarin tattara natsuwarsa waje daya tace " Kabir Ka ji gaskiyar magana akan muhseena, haka zalika ina Mai Baka shawarar Ka hakura da muhseena domin bana fatan muhseena ta shiga rayuwar kunci da takura a gidan aurenta, don ina son muhseena tayi aure a gidan da zaa karbeta da daraja ba tare da kallon ita wacece ba".

Ta Dan gyara zamanta tace " Na so ace mahaifanka sun yarda da muhseena, amma tunda Basu aminta da ita ba dole za kayi hakuri da ita duk da kafi kowa cancantar Ka aureta".

Kabir ya numfasa yace " Inna na gamsu da labarinki na Kuma yarda da duk abinda kika fada, na Kara Jin son muhseena da tausayinta a raina fiye da kullum, amma ba ni da yadda zanyi Bani da karfin hali kamar Mallam Umar ta yadda Zan bata da kowa a Kan muhseena kamar yadda ya bata da kowa a kanki, amma Allah ya sani son muhseena ina kaunarta rashinta

Kuma agare ni ba karamar masifa ba ce, amma babu yadda na iya sai dai Zan cigaba da roko da bin mahaifana har su amince".
Hajara ta girgiza Kai tace ," ba zasu yarda ba Kada Ka bata ma kanka lokaci, kayi kokarin cire ta kawai a ranka, Kuma ba Zan taba mantawa da dawainiyar da kayi da mu ba Ina fatan Allah ya baka wacce ta fi muhseena ".

Tana Gama fadin haka tayi saurin tashi ta fita daga dakin.
Kabir ya zubama muhseena Ido wacce bakinta ya rufe ta kasa cewa komai ita kadai tasan halin da take ciki.

Ya Kira sunanta a hankali ta amsa ba tare data kalle Shi ba.
Yace " kiyi hakuri kowa da irin kaddararsa a rayuwa don haka kema ki dauka wannan itace kaddararki, Kuma ki sani dukkan tsanani Yana tare da sauki babu Kuma wani abu da yake dauwama, hakuri Kuma shine matakin nasarar ko wane bawa".
Haka Kabir ya cigaba da yi Mata nasihohi ,Amma har yayi ya gama muhseena ta kasa cewa uffan tana zaune ne dai kamar gunki.

Fahimtar da yayi muhseena ba ta tare da Shi , yasa yaga kysutuwar ya bata fili ko ta Samu ta fito daga tashin hankalin data fada. Asanyaye cikin yanayi na damuwa ya fito daga dakin , zaune Kan tabarma ya tadda Hajara ya fito da kudi daga aljihunsa ya tsuguna a gabanta ya aje kusa da ita ya Kara da cewa " gobe Zan koma kano, sai ki cigaba da yi mana adduar Allah ya daidaita yasa mahaifana su amince da muhseena" ta Dan yi wani bushasshen murmushi Wanda kasan sa damuwa da tashin hankali ne kwance. Tace " Nagode Kabir, Allah ya kaika lafiya, ya Kuma zaba maka abinda ya fi alheri". Ya amsa da " Amin" sannan ya Kara Mata sallama ya tafi.

Wani abin mamaki Yana fita ya tadda Mallam Umar zaune Kan dankalin kofar gidan yanayin zamansa da alama ya dade zaune a wajen.
Mallam Umar ya waiwayo ya dube Shi yace " Kabiru kun gama?", Kabir yayi saurin risinawa ya gaishe shi. Mallam Umar ya cigaba da dubansa fuskarsa cike da damuwa yace " Tun alokacin da Hajara take baku labari na shigo , Bana son na ji komai ne yasa na fito na cigaba da Zama a waje" ya Kara kallonsa yace " duk arayuwata babu abinda na tsana sama da wani ya ce ba ni ne mahaifin muhseena ba, saboda ita din ya ta ce babu Kuma abinda zai kankare hakan saboda haka kaima ina son Ka cigaba da dauka a haka, lokuta da yawa ina Jin ràshin jindadi Akan ràshin goyon bayan da mahaifiyata bata ba ni ba na barin garin nan bayan aure na da Hajara saboda ta haka ne kadai ba zaa bijiro da irin wannan maganar agaban muhseena ba, mu je can mu rayu inda ba'a San mu ba, amma mahaifiyata ta ki yarda da hakan".

Kabir ya numfasa yace " A yau na Kara ganin kima da darajarka fiye da ko yaushe, Allah yayi maka sakayya da alheri da irin hidimar da kayi" ya gyara tsugunonsa yace " Na so a ce ina da irin jarumtarka da babu Wanda zai hana ni auren muhseena" malllam Umar ya ce " ko yanzu ina son kasama ranka duk abinda Allah yayi dai dai ne, Kuma babu jayayya tsakaninka da mahaifanka, wuce Ka tafi dare yayi".

Kabir ya Mike Yana gaya masa gobe zai koma Kano, nan ma yayi masa fatan alheri su kayi sallama ya tafi zuciyarsa cike da tausayin muhseena da Hajara mara misaltuwa.

Har ya koma gida bai Sami wata nutsuwa ba, ya so Kara yin maganar da mahaifiyarsa amma ganin yadda bata bashi fuska ba yasa ya hakura. Washegari kuwa tun safe ya shirya zai tafi.

Mallam Hamza wanzami ya zuba masa Ido Yana hango tsantsar damuwa da ràshin nutsuwar atare da Shi, ya numfasa yace " Kabiru Kada Ka taba dauka damuwarka ba damuwar mu ba ce, Allah ya sani da Zan iya hakura na taushi zuciyata Ka auri yarinyar nan da nayi amma maganar gaskiya bazan iya bata zuriata ba da abin da nasan bazai taba gogewa ba, don haka kayi hakuri ga Mata nan da yawa sai wacce Ka zaba kaje Allah ya zaba maka mafi alheri agareka". Kabir ya bude bski zai yi magana yayi saurin ce masa " Bana son wata magana data shafi wannan yarinyar Ka rufeta Ka manta da ita Ka je kayi harkar gsbanka domin Bana Jin a kwai wata magana da zaka Gaya min ko kasa a gaya min wacce zata sani na amince da bukatarka".

Ya Kara yi masa kallon tsaf yace " matukar ni na haifeka na datse dukkan wata alaka da ke tsakaninka da wannan yarinyar Bana sin Ka Kara min maganarta kamar yadda Bana son Ka Kara zuwa yanzu in da ta ke". Kabir bai fita da ga cikin tashin hankalin da ya Kara fadawa ba , daga can bakin Kofa muryar Hafsatu ta Kara dakan dodon kunnansa tace "Nima a matsayina na mahaifiyarka na haramtaka cigaba da Hulda da muhseena da gidansu domin babu abinda tarihi ya manta don haka Bana son Ka shiga mummunan tarihin wannan bakar zuri'ar, Ka je Ka Nemo yarinya yar asali yar mutunci". Cikin nauyin zuciya da fitar kwalla kamar ba namiji ba Kabir yace " Na so ace kun fahimce ni amma babu yadda zanyi don bazan iya tsallake duk sharadin da kuka gindaya min ba, sai dai Ku sani ba ni da halin cire muhseena a cikin zuciya ta domin wannan ba yi na ba ne yin Allah ne, amma Zan nisanceta kamar yadda kuka min umarni ". Komai kekashewar zuciyarka sai Ka ji tausayin Kabir yadda yayi wujuga wujuga da yadda yanayinsa ya kasance. Yana Gama yi musu wannan bayanin ya Ciro kudi masu yawa ya aje musu ya juya yayi musu sallama ya tafi, cikin matukar tashin hankali, ya so ya Kara ganin muhseena kafin ya bar garin to amma babu halin hakan domin Shi Kansa yasan cigaba da kusantar muhseena zalincine a gareta domin idan ya cigaba da kusantarta yasan babu yadda zaayi ta fita daga cikin kuncin rashinsa ko mantawa da Shi , don haka ya Zama tilas ya nisanceta . Fitar sa Hafsatu ta numfasa ta dubi Mallam Hamza tace "Mallam , yaron nan yayi nisa Ina Jin tausayinsa matuka araina, don haka ina ganin dole a hada da Nemo masa rubutun dangana ko Allah yasa ya yi dangana ya manta da wannan bakar dagar yarinyar da Bana ko son tunawa da ita". Mallam Hamza yace " Ni Kaina nayi tunanin hakan , bazan yarda yarinyar nan ta sabauta min rayuwar da ba babu gaira babu dalili, Dan da nake mora fiye da kowa, don haka ina fita Zan Sami Mallam zangija nayi masa bayani idan rubutun danganar zai masa duk yayi kawai," haka suka zauna suna cigaba da tattaunawa a tsakar gidan.

Kishiyar Hafsatu sahura ta fito daga dakinta da alama duk abinda suke tattaunawa tana jinsu, ta dube su tace " Ni ko Mallam banga illar goyama Kabiru baya ya auri yarinyar nan ba, tunda Yana sonta ina ganin tamkar an shiga rayuwarsa idan aka raba Shi da ita", Hafsatu tayi Mata wani irin kallo cikin fusata tace " Allah sarki, ai da yake ba ke kika haife Shi ba , da ace Hassan ne ai da Baki Fadi haka ba, sai kace ba ki San yarinyar da ake magana akai ba", sahura ta

jinjina Kai tace " Allah ya Baki hakuri bana nufin abinda kika fada, da Kabiru Kuma da Hassan Duka yayana ne babu wani bare acikinsu, kawai dai ina gaya muku gaskiya ne" Mallam Umar yayi Mata wani irin kallo yace " To mun ji gaskiyar mun gode Kabiru Kuma ba zai aure ta ba komai runtsi komai wuya". Fahimtar da tayi maganar tana so ta dawo wata iri yasa ta wuce kiciñ wajen girkinta ba tare da ta Kara yin magana ba.

Tabangaren muhseena kuwa, sosai ta Kara sa ma kanta hakuri, domin labarin mahaifiyarta yayi sanadiyyar data ji karfin guiwa kwarai da gaske,

Domin tasan cewa ko rabin kwatan halin kunci da tashin hankalin da mahaifiyarta ta shiga ita bata shige shi ba, ta Kara tausayama mahaifiyarta kwarai babu Kuma abinda wani zai Kara fada Akan mahaifiyarta da zai dameta. Kamar yadda son ta da son kyautata Mata ya Kara cika zuciyarta, Karo da dama Kenan da ta ji tana son Zama wata a rayuwa saboda ta jiyar da mahaifiyarta dadin da ko wace uwa take mafarki daga danta.A wannan lokacin ta Kara Shan alwashin sai ta Zama abar kwatance na alheri a kauyen Durmi Saita binne tarihin mahaifiyarta da kyakkyawan misali.

Kamar yadda ta gefe daya kima da kaunar Mallam Umar ya Kara kama ta , shine mahaifinta bata da wani uba sama da Shi , babu Wanda zai amsa sunan mahaifinta bayan Shi. Za Kuma tayi komai domin ganin ta Zama ya ta gari a gare Shi zata Zama sanyin idaniyarsa.

TO BE CONTINUE

DAGA TASKAR YAR GIDAN IMAM

NI MA MATARSA CE
NA
HABIBA ABUBAKAR IMAM
(YAR GIDAN IMAM)
BABI NA ARBA'IN DA UKU

****

kwarai matuka idan muhseena tace ràshin Kabir bai taba rayuwarta ba, hakika tayi karya sosai take Jin rashinsa , sai dai dole tasan zata sa ma kanta hakuri da dangana ta yarda da kaddararta.

Haka zalika ta jidadin hukuncin da Kabir ya dauka na nisantarta, kamar yadda ya gayá Mata a waya, bayan komawarsa, sai dai duk da haka akai akai abokinsa ya Kan kawo Mata sakon kudi ko kayan bukata, bata son Kabir ya cigaba da hidima da ita amatsayin tausayi don haka ta sanar da Shi bata bukatar komai ya dakatar da hidimar da yake yi, Wanda su kansu su Mallam Umar din sunga dacewar hakan.

Ko ya aiko da kudi ta daina Karba, gaba daya so ta ke ta manta da Shi duk da kullum zuciyarta cikin damuwa da ràshin nutsuwa ta ke, sai dai tana kokarin boyewa saboda bata bukatar aikata duk wani abu da zai zamo karin damuwa ga mahaifanta.

****

Tabangaren mujaheeda da Taufiq kuwa Zama dai ya yi dadi, abubuwa da dama sun canja tunda itama mujaheedan ta canja sosai son Taufiq ya rinjayi izza da son ranta. Tana kokarin bin duk abinda yake so.

Sai dai har yanzu ragamar kulawa da Shi ta na nan ahannun masu aiki, har yanzu bata San ta girka abinci don mijinta ya ci ba, ràshin yi Mata magana ko Kuma nuna baya jindadin hakan yasa har yanzu mujaheeda bata fahimci tana aikata kuskure ba. Ita kuwa Haj murjanatu shurun da ta ji na zaman lafiyar da Taufiq da mujaheeda su ke yi tayi zaton aikin Mallam ne ya ci kamar yadda ta ke zaton aikin Mallam dinne ya mallaka Mata nata Mijin.

Haka zalika ta wajen aikin mujaheeda duk wani tuggu da kulle kulle Alh jibrin yayi domin ya ga aikin ya fita ran mujaheeda, amma babu wani cigaba da yake samu hatta murtala da ya ke Goya masa baya ya fahimci babu wata nasara da zasu samu, hakanne yasa ya zage ya koma wajen mujaheeda Yana cigaba da biyayya da neman fada. Shima Àlh jibrin din hakanan ya hakura Yana cigaba da adduar Allah ya kawo sanadiyyar da mujaheeda zata bar aikin da kanta.

A cikin haka ne mujaheeda ta Fara laulayi , gwajin farko likita ya tabbatar Mata da tana dauke da ciki harna wata biyu.suna hanyar dawowa daga adibitinne murna da farinciki gun Taufiq ba'a magana, sabanin mujaheeda da gaba daya fuskarta da yanayin ta ya canja tunda likita yace tana da ciki babu wani alamun farinciki a fuskarta, har suka Kai gida duk irin maganganun farinciki da Taufiq ya ke yi baisa tace uffan ba. Isar su gida ne hakurin Taufiq ya gaza ya dubeta sosai yace " Ni banga alamun farinciki ba atare da ke, duk da irin wannan gagarumar kyautar da Allah ya bamu". Mujaheeda ta dan muskuta ta gyara kwanciyar ta akan gado fuska ba yabo ba fallasa tace " hmm ni fa yaya Taufiq ban shirya haihuwa yanzu ba, asalima ni ban taba kawowa araina wai Zan haihu nan ta kusa ba" ya kafe ta da kallon mamaki sannan yace " Dama haihuwar shirya Mata ake ? Ban fahimce ki ba fa" tayi masa kuri da Ido tace " Shi yasa nake son Ka fahimce ni yanzu" ta yunkura cikin ràshin karfin jiki ta zauna tana kallonsa tace " ina son kayi hakuri a cire cikin nan, domin bazan iya ba , Ka duba Kaga ni yadda na fita hayyacina Bana jindadin komai ga ciwon da ban ma gane Kansa ba, wannan cikin zai tsayar min da abubuwa da dama a rayuwata, don haka don Allah Ka barni na cire Shi ".

Tsananin mamaki da bakincikin maganganunta suka baibaye Taufiq, ya dubeta sosai Ido cikin Ido yace " mujaheeda anya kuwa kina so na?", Ta dube Shi da sauri tace " Ni ko na ke son Ka , wannan wace irin magana ce yaya Taufiq?". Ya girgiza Kai yace " idan har da irin wannan tunanin a ranki to ki Sani ni bakya so na, duk abinda kika fada na game da son da kike min karya ne, don idan kina Sona da Baki kyamaci hada jini da ni ba", tayi saurin cewa " Ya zaayi na kyamaci hada jini da Kai bayan na riga na hada rayuwata da taka, kawai dai ina son Ka fahimce ni , kayi min Kuma Uzuri, ina son na haihu da Kai amma ba yanzu ba.....?

Bata karasa abinda take fade ba, Taufiq ya juya a fusace ya fice da ga dakin cikin matukar bacin rai.Bai taba zaton Jin abinda ya ji daga mujaheeda ba, haushinta da haushin maganganun ta yake sosai.

Tun daga wannan ranar wata sabuwar fitinar ta kunno Kai tsakanin Taufiq da mujaheeda.

Domin dai dagaske take bata son cikin bata son haihuwa yanzu Shi Kuma Yana son cikin Yana kuma son haihuwa yanzu. Haj murjanatu kuwa tsabar son rai da son zuciya da Kuma soyayyar mujaheeda data makantar da ita bayan mujaheeda ta bi duk da itama can karkashin zuciyarta tana da bukatar Samun jika daga mujaheeda to amma tunda mujaheedar bata so itama bata so.

Ranar farko da Haj murjanatu ta shiga cikin maganar, ta nuna ma Taufiq menene don an cire wannan cikin bayan gaba Allah zai bata wani. Cikin fusata Taufiq yace "Wane garanti gareta na Allah zai bata cikin alokacin da take so bayan Shi ya bata alokacin da yake so tace bata so, Bana son mu Sami gagarumar matsala akan wannan maganar domin babu Wanda ya isa ya cire min ciki, me kuka dauke ni ne sakarai Wanda baisan ciwon Kansa ba ko me?" Ya tashi cike da fushi yace " Ina son Ku sani ni ba bawanku bane , na Kuma San darajata da yancina don haka duk Wanda ya taba min ciki ko waye Shi sai munyi Shari'a da shi "

Yana Gama fadin haka Bai saurari komai ba ya fita daga falon,

Yana dukan iska, Bai taba Jin zafi da damuwa akan duk abubuwan da suke biyo bayan aurensa ba irin wannan.

Haj murjanatu ta jinjina Kai ta kurama mujaheeda Ido tace " mujaheeda Taufiq ba bazai taba yarda da abinda kike so ba, " mujaheeda ta numfasa cike da damuwa tace " Ni Kuma mummy Allah ya sani Bana son haihuwa yanzu, gabana har faduwa yake yi idan na tuna wai ina da ciki, amma kwata kwata yaya Taufiq ya ki fahimtata".

Haj murjanatu tace " bazai fahimce ki ba,". Sosai Haj murjanatu ta Fara tunanin ko dai asirin da malllam yayi ya Karye ne domin ba tayi tsammanin irin wannan kafiyar daga Taufiq ba.

Wannan Karon Kuma mujaheeda ba zata iya zuwa wajen surikinta da wannan maganar ba Wanda tasan shine zaisa Taufiq yayi Mata abinda take so.

Ràshin jituwa ta Sami matsuguni tsakanin Taufiq da mujaheeda.Babu wani kwanciyar hankali, ko gidan Taufiq baya son ya dawo.

Aikin hanyar da kamfanin su Taufiq ya ke yi, yayi nisa, anyi canjin ma'aikata Taufiq Yana daya daga cikin wadanda aka tura cigaba da yin titin kauyen Durmi.

Cikin lokaci kankani Taufiq ya gama shiri. Saura kwana biyu ya tafi ranar a gidansu ya uni har dare tare da iyayensa domin dai yasan idan irin wannan aikin ya taso yakan Dade Bai dawo gida ba, tun Kuma bayan aurensa bai je irin wannan aikin ba. Sai dare da zai dawo yayi musu sallama, kamar kullum sunyi masa fatan alheri da fatan dawowa lafiya.

A Daren ranar har sun kwanta, ya kasa jurewa ya tashi ya zauna gami da kunna wutar dakin, Yana kallon gefen da mujaheeda take kwance ya Kira sunanta a hankali, ta dan motsa a hankali sannan ta amsa.

Yace " ki tashi ina son yin magana da ke".

Ta dan yi Jim kafin ta motsa sosai ta tashi ta zauna tana kallonsa Wanda rabon da ta kalli fuskarsa haka ta kwana biyu.

Tace " ina jinka", ya jinjina Kai Yana kokarin gyara zamansa.

Sannan yace " Ina son mu kawo karshen wannan matsalar da take neman ta rushe duk wata soyayya da jituwa da ke tsakaninmu".
Tace " Ni ban dauki wannan abin amatsayin abinda zamu zauna mu rasa kwanciyar hankali saboda Shi ba, Kai ne Ka dauka da zafi".

Ya jinjina Kai yace " Bana son wata magana kawai ina son ki sauka daga wannan akidar ta ki, kiyi hakuri mu rungumi kyautar da Allah yayi mana muyi masa godiya"
Mujaheeda tace " Ka kasa fahimtata yaya Taufiq,...?.

" In dai akan wannan ne bazan taba fahimtar ki ba,kawai ina son ki cire tunanin cire cikin jikinki domin wannan cikin shine farincikina" shuru kawai tayi bata Kara magana ba, har ya cigaba da maganganunsa masu kama da nasiha.
Daga bisani yace " jibi Idan Allah ya kaimu Zan tafi aiki daya daga cikin hanyoyin da kamfaninmu yake aiki, Kuma Zan dauki lokaci ban dawo ba,"

Ya dubeta sosai yace " saboda haka ina son ki Kula da kanki da abinda ke cikin ki don Allah ".
Tace " Allah ya kaimu" tana fadin haka ya juya ta kwanta abinta ba tare da nuna wani alhinin rabuwa da Shi ba.ya Dade zaune kafin shima ya kwanta amma ya kasa runtsawa matsalolin da ke cikin aurensa sun ishe shi.

Ko ranar da zai tafi ba wani sakin fuska ko wata kulawa da ya Samu daga mujaheeda.Hakanan ya tafi, zuciyarsa a jagule tunaninsa na ga cikin jikinta Yana adduar Allah ya tsare masa cikinsa.
TO BE CONTINUE

DAGA TASKAR YAR GIDAN IMAM

NI MA MATARSA CE
NA
HABIBA ABUBAKAR IMAM
(YAR GIDAN IMAM)
BABI NA ARBA'IN DA HUDU
****
Bayan isar su wajen aikin hanyar, dole kauyen Durmi suka karasa shi da sauran kananan ma'aikata Yan'uwansa domin neman dakin da zasu kama haya, domin bazai iya Zama a filin da aka Dan gine ma ma'aikatan ba a bakin hanya.

Taufiq tare da abokan aikinsa guda uku da Suma suke son Samun daki a garin .

Suka shiga cikin kauyen a motar Taufiq. Fitowar Mallam Umar Kenan da ga masallaci sallar la'sar duk da an Jima da kammala sallar yayi zamansa a masallacin bai fito ba sai yanzu biyar saura na yamma.

Taufiq ya tsaida motar a gaban Mallam Umar gami da Bude kofar motar ya fito cikin cikar

Kamala yayi masa sallama.
Mallam Umar ya dakata Yana amsa sallamar gami da Mika masa hannu sukayi musabaha.

Sannan Taufiq yace " Mu baki ne, muna daya daga cikin masu aikin hanyar da ake , mun zo ne da bukatar Samun gida ko dakunan da zamu zauna na haya, don Allah idan kasan yadda zaayi mu Samu to muna neman taimakon Ka".
Fara'ar fuskar Mallam Umar ta Kara fadada yace " Aah masha Allah , sannunku da zuwa,ai mun jidadin yin hanyar nan saboda matsalar mu Kenan tunda ake dimukuradiyya bamu taba Samun tagomashinta ba sai yanzu" Taufiq yace " Allah sarki, Dama ai hakane".

Mallam Umar yace "Akwai wani gidan haya, amma tunda Ku baki ne ba zaku iya ganewa ba , saboda haka mu je na Kai Ku".

Cike da jindadin yadda Mallam Umar ya tarbesu Taufiq yace " To mun gode Allah ya saka da alheri".

Daganan Mallam Umar ya shige mota, Yana yi musu kwatance har gidan Alh sabitu, me kudin garin Durmi Kenan shi kadaine yake da gidan haya agarin, sai yadda ya so yake yi .

Mallam Umar bai tafi ba sai da ya hada su Taufiq da Alh sabitu, sannan yayi musu sallama ya tafi bayan Taufiq yayi masa godiya mai yawa.

Sun Sami dakuna agidan Alh sabitu, ganinsu Kuma daga birni ga Kuma aikin da suka zo yi yasa ya tsauwala kudin duk da haka sun Karba.

A ranar Taufiq har katifa ya saya sauran kayan bukatun da zai nema ya bari sai ahankali.

Muhseena dai tuni ta tursasama kanta hakuri da dangana akan ràshin Kabir, ta yarda komai na Allah ne sai dai bata Jin zata Kara Samun wani da zai dauki kaddarar aurenta idan Kuma haka Allah ya tsara Mata babu yadda zatayi.

Haka zalika kullum tana adduar Allah yasa yadda ta sa hakuri da dangana akan lamarin , Allah yasa shima Kabir ya sama Kansa hakan , duk da ta Dade bata ji daga gare shi ba, tun sakon kudin daya turo Mata na karshe ta Kira Shi akan Kada ya Kara aiko Mata da ko wane sako saboda bata San wane irin alaka bane atsakaninsu yanzu,
Bayan nan aranar ta rufe nambar sa daga kiranta.saboda tana son ta mallaki natsuwarsa gaba daya tana Kuma son ta manta da Shi ta daina ma tunaninsa domin ta hakane kadai zata iya mantawa da Shi.

Ita kanta Hajara kullum addu'ar ta bai wuce Allah ya kawo ma muhseena Miji Nagari ba Wanda zai iya aurenta a yadda take ya Kuma Kula da ita cikin tausayi da Jin Kai.

Mujaheeda ta cigaba da Zama da cikin da Sam Sam bata son haihuwarsa. Zuciyarta na

yawan saka Mata ta zubar da cikin amma Kuma tana tunanin irin matakin da Taufiq zai dauka akanta idan hakan ya kasance .

Domin dai iya fushin da zatayi da Taufiq tasan tana sonsa so na hakika , ba Kuma zata iya rabuwa da Shi ba akan ko wane dalili.

Hakan ne yasa ta kasa yarda ta bi abinda zuciyarta ta ke gaya Mata. Ita kanta Haj murjanatu ta fahimci ta na dai Goya Mata baya ne kawai saboda taga abinda take so kenan ba wai don ranta na so na hakika ba.

Tun tafiyar Taufiq babu wata wayar kirki da suke yi, domin ko ya Kira sai ta ga damar dauka ita Kuma bata kiransa . Fushi take sosai da Shi. Duk da Shi burinsa kullum shine ya Kira ya ji lafiyar cikin jikinta.

Tabangaren Taufiq dai sosai yake Jindadin zaman kauyen Durmi. Duk da babu wani abu na more rayuwa to Yana matukar jindadin halayen mutanan garin na son bako tare da nuna tarbiyyar yaransu , Yana sha'awar yadda yake ganin yaran kauyen suna zuwa makarantar islamiya domin duk yamma idan ya dawo daga wajen aiki nan yake lalacewa a kofar gidan Yana kallon yadda yaran kauyen suke dawowa daga islamiyya.

Yauma kamar kullum Taufiq Yana zaune a kofar gidan, aka taso Yara Yan islamiyya kowacce na kokarin wucewa idanunsa na kansu.

Dammm gabansa ya Fadi sosai asanadiyysr hada Ido da muhseena da yayi, Wanda ya rasa dalili illa dai ya ji wani abu ya tsurga masa tun daga Kansa har zuwa Yan yatsun kafarsa.

Hakanan ya ji ya kasa dauke idanunsa daga muhseena. Harta fahimci hakan ta dan dube Shi sosai irin kallon da ya tsareta da Shi ne yasa bata San lokacin da ta gaishe shi ba, da sauri ya amsa yana cigaba da kallonta .

Hakanne yasa muhseena tayi saurin barin wajen .

Amma Taufiq ya kasa dauke kallonsa daga gareta harta bacema ganinsa, amma wani abin mamaki Shi Kansa idan an tambaye Shi dalilin kallon da yake Mata da Kuma dalilin Jin sauyin da ya ji atare da Shi to fa shi Kansa bai sani ba.

Hakanan tun daga wannan ranar Taufiq ya dorama Kansa bai tashi a inda yake har sai yaga wucewar muhseena.

Fahimtar hakan da tayi ne yasa gaba daya ta canja hanya ta daina biyowa ta hanyar da zata ga Taufiq,

Domin dai bata San dalilin wannan sa idon da yake Mata ba.

Yau kusan kwana biyar Kenan Taufiq bai Kara sa muhseena a idanunsa ba. Bai Kuma San dalilin da yasa ya ji ya damu da hakan ba, akai akai Kuma tunanin ta yake fado masa .

Kabir dai ya takurama Kansa ta hanyar yin hakuri da muhseena domin bin umarnin iyayensa duk da ji yake kamar zai mutu.

Baya farinciki baya shiga jama'a Yana neman ya sama Kansa ciwon damuwa.

Kullum Alh Musa Yana nuna masa babu abinda ya gagari ubangiji, don haka yayi ta addua , tunda da dai ya fi kowa sanin mahaifansa ba zasu taba yarda da bukatarsa ba.

Hakanne yasa Kabir ya dage da addua ya maida komai ga Allah, ya Kuma yarda yayi ràshin masoyiya, wacce har abada bazai taba mantawa da ita ba .

Makonnin Taufiq hudu a Durmi. Ranar wata laraba wacce muhseena ba zata taba mantawa da ita ba acikin tarihin rayuwarta.

Tun safe ta ke Jin irin ciwon kan da take yi Wanda yake matukar gigitata.

Duk da haka tayi kokarin tafiya islamiya saboda bata son ta zauna a gida, ko da ta je islamiyyar shima bata wani samu sukuni ba kallo daya zaka mata Ka gane cewa bata da lafiya, duk idanunta sunyi jajir haka zalika dishi dishi take gani.

Daya daga cikin malamin islamiyyar su ne ya Lura da halin da take ciki.

Hakanne yasa ya bata izinin tafiya gida.

Ba tayi masa musu ba , saboda itama tasan jarumtarta ta kusa gazawa sosai take Jin kamar zaa cire Mata rai saboda azabar ciwon Kai .

Tana tafiya rike da littafan makarantarta,cikin yanayi na jigata bibbiyu take gani. Bata da zabi da ya wuce ta bi ta hanyar da ta daina bi adalilin tafi sauri akan waccan hanyar da take bi, domin ta kosa kwarai ta Karasa gida saboda ta kusa sarewa.

Tafiya kawai take bata San inda take jefa kafarta ba. Dai dai lokacin gaba daya muhseena ta ji ganinta ya yaye duniyar na juya Mata.

Lokaci daya ta sulale kasa, bata Kara sanin inda kanta ya ke ba.

Tana nan gefen hanya har Yara sun Fara taruwa.

Dai dai lokacin motar Taufiq ta taho da nufin zuwa gida ganin Yara zagaye da wata mace yasa yayi gaggawar karasawa kofar gidan yayi parking din motarsa ya fito da sauri ya nufi wajen.

Gabansa yayi mummunan faduwa a lokacin da yayi Ido biyu da yarinyar da kusan kullum sai yayi tunanin inda zai Kara ganinta.

Ya duba duk babu wata mace ko wani babban namiji awajen da zai Taya Shi taimakama muhseena.

Hakan tasa Bai saurari komai ba ya sa hannu ya dauki muhseena cancak cikin tsuma da damuwa gami da tashin hankali.

Kai tsaye cikin gidan ya wuce da ita , ya Bude dakinsa ya shiga da ita ciki ya kwantar da ita akan katifar dakin.

Ya rasa wane irin taimako zai bata, don haka ya shiga dibar ruwa Yana zuba Mata a fuska.

A hankali ta dan Bude idonta amma har alokacin bata San inda take ba.

A lokacin da Taufiq ya shigo da ita gidan akan idon abokin Mallam kallah ne, Mallam Hakilu ya shawo kwana Kenan abinda idonsa ya gani kawai Taufiq ne dauke da muhseena ya shige da ita cikin gida.

Cikin tsoro da fargaba ya wuce da sauri kamar zai fadi saboda sauri. Kai tsaye gidan Mallam kallah ya wuce.

Ya dinga kwala sallama. Sabira ta dubi Mallam kallah tace "'kai jama'a wanene wannan yake kwala irin wannan sallama kamar yaki".

Mallam kallah ya amsa sallamar shigowarsa kenan gidan.

Yadan saki tsaki yace " ina Zan San waye, nagaji Hutu kawai nake bukata" tace " Ai sai Ka leka Ka gani".

Ya wuce ya fita, ya Sami Mallam Hakilu cikin kaguwa " yauwa Mallam kallah" cewar Mallam Hakilu, Mallam kallah ya dube Shi yace " Dama Kaine , lafiya ko irin wannan sallama haka".

Yace " ina fa lafiya, ina tabbatar maka tarihi zai maimaita Kansa a karkarar nan". Mallam kallah yace " Meya faru? Don Allah Ka natsu kamin bayani ".

Mallam Hakilu yace " wadannan bakin masu gyaran hanya da suke haya a gidan Alh sabitu ne na Ganshi ya dauki muhseena yar wajen Hajara ya shige da ita cikin gidan, Allah kadai yasan abinda ke faruwa yanzu atsakaninsu".

Mallam kallah ya bugi kirji ya zaro idanu waje yace " Ka tabbatar da abinda kake fade" yace "kwarai da gaske , mu je Ka gani da idonka" Mallam kallah yace " mu je mu Kara daukar wasu shaidun, abinda suke yi a birni ne zasu zo suyi mana anan to daga yau sun gama aikata hakan ".

Cikin fusata suka wuce suka tafi suna maganganu.sai da Mallam kallah ya kwashi mutane guda uku ya Kuma je ya taho da Mallam Umar Wanda tunda suka taho yake tambayar dalilin kiransa Amma Mallam kallah yace idan sun je ya gani.

Cikin daurewar Kai da fargaba Mallam Umar ya cigaba da binsu har gidan Alh sabitu, Kai tsaye suka fada cikin gidan.

Mallam Hakilu ya nuna wani daki yace " ina zaton nan suka shiga don kofar dakin ne kawai akwai takalimi da alamar akwai mutane aciki".

Cikin zafin Nama gaba daya suka rufta dakin.

Dai dai lokacin muhseena ta Fara dawowa hayyacinta tana kokarin tashi daga kwanciyar da take idanunta cike da neman Karin bayanin yadda akayi ta zo dakin lokaci daya Kuma tsoro ya mamaye ta don tsintar kanta a inda bata taba tsammani ba.
Karar shigowar su Mallam kallah ya Kara firgita muhseena.

Shima Taufiq din a tsorace ya Mike Yana kallon bataliyar mutanen da suka shigo dakin suke yi masa kallon tuhuma gami da tsana da kyamata.....!

TO BE CONTINUE

DAGA TASKAR YAR GIDAN IMAM

NI MA MATARSA CE
NA
HABIBA ABUBAKAR IMAM
(YAR GIDAN IMAM)
BABI NA ARBA'IN DA BIYAR
****

Mallam kallah ya saki salati Yana janyo Mallam Umar Yana fadin " shigo sosai Ka ga abinda yar taka take aikatawa, ai dama barewa bata gudu danta yayi rarrafe Ka dai gani ko".

Idanun Mallam Umar suka tsayu Kan muhseena wacce take ta kokarin tashi amma ta kasa.

Bakinta ahankali yake furta " Baba abinda kuke zato bashi bane, bansan Shi ba babu abinda ya hadani da Shi, Nima farkawa kawai nayi na ganni a dakin nan na rantse bansan inda nake ba".

Mallam kallah da sauran mutanen su kayi Kan Taufiq cikin fusata suna tambayar me kayi Mata ?. Ayayin da Mallam Umar jiri ya shiga dibarsa yayi saurin jingina da jikin bango.

Cikin tashin hankali Taufiq ya Fara kokarin kare Kansa Amma mutanen gurin sun hana Shi damar yin hakan .

.maimakon hakan ma sai ingiza keyarsa sukayi cikin fada da karaji.mallam kallah ya dubi Mallam Umar yace " mun wuce wajen megari kana iya taho da muhseena itama, domin ba zamu taba barin wanna shegantakar ba , abinda su keyi a birni ne zasu zo suna mana a kauye, idan bamu dauki mataki ba duk a haka zasu Gama bata mana yaran kauyen".

Yana Gama fadin haka ya bi bayan su Mallam Hakilu Yana cigaba da fada da sababi.

Sai bayan tafiyar su ne Mallam Umar ya zubama muhseena Ido ,Yana kokarin lafarma da zuciyarsa radadin da take.

A sanyaye ya Matso kusa da yarsa idanunsa jajir saboda damuwa, yace " muhseena ki ji tsoron Allah ki gaya min gaskiyar abinda ya faru makaranta kika tafi ta yaya kika kare anan?, Ina da kyakkyawan zato akanki Bana Jin zaki iya aikata abinda bai kai wannan ba balle wannan al'amarin da kika fi kowa sanin illarsa ta yaya kika shigo dakin nan".

Ta kasa tsaida hawayen da tuni ya ke zuba Mata ta dube Shi sosai cikin zubar hawaye tace"Dana aikata abinda ake zargi na rantse Baba gara na mutu, domin idan akwai abinda na tsana arayuwata to zina ce, don Allah Ka yarda da ni bansan lokacin da na zo dakin nan ba bansan komai ba,".

Ta cigaba da kuka tana fadin "Ràshin lafiyar da na tashi da ita tun safe ce ta matsa min a makaranta na kasa sukuni shine Mallam ya Bani izinin komawa gida, to ina cikin tafiya bansan inda Kaina yake ba na dai ji na daina gani daganan ban Kara Jin komai ba ban Kara sanin komai ba sai farkawa nayi na ganni a wañnan dakin wannan mutumin ya na shafa min ruwa a fuska ".

Mallam Umar ya dade Yana kallon gaskiyar zancen ta a cikin kwayar idonta, yasan yarsa yasan halinta hakika yasan ba zata taba aikata abinda ake zarginsu da aikatawa.kamar yadda yake ji aransa Shi Kansa Taufiq din ba zai aikata wannan ta'addancin ba ga muhseena.

Domin tun haduwarsu ta farko Wanda daga Shi ba su Kara haduwa ba ya gamsu da natsuwa da kamalar yaron.

Ya dubi muhseena jigatar ciwo ta bayyana sosai a fuskarta . Yace " ki yi shuru ki daina kuka na yarda da duk abinda kika gaya min domin nasan ba zaki taba yi min karya ba".

Ta Kara fashewa da kuka tace " na ji saukin damuwata Baba tunda Ka yarda da ni duk abinda wani zai dauka bazan taba damuwa ba,"

Mallam Umar ya umarceta da ta kokarta ta tashi su tafi. Daker ta iya tashi suka tafi alokacin sauran masu hayar gidan suka Fara dawowa duk Wanda ya wuce sai ya juyo ya Kara kallon su muhseena.

Mallam Umar ya fahimci muhseena tana cikin jigatar ciwo da yayi niyyar su wuce gida amma ya ji tsoron sharrin su Mallam kallah hakan yasa su Ka wuce wajen megari.

Suna zuwa daker muhseena ta samu waje ta zauna jiri na kwasar ta. Sun tadda takaddama da hayaniya tayi yawa daker megari ya samu su kayi shuru.

Zuwa lokacin duk inda ran Taufiq ya Kai to fa ya baci sosai ya Fara Jin danasanin taimaka ma muhseena da yayi haushi da takaicin yadda mutanen garin ke kokarin Dora masa mummunan zargin da Bai aikata ba Bai da wata niyya da ta wuce na taimakon muhseena.

Amma ana neman a dora masa mummunan kazafin da zai iya bata dukkan wani kyakkyawan halinsa. Haka zalika mutanen garin kokarin dole sai ya yarda ya Kuma karbi lefin da bai aikata ba.

Taufiq yayi gaggawar kallon muhseena yace cikin daburcewa da damuwa " ke bauwar Allah ki Fadi tsakani da Allah nayi miki wani abu" da sauri ta girgiza Kai tace " Bansan komai ba saboda bana cikin hayyacina amma nasan koma meye ni babu abinda ya shiga tsakanina da Kai ,".

Mallam Hakilu ya daka Mata harara yace " ke da Allah can , ai dama dole ki Fadi haka saboda ki Kare barnar da kuka aikata, to Baki isa ba babu Wanda ya isa ya zo garin mu ya cimu da yaki".

Mallam Umar ya daga masa hannu yace " Don Allah Ku bar wannan maganar Ina son na Kai yata asibiti saboda bata da lafiya, duk Kuma wannan maganganun da kuke yi babu gaskiya a cikinta abinda muhseena da Taufiq suka fada gaskiya ne na Kuma yarda na gasgata su".

Taufiq ya lumshe idanunsa saboda dadin maganar Mallam Umar, domin duk wajen Shi kadai ne ya Fadi abinda yake son ji.

Mallam kallah ya sakar ma Mallam Umar wata irin harara, sannan yace "Don Allah Mallam Ka

dawo hayyacinka lokaci yayi da zaka daina mara ma mara gaskiya baya harka bashi mafaka, kana kokarin boye gaskiya Ka tusama mutane karya a zukatansu kamar yadda kayi alokacin matsala irin wannan ta mahaifiyarta, Ka dage dole saika wanketa Akan laifin da ta aikata, to ayau ba zamu yarda ba".

Ya juya ya dubi megari yace " megari kaji koken mu Ka taimaki mutanen garinka , Ka taimaki tarbiyyar yayan mu, kayi hukuncin da muka roka kawai wannan yaron ko yaki ko ya so sai ya auri yarinyar nan a yanzu ba sai anjima ba domin ta hakane kadai zamu kawo karshen wannan keta haddin da mutanen birni sukema yayanmu domin idan aka barshi na rantse sun dinga cigaba da aikata hakan Kenan yanzu kuwa idan akayi hakan zai Zama ishara ga masu son aikata hakan nan gaba".

Nan da nan muhseena taji ta wartsake daga ciwon da take yi, domin Jin wannan maganar me kama da mafarki a daura musu aure? Ta tambayi kanta.

Mallam Umar ya dubesu yace " wace irin magana ce wannan". Taufiq shima ya Kara gyara tsugunonsa cike da tashin hankali yace " Ta yaya Zan auri yarinyar da ban sani ba babu wata alaka a tsakaninmu".

Megari yayi masa wani kyakkyawan kallo yace " Rufe min baki mugu, babu wata alaka atsakaninku amma aka tsintota a dakinka, maganar banza kawai wa zaka maida kananan Yara, ". Ya juyo itama muhseena ya watsa Mata harara yace "Wa zai karbi shaidarki bayan bakinku daya meya kaiki dakinsa idan ba dama kun Saba aikata Masha'a ba, idan an tura ki makaranta sai ki wuce dakinsa ko, ai Baki yar akasa ba".

Mallam Umar ya ce" megari kayi ma maganar nan kyakkyawan bincike...? Kafin ya karasa magana megari ya katse shi " kaima ban son Jin komai daga gareka saboda yarka zaka kare, ni nine Zan yanke hukuncin da ya dace Kuma dole abi abinda na zartar".

Zuwa lokacin kuka muhseena take me karfin gaske tana rike da kanta tana fadin " innalillahi wainna'ilaihirrajiun". Shi Kuma Taufiq gaba daya gumi ya Gama jike masa Riga ya Fara tunanin wace mahallaka ya kawo Kansa wace irin kaddara ce yau zata fada masa.

Ya daga idonsa gefensa mutanen gari ne daya gefen ma haka dukkan su a fusace suke sosai yake ji aransa babu abinda ba zasu iya yi masa ba.

Daker ya Bude Baki yace"Don Allah Ku yi hakuri na rantse babu abinda ya shiga tsakanina da ita taimakonta kawai nayi"
Itama cikin kuka tace "Nima na rantse babu abinda ya shiga tsakanin mu don Allah Kada Ku yi mana mummunan hukunci". Mallam kallah ya daka Mata harara yace " ki rufe min Baki ko na zuba Miki Mari".

Megari yace " fito da kudin aljihunka" cikin tsuma ya sa hannu a aljihu ya fito da duk kudin jikinsa kusan nera dubu talatin, megari yayi ma wani dogari umarnin ya amshi kudin ya Mikama Mallam Umar.

Cikin sanyin jiki ya amshi kudin Yana juya su alamun neman Karin bayani.

Megari ya dubi Taufiq yace " matanka nawa?", Cikin rawar murya yace"Matata daya". Megari ya dawo da kallonsa ga Mallam Umar yace " wannan kudin sadakin yarka ne,". Taufiq da Mallam Umar da muhseena suka zaro Ido cike da gigita kafin daya daga cikinsu ya yi magana, megari yace "Jama'a ni megari nine Zan Zama waliyyin wannan bakon Mallam Umar Kuma zai Zama waliyyin yarsa, ga shaidu ga kowa yanzun nan zamu daura auren su".

Gaban muhseena yayi dam ya Fadi gaba daya ta rikice ta rasa a wace duniya take cikin kuka take fadin " Baba Ka taimakeni Kada Ka bari su kashe min rayuwa, ta yaya Zan auri mutumin da ban San wanene shi ba"
  Shima Taufiq din gaba daya rikicewa yayi yace " ta yaya zaku hukuntani da wannan mugun al_amarin bayan ba ni da laifi taimako kawai nayi".

Mallam Umar ya wuce a sukwane gaban megari Yana cewa " Kada Ka min haka megari yata tana da gaskiya kamar yadda bakon nan ya ke da gaskiya ba ko wane Dan birni bane yake da mugun Hali Kada Ku sabauta rayuwar yayan nan".

Mallam kallah yace " haba Mallam umaru gata fa zaayi ma yarka, yanzu kana tunanin ko babu abinda ya shiga tsakanin muhseena da Taufiq, akwai wani da zai iya auren muhseena bayan bakin fentin da ke shafe a jikinta sannan ta Kara da wannan Kuma to waye zai aureta, Kuma bayan haka lalle Bama son yayan mu su cigaba da ganin mummunar tarbiyyar da wata kila su yi tunanin Fara bin irin tarbiyyar".

Gaba daya mutanen wajen suka dauka " Kwarai da gaske mun gaji da irin wannan rayuwar muna neman canji ,dole ya aureta Kuma ya dauke mana ita agarin ".
 Daker megari ya sassauta hayaniyar da ake yi a wajen.

Wanda zuwa lokacin Taufiq ya kusa shidewa a zaune saboda tsabar tashin hankali. Haka itama muhseena ta fada mugun tashin hankali mara misaltuwa.

Wanda bai sa megari ya fasa abinda yayi niyya ba domin Mallam Umar Yana ji Yana gani bashi da yadda zaayi haka aka daura auren Taufiq da muhseena.

Tashin hankali Wanda baa sa masa rana. Gaba daya Taufiq ji yayi kamar an dora masa dala da goron dutse turus yayi akasa kamar bashi da laka.

Megari ya dubi Taufiq yace " ci da sha da sutura da wajen Zama da kula da lafiya da iliminta duk ya rataya a wuyan Ka , don haka idan ka tashi tafiya zamu tabbatar da Ka tafi da matarka".
  Taufiq ya kasa magana kawai ji yayi hawaye Yana fita a idonsa.
 Ayayinda mutanen gurin kowa sai murna da son barka yake yi tare da jinjina ma hukuncin megari . Sosai suke Jin da wuya akara Samun wani me tsaurin idon da zai Kara aikata abinda Taufiq da muhseena suka aikata. Ahankali kowa ya Fara watsewa.

Amma Mallam Umar ya kasa motsa ko da kafarsa , sai alokacin ya Lura da muhseena ta sulale

kasa sumammiya a gigice ya yo kanta Yana Kiran sunanta a firgice.
TO BE CONTINUE

DAGA TASKAR YAR GIDAN IMAM

NI MA MATARSA CE
NA
HABIBA ABUBAKAR IMAM
(YAR GIDAN IMAM)
BABI NA ARBA'IN DA SHIDA
****

Amma ina muhseena ta riga ta fita hayyacinta ta Suma bata San Wanda ke kanta ba.
Mallam Umar ya cigaba da girgiza muhseena, shima megari ya taso ya taho , Amma wani abun mamaki Taufiq mikewa yayi ya Mata kallon tsaf ya juya zai tafi ba tare da nuna damuwarsa ga halin da take ciki ba.

Da sauri megari yayi masa tsawa yace " dawo ina zaka Maza Ka zo ba matarka bace ai ance kana da mota Ka dakko motar Ka kaita asibiti tun kafin kaga fushi na".
Cikin tsabar takaici da tsanar muhseena da lokaci daya ya ji ya na neman ya baibaye masa zuciya.

Ya juya ya ya tafi dakko motar ba tare da ya ce komai ba.

Duk suna Kan muhseena har Taufiq ya dawo da motar ya dauke su zuwa asibiti daya kwal na garin . Harda megari aka tafi asibitin sai da aka bata gado aka tabbatar ta dawo hayyacinta saboda taimakon gaggawar da aka bata sannan megari ya dubi Taufiq da har zuwa lokacin bakinsa Bai furta komai ba.

Yace "Komai na hidimar asibitin Yana hannun Taufiq amatsayinka na mijinta ya Kuma Zama dole Ka Kula da lafiyarta har Allah ya bata lafiya, Ka kuka da kanka idan Ka Saba wannan tsarin,"
Ya Kara kallon yadda Taufiq duk yayi wujuga wujuga ya fita hayyacinsa yace " Garama Ka karbi wannan auren hannu bibbiyu domin ba auren wasa bane zahiri ne wannan, muhseena matarka ce, Kuma ba zamu lamunci duk wani abu da zakayi Wanda ya sabama aure ba, Ido Kuma Yana kanka Baka Isa kabar garin nan ba tare da matarka ba kafin Kuma Ku tafi Kaine zaka cigaba da daukar dawainiyar Komai nata".

Ya Kara kallonsa yace " Mu Yan kauye ne Amma munsan girma da martabarmu duk Kuma Wanda yace zai sabama dokar mu to hukuncinsa bazai yi kyau ba".
Shi dai babu abinda ya ce Yana tsaye tamkar gunki, zuciyarsa na tukuki sosai yake son ya fitar da hawaye saboda ya Sami saukin tashin hankalin da yake ciki.

Wanda yafi daukar lamarin tamkar mafarki. Daga bisani megari yayi sallama da Mallam Umar ya fice.

Mallam Umar ya dago Yana duban Taufiq da yanayin tashin hankalin da yake ciki, Karo da dama tausayinsu gaba daya ya Kara kama Shi, tun ganinsa na farko da Taufiq ya ji ya kwanta masa arai saboda ya yarda da Kamala da mutuncin da yake kwance akan fuskarsa. Ya so kwarai alokacin yayi masa magana amma ya kasa ya bari tukuna a samu natsuwa,

Kamar yadda shima Taufiq din ya kasa yin magana.

Ko da zai bar asibitin baiyi ma kowa magana ba ya tafi.

Bai Jima da barin asibitin ba Hajara ta shigo asibitin cikin matukar gigita.

Duk iya yadda Mallam Umar ya so ya shawo kanta ta daina kukan da take to fa abu ya fassakara.

Kam ta kama muhseena ta rungume tun dawowar muhseena hayyacinta sai yanzu ne itama ta fashe da kuka Mai matukar karfi harda gunji,cikin jigata take fadin " Inna rayuwata ta kare tawa kaddarar ba irin taki bace,Inna an aura min mutumin da bansani ba bansan ko Shi waye ba bansani ba ko zai iya rayuwa da ni, Inna babu komai acikin kwayar idanunsa sai tsanata".

Hajara ta Kara kwakume yarta kamar zata tsaga jikinta ta maida ta ciki.

Tace " kiyi hakuri Allah zai dube ki muhseena zai kawo Miki sauki domin dukkan tsanani Yana tare da sauki".

A hankali Mallam Umar ya dubi Hajara da take gaba daya a birkice sannan yace " Ya akayi kika ji? Waye ya gayá Miki?".

Ta juyo cikin hawaye tana kallonsa tace " Baba kallah ne ya zo har gida ya sanar da ni , to na tafi gidan megari anan ake Gaya min ta Suma kun taho da ita asibiti, Mallam wannan wace irin masifa ce?".

Mallam Umar cikin tsananin bakinciki yace "Ki natsu don Allah Hajara komai Yana da iyaka, kibar wannan maganar har sai mun koma gida".

Hajara tayi shuru ba ta Kara maganar ba , amma duk da haka hawayenta ya kasa tsayuwa ita da muhseena kuka suke sosai Wanda yin hakanne kadai yake Dan lafar musu da damuwar.

Tun komawar Taufiq gidan yake zaune adakin cikin matsanancin bakincikin da bai misaltuwa , tunda yake ko a tarihi bai taba ganin mahaukacin kauye irin wannan ba.

Yanzu shikenan matansa biyu, dam! Kirjinsa ya buga ya Kara firgicewa saboda tuno mujaheeda da mahaifiyarta da yayi hakika babban tashin hankali ne a gabansa tashin hankalin da yafi Wanda yake ciki a yanzu.

Ta yaya zaayi masa haka, zaa sa Shi abinda baiyi niyya ba. A hankali zuciyarsa ta cigaba da kokarin Dora masa tsanar muhseena.

Ko a mafarki bai taba tsammanin wannan mummunan abin zai faru da Shi ba, hakika zuwansa Durmi masifa ne yayi danasanin zuwa. Shin yaya zaiyi ta ina zai bulloma wannan gagarumin al'amarin.

Gaba daya ji yake kamar Yana zazzabi jikinsa ya dauki zafi sosai.Abokin aikinsa salisu ya fado dakin a gigice Yana kallonsa yanayin da ya ganshi ciki ne ya tabbatar masa da gaskiyar abinda ya ji, ya zube gabansa Yana kallonsa fuska a dame yace "Da gaske ne Kenan abinda naji " ya dago fuska sharkaf da zufa yace " har kaji Kenan?" Ya jinjina Kai yace "Na ji, wai menene ya faru haka"?

Cikin tsabar tashin hankali ya Gama gaya masa komai.
Ya Kara da cewa
"Itace yarinyar da nake
Gaya maka ina yawan ganin wucewarta islamiyya daga baya Kuma na daina ganinta
Ranar da Kuma
Na tashi ganinta yau Kenan shine wannan masifar ta afka mun".
Salisu ya cije lebe yace "Amma mutanen nan Basu da mutunci sun Raina maka hankali wannan abu sai kace a littafi, yanzu to meye abin yi".

Taufiq yace " Na rantse maka ina cikin tsaka me wuya Nima bansan ya zanyi ba na rasa wane irin tunani zanyi".

Salisu yace " Tikisa, babbar magana lalle Kam kana cikin tsaka me wuya auren da babu shiri babu so ko Kauna, wannan shine asalin auren dolen"
Taufiq ya numfasa gami da rike Kansa yace " jama'ar kauyen nan na tabbatar Basu da hankali babu wani hukunci da na isa na yanke idan ba na yarda da wannan auren ba domin sabanin hakan babu abinda ba zasu iya yi min ba na rantse maka tsoronsu ma nake ji".

Salisu cikin damuwa yace "Gaskiya kana cikin jarabawa Allah ya kawo maka mafita.

Ya kwantar da Kansa Akan cinyoyinsa Abu goma da ashirin ga matsalar mujaheeda da har yanzu baida tabbacin zata yi hakuri ta bar cikin jikinta ga wannan auren da baisan yadda zaiyi da Shi ba,
Domin dai yasan ko ya sha giyar wake ne babu yadda zaayi ya gayá ma mujaheeda ya Kara aure da ga kawai ya zo yin aiki Durmi.
Yayi Imani duk bayanin da zai Mata ba zata taba gamsuwa ba shin yaya zaiyi?, Ko guduwa zaiyi? To idan na ya gudu wadannan fitinannun mutanen kauyen ai sai sun Nemo Shi.
Ya rasa dalilin da yasa Kuma can kasan zuciyarsa yake Jin damuwar ciwon da muhseena ta ke yi. Sai dai duk da haka baya son ganinta.

Bai koma asibitin ba har washegari ana Shirin sallamarta ya fado asibitin ,lokacin Mallam Umar Yana ta kokarin bada kudin asibitin acikin irin kudin sadakin da Taufiq ya bayar.
Amma sai Taufiq ya dakatar da Shi yace zai je ya biya, Ido kawai ya bishi da Shi kamar yadda Hajara da muhseena suka bishi da Ido har ya bace ma ganinsu.
Hajara ta dawo da kallonta ga Mallam Umar tace " shine Mijin nata",
Ya gyada Kai ahankali alamar eh, ta aje numfashi, aranta tasan baida wani makusa Amma

waye Shi? Sannan wace irin rayuwa zata yi tare da shi?, Shin yarta zata samu farinciki atare da Shi?.
Tunanin hakan yasa Hajara faduwar gaba me tsanani.ita Kam muhseena tana runtse da Ido ita fa hatta tunani ma ta rasa ta kasa gane ta ina zata Fara duk karfin halinta ji tayi tana neman ta sare.

Bayan ya dawo daga biyan kudin asibitin, hakanan ya ji bazai iya tafiya ba har sai ya maida Su gida. Cikin natsuwa ya gaida Hajara Mallam Umar ya dube Shi yace "Itace mahaifiyar muhseena".

Dama yaga alama domin tashin hankalin da ke Kan fuskarta sai Uwa.

Har ya dauke su zuwa gida bai ko kalli inda muhseena take ba ballefa ya tambayeta jikinta.

Yayi nufin Yana ajesu ya tafi Amma sai Mallam Umar ya nemi alfarmar ya shigo Yana son yin magana da Shi.

Kwarjinin da Mallam Umar yayi masa ne yasa ya kasa yi masa musu ya bishi zuwa cikin gidan.

Suna shiga Ande Dije ta dubi Taufiq Yana kokarin gaisheta ita Kuma tana sakar masa tambayar "Kaine Mijin muhseenar?",

Ya kasa bata amsa domin baisan abinda zaice mata ba.

Mallam Umar ne ya amsa da "shine".

Kafin ta Kara wata magana yayi masa umarnin shiga dakin. Adole ya shiga Hajara ta shimfida masa tabarma ta koma Kan katifar da muhseena take kwance ya zauna cike da damuwa da fargaba.

Mallam Umar ya zauna a gefen tabarmar da Taufiq ke Kai.sun Dan Jima babu Wanda ya iya yin magana kafin daga bisani Mallam Umar ya Dan gyara zamansa yace "Taufiq da farko Zan Fara da Baka hakuri Akan duk abinda ya faru, domin idan kowa bai yarda da Ku ba to ni na yarda da Ku, duk da Kai ban San Ka ba haduwa ce kawai mu kayi na Dan taki to na fahimci abubuwa da dama a game da Kai ciki kuwa harda cewa ba zaka iya aikata abinda ake zarginka da aikatawa ba".

Sosai zuciyar Taufiq take yin fari idan ya ji irin wadannan kalaman daga bakin Mallam Umar.

Malllam Umar ya cigaba da cewa "ita ko yata nasan wacece ita nasan irin tarbiyyar da nayi Mata don haka ko ita da kanta ta Bude Baki ta gaya min ta aikata wannan aikin Zan karyatata, kawai dai komai da sila don haka Allah ya kawo wannan amatsayin sila, saboda Dama can Allah ya Riga ya rubuta muhseena acikin Jerin Matan da zaka aura a duniya, duk da nasan ba ayi maka adalci ba".

Ya dubi Taufiq sosai yace " Amma don Allah ina neman taimako da alfarma awajenka".

Taufiq akaro na farko ya dago ya dube Shi yace "Wace irin alfarma ".

Mallam Umar yace "don Allah Kada Ka wulakanta mun rayuwar ya ta hanyar sakinta ko guduwa Ka barta, idan kayi min haka Ka kashe ni Ka sani ita kadai ce sanyin idaniyata Bana fatan wani mummunan lamari ya faru da ita, akwai dalilai da yawa da yasa muhseena take bukatar kulawa, kamar yadda akwai abubuwa da yawa da ya kamata Ka sani a game da ita

Wanda sai lokaci ya yi sannan zaka sani, yanzu dai wannan alfarmar nake so kayi min Ka taimaka min".
Ya karasa magana cikin kaskantar da Kai.

Maganganun Mallam Umar sun taba zuciyar Taufiq sune Kuma dalilin da yasa ya ji bazai iya juyama rokon Mallam Umar baya ba.

Duk da Yana cikin damuwa to fa ya hango tsantsar tashin hankali da fargaba a cikin kwayar idon mallam Umar.
Ya numfasa sannan yace "in sha Allah duk abinda Ka fada bazan aikata daya daga cikinsu ba, bazan saketa ba Kuma bazan gudu na barta ba".
Hajara bata San lokacin da ta ce "Allah yayi maka albarka ".

Ita kanta muhseenan wannan Karon tsayawa tayi tayi masa kallon tsaf. Sannan ta maida kanta ta kwantar.
Mallam Umar yace " Nagode Taufiq Allah yayi maka albarka".
Yace "Zan tafi" Mallam Umar yace " yi hakuri, ina son nasan wanene Kai ko ya ya ne ina son nasan wani abu daga tarihin rayuwarka".
Ahankali Taufiq ya gayama Mallam Umar abinda zai iya gaya masa daga cikin rayuwarsa.
Abu daya dai Mallam Umar ya yarda da Shi Taufiq ya fito daga kyakkyawar zuri'a shin. Yaya makomar muhseena zai kasance alokacin da yasan ainihin wacece muhseena.
Sosai ya ke Jin Bai kamata ya gayá mishi komai ba har sai an fita daga wannan sarkakiyar.

Daga bisani dai Taufiq yayi musu sallama ya fice ba tare da yabi ta Kan muhseena ba.

Yana fita Ande Dije ta shigo dakin tana kallonsu tace "To wannan yaro dai da ganinsa na Dan gidan kananan mutane bane don haka wannan karfa karfa da akayi masa nasan iyayensa ba zasu taba yarda ba balle Kuma su San muhseena bata da uba to fa nayi Imani ko sun karbeta sai sun rabata da dansu, sannan yaya zatayi Zama da kishiyarta tunda ance Yana da Mata, na rantse muhseena ta debo ruwan dafa kanta".
Mallam Umar yace " Don Allah Ande kiyi hakuri ki barmu haka, mu ji da abinda ke damunmu na roke ki Kada ki Kara mana damuwa akan wacce Muke da ita".

Ta tabe Baki tace " umm gaskiya ce dai bakwa so Kuma ita Zan cigaba da gaya muku".

Babu Wanda ya Kara tankawa hakan yasa ta fice tana maganganu.
Sai alokacin Hajara ta dago ta dubi Mallam Umar tace cikin sarkakiyar murya " Mallam Taufiq dan jigawa ne,Bana son muhseena ta yi rayuwa a wañnan garin shin wace kaddara ce kuma take bin muhseena".
Ya fada hawaye na tsiyaya akuncinta, kamar yadda itama muhseena ta Kara fashewa da kuka ko a mafarki bata son ta ji an ambaci jigawa.

Mallam Umar ya saki ajiyar zuciya ya dubi Hajara yace "ki fauwalama Allah komai domin jikina

yayi sanyi Allah kadai yasan dalilin hada auren Taufiq da muhseena ".
TO BE CONTINUE

DAGA TASKAR YAR GIDAN IMAM

NI MA MATARSA CE
NA
HABIBA ABUBAKAR IMAM
(YAR GIDAN IMAM)
BABI NA ARBA'IN DA BAKWAI
****

Taufiq ya rasa inda zaisa Kansa ya jidadi, kamar yadda baya iya bacci baya iya sakin fuskarsa.

Kallo daya zakayi masa Ka tabbatar Yana cikin matsananciyar damuwa tare da tashin hankali. Gaba daya zaman kauyen ya dame Shi.

Ko waya yake yi da mujaheeda gaba daya sai yaji ya daburce ya rasa abinda zai ce. Hakan yasa har fargabar yin waya da ita yake .

Haka zalika zuwa lokacin babu Wanda baisan abinda ya faru ba a kauyen.

Surutu Kala Kala mara dadi.

Kowa yake yi har tsohuwar maganar rayuwar Hajara sai da ta dawo sabo a kauyen ,gaba daya sun rasa inda zasu sa kansu . Musamman Mallam Umar da yake fita kullum. Domin dai tuni muhseena ta daina zuwa ko da islamiyya, Ga ciwo da ya sata a gaba duk ta rame ta kanjame saboda damuwa.

Ko Taufiq yayi niyyar ba zai je ya dubata ba, to fa yakan rasa dalilin da yakansa ya ji ya kasa hakuri, dole sai ya je ya duba yanayin jikinta.

Duk da ko ya je din babu wata magana da take hadasu da ya wuce ya jiki tace da sauki, daga nan basa Kara tankama juna har ya tafi.

Sai dai Yana kokarin biya duk wani kudin maganin da muhseena take sha.

Badon megari yasa asa masa Ido ba, a'a sai don kawai yayi ra'ayi , Kuma hakanan yake matukar Jin tausayin mahaifiyarta saboda wani irin kallo da akullum take masa idan yaje me kunshe da sakonni Kala Kala.

Wannan aure ne me cike da al'ajabi.

Taufiq ya rasa ya zaiyi ranar da duk ya tashi tafiya, shin zai gudu ne ko zai tafi da ita?.

Wannan tambayar da ita yake kwana yake tashi a ransa, Amma har yanzu ya rasa amsa.

Ta bangaren muhseena dai ta riga ta sallama rayuwarta ta yarda duk abinda ya faru da ita daga Allah ne.

Sai dai hakan bai hana

ta yima kanta fatan mutuwa ba kullum, domin a yanzu gaba daya bata son rayuwar gara ta mutu ta huta mahaifanta ma su huta da bakinciki ta dalilinta kullum.

Duk da tun faruwar al'amarin kullum Mallam Umar da Hajara suna Kan kwantar Mata da hankali, to fa ta kasa Samun nutsuwa tunda Suma Basu da nutsuwar balle kwanciyar hankali.

Sosai Hajara ta Kara ramewa, saboda damuwa, hatta Ande Dije duk mugun halinta wannan Karon ta yi shuru da bakinta daga furta munanan kalaman da ta Saba, masu Kara Haddasa damuwa a zuciyoyinsu.

Zukata dai duk sun Baci rayuwa tayi tsauri a wajen muhseena da Taufiq.Tun bayan da muhseena ta warware gaba daya sai Taufiq ya dauke kafafunsa a gidan.

Sam hakan Bai damu muhseena ba , Amma ya damu iyayenta. Wannan Karon sosai Mallam Umar yasa Ido akan Taufiq domin ji yake tamkar bazai rike alkawarin da yayi masa ba, Yana ganin kamar guduwa zaiyi ya bar muhseena Wanda yin hakan shine zai Kara kassara rayuwar yarsa Kuma bazai taba barin hakan ya kasance ba.

Watanni uku cif Taufiq yayi a garin Durmi, akayi canjin ma'aikata domin an Gama da hanyar Durmi za"a cigaba da yin wata hanyar.

Alokacin fargabar Taufiq tafi ta kullum bacci ya gagare shi.

Shin yaya zaiyi da muhseena? Tambayar da yayima salisu Kenan.

Salisu ya numfasa Yana kokarin karasa shirya jakarsa,yace " To yanzu dai yadda mutanen kauyen nan suka sa maka Ido babu yadda zaayi Ka hudu kabar kauyen nan ba tare da muhseena ba, abinda Kamar wuya".

Taufiq ya dafe Kansa da yake Sarawa yace " Amma kasan babu yadda zaayi naje gida da ita amatsayin matata ko, domin yin hakan tamkar lasisin rabuwa da matata ne, Kai ni bansan ma yadda zanyi ba".

Salisu yace " kasani ne, Ka tafi da ita bayan kunje kasan yadda zaayi Ka Sami wani waje da zaka ajeta, daga bisani kawai Ka saketa kaga batasan gidan Ka ba balle bayan kun rabu ta dawo kauyensu ace zaa biyo Ka inda kake aci mutuncinka, ni shawarata Kenan, domin dai kasan babu ta yadda zaka iya barinta a garin nan".

Sosai shawarar salisu tayima Taufiq.

Ita Kuma ya dauka, zai nemi inda zai aje ta yadda babu Wanda zaisan abinda ke tsakaninsu. Domin kuwa Shi Kansa salisun sai da ya gargade shi akan yabar maganar nan anan Kada su je da ita ko da office, Suma sauran abokan aikin nasa duk sai da ya ja kunnansu.

Amma saboda tsabar wukakanci Taufiq bai sanar da muhseena da mahaifanta batun tafiyarsu jigawa ba sai Daren da gobe zai tafi, sannan ya je gidan.

Yayi sa'ar Samun Mallam Umar a kofar gida Yana shirin shiga gida.Taufiq ya same Shi da maganar tafiyarsu gobe.

Ko gidan bai shiga ba bayan daya gaya masa ya juya yayi tafiyarsa.
A sanyaye Mallam Umar ya shiga gidan tun da ya zauna akan tabarma a waje ya kasa tabuka komai da ya wuce tagumi hatta tuwon darensa da Hajara ta aje masa ya kasa budewa balle ya ci. Damuwa ce fal a zuciyarsa da fuskarsa.
Hajara ta zauna a gefensa gami da Karo hasken fitilar Kwan da ke aje asaman tabarmar.
Sannan ta dube Shi tace " Mallam me ke faruwa ne naga duk ka canja ne". Ya dan numfasa sannan yace "Ina muhseena ", tace "Tana daki tana karatu" yace "Kira min ita".

A hankali ta Mike ta shiga daki ta kirata, muhseena ta rufe kur'anin cikin nutsuwa ta tashi taje ta aje a maajiyarsa, sannan ta fito.
Itama gefen tabarmar ta zauna, tace "Gani Baba".
Ya dubeta damuwarsa ta Kara yawa yace "mijinki yazo yanzun nan kafin na shigo gida, ya sanar da ni wa'adin aikinsa ya kare a garin gobe kuma zai koma don haka gobe zaku wuce tare zuwa jigawa".

Dam! Gaban Hajara da muhseena ya Fadi nan da nan suka daburce.
Hajara ta dube Shi Ido jajir tace "Yanzu Mallam goben nan muhseena zata barmu, babu wani shiri, zata mu barta ta tafi da mutumin da bamu San waye ba baya ga sanar da mu tarihinta bamu San komai ba akan zuriarsu".
Hawaye ya Fara zuba a kuncin muhseena ta Dora kanta a Saman cinyoyinta tana Jin tamkar zuciyarta zata fashe.
Mallam Umar yace "To yanzu me ye abin yi?Hajara barin yaron nan ya tafi ba tare da muhseena ba babban gangancine a garemu domin Yana iya idan ya tafi ya ki dawowa duk da ina kyautata masa zato, Kuma Karin wasu surutan zamu samu a kauyen nan da duk yanzu Ido ya Kara dawowa kanmu".
Hajara tace "To yanzu meye abin yi Mallam".
Ya nisa yace "abin yin Kenan muyi hakuri mu barshi ya tafi da ita, zamu karbi nambar wayarsa idan komai ya lafa daga bangarensu zamu neme Shi mu je mu ga inda yar mu take, zuwa lokacin in sha Allah ubangiji ya hore min abinda zanyi Mata kayan daki, sai Kuma mu cigaba da rokon Mata Samun nutsuwa da kwanciyar hankali a duk inda take".

Ande Dije ta amshe maganar fitowarta daga daki Kenan.
Tace "Kai dai wahala ta ganka ummaru' daukar matsalar wani ta Zama taka, tunda Ka auri

Hajara Baka da wata matsala arayuwa sai tata Allah dai ya Baka lada".

Bai tanka ba illa kallonta da yayi yace "Gobe idan Allah ya kaimu muhseena zata wuce gidan mijinta tare da Taufiq ".

Ande Dije tace "Tikisa to Allah yasa su karbeta ".

Mallam Umar yace "In sha Allah zasu karbeta".

Bata Kara magana ba ta dau butarta ta shige daki ta kullo kofa.

Mallam Umar ya dubi muhseena da take ta aikin sharar hawaye, tausayinta ya Kara kama Shi ya zuba Mata Ido yace "Allah ya sani muhseena da ina da ikon canja kaddararki da tuni na canja saboda duk duniya Bani da wani abun so da kauna sama da ke, duk wadannan abubuwan da suka faru kudura ce da ga cikin kudurorin Allah babu Wanda ya isa ya canja abinda ya riga ya rubuta acikin allon kaddararki".

Yadan gyara zamansa ya cigaba da cewa "Kiyi hakuri ki bi mijinki Ku tafi ki yi ta addua ki maida dukkan lamarinki ga Allah Shi zai isar Miki daga dukkan komai, kamar yadda muma zamu cigaba da yi Miki addua za Kuma mu kasance da ke ko da bakya tare da mu".

Kuka me karfi ya Kara kwacema muhseena duk Mai tausayi sai ya ji tausayin yanayin data fada ciki.

Nan da nan itama Hajara ta shiga kuka Mai tsanani.

Mallam Umar ya koma dukkan su Yana basu hakuri.

A wañnan Daren dai yadda muhseena da Hajara suka ga Rana haka suka ga dare, saboda tsabar tashin hankali da damuwa.

Amma tun daren Hajara ta hadama muhseena duk kayan sawanta da Wanda zata bukata sai da ta cika karuwar jaka.

Washegari damuwar muhseena tafi ta kullum , don saboda kuka daker idanunta suke buduwa.

Da wuri Taufiq ya zo, Abu daya ya Kara Sagar da guiwarsa shine irin maganganun da Mallam Umar yayi masa musamman akan ya rike amanar muhseena bata da kowa a inda zasu sai Shi don haka ya Zama dole ya Kula da rayuwarta . Karo na farko kenan da kalaman Mallam Umar suka cire masa tunanin sakin muhseena bayan sun je jigawa domin irin alkawarin da Mallam Umar yasa ya daukar masa Abu ne mawuyaci ya iya karya wannan alkawarin.

Haka zalika Basu tafi ba sai da Mallam Umar ya karbi nambar Taufiq. Iya daurewarsa Kuma sai da ya zubar da hawaye alokacin da muhseena suka tafi.

Itama tayi kuka kamar ranta zai fita.saida dogaran megari suka tabbatar da tafiyar Taufiq da muhseena sannan suka koma fada suka sanar da megari.

Shi Kam Mallam Umar dakalin kofar gidan sa ya cigaba da Zama Yana sharar hawaye tare da yi ma yarsa fatan alheri a duk inda take.

TO BE CONTINUE

DAGA TASKAR YAR GIDAN IMAM

NI MA MATARSA CE

48

Tunda suka Fara tafiya muhseena take kuka a hankali me ratsa zuciya.

Tun Taufiq Yana jurewa har ya kasa domin hakanan yake Jin kukan nata har cikin kwakon zuciyarsa, duk tsigar jikinsa sai tashi ta ke yi.

Cikin wata irin bakuwar murya ya ce "Meye amfanin wannan kukan, ko kina ganin akwai maganin da kukan zaiyi Miki ne?".

Bata tanka ba ya cigaba da cewa "Ko kina ganin Zan cutar da ke ne".

Tayi kokarin dakatar da kukan da take yi amma hawayenta bai daina zuba ba.ya gyada Kansa yace "Nasan bakya Sona auren dole akayi mana duka" ta dube Shi sosai hakanan ta ji bakinta ya furta "Kaima Baka Sona ko?". Amsar tayi masa tsaurin fada domin Shi Kansa baisan amsar ba. Don haka yace "Na Sani daga ni har ke babu Mai laifi illa kaddara data fada mana Wanda babu yadda zamu yi".

Ya Kara numfasawa damuwa mara misaltuwa ce a fuskarsa.

Ya cigaba da cewa "ina da Mata tana da ciki ahalin yanzu babu yadda zaayi na iya zuwa Kai tsaye na gaya Mata cewa nayi aure domin bansan hslin da zata sa kanta ba, domin duk duniya matata babu abinda ta tsana sama da kishiya".

Hawayen muhseena ya tsaya Karo na farko kenan data zubama kyakkyawar fuskar Taufiq Ido tana Jin wani bakon al'amari da yake shiga dukkan sassan jikinta.

Taufiq yace "Dalilin hakanne yasa nayi Mata alkawarin bazan taba yi Mata kishiya ba". Gaban muhseena yayi mummunan faduwa shin wace irin rayuwa zatayi da mutumin da bata Raba daya biyu gidansa ya fi karfinsa.

A hankali tace "To yanzu ya kake son ayi, me yasa ba zaka sake ni ba Ka maida ni wajen iyaye na".

Ya girgiza Kai yace "Bazan sake ki ba," "Saboda mene?",

Ta tambaya ya Dan waiwaya ya dubeta sosai yace "Saboda nayi ma mahaifinki alkawarin bazan taba sakinki ba" tace "Idan hakane to yaya makomar rayuwata take a hannunka".

Ya yi shuru na wasu dakikai sannan yace "Har yanzu ban tsara komai akan hakan ba, shiyasa nake son ki taimake ni ki Bani hadin Kai, Zan nemi inda Zan ajeki idan mun isa jigawa ahankali idan na gama warware matsalar sai na dawo da ke gidana".

Tace "Zuwa tsawon wane lokaci Kenan".

Ya make kafada yace "Ni Kaina ban sani ba,".

Gaba daya su kayi shuru kowa da abinda yake sakawa aransa.

Ita Kam muhseena ta rasa irin tunanin da zatayi hakika ta riga ta Fara saduda da Samun rayuwar farinciki shin wace irin rayuwa ce wannan tana matsayin MATARSA amma babu damar ya nunata.

Karo da dama Kenan da tun faruwar al'amarin Kabir ya Fado Mata arai.

Da Shi ta aura da tasan tayi aure a duniya ràshin Kabir ya dawo Mata sabo . Hakika iyayen

Kabir sun taimaka wajen kassara rayuwarta domin da sun Bari ta auri dansu duk da ba taga wannan masifar ba.

Amma ba zatayi fushi da yin Allah ba.

Domin tasan ko a dade ko ajima zai dubeta da idanun rahama.

Ta hadiye dukkan damuwarta ta zaro Dan karamin kur'anin ta acikin jaka ta shiga karantawa a zuciyarta, hakanne kadai ke lafar da tashin hankalin da take ciki.

Isar su jigawa Kai tsaye Taufiq wajen cin abinci ya aje muhseena Wanda daker ta Dan ci abincin shima din saboda ya matsa mata ne.

Bayan fitowarsu daga wajen cin abinci ne ya nuna Mata Kan wani benci yace ta zauna ta Jira Shi anan .

Yace zai je ya samo inda zai ajeta tukuna sannan ya zo ya dauke ta.

Saboda yawo da ita acikin mota zai iya Zama hatsari a gare Shi domin wani Wanda ya Sani Yana iya ganinsu.

Har Taufiq ya tafi mamakin yadda wannan rayuwa zata kasance take yi Kai da mijinka amma Yana tsoron wani ya gansu tare.

To wai ita a wane matsayi ma take agurinsa?. Ta yaya Kuma take son ta tabbatar da wannan auren da baida wani takamaiman suna ko asali.

Taufiq ya Dan dauki lokaci da tafiya kafin muhseena ta Fara tunanin Anya kuwa Taufiq ba guduwa yayi ya barta ba. Hankalinta yayi mummunan tashi, ta Fara kokarin rasa tunaninta.

Cikin dimbin tashin hankali da son gasgata tunaninta ta tashi tana kokarin Jan akwatinta .

Lokaci daya ta Fara tunanin idan ba son ya gudu yake ba don me zai sauke Mata jakar kayanta?. Tabbas Taufiq bai ajeta anan don ya dawo ya dauketa ba. Shin ina zata sa kanta a babban gari irin wannan?.

Wa zai taimaketa?.

Hawaye ya Fara wanke Mata fuska tana Jan Jakarta tana sharar hawaye.

Komai na duniyar ya tsaya Mata cak!. Dai dai lokacin da take kokarin tsallake titin ne. Cikin tsautsayi wata mota ta tunkarota duk iya yadda wacce ke tuka motar ta so ta tsaida motar Kada ta taba muhseena to fa abin ya ci tura domin kuwa sai da ta bugeta.

Jama'ar wajen suka taso kowa Yana salati da kokarin taimakon muhseena wacce tuni ta sume.

Anyi sa'a wacce take tuka motar babu abinda ya sameta.

Kamar yadda babu abinda ya Sami motar.

Don haka da taimakon mutanen wajen aka Samu akasa muhseena a motar matar da gaba daya ta Gama gigicewa.

Kai tsaye wani babban asibitin kudi ta wuce da ita hankalinta a matukar tashe yake faranta daya Allah yasa ba wani mummunan abu bane ya sameta.

Tana isa asibitin aka amshi muhseena, nan da nan aka bata gado.

Aka cigaba da bata taimakon gaggawa.

Gefe daya wacce ta bugeta duk ta Kara rikicewa tana zaune Kan kujerar karfen asibitin tana kokarin Kira a wayarta.

Bugu daya acikin na biyu mahaifiyarta ta dauka.

Ta so suyi magana sosai Amma Jin muryarta cike da tsoro da fargaba ta tambayeta "yaya akayi? Kina Ina ne najiki cikin damuwa ne".

Da sauri tace " ina nan zeenat hospital wata budurwa na buge a mota ina kokarin komawa gida bayan barina nan".

Gaban ta ya Fadi tace "Subhanallah Allah yasa babu wani mummunan abu da ya same ta, me likitan yace".

Ta numfasa tace "Baice komai ba suna can tare da ita, amma dai a sume Muka taho asibitin da ita".

Mahaifiyarta ta numfasa tace "ina fatan dai ke babu abinda ya sameki ".

Ta girgiza Kai tace "Babu abinda ya same ni" tace "To gani nan zuwa asibitin".

Haka muhseena ta yi ta Kai gauro ta Kai Mari a harabar wajen.

Ta Kara daga waya ta Kira me aikinta ta sanar da ita ,

Tayi duk abinda ya dace,

Na game da abinda megidan zai ci, domin Yana hanyar dawowa . Cike da girmamawa ta amsa.

Tana aje wayar likita na fitowa.

Da sauri tayi Kansa tana tambayarsa yanayin jikin muhseena.

Likitan ya tabbatar Mata babu karaya amma akwai buguwa a kafa da gefen kafadarta sai Yan kananan ciwurwuka, da dinki da sukayi Mata a gefen kafarta ta hagu.

Ta lumshe Ido cike da godiya ga Allah , sannan tace " sumewar da tayi fa".

Yadan dubeta yace fargaba ce fa da tsorata da tayi Amma ko yanzu ta dawo hayyacinta kina iya shiga ki ganta".

Tayi masa godiya ya wuce, itama tana Shirin shiga dakin.

Muryar mahaifiyarta ta tsaidata.

Ta juyo da sauri ta wuce ta rungumeta cike da sangarta.

.ita Kuma tana shafa bayanta cikin so da kulawa.

Duka tare suka shige dakin.

Kai tsaye suna shiga ta wuce Kan gadon da muhseena ke kwance.

Tana kallonta cike da tausayi tana yi Mata sannu.

Muhseena cikin jigata ta amsa, lokaci daya ta shiga bata hakuri.

Da sauri Karo na farko da mahaifiyarta tayi magana tun shigowarsu dakin.

"Me yasa kike bata hakuri haka, bayan kinyi dukkan kokari wajen dakkota ki kawota asibiti bayan ba kowane mutum bane yake tsayawa idan ya buge wani ".

Ta dubi mahaifiyarta tace "Don Allah ki daina wannan maganar".

Muhseena ta daga Ido sosai tana Karema fuskar ta kallo sosai take hango ràshin tausayi da wata bakuwar tsana acikin idanun matar, to dalili da me?.

Ta tambayi kanta gami da runtse idanunta.

Ta Kara matsowa kusa da ita.

Tace "kina bukatar wani abu ne", ta girgiza Kai alamar aah .

Ta Kara kallonta tace "Ko zaki iya bada nambar da zaa Kira wani naki, saboda gidanku su San abinda ya faru da ke".

Gaban muhseena ya Fadi , halin da take ciki ya fado mata.
A sanyaye tace "bansan kowa ba anan garin Kuma Bani da wani da Zan Baki number sa ki Kira, Bani da kowa".

Ta Karasa magana cikin zubda hawaye.
Wani irin tausayinta ya ratsa zuciyarta ta Kura Mata Ido.
Tana hango tsantsar damuwar da ke ciki Wanda hakane ya bata damar gasgata abinda bakin muhseena ya furta.

Mahaifiyarta ta saki tsaki tace "wane irin Baki da kowa?, Kinga ki dawo hayyacin.....?.
Da sauri ta dakatar da ita tace "don Allah ki kyaleta ta ji da abinda take ji, koma dai menene idan ta Sami lafiya sai muyi maganar".

Ta dubeta tace "Zan tafi gida zuwa anjima Zan dawo in sha Allah kinji ko". Muhseena ta gyada Kai ahankali Kuma tace "Nagode ".
Daganan suka fice Duka , mahaifiyarta na korafin yadda take son ta zubar da kimarta ga yarinyar da daga ganinta bata da wani matsayi.
Sam ita Kuma taki yarda da abinda take fada karshema cewa tayi abar maganar.
Direban ta ya dauketa zuwa gida. Ita Kuma ta shiga motar ta ja zuwa gida, zuciyarta cike da godiya ga Allah da abin ya tsaya anan.
Amma duk da haka ta rasa dalilin da yasa ta ji zuciyarta ta cika da tausayin budurwar kwarai da gaske, gashi ta yi ragon azanci ko sunanta bata tambaya ba , sai dai idan ta koma.
Tana ganin mugun damuwa da tashin hankali acikin idonta, tabbas akwai wani boyayyen al'amari atare da ita.

Tun komawar Taufiq inda ya bar muhseena bai ganta ba.
Ya shiga mugun tashin hankali mara misaltuwa duk inda zai duba awajen ya duba amma bai ganta ba.
Gashi wadanda suka San anyi hatsari awajen kusan duk sun bar wajen balle Su gaya masa akwai hatsarin da akayi ko zai bincika kila itace wacce yake nema.
Haka yayi ta bulayi cike da tashin hankali Yana cigiyar muhseena amma bai dace da wani ya ganeta ba.

Babu ta inda zufa bata karyo masa. Maganganun Mallam Umar sune suke tayi masa yawo acikin kunnansa," muhseena itace sanyin idaniyata Bani da wata damuwa sama da damuwarta babu wata alfarma da zaka min aduniya sama daka Kula min da ita".

Taufiq baisan akwai wani boyayyen al'amari a zuciyarsa game da muhseena sai yanzu .
Domin damuwar batanta tayi mugun taba shi.
Shi Kansa baisan iya lokacin da ya dauka Yana binciken inda muhseena ta shiga ba.

Kuran mujaheeda kuwa bazai kirgu ba tana son ta ji abinda ya tsaida Shi har yanzu bai karaso gida ba.

Dole karyar motarsa ta lalace yayi Mata.

Har kusan magriba babu labarin muhseena, ga gajiya ga yunwa ga damuwa .

Duk su suka taru suka maida Taufiq tamkar mahaukaci.

Dole ya hakura ya kama hanyar gida Wanda kallo daya zaka yi masa kasan Yana cikin mugun yanayi.

Yana shiga gida ana Kiran sallar magriba.

Ganin mujaheeda da alamun cikin jikinta ya Fara Dan fitowa, shine kawai ya lafar da tashin hankalin da yake ciki.

Duk inda ta juya ita yake kallo ta Kara kyau da cika fatarta ta Kara gogewa.

Haka zalika irin tarbar da ya Samu, Yana son ya tabbatar masa da cewa mujaheeda ta saduda ta amince zata haifar masa abinda ke cikin ta .

A daddafe Taufiq ya samu yayi wanka, Amma baya minti biyu tunanin. Inda muhseena ta shiga bai fado masa arai ba.

Ita kanta mujaheeda ta Lura akwai damuwa atare da Shi.

Ya Fara cin abinci Kenan , mujaheeda ta Kara zuba masa Ido tace "Naga duk Ka rame ne, kasha aiki sosai ko wata uku fa".

Yadanyi murmushi yace "AI dole na rame, tunda Baki kusa da ni da dai ina tare da ke nasan babu abinda zai ramar da ni".

Ta jidadin maganarsa tace " hmmm ai bansan na shaku da Kai ba, sai bayan tafiyarka ni kadai nasan yanayin da na fada".

Taufiq ya zuba Mata Ido yace " kin Kara kyau, kin cika da yawa, wai kinga yadda cikin nan yayi matukar karbarki kuwa".

Tayi dariya tace "Kai yaya Taufiq, kasan wai harya Fara motsi".

Ya saki murmushi yace "Masha Allah, ina cikin Maza masu saa arayuwa".

Ta danyi kasa da kanta cikin sanyin murya tace "Shi yasa nake son na Baka hakuri Akan yunkurin da nayi wajen son zubar da cikin , don Allah kayi hakuri Ka manta".

Cike da farinciki da jindadi ya aje cokalin abincin hsnnunsa yace "Dama yarinta ce ke damunki, domin idan ba yarinta ba babu yadda zaayi Allah ya Baki irin wannan kyautar sannan kice bakya so, don haka komai ya wuce Allah ya saukeki lafiya ".

Tace "Amin".

Sai bayan da ya Gama cin abinci suka koma falo.

Mujaheeda ta dube Shi sannan tace "Amma akwai damuwa a tare da Kai ".

Ya yi saurin girgiza Kai yace "damuwa ko gajiya?"
Tace "to gashi nan. Dai"
Bai Kara magana ba sai gabansa da ya cigaba da faduwa shin ina yarinyar mutane ta shiga? Tana hannun waye awannan daren?.

Tambayoyin da yake ta jera ma Kansa Kenan.
Mujaheeda tace "yaya Taufiq dazu ina kokarin dawowa gida daga gidan mu, Allah ya hada ni da tsautsayi na buge wata budurwa".
Hakanan Taufiq yaji gabansa yayi mummunan faduwa.
Ya dubeta da sauri yace"innalillahi wainna'ilaihirrajiun, ba dai abinda ya sameta ko, tana ina yanzu?".

Tace "zeenat hospital na Kai ta, Alhamdulillah babu wani abin damuwa sosai,"
Ta Kara kallonsa tace "yanzu ma nake son na koma na dubata na Kai Mata abinci".

Taufiq ya numfasa yace "Allah ya bata lafiya, ni dai na gaji sosai bazan iya zuwa asibiti yanzu ba ".
Tace "gaskiya Ka gaji domin fuskarka da jikinka sun nuna hakan , Dama na Kira direban mummy bayan shugarka wanka har ya zo Kuma Yana waje Yana jirana".....
TO BE CONTINUE

DAGA TASKAR YAR GIDAN IMAM

NI MA MATARSA CE
49

Taufiq ya gyada Kai yace "To ai gara kiyi sauri ki je ki dawo, saboda dare Yana yi".
Ya Kara kallonta sosai cikin Dan murmushi yace "Kuma kinfi kowa sanin nayi rashinki wata uku ba kwana uku bane,don haka duk lokacin nan ni yakamata aba".
Tayi dariya sosai ta tashi tana fadin "yaya Taufiq Allah baka da dama".
Nan da nan ta dakko gele sannan ta umarci daya daga cikin hadimanta biyu da suka rage, domin dayar ta koma garinsu anyi Mata aure.
Akan ta zo su tafi tare saboda ta barta acan ta cigaba da Kula da muhseena.

Uwale babu musu ta shiryo gami da daukar kwandon kayan abinci suka tafi.
Fitar su, mujaheeda tasa direban ya tsaya a super market tayima muhseena sayayyar kayan shayi da sauran Dan tarkacen kayan bukata.

Alhamdulillah sun tadda jikin muhseena ya fi dazu Jin sauki sosai.
Don ayanzu ma tana jingine a jikin gadon .
Mujaheeda ta janyo kujera ta zauna tana fadin "aah masha Allah jiki ya Fara sauki, sannu".
Cikin murmushi ta amsa
Yauwa sannu da zuwa.

Mujaheeda ta umarci uwale data zuba Mata abinci ta ci.
Sosai muhseena take Jin yunwa don haka abincin da uwale tasa Mata ta so ta ci sosai .
Amma ràshin dadin zuciya da damuwa ya hanata cin abincin yadda ya kamata.

Mujaheeda ta dubeta cike da kulawa tace "ki ci abincin mana".
Ta girgiza Kai tace
"Ya ishe ni nagode da dawainiya".

Mujaheeda ta dubeta sosai tace "ya sunanki ne".
Tace "sunana Zainab".
Ta gyada Kai tace "sannu kinji, ga uwale nan zata zauna da ke har zuwa lokacin da zaa sallameki".
Ta Dan dubi uwale tace "to nagode sosai".
Zatayi magana kenan wayarta ta dauki Kara tana dubawa taga Haj murjanatu ce.
Ta dauka "hello mummy".
Daga daya bangaren Haj murjanatu tace "kin tafi gida ko kina asibitin".
Tace "ina asibiti ".
Ta saki numfashi tace
"Wai ke me ke damunki ne,don me zaki dinga wahalar da kanki a Kan wannan yarinyar wacce babu wani galihu agareta, da wannan Daren kina yawo a titi saboda ita, ko kin manta cikin da ke gareki ne,".
Sam mujaheeda bata son muhseena ta gane fada ake Mata akanta don haka tayi saurin cewa " yanzun nan Zan koma gida".
Bata saurari komai ba
Ta kashe wayar don bata son maganar ta cigaba da nisa.
Daganan tayi sallama da muhseena da uwale ta tafi. Wasu lokuta da dama tana ganin suna da bambancin ra'ayi tsakaninta da mahaifiyarta domin yadda take kyamatar talaka Sam ita bata Jin haka aranta.
Asalima mugun tausayin sa take ji.
Tana Kuma son taimakonsa akowane hsli,
Kamar yadda take Jin tausayin Zainab tare da son ta taimaka Mata.

Tun fitar mujaheeda Taufiq ya kasa Jura, dole tasa shima ya fice.
Duk da yasan neman muhseena a wañnan Daren abu ne me matukar wahala.
Tofa ràshin kwanciyar hankalin da yake ciki yasa ya yanke shawarar fita nemanta.
Duk yadda zaa kwatanta damuwar da Taufiq ya shiga to fa ba zaku gane ba.
Shi Kansa matsalolin da ya hango suna da yawa, yanzu idan baiga muhseena ba ta yaya zai sanar da mahaifanta?.
Yaya Kuma zaiyi da jamaar garin da yasan duk boyewarsa suna iya binciko Shi.
Bayan ma haka ta yaya zai fitar da Kansa?.
Shin ina muhseena ta shiga?.
Haka Taufiq ya yi ta yawo acikin wannan Daren.
Amma Bai dace da ganin muhseena ba.

A hankali ya tsaida motarsa ya zaro ways cikin dimbin tashin hankali ya danna ya Kira salisu.
Wanda bai bata lokaci ba wajen daukar wayar.
"Ya akayi mutumina".
Salisu ya fada daga daya bangaren.
Jin muryar Taufiq cikin tashin hankali yasa ya Sami nutsuwa ya cigaba da tambayar sa abinda ke faruwa.
Sannu a hankali Taufiq ya gayá masa komai.
Ya Kara da cewa
"Yanzu ta ina Zan Fara, ina cikin muguwar damuwa Kuma bana son mujaheeda ta fahimci wani abu, babu inda ban duba ba salisu har na gaji shin ina yarinyar nan ta shiga?. Tana neman ta jefa ni cikin bala'i, sai da na gaya Mata ta tsaya inda na ajeta naje na dawo amma Ka duba fitinar data jefani ciki".

Salisu shima nan da nan ya gigice yace "to ina yarinyar nan ta shiga Allah dai yasa ba wata masifar ta fada ciki ba".
Taufiq ya numfasa yace
"Yanzu salisu ya zanyi?"
Salisu yace "hakuri zaka yi Ka koma gida kayi kokarin mallakar hankalinka ko don Kada matarka ta Fara zarginka idan Allah ya kaimu gobe sai muje mu Kai maganar wajen yansanda".
Shawarar salisu tayi don haka suka aje magana akan gobe zasu je su sanar wajen Yansandan.
Daga bisani sukayi sallama sannan Taufiq ya kama hanyar gida.

Yayi matukar saa sai bayan daya koma gida tukuna sannan mujaheeda ta dawo.

A daran ranar duk iya yadda ya so ya faranta ran mujaheeda ya nuna Mata lalle yayi kewarta.
To fa hakan ya faskara saboda tashin hankalin da yake ciki ya fatattaki duk wani farinciki da karfin da ke jikinsa.

Kusan yadda ya ga dare haka ya ga rana.
Bai runtsa ba saboda alhini.
Washegari duk sunyi Shirin tafiya wajen aiki.
Mujaheeda ta dauki abincin asibiti.
Tare suka jero da Taufiq shine ma ya rike Mata kwandon abincin.
Hakanan ya ji bakinsa ya furta "ya sunan wacce kika buge din".
Tadan dube Shi , tana kokarin shiga mota.
Sannan tace "sunanta Zainab".
Ya Dan yi Jim yace "Amma ya jikin nata".
Tace "akwai sauki sosai gaskiya, don jiyan ma da na koma a jingine na tadda ita, Kuma ta Dan ci abincin da na tafi dashi".

Yace "idan na tashi office da wuri, zanje na dubata".
A haka suka rabu.

Yana fita ya dauki salisu Kai tsaye ofishin yansanda mafi kusa suka wuce.
Sun shigar da komai an rubuta ,
Insifektan wajen Kuma yayi alkawarin bada dukkan gudunmawar sa.
Yadda Taufiq ya zauna Yana zayyana siffofinta, ba karamin mamaki yaba salisu ba.
Sai bayan barinsu ofishin Yansandan ne.
Sannan salisu ya dubi Taufiq sosai yace"Amma nayi mamakin yadda kake siffanta muhseena babu ko gargada gaba daya babu abinda Baka fada nata ba".
Yadan aje numfashi ahankali yace "ni Kaina nayi mamakin hakan".
Salisu ya Dade Yana kallon fuskarsa Yana kokarin gano abinda yake son ya gane.
Amma har suka rabu Bai samu ya gano hasashen da yake yi ba.
Taufiq Yana Kan hanyar zuwa office ne wayarsa ta dinga Kara tana neman agajinsa.
Dole tasa ya janyo wayar sannan ahankali ya sauka daga Kan titi yayi parking din motar, sannan ya dauka cikin sallama.

Daga can daya bangaren kauyen Durmi, Mallam Umar ya amsa da sauri "Taufiq Mallam ummaru ne mahaifin muhseena".
Dam gabansa yayi mummunan faduwa nan da nan ya gigice.
Bayan sun gama gaisawa ne yace"Tun jiya nake ta Kiran wayar taka amma bata shiga, ya ya kuka je gidan".
Yace "Lafiya lau"
Yace "yaya muhseenan komai dai lafiya ko".
Ya daure Yana kokarin boye tashin hankalin da yake ciki yace " komai lafiya lau, ina kokarin daidaita komai ne".

Yace To Allah yasa mu ji alheri, Ka bata wayar muyi magana ".

Yayi saurin cewa "Na Riga na fito Bana gida sai dai idan na koma Zan hadaku in sha Allah ".
Yace "to shikenan nagode ".
Daganan sukayi sallama.
Ya juya Yana kallon Hajara sannan yace "kina damuwa a banza ne, lafiyarta kalau yace ma ya idan ya koma gida zai hadamu a waya muyi magana ".
Hajara ta numfasa tace "To ai gara dai da aka ji halin da ake ciki kaga ai hankali ya kwanta".

Gaba daya Kai Taufiq ya Dora ajikin sitiyarin motar Yana maida wata irin ajiyar zuciya.
Shi Kansa yasan akwai gagarumar matsala, Shin ina zaiga muhseena?.
Zahiri Yana cikin tsaka mai wuya.

Kwanaki uku cur!
Aka kwashe yansanda na neman muhseena amma babu ita babu Labarinta.
Zuwa wannan lokacin kuwa damuwar Taufiq ta kasa buya domin sosai mujaheeda ta gane akwai abinda ke damunsa, Amma duk iya yadda zata shawo Kansa ya gaya Mata matsalar ya ki saboda baima yarda Yana da matsalar ba, yaki nuna Mata Amma ita ta riga ta Gama gane akwai damuwa, Amma tunda yaki yarda ya gaya Mata dole tasa ta hakura ta sa masa Ido.

Hatta jamaar gidansu sun gane baya cikin kwanciyar hankali, Haj saratu itama tayi tayi ya gayá Mata amma ya tabbatar Mata babu komai.

Muhseena ta Sami sauki sosai acikin wannan kwanakin, har tafiya ta nayi sannan da yawa daga cikin ciwurwukan jikinta sun Fara kamewa wajen dinki ne kawai yake Mata ciwo. Shima din makonta daya a asibitin aka kwance dinkin.

Muhseena ta Sami dukkan kulawa a wajen mujaheeda.
Hakika idan haka ake Samun masu kudi to da an huta domin dai mujaheeda tana da halin karsmci matuka da gaske. Babu abinda ta nema ta rasa.
Sai dai tsoro da fargaba da kullum yake hanata sakat saboda kullum tunaninta idan an sallameta ina zata?. Don kuwa ko kadan bata jin zata iya komawa Durmi ta Kara dorama iyayenta damuwa da tashin hankali.

Tabangaren Taufiq Kuma duk da kullum sai Mallam Umar ya Kira Shi da son ya hada Shi da mujaheeda, to fa kullum hanya hanya yake masa Yana Samun wata karyar da yake yi masa, Wanda Shi Kansa ya Fara sikewa tare da kokarin dorama Kansa tunanin Anya kuwa babu wani abu da Taufiq yake boye masa, musamman da akullum shima Hajara ke damunsa da son sanin halin da yarta take ciki.

A yayinda Haj murjanatu ta sa kahon zuka agame da yadda mujaheeda ke kulawa da muhseena, domin acewarta ita Kam bata ga wani dalili da zaisa ta dinga bata lokacinta Akan yarinyar da bata da maraba da kaskantacciya.
Anan mujaheeda ta ki saurarenta domin kullum tayi Mata irin wannan maganar tana maida Mata da cewa "yanzu mummy ya ya kike son nayi, Kada fa ki manta duk abinda ya faru da Zainab to nice sila kinga kuwa ta yaya Zan kyaleta a garin da take ikirarin bata da kowa Kuma bata San kowa ba".
Kusan kullum sai sunyi Irin wannan maganar.
Kullum Kuma sau mujaheeda ta je ta dubata ahankali ta ji sabo da son muhseena suna neman su Sami gurbi acikin zuciyarta.

Mujaheeda na zaune a gefen Taufiq. Tana matukar kokarin jansa da hira domin ràshin sakewarsa.
Karfe biyar ne na yammacin ranar asabar.
Dai dai lokacin wayar mujaheeda ta dauki ruri, cikin ràshin karsashi ta dauki wayar, "uwale ya akayi".
Ta tambaya, uwale ta gyara zamanta tace "Haj Dama an sallame mu ne yanzu, Kuma akwai kudi da zaa bada ragowar balance".
Mujaheeda ta ce cike da jindadi.
"Alhamdulillah, to Ku Jira gani nan tahowa yanzu". Ta aje wayar tana duban Taufiq.
Ya rigata yin magana yace "me jinyar taki aka sallama".
Tace "eh kaga dai har an sallameta baka Sami damar zuwa Ka dubata ba". A ransa yace ina Naga wannan lokacin ina cikin wannan masifa.

Yace "To yau ai sai muje na kaiki".
Tayi Dan murmushi tace "dako Ka kyauta, don da ganin yarinyar tana cikin matsala Shi yasa kaga na dage wajen taimakonta".
Ya zuba Mata Ido cike da son Karin bayani yace "kamar yaya tana cikin matsala".
Tace "to ai Baka cikin halin da zamu zauna mu tattauna Shi yasa na bar maganar, kasan ta gaya min bata da kowa a garin nan asalima ko an sallame ta batasan inda zata je ba".

Da sauri ya ce "bata da kowa? To ai yakamata ki tashi muje saboda tunda an sallame ta ya kamata Kiji komai agame da ita"
Nan da nan mujaheeda ta tashi ta hau shiri, zuwa lokacin kuwa hakurin Taufiq har ya kusa gazawa domin kuwa tunda ta ambaci yarinyar bata San kowa ba, yaji gaba daya tunaninsa ya karkata acan .
Zuciyarsa na matukar gaya masa abinda tasan da wuya hakan ya kasance amma duk da haka ya kosa yaje ya ga yarinyar.musamman tadda gabansa yake matukar bugawa tunda tayi maganar.

Garin babu yawan cunkoson ababan hawa, hakan ne yasa nan da nan Taufiq ya isa asibitin tare da mujaheeda.
Kai tsaye dakin suka wuce, Taufiq ya rasa dalilin da yasa yaji bugun zuciyarsa ya tsananta.
Cikin sallama suka shiga mujaheeda na gaba Taufiq Yana binta abaya.

Da sauri uwale ta tashi ta na yima uwar dakinta sannu da zuwa, tana gaida Taufiq.
Mujaheeda ta dubi muhseena da take kwance "Ashe anyi sallama?".
Cikin fara'a muhseena ta yunkura tana kokarin tashi zuwa lokacin kuwa gaba daya Taufiq idanunsa na dore akanta.
Tana dago kanta caraf suka hada Ido da Shi.
Dam! Gaban Taufiq yayi mummunan faduwa nan da nan ya rikice.
Itama muhseena cak! Komai ya tsaya Mata numfashinta ya dinga wuyar fita.
TO BE CONTINUE

DAGA TASKAR YAR GIDAN IMAM
NI MA MATARSA CE
50

Shin ina hajiya ta Samo Taufiq?, Shin tasan alakar da ke tsakaninsu ne?.
Irin Jerin tambayoyin da muhseena take ma kanta kenan, ba tare da ta dauke idonta akansa ba. Shima saurin jingina yayi da jikin bangon dakin, saboda yadda ya ji jiri Yana neman kwasar sa, shin mafarki yake ko na Ido biyu, Dama muhseena itace Zainab din da mujaheeda ke fada?, Itace ta buge a mota duk tsawon wannan lokacin da yake cikin masifa da tashin hankali Dama maganin matsalar tana hannun mujaheeda.
Lokaci daya Kuma gabansa ya cigaba da faduwa da karfi, saboda tsoro da fargabar Kada muhseena ta bude bakinta.

Muryar mujaheeda ta katse shurun da akayi a dakin.
Tadan waiwayo tana duban Taufiq tace "yaya Taufiq ga Zainab kaga jikin da sauki sosai, tunda gashi har anyi sallama". Kokarin boye firgitar da yake ciki yake yi, ya gyada Kai yace cikin shakewar murya "eh gaskiya jiki yayi sauki duk da Banga yadda take ba alokacin da aka kawota asibitin".
Kan muhseena Yana kasa magana take da zuciyarta sosai,
Tana kokarin Nemo amsoshin tambayoyinta.

Dai dai lokacin kamar da ga sama muhseena ta ji mujaheeda tace "Zainab wannan shine mijina Taufiq ".

Cikin tsantsar kidima da saura kadan mujaheeda ta gane irin tashin hankalin data fada. Muhseena ta dago kanta nan da nan idanunta suka yi jajir.

Ta shiga maimaita kalaman mujaheeda aranta " mijina". Ta shiga kokarin Nemo fuskar Taufiq ta kalla sosai ta tsaida idanunta akansa, irin yanayin da ta gan shi ciki ya tabbatar Mata da halin fargaba da firgici da yake ciki.
Wanda hakanne ya tabbatar Mata da cewa, Taufiq baya da masaniyar itace matarsa ta buge a mota.

"Uwale ki harhada kayan ki Kai mota, zanje na karasa biyan kudin asibitin", cewar mujaheeda. Uwale ta amsa da toh, ita Kuma ta juya tace "yaya Taufiq muje na karasa biyan kudin asibitin". Cikin dakewa da kokarin boye duk wata gaskiya da ke shimfide a fuskarsa yace "aah , jeki kawai ki Gama ki dawo mu tafi".
Ta jinjina Kai tace "to shikenan".
Ta juya da sauri ta fice
Yayinda uwale ta ajema Taufiq kujera alamar ya zauna. Daganan ta hada kaya ta dauka ta Fara fita dasu.

Tana fita Taufiq yayi saurin dawo da kallonsa ga muhseena yace "me yasa kika ce sunanki Zainab".
Ba tare data dube Shi ba tace "saboda shine asalin sunana, ko Ka Bani damar da zaka san wani abu ne agame da ni".
Ya kauda maganar da cewa "me yasa kika bar inda na ajeki ba bayan na hanaki yin hakan, ko taurin kai Yana daya daga cikin abubuwan da ban sani ba acikin halinki?".
Kanta na kasa tace
"Nabar wajen ne saboda banyi zaton zaka dawo ba, na dauka Ka wofintar da nine ba tare da tausayi ba ko sanin makomata ga halin da Zan shiga agarin da bansan kowa ba ".

Ya nisa yace " me yasa Baki kyautata min zato ba, Kin San halinda kika jefani aciki kuwa na ràshin kwanciyar hankali, ko bacci Bana yi saboda túnanin halin da kike ciki da inda kika shiga".
Sai alokacin ta dago da sauri suka hada idanu tace "yaushe harna Sami wannan matsayin awajenka, na dauka ai ni ba komai bace face lalura agareka".

Ji yayi kalamanta suna sukar zuciyarsa Sam Sam bai jindadin yadda take maida masa magana.

"Wannan CE matarka?"

Ya gyada Kai "itace".

Ta lumshe manyan idanunta ta Bude sannan tace "kayi saa tana da kirki da tausayi fiye da Kai".

Ya zuba Mata Ido Yana Jin wani abu Yana fisgar zuciyarsa yace "hmmm ni Bani da tausayi?"

Shuru tayi Amma bata dauke idonta akansa ba.

Sai Shi ne ya dauke kallonsa akanta,

Domin bazai juri hada Ido da ita ba.

Ta Gama nazarin fuskarsa tsaf.

A hankali tace "Ka kwantar da hankalinki Ka cire wannan tsoro da fargabar da ke tattare a fuskarka, saboda Kada abinda kake tsoro ya afku".

Nan ne ya sake kallonta yace "me nake gudun ya afku".

Ta danyi wani bushasshen murmushi sannan tace "fargabar Kada matarka tasan abinda ke tsakaninmu"

Baiyi magana ba Amma sosai idanunsa suke nuna gaskiyar abinda ta fada.

Ta Kara numfasawa tace "Kada Ka damu, hakan bazai taba kasancewa ba, Amma sai idan har Ka cire wannan fuskar da take saye da Kai, ko kadan ba Zan zamo silar rushewar farincikin gidanka ba, don babu dalilin da Zan bata dangantakar da akwai Akan wacce babu".

Hakanan ya ji karshen maganarta Bai yi masa dadi ba, yace "wace dangantakar ce babu?".

Zatayi magana kenan uwale ta yi sallama ta shigo ,

Hakanne yasa duk sukayi shuru tamakar Basu taba yin magana ba .

Bata Dade da shigowa ba Mujaheeda ta shigo tana fadin "mu je yaya Taufiq ".

Da sauri ya Mike ya Riga kowa fita .

Ba tare da taimakon kowa ba muhseena ta sakko daga Kan gadon ta gyara hijabin jikinta uwale ta rike hannunta mujaheeda na binsu abaya har zuwa wajen motar.

Uwale da muhseena Duka suna baya Taufiq shike Jan motar muhseena na gefensa.

Sun danyi nisa da Fara tafiya, mujaheeda ta dubi Taufiq tace "ina ganin mu biya super market adan sayama Zainab Kaya, saboda lokacin da na bugeta tace akwai jakar kayanta , Amma banganta ba, ina ganin mutanan mu da Basu da imani da anyi hatsari su kwashe kayan mutane bana raba daya biyu irinsu ne suka dauke Mata jakar".

Taufiq yace "duk zai yuwu tunda akwai irin mutanen da yawa".

Kai tsaye wani babban super market ya shiga. Uwale kadai aka bari acikin motar.

Muhseena tayi mamakin irin kayan da mujaheeda ta saya Mata dogayen riguna sun Kai guda shida duk daya ta Kai dubu talatin .

Sai atamfofi da less ko su ta dibar Mata da yawa harda su takalmi.

Har suka bar super market din muhseena mamakin kirkin mujaheeda take yi, gami da karamcinta.

Hakanan take ji azuciyarta tamkar bata kyauta Mata ba. Tun a motar take yi Mata godiya, har mujaheeda ta gaji da amsawa .

Jefi jefi suna hada Ido da Taufiq ta madubi.

Har suka isa gida.

Isar su gidan, muhseena tayi mamakin irin katon gidan da suka shigo. Tunda take bata taba ganin gida irin wannan ba, tsaruwar gidan ta yi yawa, komai kallon mamaki take masa har zuwa tsararren falon mujaheeda inda aka nuna Mata wajen Zama ta zauna.

Daganan fa gabanta ya cigaba da matsanancin bugawa tana tunanin daganan Kuma ina zata fada.

Tana nan zaune mujaheeda ta shigo ta kirata da sauri ta Mike tabi bayanta.

Har zuwa wani daki me kyau me dauke da setin gado da kafet da kujera ta hutawa guda daya.

Mujaheeda ta dubeta sosai tace "Zainab ga dakin da zaki zauna, ga bayi nan ki shiga kiyi wanka ki gyara kanki, zaa kawo abinci ki ci sannan Zan nemeki domin muyi magana".

Tace "to nagode Allah ya Kara sutura".

Har mujaheeda ta Kai bakin Kofa, muhseena tace "Haj ".

Ta tsaya ta juyo tana kallonta , sannan ta tako ahankali zuwa kusa da ita , tace "ina rokon Allah yayi Miki sakayya ta alheri ya Kula da ke da dukkan farincikin ki , ya karama dukiyarki albarka , dukkan hidimar da kikayi da ni ina rokon Allah ya mayar Miki da dubunsa".

Sosai mujaheeda ta ji dadin adduar da muhseena take Mata .domin tunda take babu Wanda ya taba yi Mata irin wannan adduar. Hakanan ta ji son muhseena Yana Kara shiga ranta. Sosai take ganin mutunci da gaskiya a cikin idanun muhseena. Ta yarda da cewa duk inda muhseena ta fito to ta Sami ingantacciyar rayuwa ta tarbiyya.

Ta numfasa tace "Amin Zainab nagode nima".

Daganan ta juya ta fita.

Har muhseena ta Gama wanka ta shirya cikin wata jar doguwar riga ta ji duwatsu ajikinta, haka zalika tayi matukar amsar ta, tayi kyau sosai, ramar da tayi ta Kara fito da kyawun fuskarta.

Har ta Gama Shiri zuciyarta tana bugawa tana tunanin yaya al'amarinta zai kasance?. Kamar yadda Taufiq yake can falo ya kasa zaune ya kasa tsaye cike yake da fargabar Kada muhseena ta saki baki ko ta tashi daga alkawarin da tayi masa.

Amma duk da haka Yana kokarin dakewa tare da boye duk abinda ke zuciyarsa, saboda gudun Kada mujaheeda ta Sanya zargi acikin zuciyarta.

Har daki uwale ta biyota da abincinta, ta ci abincin sosai Wanda tunda ta zo garin jigawa ba ta ci irinsa ba.

Karfe bakwai na dare uwale ta shigo ta Kira muhseena.

Tare suka jera har zuwa falon mujaheeda.

Zaune ta tadda mujaheeda kusa da Taufiq sosai ta ci kwalliya da doguwar rigar bacci me taushi sosai ta lafe ajikinta Dan matashin cikin jikinta ya Dan turo rigar sai tashin kamshi take na musamman. Muhseena ta rasa dalilin da yasa taji faduwar gaba da wani irin bakon al'amari ya na ratsa zuciyarta ganin mujaheeda daf da Taufiq ya Haddasa Mata Jin damuwar da ta rasa dalilinta.

Asanyaye ta nemi kasan kafet Zata zauna. Da sauri mujaheeda tace "aah zauna Kan kujera". Ta girgiza Kai tace "nan ma ya yi", ta zauna idon Taufiq Yana dore akanta, muhseena tayi masa

kyau sosai da sauri ya dauke Kansa ya maida Kan wayar hannunsa.

"Zainab ina son naji gaskiyar labarinki da abinda ya kawo ki jigawa duk da kina ikirarin Baki San kowa agarin ba".

Gaban muhseena ya Fadi kamar yadda Taufiq yaji kamar an tsira masa allura a kahon zuci da sauri ya dubi muhseena itama Shi take kallo.

Ya yi kasa da kanta bakinsa dauke da adduar neman rufin asiri.

A hankali muhseena ta Fara magana , kamar wacce ake karantama.

"Ni yar kauyen danzaki ce dake can jahar Kano, marainiya ce ni gaba da baya ba ni da kowa, Allah yayima mijina rasuwa (da sauri Taufiq ya dubeta cike da kaduwa, don me muhseena zata maida Shi matacce), bayan na fita takaba rayuwa tayi min tsauri hakan yasa na yanke shawarar zuwa nan garin jigawa ko Allah zai taimakeni yasa na cika burina".

Mujaheeda cike da tausayawa tace "menene burin naki?".

Ta Dan numfasa sannan tace "Duk arayuwata tunda nasan ciwon Kaina Bani da burin da ya wuce nayi karatun boko me zurfi yadda Zan Zama abar alfahari , Amma Allah Bai Bani wannan damar ba saboda ban taso a yanayin da Zan Sami cikar burina ba".

Mujaheeda ta numfasa tana cigaba da kallonta, sosai take Jin damuwarta a cikin zuciyarta, Ayanzu ne Kuma ta Kara gane dalilin da yasa take ganin tsananin bakinciki da tashin hankali a tattare da ita.

Wanda ya rasa iyaye ya rasa Miji ba Shi Kuma da wasu yan'uwa da zasu tallafe Shi, ga talauci. Lalle abin a tausaya masa ne, shin idan ta rike muhseena ta taimaketa ta cika burinta ba zata Sami lada ba?.

Hakika zata Sami dimbin ladan da ita kanta bata San yawamsa ba, domin akwai falala acikin rikon maraya, Kuma bayan hakama sosai take Jin aranta zata iya taimakonta tun ganinta na farko da ita.

Shi Kansa Taufiq yayi mamakin yadda muhseena ta zauna ta tsara wannan bayanin , Wanda ya San ta rufe komai ne domin ta cika alkawarin da ta dauka na ràshin son ta tarwatsa masa gida, to Amma Anya kuwa ita yayi Mata adalci.

Mujaheeda ta waiwayo ta dubi Taufiq tace

"Yaya Taufiq kaji labarin Zainab, zuciyata na kokarin Dora min na taimaketa, Amma menene tunaninka Akan hakan , ".

Taufiq ya Kara sanya nutsuwa acikin maganarsa yace "hakan Yana da kyau domin lada zaki samu, bazan hanaki aikata abinda nasan alheri ne agareki ba".

Ta yi Dan murmushi tace

"Nagode da kwarin guiwar da Ka Bani, Dama kaga na Saba Zama da Yan aiki uku yanzu guda biyu ne, saboda haka sai Zainab ta cike gurbin mutum dayan".

Gaban Taufiq ya Fadi yayi gaggawar kallon muhseena ta yaya zata Zama Mai aikin kishiyarta?. Anya yayi Mata adalci kuwa. Suna hada Ido tamkar muhseena tasan irin tunanin da yake yi sai tayi wani dan murmushi Mai kunshe da sakon babu komai kaddarata ce tazo da haka.

Zaiyi magana kenan muhseena ta riga Shi "nagode Haj Allah ya saka Miki da alheri, na yarda Zan Miki aiki duk abinda kike so zanyi Miki matukar zaki taimakeni na cika burina".

Mujaheeda tayi murmushi sosai tace "Kada ki damu, Zan taimake ki zakiyi karatu zaki sami cikar burinki, amma ina son ki rike amanata da amanar gidana".

Tace "wannan babu damuwa in sha Allah zaki sameni me kiyayewa Akan duk abinda ya shafeki, nagode nagode ". Tace "babu damuwa, wannan dakin shine dakin Ki, " tace "to nagode ".

Taufiq dai Bai Kara furta komai ba,

Duk da Yana Jin babu dadi aransa.

Mujaheeda tace "Aina kika tsaya a karatun boko".

Muhseena tace "iyakata aji uku na karamar sakandire".

Tace "babu damuwa, kina iya tafiya".

Ta Mike tana cigaba da yi Mata godiya ta koma daki. Dai dai lokacin wayar Taufiq ta dauki ruri nambar Mallam Umar ce dannawa yayi da sauri ya maidata silent.

. muhseena tana shiga daki ta turo kofa ta jingina da jikin kofar gami da runtse idanunta .

Jin hawaye tayi Yana zuba a fuskarta.

Rayuwa irin tata tana cike da kalubale, shin wace kaddarace tayi sanadiyyar haduwarta da mujaheeda.?

Sam bai dace tayi Mata karya ba, a irin mutuncin data nuna Mata Bai kamata ta yaudareta ba. To Amma bata da wani zabi yin hakan shine kadai rufin asirinku Duka. Da kuma tabar gidan gara ta zauna tayi Mata bauta domin Akan auren da baida wata makoma ba zata zauna tayi asarar cikar burinta ba tunda mujaheeda ta amince zata taimaketa ita Kuma tayi alkawarin aje komai ta rungumi abinda Allah ya kaddara Mata .

Amma ta rasa dalilinta na yin kuka Mai yawa har idanunta suka kumbura, ta rasa murna zatayi da zata samu cikar burinta ko kuwa bakinciki zatayi da zata jingine aurenta agefe saboda cikar burinta.

TO BE CONTINUE

DAGA TASKAR YAR GIDAN IMAM
NI MA MATARSA CE
51

Ta bangaren Taufiq shima ya kasa runtsawa a wañnan daren, tunane tunane ne fal aransa.

Har mujaheeda ta yi bacci ta barshi Yana aikin juye juye.

Karfe biyu da kwata na dare hakurinsa ya gaza.
Ahankali ya waiwaya ya dubi mujaheeda ta nutsa cikin bacci, ko motsi ba tayi.

Hakanne ya bashi kwarin guiwar yaye bargon da ya rufa ya sakko a hankali ya Bude kofa cikin taka tsan tsan ya fice gami da rufo kofar a hankali.

Kai tsaye dakin muhseena ya nufa Yana tafiya kamar barawo Yana yi Yana waige tare da adduar Kada Allah yasa wani ya gan shi. Allah ya rufa masa asiri.

Cikin karfin hali ya tura kofar ta Bude ya shiga gami da rufota.

Baiyi mamakin yadda ya Sami muhseena Ido biyu ba,tana zaune Kan sallaya da alama sallar nafila ta idar ta zauna Kuma ta na cigaba da addua .

Duk da ta girgiza da shigowarsa dakin.

To hakan baisa ta ida adduar da take yi ba. Har ya Sami gefen gadon ya zauna Yana cigaba da kallon kyakkyawar fuskarta .

Cikin nutsuwa ta shafa adduar, lokaci daya ta dawo da kallonta da hankalinta Kansa tace "lafiya zaka shigo awannan daren, ba tare da kayi tunanin kasadar da kayi ba".

Ya dubeta sosai yace "me yasa kika amince da Zama gida daya da mu amatsayin me aikin matata, ko kin manta kema matata ce ".

Ta nisa sannan tace

"Ban manta ba, amma ka sani bazan taba amsa wannan sunan ba har sai Ka tabbatar min da Shi Ka yarda ni din matar Ka ce Ka yarda zaka iya yin komai saboda Ka tabbatar min da sunan ciki Kuma harda gayama matarka cewa NI MA MATARSA KACE da bakinka da amincewarka ba tare da wani ya matsa maka aikata hakan ba".

Bai iya cewa uffan ba

Har ta cigaba da cewa "idan har babu ranar da zaka tabbatar da hakan to ina son Ka yi kokarin mantawa da cewa ni ma matarka ce,Ka cire a ranka babu wata alaka a tsakaninmu kamar yadda na cire hakan araina alokacin da na amshi bukatar matarka na Zama tare da ita".

Ta Kara kallonsa tace "ba a matsayin matarka Zan zauna a wañnan gidan ba".

Nan ne yayi saurin yi Mata tambayar "A matsayin me zaki zauna?". Ta danyi murmushi tace "Zan zauna amatsayin me neman taimako awajen matarka da zaman yi Mata aiki saboda na Sami cikar burina".

"Kina nufin zaki aje aurenki saboda cikar burinki kin sadaukar da aurenki saboda ki Sami ilimin da kike mafarki".

Tace "hmmm wai me yasa kake ta nanata auren da baida wata makoma" a fusace yace "Kada ki Kara Kiran aurena mara makoma". Sai da ya Fadi maganar ne ya gane kamar ya zura jiki da yawa domin Shi Kansa bai San dalilin daukar zafin da yayi ba , da Kuma Jin Sam baya Jin dadin maganar da take yi.

"Don Allah Ka tashi Ka tafi Kada a Sami matsala" ya dubeta sosai yace _ina son muyi magana ne sosai". Ta girgiza Kai tace "a nan aah (ta Kara girgiza Kai) kaima kasan hakan ba me yuwuwa bane, in dai kana fargabar zamana agidanka zai iya haifar maka da matsala ne to ina son Ka daina wannan fargabar saboda ina Kara tabbatar maka da cewa Baka da matsala da ni babu ruwana da Kai balle har na kawo maka matsala don haka kaima kasa aranka Baka San ni ba bansan Ka ba,".

Ya yunkura ya tashi saboda bazai jure Jin irin maganganun da take fada ba, ta yaya zata ce Bai Santa ba bata San Shi ba?, Me yasa shi da yakamata ya jidadin kalamanta sai ya ji baya jindadin su.

Har ya kusa bakin Kofa

Ya tsaya ya waigo yace "mahaifanki sun Matsu su ji halinda kike ciki kullum sai sun Kira ni a waya".

Ta numfasa cike da damuwa tace "Allah sarki, kaga ko domin su da kwanciyar hankalinsu dole na zauna a garin jigawa bazan taba komawa garesu da abinda zai tayar da hankalinsu ba". Kofa ya Bude ya fice daga dakin.

Muhseena ta lumshe Ido nan da nan hawaye ya cigaba da fita Mata.

Ta rasa wane irin tunani zatayi shin zamanta a gidan nan zai haifar Mata da da me Ido kuwa?.

Har Taufiq ya koma daki mujaheeda bata farka ba. Sai dai tunda ya kwanta bacci ya kauracema idanunsa hakika Yana cikin tsaka me wuya. Wannan al'amarin fa ba karamin al'amarin da zai yi shuru ba ne.
Bazai iya gabatar da muhseena amatsayin MATARSA ba, Kuma bazai iya sakinta ba? Shin ya ya zaiyi da dimbin hakkin muhseena da ke Kansa?. Tikisa.

Washegari duk da kasancewar muhseena batasan komai ba agame da hidimar gidan, Tofa ta Riga kowa tashi ita ta gyara ko'ina.
Su kansu uwale da hassi mamaki ta basu, domin duk aikin da suke yi ita tayi. Ita kanta mujaheeda tayi mamakin yadda nan da nan muhseena ta ta fahimci aikin gidan sosai ta ga alamar Zata jidadin Zama da ita, domin tana son mutum me karsashi mara son jiki.
Taufiq ya rigata tafiya office.
Daga bisani itama ta fita zuwa nata office din. Lalle mujaheeda ba karamar mace ba ce, ta yaya ma zata iya kishi da ita bayan ta ko'ina tayi Mata funtinkau bayan ilimi da wayewa har aiki take. Irin tunanin da muhseena ta ke yi Kenan , sannan ta koma tunanin Irin daula da kudin da mujaheeda ke facaka da su shin na ta ne ko na Taufiq?.
Bata hango ko kofa daya da zata iya budewa ta shiga domin yin kishi da mujaheeda ba, hakan yasa ta Kara daukar aurenta da Taufiq amatsayin auren wucin gadi domin tasan tabbas ba auren da zai amsa sunan sa ba ne.

Tun karfe uku mujaheeda tabar office Alh jibrin ya Sami abinda yake so domin tabar masa office dinta Akan ta tashi ya Kula da duk abinda ya kamata.
Kai tsaye gidansu ta wuce.
Haj murjanatu tana Shirin zuwa duba jikin aminiyarta Haj Nana da ta kwana biyu tana zazzabi. Amma zuwan mujaheeda yasa ta maida gyalenta ta aje ta fasa zuwa.
Duk abinda mujaheeda ke bukatar ci Shi Haj murjanatu tasa aka kawo Mata amma da yake abune na laulayin masu ciki yasa komai ta Dan ci sai ta aje ta ji ya fita aranta.

"Ina fatan dai an sallami yarinyar da kika buge, ko kya samu ki natsu waje daya".cewar Haj murjanatu.
Mujaheeda tace tana kallonta "Abinda ya kawo ni ma Kenan mummy, an sallameta tana gidana". A gigice Haj murjanatu ta dubeta tace "tana gidanki me take yi agidanki?".
Yadda taga nan da nan ta gigice yasa tace "haba mummy me yayi zafi ne, me yasa wai Abu komai kankantarsa sai Naga Yana tayar da hankalin ki, yanzu me ye abin damuwa don nace Zainab tana gidana bayan agabanki tace bata da kowa a garin nan".

Haj murjanatu ta zuba Mata Ido tana Mata kallon Bana son ki yi kuskuren da zaki zo kina danasani.
Tace " to yanzu meye dalilinki na ajeta a gidanki?".
Mujaheeda ta Dan gyara kishingidar da tayi sannan tace "tayi min bayanin komai na Kuma gamsu da cewa tana bukatar taimako , don haka banga bambancinta da sauran masu aikin

gidana ba yadda na Basu wajen Zama da ci da sha itama haka na daukar ma Kaina Zan bata domin zata zauna tare da ni ta cigaba da yi min aiki Amma bata bukaci komai ba a matsayin sakayya sai son tayi karatu to kinga nan ma idan an taimaketa tayi karatun duk lada zaa samu".

Mujaheeda tayi mamakin yadda nan da nan taga Haj murjanatu ta gigice ta shiga fada da nuna ràshin amincewarta Akan Zama tare da muhseena.

"Me yasa su sauran masu aikin nawa Baki taba nuna kiyayya a garesu ba kamar yadda kike nunawa Akan Zainab yanzu, asalima kece kika kawo su don suyi min aikin".

Haj murjanatu tace "saboda su Bana Jin abinda nake ji Akan Zainab din, don na rasa abinda yasa tun ganina da ita na farko na ji bata kwanta min arai ba sai yanzu Kuma da kikayi maganar nan na fahimci ma na tsaneta ne sosai , don haka ba zaki zauna tare da ita ba".

Ta girgiza Kai tace " aah mummy na riga na tabbatar Mata da cewa Zan zauna tare da ita Kuma da gangan kike kin Zainab na rantse Miki tana da Kyan Hali ga natsuwa sannan yau na tabbatar da cewa bazan taba Samun me aiki mara son jiki da son aiki irinta ba, yau duk wani aikin gidan nan babu abu daya da su uwale sukayi duk ita tayi komai".

Acikin muguwar damuwa Haj murjanatu tace "mujaheeda Bana son ki aikata irin kuskuren da na aikata a rayuwata, hakanne yasa nake son ki rabu da yarinyar nan ".

Mujaheeda ta tsareta da Ido tace "mummy kullum ina son na ji irin kuskuren nan da kikayi amma har yanzu kin kasa gaya min". Ta jinjina Kai alamar girman al'amarin ya wuce duk inda ake zato.

Sai dai bakinta ya kasa furta komai sai shuru da tayi.

Mujaheeda tace "in dai Zan iya rike su uwale itama Zan iya riketa don Allah mummy abar wannan maganar". Dai dai lokacin Àlh Mustapha labaran yayi sallama ya shigo cike da kauna mujaheeda ta gaida Shi, ya nemi kujera ya zauna cike da fara'a da jindadin ganinta yace " mujaheeda komai dai lafiya ko?".

Tace "lafiya lau daddy Garama daka dawo yanzu , kaji irin magánganun da mummy take yi Akan kawai ina son nayi taimako".

Alh Mustapha labaran ya dubi Haj murjanatu da tunda ya shigo ko kallon sa ba tayi ba, ballefa ya Sami arzikin sannu da zuwa Wanda wannan ba bakon al'amari bane a gurin kowa.

Duk da ta Kara hade rai kamar wacce aka aikoma da mala'ikan daukar Rai, hakan baisa Alh Mustapha labaran kasa yi Mata magana ba.

" Meya faru Haj"

Haj murjanatu tayi masa wani irin kallo sannan tace "irin kuskuren da na tafka shekara goma sha tara baya irinsa take son ta tafka". Gaban Alh Mustapha labaran yayi mummunan faduwa duk wata Kalma da yayi niyyar fade komawa tayi cikinsa yayi dif kamar ruwa ya ci Shi.

Mujaheeda tace "ni daddy na rasa wane irin kuskure ne mummy take fada kullum ni dai taimako nayi niyya Kuma nasan Allah bazai tabar da ni ba daddy yarinyar nan ce da na buge a mota nake son ta cigaba da Zama awajena tunda bata da kowa , don Allah menene aibun hakan".

Ya girgiza Kai ba tare daya damu da irin mugun kallon da Haj murjanatu take masa ba yace

"babu laifi wajen taimakon yan'uwana musulmi domin ladanki Yana ga Allah, idan kikayi komai Dominas ba zaki tabe ba Allah Kuma zai taimake ki".

Afusace Haj murjanatu tace "yanzu Ka goyi bayan ta zauna da yarinyar da batasan wacece ba sai abinda kawai ta fada a kanta babu wani shaidar gaskiya ta fada" Alh Mustapha labaran yace " ki dinga kyautatawa kowa zato Haj din Allah ". Ta saki tsaki tace "hmmmm".

Daganan Alh Mustapha labaran ya tashi ya shige daki. Kan gado ya samu ya zauna ya dafe Kansa . Har abada baya Jin zai fita daga cikin masifar damuwa da ràshin sukuni da kullum yake jinsa aciki . Baida wani farinciki ko nutsuwa Bai jindadin zaman gidansa Bai jindadin muamala da matarsa .

Ga uwa uba masifa da tashin hankalin ràshin haihuwa. Babu abinda yake so ya ke sha'awa da ya wuce ace yau ya haihu Amma gashi shekaru sun tura zuwa yanzu har ya cire ran zai tabs haihuwa a rayuwarsa.

Hakanne yasa akullum yake kallon mujaheeda a matsayin yar da ya haifa, sai dai Kuma gurbin Ido ba Ido ba ne, jininsa yake so Wanda zai iya bugun kirji yace Dan da ya Haifa ne.

Har mujaheeda ta bar gidansu, bata samu wani goyon baya daga mahaifiyarta ba, sosai bata son zaman muhseena tare da yarta. Shin wannan kiyayyar ina mafarinta?. Ita kanta mujaheeda tasan a dole Haj murjanatu ta kyaleta saboda bata son damuwarta Amma ba don tana son zaman muhseena a gidan ba.

Kafin dawowar mujaheeda Taufiq yayi hanzarin dawowa saboda yau Yana Jin idan Bai hada muhseena da mahaifanta awaya ba, to fa baisan wane Hali zasu shiga ba, saboda damuwar da suka nuna suna ciki tayi yawa.

Dawowarsa gidan yayi saa duk su uwale basa falon kowa na can wajen aikinsa. Sai muhseena da take dakinta take ta karatun kur'ani . Babu wata doguwar magana da sauri ya Danna ya kira Mata wayar ya yi sauri ya Mika Mata yace "mahaifanki ne, kiyi sauri kuyi magana, Zan koma office ne Kuma Bana son wani ya ga na Baki wayata kina waya". A sanyaye ta amshi wayar tana kallon yadda yake tsuma fuska cike da tsoro.ikon Allah wai mijinta Kenan .

Sosai Mallam Umar da Hajara suka jidadin Jin muryar yarsu.

Hajara tamkar zata kutso ta shigo cikin wayar saboda tsabar farinciki, tambayoyi take ta zubo Mata kamar su , "yaya gida daya ya hadaku da matarsa? Yaya iyayensa suka karbeki? Yaya yanayin zamanku da Taufiq? Yaya muamalar ki da abokiyar zamanki?, Kina jindadin Zaman garin?.

Ire iren wadannan tambayoyin take ta jeroma muhseena su, Wanda ko amsa daya ta kasa bata.

Maimakon hakama cewa tayi "Inna kuyi hakuri, musamman ya dawo daga office saboda ya kawo min waya mu gaisa saboda kullum kuka Kira ana Shan bam bam, yanzu haka office zai koma idan ya dawo zansa ya Kara Kiran ku".

Malllam Umar yace "Shi yasa ai ban so kika bar mana wayar hannunki ba kinga da yanzu ko yaushe zamu dinga kiranki ba tare da mun takura masa ba". Mujaheeda tace "to Baba da ban bar muku ba sai dai kullum Kuma kaje kana Aron waya kana Kirana ".

Dai dai lokacin Taufiq ya leko alamar ya Matsu,a hankali tasa hannu ta katse wayar ba tare da sunyi sallama ba.

Ta Mika masa wayarsa, ya amsa Yana kallonta yace "Me yasa kika kashe ba tare da kunyi

sallama ba". Tayi masa kallon tsaf sannan tace "saboda Ka Matsu Ka amshi wayarka don cike kake da fargabar Kada wani ya ganmu ko?"

Ba tare da yace uffan ba ya juya ya fice , Bai zauna a gidan ba fita yayi a gaggauce

Muhseena ta kwantar da kanta hawayen da baya rabo a idonta ya cigaba da fita.

TO BE CONTINUE

DAGA TASKAR YAR GIDAN IMAM

NI MA MATARSA CE

52

Hajara ta dubi Mallam Umar har yanzu akwai sauran damuwa da ràshin nutsuwa a tattare da ita.

Tace "Mallam anya kuwa kana ganin abubuwa nan zasu daidaita kuwa, ina ganin muhseena tamkar bata Sami nutsuwa ba a jigawa".

Ya dubeta cike da karfafa guiwa yace "ki daina irin wannan tunanin, dole kema kinsan baza'a Sami abinda ake so ba yanzu, amma ina da yakinin sannu a hankali komai zai tafi yadda yakamata, don haka koma dai menene yanzu ayi ma kowa Uzuri". Hajara ta jinjina Kai kwarai tana tausayin yarta, tun daga ranar da tabar gabanta bata Kara Samun nutsuwa ko farinciki ba kullum tana cikin tsoro , damuwa da fargabar abinda Ka iya zuwa ya dawo.

Tayi shaawar ace muhseena ta auri Kabir ko don irin son da yake Mata duk da yasan ita wacece, tayi Imani a gun Kabir ne kadai muhseena zata Sami duk abinda take so na game da farincikin rayuwa, amma Allah Bai hukunta Kabir a matsayin mijinta ba sai Wanda mafarkinsu bai taba Basu ba wannan kadai ya isa ya Kara tabbatar da cewa aure kaddara ne babu makawa sai Ka auri duk Wanda ya rubuta a cikin allon kaddararka Ko da sonka ko ba sonka.

Domin Hajara tasan har abada Kabir bazai taba daina son muhseena ba. Don ko bayan faruwar lamarin Kabir yayi ta Kiran waya amma muhseena bata dauka bayan tafiyarta ma yayi ta Kira sai da Hajaran ta dauka ta tabbatar masa da duk abinda yafaru Wanda dama Karin bayanin yake nema abisa abubuwan da ya Sami labarin faruwarsu.

Hajara ta gaya masa yanzu itace ke amfani da wayar da layin domin muhseena ta wuce gidan mijinta.

A ranar Kabir ya Kara tabbatar da son da yake ma muhseena daga Allah ne, yayi kuka tamkar wani karamin yaro ya so ace Shi ya auri muhseena domin ya jiyar da ita dadi ya bata dukkan farincikin da ta rasa ,Amma ba haka Allah ya kaddara ba. Aranar Kabir ya tabbatar ya rasa muhseena, ya Kuma rungumi wannan kaddarar tare da yi Ma ta fatan alheri a duk in da take.

Wanda itama Hajaran irin addu'ar ta ke Ma ta a ko wane lokaci. Amma dai tabbas tana cikin damuwa, sai dai tana kokarin boyewa saboda bata son karama mijinta damuwa akan damuwar da yake ciki.

Ta bangaren mujaheeda kuwa sosai take son ta cika alkawarin da ta dauka, na taimakama

muhseena tayi karatu. Ta toshe kunnanta daga dukkan wasu maganganu da mahaifiyarta take yi .

Domin ta Sami goyon bayan daddy da mijinta, ita kanta mummy bata San me yasa take da mugun zato akan muhseena ba, zaton da bata taba Dora Shi akan sauran masu aikinta ba.

Kawai dai abinda mujaheeda tasama ranta shine jinin Haj murjanatu da na Zainab bai hadu ba, Dama Kuma ko'ina ana iya Samun wannan dabi'ar kaga babu abinda mutum yayi maka amma Ka ji aranka Sam baka son Shi.

To haka ta ke tsammani ga Haj murjanatu.Domin duk tambayar da zata Mata akan me yasa bata son muhseena takan bata amsa ne da cewa hakanan nake Jin araina bana Sonta na tsaneta. Sai dai abu days mujaheeda ta dogara da Shi shine tasan ko a dade ko ajima muhseena zatasa Haj murjanatu ta so ta ko don kyawawan halayenta.

A wañnan lokacin muhseena tayi Saar an kusa Fara biyan jarabawar Jamb. Hakan yasa ana Fara biya mujaheeda ba tayi kasa a guiwa ba ta biyama muhseena. Murtala na kamfaninta tasa ya samo Mata malamin da zai dinga koyar da muhseena a gida.

Martaba da mutuncin mujaheeda ya Kai kololuwa a wajen muhseena sosai take Jin ta a cikin ranta. Wannan abinda tayi Mata ba zata taba mantawa da ita a rayuwarta ba, wani so ta ji tana Mata na musamman.

Haka malamin ya cigaba da zuwa Yana koyar da muhseena karatu, bayan ta Gama dukkan hidimar gidan, ta dage sosai ta cire komai ta fuskanci karatunta .

Ba'a Dade ba aka fara rugistar jarabawar fita na babbar sakandire nan ma wata makaranta me kyau mujaheeda tasa murtala ya je ya biya Mata. Ta Kuma biya wasu kudin ciki hàrda na uniform domin muhseena zata dinga zuwa makarantar tana cigaba da karatu tare da wadan da zasu fita har zuwa lokacin da zasu Jana jarabawar .

Matuka muhseena ta jidadin da bai misaltuwa. Amma abu daya ta Lura da Shi, duk wañnan hidimar da mujaheeda ta ke yi itace take yi a aljihunta, bugu da Kari Kuma ta Lura sosai babu wani neman shawara ko shigo da Taufiq cikin duk wañnan lamarin.

Alama ce me karfi take nuna Mata, tamkar Taufiq baida wani karfin iko a gidansa domin baida maraba da Dan amshin shata duk abinda matarsa tayi ra'ayi tayi niyya baya iya hanata.

Abubuwa da dama suna yi Mata nuni da cewa mujaheeda fa ba Saar ta bace babu yadda zaayi ta Kira mijinta da nata, hakan ya Kara taimakawa wajen Kara aje Taufiq da aurensa a gefe, sai dai tayi alkawarin killace kanta a matsayiinta na matar aure, zata bi duk abinda addini ya Dora Mata a matsayin ta na matar aure ,har zuwa lokacin da Taufiq zai saketa domin dai tasan shi Kansa baya bukatar ta , me Mata kamar mujaheeda Mai zaiyi da ita yar kauye mara ilimi gara ta tsaya a matsayin ta.

Hakanan Taufiq ya Sami Kansa da Jin Sam bai jindadin alakar muhseena da mujaheeda kullum cikin faduwar gaba ya ke,Yana kokarin danne fargabar sa.

A kullum Yana kokarin kafin mujaheeda ta dawo office ya dawo gida ya shammaci su uwale ya kaima muhseena waya tayi waya da mahaifanta, saboda yadda suke kwazzabarsa da Kira a kullum Wanda sosai ya ke ji aransa tamkar basu yarda da Shi ba da alama akwai shakku a cikin

ransu.

Sosai ya na son ya dinga tsayawa Yana Jin maganganun da suke yi ,Amma Bai iyawa saboda tsoron wani ya ganshi.

Sau tari ya na mamakin yadda muhseena ta Sami nutsuwa ta aje komai na damuwa take harkarta tamkar bata da damuwa.

Sabanin Shi da kusan duk fitar numfashi sai ya tuno tsaka Mai wuyan da ya ke ciki Kuma kusan duk tunaninta a kanta ya ke karewa.

Shin hakan na nufin muhseena bata da damuwa ne Akan duk halin da suke ciki?. Kuma tana tunanin makomar wata shakuwa mara amfani da ke shiga tsakaninta da matarsa.?

Ko office ya ke baida sukuni, in dai zai bar mujaheeda da muhseena tare to yakan rasa natsuwarsa har ya koma gida.

Yau tunda ya tashi office din ma ya ji baida shaawar komawa gida. Hakan ne yasa ya wuce gidansu.

Yana zaune a tsakiyar kafet din da ya malale dakin mahaifiyarsa.

Kallo da ya zakayi masa kasan ba ya cikin walwala.

Haj saratu ta shigo dauke da damammiyar fura ta Mika masa tana kallon fuskarsa.

"Ga fura nan Ka sha gama Naga alamar kamar babu abinda Ka ci, ana Shirin Kiran sallar magriba, ko azumi kake yi?.

Ya girgiza Kansa Yana amsar furar "aah Bana azumi ".

Ta Kona ta zauna tana kare masa kallon tsaf tace "To meye amfanin Zama da yunwar da kake yi".

Ya kurbi furar ya dago Yana kallonta yace "Bana Zama da yunwa umma".

Ta sakar masa wani Dan kallo tace "Tunda bansan yanayin Ka ba idan kana Jin yunwa, dubi bakinka duk ya bushe".

Shuru ya yi Yana cigaba da Shan furar duk da itama ba dadi take masa ba a bakin.

Haj saratu ta dan numfasa tace "tsawon lokaci tun dawowarka da ga aiki, duk sanda zaka zo gidan nan ina Lura da yadda kake cikin damuwa, na Jira na Jira tare da sa tsammanin zaka zo Ka Sami akan matsalar ta Ka amma har yanzu shuru kuma a kullum haka nake ganinka babu wani canji".

Gaban Taufiq ya cigaba da faduwa, tabbas Yana cikin muguwar damuwa amma har yanzu baya Jin lokaci yayi da zai gaya ma mahaifiyarsa wannan sirrin da yake ta fama da Shi, sai dai yanayin sa zai ja tonuwar asirinsa shin me yasa ba zaiyi koyi da muhseena ba wajen boye damuwa da fauwalama Allah komai.

"Da Kai nake magana"

Cewar Haj saratu tana cigaba da kallonsa. Ya Dan yi murmushin karfin hali sannan yace "dadi na da ke umma akwai Lura".

Itama tayi dan murmushi ta ce to idan ban Lura da Kai ba wa Zan Lura da Shi".

Ya jinjina Kai yace "Tunda na dawo umma Bana jindadin jikina, ko yanzu da ga asibiti na ke na biyo nan".

Tace 'haba ko da na ji, ni dai nasan akwai damuwa, kasan ràshin sabo da waje Yana sa haka Kuma nasan kasha cizon sauro dama dole ya taba Ka , ga zazzabin maleria me shegen nacin tsiya".

Ya janyo filon kujerar ya aje a kasa ya kwanta . Yana fadin "kamar kinsan maleria ce ". Tace "ahaf ai nasan bazai wuce ita ba Allah ya Baka lafiya saika dage da Shan magani, ko na Kira Haulat ta dakko maka magani a motar ne".

Da sauri yace "aah ai babu na dare sai gobe kuma". Tace "to Allah ya Baka lafiya". Ya canja hirar da cewa "wai ina ma Haulat dinne ban ganta ba tun shigowata ".

Tace "tana can bangaren Abbanku tana gyara masa yau tsafta ake ji". "Ai gara da zaman banza" tace "Autar tawa ce ke zaman banza".

Dariya kawai ya yi ya maida Kansa ya kwantar.

Haj saratu tace "ya matar ta Ka, tana ta zuwa asibitin ko awo". Yace "eh tana zuwa"

Haj saratu tace "ita dai bata rabo da masu aiki sai kace me yaya dari, tunda ta Saba Zama da guda uku dole sai ta cike". Ya dan numfasa yace "hmmm mujaheeda ce fa".

Haj saratu tace "sai dai wannan Karon Naga kamar ta yi dace da ta kwarai, zuwa biyun nan da nayi gidan na duba jikin mujaheeda ba kaga yadda yarinyar tayi ta min ba akwai mutunci da girmama manya, gata da nutsuwa gaskiya ta kwanta min arai".

Da sauri ya dago ya na kallonta yace "ta kwanta Miki arai umma" tace "sosai kuwa duk inda ta fito wannan yarinyar lalle ta Sami tarbiyya, Allah yasa ta Mata rukon amana".

Hakanan Taufiq ya ji ya na matukar jindadin irin yabon da mahaifiyarsa kema muhseena. Har wani murmushi ya ke yi.

Ya so yayi Mata bayanin yadda mujaheeda ta dakkota amma dole yayi shuru saboda mujaheeda tace bata son gidansu su San ta buge wata a mota.

Haka Taufiq yayi shuru Yana Jin irin yabon da muhseena ta ke samu daga mahaifiyarsa. Haulat ta shigo tana masa sannu da zuwa cikin kulawa ya amsa Mata ya Kara da cewa "kin Gama aikin" tayi murmushi tace "Na Gama".

Haj saratu ta dubeta tace "Ai ina gaya masa kirkin yar aikin matarsa ne Zainab". Haulat tace "hmmm gaskiya yanzu anti mujaheeda tayi yar aiki tana da natsuwa da kirki sosai".

Haushiin yadda ake Kiran muhseena da yar aiki ya ke yi sosai sai dai babu damar ya nuna. Haka sukayi ta hira wani yasa Baki wani yayi shuru. Har aka Kira sallar magriba ya tashi ya yi musu sallama Akan da ga masallaci gida zai wuce idan Abbah ya shigo a gaushe Shi, har mota Haulat tayi masa rakiya.

Bai shiga gida ba sai bayan issha'i.

Tun daga kofar falonsa ya ke jiyo sautin karatun kur'anin muhseena cikin kyakkyawan tajweed da Kira me dadi.

Wani irin farinciki ya ji Yana kwasar sa.

Daga bisani ya shige cikin falon.muhseena ce zaune tsakiyar su uwale da hassi tana Kara

musu karatu.
Rabon da ya ji irin wannan karatun a gidansa to ba ma zaice dai ya manta ba tunda dai Bai taba ji ba.
Domin in dai ba a sallah ba bai taba Katarin ganin mujaheeda tana karatun kur'ani ba , barta dai da Danna ways amma ba karatun kur'ani ba. Nan da nan ya ji wani nishadi Yana shigarsa.
Ya so ya tsaya ya kalleta son ransa Amma ba hali, dole ya shige daki . Yana shigewa muhseena ta umarcesu da su koma dakinta ta cigaba da yi musu a can.

Taufiq Yana shiga daki ya tadda mujaheeda kwance Kan gado gefenta kayan ciye ciye ne da lashe lashe. Tunda cikinta ya yi girma son jikinta da sangarta suka Karu bata yin komai hatta office a yau ta yanke shawarar ba zata Kara zuwa ba sai bayan ta haihu. Taufiq na cikin cire Kaya ya shiga wanka take gaya masa abinda ta yanke.
Gabansa ya Fadi domin Bai jidadin hakan ba, tunaninsa daya shine ta yaya zai dinga dawowa Yana kirama muhseena iyayenta suna gaisawa.
Ya dan dubeta yace "eh ai dama Yana da kyau ki huta".
Tayi murmushi tace
"Gaskiya kam, ciki akwai wahala yadda baa iya bayyanawa". A gajarce yace "Allah ya Raba lafiya". Zai shiga bandaki Kenan mujaheeda tayi karaf tace "yaya Taufiq kaji wata irin Kira"a a gun Zainab, kullum suna karatun nan sai naji kamar ni ma na je na zauna ta koya min".
Ya tsaya ya juyo Yana kallonta yace "me yasa to ba zaki je ki zauna ta koya Miki ba".
Ta dan turbune fuska tace"haba ai sai su raina ni".
Ya dade Yana kallonta
Kafin yace "yanzu a neman ilimi har akwai raini".
Tace "don Allah kabar maganar nan, ta yaya Zan shiga cikin Yan aiki yar aiki Kuma ta koya min karatu, ni fa na fada ne kawai Kuma na Kara da kamar bance wai Zan zauna ta koya min ba".
Ya shige bandaki ba tare da yace uffan ba. Komai tsiya dole dai sai mujaheeda ta dakko wani da ga cikin halayyar mahaifiyarta. Mujaheeda tana da girman Kai.
Shi yasa ya ji Yana girmama muhseena da har ta aje komai ta Zama me aikin kishiyarta , yasan babu digon girman Kai acikin jinin muhseena.
TO BE CONTINUE

DAGA TASKAR YAR GIDAN IMAM
NI MA MATARSA CE
53

Wannan Daren kamar ko wane dare a wajen muhseena ta kasa yin bacci.
Tana zaune Kan sallayarta bayan idar da sallar nafila tana rike da kur'ani tana karantawa Shi kadai ne kesa zuciyarta natsuwa da Samun sukuni.
Bata gushe tana karatun ba ta fashe da kuka me motsa zuciya.
Ta maida kanta ta kwantar tsakanin cinyoyinta tana cigaba da kuka.
Ta fahimci duk yadda ta Kai da juriya da jarumta gami da sadaukarwa hakika ba zata taba fitar da damuwa da tashin hankalin da take ciki ba

Hakika ba abu bane Mai sauki ace ki zauna a karkashin kishiyarki.
Babu Wanda zai iya kwatanta zafin da take ji.
Amma tana da rauni babu yadda ta iya bata da zabi. Idan har tace Ba zata zauna a gidan nan ba, to ina zata zauna?, Bata da inda zata zauna, sannan idan tace bazata zauna a gidan ba ya zatayi da iyayenta da kullum suke tunanin tana tare da mijinta.ko kadan bata son iyayenta su shiga damuwa adalilinta , tuntuni itace silar damuwarsu duk wani yatsa da ake nunama mahaifiyarta a kauyen Durmi saboda itane, duk wani bakin jini da ràshin kwarjini da mahaifiyarta tayi saboda itane,
Shin ta ya ya zata cigaba da Zama silar bakincikin mahaifiyarta da bata da kamarta a duniya.

Hakika ko don mahaifiyarta Zata iya jure zaman gidan nan ko da ana wulakanta ta ne, balle babu Wanda ke wulakanta ta. Ya kamata wannan auren nata ya Zama garkuwarta ba hanyar lalacewa da komawarta baya ba.
Babu yadda zaayi ta zauna ta kashe kanta Akan tunanin auren da bata San maanarsa ba, auren da mijin bazai iya nunata ba ko fadar ma ya aureta ba.

Hawaye ya Kara balle Mata da zafi, abin Yana yi Mata ciwo, Amma babu yadda ta iya. Bata fushi da jarabawar ubangiji duk abinda ya yi Mata dai dai ne tana Kuma godiya a gare Shi .

Mahaifinta a jigawa ya ke, shin Ya na mace ne ko Ya na raye?. Tsanarsa ce me yawa acikin zuciyarta ko kadan bata son tuna Shi Amma hakan ya faskara domin kullum sai tunaninsa ya fado Mata arai.shin waye Shi? Idan ya na raye ne ya na ina ne?.
Matsaloli sunyi Mata yawa Amma tana da yakinin cewa duk tsanani ya na tare da sauki kamar yadda Allah ya fada, don haka tana nan tana jiran saukin domin ta bar komai a hannunsa don shine majibancin lamuranta. Tayi kuka tayi addu'a mara adadi.

Washegari da wuri muhseena ta Gama duk aikace aikacen gidan.ita Kuma ta dafama mujaheeda duk abinda take son ta ci.
Asabar ce Taufiq ya na gida babu inda ya fita.

Yana kallon irin kaiwa da dawowar da muhseena ta ke yi. Hakanan yake Jin wani kuna acikin zuciyarsa ta yarda aka sakarma muhseena duk wani aiki a gidan. Hatta su uwale tun zuwanta gidan suka Mike Kafa ita ke komai a gidan.
Zuciyarsa bata masa dadi ya rasa dalilin da yasa ko kadan baya son ya ga muhseena cikin wahala yakan rasa nutsuwarsa Sam.
Bazai iya Jura ba , hakan yasa ya tashi zai fita. mujaheeda ta Dan dube Shi tana kwance turus cikin duk ya sukurkutar da ita daya daga cikin dalilan da yasa tace bata son ta haihu a wañnan lokacin.
Tace "idan zaka dawo Ka tsaya Ka Dan sayo min wayar da bata wuce dubu dari ba"
Ya dubeta Yana shirin magana ta rigashi "Zan tura maka kudin".
Ya gyara tsaiwarsa yace "saboda nace Miki bazan sayo ba, ko ba ni da kudin sayowa". Ta juyar da Kai tace "ni bance ba".
Ya jinjina Kai yace

"Wa zaki Saima wayar"
Tace "Zainab nake so na Saima saboda duk su uwale suna da waya ita Kuma bata da ita, duk da dai ba ta da Wanda zata bugama amma ayanzu tana bukatar waya ko don karatunta".
Wani dadi yaji ya ratsa zuciyarsa, abinda yake ta so kenan ya samu yadda zai mallakama muhseena waya.
Amma azahiri Bai ko nuna jindadinsa ba , maimakon hakama sai ya wani gintse fuska ba tare da yace uffan ba ya fice. Dai dai lokacin ya yi kacibis da muhseena da sauri zata fita.
Baisan sanda yace "ina zaki?.ta tsaya cak tana kallonsa ahankali tace "malamina ne ya zo , zanje daukar karatu ne"
Ya tsareta da wasu tsararrun idanunsa yace "ki koma ki sa hijab ki cire wannan gelen" Yana Gama fadin haka bai saurari komai ba ya wuce, ayayinda ta bishi da kallo.
Har ya bacema ganinta
Ta saki ajiyar zuciya.
Ji tayi ba zata iya kaucema umarninsa ba
Ahankali ta juya ta koma daki ta cire gelen ta Sanya dogon hijabi daya daga cikin Wanda mujaheeda tasai Mata .
Hakanan yake tafiya cike da nishadi Wanda baisan dalili ba.
Kai tsaye kantin saida manyan wayoyi Taufiq ya wuce.
Duk wayar da ya dakko sai yaga bata dace da muhseena ba, Amma yasan dole ya sassauta zabinsa saboda gudun zargi, yasan mujaheeda tana iya tambayar dalilin da yasa ya Saima muhseena waya me tsada bayan ga abinda tace, hakan yasa ya takaita zabinsa ba don son ransa ba, ya sayo Mata waya me kyau ta dubu Dari da hamsin.

Ya Kira salisu a waya ya sanar da Shi inda yake.
Daga wajen saida wayar Kai tsaye inda salisu ya ke Taufiq ya wuce.
Ya zabi salisu ne, amatsayin Wanda zai dinga bude sirrinsa awajensa saboda Shi kadai yasan ta inda aka faro.
Salisu na zaune
A Saman motarsa a bakin titi. Shima ya Sami gefe daya ya aje tashi motar suna fuskantar juna, ya karasa ya tsaya kusa da Shi. Cikin fara'a salisu yace cike da zolaya
"Ango kasha kamshi"
Ya sakar masa harara
Yace "An gogu dai, kasan Allah bana son iskanci zanyi maganinka".
Salisu ya saki dariya yace "yi hakuri mutumina ya akayi ne?".

Taufiq ya numfasa yace "kaima ai kasan matsalar". "To menene Kuma yanzu, ina ce hankalinka yanzu ya kwanta tunda kana tare da muhseena kana Jin motsinta Kuma lafiya lau matarka bata zargin komai asalima shine dalilin son ta zauna da mujaheeda ta Kuma taimaketa."
Taufiq ya numfasa yace "Ai taimakon ne Bana so salisu, saboda gudun abinda zai biyo baya, gaskiya ina son na dauki ragamar kulawa da duk wani bukatun muhseena ciki hàrda karatunta Amma na rasa yadda zanyi, na rasa yadda Zan bulloma al'amarin ".

Salisu ya jinjina Kai yace "eh Kuma gaskiya haka ne akwai cutarwa ace kishiya ce zata yi hidimar rayuwar kishiyarta, gaskiya bazan boye maka ba muhseena tana da hankali da ràshin daukar rayuwa da zafi don da watace da tuni ta tona maka asiri".

Yace "Shi yasa nake girmamata" salisu ya yi masa kallon tsaf yace"Aah babu wani girmamata da kake yi, in da kana girmamata ba zaka barta cikin rayuwar wulakanta ba".

Ya runtse idanunsa cike da takaici yace "Bani da zabi salisu".

Yace "Kai ko kake da zabi Amma Ka kasa gane komai, Kaine fa megida Ka Zama haka mana Ka gwada jarumtarka ta namiji".

Yace "ina kokarin yin hakan salisu amma kasan dole na bi a hankali, kaga matata ta kusa haihuwa, bayan haka tana da ciwon zuciya ina matukar tsoron halinda zata shiga idan komai ya bayyana".

Salisu yace "ita Kuma muhseena baka kwatanta halin da take ciki, tana kallon Ka tare da wata mace kullum a matsayin ta na matarka bata da damar da zata nemi yancinta, kana da adalci kuwa". Ya girgiza Kai yace "Bani da adalci salisu, Amma Kada Ka manta muhseena bata so na kana ganin don me Zan bata da wacce ke so na saboda wacce bata Sona?"

.....yayi masa wani irin kallo "ta taba gaya maka bata sonka?(Ya girgiza Kai) Kai kaddarama ta gaya maka bata son Ka, tunda Ka aureta dole kayi Mata adalci, ni ban San fa me kake nufi ba, nace Ka saki yarinyar nan kace Ka ma mahaifinta alkawarin cewa ba zaka saketa ba, nace Ka fadama kowa matarka ce kace kana tsoron halinda matarka zata shiga to wai me kake nufi?".

Taufiq ya yi kasa da Kansa komai ya tsaya masa ji yake yi kamar shine silar komai.

"To ni bansan me kake tunani ba, bansan abinda ke zuciyarka na".

Taufiq yace "babu komai azuciyata sai son na kyautatama muhseena amma na kasa tabbatar da hakan Amma tabbas zanyi kokarin kawo karshen duk wañnan al'amarin" .

Salisu yace "abinda ya dace Kenan, domin duk ranar da iyayen yarinyar suka San irin zaman da yarsu take agidan mijinta, kwarai da gaske zaka samu matsala".

Taufiq ya nisa yace "duk na gode da maganganun nan naka salisu domin gaskiya Ka gaya min," yace "ato Kuma ya rage ruwanka Ka dauka ".

Taufiq yace "to yanzu ya zaayi na dau ragamar kulawa da bukatun muhseena".

Salisu sannu a hankali ya Gama gayama Taufiq duk hanyar da zai bi don ganin kulawar muhseena ta dawo hannunsa.

Sun Dade suna tattaunawa daga bisani sukayi sallama.

Daganan wajen sayen layi Taufiq ya wuce, ya sai layi yayi Kuma rigista sannan ya kama hanyar gida, dai dai karfe shida da minti biyar.

Tun a harabar gidan ya fahimci suna da Baki a gidan domin ganin daya da ga cikin motocin gidan su mujaheeda.

Fata yake sosai aransa

Allah yasa ba Haj murjanatu ba ce ta zo, domin zuwanta gidan babu wani alheri adalilin tun Fara zaman muhseena a gidan in dai ta zo Saita wulakanta ta ko ta muzantata , baya son tun muhseena bata gane tsanarta tayi ba harta gane, hakanne yasa Sam yanzu bai son zuwanta gidan. Adduar sa bata ci ba domin direban da ke tsugune awaje ya tabbatar masa tare da uwardakinsa yake tun bayan azahar.

Taufiq yace aransa lalle ta Dade agidan , domin dai Yana fita gidan Kenan ta zo.

Hakanan ya shiga gidan cikin damuwa.

Yana shiga cikin falon

Ya tadda Haj murjanatu kishingide Kan kujerar hutawa gefe daya Kan doguwar kujera mujaheeda ce, ya Kara kallon gefen Haj murjanatu nan ya hango muhseena zaune tana aikin matsama Haj murjanatu kafafu.

Wani irin takaici yayi awon gaba da Shi.

Tunda muhseena ta hada Ido da Taufiq taga yadda fuskarsa ta koma tayi saurin yin kasa da kanta ta Kuma cigaba da abinda take yi.

A fusace ya ke amma irin kallon da Haj murjanatu ta tsare Shi da Shi ne yasa yayi saurin danne fushinsa. Ya yi Mata sannu da zuwa gami da gaisheta. Ta dai amsa tana cigaba da kallonsa. Ya Sami kujera ya zauna. Mujaheeda ta Dan dube Shi tace "sai yanzu". Yace "eh ya jikin" ta amsa "da sauki, bayan fitarka na ci abinci sosai fa", ya gyada Kai yace "haka ake so".

Kamar daga sama Haj murjanatu ta zungure muhseena da kafarta tace "da Allah ki matsa min a hankali sai kace zaki cire min kafar, Bana son bakar mugunta". Ta Karasa magana tana tsaida idonta Akan fuskar Taufiq tana son taga yadda zai nuna.

Jin abin yayi har cikin ransa, zahiri idan ya cigaba da Zama a falon nan akwai matsala don komai na iya fitowa, hakanne yasa ya Mike tsam ya shige cikin daki.

Mujaheeda ta dubi Haj murjanatu tace "haba mummy me yasa kike Mata tsawa haka".

Haj murjanatu ta jinjina Kai bata so Taufiq yabar falon ba ta so ya zauna ta cigaba da ganin yanayinsa da ta Fara zargi. Haj murjanatu ta sakko da kafafunta tana kallon mujaheeda tace "magriba ta yi , ni Zan tafi gida, ki cigaba da kulawa kinga dai jikinki yayi nauyi".

Tace "in sha Allah mummy badamuwa, kinga tun zuwan Zainab gidan nan na daina cin abincin restaurant, saboda ina jindadin abincinta ita ke dafa min duk abinda nake so ina jindadin abincinta".

Haj murjanatu ta tashi gami da juyawa ta dubi muhseena da take zaune kamar wacce zaace ket ta ruga saboda tsoro, sosai take Jin tsoron Haj murjanatu idan ta zo har wani tsuma take.

Tace "ta kyauta, sai ki Kara kulawa da abincinta da duk abinda take so, Bani da kowace damuwa Saita Yata don haka ki Kula". Muhseena tace "in sha Allah Zan kiyaye". Mujaheeda tace "mummy Zainab fa bata da wata matsala ". Haj murjanatu ta Kara kallon muhseena tace "Allah ya sa". Daganan ta balle jaka ta zaro dubu goma ta Mika Mata "gashi". Ta girgiza Kai tace "aah ki barshi kawai Haj nagode". Ta Dora Mata a Kan jikinta tana fadin "Bana yin kyauta aki Karba". Mujaheeda tace "ki Karba Zainab ".

Muhseena tace "to Nagode sosai".

Ta juya zata fita mujaheeda na kokarin tashi tayi rakiya ta hanata.hakanan ta tafi, zuciyarta na cike da sake sake da son ta Sami Dan wani shaida da zata kama Taufiq domin itafa bata yarda da yarinyar nan ba, bata Kuma yarda da irin kallon da Taufiq ya ke Mata ba. Amma ko kadan bata son ta Fara gaya ma mujaheeda abinda take tsoro agame da muhseena, don bata son ta sata damuwa acikin wannan yanayin. Amma tabbas tana Jin tsoron abubuwa da dama.

Taufiq na cikin daki sai ya Kai gauro ya Kai Mari bakinciki ya Gama cika zuciyarsa, Anya zai iya cigaba da Zama Yana sa Ido ana yima muhseena irin wannan wulakancin, gaskiya baiyi Mata adalci ba.

Yayi zaton mujaheeda zata shigo cikin dakin bayan tafiyar mahaifiyarta amma shuru bata shigo ba dole tasa ya Kara fitowa falon. Tana kwance inda ya barta, idonsa yayi shawagi a cikin falon Amma Bai hango muhseena ba, alamar tabar falon.

Ya nemi kujera ya zauna
Yana kallonta.

Yace "mujaheeda kece kikace kina son Zama da Zainab" ta dago tana kallonsa tace "eh wani abunne".

Yace "aah ina ganin dai dai yakamata ace kina tsare Mata mutuncinta, musamman a wajen mummy saboda irin abubuwan da take Mata Basu da amfani, don mutum baida kudi ai ina ganin ba abin wulakantawa ba ne saboda talaka da me kudi duk Allah ne yayi su".

Cikin ràshin zargin komai da kyakkyawar zuciya mujaheeda ta numfasa tace " Ni ma yaya Taufiq harga Allah Bana jindadin abinda mummy take yi Mata, ni na rasa abinda mummy take hange a tattare da Zainab , da kanta ta kawo min duk ma'aikatan gidana to meyasa bata son Zainab bayan ni banga wani aibu a tare da ita ba, Kuma akullum ina nunama mummy INA jindadin Zama da Zainab fiye da duk masu aikin gidan nan, amma na rasa damuwarta, tunda ta zo ta tadda Zainab na daukar karatu take ta min fada Akan wai Zan karar da komai na akanta Kuma ni mema na Mata."

Taufiq ya Dan gyara zamansa ya Fara magana daga cikin irin shawarar da salisu ya bashi, ya ce "Dama ina tunanin kamar don hidimar da kike yi da Zainab ne yasa mummy take da damuwa agame da ita, saboda haka ina tunanin Nima me zai hana muyi tarayya acikin Samun ladan rikon marainiya ".

Ta dube Shi tace
"Kamar yaya"

Yace "kamar daga yau ki bar min duk wata hidima da ta shafi Zainab na karatunta da komai ni Zan rage Miki nauyi na dinga yi Mata, sai kiyi kokarin Fahimtar da mummy cewar ba wata hidima da kike Mata kila a Sami saukin tsanar ba gaira ba dalilin da take Mata".

Mujaheeda ta numfasa ta gamsu da duk abinda ya fada, Kuma ko kadan babu zargi a cikin zuciyarta, domin abu ne da bata taba tsammani ba,don haka bata zaton komai.

Tace "hakane Kuma yaya Taufiq, aiko nagode shikenan kawai Zan gamsar da ita cewar kudin aikinta ne take yima kanta komai Kuma ba ni ke biyanta ba Kaine shikenan".

Sosai ya ji natsuwa a zuciyarsa ya shawo Kan wannan matsalar saura tarin sauran matsalolin. Ya Sami dan natsuwa.

Musamman yadda mujaheeda bata kawo komai a ranta ba.har suka cigaba da tattaunawa, daga bisani ya tashi ya fita zuwa mota ya dauka ledar wayar muhseena da ya barta a mota gudun Kada Haj murjanatu ta gani ta kafa kawo matsala.

Yana komawa ya Mikama mujaheeda yace "ga wayar ".
Ta amsa tana fitowa da ita tace "Kai Amma wayar tayi kyau sosai, gashi na manta nace Ka taho da layi". Ya zaro layin wayar ya Mika Mata yace "ni ban manta ba".

Ta Karba tana dariya
"Yauwa yaya Taufiq".
Ta Mika masa wayar tace "Dan sa mata layin ".

Ya amsa yasa layin ya gyara komai ya Mika Mata.
Ta amsa lokaci daya ta kwalama muhseena Kira ta amsa, kafin ta fito Taufiq ya tashi ya fice Yana Danna waya alamar zaije ya yi waya ne.
Da sauri muhseena ta fito.
"Gani Haj"
Mika Mata wayar kawai tayi , ta amsa tana kallo

Mujaheeda tace "wayar kice akwai layi da komai aciki".
Muhseena ta saki ajiyar zuciya kwarai tana bukatar waya, nan da nan ta shiga yi Mata godiya , tun tana amsawa har ta gaji. Cike da zumudi ta koma daki.
Ta fada Saman gado
Tana murna sosai, Kai wannan mace wace iri ce
Kirki da karamcinta ya wuce misali.
Sam bata jinta a matsayin kishiya. Sai a
Matsayin yar'uwa ta jini. Me yasa halin ta da na mahaifiyarta ya sha bambam.
Mamanta bata da kirki
Bata son mutane ga wulakanci da isgili, sosai itama take Jin tsanarta acan kasan zuciyarta.
TO BE CONTINUE

DAGA TASKAR YAR GIDAN IMAM

NI MA MATARSA CE
54

Burinta ta dinga yin waya da mahaifanta a duk sanda ta bukata , ba sai Taufiq ya zo ya kawo Mata wayarsa ba. Amma tasan dole tayi taka tsan tsan wajen yin wayar da su, tunda ta riga ta Kira kanta da marainiya a wajen mujaheeda.
A daran ranar, Taufiq ya Sato jiki ya shigo dakin ta, sosai ya ke jindadin yadda duk dare muhseena take raya shi da yin nafilfilu da karatun kur'ani. Domin ya Lura daya daga cikin dabi'unta Kenan.
Domin yau ma a zaune ya tadda ita akan sallayar. Cike da tsoro ta dago ta dube Shi tace "lafiya".
Ya na daga tsaye ya Mika hannu ba tare da ya amsa Mata tambayarta ba, yace "Bani wayarki". Ta nuna masa wayar tana jikin caji, ba tare da itama tayi magana ba. Ya wuce zuwa wajen wayar ya dauka ya Bude ya fito da tashi wayar ya dauki number Hajara ya sa Mata aciki, sannan ya bi duk ya gyara Mata settings din wayar. Yana gamawa ya maida wayar jikin caji, ya juyo ya dubeta sosai sannan yace "nasa miki number mamanki nasa miki kudi aciki zaki iya kiranta duk lokacin da kikaga Dama".
A hankali tace "Nagode"
Kafin godiyar ta Gama fitowa daga bakinta har ya fice daga dakin.
******
Lokacin zana jarabawar Jamb tayi, har muhseena ta zana.
Gaf da zasu zana jarabawar fita daga babban makarantar sakandire mujaheeda ta haihu. Wai

murna da doki wajen Taufiq baa magana ta haifi ya mace.

Gata fa mujaheeda ta sha Shi, domin alokacin muhseena ta Kara tabbatar da arziki da wadatar da mujaheeda ta ke da Shi. Haj murjanatu kacokan ta tare a gidan mujaheeda ko kunya bata ji, komai da ita ake yi. A wañnan lokacin wahala iya wahala muhseena ta sha ta a gidan saboda yadda Haj murjanatu take jibga Mata Komai ita ke yi su uwale sai hutu kawai suke yi.Duk da halin farincikin da Taufiq yake ciki to fa bai hana Shi fahimtar irin musgunawar da akema muhseena a gidan ba.

Karshe sai da Haj murjanatu ta Kure Shi yayi magana.

"Irin wannan aikin da ake hadama yarinyar nan gaskiya yayi yawa, me yasa ba za a dinga raba musu aikin da sauran masu aiki ba sai ita kadai zaa dinga ba irin wannan aiki ai yayi Mata yawa".

Haj murjanatu ta dube Shi sosai abinda take so ne ya samu tace " meye amfanin ta idan ba aikin ba ko bashi ta zo yi ba agidan" ya ce "Shi ta zo yi Amma ya dace a dinga Mata adalci".

Cike da zargi da fusata tace "An ki ayi Mata adalcin ubanta ne Kai ko yayanta daka damu da halin da take ciki ko kuwa akwai wata akasa ne bamu sani ba".

Dam gaban Taufiq ya Fadi, zaiyi magana kenan mujaheeda ta riga Shi shigowarta Kenan falon ta tsinkayi maganar da suke yi.

Tace "wace irin magana ce wannan kike yi mummy, meye akasa?, Haba don Allah". Ta dubeta cikin wani bushasshen murmushi tace "hmm ba zaki gane komai ba , saboda zuciyarki a tsarkake take, amma ki sani baa ba namiji amana, Kuma namiji ba Dan goyo ba ne abinda Baki taba tsammanin zaiyi ba Shi zaiyi kuma a gidanki a gaban idonki,".

Nan da nan mujaheeda ta rikice idanunta sukayi jajir tace "mummy ki daina hada mijina da irin wadannan mazajen da kike fada , don mijina ba haka yake ba , Kuma ba zai taba cin amanata ba, Kuma amanar ma ya rasa da wa sai da me aikina, aah don Allah ki bari Kada ki Kara wannan tunanin balle harki furta".

Haj murjanatu tayi wani irin murmushi me cike da tsohon bakinciki tace "ya kamata Ki daina wannan makauniyar yardar da kike ma mutane, kisa aranki Taufiq namiji ne kamar ko wane namiji duk halinsu daya ki yi gaggawar dawowa hayyacinki...?

"Don Allah mummy ki Bari" ta fada da karfi.

Taufiq ya numfasa yace "ki barta ta Fadi duk abinda take so Allah dai shine shaida, idan Kuma fadin ama wani adalci shine rashin kirkin namiji to na fada Zan Kuma cigaba da fadan abinda akema Zainab a gidannan babu adalci". Yana Gama fadin haka ya juya ya fice.

Mujaheeda tayi kasa ta zauna Kan kujera cikin tsananin bacin rai, wannan ràshin jituwar ta mahaifiyarta da mijinta ba karamin taba Mata rai yake ba, tace cike da damuwa "haka zaa zauna mummy kullum mutuncinki na yin kasa awajen surukinki, har ya zauna ya dinga gaya Miki maganganu babu Jin kunya Kuma mummy duk ke ce silar komai, yau idan kin dauki Taufiq amatsayin surukinki na hakika babu komai da zaki samu daga gare Shi face girmamawa da mutuntawa, ni dai haka ya isa don Allah mummy abari haka".

Ta zauna gefenta tana kokarin kwantar Mata da hankali, tace " ba zaki gane ba ne mujaheeda amma duk abinda nake yi saboda ke nake yi, ina kokarin nisantaki da fadawa damuwa da bakinciki ne", mujaheeda tace "me yasa kika kasa sanar da ni abinda yakamata na Sani sai dai kullum ki dinga alakanta kuskuren da kikayi da Wanda kike tunanin zanyi" tace "Zan gaya Miki mujaheeda idan lokaci yayi zaki ji dalilina, Amma kafin nan dole ki kiyaye da abubuwa da

yawa".

Mujaheeda ta kama kanta ta rike sosai ta gaji da komai ta gaji .

Yarinya ta ci sunan Haj saratu zaa dinga kiranta da Fadwa. Shima wajen sa sunan sai da Haj murjanatu tayi korafin don me baasa sunanta ba ko don baya kaunarta. Tunda Taufiq ya fahimci rigima Haj murjanatu take nema bai bi takan ta ba balle maganganun da take yi.

Duk wannan abin muhseena bai cika damunta ba, tunda yadda ta fahimci Haj murjanatu bata kaunarta haka nan ta fahimci Haj saratu tana matukar kaunarta. Kwarai tana jindadin yadda take nuna Mata a duk lokacin da ta zo gidan.

Komai ya lafa anyi suna .Ba'a Dade ba su muhseena suka Fara jarabawa, gaba daya ta maida hankalinta Kan karatunta.

Haka zalika an rage Mata mafiyawan ayyukan gidan saboda ta samu tayi karatun jarabawa yadda ya kamata. sosai Taufiq ya sa Ido akan jarabawar muhseena. Domin har makarantar yaje ya Sami wani ya biya Shi Akan ya dinga Kula masa da komai na muhseena.

A ranar da zasu Fara jarabawar ta Kira mahaifiyarta Akan tana bukatar adduarsu domin zata Fara jarabawa.

A ranar Tasha addua wajen Hajara da Mallam Umar ba adadi. Bayan sun gama wayar ne Mallam Umar ya dubi Hajara da take cike da farinciki bakinta yaki rufuwa, ya yi murmushi yace " kinga abubuwa suna ta gyaruwa ko?".

Tayi murmushi tace

"Eh, Dama adduar da Muke tayi Kenan kullum"

Yace "ai dama na gaya Miki komai lokaci ne Kuma dole muyi ma kowa Uzuri agame da wannan al'amarin da sannu Kuma komai zaiyi dai dai yanzu ba gashi ba, har ya sata a makaranta". Tace "oh Ashe da rabon dai muhseena zata samu cikar burinta na yin karatun boko, gaskiya Taufiq yayi min bazata ban taba tsammanin nan ta kusa zai karbi muhseena ba, balle har yayi tunanin inganta rayuwarta haka".

Mallam Umar yace cike da jindadi "Allah ubangiji ya Kara daidaita tsakaninsu, Allah yasa wannan aure ya Zama silar farincikin muhseena da korar duk wata damuwarta".

Hajara ta Dan gintse fuska tana kallonsa Ido a raunane.

Mallam Umar yace "menene Kuma". Ta saki ajiyar zuciya tace " Mallam damuwa ce ke Kara kamani a duk lokacin da na tuna Taufiq baisan komai ba agame da bakin fentin dake jikin muhseena ba, ina tsoron ranar da duk ya sani wane mataki zai dauka shin zai iya Zama da ita a haka ko zai rabu da ita ne". Malllam Umar ya jinjina Kai yace "ki kwantar da hankalinki komai na Allah ne, idan har Taufiq Yana son muhseena ko wane irin bakin fenti akayi Mata bazai dame Shi ba zai karbeta kamar yadda Kabir ya karbeta". Tace "To Baka ganin lokaci yayi da zamu Gaya masa gaskiya". Ya girgiza Kai "lokaci baiyi ba Hajara, domin ina son sai Randa na tabbatar Yana son muhseena Kuma ba zai iya rayuwa ba idan bata alokacinne nake ganin ya dace na sanar da Shi komai, domin alokacinne nake da yakinin bazai iya rabuwa da ya ta ba balle har ya sata damuwa".

"Da dai kun Gaya masa tun yanzu da ya fi don wannan boye boyen duk ba mafita ba ne, don dai baa canjama tuwo suna Kuma babu ta yadda zaka Zama mahaifin abinda ba Kai Ka Haifa ba". Cewar Ande Dije da ta fito daga daki. Malllam Umar ya dubeta rai bace yace "na rantse Ande da kinsan yadda nake ji araina idan na ji kina fadin ba nine mahaifin muhseena ba da kin daina fade, domin ji nake kamar kina goranta min ne agame da ràshin haihuwata". Ta Kada

hannu tace "la la ni ban taba yi maka gorin ràshin haihuwa ba, idan na Maka gori ai Kaina nayima, kawai dai irin zura jikin da kake yi ne akan muhseena naga yayi yawa hakanne yasa nake tunatar da Kai kullum cewar bafa Kaine mahaifinta ba". Hajara ta Dan yi murmushi tace "muhseena yar sa ce halak malak babu wani da zai amsa wannan sunan bayan Shi domin abinda ya yi Mata ko mahaifinta ne Shi iya abinda zaiyi Mata Kenan , don haka muhseena ba ta da wani uba bayan Mallam".

Ande Dije ta tabe Baki

Tace "Allah ya baku hakuri ". Ta juya ta cigaba da Kaye Kaye a tsakar gidan.

Cikin nasara da taimakon Allah, su muhseena suka kammala jarabawa sai fatan Samun nasara. Daganan kacokan ragamar kulawa da Fadwa ya dawo hannunta, ita ke Mata komai idan kin ganta a hannun mujaheeda to Shan Nono take yi. Duk yadda Haj murjanatu ta so ta hana mujaheeda mallaka Mata ragamar kulawa da yarta ta ki ta gane.

Ita Kam Haj murjanatu ko kadan bata son hakan domin ita kanta tasan illar da hakan ya jawo Mata a rayuwa.amma babu yadda zatayi tunda mujaheedar ta kasa fahimtar ta ta fi son tayi Mata bayanin da zata gane dalilinta to amma ba zata iya fada Mata dalilin ba. Don haka dole ta kyaleta ta yi yadda ta ke so.

Ita Kam ta bangaren muhseena abubuwa da dama sun Fara Mata sauki, a zuciyarta. Duk da komai na cikin zuciyarta ta to ta dage bata son ya taba Mata karatunta da ta daura dammara akansa.

Musamman a wani dare da Taufiq ya shigo dakinta. Aranar ta dube Shi sosai tana Jin wani irin nauyi a ranta a duk lokacin da suka hada Ido da Shi , tayi kasa da kanta tace "Bana son shigowar nan da kake yi dakina da daddare ina tsoron Kada wata Rana wani ya ganmu,". Taufiq yace Yana kallon tsakiyar idonta "idan wani ya ganmu ke ba matata bace?" Ta aje numfashi a hankali tace "hmm matarka ce a suna". Ya langabar da Kai gefe yace "ke matata ce ina da ikon zuwa duk inda kike". Tayi saurin canja maganar da cewa "yanzun dai me ya kawo Ka".

Ya natsu sosai ya Fara Mata magana "ina rokon kiyi hakuri da duk abubuwan da ke faruwa harga Allah ina son kawo karshen wannan matsalar Amma har yanzu Bani da wannan karfin guiwar". Ta dago Ido cike da hawaye tace "to yanzu me zanyi maka, kana son na amince Ka sake ni ne?" Da sauri ya dakatar da ita yace "Kada ki Kara wannan maganar, hakuri kawai na ke baki tare da tabbatar Miki da cewa komai ya kusa zuwa karshe," ta dube Shi tana kokarin goge hawayenta tace "Kada Ka yaudari kanka in dai da wannan dabi'ar taka zaka dauwama ba zaka taba iya Zama da Mata biyu ba, Kuma ma ni ba ni da matsayin da Zan shiga tsakiyarku saboda haka Ka je kayi tunani". Shuru yayi Yana nazarin maganar ta " me cece dabi'ar tawa?" Tace "kafi kowa sani".

Ya saki numfashi yace

"Dukkan nauyin karatunki da hidimarki duk sun dawo hannuna basa hannun mujaheeda, don haka ki cire aranki cewar mujaheeda ce ke hidima da ke, mijinki ne ya ke hidimarki kamar yadda Allah ya Dora masa".

Wani irin sanyi ne ya ratsa zuciyarta hakika ta jidadin wannan maganar domin ko banza ta fita daga cikin fargabar abinda Ka iya biyo baya wata rana.

Yana Gama Mata wannan bayanin ya Mike ya fice daga dakin.

Ta Kara goge hawayenta ta fada a fili "Allah ka kawo karshen wannan matsalar Amma tabbas

akwai damuwa ranar da duk mujaheeda tasan sirrin da ke boye".

Jarabawar su muhseena ta fito daga WAEC din har NECO da jamb duk muhseena ta Kara saa domin duk ta cinye hatta jamb ta ci makin da duk karatun da take son tayi zata yi Shi ba tare da matsala ba.

Hakanne yasa Taufiq bai sha wata wahala ba wajen Samo Mata admition a federal university dutse Kuma baa Sami wata tangarda ba wajen bàta course din da ta ke so wato engineering course din da yake wahalar yi ga mata Domin dai mawuyacin abune kaga mace yar arewa tana karatun engineering.

Aranar da Taufiq ya kawo Mata admition sai da tayi kuka saboda tsananin farinciki, domin dai burinta Kenan a duniya. Ita kanta mujaheeda ta jidadin Samun admition din domin tabbas tasan zata iya a irin kokarinta.

Babu wani bata lokaci nan da nan Taufiq ya Gama Mata duk wani shiri na makaranta. Ta Fara zuwa.

Da farko muhseena ta Sami rikicewa a makarantar saboda ràshin sabo amma daga bisani sai ta warware ta fahimci komai a makarantar ta Kuma daina bata tsoro.

Ta Sami kawaye da yawa amma da yake bata da raayin yin kawaye yasa guda daya ce ta zaba a matsayin kawarta. Hannatu yarinya mai nutsuwa da hankali, tamkar ba yar masu kudi ba,ko a shekaru ba zata wuce sa'ar muhseena ba.

Sosai muhseena ta maida hankalinta Kan karatunta domin Samun cikar burinta.

Zuwa tsawon wannan lokacin kuwa duk wani kaucewar da Taufiq yake yi agame da fadawa soyayyar muhseena to fa abu ya fassakara. Domin dai Shi Kansa zuwa yanzu ya tabbatar da cewa Yana son muhseena matukar so, son da baya Jin ya taba kwatanta Shi akan ko wace mace.

Muhseena duk inda yake baya rabo da tunaninta haka zalika ko bacci yake yi baya rabo da mafarkinta, yarinyar da baya son wani ya kalleta Yana tsananin Jin kishinta a ransa. Shin menene wannan idan ba so ba?.

Ko makaranta zata baya samun sukuni sai ya ganta da katon hijabi a jikinta. Sabuwar number ya samu wacce babu Wanda yasan Shi da ita da ita yake Kiran muhseena ko yaushe.

Sosai itama abin yake daure Mata Kai, domin ita kanta taga canji daga gare Shi. Hakanan zai bita makaranta idan ta Gama lectures ya dakkota ko da bata so. Irin tsoro da fargabar da take gani acikin kwayar idon sa kullum kwana biyun nan gaba daya ta daina gani.

Bugu da Kari ta Lura

Yana kokarin Zama jajirtaccen namiji a gidansa yanzu taga Yana iya sawa Kuma ya Hana idan Kuma mujaheedan bata bi abinda yace ba ta na Lura da takun sakan da suke yi. Shin menene dalilin wannan canjawar tasa?. Irin tambayar da takema kanta kenan kullum.

Yau asabar muhseena bata da makaranta.

Tana dauke da Fadwa wacce tuni harta Fara kokarin neman yin dabo tayi wayau sosai tayi girma hakora duk sun Fara fita Mata.

Wayar mujaheeda ta dauki ruri Dama wayar tana hannunta ganin Haj murjanatu ce ke Kiran yasa ta dauka da sauri suna Fara yin magana ta fahimci akwai matsala.

A gaggauce ta tambayeta "lafiya kuwa mummy" daga daya bangaren Haj murjanatu cikin yar damuwa tace "babanki ne bashi da lafiya muna nan asibitin da kike zuwa".

Cikin damuwa mujaheeda tace "subhanallah mummy akwai dai sauki ko" tace "to gashi nan dai tunda Muka zo asibitin dai Yana kwance likitoci na ta kokarinsu akansa".

Cikin rawar murya tace "gani nan zuwa".

Ta dubi muhseena tace "shirya Fadwa kizo mu tafi asibiti".

Itama cikin damuwa tace "waye ba lafiya, ba dai mummy bace ko". Ta tashi tana shiga daki tana cewa "daddy ne ".

Nan da nan suka Gama Shiri sai da suka fito sannan mujaheeda ta Kira Taufiq ta sanar dashi ta tafi asibiti duba Alh Mustapha labaran.

Taufiq yace "kina gaya min kin tafi ne ko kina neman izini".

Jin maganar tayi kamar daga sama, a fusace tace "wace irin magana ce wannan, to duka gaya maka da Kuma neman izinin tunda Naga wani isa kake ji kwana biyun nan". Ba tare da yace uffan ba ya kashe wayarsa .

Ita ce ta ja motar har zuwa asibitin.

Yau itace rana ta farko da muhseena ta Fara ganin Àlh Mustapha labaran a matsayin baban mujaheeda.

Domin duk tsawon zamanta a jigawa Basu taba haduwa ba, ko rakiya ta yima mujaheeda gidansu Basu taba haduwa ba sai yau.

Tunda suka shiga dakin asibitin Haj murjanatu ta Kara daure fuska daker take amsa gsusuwar muhseena daga bisani tasa hannu ta karbe Fadwa a hannunta ta riketa.

Sam muhseena bata damu ba domin idan da sabo ta riga ta Saba, tun ma abun na tayar da hankalinta har ta daina tunda ta fahimci kin ta Haj murjanatu take yi babu Kuma Wanda ya isa yasa ta so ta.

Mujaheeda ta matsa kusa da Alh Mustapha labaran tana Kiran daddy ya jikin.

Ya Dan motsa .ba tare da ya Bude idonsa ko ya amsa ba.

Har muhseena itama ta Matso tace "sannu ya jikin".

Jin muryar muhseena yayi tamkar wani abu Yana fisgar kwakwalwarsa da sauri ya Bude idanunsa gaba daya ya Dora akan muhseena.

Mujaheeda ta juyo wajen Haj murjanatu wacce keta wasa da Fadwa tace "mummy wai me ya same Shi ne". Ta dago ta dubeta tace " hakanan fa ya Fadi, to Allah dai ya rufa masa asiri Bai samu mutuwar barin jiki ba, domin likita ya tabbatar da cewa hawan jini ne ya kama Shi". Mujaheeda ta dafe kirji cike da damuwa tace "hawan jini Kuma,". Tace "iyi hawan jini, likita yace Yana matukar matsawa Kansa tunani da damuwa shine dalili".

Mujaheeda tace "to mummy tunanin me daddy zai dinga yi haka da har zai sa masa hawan jini". Haj murjanatu ta yi Dan Jim sannan tace "to wa ya sani".

Har yanzu Alh Mustapha labaran ya kasa dauke idonsa akan muhseena . Domin ita kanta muhseenan ta rasa dalilin wannan kallon da ya tsareta da Shi.

Har mujaheeda ta Kara dawowa kusa da Shi. Amma idonsa na kafe akan muhseena. A sanyaye muhseena ta bar bakin gadon ta koma can kujera ta zauna domin itama gaba daya ji tayi kafafunta sunyi Mata sanyi kamar ba zasu iya daukarta ba, kamar yadda taji sai kace an cire lakar jikinta.

Mujaheeda tana ta masa magana ya ci abinci Amma kokari yake ya Kara Nemo fuskar muhseena ya kalla.

TO BE CONTINUE

DAGA TASKAR YAR GIDAN IMAM

NI MA MATARSA CE

55

Ita Kam muhseena ta natsu a waje daya domin ta rasa irin bugun da zuciyarta yake yi. Fadwa ke ta kokarin kwacewa a hannun kakarta ta dawo wajen muhseena amma Haj murjanatu ta kwakume yarinya ta ki saki.

Har sai da Fadwa ta saka kuka me karfi Wanda ya dawo da hankalin mujaheeda kansu nan da nan Kuma ta fahimci dalilin kukan Fadwa.

Don haka ta baro jikin gadon Àlh Mustapha labaran ta dawo ta amshi Fadwa a hannun Haj murjanatu ta mikata hannun muhseena tana karbarta ta daina kuka ta kwanta lamau jikin muhseena tana maida ajiyar zuciya.

Haj murjanatu ta sakarma muhseena harara ta Kara hade girar sama da ta kasa. A yayinda Alh Mustapha labaran yake ta kokarin ta Shi idonsa Kuma na Kan muhseena.

Haj murjanatu ta karaso bakin gadon tana fadin "kayi a hankali, ikon Allah ko motsi me karfi baya yi tunda Muka zo asibitin nan, Amma ji sauki daga Allah har kokarin tashi ya zauna ya ke yi". Tana magana tana kokarin taya Shi jingina da filo.

Mujaheeda ta ce "Alhamdulillah Allah ya Kara sauki daddy". Alh Mustapha labaran ya amsa a hankali"Amin". Ta zauna a gefen gadon tana kallonsa tace "daddy tunanin me kake yi ne da har zai Haddasa maka Samun wannan mugun ciwon na hawan jini".

Kafin Alh Mustapha labaran yayi magana Haj murjanatu ta amshe maganar cikin fusata "duk dai abinda zai sa shi tunani da damuwa kinsan sirrinsa ne, da kuma kina son sanin damuwar tasa ai da baki taho da bare ba, ko kina tsammanin a gaban wannan yarinyar ne Alh zai gaya Miki damuwarsa ".

Hakanan Alh Mustapha labaran ya Sami Kansa da ràshin jindadin irin maganar da Haj murjanatu ke fade Akan muhseena. Mujaheeda tace "Kai mummy meya kawo wannan maganar Kuma".

Muhseena ta Mike ahankali rike da Fadwa ta dubi Àlh Mustapha labaran cikin faduwar gaban da batasan dalili ba tace "Allah ya Kara sauki, bari na jiraki a waje". Sam ji Alh Mustapha yayi baya son tafiyar muhseena hakanan yaji Yana matukar Samun nutsuwa idan ya kalleta.

Babu Wanda ya yi magana har muhseena ta fice daga dakin , sannan Haj murjanatu ta bita da tsaki Mai karfi.

Cikin ràshin jindadin fitar muhseena. Alh Mustapha labaran ya dubi mujaheeda yace "mujaheeda wacece wannan?".

Haj murjanatu ta sakar masa harara tace "meye na tambayar". Ahankali yace "saboda ban Santa ba Kuma ban taba ganinta ba". Mujaheeda ta dawo kusa da Shi sosai tace "daddy itace wacce na buge da mota daga baya nace zata zauna a guna,har Ka Goya min baya". Yace "oho itace" tace "eh itace, daddy ai mun sha zuwa gida Baka nan Shi yasa baku taba haduwa ba".

Haj murjanatu tace "to meye amfanin haduwar ta su ina ruwan mu da ita, ba dai ke kince kin ji kin gani ba to Allah ya bada saa".

Alh Mustapha labaran cikin jigatar ciwo yace "Kai Haj ki rage wannan izzar da isar ki daina

wulakanta mutane ina tabbatar Miki zaki sha mamaki wata rana ".

Ta ta so zata Fara hayagaga, mujaheeda ta dau Jakarta tayi sallama da Alh Mustapha ta fice ba tare da ta bi ta Kan Haj murjanatu ba.

Tun bayan tafiyarsu Alh Mustapha labaran ya koma ya kwanta ya rufe idanunsa.

Tunanin Zainab ne fal aransa,shin wacece ita da yake Jin wani shauiki a game da ita?.

Ya yi saurin Kauda tunanin da yake aransa, ya koma tunanin halin da yake ciki. Duk iya yadda zai yi ya boye danuwar halin da yake ciki abin ya faskara a yanzu , abubuwa da yawa suna damunsa baya cikin sukuni da kwanciyar hankali rayuwar kawai yake yi Amma Sam baya jindadinta.

Haka Alh Mustapha labaran ya cigaba da jinya likitoci na kulawa da Shi. Haka zalika baisan dalilin da yasa ya ke son mujaheeda ta dinga tahowa da muhseena ba idan zata zo duba Shi , ko ba ta zo da ita ba sai ya tambayeta me yasa Basu taho tare ba, takan Gaya masa tana makaranta ne Shi yasa basu taho tare ba.

Sosai mujaheeda tana jindadin yadda daddy ya karbi zainab fiye da mummy da bata kaunarta.

Ita kanta muhseenan ta fahimci ta samu karbuwa a wajen mahaifin mujaheeda, sai dai ita batasan dalilin da yasa take Jin acan kasan ranta tana Jin tsanarsa. Bayan Shi babu abinda yake nuna Mata sai kauna.

Jikin ÀIh Mustapha labaran yayi sauki har an sallame Shi Wanda kafin hakan Alh Yusuf lamido da Taufiq sun yi ta zuwa duba Shi .A Daren ranar da ya koma gida Haj murjanatu ta sa Shi a gaba, "Ai damuwa da bakinciki yanzu Ka Fara domin ba kaga komai ba, domin idan har laifin daka aikata bai Sami yafiya daga gare ni ba, to tabbas ba zaka taba Samun kwanciyar hankali ba, domin Allah baya yafe laifin tsakanin bawa da bawa har sai bawa ya yafema dan'uwansa, "

Ta dube Shi sosai tace "Kuma Ka dai San har yanzu ban yafe maka ba, Kuma Bana Jin Zan iya yafe maka, saboda munin abinda Ka aikata a gare ni".

Ya numfasa gami da runtse idanunsa, hakika da hannun agogo Yana iya dawowa baya hakika da ya dawo da Shi, domin ya gyara kurarensa, ya tafka kuskure mai yawa, wannan kuskure Shi yake Hana Shi sukuni a rayuwarsa, shine yake korar duk wani farinciki da ya doso Shi.

Shin ta yaya zai gyara kuskurensa Wanda ya Dade da yin nadamarsa? Ta ina zai Fara?

Wacce ya ke tare da ita da ya kamata ta Fara yafe masa mugun halinta ya danne tausayinta, baya Jin Haj murjanatu zata yafe masa idan yayi laakari da tsawon shekarun da yake bin ta ta yafe masa Amma ta ki, sai dai ta bishi da wata muguwar maganar.

Kamar ko yaushe idan suna yin irin wannan maganar ÀIh Mustapha labaran ya dago Kansa cike da jigatuwa na ciwo da nadama.

Sannan yace

"Don Allah Haj ki yafe min ki manta da wannan maganar , tsawon wannan shekarun kina hukunta ni da mummunan hukunci, ki barni na ji da sauran damuwa da tashin hankalin da nake ciki ki sassauta min ta bangarenki".

Tayi masa wani mummunan kallo tace
"Ai na gaya maka babu yafiya a tsakaninmu , raina Kuma bazai yi fari ba har sai ranar da Allah ya nuna min cewar ya kone Ka a wuta sakamakon abinda Ka aikata to a ranar ne zanyi farinciki mara misaltuwa, Allah ya kaimu lahira ranar da asirinka zai Tonu a wajen dukkan jama'ar duniya".

Tana gama fadin hakan ta fice daga dakin saboda yadda take Jin zuciyarta kamar zata Faso ta fito waje saboda tsabar bakincikin da kullum ta tuno Shi ta Kan ji tamkar ranta zai fita.

Wasu irin zafafan hawaye ne ya ji suna fita masa. Bai tsaida su ba domin yasan futarsu shine Samun saukinsa.

******

Kwanaki suna tafiya, muhseena na dada ganin canji a wajen Taufiq Wanda har yanzu ta rasa Gane wane irin canji ne.

Hankalinta na gun karatu amma duk da haka muhseena wani irin kyau da cika take na musamman tayi jawur Fata ta goge tayi luwai luwai sai kyalli take yi. Duk wani boyayyen kyawun muhseena da wahala ta boye da ràshin kwanciyar hankali yanzu fa ya fito.

Wanda ya Santa idan ya ganta daker zai iya ganeta. Kamar yadda akullum Taufiq baya iya dauke idonsa akanta, ko Yana tare da mujaheeda ne in dai muhseena ta zo wucewa sai ya tsaya ya yi ta satar kallonta, numfashinsa har kokarin tsayawa ya ke yi idan muhseena ta juya baya tana tafiya, saboda tsananin daukar hankalinta.

Yanzu babbar masifar da take damunsa bayan soyayyar muhseena harda matukar shaawarta yadda daker yake dawowa hayyacinsa.

Shi Kansa ya rasa wane irin so ne ya shige shi ba tare da ya ko gane hakan ba sai bayan da ya cinye Shi sannan ya bayyana Kansa.

Ranar jumaa Taufiq ya Kira muhseena a waya har zuwa wannan lokacin bata yi serving number dinsa da sunan komai ba number ce kawai har yanzu sai dai harta haddace number akanta saboda yawan Kira da kuma ta ganta tasan number sa.

"Kun gama jarabawa ko"
Ya tambaya a gajarce, duk da tayi mamakin tambayar Bai Hana ta amsawa ba "Eh mun gama", domin dai tasan bata gaya masa ta Gama jarabawa ba.

Taufiq yace "Duk da haka gobe ki shirya ki sanar da mujaheeda akwai abinda zakuyi a makaranta , idan kin fita ki Jira ni a inda na ke ajeki idan na dakko ki daga makaranta".

Muhseena ta so tayi masa tambayar dalilin yin hakan amma bai bata Dama ba domin ya na Gama yi Mata maganar ya kashe wayar.

Ta uni cikin tunanin me Taufiq yake nufi? Ina Kuma zasu?.gashi Sam bata iya ketare umarninsa don haka tun dare ta sanar da mujaheeda batun zata je makaranta gobe, mujaheeda bata ko tambayi dalilin ta na zuwa ba bayan ta gaya Mata sun gama jarabawa domin dai tasan shiga makaranta zai iya kama ko wane dalibi ko da ace ya Gama jarabawa.

Cikin dare bayan idar da sallolin ta na nafila text din Taufiq ya shigo wayarta "ki fito da wuri ". Kawai abinda ya turo Kenan.

Ta jinjina Kai ta maida wayar ta aje.

Washegari da wuri ta tashi ta kammala ayyukanta.

Tana karasa goge falo Taufiq ya fito cikin kyakkyawar kwalliyarsa zai fita, tsayawa yayi sosai

Yana yi Mata wani irin kallo na me kike yi har yanzu Baki shirya ba.
Ya jinjina Kai gami da nunata da Dan yatsan sa ba tare da ya ce komai ba ya fice.
Nan da nan muhseena ta koma daki ta kama shiri.
Cikin kankanin lokaci ta Gama shiryawa.itama bata tsaya karyawa ba ta fito dauke da Fadwa da tun da ta tashi da asuba mujaheeda ta kawo Mata ita. Bacci take sosai ahankali ta shiga dakin ta kwantar da ita a kusa da mujaheeda da take ta kwasar bacci tabbatar ma cikin bacci ta yi sallama da mijinta .
Ita kanta muhseenan tasan akwai abubuwa da dama da mujaheeda take bukatar shawara akan su, ciki kuwa harda yanayin zamantakewar ta da mijinta. Ta yarda mujaheeda tana da kirki kwarai amma ta samu tawaya a wajen kulawa da mijinta.
Ta Kada Kai ta juya ta fita ba tare data tayar da ita daga baccin ba.
Zaune cikin motarsa ta tadda Taufiq Yana zaman jiran ta.ta bubbuga gilas din kofar hakan yasa ya gane ta iso.da sauri ya Bude Mata kofar motar ta shiga cikin sallama gami da rufe kofar.

A gaggauce ya ja motar suka harba titi.

"Ina kwana" ta katse shurun da gaishe shi.ya dubeta ta gefe ya amsa, tun daga lokacin shuru ya Kara biyo bayan maganar.
Basu tsaya ko'ina ba sai wajen cin abinci.
Ta dube Shi alamun neman Karin bayani ya fito Yana cewa "Abinci zamu ci domin nasan Baki karya ba kema". Ta girgiza Kai tace "in dai don nice Kada kadamu mu tafi kawai".
Ya girgiza Kai
"Fito mu ci abinci"
Bata iya masa musu hakan yasa ta biyo bayansa har cikin wajen cin abincin.
Da Kansa ya yi umarnin akawo masa duk abinda suke so.
Sam muhseena ta kasa sakin jiki ta ci abincin saboda hakanan ta ji tana matukar Jin nauyin cin abinci a gaban Taufiq.
Don haka kadan ta ci abincin ta nuna ta koshi. Bai matsa Mata ba , shima yayi saurin kammalawa suka bar wajen Dama burin muhseena Kenan su yi su bar wajen kada wani da ya San Taufiq ya gansu.
Kai tsaye wani babban super market ya wuce.
Nan ma cike da taka tsan tsan muhseena ta bishi.
Wajen Kaya dinkakku ya Fara Kai muhseena ya dubeta yace "ki zabi kayan da zaki canja na jikinki da su, masu kyau sosai da tsada zaki zaba".
Sosai ta Fara mamakin abinda Taufiq yake nufi.
Duk da haka tayi abinda yace ta zabi Kaya masu kyau dai dai jikinta an hada Mata da gyale da takalmi da jaka.
An Kuma nuna Mata inda zata shiga ta gwada kayan.
Tikisa! ai alokacin da muhseena ta fito sanye da doguwar rigar shadda wacce ta ji ado daga sama har kasa, rigar ta lafe a jikinta tayi Mata cif tamkar don ita akayi .
Tayi matukar kyau nan da nan Taufiq ya gigice ya rasa natsuwarsa ya dinga Jin wani abu na shawagi a Saman Kansa , daker yayi kokarin mallakar hankalinsa.

Cikin rawar murya yace
" Sun yi Miki kyau sosai kayan, Ashe kin iya zabe".
Dan murmushi kawai tayi ba tare da ta ce komai ba. Sai dai da ta ji kudin kayan da ta dauka sai da ta firgice ta Fara fadin "wai ban San suna da tsada haka ba, Bari na cire a canja wasu". Ya Matso sosai daf da ita yadda har suna iya Jin bugun numfashin juna a cikin wata kasalalliyar murya yace "kin fi karfin wadannan kayan Wanda ma suka fi su kinfi karfinsu, Kyan da suka yi Miki ajiki ko nawa akace ba su ci kudinsu ba, Zan iya kashe ko nawa ne domin na cigaba da ganinki cikin wannan kyakkyawar kamar".
Muhseena ta yi matukar gigicewa da Jin irin kalaman da ke fita da ga bakin Taufiq tamkar Wanda ya fada komar soyayya.
Tayi saurin matsawa domin ta fahimci tamkar Taufiq yau ba dai dai yake ba.
Sai bayan ta matsa ne sannan shima ya fahimci irin subutar da bakinsa yayi.da sauri shima ya ja baya Yana kokarin tsare gidansa.
Haka suka dinga zaga super market din nan Taufiq Yana jidar kayan abinci shinkafa buhu biyu taliya kwali uku macaroni kwali uku katon galan din mangyada kayan shayi Maggi atamfofi kusan guda biyar shaddoji kusan Kala biyar da Karin wasu atamfofin guda biyu. Kai tun muhseena tana kirga irin kayan da ya ke diba har lissafinta ya bace.
Mamaki ma yawa ya kamata shin wannan bataliyar kayan na waye ? Shin yasan irin kudin da ya kashe kuwa?. Kuma taga ko a jikinsa.
Da ko suka je wajen biyan kudi. Komawa gefe tayi ta rakube saboda kudin da taji an yanko sunyi yawa. Amma sai taga ya fito da Katin bankinsa ya Mika musu domin su cire kudinsu.
Ta jinjina Kai lalle ko su wa yayi ma wannan sayayyar to suna da matukar muhimmanci a gare shi.shin wai me Taufiq yake nufi ne?.
Me yasa ba zaiyi Mata bayanin manufarsa ba don ta sani.
Daga boot din motar har kujerun bayan motar duk a cike suke da Kaya.
Muhseena ta kulle kayan da ta cire a cikin ledar da akasa ta nemi waje ta aje.
Yau dai tasa kayan alfarmar da bata taba sa irinsu ba a rayuwarta, shin yau ina zasu.

Hanya sosai Taufiq ya dauka. muhseena kuwa ta zuba tagumi tana kallon hanya tana sake sake aranta.
Kamar yadda shima Taufiq din ya dauke wuta. Tunani ya cika zuciyarsa hakika Yana son muhseena ya tabbatar da hakan, ya na Ji aransa zai iya komai saboda soyayyarta.
Ya waiwayo ya dubi fuskarta ,gabansa ya Fadi sosai domin har yanzu bai taba ganin wani alamun muhseena tana sonsa ba ko yaya ne a cikin idanunta.
A duk sanda ya kalli fuskarta ya yi Kuma Katarin kallon tsakiyar idanunta baya ganin alamun komai na so agame da Shi.
Babbar magana
Yanzu muhseena bata Jin irin abinda yake ji a ransa, bata Jin irin bugun da zuciyarsa take yi akanta.
Hakika akwai babban kalubale agabansa. Domin ya tabbatar har yanzu a matsayin auren dole ta ke kallon aurensu.
Ji yayi cikinsa na kugi wata sabuwar damuwar ta Kara yin awo gaba da Shi .

Tafiya tayi nisa , zuwa lokacin muhseena ta Kara cika da mamaki, domin ta fahimci hanyar Durmi suka kama.

Ta juyo ta kalle Shi a sanyaye tace "ina zamu je ne" idonsa nakan hanya yace "Durmi".

Wani irin dadi yayi awon gaba da ita.dama Taufiq Yana da irin wannan kirkin bata sani ba?.

Shin ko dai yasan irin yadda mahaifiyarta ta ke cike da son ta zo ta gansu ne?. Kullum su kayi waya maganar ta Kenan tana son su zo ta ga inda suke rayuwa.

Amma kullum sai kauce Mata take yi, domin dai tasan babu yadda zaayi ta Bari ta zo ta fahimci halin da ake ciki, zuwanta ba karamin damula komai zai yi ba.

Amma duk da haka tana cikin damuwar ranar da duk ta gaji suna iya tahowa jigawa ba tare da saninta ba.

Wannan zuwan da zasuyi shine kadai abinda zai kawo daidaito tsakaninta da mahaifiyarta. Domin dai duk tasan fargabarta Bai wuce wace irin rayuwa take yi a gidan mijinta. Amma wannan gani da zata yi Mata ta tabbatar zai Kori dukkan shakkun dake cikin zuciyar Hajara.

Yanzu ta fahimci dalilin Taufiq na bàta irin wannan Kaya na alfarma. To Amma Yana nufin duk wañnan kayan da ya sayo gidansu zai Kai?.

Bata gasgata hakan ba

Har sai da ta tambaye Shi tace "duk kayan nan da Ka saya kana nufin na gidan mu ne".

Ya gyada Kai yace "eh, ko sunyi kadan ne" ta yi saurin girgiza Kai tace "aah sun dai yi yawa".

Bai Kara magana ba itama haka illa tunani da ya cika ranta.

Sun Kai Durmi akan lokaci a dalilin gudun da yayi.

Irin dadewar da tayi rabonta da garin sai taga duk Ya canja Mata , duk da ba wani cigaba aka Kara samu a kauyen ba.

Suna tsaida motar a kofar gidan.

Mallam Umar Yana fitowa daga cikin gidan, alamar zai tafi wani uzirin.

Cak ya tsaya Yana kallonsu har muhseena ta Bude kofar motar cike da farinciki da dariya tana fadin "Baba".

Mallam Umar fara'ar sa ta fadada kallon mamaki ya kema muhseena, domin sai ya ga gaba daya muhseena ta canja ta Zama kamar ba ita ba , tamkar an canjata.

Cike da murna yace " muhseena kune ba zato ba tsammani kamar daga sama" cikin dariya tace "mune Baba".

Taufiq ya durkusa har kasa ya fito a suruki na gaske ya shiga gaida Mallam Umar.

"Taufiq tashi tashi don Allah, mu shiga ciki muje , muje".

Gaba daya suka jera zuwa cikin gidan.

Mallam Umar Yana kwalama Hajara Kira "Hajara fito ki ga abin mamaki".

Da sauri Hajara ta fito da ga dakin girki, tana son sanin dalilin wannan taratsi da Mallam Umar ya ke yi. Itama Ande Dije da sauri ta bankado labule ta fito daga baya.

Duka tsayawa sukayi suna kallon muhseena suna tunanin ita ce kuwa. Da gudu muhseena ta nufo Hajara ta rungumeta sosai sai hawaye.

Itama Hajaran hawayen take yi tana fadin "da gaske kece muhseena".

Taufiq tsayawa yayi kawai Yana kallon karfin kaunar da ke tsakanun Hajara da muhseena. sha'awarsu ya ke yi sosai.

Mallam Umar ya wuce da Taufiq cikin daki.daga bisani Su Hajara suka shigo Suma cikin dakin .

Ande Dije ta dinga gyada Kai kamar Wata tsohuwar kadangaruwa.cike take da mamakin wannan canjawa ta muhseena da ganinta tana cikin daula da jindadin rayuwa.

Shin hakan na nufin Mijin nata ya karbeta ne a matsayin Mata? Kenan muhseena bata da wata matsala kamar yadda suke hasashe.

Idan haka ne Kenan muhseena ta Sami daula ne , su Kuma ta manta da su tsawon wannan lokacin bata taba waiwayarsu ba sai yau.

Nan da nan Hajara ta shiga hidimar abinci Dana ta Gama gaba daya ta juye ta kawo ma su Taufiq.

Muhseena tayi mamakin. Yadda ya saki jiki ya ci abincin sosai fiye da yadda ma ta ci. Bugu da Kari ya saki jiki sosai sai hira suke yi da Mallam Umar hira me nuna alamun girmamawa da mutuntawa..

Muhseena ta numfasa a ranta tace "me yasa Taufiq ya ke yi kamar ya amshi mahaifanta a matsayin surukansa?".

Duk irin tambayoyin da Mallam Umar ya kema Taufiq a game da zaman Shi da muhseena Yana kokarin bashi amsar da babu yadda zaayi su taba zargin wani ràshin gaskiya a tare da Shi.

Hajara ta Sami nutsuwa iya nutsuwa, bata gajiya da kallon irin Kyan da yarta ta yi.ta Kuma fahimci ta na damuwa da gangan ne Amma yarta na cikin hannu na gari.

Ita kanta Ande Dije duk yadda ta so ta yi maganganun da ta Saba yau bakinta yayi shuru.

Sun Jima sosai don sai da Mallam Umar yace ya kamata su tafi haka, tunda ba kwana za suyi ba , to bai kamata suyi dare ba.

Nera dubu ashirin ya ajema Hajara ya ba Mallam Umar dubu talatin ya ba Ande Dije dubu goma, da ta gigita ta don murna da mamaki daker ta Sami bakin godiya.

Suma su Hajara sunyi godiya.

Amma Basu gigita sun dimauce ba sai da Taufiq ya fita da Mallam Umar. Yara suka Fara shigo da Kayan abinci.

Jikin bango kawai Ande Dije ta samu ta jingina tana cigaba da kirga duk abinda ake shigowa da Shi cikin rawa da tsumar hannu.

Tunda Mallam Umar ya tsiru a rayuwarsa Bai taba aje irin wannan kayan abincin a gidansa ba. Sai kace zaa Bude shago.

Ita kanta muhseenan tana jinjina abin aranta domin bata kallon Taufiq a matsayin Wanda zai iya yin irin wannan hidimar ba tare da ya wani girgiza ba. Shin hakan na nufin shima Yana da kudinsa na rufin asiri , kamar yadda mujaheeda take da arziki?.

Godiya dai da sa albarka Taufiq ya shata babu iyaka.

Atamfofin guda biyu da aka ware na Ande Dije ne.

Kai har suka bar kauyen Durmi Albarka ake Sanya musu Hajara ko da muhseena kuka suka dinga yi da zasu rabu.

Domin har sukayi nisa da Fara tafiya muhseena bata daina kuka ba.

A hankali Taufiq ya tsaida motarsa a gefen titi. Ba zato babu tsammani. Muhseena ta ji tausasan hsnnayen Taufiq sun ruko hannunta gaba daya ya Dora su a Kan kirjinsa.

Da sauri ta shiga kokarin kwace hannun Amma yaki sakinta maimakon hakama Ido ya zuba Mata .

"Ka sakar min hannu don Allah".

Ya numfasa yace "bazan saki ba har sai kin Gaya min me kike ji a game da ni".

Idanunta sunyi jajir jikinta ya Fara sanyi wani irin bakon yanayi ne take jinta a ciki.

"Bana Jin komai a game da Kai".ta fada cikin rawar murya, ya lumshe idonsa ya Bude yace "karya kike yi, ko yaya ne baki ji komai ba da hannuna ya rike ki" da karfi tace "nace ban ji ba".

A sanyaye ya saki hannunta, ya maida Kansa ya kwantar a Saman sitiyarin motar Yana maida ajiyar zuciya rike hannunta kawai da yayi ba karamin masifa ya jefa Shi ba, Amna ta yaya zata ce ita bata ji komai ba, hakan ya Kara tabbatar masa da cewa muhseena bata son Shi.

Shin ya gayá Mata yadda yake ji agame da ita ne ko ya kyaleta?.

Cikin sanyin murya muhseena tace "me ya faru ne? Me yasa duk Kabi Ka canja cikin kankanin lokaci ".

Ya yunkuro ya taso yau dai Yana Jin idan Bai amayar da abinda ke cikin zuciyarsa ba akwai matsala sosai.

Don haka ya Fara magana cikin wata bakuwar murya me cike da kasala.

"Muhseena soyayyarki ce ta canja ni , ina cikin tsaka me wuya Akan kaunar ki".

Jin maganar tayi cikin bazata.

Gabanta yayi mummunan faduwa ta dafe kirji tace "soyayyata ?". Ya gyada Kai kamar maraya yace "ya wuce wai,".

TO BE CONTINUE

DAGA TASKAR YAR GIDAN IMAM

NI MA MATARSA CE

56

Ta saki hannunta kasa cike da ràshin karfin guiwa da matukar mamaki tana yi masa kallo Ido cikin Ido.

"Yaushe har Kayi wannan saken, ta ina har Ka bari Ka Fara Sona bayan kafi kowa sanin bamu dace da juna ba"

Ya cigaba da yi Mata wani irin kallo me cike da sakonni Kala Kala sannan yace,

"Kamar ya ya bamu dace da juna ba,".

Ta ce "dube ni da kyau babu wani abu da Zan iya rudarka da Shi, Wanda matarka bata mallaka ba, ko Ka manta matarka ta hada komai Wanda duk wani namiji zai so ace matarsa ce, me zaka nema a guna me zaka yi sha'awa awajen yar kauye yar talakawa Irina?".

Yayi saurin cewa

"Soyayyarki, itace kadai nake nema daga gareki, babu Kuma ruwanki da matata ko wacece, ni maganarki nakeyi ba maganarta ba".

Ta jinjina Kai tace "mu tafi".

"Bazamu bar nan ba har sai na ji matsayina a gunki.".

Ta turbune fuska ta juya bayanta, yadda tayi ba karamin saukar ma da Taufiq sha'awarta yayi ba, baisan lokacin da gaba daya ya rungumo ta ta baya ba ya Dora Kansa a bayanta Yana shinshinar kamshin da ke fita daga jikinta, wani irin rikitaccen yanayi ya fada me wuyar fassarawa.

A yayinda duk ilahirin jikin muhseena ya dauki rawa. Tunda take a duniya yauce Rana ta farko da wani namiji ya taba kusantar jikinta haka.

Hakanne yasa tsoro ya fi komai yawa a tare da ita.

A gigice ta shiga kici kiciñ kwace kanta daga hannun Taufiq.

Cikin wata irin murya yake fadin "kefa matata ce me yasa kike guduna, don Allah muhseena ki so ni ko ya ya ne".

Ko a mafarki akace Mata Taufiq zai iya canjawa zuwa haka za tace karya ne, duk wani daukar Kai da nuna halin Ko'in Kula da yake nuna Mata yau shine a gabanta cikin wannan yanayin Mai wuyar fassarawa.

Daker ta Samu Taufiq ya saketa.

Amma duk da haka ya Dade Bai iya tuka motar ba domin ya fi minti biyar Yana kokarin dawowa hayyacinsa.

Ita kuwa ta kudundune kanta acikin gelenta tana maida wani nannauyan numfashi kanta ya daure ta rasa tunanin da zatayi.

A hankali ta ji ya Fara tuka motar. Lokaci daya Kuma ta ji ya fisgi motar da karfi .

Addu'a kawai take yi akan Allah ya kaisu gida lafiya, domin irin wannan gudun da yake yi akwai matsala acikinsa.

Ko kallonta bai Kara yi ba. Ita kuwa a Kai akai take kallonsa domin tana son ta tabbatar shine ko ba Shi ba ne.

Sai da suka shiga jigawa , sannan ba tare da ya dubeta ba, yace "kina da inda zaki iya shiga ki canja kayan jikinki ne?". Ta amsa "eh Ka aje ni gidan su hannatu wannan daka taba aje ta a gidansu daka dakkoni Muka taho tare...?

Ya dakatar da ita "ya isa na gane". Ya juya Kan motar zuwa hanyar unguwar su Hannatu, fuska a tamke rai abace.

Ananne muhseena ta dan dube Shi tace "kana Jin haushina ko?".

Yace "don me Zan ji haushinki bayan abinda yakamata kiyi min ne kika yi". Ta fahimci a wuya yake saboda haka yin maganar babu abinda zai Kara haifarwa face wani tashin fahimtar a tsakaninsu, don haka tayi shuru tasa aranta ba zata Kara yi masa maganar ba har sai ya huce.

Bata Dade agidan su Hannatu ba, tana canja kayan ta fito, Amma tabar wadancan kayan a hannun Hannatu ta aje Mata.

Kafin su isa gida Taufiq ya aje ta, Yana ajeta ya ja motar ba tare da yace Mata uffan ba ya yi tafiyarsa.

Tabi motar da kallo har ta bacema ganinta.

Sannan ta juya ta Karasa gida zuciyarta cike da damuwa iri iri.

Taufiq Kai tsaye wajen salisu ya wuce .

Ya same Shi a kofar gidansa daga bisani suka shige cikin gidan.bayan sun gaisa da matar

salisu Hauwa.

Sannan suka shige bangaren salisu suka zauna.salusu ya kare masa kallo sosai sannan ya tashi yaje ya dakko ruwa da lemo me sanyi acikin firjin ya tsiyaya ruwa a Kofi ya Mika masa yace " sha ruwan sanyi, Ka yi kokarin saukar da duk damuwa da fushinka, kafin muyi magana".

Ya amshi ruwan

Salisu ya koma Kan kujera ya kishingide Yana cigaba da kallon fuskar abokinsa.

Sosai ya sha ruwan gami da runtse idanunsa ya huro da iska daga bakinsa.

Ya dauki wasu Yan mintoci kafin ya ji ya dawo dai dai . Fushinsa ya Fara sauka ya daina Jin nauyin da zuciyarsa tayi masa.

Salisu ya dube Shi yace

"To ya aka yi menene ya faru, ko an Sami matsala ne sakamakon zuwan Ku Durmin, Allah dai yasa ba su gane yar su aiki take yi a gidanka ba".

Taufiq ya girgiza Kai yace "duk babu ko daya salisu, kawai abubuwa ne suke nema su sauya ko nace suka sauya". Salisu ya kafe Shi da Ido yace "na mene?".

Taufiq ya numfasa sannan ya Kara daukar ruwa ya sha sosai , ya Kara kallon salisu yace "salisu ayanzu na wayi gari zuciyata na matukar son muhseena, Kada Ka dauka so na wasa ko dan kadan (ya girgiza Kai) so Mai tsanani Wanda ina iya tabbatar maka da cewa bansan ma meye so ba sai akan yarinyar nan".

Cikin ràshin nuna mamaki salisu yayi dariya yace "Kai sai yau Ka fahimci hakan". Ya gyara Zama Yana cigaba da kallonsa yace "kallonka kawai nake yi ina Kuma Jiran irin wannan lokacin yayi , ina son Ka sani tun daga ranar da muka Kai cigiyarta wajen yansanda na tabbatar da kana son muhseena matukar so, to yanzu na ji menene abin damuwar, Kada fa Ka manta muhseena matarka ce halak malak ".

"Abinda nake son muhseena ta gane Kenan salisu, a yau na fahimci ni kadai Allah ya jarafta da kaunarta amma ita bata Jin soyayyata a cikin ranta kamar yadda babu soyayya ta a cikin idanunta, na rantse salisu idan na tuna hakan nakan ji tamkar zuciyata zata Faso waje saboda bakinciki da damuwa".

Salisu ya ce "aah Kada Ka dorama kanka wannan jidalin, muhseena dai ba budurwa bace , balle kace kana tsoron a kasaka, matarka ce, Kuma tana da dukkan dalilan da zasu sa ta ji bata sonka a ranta".

Taufiq yace "kamar yaya".

Salisu ya gyara zamansa yace "haba Taufiq matarka da Ka aureta tsawon wannan dogon lokacin, Baka taba kallonta a matsayin Mata ba , bayan haka zaune take agidan Ka amatsayin baiwa tana kallonka kullum tare da wata matar Ku shiga daki Ku kwana tare Ku tashi tare, shin don Allah Ka taba tunanin yadda take ji a cikin zuciyarta?".

Nan da nan Taufiq ya natsu sosai ya sakko daga Kan kujera ya zauna durshan a kasa tamkar Mai daukar karatu yasa ma salisu idanu, tabbas maganganun da take fada gaskiya ne.

Salisu ya cigaba da cewa "yadda kake ganin baayi maka adalci ba Akan aurenta, haka itama baayi Mata adalci ba, amma da yake ita macece babu Wanda ya damu da halin da ita zata shiga ni kaina sai bayan dawowar mu jigawa na zauna nayi nazarin al'amarin sosai nan na gane anfi cutar da yarinyar nan".

Ya danyi shuru Amma Jin Taufiq baiyi magana ba yasa ya cigaba da cewa "kalli tsawon lokacin nan da aka dauka, ta sadaukar da farincikinta saboda naka farincikin, ta yarda ta zauna

ta boye alakaku saboda Ka Sami kwanciyar hankali da matarka, ta Hana kowa nata zuwa inda ta ke saboda ta rufa asirinka, ta aje yancinta na matarka saboda ta rufa asirinka, shin duk wacce tayi maka hakane kake ikirarin bata sonka?".

Sosai maganganun salisu suke tasiri acikin zuciyar Taufiq.

Salisu yace "kawai abu daya ne idan har kana son soyayyar da take maka ta fito , to dole sai Ka koma kayi Mata adalci, adalci kuwa shine Ka bata yancinta na matarka Ka Kuma daina boyeta kamar kayan wanki Ka fito Ka bayyanama duniya matsayiinta, domin ina tabbatar maka wannan boyewa kowa sirrin da kayi Bai kamata ba kayi kuskure, don haka dole Ka je Ka gyara kuskurenka, idan ba haka ba kuwa muhseena ba zata daina kallonka a matsayin azzalumi ba, don haka wani fushi wani Jin zafin ta nuna bata sonka duk ba Shi bane Mallam kaje Ka gyara kawai ".

Taufiq ya yi ajiyar zuciya yace "lalle nasan nayi kuskure, amma in sha Allah Zan gyara kuskurena, Zan gyara". Ya karasa magana Yana dafe Kansa da yake Sarawa.

...shin ta ina zai Fara?

Lalle lokaci yayi da zai daidaita komai.

Ita Kam muhseena tun komawarta gida, ta tsinci kanta cikin damuwa sosai.

Abubuwan da suka faru sun kasa bace Mata , duk fitar numfashi sai abin ya fado Mata arai.

Taufiq yayi Mata bajinta a yau.ya yi matukar faranta Mata rai zuwansu Durmi ya sa yayi matukar Samun kima da daraja agunta, sai dai abinda ya bijiro da Shi ya tsaya Mata arai.

Ko kadan bata taba tsammanin zai so ta haka ba, shi yasa bata dorama kanta son ta rayu da Shi ba, don tasan wahala kawai zata sha, amma yanzu da yake Sonta, ya ya zata yi da halaccin da mujaheeda tayi Mata?. Ta yaya Kuma zata iya yin kishi da ita bayan tana ganin ba zata iya kishi da ita ba domin ta fi karfinta.

Sosai take cikin damuwa Wanda ta ke kokarin boyewa.

Dawowar Taufiq ya Kara jefata a damuwa, domin ji tayi tamkar bata taba ganinsa ba sai ranar. Ita ta gabatar masa da abinci kamar yadda ta Saba. Mujaheeda na gefe cikin kwalliya rike da waya tana aikin charting ko kallon inda Taufiq yake bata yi, sai dai tayi dariya ko murmushi idan taga abinda ya burgeta a wayar.

Idon Taufiq na Kan muhseena wani irin soyayyarta ne ke Kara fisgarsa irin kallon da yake Mata Sam ba zata iya Jura ba , hakanne yasa ta koma daki ita da Fadwa.

Duk iya yadda ya so ya ci abincin ya kasa, domin damuwar da yake ciki ta fi karfinsa, ya waiwaya ya dubi inda mujaheeda take tun bayan sannu da zuwa da tayi masa babu abinda ya Kara shiga tsakanin su hankalinta Kan wayarta yake ba Kan sa ba.

Ya Mike ya shige daki ya yi wanka yayi Shirin kwanciya yayi kwanciyar sa. Ya rasa wace irin macece mujaheeda bata San komai ba a game da irin kulawar da Zata ba mijinta, tana ikirarin tana sonsa fiye da komai Amma bata da lokacin kulawa da Shi.

Macen kirki da take son tayi rayuwa me dadi da tsafta da mijinta ba zata yi halin mujaheeda ba.

Tun faruwar al'amarin muhseena ta hanama kanta kebewa da Taufiq, ko kwanciya zatayi da daddare sai tasa makulli ta kulle kofarta gudun Kada ya shigo. Ya fahimci hakan sosai Shi yasa ya bata iska shima ya daina shiga harkarta.

Yau dai gidan su mujaheeda, muhseena da mujaheeda suka uni da Fadwa.

Sosai mujaheeda take Jin dadin irin kulawa da Alh Mustapha labaran yake ba muhseena, domin ko yanzu Shi ya bukaci idan zata zo ta taho da ita.

Sai dai tun zuwansu gidan Haj murjanatu ke nunama muhseena iyakarta.kusan duk aikin gidan yau ita aka sakarma , Yan aikin Haj murjanatu Hutu kawai suke yi.

Alh Mustapha labaran ya rasa dalilin da yake Jin babu dadi, ransa na matukar kuna idan Haj murjanatu nasa muhseena aiki ko daka Mata tsawa, Jin abin yake har cikin zuciyarsa.

Ita kanta mujaheeda bata son irin wannan dabi'un da mahaifiyarta take nunawa.

Haj murjanatu tana cikin daki, Alh Mustapha ya shiga ya tsaya jikin kofa Yana kallonta, ta dago ta dube Shi tace "uhum, menene?".

Ya jinjina Kai yace "haba Haj yaya daga zuwan yarinya zaki buwayeta da aiki sai kace wata baiwarki, gaishe mu fa suka zo yi".

Ta dago tana yi masa wani irin kallo, "wai na tambayeka meye tsakaninka da yarinyar nan ne da kake nuna Mata kulawa da tausayawa menene wai Wanda ban sani ba Ka gaya min ?". Ya jinjina Kai yace "yanzu ba zaka Kula da mutum ba sai akwai wani abu" tace "kwarai kuwa,ko kuwa har yanzu Baka yarda da Ka girma ba ne? Ko har yanzu idonka da hankalinka na Kan kananan Yara ne ? Turban muzuru kayi".

Wani irin bakinciki da takaici ya kama Shi, Kansa ya shiga juyawa cikin rawar murya yace "wace irin maganar banza ce kike min haka , idan kika Kara min irin wannan maganar akan yarinyar can na rantse sai nayi Miki abun da zaki yi matukar mamaki na, na gaji da wannan wulakancin da kike min".

Baki kawai ta hangame tana matukar mamakin yadda yau Alh Mustapha ya tsaya Yana gaya Mata magana akan muhseena.

Ta Mike itama cikin fusata tace "oho ko itama zaka yi Mata abinda.....?

Kafin ta Karasa maganar gaba daya Alh Mustapha labaran ya yo kanta cikin matukar fushi Yana tsuma "idan kika Kara danganta wannan yarinyar da abinda kike kokarin fada sai na ganar da ke kuskurenki, ke da akullum bakinki baya taba furta alheri, ki karasa maganar kiga abinda zai biyo baya".

Tsantsar mamaki yasa Haj murjanatu ta dauke wuta tana kallon hannun Alh Mustapha labaran da yake rawa alamar gaf yake da ya daketa.

Shin mafarki take yi ko Ido biyu,ta kasa gasgata abinda ke faruwa a yanzu.

Maganganun da Alh Mustapha ya cigaba da yi ne masu zafi ya janyo hankalin mujaheeda cikin dakin, da sauri ta tashi ta shigo dakin.

Sam bata jidadin ganinsu a irin yanayin da ta gansu ba.

Ta koma ta jingina jikin bango ta runtse idonta da karfi tace "haka ya isa, don Allah daddy Ku daina wannan abin, me yasa bakwa jituwa Da junanku ne, me yasa Kuna rayuwa a matsayin ma"aura amma kullum kunfi kama da makiya".

Haj murjanatu ta dago Ido jajir cike da bakinciki tana kallonsa tace "oya Maza Ka gaya Mata dalili, Ka gaya Mata ko yau na gaya Mata, ko an gaya maka kana da wata kima ne ko daraja a guna".

Alh Mustapha labaran yayi saurin kallon mujaheeda yace "mujaheeda Ku tafi gida, wuce ki dauki Zainab Ku tafi,".

Da karfi Haj murjanatu tace "idan kika Kara zuwa min da yarinyar nan gidana na rantse Miki

sai na la'antata Kada ki sake kawo ta gidana, ke dai da kike ganin zaki iya rayuwa da ita kije kiyi tayi (ta juya ta dube Shi) Kai Kuma da kake son ganinta sai Ka bita inda take kaga daganan tarihi sai ya maimaita Kansa saboda Mai hali Bai taba barin halinsa".

Mujaheeda cikin muryar kuka tace "mummy don Allah me daddy yayi Miki ne ?". Ta Kara fusata ta nuna Shi da hannunta tace "ki tambaye Shi ".

Alh Mustapha ya sa hannu ya rike hannun mujaheeda Kam ya Fito da ita daga cikin dakin.

Tsaye suka tadda muhseena cikin matukar firgici idonta na Kan Alh Mustapha labaran shima ita yake kallo.

"Don Allah daddy kayi hakuri, bazan Kara zuwa gidan nan ba balle har Ku cigaba da Samun sabani da mummy, na Sani ina Kuma Lura kullum na zo gidan nan sai kun Sami matsala da ita , ni Kuma Bana so Bana jindadi".

"Idan har bakya jindadi da gaske meyasa kike zuwa gidana, Dama abinda kike so kenan Kuma kin samu, tunda na nuna Miki kin kasa ganewa to yau Bari na gaya Miki da bakina Bana sonki , Bana kaunar ki har cikin raina".

Cikin zubar hawaye muhseena tace "me yasa bakya Sona ? Me nayi Miki?" Ta make kafada tace "ni kaina bansan dalili ba, hakanan nake Jin na tsaneni".

Alh Mustapha labaran yace "kamar yadda ni Kuma nake Jin duk duniya ba ni da wacce na ke kauna irinta".

Nan da nan mujaheeda ta dube Shi a tsorace Amma sai ya yi Mata nuni da cewa ya fada ne saboda Haj murjanatu ta ji zafi a ranta.

Ta Kuma gamsu da hakan.

Don haka bata damu da yadda Haj murjanatu ta haukace ba da fadan maganganu masu zafi. Duk da yau shima ya tsaya ya amayar da duk maganganun da ke ransa. Hakan Bai hana Shi fargabar Kada yau bacin rai yasa Haj murjanatu bude bakinta ba a gaban mujaheeda da yarinyar da ya ke Jin nauyin ta sosai Wanda Shi Kansa ko bindinga akasa masa Bai San dalili ba.

Hakanne yasa ya umarci su mujaheeda da su gaggauta barin gidan.

Suna tafiya shima duk da Yana Jin jikinsa ba dadi haka ya fice yabar gidan, saboda yadda Haj murjanatu ta koma kamar Wata mahaukaciya hatta masu aikin gidan duk daki suka shige suka rufo Kofa Suna kakabin irin wannan rayuwa ta Haj murjanatu da take yinta tamkar wata karamar yarinya babu tunani aciki ko lissafi.

Alh Mustapha labaran bai dade da barin gidan ba itama Haj murjanatu ta fice, ita kadai ba tare da direba ba.

Kai tsaye gidan Haj Nana ta wuce.

Ta Jima acikin falon zaune shuru tana aje ajiyar zuciya cikin matukar fusata take. Hakan yasa Haj Nana bata matsa Mata da tambayar abinda ke faruwa ba, har sai da ta tabbatar ta Fara dawowa hayyacinta.

Sannan ta matsa sosai kusa da ita tana kare Mata kallo tace "Haj meke faruwa ne, na Dade ban ganki cikin irin wannan mummunan yanayin ba,idan bazan manta ba rabon da na ganki haka sama da shekara ashirin Kenan Kuma abin mamaki a rana irin ta yau".

Haj murjanatu ta cije lebe, gaba daya fuskarta ta canja kamar ba ita ba, tace "Kuma ina

fargabar gaya Miki kusan irin matsalar ce ta Kara faruwa a yau din nan".

Haj Nana ta shiga salati tana tafa hannayenta biyu cike da tashin hankali tace "wannan wane irin mutum ne, jarababbe tsofai tsofai da Shi har yanzu idonsa na Kan Mata, kenan".

Ta girgiza Kai

Tace "aah ba haka nake nufi ba , ina dai tsoron faruwar irin abinda ya faru ne a baya, ina tsoron Kada tarihi ya maimaita Kansa ne Haj ".

Ta gyara zamanta tace "to yanzu meya faru Haj ki kwantar da hankalinki kiyi min bayani".

Haj murjanatu tace "ina yarinyar da nake Gaya Miki mujaheeda ta bugeta a mota kwanaki da dadewa har na gaya Miki tace zata zauna ta maye Mata gurbin mai aikinta daya da tayi aure" Haj Nana cikin kaguwa tace " na gane ba Zainab ba da kike gaya min hakanan bakya Sonta ba Kuma kya son zamanta tare da mujaheeda ".

Tace "kwarai kuwa to itace take neman ta zamar min balai ko Kuma nace ma ta zamar min".

Sannu a hankali ta kwashe labarin duk abinda ya faru ta gaya ma Haj Nana.

Ta Kara da cewa "duk saboda yarinyar da baisan wacece ba, Bai hada komai da ita ba zai zauna Yana gaya min maganganu masu zafi harda yunkurin dukana, ni Haj murjanatu Alh Mustapha zai daga hannu ya nemi marina akan Zainab, Shi yasa nake tunanin ko Sonta ya ke yi ne? Ina jiyema mujaheeda Kada ta Sanya kafafunta acikin takalmina ashe nice wata fitinar zata Kara yankoma, shin me Alh Mustapha labaran yake ji a wajen Yan aiki".

Haj Nana ta jinjina Kai tace cike da nazari "Kai aah ke yanzu kina zaton son Zainab Alh yake yarinya yar cikinsa , Kuma bayan haka kina zaton asirin da kikayi masa zai Kara kallon wata ya mace da sunan so balle har ta Kai Shi ga aikata irin aikin da ya aikata a can baya".

Haj murjanatu ta saki tsaki tace "ban yarda wani asiri yanzu Yana tasiri a cikin zamana da Alh ba, ayau na Kara tabbatar da hakan , idan har asirin Yana jikinsa har yanzu Shi Bai Isa yayi min abinda ya yi min yau ba, Kuma na Fara tunanin ko da can din ba asirin bane yake dawainiya da Shi, har ya sa Shi kwantar da Kansa a gare ni ".

Ta girgiza Kai ta cigaba da cewa "aah ina ganin kawai tsabar yarda da ya cutar da ni ne ya ha'ince ni, yasa duk tsawon wannan shekarun ya kwantar da Kansa a wajena nake juya Shi na ke Kuma yin abinda nake so".

"To yanzu kina nufin ya dawo daga rakiyarki Kenan, ya Fara dawo da asalin halinsa" cewar Haj Nana, Haj murjanatu ta gyada Kai tace "shine fargabata, Kuma duk abinda ya faru Zainab itace sila, don haka yaya kike ganin Zan bulloma al'amarin".

Haj Nana tace "ni kawai abinda nake gani me zai hana mujaheeda ta sallameta ta bar gidanta ta tafi can in da ba zaa Kara Jin duriyar ta ba".

Haj murjanatu tace "hmm ai da kamar wuya, domin kamar yadda na gaya Miki ne yadda kika San ta yi ma mujaheeda asiri haka take don ko kadan bata son ta rabu da ita babu yadda banyi ba tuntuni ta sallameta Amma ta ki , ga wani sakaci da ta Kara yi shine yadda ta Bari shakuwa ta shiga tsakanin Fadwa da Zainab, kamar yadda shakuwa ta shiga tsakaninta da Hajara ke dai shaidata kinfi kowa sanin mugun halin da na shiga itama mujaheedan ta shiga a dalilin rabata da Hajara".

Fadin sunan Hajara da tayi abskinta ji tayi har wani kuna bakinta yake yi.rabon da ta ambaci sunan Hajara sama da shekara ashirin Kenan ko me sunan bata fade saboda bata son ma ta tuna komai agame da Hajarar.

Yau Kam bakinciki yasa ta faden sunan Hajara ya Kuma dawo Mata da munanan abubuwan da suka faru a baya Wanda suke gudunsu suke ta boyewa.

Haj Nana tace "kwarai nasan komai Haj , ba sai kin tuna min ba. Don haka yanzu ma yaki zaki tashi kiyi ki raba Zainab da mujaheeda ba tare da kin duba damuwae da mujaheeda zata shiga ba, domin ke nakasunki Kenan a rayuwa mujaheeda, duk abinda zai hada da ita matukar zai bata Mata rai kikan kiyaye Shi, saboda haka wannan Karon kiyi ma kanki da ita kanta mujaheedan gata ki raba tsakaninsu, idan ko ba haka ba sirrin da kike ta boyewa mujaheeda tabbas ya kusa fitowa fili".

Haj murjanatu ta kama kanta ta rike tana fadin shin wacece Zainab? Gaba daya ta Gama rikita Mata lissafi. Ayayinda Haj Nana tayi ta ingizata a matsayin tana bata shawara, bata bar gidan ba sai dare.

Abubuwa sun hadu sun cushema muhseena abu goma da ashirin.

Ga matsalar Taufiq da kullum gaba ta ke yi, domin zuwa wannan lokacin ta tabbatar da irin son da yake Mata Yana da yawa, sosai yake son ya shawo kanta.

Tabangare daya Kuma matsalar gidan Haj murjanatu.kullum abin Yana nukurkusar zuciyarta, ta rasa dalilin kiyayyar da Haj murjanatu take Mata, kamar yadda ta rasa dalilin soyayyar da Alh Mustapha labaran yake yi Mata?.

Ta kasa gane komai.

Tun daga wannan ranar tsananin ràshin jituwa da ràshin zaman lafiya ya Kara Samun matsuguni a gidan Alh Mustapha labaran.

Domin Haj murjanatu ta hana kwanciyar hankali agidan, kullum cikin neman rigima take tare da gayama Alh Mustapha maganganu masu zafi masu tsayawa arai, musamman akan kuskuren da ya aikata a baya.

Sai dai wannan Karon duk abinda ta gaya masa baya bari, sai ya mayar Mata gaba daya ya canja, yadda yake tsayawa Yana gaya Mata magana abin har tsoro yake bata.

Tamkar ba Shi ba ne Wanda yake Jin tsoronta ya ke Kuma kaffa kaffa da fushinta.

A yanzu akalla sai suyi kwana biyu babu me yi ma wani magana.

Rikici suke yi sosai.

****

Karfe biyu da kwata na dare, muhseena na zaune Kan sallayarta wannan Karon tunda ta idar da sallah ta kasa yin adduar komai sai kuka take yi.

A hankali ake kwankwasa kofar , firgigit ta daga kanta tana kallon kofar.

Aka cigaba da kwankwasawa a hankali. Ta tashi ta isa bakin kofar tace a hankali "wanene".

Taufiq ya gyara tsaiwarsa yace "ki Bude nine".

Ta langabar da Kai gefe cike da gajiya da faruwan abinda ke faruwa tace "don Allah Ka koma".

A kagauce yace "babu inda Zan koma , na Kuma rantse Miki idan Baki Bude kofar nan ba yau duk abinda zai faru zai faru domin banki ayau mujaheeda tasan komai ba". Da sauri ta Bude kofar tana cewa "shigo". Har wani tafiyar kasaita yake yi.

Kai tsaye ya haye Saman gadonta ya kishingide. Gabanta ya Fadi ta koma bakin madubi ta tsaya idanunta cike da tsoro tace "menene haka, don girman Allah Ka tashi Ka fita don Allah".

Ya tsareta da Ido yace "babu inda zani , saboda na yanke shawarar raba muku kwana ke da mujaheeda". Yadda ya ga ta firgice ta fiddo idanu waje cike da tsoro ne ya bashi dariya. Sosai

ya yi dariya har sai da muhseena ta Fara kaiwa wuya.

Sannan ya tashi ya zauna Yana kallonta, yace "muhseena lokaci yayi Kuma a shirye nake da na gaya ma duniya ke ma matata ce ciki kuwa harda mujaheeda".

Tayi kasa ta zauna dirshan, tana kokarin mallakar hankalinta, sannan tace " ya kamata kayi tunanin makomar komai kafin Ka aikata abinda zaka aikata ". Yace "Na gama duk tunanin da zanyi , na gaji da wannan nauyin da ke Kaina Wanda na kasa saukewa, shine Kuma yake wahalar da ni kullum". Ya cigaba da kallonta yace "nasan banyi Miki adalci ba, yanzu Kuma ina bukatar yin adalci a gareki domin ta hakane kadai Zan samu kwanciyar hankali".

Muhseena ji tayi hawaye Yana zuba Mata

"Ban so lamarin ya tafi ahaka ba, har ga Allah ina son nayi rayuwa tare da matarka a matsayin ya da Kanwa ba matsayin kishiya ba, ina Sonta sosai, amma nayi Imanin idan har ta ji wannan maganar ba zata taba so na ba, kilama ta tsaneni fiye da yadda mahaifiyarta ta tsane ni , idan Kuma hakan ya kasance ta ina Zan jidadin rayuwa da Kai".

Ya sakko daga Kan gadon ya zauna a gabanta gami da Kamo hannayenta biyu ya rike wani irin abune taji Yana yi Mata yawo a cikin jikinta wani irin shauiki Wanda bata taba Jin irinsa ba.

Wannan Karon Kuma ta kasa kwce hannun nata, maimakon hakama sai lumshe idanunta tayi . Tana Jin wani bakon lamari a tare da ita.

Hakan yasa Taufiq ya cigaba da murza hannunta cikin wani irin salo. Murya a dishe yace "dago ki kalle ni", ta girgiza Kai gami da Kara rufe idanunta. Yasa hannu Yana kokarin shafa fuskarta ahankali yake cewa "kalle ni muhseena".

A hankali ta Bude Ido ta Dora akan idanunsa wani irin abune take ji a jikinta. Ya tsareta da Ido yace "Kada wani abu ya dame ki, ko mujaheeda ta fahimce ki ko ba ta fahimce ki ba, ko ta yarda da ke a matsayin abokiyar Zama ko bata yarda da ke ba, na daina Hana Kaina jindadi saboda ita, lokaci yayi da zata ba ni damar yin rayuwata yadda nake so, ina son yau ki sani, ba wai ina bin abinda mujaheeda ta ke so ba ne don tsoro (ya girgiza Kai) aah ina bi da ita yadda take so ne saboda tausayinta na lalurarta na ciwon zuciya, da Kuma son a zauna lafiya Amma ba don tsoro ko shakka ba,".

Ya Kara tallafo fuskarta Yana kallonta, yace "ni kuma a yanzu babu abinda nake so sama da na zauna da ke a matsayin Mata, ina son ki ina sinki so na hakika don haka dole Zan sanar da mujaheeda komai kafin ta ji awani wajen ni ya kamata ta Fara ji daga bakina, don haka ina neman hadin kanki, duk da nasan bakya so na".

Muhseena ta numfasa sosai.

Tace "ina son Ka sa ni , matukar mujaheeda bata yarda da ni a matsayin kishiyarta ba sai dai kayi hakuri da ni domin bazan iya rayuwa da Kai ba".

Gaba daya sai Taufiq ya janyota ya rungumeta tsan tsan tamkar zai tsaga jikinsa ya maidata ciki, sai wata irin ajiyar zuciya ya ke saki, ita kanta ta kasa tabuka komai domin kubutar da kanta daga hannun Taufiq. Yana rungume da ita yana tambayar ta " yanzu saboda mujaheeda sai ki haramta mana juna". A hankali tace "Kai don me Ka haramta mana junan saboda ita, ko sai yanzu da Ka Fara Sona ne hakan ". Ya Kara matseta Yana fadin kiyi hakuri Zan gyara komai.

Ta girgiza Kai tace "ko Ka gyara aurenka na hannun mujaheeda idan ta yarda da ni shikenan idan bata yarda da ni ba, ni kuma Zan bar Mata mijinta har abada".

"Kada kiyi min haka muhseena Kada ki Dora ni Akan mizanin da bazan Sami rinjaye ba, ".

Sosai ta fahimci Taufiq na neman zurmewa don hska cike da karfin hali ta zare jikinta acikin nasa ta Mike jiki babu karfi, tace "wannan itace matsayata". Bata saurari maganar da yake yi ba ta fada bandaki ta kulle kofar.

Duk yadda ya so ta Bude kofar ta ki , haka ya Gama magiyarsa ya fita batare da ta Bude kofar ba.

Ta ci kuka a bandaki har ta ba uku lada.ita kanta tana son akawo karshen wannan badakalar, ko ta Sami sukuni a cikin zuciyarta. Domin ta Fara zargin zuciyarta da yi Mata ràshin adalci, na kokarin Fara Sanya Mata soyayyar Taufiq a cikin zuciyarta,sai dai ba zata bari tayi irin sakacin da Taufiq ya yi ba.

Muhseena ta maida hankalinta Kan karatu, duk da duk Wanda ya dubeta yasan tana da damuwa. Awannan lokacin kusan kullum Taufiq Yana makarantar su, tun tana boye Shi har hakan ya faskara.

Zuwa lokacin tuni Hannatu tasan halin da muhseena ta ke ciki, ta Kuma tsaya ta bata shawarar data dace , Akan ta karbi mijinta itama tayi rayuwa me dadi ta bar maganar wai sai MATARSA ta yarda da ita amatsayin kishiya sannan Zata yarda da Taufiq.

Hannatu ta Kara kallonta sosai tace "shin kin taba ganin matar da ta amince ma mijinta yayi Mata kishiya, saboda haka batun kice wai sai ta yarda sannan zaki yarda da mijinki wannan ganganci ne".

Muhseena ta dubeta tace "mujaheeda tayi min halacci ta Kuma taimske ni Bai kamata nayi Mata butulci ba". Hannatu tace "duk tayi Miki abinda tayi Miki ne adashin sanin ko wacece ke, inda tun farko tasan ke wacece. Da duk batayi Miki haka ba, sabod haka Kada ki sake ki cutar da kanki saboda hakan".

To komai dai ya cakudema Muhseena, Taufiq dai tayi Imanin gaf yake da ya tone dukkan sirrin ga mujaheeda. Zuciyarta cike take da tsoron faruwar hakan.

Ranar wata asabar , kamar daga sama, Alh Mustapha labaran ya zo gidan mujaheeda.

Hakan ko ba karamin dadi yayima mujaheeda ba. Nan da nan muhseena ta shiga hidimarsa , duk inda ta bi idon Alh Mustapha yana bin ta da kallo. Idanuwan Zainab suna matukar yi masa yanayi da wasu idanuwa wadanda ba zasu taba bace masa ba, shin wacece Zainab?. Irin tambayar da yake ma Kansa Kenan.

Me yasa a duk sanda ya ganta yake Samun nutsuwa.

Ya dubi muhseena da take ta wasa da Fadwa, ya Dan yi gyaran murya yace "Zainab ina iyayenki suke da Zama"..

Kafin ta bashi amsa mujaheeda ta amshe "daddy Ka manta na gaya maka marainiyace bata da Uwa bata da uba".

Ya numfasa yace "Allah sarki, na manta kuwa, Allah ya jikansa". Hakanan muhseena taji ta Sami kanta da ràshin jindadin karyar da tayima mujaheeda tun farko.

Alh Mustapha ya na Shirin tafiya Taufiq ya shigo nan ma ya koma ya zauna suka cigaba da sabuwar hira.

Daga bisani Àlh Mustapha labaran yayi musu sallama zai tafi nera dubu ashirin ya ba muhseena Akan ta rage kudin zuwa makaranta. Ta Karba tare da godiya.

Alh Mustapha labaran Yana tafiya Haj murjanatu tana dawo hancin motarta cikin gidan, har idanu suka hada da shi.

Bai tsaya ba ya wuce abinsa.

Tuni jikin ta ya Fara rawa Allah yasa ba itace ke tuka motar ba, don da tuni ta saki sitiyarin.

Tun kafin direban ya tsaida motar Haj murjanatu ta balle kofar motar ta fito.

Ko sallama ba tayi ba ta fara fada " me Alh ya zo yi". Mujaheeda tace arazane "haba mummy yanzu daddy ba zai zo gidana ba sai Yana da abin yi". Muhseena tuni jikinta ya Fara tsuma tana kokarin boye kudin hannunta.

Haj murjanatu tace a fusace "inda ya Saba zuwa ai bazan tambayi me ya zo yi ba, ". Ta juya ta dubi muhseena Rai a bace tace "ba shakka shine ya baki kudin hannunki ko". Ta kasa magana saboda tsoro. Taufiq ya dubeta yace "shine ya bata,wani abu ne". Ta sakar masa harara tace "wani abu ne, domin ina tabbatar Muku da cewa yau ba sai gobe ba wannan yarinyar zata bar gidan nan".

Mujaheeda tace "saboda mene mummy, wai lafiya kuwa,". Gefe kawai Taufiq ya koma ya harde hannayensa a kirji Yana kallon haukatacciyar fuskar surukarsa.

Ta dubi mujaheeda tace "ko ki Kori yarinyar nan ko na cire hannuna akanki, ba ni ba ki mujaheeda matukar baki koreta ba"

Cike da mamaki mujaheeda ta ce "mummy yau ni ce kike ikirarin zaki iya rabuwa da ni ". Tace "kwarai da gaske saboda na gaji da son fahimtar da ke illar da ke tattare da zamanki da yarinyar nan".

Taufiq ya zo iya wuya hakika ba don yayi alkawarin mujaheeda kadai zai Fara gayama matsayin muhseena a wajensa ba , to fa tabbas ds ya fasa Kwan yanzu kowa ya ji.

Amma dole ya hadiye fushi da bakincikinsa. Ya Kuma cika da mamakin yadda gaba daya Haj murjanatu ta haukace Akan sai muhseena ta bar gidan a wañnan lokacin.

A fusace ya dubi muhseena yace "jeki hado kayanki ".

Muhseena ta shige daki da sauri Dama tana neman yadda zata kubuta da ga wannan masifa ta Haj murjanatu.

Mujaheeda ta dubi Taufiq bayan fitowar muhseena dauke da akwatin kayanta "yaya Taufiq Kada Ka biyena mummy ina zaka Kai Zainab".

Ya daga Mata hannu

Kada ki damu".

Haj murjanatu ta saki tsaki tace "oho dai duk inda zaka kaita ma kaje Ka kaita , ni dai ina son ta bace ma ganin mijina har abada".

A gaba Taufiq yasa muhseena suka fice daga gidan.

TO BE CONTINUE

DAGA TASKAR YAR GIDAN IMAM

NI MA MATARSA CE

57

Kukan da muhseena take yi ba karamin taba zuciyar Taufiq take yi ba.

Gaba daya ya kasa tukin a hankali ya saukar da motarsa bakin titi ya kasheta gaba daya gami da dora Kansa a jikin sitiyarin motar.

Hakan baisa muhseena daina kukan da take yi ba, har sai da ya dago gaba daya yasa hannu

ya janyota jikinsa ya kwantar Yana bubbuga bayanta, sai kace Wanda ya ke lallashin karamar yarinya.

Ga mamakin muhseena ji tayi ta Kara kwanciya a faffadan kirjinsa alama me karfi na nuna tana neman kafadar da zatayi kuka.

"Don Allah muhseena kiyi shuru, ki daina kukan nan, Allah kadai yasan abinda nake ji a cikin zuciyata sakamakon Jin kukan ki".

Ta dan yi shuru amma bata daina sharbar hawaye ba.

" Idan da sabo kin riga kin Saba da halin Haj ,".

Tace tana kokarin tashi daga jikinsa.

"Da ace ana sabawa da cin mutunci da tashin hankali to da ba makawa Zan Saba da halinta a gare ni, ba Kuma zai taba damuna ba, Amma baa sabo da hakan Shi yasa kullum zuciyata ta ke kuna da kunci idan tayi min irin wannan tijarar, tun ina shakka da tsoronta na rantse maka a yau zuciyata ta Fara hasala da ita ta Kuma Fara daina Jin tsoronta, ".

Ta numfasa ta cigaba da cewa "ina matukar fargabar fahimtar cewa nima har cikin raina tuni na Fara tsanarta, don na rasa dalilin irin wannan tsana da tayi min".

Taufiq ya numfasa yace "halinta ne, nuna tsana da kiyayya ga duk Wanda baiyi Mata ba, ni Kaina a hakan nake da ita,"

Muhseena ta dago suka hada Ido, tayi saurin dauke kanta don bata jure kallon abinda ke cikin kwayar idon sa. Tace "To yanzu tana yi min Irin wannan tsanar, ina Kuma da ta San abinda ke tsakanina da Kai".

Ta girgiza Kai cike da fargaba tace "don Allah Ka taimakeni, Kada ku hadu Ku karasa nakasa rayuwata, Ka hakura da ni". Ya fiddo idanu waje Yana yi Mata kallon kin haukace .

Sannan yace "Na hakura da ke?na rantse Miki duk duniya babu Wanda ya isa ya sa na rabu da ke, ina son ki sani na daina fifita farincikin kowa Akan nawa, Kuma a yau ba sai gobe ba Zan bayyana ma mujaheeda asalin gaskiyar, sai dai kiyi Mata fatan Samun saukin zuciya".

Muhseena ta yi ajiyar zuciya Mai karfi sannan tace "Ni Kuma idan kayi hakan Kada Ka manta sai ta amince da ni a matsayin da Ka ba ni sannan Zan yi zaman aure da Kai".

Ya girgiza Kai yace "na gaya Miki Kada ki Fara yin wannan kuskuren, babu ta yadda zaayi mujaheeda ta amince da ke a matsayin kishiyarki sai dai kawai Dama idan kina so ne ki tabbatar min da cewa ba kya so na, ni Kuma wannan hukuncin na ki bazai canja komai ba daga Mai da ke matata ta hakika tare da sauke duk wani hakkinki da ke Kaina ciki kuwa har da maida ke cikakkiyar mace,".

Shuru ta yi ba tare da ta Kara yin magana ba.

Shima da sauri ya yi ma motar key ya ja ya Kara harbawa titi.kowa na cike da sake sake a cikin zuciya sa. Ita tunani ne fal a ranta na tunanin inda zai kaita, tana son ta tambaye Shi inda zai Kai ta amma yadda ya tamke fuska yasa ta kasa yi masa magana.

Taufiq bai tsaya ko'ina ba sai cikin get din gidansu.

Sai a lokacin muhseena ta Sami sukuni da ta gansu a gidan Alh Yusuf lamido, hakan ya tabbatar Mata da cewa Taufiq Yana da kyakkyawan tunani a kanta.

Tun daga kofa Haulat ta taho da gudu tana murnar ganin muhseena ta rungumeta ganinta da akwati yasa ta dubeta cike ds fara'a ", Allah yasa kwanaki zaki yi mana"

Murmushi kawai tayi tace "in sha Allah Haulat ". Sai alokacin hankali ya Mari Haulat a lokacin da ta Lura da fuskokinsu Duka babu Wanda ya ke cikin walwala Garama muhseena tana yake ne kawai Wanda ya fi kuka ciwo Shi kuwa Taufiq fuskarsa kamar an aiko masa da manzon daukar mutuwa. Don kafin su Gama magana tuni har Taufiq ya tsufa a wuce falon. Haj saratu ya zauna a kujera ya rufe idanunsa, Shi kadai yasan abinda ke yawo a cikin kwakwalwarsa .

Suna shigowa itama muhseena ta Sami kasan kafet ta zauna.

Yayin da Haulat ta shige cikin dakin Haj saratu da sauri tana kiranta "umma ki zo , ga yaya Taufiq Shi da Zainab ".Haj saratu ta dubeta "to meye na wannan karajin". Haulat tayi dan kasa da murya tace "umma ai ina ganin kamar zuwan ba na dadi ba ne, gasu can dai a falo".

Haj saratu ta numfasa tace "jeki gani nan zuwa".

Ta aje duk abinda take yi a dakin ta fito da sauri.

"Zainab ya ya ? Daga ina kuke ? Me nene ke faruwa". Duk tana jero wannan tambayoyin ne alokacin da take zaunawa tana fuskantar Taufiq da muhseena.

Sai alokacin Taufiq ya bude idanunsa ya gyara zamansa Yana kallonta da fuska me cike da damuwa. Ayayinda cikin ladabi da biyayya muhseena ta gaida Haj saratu ta amsa Mata cike da kulawa.

"Zo nan kusa da ni Zainab". Cewar Haj saratu, a hankali muhseena ta rarrafo ta dawo gefen kafafun Haj saratu ta zauna tana kokarin maida hawayenta.

"Meya faru Zainab, domin da ganin fuskarki a kwai alamun damuwa da tashin hankali". Muhseena ta kasa cewa komai sai hawayenta da ta ke kokarin tsaida su.

Haj saratu ta dawo da kallonta Kan Taufiq tace "wai menene, kun shigo cikin damuwa Kuma kun kasa yi min bayanin komai, Kai Taufiq menene?".

A nanne Taufiq ya ce "damuwar da aka sabace". Haj saratu ta tabe baki tace "Ta matar Ka da surukar ko?".

Ya jinjina Kai yace "hakane" tace "to yanzu me ya faru".

Sannu a hankali ya Gama sanar da Haj saratu duk abinda ya faru ya Kara da cewa , "To Naga babu inda ya kamata na kawota sai nan, gata nan zata zauna a hannunki umma, sannan gobe in sha Allah Zan zo akwai wata muhimmiyar magana da nake son muyi ni da ke, Wanda kila shine zai kawo karshen komai".

Haj saratu ta dubi muhseena cike da tausayawa tace "ni fa tun da nake ban taba ganin mace me irin halin Haj murjanatu ba, kawai dai matar mutum kabarinsa Amma da sai nace sam ba kayi dacen Mata da suruka ba, auren da tunda Ka yi Shi baka huta ba daga wannan sai wannan"

Taufiq ya numfasa yace "irin tawa kaddarar Kenan umma". Ta maida kallonta ga muhseena tace ,"yanzu idan ba bakin Hali irin na Haj murjanatu ba, me wannan yarinyar ta tsare Mata, yarinya Mai hankali da girmama mutane, idan Baka sani ba yau ina son na sanar da Kai zamanta a gidanku ba karamin Raya Muku gidà ta yi ba , don da yawan abubuwan alheri banga ana yinsu a gidanka ba sai bayan zuwanta, duk tsawon aurenka da matarka ban taba Jin shaawar zuwa gidanka ba sai bayan zuwan yarinyar nan gidanka, kasan dalili saboda hankalin Zainab da iya tarbar mutane da Kuma kulawa da mutane, don haka babu dalilin da wani zai ki ta don idan ba Ka so ta ba, ba zaka kita ba, ni dai bansan irin tunanin da Haj murjanatu take da Shi ba a kwanyarta".

Taufiq yace "umma ni Kaina na gaji da komai ina bukatar nayi rayuwa a Karan Kaina,".

Ta jinjina Kai tace

"Na Dade ina son kayi hakan, saboda haka ni ina tare da Kai a duk abinda Ka yanke ".

Cikin wani kwarin guiwar da ya dade baiji irinsa ba, yace ",nagode umma nagode".

Ta juya ta dubi muhseena tace "kiyi zamanki anan Zainab , ki dauki nan gidan tamkar gidan iyayenki, ki dauke ni tamkar mahaifiyarki kisa a ranki Baki da wata matsala anan gidan". Cike da biyayya muhseena ta yi ma Haj saratu godiya. Ayayinda da Haj saratun ta dubi Haulat ta umarceta da ta tafi da muhseena dakinta.

Haka Taufiq ya bi muhseena da kallo har suka shige cikin dakin.

Sun dade suna cigaba da tattaunawa akan matsalolin da ke dankare a cikin aurensa da mujaheeda. Har dai Taufiq ya bar gidan Alh Yusuf lamido bai dawo gidan ba.

****

Tun bayan komawar Haj murjanatu gida ta kasa zaune ta kasa tsaye, me yasa take son ta tabbatar da zarginta akan Alh Mustapha labaran? Me yasa idanun mujaheeda suka rufe bata tunanin cin amana da ga Alh Mustapha ko daga Taufiq?.

Anya kuwa ba laifinta ba ne da ta kasa sanar da ita sirrin da ta lullube? Saboda kawai rufuwar asirinsu da Kuma rufewar kima da darajarsu, gami da kokarin boyema hukunci.

Shin ko dai abinda ta shuka ne Zata girbe Shi a dai dai wannan lokacin da abubuwa suke da tsauri fiye da da.shin idan ba son Zainab mijinta ya ke yi ba, to menene alakar da ke tsakanin Shi da ita da ya dauki wani bangare na kulawa ya bata, me yasa baya son ta bata Mata ko ta aibatata, Wanda idan hakan ya faru yake mance komai ya tsaya ya gaya magana, a tsawon shekaru ashirin da wani Alh Mustapha Bai da katabus baida karfin guiwar da zai iya tsayawa a gabanta Yana yi Mata irin abinda yake Mata yanzu sai a dalilin Zainab.

Shin wacece ita a gare Shi?.

Irin Jerin tambayoyin da suke ta yawo a kwakwalwarta Kenan , Kuma tana matukar bukatar Jin amsar su daga Alh Mustapha labaran.

Kafin dawowar Alh Mustapha Haj murjanatu ta kusa zarewa saboda tsabar tashin hankali.

Hakan yasa Yana dawowa kallo daya ya yi ma fuskarta ya fahimci akwai tashin hankali, don haka ko a falo bai zauna ba domin ya gaji da raba hali gaban masu aiki, yasan babu daraja aciki.

Shima dakin nasa ya na shiga ya yi saurin Sanya makulli ya kulle kofar.

Ya gaji baya tunanin a yau zai jure tsayawa yin fada da Haj murjanatu domin ko cikakkiyar lafiya ba ya da ita.

Cikin fusata Haj murjanatu take jijige kofar ta na Kiran sunansa Kai tsaye "Mustapha na rantse da Allah Ka Bude kofar nan". Gadonsa ya haye ya Dora kafa daya Kan daya Yana jijjigawa alamar baida lokacinta.

Haka tayi ta bugun kofa Amma yaki budewa ,don haka ta cigaba da maganganunta " Na yi maka rantsuwa matukar ba Ka gaya min abinda ke tsakaninka da Zainab ba , sai na kunna maka wutar da ba zaka iya kwashewa ba, ina tabbatar maka wannan Karon idan Kayi min irin cin amanar da kayi min da bazan tausaya maka ba, bazan boye laifinka ba da hannuna Zan dauki matakin da ya kamata na dauka a kanka, tsohon najadu Wanda idanunsa suke karewa Akan gajiyayyun Mata duk matan kirki a duniya ba su gsbanka sai Yan aiki, shin me kake ji

awajensu, mugu azzalumi "

Munin kalamanta yasa Alh Mustapha ya rufe kunnuwansa, haka tayi ta maganganu marasa dadi saboda hankalinta ya gushe bata ji ba ta gani.
Cikin maganganunta ne ta sanar da Shi ta Kori muhseena a gidan mujaheeda idan akwai abinda zai yi to yayi gaggawar yi idan Kuma zai bita ne to ga fili ga Mai doki.

Haka tayi tayi har sai data gaji sannan ta koma dakin ta cike da bacin rai da tsantsar damuwa.
Kamar yadda tunda ta ambaci ta Kori muhseena a gidan mujaheeda ya ji komai ya kwance masa tsananin damuwa ta baibaye Shi , shin ina zata shiga ? Kada fa ta fada mummunan hannu. Ya yi matukar damuwa da Zainab kamar yadda zai ji damuwa alokacin da dan cikin sa ya shiga garari.
Da sauri ya janyo waya ya Kira mujaheeda bugu daya ta dauka kamar tana Jiran Kiran nasa ta dauka.murya cike da damuwa zata Fara magana Alh Mustapha labaran ya rigata ,
"Mujaheeda ina Zainab ta tafi , Haj ta tabbatar min da cewa ta koreta da ga gidanki".
A damuwa mujaheeda tace "hakane daddy ba kaga abinda mummy tayi ne ni tsoroma ta ba ni".
Ya nisa yace "Abinda ya fi hakama zatayi babu ruwanta, yanzu kina da masaniyar inda Zainab din ta tafi?".
Ta girgiza Kai tace " yaya Taufiq ne ya dauketa hsr yanzu Kuma bai daga wayata ba balle nasan inda ya kaita".
Alh Mustapha yace "to shikenan ina zuwa".
Yana kashewa ya Kara dannawa ya Kira Taufiq, shima ya na Kira ya dauka , sama Sama suka gaisa sannan yace "Taufiq ina Ka Kai Zainab, mujaheeda ta gaya min Kai Ka tafi da ita bayan faruwar abinda ya faru".
Anan Taufiq ya tabbatar masa da cewa tana gidansu hannun mahaifiyarsa. Alh Mustapha labaran ya lumshe Ido cike da Samun nutsuwa da jindadi yace "nagode Allah ya yi maka albarka".
Taufiq ya ji maganar ta yi masa banbarakwai shin me yasa ya ke masa godiya don kawai ya killace muhseena.
Shi Kam tuni ya aje wayar Yana yi ma Allah godiya da yasa Zainab take kyakkyawan hannu.
Shi Kansa da zai samu Wanda zai gaya masa dalilin damuwar da yayi da lamarin Zainab hakika da ya gode, domin dai Shi Kansa bai San dalilin tsintar Kansa awannan yanayin ba.

A wañnan rana dai Taufiq ya riga ya Gama dukkan shirinsa na fitowa cikin rigar gaskiya ya gayá ma mujaheeda gaskiyar Lamari.
Ya riga ya dorama Kansa duk abinda zai faru sai dai ya faru amma fadama mujaheeda gaskiya wannan dole ne.
Komawarsa gida kusan karfe Tara na dare , ya tadda mujaheeda ta cika ta batse tana goye da Fadwa a bayanta tana aikin jijiga Wanda rabon da ya ganta a bayanta har ya manta a rayuwarsa.
Ko Zama baiyi ba ta bishi da tambaya me cike da fushi.
"Me yasa na kiraka har sau biyu amma Baka daga wayata ba Kuma Baka Kira ni ba" ya girgiza

Kai yace "na Kira bayan na ga kiranki Amma network babu kyau bata shiga ba".

Tayi masa kallon tsaf tace "ina Ka Kai Zainab?, Domin bayan tafiyarku da na Sami nutsuwa na shiga wani tunani da Bana son ya Zama gaskiya ".

Ya dubeta sosai yace
"Wane irin tunani?".

Ta dawo gabansa sosai ta cigaba da tsayuwa sannan tace "ina ta hango irin kunci da damuwar da Ka shiga ne alokacin da mummy ke ma Zainab fada, sai Naga tamkar bata Kai matsayin da zaka nuna irin wannan damuwar akanta ba, bayan haka Kuma abubuwa da dama sun ta dawo min a Kaina, na yadda kake nuna kulawa a gareta irin kulawar da ta sha bam bam da irin kulawar da nake bata".

Ya dan numfasa babu alamar tsoro ko girgiza fa GA kalaman da tayi duk ds irin tsare Shi da Idon da tayi.

Ya muskuta ya ce "babu inda na kaita sai gidan mu wajen umma".

Ta aje ajiyar zuciya tace
"Oho".

Ta koma ta zauna tana kokarin sakko Fadwa daga bayanta, tana cewa "tunda Zainab ta tafi take kuka daker na Samu tayi shuru shima din Yan mintoci tana farkawa zata fashe da kuka tana nemanta".

Ya gyada Kai yace "to ko don wannan dalilin ina ganin ba zaki so Zainab tabar gidan nan ba".

Ta juyo tana yi masa wani irin kallo sannan tace "Zan so haka , Amma bayan faruwar abinda ya faru yau , ina ganin tamkar mummy ta fi ni gaskiya, don ba karamin abu ba ne zaisa ta furta babu ni babu ita, tabbas akwai abinda ta ke hangar min Wanda ni Bana hangoma Kaina, domin nima a yanzu ina ganin bazan iya cigaba da Zama tare da ita ba, ko don ceto rayuwar aurena, domin Bana son shaidan ya ci galabar Sanya min zarginka a cikin zuciya ta".

Taufiq ya Kai hannu ya amshi Fadwa ya rungume a kirjinsa, Abinda ba ya son faruwarsa ne ya ke son ya faru ko ma yace ya faru wato Fara zarginsa da mujaheeda ta Fara akan muhseena gara yau dai ayi ta ta kare.

Ya dan dago ya dubeta , ga mamakinsa itama wani irin kallo take yi masa.

Ya yi saurin dauke Kansa kafin ya Fara magana.

"Duk wannan ba Shi ba ne mujaheeda, kawai dai ina son kisa aranki bawa baya wuce kaddarar sa, kamar yadda komai ya ke rubuce a jikin allon kaddararka don haka duk abinda zai Sami bawa babu makawa rubutacce ne".

Ji tayi ta samu kanta da faduwar gaba me tsanani sannan ta kasa dauke idonta daga gare Shi. sosai ya ke cikin nutsuwa tabbatar duk abinda yake kokarin fada abu ne me matukar muhimmanci, hakan yasa itama ta samu nutsuwa.

Ya cigaba da cewa " Babu abinda ya kamata na rufe Miki domin kema ya shafeki kusan ma ya fi shafarki fiye da kowa, haka zalika na gaji da aje abin a cikin zuciyata domin idan na cigaba da hakan tamkar ina kokarin jefa Kaina açikin wuta ne Wanda nasan idan har son da kike min na gaskiya ne ba zaki so haka ba".

Zuwa wannan lokacin fa tuni jikin mujaheeda ya Fara rawa.

Amma bakinta ya kasa furta komai domin yadda ya yi Mata nauyi.

Sosai Taufiq ya dake bai damu da yanayin da ya ga ta Fara nunawa ba.

Ya cigaba da magana

" Abubuwa da dama sun faru lokaci Mai tsawo da naje aikin titi a wani kauye Durmi, ina fatan Baki manta ba".

Dama baisa ran zata amsa ba don haka Bai Jira amsarta ba ya shiga bata labarin duk abinda ya faru da Shi da muhseena a Durmi da zamanta matarsa .

Ya karasa da cewa

"Zuwanta gidanki baya cikin wani shiri daga garemu Allah ne kawai ya hadaku , Kuma muhseena bata taba nuna mugunta a gareki ba ta rayu tare da ke tsawon wannan lokacin bata taba nuna damuwarta akan tarayyar mu ba, abinda ta Miki babu wata mace ta wannan zamanin da zatayi Miki, don haka lokaci yayi da ya kamata muyi Mata adalci matukar Bama so Allah ya kama mu da hskkinta, daga kafin auren mu har bayan Auren mu ban taba tunanin Zan iya Kara aure ba don babu hakan acikin tsarina don da ina da tsarin hakan da tuni na Kara aure Ko don fitinar da ta dinga afkuwa a tsajanin mu, Amma da yake Allah ya riga ya tsara min hakan babu yadda zanyi dole na karba da hannu biyu".

Shirun da ya ji mujaheeda ta yi ne yasa ya dawo da idonsa gare ta.

Me zai gani mujaheeda ya gani duk ta sankare, a gaggauce ya kwantar da Fadwa ya Mike a sukwane ya yo kanta Yana jijjigata Yana Kiran sunanta.amma ina hannunta na dore Kan zuciyarta ta sankare babu numfashi babu alamarsa alamar tuni ta Suma.

Karan Kiran sunanta da yake yi ne da karfi ya janyo hankalin su uwale da hassi da gudu suka fito da ga daki suna tsuma.Ganin halin da uwardakinsu take ciki ya jefa damuwa acikin zukatansu.

Taufiq ya ba uwale umarnin ta dauki Fadwa , ayayinda ya kinkimi mujaheeda zuwa wajen mota. Cikin kankanin lokaci yayi asibiti da ita. Cike da tashin hankali.

Taufiq ya yi matukar Saar Samun likitan mujaheeda a asibitin Dr Balarabe Yana daya daga cikin likitocin da suke aiki a wañnan daren.

Nan da nan babu bata lokaci Dr Balarabe ya amsheta zuwa daki na musamman.

Taufiq ya koma turus ya fada Kan kujerar da aka aje domin irin su masu kawo marasa lafiya.

Jikinsa sharkaf ya yi da zufa, yau dai ya sauke wannan gagarumin nauyi da ya ke Kansa. Sai dai ya taya mujaheeda da adduar Samun lafiya tare da amsar wannan kaddarar.

Ya duba a gogwan da ke daure a tsintsiyar hsnnunsa karfe goma sha biyu da minti hudu ne na dare.

Ya zaro wayarsa Yana nazarin Wanda zai Fara Kira a wañnan daren..Haj murjanatu ya Fara tunanin ya Kira Amma ya fasa yayi tunanin ya Kira Alh Mustapha labaran shima ya fasa.

Gaba daya sai ya koma ya kurama wayar Ido domin ya kasa Samun karfin guiwar iya Kiran kowa.

Kowa ya Kira a wañnan Daren yasan bai yi masa adalci ba, domin yasan babu Wanda zai iya yin bacci ko Samun nutsuwa daga sanda ya ji abinda ke damun mujaheeda.

Zaune ya ke Shi kadai Yana sa ran fitowar likita Amma babu Wanda ya fito daga dakin.

Ya Kara daukar waya ya Danna ya kira uwale domin ya ji halin da Fadwa ta ke ciki.

Ta gaya masa ta tashi ta yi ta kuka tana neman muhseena amma ta bata abincinta , ta Kuma samu ta koma bacci. Yace "to don Allah ki Kula da ita yadda ya kamata" ta amsa da babu komai zanyi iya kokarina.

Hakanan ya cigaba da Zama a asibitin Shi kadai cike fargaba.har zuwa karfe uku da rabi na

dare, sannan Dr Balarabe ya fito cikin tashin hankali Yana duban Taufiq Wanda ya tashi da sauri ya nufo Shi, Yana tambayat lafiyar mujaheeda.

Dr Balarabe ya girgiza Kai yace "ina fargabar faruwar abubuwa da dama Wanda a yanzu dai babu abinda Zan iya cewa sai zuwa gobe, idan munga abinda Hali yayi".

Taufiq ya zuba masa Ido yace "to Amma likita yaya jikin nata me ke faruwa da ita".

Dafa kafadarsa kawai yayi yace "Ka dai yi ta addua".

Bai Jira komai ba ya wuce, a hankali kamar kazar da kwai ya fashema a ciki Taufiq ya taka zuwa dakin da mujaheeda ta ke kwance.

Ya tura kofar a hankali ya shiga, ya firgita da ganin yadda nan da nan mujaheeda ta kwantsame ta rame sosai saboda wahala.

Kamar yadda ya gigita da ganin irin na'urorin da ke manne a jikinta an Sanya Mata iskar oxygen Wanda shine a yanzu ya ke taimakonta rayuwa. Babu inda ke motsi a jikinta.

Taufiq ya zube kasa , Yana maida ajiyar zuciya kamar Wanda ya shiga gasar gudu.

Yayi zaton hakan zai faru ranar da duk mujaheeda tasan wannan sirrin Amma baiyi tunanin ràshin karfin imaninta ya Kai ta jefa kanta cikin wannan mugun yanayin saboda kawai kishi.

Haka zalika ko kadan bai ji nadamar Gaya Mata komai ba, domin ko Bai Gaya Mata ba duk sanda ta Sani sai irin haka ya faru.kuma ya fi Jin tsoron ubangijinsa a kanta.

Sai dai ya tausaya Mata matuka shima Kuma ya shiga damuwa da ya kasance shine sila.

Nan bakin gadon ya koma ya zauna Yana kallon mummunan halin da mujaheeda ta ke ciki tare da yi Mata adduar Samun sauki.

Yadda ya ga rana haka ya ga dare, duk shaharar satar bacci yau Bai sace Shi na.

A masallacin asibitin ya yi sallar asuba.yana fitowa uwale ya Fara Kira domin ya ji lafiyar Fadwa. Ta tabbatar masa tayi rigima sosai da daddare Amma ta Kara Samun bacci kusan asuba har yanzu Kuma bata farka ba ta Kara da tambayarsa "ya jikin Haj" yace "da sauki, idan ta tashi ki bata abinci sosai" tace "ai Samun saukin ma Kenan da take cin abincin nata".

Bayan sun gama waya ne ya Danna ya kira Alh Mustapha labaran ya sanar da Shi a asibiti ya kwana saboda ciwon mujaheeda ya tashi .

Nan da nan Alh Mustapha ya shiga damuwa, da sauri ya shirya ya Bude kofar a hankali ya fito.

Wani abin mamaki da takaici a kofar dakin ya ga Haj murjanatu zaune ta jingina da bango tana bacci, tabbatar kila anan ma ta kwana don kawai ya ki Bude kofarsa suyi fada.

Firgigit ta Bude idon ta ganinsa a gabanta yasa ya Mike da sauri cike da jaraba, da alama zata dora ne daga inda ta tsaya.

Hakan yasa yayi saurin dakatar da ita ta hanyar gaya Mata, mujaheeda tun dare tana asibiti ciwon ta ya tashi batasan ma Wanda ke kanta ba.

Ya Kara da cewa "kinga idan abinda kika aikata ne a gidan ta jiya ya janyo wannan matsalar ke kika jiyo kin fi kowa shiga damuwa da garari, ni na wuce asibitin".

Har ya rstseta ya wuce ta kasa gane a wane halima ta ke ciki. Gaba daya ta gigice ta fita hayyacinta, idan akwai Kalmar da ta tsana tabbas Bai wuce ace ciwon mujaheeda ya tashi ba.

A kidime ta yi daki domin tayi Shirin zuwa asibiti cikin tsananin tashin hankali da ràshin sanin madafar dafawa.

Shin wannan Zainab din wacece da take neman ta tarwatsa Mata zuri'a?.....

TO BE CONTINUE

DAGA TASKAR YAR GIDAN IMAM

NI MA MATARSA CE
58

Hajaran majaran Haj murjanatu ta isa asibitin da taimakon direbanta. Cike da kidima.
Zuwa lokacin kuwa Alh Mustapha labaran da Alh Yusuf lamido duk Suna gaban gadon mujaheeda wacce bata San a duniyar da take ba.
Gefe daya Taufiq ne zaune Kan kujera ya buga tagumi hannu biyu kallo daya zakayi masa Ka yarda da cewa Yana cikin matsananciyar damuwa.
Haj murjanatu ta zube gaban mujaheeda tana shasshekar kuka tana fadin "mujaheeda kece haka cikin oxygen, Innalillahi wainna'ilaihirrajiun, ya Allah Ka kawo min dauki".
Alh Mustapha labaran ya sakar Mata harara a fakaice haushinta ya ke ji sosai , a zuciyarsa yace yanzu ne kika San da Allah.
Alh Yusuf lamido cike da tausayawa yace "Haj sai dai hakuri ayi hakuri Allah zai bata lafiya".
Ta waigo ta dube Shi sosai sannan ta dauke kallonta a Kansa ta dora akan fuskar Taufiq.
Sannan ta ta so tana magana cike da zargi "Taufiq meye ya faru da ya ta meya sameta, hanzarta Ka gaya min".

Taufiq ya dan muskuta gami da Kara yin kasa da Kansa ba tare da yace uffan ba. Harta Matso sosai kusa da Shi tana cigaba da tambayarsa.
Ananne Alh Mustapha ya dakatar da ita yace "don Allah Kada ki tada wata fitina anan, ki Sami nutsuwa ba sai kin zo kin gwada hali ba, nan asibiti ne ba wajen hayaniya ba, Shi Taufiq din shine ya ke dora Mata ciwo da lafiya da zaki tambaye Shi"?
Ta watsa masa harara tace "bashi ya ke dora ciwo ba , bavkuka Shi yake ba da lafiya ba, Amma dole na tambaye Shi dalilin tashin ciwon ya ta domin daga ni har Ku kunsan dalili me karfi na tashin ciwon nata nasan Kuma duk duniya shine damuwarta Shi ke sa ciwonta ya tashi".
Alh Yusuf lamido gefe ya koma ya jingina da bango Yana cigaba da kallon ràshin albarka irin na Haj murjanatu.
Alh Mustapha labaran ya girgiza Kai yace "to wannan Karon ina tsammanin kece silar tashin ciwon nata domin Bana raba daya biyu saboda kin Kori Zainab daga gidan ta ne damuwa ta yi Mata yawa ta kasa jurewa shine ta Sami kanta a cikin wannan mugun Yana yin ".
Zata yi magana kenan Dr Balarabe ya shigo hakan yasa gaba daya su kayi shuru.
Ayayinda Haj murjanatu ta yi Kansa da tambaya duk ta fita hayyacinta." Likita meya Sami mujaheeda ".
Ya matsa kusa da mujaheeda sai da ya Gama tattabata ya Gama Yin duk abinda ya dace sannan ya dubi Haj murjanatu yace "Haj mu je office (ya Kara duban Alh Mustapha) Alh kaima muna da bukatarka".
Ya waiga ya Kara kallon Taufiq irin damuwar da ke tattare da Shi ta fi wacce ya zo da ita asibitin, Wanda tunda ya gaya masa halin da mujaheeda ta shiga ya fahimci gaba daya ya susuce.

Haj murjanatu da Àlh Mustapha sun ma riga likitan fita daga dakin, sai daga baya ne ya bi bayansu,

Tare suka jera har zuwa office dinsa.

Alh Yusuf lamido ya tako ahankali zuwa inda Taufiq ke zaune.yasa hannu ya dafa kafadarsa , yau ne Karo na farko da ya ji Yana tausayin dansa da ya kasance surikin mace irin Haj murjanatu wacce bata San Allah ba Kwata kwata, a duk lokacin da ciwon mujaheeda ya tashi ya ji Haj murjanatu tana dorama Taufiq laifin tashin ciwon nata ya Kan ji matukar zafi a cikin ransa.

Ya dago da jajayen idanunsa ya dubi mahaifinsa.gaba daya sai ya kwanto da jikinsa Kan Alh Yusuf lamido ya rungume Shi sosai Yana Jin saukin damuwar da ke tare dashi.

Alh Yusuf lamido ya karasa hannayensa biyu ya rungume Taufiq Yana cewa "kayi hakuri, ko wane mutum akwai jaraftar da Allah ya ke dora masa kasa aranka Kai wannan ce taka jaraftar don haka kayi hakuri, kayi tawakkali domin shine musuluncin, komai zai yi dai dai in sha Allah zata Sami lafiya".

Jinsa kawai ya ke yi domin ya kasa furta komai illa adduar da ya ke yi acikin zuciyarsa na cewa .

Allah kaima ya Sanya fahimta a tare da Kai a duk lokacin da na sanar da Kai dalilin ciwon mujaheeda.

"Likita Ka gaggauta sanar da ni halin da mujaheeda ta ke ciki, tun kafin na karasa rasa tunani na".

Dr Balarabe ya numfasa gami da duban Alh Mustapha labaran don ya fahimci Shi kadai ne zai fi fahimtar sa don shine ya ke cikin nutsuwarsa, sabanin Haj murjanatu da ya fahimci Sam bata cikin hayyacinta.

"Alh, ina fargabar sanar da Ku cewar zuciyar mujaheeda ta tsaya da aiki, sakamakon hakan yasa .....?".

Yayi shuru Shi Kansa Yana ganin girman abinda zai fada.

Cikin kaguwa Alh Mustapha yace "ina jinka likita".

Haj murjanatu ta cigaba da kallonsa cikin kosawa da son Jin karshen maganarsa.

Dr Balarabe ya jinjina Kai ya cigaba da cewa "Adalilin hakan munyi iya bakin kokarin mu domin ta dawo hayyacinta, amma bamu Sami nasarar yin hakan ba, kasancewar ta riga ta fada coma".

Gaban Alh Mustapha labaran yayi mummunan faduwa , ya fiddo idanu waje cike da tsananin firgita da tsoro,

"Coma" ya maimaita cikin tashin hankali. Gami da juyawa Yana duban Haj murjanatu da tunda likita ya ambaci coma ta rasa a duniyar da take idanu kawai ta ke zarewa tamkar zautacciya.

Dr Balarabe yace "zata cigaba da kasancewa a haka mu kanmu bamu San iya lokacin da zata kasance a cikin wannan rayuwar ba, rayuwar da banbancinka da matacce kadan ne , babu abinda zata iya yi sai dai wasu lokutan zata iya Jin irin maganganun da ake yi a kusa da ita Wanda muna ganin sune zasu iya yin tasirin dawo da ita duniyar rayuwa, fiye da magungunan da zata dinga sha.....?.

Hadiye sauran maganar ya yi alokacin da Haj murjanatu ta rikito daga Kan kujera ta Fadi kasa sumammiya.

Gaba daya Alh Mustapha da Dr Balarabe suka yo kanta.

Dr Balarabe Yana kwalama nurse Kira Wanda nan da nan suka shiga shigowa cikin office din. Gadon daukar marasa lafiya , aka dora Haj murjanatu aka gungurata zuwa dakin da aka ware Mata .

Dr Balarabe ya bi bayansu Shi da Alh Mustapha labaran.

Ya duddubata sannan ya daura Mata ledar ruwa.

Abin duk ya hade ya Kara cakudewa.

Taufiq da Alh yusuf lamido har suka shiga duba Haj murjanatu itama bata farfado ba Haka suka dunguma suka Kara komawa wajen Dr Balarabe inda ya cigaba da yi musu bayanin ciwon mujaheeda ita Kuma Haj murjanatu ya tabbatar musu kidima ce ta sata sumewa Amma zata farfado nan ba da jimawa ba.

Alh Yusuf lamido ya dubi Taufiq cike da damuwa yace 'daman kasan mujaheeda ta fada coma?"..

..ya gyada Kai ya ce "eh dazu kafin zuwanku asibitin likita ya sanar min da hakan ".

Zuwa yanzu wani kallo Alh Yusuf lamido ya kema Taufiq me cike da tuhuma yace"Kuma kana ganin dalilin barin Zainab gidanne mujaheeda ta samu wannan matsalar? Idan haka ne wane irin matsayi mujaheeda ta ba Zainab da fifiko".

Taufiq ya kasa cewa komai.

Alh Yusuf lamido ya jinjina Kai alamar ràshin gamsuwa sannan yace "Kai Taufiq dube ni nan ina bukatar Jin gaskiyar abinda ke faruwa ".

Ananne Taufiq ya motsa bakinsa a hankali yace "Abba ko ba Ka bukaci sanin dalili ba, tabbas a yau Zan sanar da Kai komai ".

Alh Mustapha labaran yayi saurin dubansa yace "Taufiq kana nufin akwai wani abu ne a kasa? Kana nufin akwai dalilin da ya jefa mujaheeda cikin wannan halin ,bayan dalilin da nake zato".

Ya gyada Kai

Yace "eh ".

"To menene"

Cewar Àlh Mustapha, Taufiq ya girgiza Kai sannan yace "Maganar duk bata nan bace, domin magana ce da take bukatar natsuwa da kyakkyawan nazari, don haka gida ne ya kamata a yi maganar a can"

Alh Mustapha labaran ya gyada Kai yace "hakane to babu damuwa" Alh Yusuf lamido dai yayi shuru cike yake da fatan ba wani mummunan al'amari bane ya faru a tsakaninsu .

Don yasan jarabar Haj murjanatu ba zasu iya jureta ba.

Tun lokacin da Alh yusuf lamido ya tabbatar ma da Haj saratu ciwon mujaheeda ya tashi Taufiq ya Kira Shi ya sanar da Shi.

To tunda ya tafi asibitin muhseena ta kasa Samun nutsuwa, hankalinta a matukar tashe ya ke ta kasa yin komai banda damuwa.

Bata Sami Dan natsuwa ba saida Haj saratu ta amince Mata zuwa ta dakko Fadwa.

Wanda cikin kankanin lokaci suka je suka amso ta a hannun uwale ita da Haulat.

. Tunda suka dawo gida muhseena ta koma hidimar Fadwa, ta ji ba dadi sosai musamman yadda taga har Fadwa ta rame.

Dole dai anyi Mata yayen karfi da yaji.

Duk da dama ta isa yayen Amma ba irin wannan ba na ràshin shiri.

Cikin faduwar gaba muhseena ta ke, shin meya faru? Kar dai ace Taufiq ya gayama mujaheeda abinda ke tsakaninsu ne?.

Wani irin tashin hankali ta ji ta fada ciki, ina zata sa kanta idan har itace silar wannan damuwar, bata son kowa ya shiga tashin hankali saboda ita.

Duk bayan sakwanni Saita kalli wayarta tana son Kiran Taufiq don ta ji halinda ake ciki Amma ta kasa.

Ita kanta Haj saratu ta fahimci damuwar muhseena tayi yawa, shin Anya damuwar ciwon mujaheeda ne kadai ya ke damunta ko kuwa akwai wani abin bayan hakan ".

Sosai ta ke Lura da yanayin muhseena.

Alh Yusuf lamido ya riga, Taufiq barin asibitin.

Domin Shi Taufiq Bai bar asibitin ba har sai da Haj murjanatu ta farfado.

Wanda tunda ta farfado da kanta ta cire Karin ruwan da ake Mata ta koma dakin mujaheeda ta sata gaba tana zubar da hawaye.

Ta Kuma rasa dalilin da yasa, daga Alh Mustapha har Taufiq din wani irin mugun haushin su take ji ko kallonsu bata son yi.

Fahimtar hakan da Taufiq ya yi ne ya tattara ya bar asibitin ya wuce gida cike da son ganin Fadwa.

Amma Yana zuwa gida uwale ta tabbatar masa da cewa muhseena ta zo ita da Haulat sun tafi da ita.

Taufiq ya numfasa son muhseena ya Kara cika zuciyarsa, hakika da mujaheeda tasan yadda muhseena ta dauketa hakika da bata jefa kanta acikin wannan masifar ba, na ràshin tawakkali da dora ma Kai masifa akan abinda Allah ya halarta.

Wanka ya yi ya kintsa ya Dan ci abinci Sama Sama sannan.

Sannan ya samu ya kwanta domin ya Dan yi ramuwar bacci, Amma ina duk yadda ya so ya runtsa ya faskara.

Ya kosa ya sanar da kowa komai , ya kosa ya mallaki muhseena a matsayin ta na matarsa ya kosa ya lafar da wutar kaunarta da ke cin zuciyarsa, domin ya Kara tabbatar da cewa Babu yadda zaayi ya iya rayuwa babu muhseena.

Hmmmm Mata na wahalar da kansu sbanza Akan kishin da Wanda kake yi Domin sa baima San kana yi ba. Yanzu dai ga mujaheeda can a coma Wanda baisan Taufiq ya yi abinda take so ba asalima ciwonta ba zaisa ya bar komai ba, yanzu ma zai Fara babu abinda zai tsaida saboda ita.

Muhseena ce ta ja ta shiga coma , amma babu wacce ya ke so Kuma zai cigaba da so sai ita.

Babu ranar kishin da mujaheeda take yi. Domin akwai damuwa ga duk Wanda ya ce ba zai karbi hukuncin da Allah yayi ba.

Sai bayan da Taufiq ya idar da sallar magriba da issha'i sannan ya nufi gidansu.

Haj saratu ta dube Shi Yana zaune Kan kujera yayi jugum.

Tace "daga asibitin kake ya mejikin".

Ya numfasa yace "aah daga gida nake ,jiki Kam ba dadi"

Dai dai lokacin muhseena ta fito dauke da Fadwa da take yunkurin zuwa wajen babanta .

Ido ya kurama muhseena ji yake kamar ya janyota ya rungumeta ko ya samu ya lafar da

damuwar da yake ciki.

Ya amshi Fadwa ya rungume .

Tausayin sa ne ta ji Yana neman ya kamata ta matsa can ta zauna a kasa. Lokacin da Haj saratu take cewa "Alh ya Gaya min jikin nata sai hamdala wai ta shiga coma , sai dai maganganun da suka biyo baya sune suka dame ni". Ya Dan dubeta yace "wane irin maganganu umma". Ta numfasa tace "Yana ta fada ne din Yana ganin kamar fada kuka yi ya janyo Mata wannan matsalar".

Ya ce " banyi fada da ita ba sai dai magana ta gaskiya da na gaya Mata , Wanda gaskiyar ce ta kasa dauka ta kasa yarda da kaddara hakanne yayi sanadiyyar fadawarta halin da take ciki".

Zaton da muhseena tayi ya Zama gaskiya.

Gabanta yayi mummunan faduwa a sanyaye ta Mike zata shige cikin daki.

Kamar da ga sama taji Taufiq yace "muhseena ki dawo ki zauna domin duk abinda Zan sanar da da umma ya kamata na sanar da ita a gabanki ne".

Jin kafafunta ta yi suna rawa.

Musamman da ta ga Haj saratu ta zuba Mata Ido tana cewa "wacece muhseena". Taufiq ya nunata da hannunsa "Zainab itace muhseena".

Ta Kara juyawa ta kalleta ayayinda muhseena ta juya da sauri zata shiga daki. Ya Kara kiranta da karfi "nace ki dawo ki zauna, dole ysuva yita ta kare". Cike da mamaki Haj saratu tace "aah ayi ta ta kare na mene Kuma?.me ke faruwa ne"

Muhseena ta dawo cike da dimbin tashin hankali ta zube akasa ta maida kanta kasa.

Haj saratu ta dawo da kallonta Kansa tace "Kai Taufiq menene wai, ya akayi kasan sunan Zainab muhseena bayan ban taba Jin Ka ambaceta da haka ba".

Taufiq ya numfasa yace "Da farko dai ina neman afuwarki, sosai na gane Bai kamata na boye Miki irin wannan babban al'amarin ba ko da ko Zan boyema kowa to ke Bai kamata na boye Miki ba, domin idan akwai wacce ta fahimce ni a duniya to bayan ke ce".

To fa nan da nan Haj saratu ta Fara tsuma, tana tunanin Allah yasa ba wata masifar Taufiq ya dangwalo ba agame da mujaheeda.

Tayi saurin kallonsa tace "gaya min koma menene, na yi Maka afuwa na Kuma yi maka uziri, yanzu gaya min menene?".

Ya dago ya dubi muhseena yadda ta takure gefe cike da tsoro da fargabar abinda zai fito daga bakin Taufiq, yasa Taufiq ya Kara tabbatar da ya zaluunci muhseena don kawai zai bayyana matsayiinta a wajen mahaifiyarsa yasa ta shiga irin wannan tashin hankalin abinda tun farko daya fada da duk ba aje nan ba".

Dole yau ya sauke ma Kansa nauyin da ya ke barazana a gare Shi.

"Taufiq yi min magana "

Cewar Haj saratu.

Taufiq ya sauke Fadwa kasa da take son komawa hannun muhseena.

Sannan ya dubi Haj saratu yace

" Umma zaki iya tuna shekaru kusan biyu da suka wuce, wani lokaci da na taba zuwa wani aikin hanya wani kauye Durmi, Wanda ke kanki kin Lura da ràshin nutsuwata da kwanciyar hankali har kika yi min magana ".

Ta gyada Kai tace "Na tuna Taufiq,menene ya dawo da maganar yanzu"

Yace "saboda shine mafarin abinda ya faru da ni da muhseena ".

Ta fiddo idanu cike da mamaki tana kallon muhseena tana kallon Taufiq 'dama Ka Santa ne, me ya hadaku".

Sosai Taufiq ya natsu ya tattara hankalinsa kaf akan mahaifiyarsa, sannu Kuma a hankali ya kwashe labarin duk abinda ya faru tsakaninsa da muhseena a kauyen Durmi ya sanar da ita.

.....?

TO BE CONTINUE

DAGA TASKAR YAR GIDAN IMAM

NI MA MATARSA CE

59

Haj saratu tayi matukar kidimewa da Jin bayanin Taufiq me kama da alamara.

Ta nuna muhseena ta ce cikin dishasshiyar murya "Zainab matar ka ce?".

Ya jinjina Kai yace "hakane umma muhseena matata ce kamar yadda na gaya Miki komai, amma na rantse Miki haduwarta da mujaheeda kawai Allah ne ya tsara domin baya cikin shiriina ko kadan".

Haj saratu fa gaba daya ta rasa tunanin da zatayi sai kallon su kawai take yi tana Jin abin kamar almara.

"Ikon Allah "

Ta fada cikin rawar murya lokaci daya Kuma ta Mike kamar wacce akayi ma allura da sauri ta fice .

Muhseena ta dago suka hada Ido da Taufiq.

Ya Dan saki ajiyar zuciya yace "kiyi hakuri muhseena wannan itace kadai hanyar da Zan gyara kuskurena , Kuma Bana Jin Zan Sami kwanciyar hankali matukar ban baki dukkan yancinki ba".

Cikin nauyin baki muhseena tace "Idan Suma iyayen Naka basu amshe ni ba fa". Ya girgiza Kai yace "Bana tsammanin hakan daga gare su".

Zata yi magana kenan Haj saratu ta dago labule tace "Ku zo Duka Alh ya na bukatar ganinku, ".

Hakan ya tabbatar musu da cewa ta je ta sanar da Alh yusuf lamido abinda ke faruwa ne .gaba daya sai muhseena ta Kara gigicewa , shigowar Haulat Kenan dakin muhseena ta Mika Mata Fadwa ta Mike jiki a sanyaye.

Taufiq ya rigata fita da sauri ta bi bayansa tana karasa gyara zaman hijabin da ke jikinta. Haulat ta bi su da kallo tana tunanin me ye ya ya rikita su haka.

Zaune tsakiyar doguwar kujerar falon, muhseena ta hango Alh Yusuf lamido zaune kafe da gilashi a idonsa, fuskar sa tamke babu alamar wasa. Gefe Haj saratu ce zaune itama ta yi jugum.

Kasa muhseena ta zube ta zauna kamar yadda Taufiq ya zauna a kasa gami da lankwashe kafafunsa Kansa a kasa , ya ke kokarin gaida Alh Yusuf.

Wanda bai bi ta Kan gaisuwar ba, illa Ido da ya zuba masa masu cike da neman Karin bayani, yace "Taufiq wace magana ce nake ji a wajen mahaifiyar Ka , maganar da ta fi kama da labarin gizo da koki".

Taufiq ya numfasa, cike da karfin guiwa yace "Eh Abba dama Maganar da nace maka zamu yi ne idan Muka dawo gida".

Yace ba tare da ya cire idonsa akan Taufiq ba "ihum, ina jinka".

Ba tare da bata lokaci ba ya Gama sanar da Alh yusuf lamido komai babu abinda ya rage masa,sannan yace "To a jiya ne da daddare na sanar da mujaheeda komai, Wanda hakan ne yayi sanadiyyar fadawarta halin da ta shiga,"

Àlh Yusuf lamido ya yi dif ya kasa cewa komai tsawon wasu mintoci , zuwa lokacin kuwa tuni muhseena ta Kara gigicewa tana fargabar abinda zai fada matukar ya Bude bakinsa.

Haj saratu kuwa sai ta kalli Taufiq ta kalli muhseena, tana cike da mamaki, domin ko a mafarki bata taba tunanin Jin wannan zancen ba, Zainab matar Taufiq ce!.

Alh Yusuf lamido ya yi gyaran murya gami da cire gilashin fuskarsa ya na kallon Taufiq cikin tsananin fushi da fusata ya ce "Na tarbiyyantar da Kai, na yi kokarin Baka ilimin boko da na addini duk domin kasan me kyau da mara kyau kasan Kuma girman hakki, duk da wannan Amma kasa kafa Ka Shure , san rai ya rinjayi imaninka".

Ya nuna Shi da hsnnu "yanzu Taufiq Ka na matsayin mujin yarinyar nan amma Ka danne Mata hakki, Ka wulakanta ta Ka wofintar da ita ta zauna tana yi ma matarka bauta, Taufiq me Ka dauki aure ne? Wasan Yara ko me?, Don me baka sanar da mu ba har sai da aka dauki irin wannan dogon lokacin, tunda abin ya faru me yasa ba Ka Kira ni a waya kasanar da ni ba na taho kauyen".

Haj saratu tace "Nima Kaina ya daure Alh , na rasa yadda akayi Taufiq ya yi wannan gangancin".

Ya dubeta ya ce"ganganci ko shirme saratu, Kuma ba Shi kadai ya yi wannan shirmen ba har da iyayen yarinyar nan".

Ya kalli muhseena da kyau , sannan ya cigaba da cewa "saboda ko yar tsana ce yar su bai kamata su ba da ita a taho da ita ba tare da su ba, ya kamata ko Shi mahaifinta ya taho ya zo ya nemi iyayenka muyi magana, amma su Baka yarinya Ka taho da ita sannan duk tsawon wannan lokacin su kasa biyo ta su ga in da ta ke rayuwa haba".

Taufiq ya ce "nasan nayi kuskure, shine dalilin da yasa nake son gyara kuskuren nawa, don Allah Abba kayi hakuri Ka yi min afuwa".

Ya ce "Ita zaka nema gafara domin itace take da hakki akanka, don idan bata yafe maka ba kana cikin tsaka me wuya".

Taufiq ya dube Shi yace "yanzu Abba hakan Yana nuna cewa Ka amince da muhseena a matsayin surukarka".

Ya dubi muhseena yace "Bana cikin irin mutanen nan masu fifita son na su akan na wani, Kuma ni uba ne, babu yadda zaayi na sa hannu wajen tauye rayuwar yarinyar da ba ta ji ba bàta gani ba, wannan auren naku duk ràshin Imani da ràshin yarda da kaddarar mutum ba zai ki amincewa da Shi ba saboda abu ne Wanda Allah ne ya kaddara babu kuma Wanda zai ja da hukuncin ubangiji, Kuma dole ayima yarinyar nan adalci".

Wani sanyi ya ratsa zuciyarta hakika iyayen Taufiq sun cika dattawa , bata taba ganin mutane irin su ba, da son Kai da son zuciya baya tasiri idan anzo wajen gaskiya. Ko kadan bata taba zaton zasu amshe ta haka ba.

Haj saratu ta dubi muhseena tace "kwarai kuwa dole ayi Mata adalci, itama ta amsa sunan matar Taufiq Kuma na jidadi na Kuma yi farinciki domin nasan Taufiq ya yi dacen Mata don na

yarda da hankali da tarbiyyar Zainab, Allah yasa ma auren albarka ya kare dukkan sharri".

Cike da kunya da farinciki muhseena ta Kara janyo hijabi ta rufe fuskarta.

Alh Yusuf lamido ya dube ta yace " Tashi ki tafi Zainab, Kai Kuma Ka tsaya ina da magana da Kai". Muhseena ta Mike a hankali ta fita , zuciyarta cike da farinciki, bata taba zaton komai zai zo Mata da sauki ba ta bangaren gidansu Taufiq.

Alh yusuf lamido ya gyara zamansa ya na kallon Taufiq sannan yace " Taufiq ina son gobe idan Allah ya kaimu Ka tafi kauyen Durmi Ka dakko mahaifan Zainab Ka taho da su". Haj saratu ta gyada Kai tace "kwarai kuwa hakan ya yi".

Taufiq ya jinjina Kai ya ce "To Abba Allah ya kaimu goben".

Ya sake kallonsa yace "ina Kuma son Ka sani Bana son wata fitina ta faru tsakaninka da Haj murjanatu don kasan dai ba karamin tashin hankali ba ne ke Jiranka , a duk lokacin da Haj murjanatu ta ji wannan maganar, don haka ina umartarka da duk abinda zata fada Kada Ka sake Ka maida Mata martani , kayi Mata uziri ".

Yace "in sha Allah ba Zan biye Mata ba Abba"

Haj saratu tace "Ai ba Shi ba mu kanmu sai mun Kai zuciya nesa akan irin maganganun da zata gaya mana, tunda macece ita da batasan Allah ba, mara Kuma yin uziri,".

Alh Yusuf yace "Bana son kowa ya kulata mu toshe kunnan mu, ita Kuma mujaheedan Allah ya bata lafiya, ya Kuma bata juriyar yarda da kaddara".

Haj saratu ta tabe baki tace "in Banda ma halin mujaheeda da dorama Kai wahala ina ita ina dorama kanta irin wannan kishin, ai an San kishi babu macen da bata da Shi amma yakamata a dinga yin kishi na hankali da nutsuwa amma saboda kishi Ka nemi kashe kanka saboda me? Zaman duniya Bana kiyama ba, Wanda Allah ya kaddarama ita sai yayi hakuri ya karbi kaddara kawai shine zaman lafiyar mutum".

Alh yusuf lamido ya jinjina Kai ya ce "To ni dai Zan yi ma mujaheeda adalci kamar yadda Zan yima Zainab adalci babu wacce Zan ki a ciki tunda duk Suna da hakki a Kan mu". Haj saratu tace "kwarai kuwa babu wacce za mu ki a ciki".

Shi dai Taufiq ji ya yi tamkar an sauke masa dala da gauron dutse akansa , ya dinga Jin wani farinciki ya na bin cikin jikinsa, ya Sami nutsuwa kwarai da yadda mahaifansa suka fahimce Shi. Haka ya zauna suka cigaba da tattaunawa, kafin ya tashi ya tafi asibiti duk da ya so ya Sami kebewa da muhseena amma babu Dama tunda tana can dakin Haj saratu.

A asibitin ya tadda mujaheeda kamar yadda ya barta.

Haj murjanatu tana kusa da ita a zaune idanunta har sun kumbura saboda kuka ga wata rama da nan da nan tayi duk ta fige.

Irin kallon da take ma Taufiq na muzanta , Sam Taufiq bai son sa, ya koma kusa da gadon ya tsaya Yana kallon ta oxygen ke ta aiki a jikinta.

Yana Jin tausayinta sosai.

Ya dubi Haj murjanatu yace "ya jikin nata".

Ta watsa masa harara tace "Jiki Yana nan yadda Ka barshi, tunda Ka tafi dazu baka dawo ba sai yanzu da dare ya Mika, saboda ba Ka da damuwa, dole Ka Fara nuna Mata halin Ko'in Kula tun kafin aje ko'ina saboda kaga bata da sauran wani amfani a gareka".

Duk da ya ji zafin maganar ta, to fa ya danne zuciyarsa bai mayar Mata ba.

Ya Sami kujera ya zauna ba tare da ya ce uffan ba.

Ko kallonsa ba ta Kara yi ba.

Haka ya yi ta Zama babu me yima wani magana .
Karfe goma sha biyu da minti daya na dare, Alh Mustapha labaran ya shigo dakin.
"Aah Taufiq sai da Ka dawo ai da Ka zauna Ka huta". Cewar Àlh Mustapha Taufiq ya Mike ya gaishe shi ya amsa cike da kulawa.
"Ka dai ganta nan tana nan yadda Ka barta".
Taufiq yace "Allah ya bata lafiya" yace "Amin".
Haj murjanatu dai tana jinsu bata tanka ba.
Nan shima ya zauna sai kusan karfe daya sannan Àlh Mustapha ya dubi Taufiq yace "yau dai ba nan zaka kwana ba , tunda ga Haj nan, Ka tashi Ka tafi , Nima tafiya zanyi". Kafin yayi magana Haj murjanatu ta amshe "Dama ai ni ya kamata na zauna , duk Ku tafi ba ni da bukatarku". Alh Mustapha ya dagama Taufiq hannu alamar Kada ya ce komai.
Taufiq ya dubeta yace "sai da safe Haj".
Bata tanka ba, Alh Mustapha baice Mata Komai ba ya fice Taufiq ya bi bayan sa.
Alh Mustapha yace "Ka daina damuwa da wadannan maganganun da Haj ta ke yi, domin gaba daya gani nake kamar tun faruwar al'amarin nan tamkar akwai matsala a tare da ita, kasan yadda take da mujaheeda don haka sai muna yi muna Mata uziri".
Ya gyada Kai yace "babu Komai, Sam ni Bai dame ni ba". Yace "Allah ya maka Albarka, " yace "Amin".
Ya Kara kallonsa yace "yaya Zainab a gidan naku, ba dai wata matsala ko". Yace "Aah babu komai , lafiya lau ta ke", ya gyada Kai yace "yaya Fadwa?".
Taufiq yace "Fadwa tana wajen Zainab, bata rigima a hannunta lafiya lau". Yace "Masha Allah, Allah ya saka Mata da alheri,don Zainab yarinya ce me hankali da nutsuwa". Taufiq yace "gaskiya ne". Daganan ya dan dube Shi yace "Don Allah daddy ayi min afuwa, gobe bazan zo asibitin da wuri ba saboda ina da wani muhimmin aiki da zanyi , "
Alh Mustapha yace "Haba babu komai don ba zaka zo asibiti da wuri ba shine har sai Ka kawo uzirin Ka, kaje kayi uzirinka Allah ya ba da sa'a". Sosai Taufiq ya ke mutunta Alh Mustapha labaran saboda Yana da kirki ya dauke Shi tamkar dan da ya haifa.
Daga bisani dai sukayi sallama kowa ya shiga motarsa ya tafi.
Ko da ya koma gida bai wani samu bacci ba.
Karfe uku saura na dare hakurinsa ya gaza sosai yake son Jin muryar muhseena. Ya dauki wayarsa ya Kira ta, baiyi mamakin yadda bugu daya ta dauka ba, domin yasan a dai dai wannan lokacin tana raya dare ta hanyar yin nafilfilu.
"Ranki ya dade"
Ya fada cikin kwantar da murya , ta Dan yi murmushi tace "ba kayi bacci ba", ya mirgina Kan gadon yayi rigingine yace "Ta ya zaayi nayi bacci bayan Tunaninki ya Hana min sakat".
Wani iri ta ji, domin ba tayi tsammanin Jin hakan da ga bakinsa ba, domin a ganinta tunanin mujaheeda ya dace yayi ba tunanin ta ba, hmm namiji Kenan lamarinsa ya na da daure Kai , gaskiya da Mata zasu gane da sun daina wahalar da kansu akan namiji.
Saurin canja maganar tayi tace "ya jikin mujaheeda, akwai sauki kuwa", ya dan numfasa yace "Tana nan yadda ta take har yanzu tana cikin coma tana Samun numfashi da taimakon oxygen". Cike da tausayawa tace "na kasa Samun nutsuwa ina ganin kamar nice silar duk abinda ya faru da ita," ya girgiza Kai yace "Kada ki sa ma ranki wannan, ki Kuma cire ma kanki damuwa, ki Bani hadin Kai mu kasance daya ni da ke, saboda hakurina ya kusa karewa muhseena ina

matukar shaawarki ina son kasancewa da ke"
Muhseena tace "Don Allah baban Fadwa Ka daina wadannan maganganun domin ba wannan lokacin ba ne ya dace ayi su, Ka Jira har mujaheeda ta Sami sauki".
Bai San sanda ya tashi da sauri ya zauna ba yace "na Jira ta Sami sauki, kinsan abinda kike fada kuwa, ciwon da baa San ranar Samun saukin sa ba, wai me yasa kike son Ki dinga Dora min hukuncin abinda ba Zan iya ba ne", Jin tayi shuru yasa ya cigaba da cewa "haba muhseena don Allah don son Annabi kiyi hakuri ki yafe min, kisa aranki wannan masifar son naki da Allah ya Dora min sakayya ce Allah yayi Miki, ba sai kin cigaba da hukunta ni ba, domin tuni Allah ya Gama hukunta ni, don Allah kiyi hakuri ".

Sosai ta ke Jin wani irin abu nayi Mata yawo a cikin kwanyarta idan Taufiq nayi Mata irin wadannan maganganun, shin ko dai itama ta Fara son sa ne?.

Da sauri ta kauda wannan tunanin , sannan tace "kaje Ka kwanta, Ka Sami bacci kaga kana da tafiya gobe".

Yace " Jin muryarki ya fi min komai a yanzu idan har zaki Bani Dama Zan cigaba da Jin muryarki har a Kira sallar asuba".
Tayi jugum abin mamaki yake bata wai Taufiq ne ya koma haka akanta.

Ita kanta ta kasa aje wayar , haka Taufiq ya yi ta budema muhseena sirrin zuciyarsa, Bai gushe Yana sanar da ita ba har sai da muhseena ta gamsu da cewa hakika a yanzu Taufiq ya na yi Mata so na hakika, sai dai har yanzu ta kasa ba Shi amsar tambayarsa da yayi Mata na cewa " muhseena kina so na?".
Ta kasa ba Shi amsar ne saboda itama bata San amsar ba.
Sai da aka Kira sallar asuba sannan Taufiq ya kyale muhseena, yayi Shirin zuwa masallaci.

Yau tun safe kanwar Alh Mustapha labaran Haj madina ta ke asibitin tana taya Haj murjanatu kulawa da mujaheeda. Daker ta Samu Haj murjanatu ta yarda ta koma gida domin ta Dan yi wanka ta canja Kaya.

Shi ko Taufiq tun safe ya Gama Shiri ya dauki hanyar Durmi. Ko kadan Bai so iyayen muhseena su San halin da yake ciki da yarsu ba tun zuwanta jigawa.

Amma babu yadda zaiyi tunda a yanzu Yana son komai ya tafi dai dai.
Cikin lokaci ya isa kauyen Durmi . Hajara ta yi mamakin ganinsa , malllam Umar baya gidan amma cikin saa ba a dau wani lokaci ba sai gashi ya dawo, shima yayi matukar mamakin ganin Taufiq. Sai dai alokacin da ya sanar da su dalilin zuwansa. Gaba daya sai suka cikin tashin hankali da tsoro, malllam Umar ya dube Shi jiki a sanyaye yace "lafiya dai ko, me ya faru mahaifinka ke son ganin mu".
Taufiq ya gyara zamansa yace "babu komai Baba , kawai dai yace na zo na taho da Ku ne tunda Baku taba haduwa ba ". Hajara ta dubi Mallam Umar cikin ràshin gamsuwa da maganar Taufiq.
Mallam Umar ya gyada Kai yace "shikenan , bari mu kintsa". Hakanne yasa Taufiq ya fita daga gidan domin ya Basu damar shiryawa.
Yana fita Hajara ta dubi malllam Umar tace"Anya malllam kana ganin abinda Taufiq ya fada gaskiya ne kuwa, ta yaya rana tsaka zaace mu je jigawa Wanda duk tsawon wannan lokacin ba'ace mu je ba, ko dai muhseena ta yi wani abunne?".

Ya jinjina Kai yace "to yanzu dai Hajara babu abinda Zan iya cewa, illa mu Jira har mu je mu

tabbatar da abinda yafaru," cike da damuwa tace "To Allah yasa mu ji alheri".
Cikin kankanin lokaci suka Gama shiryawa.. malllam Umar ya yi ma Ande Dije bayanin komai , wannan Karon ba tayi mugayen maganganun da ta Saba ba, fatan dawowa lafiya kawai tayi musu tare da adduar Allah yasa ba wani mugun abin muhseena ta aikata ba.
Ranta ya Kara fari alokacin da zasu tafi Taufiq ya dauki kudi ya bata , ta jidadin kudin sosai domin dai bata da ko Sisi dama.Bayan sun gama komai ne Taufiq ya dau hanyar jigawa zukatan malam Umar da Hajara cike da tsananin tashin hankali.
TO BE CONTINUE

DAGA TASKAR YAR GIDAN IMAM
NI MA MATARSA CE
60

Haj murjanatu tayi sallama ta shigo cikin dakin , Kai tsaye gadon mujaheeda ta wuce tana kallonta, tana nan yadda ta barta. Haj madina ta dubeta tace "Haj kin dawo", tace "eh, na dawo, tana nan dai yadda na barta ko madina, ta Karasa magana muryarta na rawa alamun son yin kuka, Haj madina ta numfasa tace "sai hakuri Haj , ayi Kuma ta addua in sha Allah zaa Sami mafita Allah zai bata lafiya", tasa hannu ta goge hawayen da ya Fara fita Mata, ta koma ta fada Kan kujera ta rike kanta tana jujjuyawa , tana fadin "madina Bana cikin natsuwa, na rantse ni kadai nasan halin da nake ciki Jin zuciyata na ke kamar zata fashe saboda zafin da take min, a duk sanda na kalli mujaheeda na ga halin da take ciki nakan ji gaba daya duniyar tayi min zafi". Cike da tausayawa Haj madina ta dawo kusa da ita ta tsaya tace "nasani Haj , fadema batawa duk Wanda yasan irin soyayya da shskuwar da ke tsakaninki da mujaheeda yasan a hakama yadda kika zauna to kinyi matukar kokari, kawai dai ki daure ki rage damuwa ita Kuma ki cigaba da yi Mata addua". Haj murjanatu ta Kara sakin sautin kukanta waje tace , "Bani da kowa sai mujaheeda, itace sanyin idaniyata itace komai nawa, idan ta shiga damuwa nakan fita shiga damuwar ,yanzu ko da take wannan halin ji nake ni ma tamkar rayuwata ta tsaya, Bana iya cin abinci ni bansan ma awane hali nake ba, ji nake kamar ba ni ba". Haj madina tace "kiyi hakuri kiyi addua ne, dukkan tsanani Yana tare da sauki in sha Allah mujaheeda zata ji sauki zata warke ke dai kibar komai hannun ubangiji ".

Ta numfasa ta dago tana kallonta tace "Bayan tafiyata Alh ya zo asibitin nan kuwa?"ta gyada Kai tace "yaya ai ya Dade a asibitin nan , ko ya tafi baya awa daya ya ke dawowa, yanzuma Yana fita kina shigowa, nayi zaton ma ko kun hadu,"
Ta girgiza Kai tace "bamu hadu ba , ai nayi zaton bai zo ba".
Ta girgiza Kai tace ",ya zaayi kiyi zaton hakan Haj bayan kinfi kowa sanin matsayin da mujaheeda take da Shi awajen yaya , Yana matukar Sonta son da nayi yakini da cewa ko Shi ya haifeta ba lalle bane ya so ta kamar yadda yake Sonta a yanzu, ko ba ki Kula da irin ramar da shima yayi ba acikin kwanaki biyu kacal".
Haj murjanatu ta dan muskuta abinda Haj madina ta fada gaskiya ne, Amma sai dai ayanzu Sam bata ganin irin wannan halaccin nasa, haushinsa take ji sosai, ba don wannan lalurar da ta gitto ba da tuni sunyi mugun Samun matsala da shi, to yayi saa ayanzu ta lafiyar yarta take amma ba don haka ba da ya sha mamaki.

Tayi saurin kau da wannan tunanin aranta ta Kara kallon Haj madina tace "Taufiq fa ya zo?, Domin kamata ya yi na Ganshi a zaune Yana jinyar mujaheeda musamman da Bana asibitin ". Ananne Haj madina ta girgiza Kai tace " Aah, Taufiq bai karaso ba har yanzu, ni ma nayi mamakin hakan Allah dai yasa lafiya". Haj murjanatu ta saki tsaki tace "ke har tunanin lafiya kike yi, wannan yaron da babu komai agaban sa sai yaudara, ba wai tun yanzu na Lura da take takensa ba, bai damu da halin da mujaheeda take ciki ba, saboda Yana ganin ayanzu bata da wani amfani da zatayi masa, ".

Tayi saurin girgiza Kai tace""don Allah Haj Kada ki zargi Taufiq da wannan hasashen naki, Wanda na tabbatar ba gaskiya ba be, ta yaye ko Bai San mujaheeda ba zai kasa Jin damuwa akanta a irin wannan halin da take ciki , balle matarsa uwar yarsa,kila da akwai wani uziri da ya Hana masa zuwa" tayi Mata wani kyakkyawan kallo tace "haba madina, yanzu har Taufiq ya na da wani uziri sama da na ciwon mujaheeda ".

Haj madina zatayi magana kenan sallamar Haj Nana da Haj Binta ya sa ta hadiye maganarta.

Kai tsaye bakin gadon mujaheeda suka wuce cike da jimami.

'ikon Allah yanzu mujaheeda ce haka "

Cewar Haj Nana wacce tsoron Allah ya Fara Kamata ta cigaba da cewa "Dan Adam ba a bakin komai ya ke ba" Haj Binta tace "Allah ya bata lafiya, Allah ya tashi kafadarta".

Haj Nana ta dawo kusa da Haj murjanatu tasa hannu ta dafa bayanta , tana bata hakuri , daga bisani itama Haj Binta ta dawo inda suke itama tana bata hakuri , suna ta tausar zuciyarta, ita Kuma tana ta aikin sharar hawaye.Daga bisani Haj Nana ta dubi Haj murjanatu tace "Haj mu je daga waje, muyi yar wata magana ", Haj madina tayi saurin kallonsu tace tana kokarin Tashi, "aah basai kun fita ba kuyi zamanku, dama ina son yin sallah Bari na je nayi" kafin su ce wani abu, tuni Haj madina ta gyara hijabin kanta ta Bude kofa ta fice abinta. Haj Nana ta tabe Baki tace "ita wannan kanwar Mijin naki ta Faye nuna isa", ta dubeta tace "menene Haj Nana kike son ki fada".

Haj Nana ta koma ta zauna kusa da Haj murjanatu tana kallonta tace "Naga jikin mujaheeda yayi tsanani, ko da kike min bayani a waya ban taba tsammanin zanga jikin nata haka ba, hakanne Kuma ya tabbatar min da cewa akwai kalubale masu yawa da zasu fiskanto rayuwar mujaheeda marasa dadi".

Nan da nan Haj murjanatu ta dubeta cike da tashin hankali tace "Me kika fuskanta Haj , wane irin kalubale Kuma kike magana".

Haj Nana ta gyara zamanta tace "Ta bangaren aurenta, Haj nayi Imani yanzu ne mijinta zai nuna ainihin halin nasu na Maza, don Yana ganin mujaheeda ta koma haka ya Kuma tabbatar bata da wani sauran amfani a gare Shi , to fa Kada ki raba daya biyu, mantawa zaiyi da ita ya je can ya Kara aurensa ya bar Miki yarki Wanda nasan shine Abu na karshe Wanda ba zaki iya dauka ba". Haj murjanatu tayi dif tana nazarin maganganun Haj Nana Wanda tasan duk gaskiya take fada, Haj Binta ta gyara tsaiwarta tace ,"to wannan har sai an zauna ana ma fada, tabbas idan kinga Mijin mujaheeda bsi juya Mata baya ya Kuma Kara sure ba to ki rubuta ki aje ba namiji ba ne". Haj murjanatu ta yi kwata tace "Aiko da na bàta rayuwarsa, da na nuna masa Banda makiyi Sama da Shi, Kuma fa kinga wannan abinda kuka fada har ya ma ya Fara faruwa"

....Haj Nana tace "kamar ya ya, nan da nan haka tun kafin aje ko'ina, me yasa kikace haka"

Tace a kufule "ko kinsan yau kwata kwata yaron nan bai leko asibitin ba , Kuma ko waya bai

Kira ba, jiya ko tunda ya tafi gida da rana bai dawo asibitin ba sai wajen karfe goma sha biyu na dare, bugu da Kari tunda aka fara hidimar asibitin nan nerarsa bai bada ba".

Haj Nana tace "iye, lalle Taufiq ya cika butulu, to ta yaya zai bada kudin don hidimar asibiti bayan Yana ganinku masu kudi kun fi karfin Komai, ai cewa zaiyi ba zai yi asarar kudinsa a banza ba". Haj murjanatu tace "to yanzu meye abin yi , kinsan dai bazan zuba Ido Taufiq ya bar mujaheeda ba alokacin da tafi kowa bukatarsa, kamar yadda bazan bar wata ya ta sure Shi ba domin ina nan da takardar da ya sa hannunsa na cewar ba zai tabs yi ma mujaheeda kishiya ba, ke duk da bana son tarayyar mujaheeda da Taufiq na rantse bazan yarda da duk wani abu Mai kama da musgunawa ga mujaheeda ba yadda Zan kare Mata hakkinta, da bata farinciki sanda take da lafiya hakanan zai yi Mata lokacin da ta ke jinya, yanzu meye abin yi".

Haj Nana za tayi magana kenan .

Alh Mustapha labaran ya turo kofa ya shigo cikin sallama hakanne yasa ta hadiye maganarta, ta hau washe Baki tana gaida Shi.

Babu wani sakin fuska ya amsa lokaci daya ya wuce wajen mujaheeda ya janyo karamar kujerar da ke bakin gadon ya zauna Yana kallon yarsa cike da tausayawa, lokaci daya Kuma Yana bayyana ràshin jindadin ganinsu Haj Nana, domin idan akwai abinda ya tsana to bai wuce tarayyar Haj murjanatu da wadannan kawayen bata biyu ba, wadanda ya tabbatar Basu taba sanyata a hanya ta gari ba sai muguwar hanya , ko yanzu kallo daya yayi musu ya tabbatar ba alheri suke kullawa ba.

Da alama Haj Nana ta fahimci Basu Sami karbuwa a wajen Alh Mustapha labaran ba, dalilin hakan ne yasa Haj Nana da Haj Binta su kayi musu sallama gami da Kara nemama mujaheeda afuwa sannan suka fice.

Da sauri Haj murjanatu ta tashi ta bi bayansu.

Suna fita Haj Nana ta dubi Haj murjanatu tace "Haj ni naga Alh duk ya canja ne , ji irin kallon wulakancin da yake mana".

Haj murjanatu ta tabe baki tace "Aini Zan gaya Miki ya canja, yanzu wani irin izza da iko ya dorama Kansa,Shi a dole namiji ne yanzu, nifa abubuwa sunyi min yawa komai Yana neman cabe min, tun zuwan Zainab rayuwarmu ta kwace min dukkan farinciki".

Haj Nana ta yi kasa da murya tace "Shi yasa nake ganin idan kin Sami lokaci , ki zo mu je wajen Mallam me guru, duk da Baki zuwa kuna gaisawa ki mutstsuke kawai ki zo muje".

Ta gyada Kai tace

"Eh abinda zanyi Kenan ,Zan Sami lokaci na zo, sauran maganar dai ma karasa a waya".

Daganan dai su kayi sallama suka tafi ita Kuma ta koma cikin dakin.

A kufule ta shiga dakin tana kallon Alh Mustapha tace"kasan Taufiq bai zo asibitin nan ba kwata Kwata balle ya duba halin da mujaheeda take ciki, saboda bashi da Imani ".

Ya waigo Yana kallonta yace "don Allah ki dinga daurewa kina yi ma mutane zaton alheri ,"

Ta saki tsaki tace "Aida yake Baka son laifinsa Ka Fadi haka mana, nifa Bana bukatar taimakon kowa, ko ya zo ko Kada ya zo duk daya ".

Yace "inda duk daya ne ai da Baki yi maganar ràshin zuwan nasa ba, yaron nan tun jiya ya sanar da ni Yana da uzirin da zaiyi yau ba zai Sami damar zuwa asibiti da wuri ba, to ba sai ayi masa uziri ba".

Ta juya ta koma ta zauna tana kunkunin maganganu.

Shi dai Bai Kara tanka Mata ba.

Tun saukar su Hajara a jigawa, abubuwan da suka faru da ita a baya su Ka dinga dawo Mata a Kai .Duk da garin ya yi matukar canjawa to hakan Bai goge komai na daga abinda ya faru da ita ba a garin.

Isar su gidan Alh Yusuf lamido, malllam Umar da Hajara sun Sami kyakkyawar tarbar da ba suyi tsammanin ta ba, hakan ne ya dan rage musu damuwa a cikin zuciyar su.

Sai dai ganin muhseena a gidan surukanta ya dan daga hankalin su, Hajara duk motsi sai ta tambayi muhseena dalilin zamanta a cikin gidan , ko kuwa Dama tuntuni nan ta ke Zama, muhseena ta rasa amsar da zata ba ta.

Haj saratu ta shigo dakin cike da fara'a tana Jin irin tambayoyin da Hajara ke ta jeroma muhseena, shigowarta yasa ta yi shuru.

Haj saratu ta dube ta tace "don Allah ki kwantar da hankalinki, na Lura tun zuwanku ba kya cikin natsuwa danuwar da kike ciki ta nuna kanta a fuskar ki, ko abinci kin kasa natsuwa ki ci".

Ta cigaba da magana tana kallonta "babu wani abu na damuwa , ki kwantar da hankalinki alheri yasa aka dakko Ku ba sharri ba, nasan abinda ke damunki ba zai wuce tunanin ko auren Zainab ya Sami matsala bane, aah babu abinda ya faru da aurenta".

Hajara ta numfasa cike da gamsuwa tace "to Alhamdulillah har na Sami nutsuwa".

Haj saratu ta yi murmushi sosai tace "ki saki jikinki babu komai mun riga mun Zama daya".

Daganan waje Haj saratu ta zauna aka cigaba da hira, sai dai idon Hajara na Kan muhseena a zuciyarta babu abinda ta ke yabawa sai tsantsar Kyan da tayi, da Kuma irin gidan da take ciki, ashe Taufiq dan manyan mutane haka? Hakika muhseena tayi matukar Saar kasancewa bangaren wannan zuria masu cike da karamci da mutunci.

Shima can malllam Umar Yana dakin da aka sauke Shi, a cikin Jerin dakunan da suke a matsayin masaukin baki a gidan.

Yana zaune Akan makeken kafet din da ya malale tsakiyar dakin, gabansa cike ya ke da Kayan abinci Kala Kala ya ci ya koshi yayi hamdala. Zuciyarsa ta Fara Samun saukin damuwa bugu da Kari ya na cike da Yaba karancin Alh Yusuf lamido Wanda tun zuwansu garin yake kokarin maida Shi dan gida ba bako ba, ya Lura sosai da irin dacen da muhseena ta yi. Sai dai har yanzu Yana fatan ace ba Wata matsala bace tasa aka yi musu irin wannan Kiran na gaggawa.

Taufiq kuwa tun bayan da ya aje su a gidansu, ya wuce gida ya yi wanka ya Sami dan abinci ya ci , ya natsa sannan ya kama hanyar asibiti.

Cikin sallama ya shiga dakin, Amma Haj murjanatu bata amsa masa ba, sai Alh Mustapha ne ya amsa Yana kallonsa fuska sake yace "Ka shigo Taufiq".

Ya karaso gabansa Yana fadin "eh, ya jikin nata".

Kafin Alh Mustapha yayi magana Haj murjanatu ta amshe a fusace , "Ina ruwanka da jikinta, hidimar Ka ai tafi Ka zo kaga halin da take ciki, duk abinda kake yi na rantse bana mamaki domin idan ba kayi hakan ba ba zaka amsa sunanka na namiji ba butulu".

Alh Mustapha labaran ya tashi yayi Mata kallon tsaf yace fuska tamke, "ke dai tir da wannan halin naki na barin mutunci a inda bai kamata ki barar ba, meye na wannan maganar?".

Ta Kara fusata tace "kaga Ka fita harkata babu ruwanka da shiga sha'anina tunda ba zaka

taba goyon baya na ba, duk abinda nayi kuskure ne a gareka".

Zai yi magana kenan Taufiq ya Hana Shi , yace "don Allah kuyi hakuri, abar maganar".

Alh Mustapha ya jinjina Kai ya juya ya fita a yayinda Taufiq ya bayansa da kallo.

Yana kusa da mujaheeda Yana kallon halinda ta ke ciki, har yanzu tana nan kamar matacciya , wannan kadai ya isa ya dawo da Haj murjanatu hayyacinta amma ya ga tamkar abubuwan nata gaba kawai suke yi.

Ya zubama fuskar mujaheeda idanu, Yana Jin damuwa aransa musamman idan ya tuna shine silar kwanciyar mujaheeda a wañnan gadon.

Babu wani abu da mujaheeda zatayi masa da zaisa ya tsaneta ko ya juya Mata baya , Amma Kuma ba ya túnanin saboda kwanciyar hankali da farincikinta Shi zai salwantar da nashi farincikin, domin dai tabbas yasan ayanzu dai muhseena itace farincikin sa itace kwanciyar hankalin sa, zai iya cewa bai San so ba sai akan muhseena, da ita kadai yake Jin zai iya rayuwa cikin farinciki da jindadi.

Don haka zai cigaba da yima mujaheeda fatan Samun lafiya, da Kuma yarda da duk kaddarar da ta hau kanta.

Haj madina ta shigo ganin Taufiq suka gaisa , sannan ta dubi Haj murjanatu tace " Haj Zan leka gida na dakko kayan Sawa na , yaya yace anan Zan kwana". Haj murjanatu ta dubeta sosai take Jin tana son Haj madina a ranta a yanzu , saboda ta shiga lamarinta a lokacin da take tsananin bukatar hakan, tace "to shikenan sai kin dawo ".

Taufiq ya dubeta yace "Bari na zo na kaiki ".

Tace "Aida kayi zamanka Taufiq nagode"yace ""aah, muje na aje ki".

Dole dai ta amince da hakan , ita kuwa Haj murjanatu ko tankawa batayi ba har Taufiq ya fice, shima ba tare da ya ce Mata uffan ba.

Alh Yusuf lamido da Mallam Umar sun fito daga masallaci sallar isshai Kenan, Alh Yusuf lamido ya daga waya ya Kira Alh Mustapha bayan sun gaisa da tambayar mai jiki, sannan ya Kara da cewa "idan babu damuwa don Allah Ka zo gida yanzu, akwai wasu muhimman maganganu da zamu tattauna", Alh Mustapha labaran yace "To Allah yasa lafiya ".

Yace "lafiya lau, Kan maganar da Taufiq yace zai sanar da mu ne, shine nake son Ka Kara so domin mu tattauna". Yace "to shikenan gani nan zuwa in sha Allah yanzun nan".

Bayan ya aje wayar ne, suka karasa gida falon Alh Yusuf suka yada zango, malllam Umar dai Yana ganin karamci domin gaba daya Alh Yusuf ya maida Shi tamkar wani dan'uwansa, sosai suke ta hira Mallam Umar Yana sanar da Shi labarinsa.

Gaf da zuwan Alh Mustapha labaran,Alh Yusuf lamido ya Kira Taufiq a waya yace ya dawo gida yanzun nan , Yana nemansa.

Kusan tare suka karaso da Alh Mustapha.

Duk falon Alh Yusuf lamido suka zauna, ga Mallam Umar ga Alh Mustapha labaran ga Alh Yusuf lamido sannan ga Taufiq zube a Kasan kafet din falon.

Alh Yusuf lamido ya dubi Alh Mustapha labaran sannan ya dubi Mallam Umar yace "Alh Mustapha wannan sunansa Mallam Umar, shine Kuma mahaifin Zainab ". Alh Mustapha yayi saurin Kara Mika masa hannu suka Kara gaisawa, Yana fadin "Allah sarki, ashe Kaine mahaifin Zainab, yarinya me nutsuwa da hankali". Mallam Umar yace cikin fara'a "ai in dai muhseena ce haka take, ba yabon Kai ba tana da matukar hankali da tunani, kaifin hankalinta har ya fi yawan

shekarunta". Alh Mustapha ya jinjina Kai yace "Tabbas na Lura da hakan, Allah ya yi Mata albarka" gaba daya suka amsa da Amin.

Sannan Àlh yusuf lamido ya dubi Alh Mustapha labaran yace "Na zabi mu Fara Zama ne mu Maza kafin mu shigo da Mata cikin maganar, na fi son mu Fara fahimtar juna kafin su, su San abinda ke faruwa". Alh Mustapha yace "hakane, yanzu menene ke faruwa". Alh Yusuf ya numfasa yace "Wato Alh abin zai Baka matukar mamaki idan na gaya maka irin wautar da Taufiq ya yi". Alh Mustapha labaran yace "me Taufiq yayi".

Alh Yusuf lamido ya gyara zamansa yace "kasan cewa duk tsawon lokacin nan, Zainab a matsayin Mata take a wajen Taufiq".

Gaban Alh Mustapha ya yi mummunan faduwa ya zaro Ido bakinsa na rawa yace "Zainab Kuma, ta yaya ?".. Mallam Umar Kuma ya shiga musu kallon mamaki yace "aah, wai kuna nufin ba kusan muhseena matar Taufiq ba ce sai Yanzu".

Alh Yusuf lamido yace "kwarai kuwa Mallam Umar Ka gafarcemu, domin bansan matarsa ba ce sai jiya, shine Kuma dalilin da yasa nace masa ya je ya dakko min Ku".

Dif falon yayi kowa yayi shuru kamar ruwa ya ci su. Alh Mustapha gaba daya jikinsa ya jike da zufa, tuni Shi tunaninsa yayi nisa Yana hango masifar da muhseena zata fada matukar Haj murjanatu ta ji wannan maganar me kama da tatsuniya, ahakan ma babu wacce ta tsana Sama da ita balle ta ji wannan maganar, gashi Kuma har ga Allah baya Jin zai juri aibatawar da Haj murjanatu zatayi Mata domin har yanzu Yana Jin muhseena acikin jinin jikinsa. Amma Taufiq ya auri Zainab to ta yaya?.

Irin tunanin da ya fada, shima Mallam Umar tunanin ne aransa, Shin idan har Basu San muhseena matar Taufiq bace sai yanzu, to duk tsawon wannan lokacin wace irin rayuwa muhseena take yi?, Shin rayuwar wulakanta da ràshin yanci take yi KO me?, Shin duk abinda idanunsu suka gani ba gaskiya ba ne, yadda Taufiq ya nuna musu suna cikin zaman lafiya da kwanciyar hankali a matsayin ta na matarsa duk karya ne?..

Ido ya zubama Taufiq, Wanda Taufiq din ya kasa jurar irin kallon da yake masa ,ya sunkiyar da Kansa kasa cike da kunya.

Alh Yusuf lamido ne ya Kara gyara zamansa, ya sanar da Alh Mustapha labaran komai na yadda akayi muhseena ta Zama matar Taufiq, babu abinda ya rage masa, sannan ya cigaba da cewa "shine don shirme da wauta ya boye mana komai, ya Kuma Hana yarinya yancinta na matarsa, sai yanzu da hankali ya mare Shi, ya gane kuskurensa ya ke Kuma bukatar ya gyara kuskuren nasa shine ya sanar da matarsa komai ita Kuma ta kasa daukar kaddara shine ta fada wannan halin da take ciki a yanzu".

Alh Mustapha ya saki wata irin ajiyar zuciya yace "iko sai Allah, yanzu haka akayi Alh".

Yace "kwarai kuwa"

Ya juya ya dubi Mallam Umar da tashin hankali ya bayyana sosai a fuskarsa yace "kayi hakuri Mallam Umar nasan baa kyauta ba, Amma Kaima kana da laifi, don bai kamata ace irin wannan babban al'amarin ya faru ba , Amma Ka kasa neman mu , mu hadu musan Juna musan abinda ake ciki ba, aa ba Kayi hakan ba a matsayin Ka na uba, kawai sai Ka hado Taufiq da yarka ba tare da kasan inda zai Kaita ba, sannan Kuma a zauna tsawon irin wannan lokacin Baka nemi inda take kaganta ba abinda da mamaki sosai".

Malllam Umar ya numfasa yace "hakane Alh Amma mun ki biyota ne alokacin da suka taho saboda tashin hankalin da Taufiq ya Baro kauyen da Shi shine dalilin da nace Zan Bari har sai

ya sakko ya dawo cikin hayyacinsa sannan zamu taho, to bayan mun tabbatar da komai ya yi dai dai kusan ko yaushe muna Gaya musu muna son mu zo sai su kawo mana wani uzirin da ban Wanda zai hanamu zuwa, sai yanzu na fahimci dalilin da yasa basa son mu zo, saboda Kada mu ga halin da muhseena ta ke ciki ne?".

Alh Yusuf lamido ya dubi Alh Mustapha labaran yace to Àlh Ka dai ji abinda ke faruwa yanzu meye abin yi".

Alh Mustapha ya numfasa yace "Abin yi Kenan ayi ma muhseena adalci, itama tayi rayuwar auren da ko wace mace ke kwadayin yi da mijinta, babu son Kai ko son rai don mujaheeda tana matsayin yata ba Shi zaisa na yarda a tauye hakkin Wata mace ba, don haka dole kowa ya amshi wannan kaddarar".

Alh Yusuf lamido yace ",kwarai kuwa Alh , saboda haka gobe Ka dakko Haj murjanatu Ka taho da ita, domin yi Mata bayani Kai da ita zai iya yuwuwa ta dauki al'amarin da matukar zafi, Amma idan aka taru Duka ina ganin ko don idanun mutane ba zata tashi hankalinta da yawa ba, ta zo a zauna Duka da mahaifiyar Zainab din da Haj saratu idan Allah ya taimaka sai a fahimci juna".

Aran Alh Mustapha yace "hmm bakasan wacece Haj murjanatu ba, ganin mutane ba zaisa ta fasa abinda tayi niyya ba, ina Jin tsoron irin tashin hankali da dibar albarka da zatayi matukar ta ji wannan maganar".

A fili kuwa cewa yayi "to the Allah ya kaimu goben in sha Allah Zan taho da ita". A sanyaye Taufiq ya dago ya dube su yace "don Allah kuyi hakuri nasan ban kyauta ba amma ina neman afuwar Ku duka ". Alh Mustapha yace "babu komai Taufiq domin Shi bawa baya kaucema kaddarar sa, laifinka daya boye maganar da kayi, kila da Ka fada da duk baa zo nan ba, da Kuma wata kila mujaheeda bata shiga halin da ta shiga ba". Mallam Umar ya jinjina kai yace" Allah ya bata lafiya ya Kuma tashi kafadarta , babu dadi Sam Sam ". Haka suka cigaba da tattaunawa har dare yayi sosai Alh Mustapha labaran yayi sallama da su ya kama hanyar gida cike da tashin hankali da tunanin mummunan al'amarin da zai faru gobe idan Haj murjanatu ta ji abinda ke faruwa.....

TO BE CONTINUE

DAGA TASKAR YAR GIDAN

NI MA MATARSA CE

61

Domin ya fi kowa sanin wacece ita, ya kuma fi kowa sanin yadda ta dauki muhseena a ranta, ba ya jin zata iya amsar wannan kaddarar akan ko wace mace balle muhseena.

Sosai Alb mustapha ya ke jin fargaba ya kuma rasa dalilin da yasa ya ke jin matukar tausayin muhseena, da kuma tsoron abinda ka je ya dawo.

Hakanan ya ke jin baya son wani abu ya sami muhseena ba kuma ya son ta shiga damuwa domin a cikin ransa ya ke jinta. Shi kansa kuma ya rasa dalilin hakan,Abu daya dai ya sani shine yana jin komai na muhseena acikin jikinsa alheri ko akasin hakan.

Kai tsaye asibiti Alh Mustapha ya wuce , duk da dare yayi, zaune ya tadda haj murjanatu a gaban Mujaheeda tana aikin kuka, haj madina na gefe tana bata hakuri.

Guiwar Alh mustapha ta kara yin sanyi,ya dade a tsaye yana kara tunanin al'amarin kafin ya Yi mata maganar ta tashi su tafi, shima daker ta tashi.

Haj madina cike da tausayawa tayi sallama da su, suka tafi.

A mota bayan sun Fara tafiya ne , Alh Mustapha labaran ya dubi Haj murjanatu yace "ya kamata ki dinga sassauta ma kanki irin wannan damuwa, ki sani komai daga Allah yake babu Kuma Wanda ya isa yace don me yayi abinda yayi, saboda Allah ya fi mu son kanmu, Kuma akwai sakayya ta alheri ga masu hakuri, babu amfanin wannan tashin hankalin da kika dorama kanki, domin ba Shi zaisa ALLAH yayi abinda baiga Dama ba, bayan hakama wannan abin da kike yi tamkar kina Jin haushin Allah ne akan irin kaddarar da ya saukar Miki".

Hawaye kawai ta ke zubarwa , ba tare da tayi ko kwakkwaran motsi ba,hakan yasa ya cigaba da cewa "wannan kaddarar yarda da ita shine cikar Imani amma kin kasa yarda da hakan, wannan ciwon da mujaheeda take yi a duk lokacin da Allah ya so Yana iya yaye Mata kiga ma kamar ba tayi ba, idan Kuma ya so ya na iya karbar ranta shima duk cikin hukuncinsa ne, saboda haka tashin hankalin nan ya kamata ki dakatar da Shi ki koma ga Allah ki sama kanki dangana da juriya ki yawaita yin addua shine Allah zai dube ki ya Kuma kawo Miki sauki".

Yau dai ta tsaya ta saurari nasihar Alh Mustapha ta Kuma gamsu haka zalika ta ji yar natsuwa acikin zuciyarta.

Haka ya cigaba da yi Mata nasiha har suka isa gida, Amma ya kasa gaya Mata zasu je gidan su Taufiq gobe.

Har suka Kai gida bai Sami wannan karfin guiwar ba.

Har yayi Shirin kwanciya ya koma Kan gado ya zauna yayi jugum,tunanin makomar muhseena ya ke yi sosai, daker ya Sami karfin guiwar da ya tashi ya wuce dakin haj murjanatu, zaune ya taddata babu alamun bacci a tare da ita ta dago ta dube Shi tace "lafiya" ya Dan jinjina Kai yace "na manta na gaya Miki ne, gobe bayan munje mun duba mujaheeda zamu wuce gidan Alh Yusuf lamido, ".

Tayi masa kallon tsaf tace"me
Zamu yi agidan su".

Ya dan makale kafada sannan yace "Ban sani ba, Alh Yusuf din ne dai ya nemi alfarmar mu je Yana son ganin mu, sai dai idan munje zamu ji dalilin Kiran"

Ta tabe baki tace "Ni fa ba na son raini, da zasu je mu je gidansu , su ba su San hanyar gidan mu ba ba ne?".

Yace "mu dai je, meye a ciki ai ba wani abu".

Tace "A wajenka Kenan ba wani abu Amma ni a wajena wani abu ne don na fi karfin Alh Yusuf ya Kira ni gidansa".

Kai kawai Alh Mustapha ya Kada ya juya ya fita Yana cewa "hakuri kawai za kiyi mu je, sai Allah ya kaimu goben".

Yana fita ta saki tsaki, me yasa Alh yusuf yake Kiran su? Menene?. Tambayar da takema kanta kenan.

Kamar ko wane dare Haj murjanatu bata runtsa ba, saboda damuwa,kamar yadda Taufiq ya ke can duk tsawon wannan Daren Yana rike da waya Yana aikin magana da muhseena, wacce zuwa yanzu ta Saba da raba dare tana waya da Shi, Wanda har idan yayi nawar Kira ta Kan ji

ta Matsu ya Kira, sosai maganganunsa da muryarsa suke sanyata nutsuwa da kwanciyar hankali.
Shin hakan na nuna cewa itama ta fada fagen kaunarsa ne ko me?".

Washegari fargabar Alh Mustapha labaran ta Kara tsananta, har ya Fara yi ma Kansa tambayar Anya fargabar a gayama Haj murjanatu gaskiya kadai ya ke yi ko dai akwai wata a kasa ne? Domin tabbas fargabar tasa tayi yawa matuka irin yadda gabansa ke faduwa yayi yawa, shin menene zai faru bayan gayama Haj murjanatu gaskiya.
Har suka je asibiti cike yake da fargaba.

Basu Jima sosai a asibitin ba Alh Mustapha labaran ya wuce gidan Àlh yusuf lamido Kai tsaye tare da Haj murjanatu.
Fitar su ke da wuya Haj madina ta daga waya ta Kira "ki dawo sun tafi" ta amsa "Toh".

Cikin kankanin lokaci muhseena tayi sallama cikin dakin ta shigo, tana fadin "har sun tafi". Haj madina ta dan yi murmushi tace "eh, Ina tsammanin akwai inda zasu je ne,Shi yasa".
Muhseena ta wuce wajen mujaheeda tana cewa "gaskiya idan ba don haka ba, ai sai dai na koma gida tafiyarta ba yanzu ba".
Haj madina ta zubama muhseena Ido tace " Na rasa dalilin tsanar da Haj tayi Miki, domin Hali irin naki banga Wanda zai ki ki ba, ki duba ki gani duk irin kiyayyar da take nuna Miki, hakan bai hanaki zuwa ki Kula da mujaheeda ba, ba tare da Sanin ta ba, duk safe idan ta tafi zaki zo ki gyara mujaheeda ki shiryata Wanda tana zaton ni ce nake yi".

Muhseena ta yi murmushi tace " sanin ina zuwa ai bala'i zai ja min a wajenta karshema ta hana ni zuwa kwata kwata, ni Kuma har ga Allah ina son yarta Zan iya jinyarta iya tsawon lokacin da zata Sami lafiya".
Haj madina tace "na Sani zainab tabbas zaki iya don ko yanzu kina iya bakin kokarinki ba tare da Sanin kowa ba, tun ranar da kika zo kika karbi nambar wayata nake sanar da ke idan Haj bata asibitin, ba ki taba gajiyawa ba".
Muhseena ta dakko tawul da ruwan zafi ta shiga gogema mujaheeda jikinta kamar yadda ta Saba duk safe. Ta gyarata ta tsaftaceta sannan ta dau kayan ta je ta wanke ta Shanya ta dawo.
Ta dubi Haj madina tace
" Haj yau ina da karatu, Zan wuce makaranta, sai Kuma gobe da safe".
Haj madina tace "to Zainab angode Allah ya yi Miki albarka"
Daganan su kayi sallama ta tafi.
Kamar kullum haka Haj madina tayi ta yabon halayen muhseena tare da sa Mata albarka yarinya me natsuwa da hankali, Amma ta rasa dalilin da yasa Haj murjanatu bata Son ta , shin me tayi Mata? Me Kuma ta tsare Mata?.

Cikin matsananciyar faduwar gaba da fargaba , Alh Mustapha labaran ya isa gidan Alh Yusuf lamido.

Ya Sami harabar gidan ya aje motarsa, gaba daya suka fito tare da Haj murjanatu wacce ko

kadan ba wani sakin fuska ko walwala atare da ita.
Musamman da suka shiga gidan, Kai tsaye falon Alh Yusuf lamido suka wuce.
Wanda dama tun kafin isowarsu Alh Mustapha ya sanar da Alh yusuf gasu nan zuwa. Hakan yasa a shirye yake Yana zaune Kan kujera me zaman mutum biyu, Mallam Umar Yana daya kujerar me zaman mutum daya.
Zaune a kasa Taufiq ne
Hakanne ya Kara sa Haj murjanatu tamke fuska domin bata ga dalilin da zaace har yanzu Taufiq na zaune a gida bai kama hanyar asibiti ba, wani irin mugun kallo take sakar masa Wanda Kula da hakan da yayi ne yasa bai Kara kallon gefen da take ba. Domin dai babu wani sauran tsoro ko shakkar tasan abinda ke faruwa a zuciyarsa, duk wani hukuncin da take ganin zata iya dauka dai dai yake da Shi.

Kujeran me zaman mutum uku suka zauna duka lokaci daya.

A yayin da Alh Mustapha ya Kara tashi duk ya bi su ya basu hannu suka gaisa, gami da tambayar me jiki.
Ita Kam Haj murjanatu babu Wanda ta gaisar sai su ne suka gaisheta ba tare da nuna wata damuwa ba Akan ràshin gaishe sun da bata Fara yi ba.

Shima Taufiq ya gaisheta amma bata amsa ba, ranta Kuma a kufule take yau dai tabbas kafin ta bar gidan nan sai tayima Taufiq wankin babban bargo a gaban iyayensa.

Alh Yusuf lamido ya dan gyara zamansa ya dubi Mallam Umar da tun shigowar su Haj murjanatu yake jinjina irin bakin halin da ya fahimci tana da Shi, shin irin isa da izzar da yaga Haj murjanatu nayi ko don tana da abin duniya ne? Nan ya Kara jinjina ma halin karamci irin na Alh Yusuf lamido, da ba su dauki duniya da zafi ba.
Ya nuna Shi da hannunsa yace "Haj , wannan sunan sa Mallam Umar, shine Kuma mahaifin Zainab daga kauyen Durmi".

Gaban Haj murjanatu ya yi mummunan faduwa, mahaifin Zainab daga Durmi?,

Ta Kara maimaitawa a zuciyarta
Sannan ta juyo ta na kallon Mallam Umar Ido a Bude.

Durmi, gabanta ya Kara faduwa sunan kauyen bazai taba barin zuciyarta ba, domin kauyen Yana daya daga cikin bakin tarihin rayuwarta.
Ta Kara kallonsa tace "meya hada Zainab da Durmi, ita da tace yar Dan zaki ce, Kuma ta yaya mahaifinta yake Raye bayan ta ce ita marainiya ce?".

Alh yusuf lamido ya ce "shine dalilin da yasa na bukaci ki zo, saboda a bayyana duk abinda ke boye, domin wannan maganar da Zainab ta gaya muku ba gaskiya ba ce, ta fada ne saboda ta taimaka ma mijinta rufe sirrin da suke Jin tsoron bayyanawa ".

Alh Mustapha labaran ya yi kasa da Kansa Yana adduar Allah ya kawo sassauci a lamarin.

Gabanta Yana dakan uku uku ta dubi Àlh yusuf tace "bangane ba, tana da aure ne Zainab din, Kuma waye Mijin nata?".

Ta Karasa magana bakinta na rawa.
Sannu a hankali Alh Yusuf lamido ya Gama bayyanama Haj murjanatu asalin gaskiyar al'amarin da matsayin muhseena a wajen Taufiq.
Ya cigaba da cewa "Daga auren har boyewar da sukayi anyi Shi ne bisa kuskure, aure dai ya dauru domin ko da wasa aka daura aure a addinance ya dauru balle auren da aka daura Shi da sadaki da waliyyai da komai, don haka Zainab matar Tau.....?

Cikin mummunar fusata hade da tashin hankali, Haj murjanatu ta Mike tsaye idanunta sun rine sun koma jajir kamar Jan Gauta, nan da nan fuskar ta ta canja ta yi baki ta fita hayyacinta.

Alh Mustapha labaran ya yi saurin Kallonta yace "ki yi hakuri ki mallaki Tunaninki Kada kiyi wani abu da zai janyo danasani". Ta watsa masa harara tace cikin tsawa "na Dade banyi danasani ba , mayaudara ma ciya amana".
Ta juya tana kallon Taufiq cike da tsana ta nuna Shi da hannunta tace "kalleni da kyau Kada Ku Raina min wayau Ku maida ni shashasha , wato saboda mujaheeda tana jinya shine zaka Kara aure " ta juya ta dubi Àlh yusuf lamido tace "Kai Kuma Baka ji kunyar tsayawa Ka goyi bayan danka ba Ka Kuma yi Karya ba wani ya aureta tuntuni nayi Imani kwanciyar mujaheeda a asibiti ne kuka hadu kuka aura masa wannan makirar yarinyar, wacce Dama nasan masifa zata zame mana arayuwa muguwa".

Mallam Umar zaiyi magana kenan Alh Yusuf lamido ya daga masa hannu alamun yayi shuru Kada ya tanka.

Ta nuna Taufiq da hannu tace "Baka Isa kayima Yata kishiya ba, ko Ka manta takardar da kasa hannu Akan ba zaka taba yi Mata kishiya ba,butulu mugu annamimi Wanda Bai da mutunci tir da Hali irin naka".
Ananne Alh Yusuf lamido ya dubi Taufiq yace "Taufiq wace takarda ce kasa hannu ". Ta saki tsaki tace ,"ni zaka tambaya ,".
Bai bi ta kanta ba. ,ya Kara yi masa tambayar.
A sanyaye Taufiq ya gayama Alh Yusuf lamido komai.
Alh Yusuf yace "Kai Kuma saboda alokacin Kana cikin Mayen soyayya shine kasa Mata hannu a takardar".

Haj murjanatu ta ce "magana ta kare dole ya saki Zainab yanzun nan , matukar kuna son Zaman Lafiya da kwanciyar hankali".
Alh Mustapha ya girgiza Kai yace "Haj ki bar wannan maganar domin babu yadda zaayi Taufiq ya saki Zainab saboda babu wani dalili ".
Ta juyo a harzuke tace da karfi "eh, dole Ka Fadi hakama tunda ba Kai Ka haifi mujaheeda ai

dole yau Ka nuna bakin halin Ka a kanta, Ka Kuma zabi bare akanta, na rantse duk na ishe Ku".
Alh Yusuf lamido ya ce "Haj ki kwantar da hankalinki ki natsu kisan abin nan da Taufiq ya aikata babu inda addini ya haramta masa don haka tunda Allah Bai haramta masa ba babu Wanda ya isa ya haramta masa, kiyi hakuri kawai ayima yarinyar nan adalci itama ta rayu tare da mijinta".
Haj murjanatu ta zazzaro idanu waje cike da bala'i tace "na rantse kotu Zan Kai Ku, ai takardar yarjejeniyar da mukayi tana nan Zan Kai kotu sai munyi sharaa da Ku".

Alh Yusuf lamido ya jinjina Kai yace "babu wata kotu da ta isa tasa Taufiq ya saki Zainab don kawai yasa hannu a takarda Akan bazai yi Mata kishiya ba, saboda ita kotun ba jahila bace ba ta Kuma isa ta goge umarnin ubangiji ba, don haka da wannan takardar da takardar tsire duk uwar su daya uban su daya, idan zaki dawo hayyacinki ki amshi wannan kaddarar gara ki dawo don ni banga amfanin wannan hayagagar ba".
Shi dai Alh Mustapha tunda Haj murjanatu ta ambaci ba shi ya haifi mujaheeda ba ya ji komai ya tsaya masa, tashin hankalin ràshin haihuwar sa ya dawo masa sabo, komai ya tsaya masa ya Kuma zafafe Shi gefen kirjinsa sai zafi yake masa,
Da karfi cikin fusata tace "to shikenan dole a cikin biyu Taufiq ya zabi daya ko ya saki Zainab ya zauna da mujaheeda ko ya zauna da Zainab ya saki mujaheeda don bazan taba daukar wannan bakin kaskancin ba wacece Zainab da zatayi kishi da mujaheeda bata isa ba , ba Saar yata ba ce ".

Dai dai lokacin muhseena ta shigo gidan ,dawowarta kenan daga makaranta.
Ta ji maganar da Haj murjanatu ke yi , gabanta ya yi mummunan faduwa, musamman da ta cigaba da Jin yadda Haj murjanatu ta dage da masifa da bala'i iya karfinta Wanda ba cikin gidan ba har Makota sai sun jiyo irin tartsatsin da take yi.

Da sauri muhseena ta nufi falon Alh Yusuf lamido, dai dai lokacin Suma Haj saratu da Hajara suka fito a gigice, saboda Jin irin ihun da Haj murjanatu take yi, duk a gigice suka runtuma falon Alh Yusuf lamido.

Gaba daya suka fada,cikin falon, Haj saratu na fadin "Haba Haj murjanatu menene haka, ya kike kokarin maida kanki wata mahaukaciya ne, menene abin tashin a wañnan maganar sai kace Wanda aka aikata haramun haba sai kace ba musulma ba".

Haj murjanatu ta juyo da karfinta,zata zazzagama Haj saratu nata balain.

Amma matar data gani a gefen Haj murjanatu yasa tayi dif. Ta hadiye abinda tayi nufin fada.

Shin wa take gani kamar Hajara, wannan fuskar ba zata taba boye Mata ba, ko da ace ta canja balle Hajara bata canja da komai ba sai manyanta da fuskarta ta nuna, har yanzu ta na nan siririya ba tayi Wata kiba ba, Haj murjanatu tasa hannu tana murza idanunta don ta Kara tabbatar da abinda take gani.

Yayin da Hajara ta Dora idonta Akan Haj murjanatu. A hankali ta tako zuwa cikin falon suna

cigaba da kallon kallo, lokaci daya duk jamaar falon suka maida kallonsu ga abinda yasa Haj murjanatu yin shuru ga barin balain da take yi.

Gabanta Hajara ta tsaya suna kallon kallo.

Zumbur Alh Mustapha labaran ya Mike Yana kallon Hajara ya tako har zuwa inda take tsaye Yana zaro Ido domin ya tabbatar Hajara ce ko ba ita ba ce.

Cikin rawar murya Hajara ta nuna Haj murjanatu tace "Haj". Itama Haj murjanatu hannunta na rawa ta nuna Hajara tace "Hajara, ke ce?".

Cikin matukar gigita gami da dimauta, Hajara ta dubi Àlh Mustapha labaran Wanda gaba daya ya dauke wuta Ido kawai ya Dora Mata ko motsi ya kasa yi. Alh yusuf lamido shima ya Mike Yana cewa " aah Dama kunsan juna ne, Amma Kuma wannan firgici da kuka fada ciki meye dalili".

Mallam Umar ya tashi ya nufi wajen Hajara da gaba daya ta Gama birkicewa kuka me karfi ya kwace Mata, ya dubeta a dimauce yace "Hajara kwantar da hankalinki menene? Su waye su a gareki".

Gaba daya guri ya gaure da kukan Hajara,su Kuma SU Haj murjanatu da Àlh Mustapha suna tsaye kamar wadannan aka dasa.

Muhseena ta rungumo mahaifiyarta itama tana hawayen da ganin mahaifiyarta na kuka ya kawo su fuskarta tace "Inna menene ? Meye ke faruwa?". Haj murjanatu ta Kara rikicewa ta dawo da birkitattun idanunta Kan muhseena cikin nauyin harshe tace "zainab yar ki ce Hajara". Hajara kuka kawai take me karfin gaske Mallam Umar ya cigaba da tambayarta menene.

Hannunta na rawa ta nuna Alh Mustapha labaran tace "Mallam ga mahaifin muhseena ".

Tashin hankali Wanda baasa masa rana. Yawun bakin haj murjanatu ya kafe ayayinda Alh Mustapha ya yi taga taga zai Fadi Alh Yusuf lamido ya tallafo Shi ya rike. Cike da mamaki da tashin hankali yace "Alh wace magana ce wannan me kama da tatsuniya Kaine mahaifin Zainab ta ya ya? ta ina?".

Muhseena gaba daya ta Kara dimaucewa ta saki mahaifiyarta ta tako a hankali har gaban Alh Mustapha labaran tana yi masa wani irin kallo me cike da tsana da kyamata, shima cikin fitar da hawaye ya zuba Mata Ido ya kasa magana saboda wani abu da ya tokare kirjinsa. Muhseena tace "Dama Kaine mahaifina, duk tsawon wannan lokacin ina tare da Wanda ya rusa rayuwata da ta mahaifiyata, ina tare da Wanda Bana kaunar ganinsa saboda bakinka da nake gani, duk duniya banga abinda na tsana sama da Kai ba".

Nan fa kallo ya koma Sama maganar muhseena ta sakar da guiwar kowa a cikin falon. Musamman Taufiq da Alh yusuf lamido Wanda tuni ya zare jikinsa daga jikin Àlh Mustapha ya na yi masa wani irin mummunan kallo.

Yayin da Haj murjanatu ta ce cikin galabaitacciyar murya wacce take cikin mugun Hali me wuyar fassara.

"Ta yaya zaki Kira Zainab da yar Alh ".

Hajara tayi Mata wani bushasshen kallo tace"Dalilin mummunan abinda Alh yayi àgare ni na Sami cikin muhseena, kin ji ta yadda ta Zama yarsa". Taufiq ya dafe kirji gami da zaro Ido ya so fitar da kalaman bakinsa Amma dimauta tasa sun kasa fita illa ya nuna muhseena da hannu ya

nuna Alh Mustapha da hannu ya kasa cewa uffan.

Haj murjanatu tayi luuuu ta Fadi kasa , tana dukan kasa gaba daya hauka ta bayyana a tare da ita, tana fadin "na shiga uku na lalace ni murjanatu karshena ya zo , da Naga wannan Rana gara na mutu na bar duniya wayyo Allah kaicona kaicon abinda na aikata, da ace na biki na Baki hakki da yancin ki kila Allah da Bai yi min wannan mugun kamun ba, na shiga na Gama wulakanta a duniya, yau bayan shekaru Sama da ashirin abinda na aikata ya dawo gare ni zai kashe ni".

Mallam Umar a fusace yace "Allah ya nuna Miki ishara ne don kisan Allah baya zaluunci Kuma ya Sanya zaluunci abin haramtawa a tsakanin mu, kun zakinci Hajara amatsayinki na ya mace na yi zaton zaki ji irin zafin da macen da ta tsinci kanta a irin wannan halin take ji, Wanda hakan zaisa ki ji tausayin Hajara ki Kuma tsaya Mata domin Samun yanci da hakkinta, aah maimakon kiyi hakan sai kika goyi bayan mijinki kika Kuma kare Shi da ga fuskantar hukunci kika tauye yanci da hakkinta kika lullube asirin mijinki kika tone na Hajara, ta yaya kuke zaton zaku Sami kwanciyar hankali a duniya".

Alh Mustapha labaran ya fada Kan kujera Yana kokawa da numfashin sa da ya ke kokarin saukewa, muhseena ko a jikinta ta juya ta koma wajen mahaifiyar ta ta rungumeta suna kuka.

A yayinda dole su Alh Yusuf lamido suka yi Kan Alh Mustapha suna taimakonsa , Taufiq ya dakko ruwa suna shafa masa a fuska.

Falo dai gaba daya kowa ya fada tashin hankali, don Haj saratu can ta koma ta zuba tagumi hannu biyu, tunda ta fahimci inda zancen ya dosa ta ji komai ya kwance Mata.

Ita Kam Haj murjanatu Abu goma da ashirin ya hade Mata , duk ràshin imaninka idan kaga yadda ta koma hakika sai Ka tausaya Mata .

Tsawon minti arba'in aka kwashe a falon cikin tashin hankali, kafin daker Alh Yusuf lamido ya shawo Kan al'amari aka Samu kowa ya dawo hayyacinsa.

Sannan Àlh yusuf lamido ya dubi Hajara yace "Hajara,ki Kara Samun nutsuwa kiyi hakuri, mu da ba mu San komai ba kiyi mana bayanin komai saboda mu fahimci yadda al'amarin ya ke , kafin mu ce komai".

Hajara ta girgiza Kai tace "bazan iya faden komai ba da bakina(ta juya ta kalli Mallam Umar) Mallam Ka yi masa bayani ". Muhseena ta goge hawayenta gami da kudundune kanta acikin hijabin jikinta.

Mallam Umar ya muskuta , sannu a hankali ya warware masu komai, sannan ya Kara da cewa "saboda tsabar zaluunci duk tsawon wannan shekarun , Basu taba waiwayar Hajara ba duk da sun San inda zasu ganta, sannan ita Hajaran da suka San tasan inda zata gansu ko ba su je ba ita zata zo wajen su shine suka tattara suka bar kasar gaba daya, sun manta Allah shine me sakayya Kuma baya yafe laifin da ke tsakanin bawa da bawa, yau gashi duk kun gama guje gujen Allah ya hada Ku ba tare da Shan wahala ba".

Tsananin kunya tasa Alh Mustapha labaran kasa dago Kansa sai hawaye ke zuba kamar an Bude famfo.

Haka Haj murjanatu duk jarabar nan ta yi lakwas sai Ido take zarewa tana kallon muhseena tana kakabin kasancewarta yar Alh Mustapha.

Duk falon nan babu Wanda baiyi tir da abinda Alh Mustapha labaran ya aikata ba, duk wani

mutunci da kimar da suke ganinsa da Shi duk ya zube, kallon mugu azzalumi suke masa .
Alh Mustapha labaran ya dago cikin zubar hawaye yace "Don Allah don son Annabi Hajara ki yafe min nasan nayi kuskure ba tun yau ba , tun faruwar al'amarin na rantse Miki ban Kara Samun kwanciyar hankali ba, kullum ina cikin zullumi da tunani babu abinda ke min dadi a duniya, ki yafe min Hajara ki yafe min , na Dade da yin nadama ".
..Mallam Umar ya watsa masa harara yace "idan har Kayi nadama meya hanaka nemanta Ka nemi yafiyarta, mu kasan sau nawa muna zuwa nemanka ?".
Ya waiwayo ya dubi Haj murjanatu cike da tsana yace "kaga wacce ta Hana komai nan, masifa da bala'inta yasa ba Zan iya tunkararta da tambayar garin da Hajara ta ke, domin ita kadai tasan kauyen da Hajara take, domin tun faruwar lamarin ban Kara Samun kwanciyar hankali a cikin zaman aurena da murjanatu ba, saboda ita kanta ta kasa yafe min".
Malllam Umar ya ce cike da fusata "me yasa kuka bar Nigeria bayan faruwar al'amarin, ko kun tafi ne saboda Ku Kara tabbatar ma duniya da mugun halinku da zalincinku".

Nan ma Haj murjanatu ya duba wacce take cikin masifa me girma ko Kai bata iya dagawa duk wani abu ajikinta bata iya sarrafa Shi.
Ya jinjina Kai yace

" Bayan faruwar masifar da babu na biyun ta a rayuwata, a ranar ban dawo gidan ba saboda tashin hankali da damuwa, domin tun a lokacin da me faruwa ta afku na yi nadama na rasa inda zansa Kai na kamar yadda na rasa dalilin da yasa na aikata abinda na aikata.
Abu dai daya na Sani shaidan yayi amfani da son da nake ma Hajara ya ingiza ni na aikata aikin danasani.
Nayi ta fargabar Kara komawa gida saboda bansan masifar da Zan tarar ba a wajen murjanatu hakan yasa sai da nayi kwana bakwai a hotel ban dawo gida ba, ina ta istigfari ina neman gafarar ubangiji,sosai na tsani Kaina nayi kuka bansan iya yawansa ba, na zama tamkar mara lafiya, ko abinci Bana iya ci na rame na fita hayyacina gaba daya harkokina sun tsaya cak.
Daga bisani na yanke shawarar komawa gida domin ina da tabbacin kila zuwa yanzu murjanatu ta Fara hucewa ko hukunci zatayi nasan ba zatayi hukunci cikin fushi ba.
Nayi saa kuwa duk da mummunar tarbar da tayi min ta saurare ni na bàta hakuri sai dai tayi rantsuwar ba zata taba yafe min ba, Kuma ba zata kashe aurenta ba Amma ba zan taba Samun jindadin aure daga gareta ba, tayi alkawarin Sai dai mu zauna zaman doya da manja.
Haka rayuwar mu ta cigaba har zuwa yau babu wani jindadin aure bata mutunta ni bata daraja ni bata Jin maganata. Saboda nayi watsi da darajata ita Kuma ta hau Kai ta take.
Ita ce Kuma tayi tunanin tabbas idan Hajara ta fadama mahaifanta abinda ya faru zasu zo su neme mu karshe kowa sai ya ji abinda na aikata Wanda zubewar kima da darajar mu ce duka, ba Kuma zata juri wannan tozarcin ba, hakanne yasa tayi mana biza da ni da ita da mujaheeda Muka tattara Muka tafi London .
Mun zauna tsawon lokaci acan Wanda saida ta tabbatar Kura ta lafa sannan Muka dawo Nigeria.
Kasancewar tunda zamu bar Nigeria ta saida gidan da Muke ciki, yasa bayan dawowar mu Muka koma wani gidan Wanda babu yadda zaayi ko wata rana Hajara ta gane inda Muke. Domin bata San wannan gidan ba sai wancan.

Sai dai Kuma duk wañnan abin babu natsuwa ko kwanciyar hankali a gare ni, Bana iya bacci kullum ina tunanin Hajara da zalincin da nayi Mata.
Sai dai Banda wani damar da Zan tambayi murjanatu garin da Hajara take domin gudun fitina da tashin hankali.
Ga uwa uba Allah ya jarabce ni da ràshin haihuwa, domin har yanzu ban taba haihuwa ba ba ni da da Wanda shima ina tunanin Yana daya daga cikin sayayyar da Allah ya yima Hajara".
Ya juya kunya ta Kara kama Shi da ya ga yadda duk jama'ar falon suka zuba masa Ido.
Ya dauke Kansa ya dubi muhseena da ta kafe Shi da Ido sai dai baya jindadin irin kallon da take yi masa.
Ya ce"Tun ranar da na Fara ganin Zainab na ji wani irin kaunar da ban taba Jin irinta ba agame da ita, ya zamana ko bacci nake sai nayi mafarkinta, gashi ko kadan Bana son na ganta cikin damuwa sosai nake jinta a raina, kullum nakan tambayi Kaina me yasa nake kaunarta?.
Sai yau na Sami amsata dalilin da yasa nake kaunarta saboda ita din jinina ce ya ta ce, Allah na gode maka da Ka azurtani da Samun ya kamarta"
Muhseena ta goge hawayenta ta dube Shi sosai tace tana nuna Mallam Umar, "Ba ni da wani mahaifi da ya wuce Shi (ta nuna Mallam Umar), saboda shine cikakken UBA shine Wanda ba ni da na biyunsa duk duniya kowa ya sanni ne a matsayin yarsa,don haka ba na kallonka a matsayin mahaifina asalima ina Jin kunya ina kyamatar a danganta ni da Kai ".
Kalamanta sun taba zuciyar sa Kuka me karfi ne ya Kara kwace ma Alh Mustapha,a yanayin da Mallam Umar ya ke gyada Kai saboda tsananin Jindadin kalaman muhseena.
Alh Mustapha yace "don Allah Zainab ki yafe min ki yafe min ko na Sami saukin wannan masifar na rantse ko da wannan kunyar da na ji yau aka bar ni duk Allah ya Gama yi muku sakayya , Wanda bayan haka har ciwon hawan jini na Samu saboda tashin hankalin da nake ciki kullum".
Ya Kara kallon Hajara yace "Hajara ki yafe min ki min afuwa ki yafe min".

Ita dai Haj murjanatu gaba daya batasan a duniyar da take ba, gaba daya ta fita hayyacinta.
Alh Yusuf lamido ya numfasa ya Kara numfasawa sannan ya dago da Kansa yace " Duk inda irin wannan ta kasance Yana Zama abin tir, amma babban abu shine yadda Alh Mustapha labaran yayi nadama ya ke Kuma neman yafiya ga wadannan ya zalunta , hakika fadan baa kyautama Hajara ba ma duk Bai ta so ba domin iya ràshin kyautawa anyi Mata sai dai babu wani abin da zamu yi illa ahadu Duka ayi hakuri akuma yima juna afuwa domin Allah Yana son bayinsa masu yafiya, duk ayi hakuri a taushi zuciya".
Malllam Umar yace "hakane , babu komai tunda yau dai Alh Mustapha ya karbi muhseena a matsayin yarsa ya Kuma yi nadamar komai to Allah ya yafe mana gaba daya".
Taufiq dai Kansa na kasa yau ya sha mamaki har ya gaji, wai Dama Alh Mustapha shine mahaifin muhseena ba Mallam Umar ba, lalle Mallam Umar ya cika mutumin kirki, a yau ya Kara ganin girma da mutuncina fiye da kullum.

Alh Mustapha ya dubi Alh Yusuf yace "don Allah Alh kasa Baki na Sami Hajara ta yafe min".
Alh Yusuf ya dubi Hajara wacce tuni fuskarta ta kumbura saboda kuka .
Yace "Hajara ki sani Allah Yana tare da masu hakuri, Yana kuma son masu yafiya adalilin yafe

masa da zakiyi Alka Yana iya Jin kanki kema ya yafe Miki duk kurakuranki ,ansan an zakunce ki kwarai da gaske Amma idan kinyi hakuri kin yafe masa tabbas kinyi babban jihadi, don haka kiyi hakuri ki yafe masa"
Asanyaye cikin taushin murya me cike da sakonni Kala Kala aciki, tace "babu komai na yafe masa domin ràshin yafe masan ba Shi zai goge duk masifar da na fada ciki ba a dalilin faruwar hakan saboda haka na yafe masa".

Sai a lokacin haj saratu tayi magana tace "lalle Hajara kin cika mutum domin yafe irin wannan laifin ba abu ba ne me sauki, Amma ladanki na gun ubangiji, sosai kimarki ta Karu a wajena na Sara Miki".

Alh Mustapha ya zuba Mata Ido yace " nagode Hajara Allah ya saka da alheri nagode"
Alh yusuf yace"Alhamdulillah Allah ya saka Miki da alheri," ya dubi Taufiq da sauran jamaar falon yace"to kunga dai yadda al'amari ya kasance da mujaheeda da muhseena duk abu daya ne saboda haka komai ya zo karshe".

A fusace Haj murjanatu ta Mike idanu jajir tace "ba Abu daya ba ne hanyar jirgi da ban ta mota da ban babu abinda ya hada mujaheeda da muhseena sai gaba da masifa da bala',I na rantse bazan sassauta ba zanyi yaki da kowa Akan wannan lamarin domin yanzu nagane dalilin tsanar da nayi ma muhseena Bana Sonta Bana kaunarta Kuma Saina tarwatsa rayuwarta".Gaba daya Baki suka saki suna kakabin mugun halin Haj murjanatu suna mamakin yadda duk wañnan abin baisa ta saduda ba.

Alh Mustapha ya Mike shima ya nunata da hannu Yana tsuma yace "ni Kuma na rantse Miki bazan Bari ba duk abinda ya Sami muhseena sai na daureki har igiya tayi rara bazan Raga Miki akanta ba domin Zan iya rabuwa da ke Zan Kuma iya sa kafar wando daya da ke akanta".
Ta buga hannunta a cinya tace "mu zuba shege Ka fasa saboda yar shegen zaka ce zaka iya rabuwa da ni.....

Ya katsa Mata tsawa yace "idan kika Kara Kiran muhseena da yar shege na rantse Miki sai nayi Miki dukan kawo wuka anan ".

Ganin yadda yake tsuma ya tabbatar ma da Haj murjanatu tabbas Yana iya sa Mata hannu a gaban makiyanta,hakan yasa ta fisgo Jakarta ta juya ta zubama Hajara da muhseena harara tace "zakuyi namakina zaku San kun shigo gona ta domin sai na maida rayuwar Ku abar kwatance".
Tana gama fadan hakan ta juya fuu cikin fusata da masifa ta fice batasan inda take wurga kafarta ba harta isa bakin titi ta ta tare me a daidaita sahu ta bashi umarnin ya kaita asibiti Kallo daya zakayi mata Ka dauka daga turu ta fito .

Tunda take a duniya bata taba wukakantuwa irin na yau ba , yau duk isa da izzar ta sun kare agaban makiyanta. Ji take kamar ta mutu ta huta da bakinciki.

Fitarta Alh Mustapha labaran ya cigaba da neman gafara duk yayi wujuga wujuga.
Muhseena ce ta Fara mikewa tayi masa kallon tsaf ta fice daga fakon tana fita Hajara ta bi bayanta , itama Haj saratu ta tashi ta fita.
A hankali shima Taufiq ya zare jikinsa ya fice.
Alh Mustapha ya kara fadawa cikin dimbin tashin hankali da damuwa. Ganin halin da ya Kara shiga ne yasa Alh yusuf lamido ya cigaba da kwantar masa da hankali domin iya nadama ya Gama ganinta a cikin fuskarsa.

Shi dai Mallam Umar babu abinda yake cewa sai kallonsa kawai da yake yi, domin gaba daya ji yake kamar ya tashi ya shake masa wuya saboda tsana.mugun mutum kawai Wanda ya jefa abar kaunarsa cikin mawuyacin hali.

Daker Alh Yusuf lamido ya shawo Kansa ya iya tashi ya tafi Amma sai da ya rike Shi yayi masa rakiya har wajen motarsa saboda yadda jikinsa ya mutu daker yake iya tafiya, ga wani matsanancin ciwon Kai da ya addabe Shi gami da faduwar gaba.

Ya dai shiga mota ya ya tafi cikin rikitaccen hali mara dadi . Kai ya Allah ya Raba mu da mummunar kaddara.

TO BE CONTINUE

DAGA TASKAR YAR GIDAN IMAM

NI MA MATARSA CE

63

Jin Haj murjanatu bata yi magana ba yasa ta cigaba da magana "Ni banga amfanin wannan boyewar da kika yi ba, na dauka tunda Allah ya biya Miki bukatarki mujaheeda ta Sami lafiya zaki dawo cikin mutunci, a gaskiya ya kamata ki dauki darasin rayuwa yadda na dauka domin ni gaba daya yanzu na dawo daga rakiyar duniya na fahimci aikin banza ce abinda Kuma arziki Bai Baka ba na rantse ràshin arziki bazai ba Ka ba, Naga haka acikin aurena yadda na dauka da sai da malamai zaka mallaki mijinka Ashe biyayya da girmamawa suke sa Ka mallaki miji idan kinga yadda mijina yake lallabani ke kyace karamar yarinya ce, to gara kema ki dawo ki Yagi rabonki abinda kika kasa yima aurenki yanzu kiyi ki aje izzarki ki yarda da abinda Allah ya kaddara kawai sai ki zauna lafiya".

Ta Dan aje numfashi sannan ta cigaba da cewa.

"Sannan kin taba tambayar mujaheeda shin bata son dawowa ga mijinta? Sannan ta manta da rayuwar yarta ne? Ko Kuma ta daina son mijinta ne?. Ki gwada tambayar ta hakan domin Bana son ki shiga hakkinta, ina baki shawarar nan ne a matsayinki na aminiyata wacce Bana son ganin nakasu a rayuwarta,".

Tana Gama fadin hakan ta kashe wayar.

Ayayin da itama Haj murjanatu tayi kasa da wayar cikin sanyin .jiki.

Ta yunkura ta tashi sosai ta zauna tana aje numfashi a hankali, maganganun Haj Nana sun shigeta sun Kuma tsaya Mata a zuciya, hakika ita kanta bata da wani kwanciyar hankali a garin

da ba na ta ba, bata mu'amala da kowa bata da kowa daga ita sai yarta.
Tun bayan Samun lafiyar mujaheeda Haj murjanatu itace ta bada karfin guiwar su yi zaman su a Germany ko sa Sami saukin bakinciki da damuwar su, sai dai Kuma tsawon wannan shekarun ba su Sami kwanciyar hankalin da suke tunanin samu ba,sai azabar kashe kudi da suke yi domin tuni tattalin arzikin su yayi kasa kudadensu na cikin account dinsu duk sun kare sai dai daga kamfanininta ake turo Mata da kudaden bukatunsu, Anya kuwa lokaci Bai yi ba da zasu koma mahaifarsu.

Hatta wacce take yi domin ta mujaheedan tun daga ranar da ta Sami kanta, ta fahimci ta canja matukar canjawa, ta sa ma kanta tawakkali sosai na duk abinda ya faru, domin ta tabbatar yadda ta leka lahira ta dawo duniya to komai na Allah ne idan Kuma tace zatayi jayayya da hukuncin ubangiji to hakika zata ga fitinar da tafi wacce ta shiga, hakanne yasa ko da ta dawo hayyacinta bata zafafama kanta ba illa godiya da tayi ma Allah da ya sa ta Sami lafiya, duk jinyar da ta cigaba da yi bayan fitarta daga coma kokarin cirema kanta duk damuwa da wani kishin banza tayi.
Haka zalika kullum tana yawan Jin maganganun a cikin kwakwalwarta muryar muhseena Kuma take ji, kafin a sallameta daga asibitin ne wata Rana tayi ma likita tambayar me yasa take Jin maganganu acikin kwakwalwarta, likita yayi Mata bayani sosai Akan zai yuwu muryoyin da take ji irin muryoyin wadanda suke tare da itane alokacin da take cikin coma.

Haj murjanatu ta tuna ranar da mujaheeda ta zuba Mata Ido tace "mummy Zainab ta taba zuwa ta duba ni a asibiti?". Ta girgiza Kai tace "Bata taba zuwa ta duba ki ba, madina ce a tare da ke kullum sai Kuma ni".
Ko da zata cigaba da maganganu hanata tayi ta hanyar nuna Mata abar maganar.

Haj murjanatu ta numfasa bayan ta dawo daga dogon tunaninta. Bata taba Jin kwadayin komawa gida Nigeria ba irin na wannan lokacin.

A dai dai wannan lokacin itama mujaheeda tana cikin wani kayataccen lambu dake cikin hotel din da suke Zama.
Kamar kullum nanne take Zama domin debe kewa, tana zaune tana kallon jama'ar da ke kaiwa da komawa Amma a badini tunani ne fal a ranta kamar ko yaushe.

Tunanin fadwa ya fi komai ci Mata rai, shin awane Hali yarta take ciki? Shin meye matsayin ta a wajen Taufiq?. Shin ta yaya zata barma muhseena yarta da mijinta,?wace riba ta samu wannan bakaramin wauta tayi ba. Babu abinda zaa fasa ko da mutuwa tayi balle tana Raye.
Shin shikenan tabar yarta da mijinta saboda kishi na banza da wofi Wanda babu wani riba da ta ci aciki.
Wata zuciyar tace ",ya Zama dole ki koma kiyi yaki ki kwaci mijinki da yarki, wannan zaman ba Shi ba ne mafita".

Ta runtse idanunta hawaye ya shiga fita mata.shin kanta aka Fara kishiya? Ko kanta zaa daina? Don me zata kashe rayuwarta saboda kishi.

A wañnan yammacin dai mujaheeda ta yi tunani da naxarin da ta Dade batayi irinsa ba Kuma dukkan tunanin ya dora Akan yarda da komawa Nigeria domin yarta da Kuma mijinta.

****

Rayuwa dai tayi ma Àlh Mustapha labaran dadi baida sauran wata damuwa data wuce na dawowar Haj murjanatu da mujaheeda.

Kyakkyawar alakace tsakaninsa da muhseena, har Durmi suna zuwa tare a duk lokacin da wani abu ya faru. Zuwa wannan lokacin duk jama'ar Durmi sun shaida Alh Mustapha labaran mahaifin muhseena ne masu Mata mugun Baki da bakin fenti duk bakunansu sunyi shuru.

Musamman Mallam kallah Wanda Alh Mustapha labaran na shigowa garin zai bar duk abinda yake yi ya taho gidan mallam Umar domin ya kwashi gaisuwa don yasan ranar sai ya cika aljihunsa da kudi.

Tabangaren Mallam Umar kuwa duk yadda ya so kin yin mu'amala da Alh Mustapha to abin ya ci tura domin Alh Mustapha labaran a matsayin dan'uwa Kuma amini ya dauke Shi,babu abinda baya masa na alheri domin hatta gidan Shi ya gyara masa ya saya masa sabuwar mota ga abinci baya yankewa Shi yayi Taufiq yayi Ande Dije duniya sabuwa arzikin da take tunanin sai a mafarki zata Samu yau gashi a zahiri tana dangwalar arzikin Hajara da muhseena data ke daukar su a banza, gaba daya bakinta ya mutu Hajara ta Sami yancinta a gidan sai abinda taga damar yi take yi, ita kanta bata taba tsammanin Allah zai kawo irin wannan ranar da zata mallaki yancinta ba Kuma a goge bakin fentin da akayi Mata.

Acikin hakane muhseena ta kammala jarabawarta ta karshe burinta ya cika.NNPC kaduna aka turata yin service dinta. Taufiq ya so a barta a jigawa Amma Alh Mustapha labaran ya nuna babu damuwa domin abokinsa Alh Sani a nnpc din yake aiki don haka zai Kula da ita yadda ya kamata ba zaa samu wata matsala ba.

Amma duk da haka duk bayan sati biyu sai ta dawo jigawa, ko don fadwa da bata son ta zauna tare da kowa sai ita, hannun Haj saratu take barinta tunda ta Fara zuwa makaranta, Amma duk da haka hankalinsu na Kan juna.

****

Sassanyar ranar wata talata ce misalin karfe uku da minti goma, jirgin su Mujaheeda ya sauka.

Wani irin sanyi mujaheeda ta ji a ranta alokacin da kafarta ta taka kasar Nigeria, ta lumshe idanunta ta Bude tana yima Allah godiya .

Shatar mota suka dauka zuwa gida.

Cikin matukar saa sun tadda gidan abude adalilin dawowar Alh Mustapha Kenan daga kamfaninsa.

Yana zaune a kujera me zaman mutum biyu Yana rike da Kofin lemo zai Kai bakinsa Kenan sallamar mujaheeda yasa ya tsaya cak gami da juyowa Yana murza idanunsa "mujaheeda

kece?", Ta saki jakar hannunta ta taho da gudu , lokaci daya yayi wurgi da Kofin hannunsa ya ware hannayensa ya rungume mujaheeda Kam Yana yima Allah godiya.
Tsayawa kawai Haj murjanatu tayi tana kallon irin murna da shaukin da Alh Mustapha ya shiga na ganin mujaheeda.

Ya saketa ya shiga duddiba jikinta Yana fadin "Alhamdulillah mujaheeda kin warke, Allah na gode maka". Hawaye ya shiga fita daga idanunta hakika Basu kyauta ba zaman da sukayi a Germany na tsawon lokaci bai kamata ba.

Ya zaunar da ita sannan ya dubi Haj murjanatu, tayi zaton ganin wulakanci da tozarci daga gare Shi , Amma sabanin hakan sai taga yayi murmushi yace "sannunku da zuwa".
Ta zame ta zauna Akan kujera tana kallonsa.
Ya dawo gefenta ya zauna Yana kallonta "me yasa Baki sanar da ni zaku dawo ba da naje da Kaina na dakko Ku, ko da yake bakya son nasan komai a game da Ku".

Shuru kawai tayi duk jikinta yayi sanyi.
Ya tashi ya dawo kusa da mujaheeda yace "jeki kiyi wanka ki huta Zan sa a kawo abinci daga restaurant".
Cikin faraa tace "To daddy".
Harta tashi ya dubeta yace "Bari nayima Taufiq albishir din dawowarki". Ta tsaya ta na kallonsa sannan tace " Daddy har yanzu Yana tunawa da ni ne".
Yace "ta yaya Taufiq zai manta da ke mujaheeda? kece kika manta da Shi Amma Shi kullum kina cikin tunanin sa".
Kai kawai ta jinjina ta juya ta shige cikin daki.
Daga bisani itama Haj murjanatu ta kasa jurar irin kallon da Alh Mustapha yake yi Mata hakan ne yasa itama ta tashi ta shige nata dakin Wanda tayi mamakin yadda ta Sami dakin tsaf tsaf a gyare domin dai tasan babu wata me aiki daya da ta bari a gidan kafin tafiyarsu duk ta sallame su.

Cikin kankanin lokaci gaba daya labarin dawowar Haj murjanatu da mujaheeda ya iske duk wanda yakamata ya iske ta hanyar Alh Mustapha labaran.
Taufiq ya Fara sanarmawa, zahiri yayi matukar jindadi da murnar dawowarsu, domin dai ko kadan bai kullacesu da ràshin dawowar su ba domin yasan cewa bacin rai ne ya haddasa hakan.
Sosai yayi kewar mujaheeda, ya na Kuma cike da dokin son ganinta domin tayi jinyar da ya cire rai da ita.
Muhseena ta dago fararen idanunta ta dubi Taufiq Yana ta faraa da murna sosai ta dan numfasa tace "kana murnar dawowar anti mujaheeda sosai ko?", Ta Karasa maganar a raunane, ya juyo ya dubeta sannan ya tashi ya dawo inda take ya zauna sosai gami da kwanto da Kansa a Saman kafadarta, tasa hannu daya ta tura cikin gashinsa tana daddanna gashin.
"Kina da damuwa ne Akan hakan".
Ta girgiza Kai tace "Ko daya, yaya Taufiq Nima ina murnar dawowarsu, Amma Kuma ina fargabar abubuwa da dama". Ya Kara kwantar da Kansa Yana lumshe idanunsa.

Yace "fargabar me kike yi"
Ta Dan numfasa sannan tace "ina fargabar Kada anti mujaheeda ta ki amsata bayan tasan dangantakar da ke tsakaninmu na hada Miji da Kuma hada iyaye".
Ya girgiza Kai sannan ya dago yasa hannayensa biyu ya rungumeta Yana sunsinar kamshin jikinta.
Yace "ko hakan ya kasance ba zai canja komai ba a game da matsayin mu, domin ke jinin jikina ce don haka rabo da ke tamkar rabo da Raina ne".
Ta saba Jin irin wadannan kalaman masu sanyaya rai daga gare Shi.
Don haka ta gyara zamanta tace "Bana kishin anti mujaheeda hakanne yasa a kullum nake adduar Allah ya daidaita tsakaninmu domin bazan taba yarda ace akaina aurenku ya samu matsala ba, don haka don Allah kayi iya kokarinka domin anti mujaheeda ta dawo gareka".
Ya lumshe idanunsa,bai taba ganin mace mara son Kai irin muhseena ba, wannan halin nata Yana daya daga cikin dalilan da suke Kara Sawa yake matukar kaunarta.
Ya Bude idonsa suka hada Ido yace "in sha Allah zanyi iya kokarina".
Tace "idan zaka dubata Zan bika".
Ya girgiza Kai Yana kallon cikin jikinta watanni biyar har ya Fara turo Riga yace "ki huta yau kinga kin jigata dazu Aman da kikayi", tace "Lafiya lau nake yaya Taufiq, ai na gaya maka dalilin yin aman nawa, kamshin turarenka ne da bana so yanzu".
Yayi murmushi yace "To ai na fitar da su daga gidan". Gaba daya sukayi dariya.

Karfe biyar da rabi Taufiq da muhseena suka isa gidan Alh Mustapha labaran. Dukkansu a falo suka taddasu a zaune Alh Mustapha labaran Yana kusa da mujaheeda labari suke yi sosai. Shigowar su muhseena gaba daya sai mujaheeda ta kidime, idanunta suka sauka akan cikin muhseena wani irin bakinciki ya tokare zuciyarta, tayi saurin dauke kallonta daga muhseena ta dawo da Shi Kan Taufiq inda take Jin numfashin ta na saurin fita , duk yadda ta so da ta tsani Taufiq ta kasa domin dai wani irin matsanancin sonsa ne ya ke yawo acikin jininta, tana son daina kallonsa Amma idonta ya kasa Shi kawai take son gani kamar yadda shima ya zuba Mata Ido duk da irin ramar da tayi to fa sai yaga ta Kara masa matukar kyau.

Kai tsaye muhseena gun mujaheeda ta wuce ta rungumeta tana tambayar ta jikinta.
Mujaheeda ta yi kokarin daidaita tunaninta , hakan yasa ta amsa duk gaisuwar muhseena ba tare da nuna wata alama ta damuwa ko tsanarta ba.ita Kam Haj murjanatu ko yaya ta dubi muhseena Jin wani bacin rai take tana Kara jinjina cewa wai muhseena YAR Alh Mustapha ce.
Har muhseenan ta tashi ta dawo gaban Haj murjanatu ta durkusa har kasa ta gaisheta , yadda Alh Mustapha ya Kura Mata Ido domin ganin irin karbar da zata ma muhseena yasa ta yi kokarin boye komai ta amsa Mata sannan ta Kara da cewa ta tashi ta hau kujera.
Hakan ko ba karamin mamaki yaba muhseena da Alh Mustapha labaran ba, tambayar da suke ta yima kansu itace "shin Haj murjanatu ta shiryu ne ta Kuma karbi muhseena a matsayin kaddararta ko kuwa wani sabon wasan zaa Fara?.

Taufiq ma ya gaida Haj murjanatu yadda yayi zaton zata amsa yaga sabanin hakan domin ta amsa a mutunce.

Alh Mustapha ya Kula da irin yadda Taufiq da mujaheeda ke kallon juna,don haka ya dubi mujaheeda yace "mujaheeda ki tashi Ku Koma wancan falon ke da Taufiq Ku gaisa".

Ya karasa maganar Yana kallon muhseena itama Shi take kallo , ta idonsa yake lallashinta ta Kuma fahimci hakan don haka ta jinjina masa Kai gami da yin dan murmushi sannan tayi kasa da kanta, har su mujaheeda suka wuce ta gabanta bata dago kanta ba, duk da idon Taufiq na kanta ya so su hada Ido don ya fahimci yadda take ji amma hakan bai samu ba.

Suna shiga falon mujaheeda zata wuce ta zauna akan kujera Kenan, Taufiq yasa hannu ya janyota gaba daya zuwa faffadan kirjinsa, tun tana kicikicin kwace kanta harta sallama ta koma ta kwantar da kanta Shi Kuma ya sa hannayensa biyu ya Kara rungumeta ya runtse idonsa sosai cikin wata kasalalliyar murya yace "Mujaheeda me yasa kika guje ni?, Me yasa kika ki dawowa bayan kin Sami lafiya?".

Cikin kuka tace "saboda Baka Sona yaya Taufiq Ka Sami makwafina, baka bukatata a rayuwar Ka".

Ya dago da fuskarta ya manna bakinsa a nata hakan yas dole ta hadiye sauran kalaman nata, bata Hana Shi ba domin itama tasan tayi matukar rashinsa.

Gaba daya Kan kujera suka zube, ya zare bakinsa a nata ya kura Mata Ido tsawon lokaci suna kallon juna, sannan yace "waye ya gaya Miki Bana son ki? Waye ya gaya Miki bana bukatarki, na rantse Miki mujaheeda ina sonki na Kuma fi kowa bukatarki, ina son kiyi min uziri ban auri muhseena don Bana sonki ba ko don ina son na wulakantaki, kaddara CE kawai tafi karfin mu Wanda nake son kema ki yarda da wannan kaddarar don Allah mujaheeda mu bar maganar nan tun da kin Riga ayanxu kinsan matsayin muhseena agareki bayan abokiyar zamanki ita din yar'uwarki ce, sannan mahaifiyarta tana sonki kamar ita ta haifeki nasan an sanar da ke komai itace wacce ta yi rainonki wacce baki son ta tafi ko'ina ta barki".

Kuka me karfi ta Kara fashewa da Shi tace "naji komai, don Allah Ka daina tunatar da ni".

Ya Kara matseta Yana shafar ko'ina a jikinta, "ina tunatar da ke ne saboda ki Kara yarda da cewa komai hukuncin Allah ne, mujaheeda ki dawo gare ni".

Ta kasa tabuka komai daya wuce fitar da hawaye.

Taufiq ya cigaba da sumbatar ko'ina a jikinta, tun bata maida masa martani harta Fara mayar masa "ki dawo gare ni mu cigaba da rayuwa".

Mujaheeda batasan lokacin da tace "Zan dawo gareka yaya Taufiq domin bazan iya rayuwa babu Kai ba,na fusata da Kai Amma ina ganinka komai ya fita araina".

Abinda Taufiq yake son ji kenan , tana Gama fadin haka ya zare jikinsa daga nata ya janyo hannunta ya rike idanunsa jajir yace "Alhamdulillah nagode mujaheeda ko yanzu ki zo mu tafi gidan mu mu shimfida sabuwar rayuwa".

Ta girgiza Kai tace "muhseena fa?"

.ya girgiza Kai yace "Baki da matsala da ita tafi kowa son ki dawo dakinki a matsayin yaya uwa daya uba daya take kallonki nasan muhseena ba zata taba baki matsala ba,".

Ta yi kasa da kanta zuwa wasu dakikai sannan tace "shikenan, zanyi magana da mummy idan nasa ranar dawowa sai na sanar da Kai".

Kafin yayi magana tace "ina fadwa?, Me yasa baku taho da ita ba?".

Yace "zasu taho tare da Haj don tana gidan mu jiya Haj ta tafi da ita".

Ta dago tace "Ta yi girma ko?".

Ya zaro wayarsa a aljihu ya fito da hotonta ya nuna Mata. Ta Kara kyau ga girma da tayi sosai.

Haka Taufiq ya cigaba da lallashi da nuna ma mujaheeda muhimmancinta a gare Shi , har sai da ta ji ta aminta sosai da maganganunsa, zuciyarta Kuma ta natsu da ta koma gidansa.

Sun Dade Basu fito daga falon ba , tun Alh Mustapha na Jan muhseena da hira domin kauda mata shiga damuwa har ya Rasa abinda zai fada. Ita kanta muhseena ta Kula kwarai da dalilin da yasa Alh Mustapha ke kokarin dauke hankalinta don haka nunawa tayi babu komai, amma ta rasa dalilin da yasa can kasan zuciyarta take Jin zafi da Kunar kebewar Taufiq da mujaheeda.

Ita ko Haj murjanatu dadi ne ya cika zuciyarta domin ko banza dai Taufiq ya nunama muhseena Yana son mujaheeda tunda har gashi ya manta da ita alokacin da yayi tozali da mujaheeda.

Wannan Kuma shine Karon farko da ta ji , mujaheeda ba zata bar ma muhseena Taufiq ba, zata koma dakinta tayi rayuwa yadda take so , domin muhseena bata isa ta Hana mujaheeda jindadin rayuwa ba.

Daga bisani dai Taufiq ya fito yayi sallama dasu Haj murjanatu suka dauki hanyar gida Shi da muhseena. Har sun Dan yi nisa muhseena ta Kara kallonsa ranta cike da kuna tace "Ka gyara maballin rigarka a balle yake, sannan idan mun ISA gida kayi saurin canja rigar jikinka domin janbakin matarka ya bata rigar".

Duk da ya Sami faduwar gaba sai ya dake, yayi kamar baiji.abinda tace ba. Domin ya Kula kwarai da fushin dake makale a fuskarta.

Kai kishi na wahalar da Mata, komai dai kauda Kan mace Akan mijinta sai tayi kishi matukar tana sonsa.

A ranar Haj saratu da Alh yusuf lamido da fadwa da Haj bilki da haulat suka je gidansu mujaheeda suka dubata. Kam mujaheeda ta rike fadwa tana Jin kaunarta har cikin bargonta tayi rashinta sosai, don ko da suka tashi tafiya nan suka bar Mata fadwa.

Kwanaki uku da dawowar mujaheeda kullum Taufiq sai ya je gidan su, fadwa Kuma na gunta ta hanata dawowa.

Rana ta hudu shima can gidan Taufiq ya uni, damuwa sosai muhseena take yi ko kadan bata son kishin mujaheeda yayi tasiri a zuciyarta, domin ta Fara Sama ranta cewa Taufiq ya koma ga mujaheeda. Uni Kuna ranta yake yi, tana tunanin abubuwa da dama Sam bata son shaidan yayi galaba akanta.

Sha daya saura minti goma na dare, Taufiq ya dawo, muhseena na kwance a Kan doguwar kujera innalillahi wainna'ilaihirrajiun kawai take ta maimatawa acikin zuciyarta.

Cikin dakushewar murya muhseena tace "sannu da dawowa". Ya zauna a gefenta yasa hannu ya Fara shafan Saman bayanta domin ya fahimci sautin damuwa acikin muryarta "yauwa tauraruwata".

Ta lumshe Ido ta Bude hakan nan ta ji hawaye ya na kokarin fita Mata.

"Ya anti mujaheeda"

Bai amsa ba illa cigaba da shafata da yake yi , bata damu da ràshin amsawar tasa ba ta cigaba da cewa "yaushe zata dawo dakinta".

Taufiq duk ya fahimci halinda ta ciki ya Kuma fahimci dalilin tambayoyin da take masa. Cikin sanyin murya yace, "muhseena tashi muyi magana".ta makale kafada , ya jinjina Kai Yana kokarin dagata "aah tashi muyi magana tashi".

Ya mikar da ita ya zaunar ya rike hannunta sosai Yana murzawa, yace "kalleni". Ta dago da idanunta masu fitar da hawaye tana kallonsa Amma ta kasa jurar hakan don haka ta runtse idanunta hawaye Yana fita. Cikin sanyin guiwa ya sa harshe ya shiga dauke hawayen daya bayan daya , tsigar jikinta ya cigaba da tashi lokaci daya Kuma kaunarsa Yana Kara ratsa dukkan zuciyarta.

"Kiyi hakuri, ki daina kuka ki tsaya ki fahimce ni".

Ta Bude idonta tace 'ina jinka me kake son na fahimta?".

Ya gyara zamansa har yanzu hannunsa yana cikin nata ya Fara magana cikin sanyin murya, "Kada kiyi zaton ina yin duk abinda nake yi ne saboda na bata Miki rai, ko don na nuna Miki Ina son mujaheeda " ya girgiza Kai "ko daya ba haka bane, ina yi ne saboda na cika alkawarin da kikasa na Miki akan nayi duk yadda zanyi mujaheeda ta dawo gare ni, hakanne yasa nake lallabata tare da nuna Mata muhimmancinta agare ni, Kuma ta amince zata dawo nan da kwanaki biyu".

Muhseena ta danyi murmushi sannan tace "kana son anti mujaheeda?".

Duk da tambayar tayi masa nauyi , hakan Bai hanata gaya Mata magana ta gaskiya ba, inda ya dubeta yace "bazanyi Miki karya ba, ina son mujaheeda sosai". Taji maganar kamar cakawar wuka a kirjinta, tayi saurin boye damuwarta sannan tace "ina fatan zakayi adalci a tsakaninmu, Kada Ka wulakanta ni domin wacce kake so ta dawo gareka".

Ya janyota da karfi Kan kirjinsa ya kwantar , maganarta tayi masa zafi, yace "kina zaton Bana sonki ne, don nace ina son mujaheeda, muhseena ina sonki son da ban taba yi ma wata mace ba ina jinki a cikin zuciyata da jinina".

Hannunta tasa ta rungume Shi sosai sonsa na cigaba da zafafa a cikin ranta. Shima rungumeta yayi tsam tsam, Yana cewa "nayi Miki uziri nasan kishi na ne a ranki Wanda ban isa na Hana ki ba domin halittace , sai dai ina rokonki Kada ki zafafa ma kanki kishi irin na mujaheeda, Wanda itama kullum naje ina yi Mata nasihar ta rage kishi Kuma Alhamdulillah tun dasowarta na fahimci kishinta ya ragu sai dai Wanda baa rasa ba, Wanda kullum na je ina kokarin cire Mata kishinki domin ina shaawar Ku zauna lafiya".

A hankali tace "Allah yasa mu zauna lafiyan "

"Amin ya Allah, Shi yasa ba zaku zauna gida daya ba zaki cigaba da Zama a gidanki itama zata cigaba da Zama a gidanta , hakanne zaisa Ku zauna lafiya don idanun Ku ba zasu ga komai ba balle zuciya ta so su".

Ta yarda da maganarsa hakan ya fi, saura Kuma ta yi yaki da shaidan akan abinda yake son tusa Mata arai.

Ta Kuma sa aranta ranar da mujaheeda zata dawo ranar zata koma Kaduna ba Kuma zata dawo ba har sai ta Gama service din ta gaba daya Wanda watanni uku ya rage.

Tabangaren mujaheeda kuwa zafi da kushin muhseena sun ragu sosai a zuciyarta, tun daga ranar da Haj madina ta sanar da ita irin kokarin da muhseena tayi Akan jinyarta Wanda kullum sai ta zo asibitin ta Kula da ita har tabar kasar.

Sosai take ganin kima da mutuncinta, ita kanta Haj murjanatu jikinta yayi sanyi da Jin abinda

bata sani ba.
Hakanne ma yasa da mujaheeda ta yanke shawarar komawa dakinta bata shiga cikin hukuncinta ba, sai ma karfafa Mata guiwa tayi kamar yadda Alh Mustapha ya karfafa Mata ,
Aranar ita kanta Haj murjanatu tayi mamakin yadda Alh Mustapha ya nuna lalle mujaheeda yarsa ce, Wanda tayi zaton zaiyi son rai ya nuna muhseena yake so amma a maganganunsa ya tabbatar mata matsayin mujaheeda da muhseena daya awajensa.

Kuma da Kansa ya dauki mujaheeda ya maidata dakinta. Ya Kuma sa Taufiq ya kawo muhseena ya zaunar da su yayi musu nasiha me tsuma zuciya, ya Kuma gaya musu su aje alakar kishi dake tsakaninsu su dauki alakar ya da kanwa da rayuwa ta kaddaro musu, ya tunanar da SU dukansu yayansa ne. Ya Dade sosai a gidan da Kuma ya tashi tafiya tunda dare yayi cewa yayi Taufiq yayi zamansa Shi zai aje muhseena a gida. Duk da ransa Bai so ba haka ya daure ya karbi hukuncin surukinsa.
Ko a motar tun fitar su gidan, Alh Mustapha labaran yake cigaba da yima muhseena nasiha ya Kara da cewa "kwanciyar hankalinki shine nawa domin Bani da wani abu da nake so sama da ke ina sonki ina jinki acikin bargona Bana son damuwarki don haka ki kwantar da hankalinkinki Zama da kishiya ba wani abu bane idan kika dauka da zafi yafi wuta zafi idan kika dauka da sanyi yafi kankara sanyi, illa iyaka ki rike ibada da addua da Kuma biyayya ga mijinki ki yarda shine shugabanki Kuma ibada kike yi , sannan ki zauna da mujaheeda da zuciya daya ki so ta ki kaunace ta to komai zai zo Miki da sauki".

Muhseena ta dauki nasihar mahaifinta sosai. Bayan ya ajeta a gida.
Har tayi Shirin kwanciya wayar Taufiq ta tsaidata ta dauka cike da faraa tace "Ango kasha kamshi" yayi dariya yace 'Kin sha magani" ta amsa "Na sha", "Kin kashe AC KO, kinsan dai matsalar da yske janyo Miki, Kuma Bana nan" tace "Kada Ka damu duk abinda Ka Saba yi min nayi da Kaina nagode da kulawa", ya gyada Kai yace "ko nasa Haulat ta zo ta kwana da ke ne" ta girgiza Kai tace "aah babu damuwa, sai Allah ya kaimu goben" yace "to Allah ya kaimu" . Daganan suka aje wayar.
Yadda muhseena tayi zaton zata Dade bata iya bacci ba saboda ràshin Taufiq, ba haka bane domin tana Gama addu'onin baccinta bacci ya kwasheta.

Ta so komawa Kaduna washegari Amma Taufiq ya ki har sai ranar litinin da kanshi ya dauketa zuwa Kaduna bayan ya kaita tayi sallama da mujaheeda.ta jidadin yadda taga fadwa ta sake da mahaifiyarta sosai sai dai Kuma ganin muhseena zata tafi yasa tayi ta kuka daker mujaheeda ta lallasheta tayi shuru bayan tafiyarta.
Irin rukon da muhseena tayi ma fadwa kadai ya isa yasa mujaheeda ta so muhseena,kamar yadda take kokarin yi a yanzu domin da karfi da ya ji tana ta turama kanta kaunar muhseena, irin soyayyar da take Mata tun farkon zuwanta gidanta Shi take kokarin dawowa da Shi, domin dai ta tabbatar da cewa muhseena bata da tunanin raba ta da mijinta.

Washegarin komawar muhseena Kaduna, mallam Umar da Hajara suka iso jigawa takanas domin duba mujaheeda. Hajara cike take da dokin ganin mujaheeda domin dai har yanzu kaunarta na nan makale acikin zuciyarta.

Haj. Saratu ce tayi musu rakiya har gidan mujaheedan, yayin da Taufiq ya bar komai ya baro office ya dawo gida domin gaisawa da surukansa. Tun zuwansu gidan sabbin Yan aikin mujaheeda suke dawainiya da su, ita ko mujaheeda duk da karancin shekarun ta alokacin da tayi rayuwa da Hajara to fa ta dan tuna wasu abubuwan da dama, haka zalika sosai take ganin girman Hajara musamman yadda ta zauna tayi ta Mata nasiha gami da nuna Mata muhimmancinta a gareta, ta Kara da cewa "Nasan ba zaki iya tuna irin shakuwa da soyayya me karfi da ke tsakanina da ke a wancan lokacin ko bandaki Zan shiga sai kin tsaya bakin kofa kina jiran fitowa ta.....?.

Mujaheeda ta numfasa tace "Zan iya tuna wasu , wasu Kuma na manta, amma tun kafin zuwanki daddy ya tunatar da ni hakan, cikin abinda ya tunatar da ni harda alakata da muhseena ta bangarenki". Cikin nauyin baki Hajara tace "hakane ba zamu ja da kaddara ba domin yin Allah ne, Alh Mustapha shine mahaifin muhseena Shi yasa nake son Ku hada Kai don Allah Kada Ku kalli junanku a matsayin kishiyoyi don da ina da ikon canja wannan kaddarar na Zama karkashin Miji daya ke da muhseena hakika da na canja, Amma bamu da yadda zamuyi".

Mujaheeda dai ta natsu tana sauraron maganganun Hajara, bayan ta Gama itama Haj saratu ta dora da nata, Taufiq dai Yana gefe ransa yayi fari kal, irin nasihohin da sukema mujaheeda Yana yi masa dadi kwarai.

Daga karshe shima Mallam Umar ya dora da na Shi, duk abinda suka fada gaskiya ne mujaheeda Kuma tayi alkawarin yin amfani da duk abinda suka ce. Da zasu tafi rafar dubu daya mujaheeda ta ba Hajara nera dubu dari,ta amsa gami da sa Mata albarka.

Kwanan su Hajara biyu a jigawa suka koma Durmi, Amma kafin su koma sai da Mallam Umar ya Kai Hajara gidan Alh Mustapha suka gaisa da Haj murjanatu tare da yi Mata murnar Samun lafiyar mujaheeda. Yadda Hajara ta dauka Haj murjanatu zata karbeta sabanin hakan ta gani domin duk da fuskarta babu yabo babu fallasa to fa bata wulakanta su ba, har suka bar gidan Hajara na cike da mamakin hakan gami da fatan Allah yasa ta shiryu ne ta dawo hanya madaidaiciya.

****

Kamar yadda muhseena ta kudurta a ranta ba zata Kara komawa jigawa ba sai ta kammala bautar kasarta, haka ta dage duk iya yadda Taufiq ya so ta dawo ta ki dawowa acewarta ta ba su damar cin amarcinsu ne, Har fushi sai da Taufiq ya yi amma ta ki dawowa sai dai kullum ta tura masa sakon ban hakuri da neman yafiya.

Dole shine hakurinsa ya Gaza ya sanar da mujaheeda zai je aiki na kwanaki biyu . Daganan Kaduna ya wuce. Ko da ya je duk yadda ya so da ya nuna Mata ransa ya baci sakamakon kin dawowarta gida ya kasa saima tausaya Mata da yayi sakamakon ganin yadda cikinta yayi girma sosai, sai dai duk da haka ya kasa hakura da ita sai da ya dauketa daga gidan Alh Sani gidan abokin Alh Mustapha inda take Zama ya kaita hotel din da ya kama, anan ya lafarma Kansa da duk wata sha'awarta da ta addabe Shi, ita kanta duk da jikinta yayi nauyi bai hanata kokartawa ta Fara ta masa rai ba yadda yakamata.

Kwana biyu yayi a Kaduna sannan ya dawo jigawa.

Yau litinin aranar mujaheeda ta koma office, kamfani na nan inda ta barshi babu abinda ya

sauya Àlh jibrin ne ke yin yadda ya so Yana ta cin karensa babu babbaka.

Sai dai tana shigowa kamfanin Alh jibrin ya kidime , nan da nan ya hada files ya Kai Kan tebur dinta ya sanar da ita Dama Yana Shirin yin tafiya , ga duk abinda zata bukata nan , yayi Mata Kuma fatan alheri tare da tayata murnar Samun lafiyar ta. Daganan a gaggauce ya bar office din. Haka sauran ma'aikatan suka yi ta shigowa suna yi mata murnar Samun lafiya.

A gigice mujaheeda ta shigo falon Haj murjanatu tana kwala Mata Kira, da sauri Haj murjanatu ta fito daga cikin daki, tana fadin "mujaheeda menene Lafiya?".

Mujaheeda ta fito da takarda ta Mika Mata sannan ta fada Kan kujera tana aje numfashi. Da sauri Haj murjanatu ta bude takardar ta Fara dubawa, itama a hankali takardar ta sulale a hannunta ta Fadi kasa.

Ta dubeta Baki na rawa "mujaheeda ina duk aka Kai wadannan kudaden", mujaheeda ta dubeta Ido jajir tace "Duk iya binciken da nayi manager shine ya tattaresu ya handame, tsawon wannan shekarun da mukayi. Bama kasar babu wani abu daya na cigaba da kamfanin ya samu, da yawan ma'aikatan ma wasu an koresu saboda ba'a iya yin albashi , an daina shigo da Kaya hakan yasa babu wasu Kaya da kamfani yake sarrafawa balle har afitar da su a samu riba, kayan aiki da Muke ajewa a ma'adanar kamfani babu komai, murtala ya tabbatar min da cewa manager jibrin shine ya ke fita dasu Yana sayar ma da sauran kamfanoni irin namu Shi yasa yanzu baa maganar kamfanin mu domin duk abinda Muke sarrafawa mu fita dashi sauran kamfanonin irinsa suke yi, babu ko sisii a asusun kamfanin, babu dai komai sai ginin kamfanin da Kayan aikin ciki amma bamu da kudin cigaba da Kula da kamfanin , sai dai a rufe Shi.".

Haj murjanatu ta fada Kan kujera turus, tana fadin " jibrin yayi mana illa, innalillahi wainna'ilaihirrajiun,na yarda da jibrin na bashi duk amanata me yasa zai min haka, na rantse yanzu zansa yansanda su kamo Shi duk abinda ya ci sai ya dawo da Shi". Mujaheeda ta girgiza Kai tace "ban shigo gidan nan ba sai da na Gama bincike akan Alh jibrin, baya cikin jigawa domin tun shigata kamfani ya tafi ya ce Dama zaiyi tafiya ,sai yanzu na gane dalilin tafiyar tasa iyalansa ya dauka suka bar jigawa, mummy ban san inda suka koma ba, bansan ta yadda zamu iya kama Shi ba".

Iya gigita da tashin hankali Haj murjanatu ta shiga, domin wannan kamfanin kusan Rabin dukiyarsu Yana ciki. Nan da nan ta shiga sambatu, mujaheeda ta dawo kusa da ita ta zauna tana tausarta tare da karfafa Mata guiwar za'aga Alh jibrin. Amma ina Haj murjanatu ta riga ta gigice, a haka Alh Mustapha ya shigo ya taddata cikin mawuyacin Hali, mujaheeda ce ta iya yi masa bayanin duk abinda yafaru.

Shima ya jinjina al'amarin ya Kuma samu damuwa kwarai, nan da nan ya fito da wayarsa ya Kira dpo din yankinsu ya sanar da Shi duk abinda ke faruwa ya Kuma bukaci taimakonsa akan yasa a Sanya Ido akan Alh jibrin a binciko inda ya gudu da iyalinsa ,dpo ya jajanta sannan yayi alkawarin taimakonsa.

"Suma sauran kamfanonin ya kamata a bincike su asan Suma wane Hali suke ciki". Mujaheeda tace "hakane daddy, domin jikina yayi sanyi duniya babu amana mutane duk sun

gurbace, son duniya yayi musu yawa kowa so yake yayi arziki ba tare da ya wahala ba, Burinsu wani yayi musu wahalar su su kwashe kudin , shin ina son Kai da son rai zai kaimu ne"?.

Alh Mustapha labaran ya 'Allah dai yasa mu fi karfin zuciyar mu, yanzu yamma tayi Amma gobe Zan aje duk abinda nake Zan je duk sauran kamfanonin na zauna da manajojin, na ji inda aka kwana". Mujaheeda tace "hakan yayi daddy Allah ya kaimu goben". Daganan ya koma wajen Haj murjanatu da ta dauke wuta ta rasa inda kanta yake komai sai juya Mata yake akai. Haka Alh Mustapha ya dinga kwantar Mata da hankali tare da nuna Mata sai inda karfinsa ya kare, ta kwantar da hankalinta. Amma har mujaheeda tabar gidan Haj murjanatu bata dawo dai dai ba.

Washegari tun safe Alh Mustapha labaran ya fita zuwa sauran kamfanoni hudu na Haj murjanatu domin sanin halin da ake ciki. Ita kuma mujaheeda ta je kamfaninta ta hada ma'aikatan tayi musu bayanin komai Wanda hakanne zaisa ta rufe kamfanin a yau har sai zuwa lokacin da komai zai daidaita.hankalin ma'aikatan yayi mummunan tashi sai dai babu yadda zasu yi domin babu yadda zaayi su dinga yin aiki babu albashi. Tana gamawa da kamfaninta gidansu ta wuce.

Hankalin Haj murjanatu idan yayi dubu ya tashi ko abinci daker mujaheeda ta matsa Mata ta ci. Hankalin ta bai Kara tashi ba sai da Alh Mustapha labaran ya dawo da nashi labarin.

Ko wanne kamfani ga file dinsa nan na inda akayi da kudinsa, kusan duk kamfanonin kudaden da suka dinga turama Haj murjanatu zamanin zamansu a Germany da kudaden jinyar mujaheeda da kudin aikin zuciya da akayi Mata duk sune suka karya kamfanonin Suma maganar da ake yanzu babu kudi a kamfanonin ma'aikata na bin albashin watanni hudu wasu uku , babu Kuma kayan da zaa dinga sarrafawa ana fitarwa, duk a bayanan manajojin sunce babu wata hanya da zasuyi magana da Haj murjanatu balle su Gaya Mata halin da ake ciki, tunda ta kirasu sau daya ta Basu dollar account dinta ta sanar dasu duk bayan wata daya ga adadin kudin da zasu dinga sa wa a cikin account din shikenan Basu Kara ji daga gareta ba sai dai sun cigaba da cika umarninta.

TO BE CONTINUE
DAGA TASKAR YAR GIDAN IMAM

NI MA MATARSA CE
64

Tashin hankali Wanda ba'asa masa rana, gaba daya neman yawun bakinta Haj murjanatu tayi ta rasa, sai wani daci da makaki da zuciyarta take yi, tayi ma Àlh Mustapha labaran kuri da idanunta.

Ya jinjina Kai ya dubeta sosai yace "ki kwantar da hankalinki, dukkan bayanan da manajojinki suka min da Wanda na karanta a cikin files din nan gaba daya na gamsu da Shi, ba su cuceki ba kamar da jibrin ya cutar da ke, don haka hakuri ki Sami natsuwa".

Ta dube Shi Ido cike da hawaye tace "ta yaya Zan kwantar da hankalina, bayan asirina Yana neman tonuwa a duniya, Alh idan na rasa kudi na rasa komai domin kudin nan sune ni,". Ya

girgiza Kai yace "ki daina fadin haka domin kudi basu bane komai, kiyi tawakkali , don yanzu ma naba manajojinki umarnin su sallami ma'aikatan su rufe kamfanin batun bashiin da suke bi Kuma in sha Allah idan Allah ya buda duk zaa biya su ".

Mujaheeda ta goge hawayenta tace "gara da kasa a rufe din daddy, Nima na rufe nawa, Allah ya bamu mafita"ya dubeta yace "Amin". Daganan ya juya wajen Haj murjanatu irin tsantsar damuwar da take ciki yasa ya cigaba da bata hakuri gami da bata misalai Kala Kala bai gushe Yana bata baki ba har sai da ta sakko ta dawo hayyacinta ta Kuma tabbatar da bata da wata mafita da ya wuce yin hakuri tare da fauwalama Allah komai sosai tsoron Allah yakamata domin ta Kara tabbatar da shine yake tsara komai yadda ya ga Dama talakawan da take rainawa haka Allah ya tsara musu rayuwarsu Kuma ko yaushe ya ga Dama zai iya azurtasu kamar yadda ya azurtata gashi Kuma lokaci daya ya talautata, komai daga gare Shi yake.

...faruwar wannan al'amarin gaba daya ya Kara canja Haj murjanatu, ta Kara fahimtar duk abinda Allah ya kaddara ma bawa ba Shi da yadda zaiyi,

Alh jibrin dai Yayi batan dabo domin har yanzu babu labarinsa, duk binciken da ake yi har yanzu babu labarinsa.

Muhseena ta kammala bautar kasarta da wata daya ta haihu, ta haifo danta sankacece kyakkyawa inda ya ci sunan Alh Yusuf Lamido, suna kiransa da Hanif.

Mujaheeda da ita akayi komai na suna gwanin ban sha'awa, kwarai da gaske mujaheeda ta canja, Shi Kansa Taufiq ya yarda da canjawarta, zaman lafiya ya wanzu a gidan Taufiq kowacce rige rigen faranta ransa take yi, zamansu da ban da ban ya taimaka wajen Samun zaman lafiyarsu.

Ma'aikatar da muhseena tayi bautar kasa NNPC ,sakamakon hazakar da ta nuna da Kuma hanyar da Alh Sani yayi Mata suka dauketa aiki,Samun aiki a irin wannan wajen ba abu bane na wasa sai mai rabo hakanne yasa murna awajen muhseena da Taufiq da duk wani masoyinta baa magana domin dai yanzu muhseena ta kerema saa.

Sai dai Nisan da muhseena zata yima Taufiq shine damuwarsa amma babu yadda zaiyi tunda cigaba ne ta samu.

Wata hudu bayan haihuwar muhseena ta tattara ta koma Kaduna , kudaden da wajen ajikinta suka bata domin ta kama gida da sauran bukatu sune ta hada gaba daya ta sayi gida a Kadunan.

Duk sati Taufiq ke kokarin zuwa Kaduna nan yake yin weekend dinsa, sau tari wani zubin Yana zuwa da fadwa Wanda ba dan makaranta ba da tayi zamanta a Kadunan kasancewar yadda kullum zai koma da kuka ake rabuwa.

****

Rayuwa ta Mika lokaci Yana ta tafiya , alokacin da Allah ya azurta muhseena alokacin Allah ya talauta Haj murjanatu da mujaheeda. Domin har zuwa wannan lokacin baasan inda Alh jibrin yake ba, Yan ragowar kudaden da suke cikin asusun ajiyarsu yau da gobe sun sa duk sun kare.Rayuwa ta Fara yima Haj murjanatu wahala abinda tafi karfinsa Yanzu yafi karfinta. Yanzu gaba daya hidimarta ta koma hannun Alh Mustapha Wanda da take ganin tafi karfin ta tsaya yayi Mata hidimar rayuwarta duk da Shi Allah ya dorama yayi Mata, a dole yanzu ta yarda da

cewa itace matar shine Mijin wannan gadarar da izzar duk ta sauke su domin babu abinda zatayi gadarar da Shi tunda ba tafi karfin komai ba, kullum cikin damuwa da tashin hankali take Shi Kuma Alh Mustapha Yana tausarta Wanda ba don asara da tayi ba da yayi ma Allah godiya da yasa ta rasa komai domin hakan ne yayi sanadiyyar da ya mallaki matarsa yanzu yasan cewa Yana da Mata , tunda zai ce ayi ayi agidansa kamar yadda zaice a bari a bari, ya Kuma samu damar yin cafane kamar kowane magidanci sabanin da da sai dai adafa a bashi babu me cewa asayo kaza, ko raayi yayi ya sayo baya burgeta don ba lalle bane ayi amfani da Shi,. Unguwa bata tambayarsa amma yanzu Saita tambaya, Yan aiki duk shine yake biyansu Shi yasa yake iko kamar kowane magidanci.

Itama can mujaheeda tuni ta Gama yarda da cewa mijinta shine gatanta tana binsa sauda Kafa, tsakaninta da muhseena Kuma babu komai sai zaman lafiya. Ayayinda Alh yusuf lamido yake jaddadama Taufiq kullum Kada ya sake ko da wasa ya wulakanta mujaheeda ko ya ci zarafinta domin tana nan amatsayin yar gaban goshinsa , Shi yasa yafi kowa jindadi da murnar gyaruwar halayen mujaheeda da mahaifiyarta.

Tabangaren muhseena kuwa rayuwa sai Alhamdulillah domin ta mallaki duk abinda take mafarkin mallaka a rayuwa, kudi kima da darajar da take ganin bata da su a da ,ayanxu duk ta hadasu.

Acikin shekaru uku da Fara aikinta ta cika burika da yawa a rayuwarta.

Ta sayama mahaifanta gida me kyau a Kaduna. Su Hajara da hajja Ande sun bar Durmi sun dawo Kaduna cikin gata, hajja Ande kwana tayi ranar tana kuka tare da Sama muhseena albarka, abinda bata taba tunanin zai faru ba yau shine yake faruwa, muhseena da take ganinta wulakantacciya itace ta Zama gatansu , itace komai na su itace abin alfarinsu itace sanyin idaniyarsu.

A ranar har kasa ta durkusa tana yima muhseena godiya tare da neman afuwarta, ta durkusa ta dagota tace "haba Ande kinfi karfin haka a wajena na rantse babu abinda bazan Miki ba domin Bani da kamarku, ki manta da faruwar komai Ki jidadinki kakata".gaba daya suka sa dariya. Mallam Umar ya dubeta yace "Allah yayi Miki albarka muhseena Dama ni nasan sai nayi alfari da ke a duniya kafin Allah ya dauki raina, Allah yayi Miki albarka Allah yasa kifi haka".

Muhseena ta zuba masa Ido kaunarsa na Kara kamata tace "Babana burina kullum na faranta ranka in dai akwai albarkarka in sha Allah cigaba yanzu aka Fara gani".

Yayi murmushi yace "Allah yayi Miki albarka Allah ya dafa Miki".

Itama Hajara kukan dadi tayi tayi tana sa Mata albarka duk wañnan katon gidan ace na sune a gari kamar Kaduna hakika haihuwar muhseena tayi Mata Rana, duk wani bakinciki data taba yi yau ya kau.

Garin Durmi asibiti daya ne har yanzu , muhseena tasa aka gina katon asibiti, duk inda Ka bi garin Durmi maganar muhseena ake yi , kowa so yake ma ya ganta , Amma tana daga gefe sai ruwan alhairai take ta yi musu, ga asibiti ga ma'aikata da aka diba ga ruwa data sa aka janyo musu. Hatta megari sai da ya nemeta da manyan fadarsa SU kayi ta Mata godiya , megari yaji kunyar abubuwan da suka faru abaya Bai ma Kara yin nadama ba sai da muhseena ta biya masa kujerar aikin hajji da Shi da Mallam kallah, domin ba zata taba manta cewa megari shine

silar farincikinta domin shine yayi sanadiyyar aurenta da Taufiq Wanda hakan ya Zama alheri a rayuwarta Mallam kallah Kuma duk da mahaifiyarta wahala ta ci a gidansa to ba zata taba manta cewa ya taimakama mahaifiyarta da wajen Zama ba alokacin da kowa ya ki ta.

Wai aiko bakin mallam kallah har kunne Shi da matarsa itama tana adduar Allah yasa wata rana itama ta biya Mata .

Har Kaduna megari da Mallam kallah suka je sukayi Mata godiya, mallam kallah kallon gidanta kawai yake Yana fadin "ikon Allah tikisa Zainabu kece da wannan gida Allah abin tsoro".

Ta Basu kudi masu yawa na mota suka tafi cike da al'ajabi da tsoron Allah,domin ganin abinda basu taba mafarkin faruwa ba Ya faru. Duk inda kabi kauyen Durmi maganar muhseena ake yi da irin cigaba da canjin da ta samu a rayuwarta.

A wannan lokacin ta kare dire danta na biyu Wanda ya ci sunan Mallam Umar ana kiransa da Ansar, tsakaninsu wata uku da mujaheeda itama ta haifo yarta mace inda aka sa Mata Hajara ta ci sunan mahaifiyar muhseena Wanda hakan ba karamin jindadi Hajara da muhseena sukayi ba, domin komai na sunan Hajara muhseena ta dauke bayan sha Tara na arziki da ta saukema mujaheeda da Hajara wacce zaa dinga kiranta da Aleena.

Hadin Kai sosai mujaheeda da muhseena suke yi Basu yarda shaidan ya shiga tsakaninsu ba domin ko shaidan ya shiga tsakaninsu sun Sami matsala to da sauri suke gyara matsalar basa bari abin yayi nisa.

Dole mujaheeda ta nemi aiki da takardunta saboda abubuwa duk sun canja, ta fahimci dole ta tashi ta nemi na kanta abinda ba'a taba nuna Mata ba saboda Haj murjanatu ta manta ba kowane abu bane yake tabbata kamar yadda ayanzu rayuwar ta canja musu.

Amma Alh Mustapha labaran da Kansa ya dauketa aiki a kamfaninsa tunda ta dage sai ta nemi aiki.

Haj murjanatu ta na matukar jindadin yadda Alh Mustapha bai wofintar da su ba duk da rashi da ya samesu , hakan ya tabbatar Mata da cewa domin Allah Alh Mustapha yake tare da su, tunda talaucinsu da Samun yarsa ta jini baisa ya juya musu baya ba , Alokacin ne ta ji zuciyarta ta aminta da ta yafe masa duk abinda ya yi Mata, ta Kuma yafe masa, alokacin da ta gaya masa ta yafe masa, ji yayi kamar an cire masa Kaya, ya dubeta sosai yace "Na dade da son Jin wannan maganar daga bakinki ,ban Samun kwanciyar hankali matukar na tuna har yanzu baki yafe min ba,to nagode Allah ya yafe min ". Hankalin sa ya Kara kwanciya kwarai da gaske.

Taufiq cike yake da alfari da muhseena kullum Kuma kaunarta tana Kara Samun matsuguni acikin zuciyarsa. Gidajensa sun Zama biyu Kaduna da jigawa duk Kuma da tazarar da ke tsakani Bai taba gazawa ko fashin zuwa wajen muhseena ba,Sam ma ya daina ganin nisan wajen.Haka zalika shima tabangaren aikinsa Yana ta Samun cigaba domin ya Zama shugaban shashin kasuwanci na kamfanin duk wata kwangilar hanya da za'a bayar ta hannunsa yake zuwa arziki ya ci uban na da sai hamdala kawai.

Wannan shekarar mallam Umar da Hajara da Ande dije suka sauke farali muhseena ta biya musu. Ande dije dai ko bayan dawowarsu hakanan Saita rushe da kukan dadi ita kanta cike take da kakabin wai ta sauke farali Kuma ta dalilin muhseena tsakani da Allah taga ishara ita

Kam yanzu ko cewa muhseena da Hajara sukayi ta kwanta su takata su wuce to zata kwanta ta gamsu da cewa muhseena itace gatanta.

Wata shekarar tana zagayowa ta biyama mallam Hamza wanzami mahaifin Kabir, domin dai har kasa ta nade ba zata taba mantawa da Kabir ba domin Yana cikin tarihin rayuwarta. Alokacin da labarin biyan makkan ya Sami Mallam Hamza wanzami rasa inda zaisa Kansa yayi saboda tsananin kunya da nadamar abubuwan da suka faru a baya, Dama tun kafin faruwar hakan yayi nadama saboda irin abin arzikin da muhseena take yi a garin da irin yadda Allah ya daukakata a matsayin ta na wacce suke kyamata yau gashi tafi wasu dubban yayan da aka Haifa ta hanyar aure.

Shima har Kaduna ya je ya nemi gidanta ya je yayi Mata godiya kwarai da gaske nan ma bata barshi haka ba sai da ta bashi kudi masu kauri, lalle arzikin bawa Yana kashinsa Mallam Hamza wanzami ya tsinke da lamarin duniya.

Muhseena bata San inda Kabir ya Sami number ta ba, wata ranar laraba tana zaune a office kiransa ya shigo wayarta, sallama kawai yayi ta ji wani abu ya tsirga a cikin jijiyoyin jikinta, "kin gane me magana".

Ta numfasa a hankali tace 'ko cikin wane Hali nake Kabir idan naji muryarka ai Zan gane".

Jikin Kabir ya Kara yin sanyi kaunar muhseena da duk tsawon shekarun nan yake dakonsa ya shiga dawowa cikin zuciyarsa, cikin taushin murya yace "Baki manta da muryata ba muhseena duk tsawon shekarun nan ". Ta girgiza Kai tace "Ta yaya Zan manta, ya gida ya aiki ". A sanyaye yace "duk lafiya lau",daganan ya cigaba da yi Mata godiya, tace "Don nayi ma mahaifinka wani abu bai kamata kayi min godiya ba, domin har yanzu ban manta irin hidima da kayi da ni arayuwata ba, Kaine ke sayama mahaifiyata magani Kai ke bamu abinda zamu ci agidan mu, Kai Ka Fara nuna min akwai jindadi a duniya shin ta yaya Zan manta da Kai ko alhairinka agare ni,". Kamar Wanda ya Fado daka Kan gado Kabir yace cikin tsumuwa da maganganun muhseena "ina sonki,har abada bazan taba son wata yadda nake sonki ba tsawon wannan shekarun har yanzu son ki na nan acikin zuciyata babu abinda ya canja".tausayin Kabir yayi matukar kamata yadda yake maganar kadai ya tabbatar Mata da gaske har yanzu tana cikin ransa.wanda ita ayanzu mutuncinsa da kimarsa kawai take gani amma babu sonsa aranta ta tattara duk taba Taufiq, tace "ya sunan matarka?", Ya numfasa yace "sunanta Habiba, bayan rabuwar mu na kasa hakura da ke hakan yasa na kasa Kara yin soyayya da ko wace mace a dalilin hakan kawuna Alh Musa da mahaifana suka yanke shawarar hada ni aure da yar kawu musan Habiba, ba nj da wani zabi da ya wuce na yarda da zabinsu domin dai nasan har abada babu ranar da Zan gabatar da wata mace a matsayin wacce nake so, yar mu daya da ita Zainab".

Muhseena ta aje numfashi da karfi tace "Zainab?".

Yace "eh, sunanki nasa Mata"

Tace "don Allah Kada Ka bari tasan sunan wacece kasama yarta, don Bana son ta tsaneta".

Yayi murmushi yace "Aita sani, Habiba ta bambamta da sauran Mata bata da irin wannan kishin na kwatance, ta San sunanki nasa domin tasan komai akanki, kin San me?"

Ta girgiza Kai kamar yana ganinta tace "aah"

Yace "wani lokacin har tsokana ta take tace zo nan muhseena masoyiyar mijina ".

Muhseena tace da sauri "itama muhseena ake kiranta".
Ya gyada Kai yace "haka Muke kiranta", tace"Allah yayi Mata albarka, don Allah Kabir Ka hadani zumunci da Habiba, Ka nemi ni ta whatapp da number nan Ka tura min hotunan ya ta ina son na ganta".
Yace "in sha Allah duk zanyi hakan, yaranki nawa yanzu"tace "yarana biyu Yusuf (Hanif) da Umar (Ansar), da nace na Gama haihuwa amma yanzu Nima in sha Allah zanyi maka takwara".
Gaba daya suka sa dariya sun Dade suna hira kafin suyi sallama.

Wannan shine asalin Fara zumuncin muhseena da matar Kabir Habiba, zumunci suke sosai tare da yayansu.

****

Duk zuwa wannan shekarun Alh Mustapha labaran bai taba gajiyawa ba wajen neman Alh jibrin.
Cikin ikon Allah yansanda sun Sami nasarar cafke Alh jibrin a wani yammaci da ya shigo garin jigawa ba tare da Sanin cewa yansanda suna saye da Ido Akan shi.an kamo Shi zuwa hedkwatar yansanda, dpo Yana Kiran Alh Mustapha labaran ya sanar da Shi Bai Jira komai ba ya dauki Haj murjanatu suka tafi.
Haj murjanatu ta tsinema Alh jibrin yadda yakamata ta Kuma tabbatar masa da cewa duk abinda ya ci nata sai ya fito da Shi, Alh Mustapha yace "wannan Kuma aikin hukuma ne, ki barsu suyi aikinsu". Ya waiwaya wajen dpo yace ",yallabai duk abinda ya dace ayi don Allah ayi duk kudaden da ya nade na kamfani ya dawo da su ko Sisi Kada yayi ciwon Kai". Dpo yace "in sha Allah Kada kadamu zamuyi iya bakin kokarin mu akan hakan". Daganan suka dawo gida suka bar Alh jibrin tsare a wajen yansanda cikin tuhuma.
Kwarai da gaske mujaheeda ma ta jidadin kama Alh jibrin da akayi, domin ita harma ta cire rai duba da irin tsawon lokacin da aka diba ba tare da an ganshi ba.

Yansanda sun Sami nasarar bincikar bayan barinsa jigawa Katsina ya koma da Zama inda kudaden da ya sata ya shiga kasuwanci hakanne yasa kudaden Basu durkushe ba, ayanxu Kuma wulakanta da tijarar da ya gani a wajen yansanda Wanda suke Shirin tura Shi kotu yasa ya amince da zai dawo da kudaden duk da yasan lokacin durkushewarsa yayi domin ba kananan kudade ya samu a kamfanin ba. Dama abinda suke bukata Kenan ya dawo da kudin tunda Kuma ya dawo da su Alh Mustapha da Kansa ya ce a sake Shi . Haka aka sake Shi ya koma cikin talauci tunda bai godema abinda Allah ya azurta Shi da Shi ba sai ya ci amana, ga shinan hatta na shin da ya raina ya rasa domin sun shige cikin kudaden da ya dawo ma da Haj murjanatu.
Alhamdulillah tuni Haj murjanatu ta farfado da kamfaninta , mujaheeda ta koma office dinta,talaucin da ya zamar musu ishara ya yaye arzikinsu ya dawo,sai dai Haj murjanatu tayi alkawarin ba Zata Kara komawa halinta na baya ba wanna izzar ta barta har abada.

Haka rayuwa ta cigaba da tafiya Allah Yana tsara komai yadda ya ga dama, abinda mutum bai taba tunanin faruwar sa ba shine ya ke ta faruwa domin Allah ya nuna ma kowa cewa shine me

yin yadda ya so. Muhseena ta Sami daukaka ta Zama abin alfarin kowa, tabangaren wajen aikinta ma ta Sami daukaka domin hazakarta yasa tana ta Samun cigaba.

Hajara tayi fes idan ba labari aka baka ba ba zaka taba yarda da cewa ta taba dandanar dacin talauci ba. Daga ita har mallam Umar da Hajja Ande kullum cikin sa ma muhseena albarka su keyi. Haka Alh Mustapha labaran shima kullum cikin yabo da sa ma yayansa albarka yake musamman a bangaren zaman aurensu da suka ba mara da kunya suka rike junansu da zuciya daya cikin gaskiya da amana.

Ayayin da adalcin da Taufiq yake kwatantawa tsakanin muhseena da mujaheeda ya sa gidansa ya Kara Samun zaman lafiya da kwanciyar hankali , ga yawaitar arziki.

Duk da irin daukakar da muhseena ta samu a wajen aikinta, bata taba fifita aikinta akan aurenta ba, duk runtsi bata taba tauye hakkin mijinta ba duk abinda yake so Shi take yi , tana daya daga cikin Mata masu biyayyar aure da zaa iya yin kwatance da su.

Shi yasa har yanzu Taufiq bsi hango wata kamarta ba,

Muhseena ta Sami hutun karshen shekara hakan yasa ta kwashe yayanta Hanif da Ansar da yayan mujaheeda fadwa da Aleena sai yarinyar Kabir muhseena suka daga zuwa Dubai domin ta samu ta huta,

A Daren ranar da ta dauka a Dubai suna waya da Taufiq Wanda yake Jin kamar ya kutso ya shigo ta cikin wayar "kin kwashe yayanki kin tafi kin bar yayanki cikin kewa".

Tayi murmushi tace "yaya Taufiq kaima kasan idan akwai abinda ke min kuna a raina bai wuce nisantarka ba, amma ina danne wasu abubuwan da yawa saboda Kada na kawo matsala tsakanina da anti mujaheeda, domin tabbas nasan kishi idan na taho tare da Kai dole sai ta ji babu dadi sai shaidan ya buga gangarsa ni Kuma Bana fatan ace nice silar Samun Wata baraka a tsakaninmu".

Ya lumshe Ido ya bude yace "Allah na gode maka da Ka ni'imta ni da Samun abokiyar rayuwa irinki muhseena, ina sonki ina sonki". Tayi murmushi tace "Ni ma ina sonka yayana, Kai wani bangare ne na rayuwata, awajena baka da tamka", ya aje numfashi me dauke da sakonni Kala Kala yace "har na Fara kewarki ke din ta dabance lalle Allah yayi gaskiya da baisa namiji yayi adalci a cikin soyayyar matansa ba, saboda yadda nake Jin sonki araina na rantse tamkar babu wasu Mata a duniya ban taba son wata mace yadda nake sonki ba".

Cikin jindadin maganganun sa tace " Shi yasa kullum nake gaya maka Ka dinga kokarin boye wannan soyayyar agaban anti mujaheeda domin hakan zai iya dasa Mata damuwa ni Kuma Bana son hakan".

Yace "ina kokarin boyewa sosai muhseena " tace "Allah ya barmu tare " "Amin ya Allah gimbiyata". Daga karshe su kayi sallama

Tayi kasa da wayar gami da daga hannayenta biyu tana yi ma Allah godiya, "Allah Alhamdulillah nagode maka da dukkan ni',imominka gare ni nagode Alhamdulillah Alhamdulillah Alhamdulillah".

Ta maida hannayenta kasa idanunta cike da hawaye tace idan ba Allah ba waye zai maka wannan, na Sami budin arziki, na Sami daukaka, na Zama abar sha'awa kowa na so ya San ni

yayi mu'amala da ni, ga iyayena na cikin daula da kwanciyar hankali, ga Kuma miji daya tamkar da dubu da Allah ya ba ni , duk burika na na rayuwa Allah ya cika min.

Ta goge hawayenta, tana fatan cigaba da rayuwa a yadda take yin ta yanzu.

ALHAMDULILLAH

SAI MUN HADU A SABON LITTAFINA MAI SUNA, A MACE KO A RAYE.

DAGA TASKAR YAR GIDAN IMAM.

MRS ALIYU MAYARE